# Holy Bible

## Aionian Edition®

## Littafi Mai Tsarki

## Hausa New Testament

AionianBible.org
The world's first Holy Bible untranslation
100% free to copy and print
also known as " The Purple Bible "

*Holy Bible Aionian Edition* ®
Littafi Mai Tsarki
Hausa New Testament

Creative Commons Attribution ShareAlike 4.0 International, 2018-2025
Source text: eBible.org
Source version: 4/18/2025
Source copyright: Creative Commons Attribution ShareAlike 4.0
Door43 World Missions Community, 2020

Formatted by Speedata Publisher 5.1.9 (Pro) on 6/3/2025
100% Free to Copy and Print
TOR Anonymously
https://AionianBible.org

Published by Nainoia Inc, https://Nainoia-Inc.signedon.net
All profits are given to https://CoolCup.org

We pray for a modern Creative Commons translation in every language
Translator resources at https://AionianBible.org/Third-Party-Publisher-Resources
Report content and format concerns to Nainoia Inc
Volunteer help is welcome and appreciated!

*Celebrate Jesus Christ's victory of grace!*

# Preface

Hausa at AionianBible.org/Preface

The *Holy Bible Aionian Edition* ® is the world's first Bible *un-translation*! What is an *un-translation*? Bibles are translated into each of our languages from the original Hebrew, Aramaic, and Koine Greek. Occasionally, the best word translation cannot be found and these words are transliterated letter by letter. Four well known transliterations are *Christ*, *baptism*, *angel*, and *apostle*. The meaning is then preserved more accurately through context and a dictionary. The Aionian Bible un-translates and instead transliterates eleven additional Aionian Glossary words to help us better understand God's love for individuals and all mankind, and the nature of afterlife destinies.

The first three words are *aiōn*, *aiōnios*, and *aïdios*, typically translated as *eternal* and also *world* or *eon*. The Aionian Bible is named after an alternative spelling of *aiōnios*. Consider that researchers question if *aiōn* and *aiōnios* actually mean *eternal*. Translating *aiōn* as *eternal* in Matthew 28:20 makes no sense, as all agree. The Greek word for *eternal* is *aïdios*, used in Romans 1:20 about God and in Jude 6 about demon imprisonment. Yet what about *aiōnios* in John 3:16? Certainly we do not question whether salvation is eternal! However, *aiōnios* means something much more wonderful than infinite time! Ancient Greeks used *aiōn* to mean *eon* or *age*. They also used the adjective *aiōnios* to mean *entirety*, such as *complete* or even *consummate*, but never infinite time. Read Dr. Heleen Keizer and Ramelli and Konstan for proofs. So *aiōnios* is the perfect description of God's Word which has *everything* we need for life and godliness! And the *aiōnios* life promised in John 3:16 is not simply a ticket to eternal life in the future, but the invitation through faith to the *consummate* life beginning now!

The next seven words are *Sheol*, *Hadēs*, *Geenna*, *Tartaroō*, *Abyssos*, and *Limnē Pyr*. These words are often translated as *Hell*, the place of eternal punishment. However, *Hell* is ill-defined when compared with the Hebrew and Greek. For example, *Sheol* is the abode of deceased believers and unbelievers and should never be translated as *Hell*. *Hadēs* is a temporary place of punishment, Revelation 20:13-14. *Geenna* is the Valley of Hinnom, Jerusalem's refuse dump, a temporal judgment for sin. *Tartaroō* is a prison for demons, mentioned once in 2 Peter 2:4. *Abyssos* is a temporary prison for the Beast and Satan. Translators are also inconsistent because *Hell* is used by the King James Version 54 times, the New International Version 14 times, and the World English Bible zero times. Finally, *Limnē Pyr* is the Lake of Fire, yet Matthew 25:41 explains that these fires are prepared for the Devil and his angels. So there is reason to review our conclusions about the destinies of redeemed mankind and fallen angels.

The eleventh word, *eleēsē*, reveals the grand conclusion of grace in Romans 11:32. Please understand these eleven words. The original translation is unaltered and a highlighted note is added to 64 Old Testament and 200 New Testament verses. To help parallel study and Strong's Concordance use, apocryphal text is removed and most variant verse numbering is mapped to the English standard. We thank our sources at eBible.org, Crosswire.org, unbound.Biola.edu, Bible4u.net, and NHEB.net. The Aionian Bible is copyrighted with creativecommons.org/licenses/by/4.0, allowing 100% freedom to copy and print, if respecting source copyrights. Check the Reader's Guide and read at AionianBible.org, with Android, and with TOR network. Why purple? King Jesus' Word is royal and purple is the color of royalty! All profits are given to CoolCup.org.

# History

Hausa at AionianBible.org/History

06/21/75 - Two boys, P. and J., wonder if Jesus saves all and pray.
04/15/85 - Aionian Bible conceived as B. and J. pray.
12/18/13 - Aionian Bible announced as J. and J. pray.
06/21/15 - Aionian Bible birthed as G. and J. pray.
01/11/16 - AionianBible.org domain registered.
06/21/16 - 30 translations available in 12 languages.
12/07/16 - Nainoia Inc established as non-profit corporation.
01/01/17 - Creative Commons Attribution No Derivatives 4.0 license added.
01/16/17 - Aionian Bible Google Play Store App published.
07/01/17 - 'The Purple Bible' nickname begins.
07/30/17 - 42 translations now available in 22 languages.
02/01/18 - Holy Bible Aionian Edition® trademark registered.
03/06/18 - Aionian Bibles available in print at Amazon.com.
09/15/18 - Aionian Bible dedicated as J. and J. pray again.
10/20/18 - 70 translations now available in 33 languages.
11/17/18 - 104 translations now available in 57 languages.
03/24/19 - 135 translations now available in 67 languages.
10/28/19 - Aionian Bible nursed as another J. and J. pray.
10/31/19 - 174 translations now available in 74 languages.
02/22/20 - Aionian Bibles available in print at Lulu.com.
05/25/20 - Illustrations by Gustave Doré, La Grande Bible de Tours, Felix Just.
08/29/20 - Aionian Bibles now available in ePub format.
12/01/20 - Right to left and Hindic languages now available in PDF format.
03/31/21 - 214 translations now available in 99 languages.
11/17/21 - Aionian Bible Branded Leather Bible Covers now available.
12/20/21 - Social media presence on Facebook, Twitter, LinkedIn, YouTube, etc.
01/01/22 - 216 translations now available in 99 languages.
01/09/22 - StudyPack resources for Bible translation study.
01/23/22 - Volunteers celebrate with pie and prayer.
02/14/22 - Strong's Concordance from Open Scriptures and STEPBible.
02/14/23 - Aionian Bible published on the TOR Network.
12/04/23 - Eleēsē added to the Aionian Glossary.
02/04/24 - 352 translations now available in 142 languages.
05/01/24 - 370 translations now available in 164 languages.
08/05/24 - 378 translations now available in 165 languages.
08/18/24 - Creative Commons Attribution 4.0 International, if source allows.
10/20/24 - Gospel Primer handout format.
11/24/24 - Progressive Web Application off-line format.
01/28/25 - All profits are given to CoolCup.org.
03/12/25 - 382 translations now available in 166 languages.
05/04/25 - 393 translations now available in 175 languages.
05/27/25 - 462 translations now available in 229 languages.

# Table of Contents

## NEW TESTAMENT


Mattiyu ........ 11
Markus ........ 37
Luka ........ 53
Yohanna ........ 82
Ayyukan Manzanni ........ 103
Romawa ........ 130
1 Korintiyawa ........ 142
2 Korintiyawa ........ 154
Galatiyawa ........ 162
Afisawa ........ 166
Filibbiyawa ........ 170
Kolossiyawa ........ 173
1 Tessalonikawa ........ 176
2 Tessalonikawa ........ 179
1 Timoti ........ 181
2 Timoti ........ 184
Titus ........ 187
Filemon ........ 189
Ibraniyawa ........ 190
Yaƙub ........ 199
1 Bitrus ........ 202
2 Bitrus ........ 206
1 Yohanna ........ 208
2 Yohanna ........ 211
3 Yohanna ........ 212
Yahuda ........ 213
Ru’uya ta Yohanna ........ 214


## APPENDIX


Reader's Guide
Glossary
Maps
Destiny
Illustrations, Doré

# NEW TESTAMENT




*Yesu yace, "Uba, ka yafe masu, gama basu san abin da suke yi ba."*
*Sai suka jefa kuri'a, suka rarraba tufafinsa.*
Luka 23:34

# Mattiyu

1 Littafin asalin Yesu Almasihu Dan Dauda, Dan
Ibrahim. 2 Ibrahim shine mahaifin Ishaku, Ishaku
shine mahaifin Yakubu, Yakubu shine mahaifin Yahuza
da 'yan'uwansa. 3 Yahuza shine mahaifin Farisa da
Zera, ta wurin Tamar. Farisa kuma shine mahaifin
Hasruna, Hasruna kuma shine mahaifin Aram. 4
Aram shine mahaifin Amminadab, Amminadab shine
mahaifin Nashon, Nashon shine mahaifin Salmon.
5 Salmon shine mahaifin Bo'aza ta wurin Rahab,
Bo'aza shine mahaifin Obida ta wurin Rut. Obida
shine mahaifin Yesse, 6 Yesse shine mahaifin sarki
Dauda. Sarki Dauda shine mahaifin Sulaimanu ta
wurin matar Uriya. 7 Sulaimanu shine mahaifin
Rehobo'am, Rehobo'am shine mahaifin Abija, Abija
shine mahaifin Asa. 8 Asa shine mahaifin Yehoshafat,
Yehoshafat shine mahaifin Yoram, Yoram kuma shine
mahaifin Uziya. 9 Uziya shine mahaifin Yotam, Yotam
shine mahaifin Ahaz, Ahaz shine mahaifin Hezekiya.
10 Hezekiya shine mahaifin Manassa, Manassa shine
mahaifin Amon, sannan Amon shine mahaifin Yosiya.
11 Yosiya shine mahaifin Yekoniya da 'yan'uwansa,
dai dai locacin da aka kwashe su zuwa kasar Babila.
12 Bayan kwasar su zuwa kasar Babila, Yekoniya
shine mahaifin Sheyaltiyel, Sheyaltiyel shine mahaifin
Zarubabel. 13 Zarubabel shine mahaifin Abihudu,
Abihudu shine mahaifin Eliyakim, sannan Eliyakim
shine mahaifin Azuru. 14 Azuru shine mahaifin
Saduku. Saduku shine mahaifin Akimu, sannan Akimu
shine mahaifin Aliyudu 15 Aliyudu shine mahaifin
Ali'azara, Ali'azara shine mahaifin Matana, sannan
Matana shine mahaifin Yakubu. 16 Yakubu shine
mahaifin Yusufu maigidan Maryamu, wadda ta wurin
ta ne aka haifi Yesu, wanda ake ce da shi Almasihu. 17
Tun daga Ibrahim zuwa Dauda, an yi tsara goma sha
hudu ne, daga Dauda zuwa lokacin da aka kwashe su
zuwa Babila, tsara goma sha hudu ne, sannan daga
lokacin da aka kwashe su zuwa Babila zuwa Almasihu
tsara goma sha hudu ne 18 Ga yadda haihuwar Yesu
Almasihu ta kasance. Mahaifiyarsa, Maryamu, tana
tashi da Yusufu, amma kafin su yi aure, sai aka
same ta da juna biyu ta wurin Ruhu Mai Tsarki. 19
Mijinta, Yusufu, adalin mutum ne, amma ba ya so ya
kunyatar da ita a sarari. Sai ya yi shawara ya sake ta
a asirce. 20 Yana cikin tunanin wadannan al'amura,
sai mala'ikan Ubangiji ya bayyana gareshi a mafarki,
ya ce masa, "Yusufu, dan Dauda, kada ka ji tsoron
daukar Maryamu a matsayin matarka. Gama abinda ke
cikinta, ta wurin Ruhu Mai Tsarki aka same shi. 21 Za
ta haifi Da, za ka kira sunansa Yesu, domin za ya ceci
mutanensa daga zunubansu." 22 Duk wannan ya faru
ne domin a cika abinda aka fada ta bakin annabin,
cewa, 23 "Duba, budurwa za ta sami juna biyu sannan
za ta haifi da, za su kira sunansa Immanuel"-ma'ana,
"Allah tare da mu." 24 Yusufu ya farka daga barci, ya
yi kamar yadda mala'ikan Ubangiji ya umarce shi, sai
ya dauke ta a matsayin matarsa. 25 Amma Yusufu bai
sadu da ita ba sai bayan da ta haifi da. Ya kira sunansa
Yesu.

2 Bayanda aka haifi Yesu a Baitalami ta kasar
Yahudiya, a zamanin sarki Hirudus, sai ga wadansu
masana daga gabas suka zo Urushalima, suna cewa,
2 ''Ina wanda aka haifa sarkin Yahudawa? Mun ga
tauraronsa a gabas mun kuma zo mu yi masa sujada.''
3 Da sarki Hirudus ya ji haka, sai ya damu kwarai,
haka kuma dukan mutanen Urushalima. 4 Hirudus ya
tara dukan manyan firistoci da marubuta na jama'a,
ya tambaye su, "Ina za a haifi Almasihun?" 5 Suka
ce masa, ''A Baitalami ne ta kasar Yahudiya, domin
haka annabin ya rubuta, 6 'Ke kuma, Baitalami, ta
kasar Yahudiya, ba ke ce mafi kankanta ba a cikin
shugabanin Yahudiya, domin daga cikin ki mai mulki
zai fito wanda zai zama makiyayin jama'a ta Isra'ila.'''
7 Sai Hirudus ya kira masanan a asirce ya tambaye su
aininhin lokacin da tauraron ya bayyana. 8 Ya aike su
Baitalami, ya ce, ''Ku je ku binciko mani dan yaron da
kyau. Idan kun same shi, ku kawo mani labari, don ni
ma in je in yi masa sujada." 9 Bayan sun ji maganar
sarkin, sai suka yi tafiyar su, ga shi kuwa, tauraron da
suka gani a gabas yana tafe a gaban su, har ya zo ya
tsaya bisa inda dan yaron nan yake. 10 Da suka ga
tauraron, sai suka yi matukar farin ciki. 11 Sai suka
shiga gidan, suka ga dan yaron tare da mahaifiyarsa
Maryamu. Suka rusuna gabansa suka yi masa sujada.
Sa'an nan suka kwance kayansu, suka mika masa
kyautar su ta zinariya da lubban, da mur. 12 Allah
kuma ya gargade su a mafarki kada su koma wurin
Hirudus, sai suka koma kasarsu ta wata hanya dabam.
13 Bayan sun tashi, sai ga wani mala'ikan Ubangiji
ya bayyana ga Yusufu a mafarki, ya ce, ''Tashi, ka
dauki dan yaron da mahaifiyarsa, ka gudu zuwa kasar
Masar, ka zauna a can sai na fada maka, don Hirudus

yana shirin binciko dan yaron ya hallaka shi.” 14 A
wannan dare fa Yusufu ya tashi ya dauki dan yaron
da mahafiyarsa ya tafi Masar. 15 Ya zauna a can har
mutuwar Hirudus. Wannan kuwa domin a cika abin
da Ubangiji ya fada ne ta bakin annabin, ''Daga Masar
na kirawo Da na.'' 16 Da Hirudus ya ga masanan nan
sun shashantar da shi, sai ya hasala kwarai, ya aika
a karkashe dukan 'yan yara maza da suke Baitalami
da kewayenta, daga masu shekara biyu zuwa kasa,
gwargwadon lokacin da ya tabbatar a gun masanan.
17 A lokacin ne aka cika fadar Annabi Irmiya, 18 ''An
ji wata murya a Rama, tana kuka da bakin ciki mai
zafi, Rahila ce take kuka saboda 'ya'yanta, kuma ta
ki ta ta'azantu, domin ba su. 19 Sa'adda Hirudus ya
mutu, sai ga mala'ikan Ubangiji ya bayyana ga Yusufu
a mafarki a Masar ya ce, 20 ''Tashi ka dauki dan
yaron da mahaifiyarsa, ka tafi kasar Isra'ila, domin
masu neman ran dan yaron sun mutu.'' 21 Yusufu ya
tashi, ya dauki dan yaron da mahaifiyarsa, ya zo kasar
Isra'ila. 22 Amma da ya ji Arkilayus ya gaji mahaifinsa
Hirudus, yana mulkin kasar Yahudiya, sai ya ji tsoron
isa can. Bayan da Allah ya yi masa gargadi a mafarki,
sai ya ratse zuwa kasar Galili 23 sai ya je ya zauna a
wani gari da ake kira Nazarat. Wannan ya cika abin
da aka fada ta bakin annabawa, cewa, za a kira shi
Banazare.

3 A kwanakin nan Yahaya Mai baftisma ya zo, yana
wa'azi a jejin Yahudiya yana cewa, 2 “Ku tuba,
domin mulkin sama ya kusa.” 3 Wannan shine wanda
annabi Ishaya ya yi maganarsa, ya ce, “Muryar wani
mai kira a jeji yana cewa, 'Ku shirya wa Ubangiji
hanyarsa, ku daidaita tafarkunsa.'' 4 Yahaya kuwa
yana sanye da tufa ta gashin rakumi, yana kuma
daure da damarar fata, abincinsa kuwa fara ne da
zuman jeji. 5 Sai mutanen Urushalima, da na dukan
Yahudiya, da na duk kasashen bakin Kogin Urdun,
suka yi ta zuwa wurin sa. 6 Ya yi masu baftisma a
Kogin Urdun, yayinda suke furta zunubansu. 7 Amma
da ya ga Farisawa da Sadukiyawa da yawa, suna fitowa
domin a yi masu baftisma, sai ya ce masu, “Ku 'ya'yan
macizai masu dafi, wa ya gargade ku ku guje wa fushi
mai zuwa? 8 Ku ba da 'ya'ya da za su nuna tubanku.
9 Kada kuwa ku dauka a ranku cewa, 'Ibrahim ne
ubanmu.' Domin ina gaya maku, Allah yana da iko ya
ta da wa Ibrahim 'ya'ya daga cikin duwatsun nan. 10
Ko yanzu ma an sa gatari a gindin bishiyoyin. Saboda
haka duk bishiyar da ba ta ba da 'ya'ya masu kyau ba,
sai a sare ta a jefa a wuta. 11 Na yi maku baftisma da
ruwa, zuwa tuba. Amma mai zuwa baya na, ya fi ni
girma, wanda ko takalmansa ma ban isa in dauka ba.
Shi ne zai yi maku baftisma da Ruhu Mai Tsarki, da
kuma wuta. 12 Kwaryar shikarsa na hannunsa, zai
kuwa share masussukarsa sarai, ya tara alkamarsa
ya sa a rumbunsa, amma zai kona buntun da wutar
da ba za a iya kashewa ba.” 13 Sai Yesu ya zo daga
kasar Galili, ya je Kogin Urdun wurin Yahaya, domin
ya yi masa baftisma. 14 Amma Yahaya ya yi ta kokarin
ya hana shi, yana cewa, “Ni da nake bukatar ka yi
mani baftisma, ka zo gare ni?” 15 Yesu ya amsa masa
ya ce, “Bari ya zama haka a yanzu, domin a cika
dukan adalci.” Sai Yahaya ya yarje masa. 16 Bayan
da aka yi masa baftisma, Yesu ya fito nan da nan
daga cikin ruwan, sai kuma sammai suka bude masa.
Ya ga Ruhun Allah yana saukowa kamar kurciya, ya
sauko a kansa. 17 Duba, wata murya daga sammai tana
cewa, ''Wannan shi ne kaunataccen Da na. Wanda ya
gamshe ni sosai.''

4 Sa'an nan Ruhu ya bi da Yesu zuwa cikin jeji, domin
Ibilis ya gwada shi. 2 Da ya yi azumi kwana arba'in
dare da rana, daga baya yunwa ta kama shi. 3 Sai
mai jarabtar nan ya zo, ya ce masa, “Idan kai Dan
Allah ne, ka umarci duwatsun nan su zama gurasa.” 4
Amma Yesu ya amsa ya ce masa, “A rubuce yake cewa,
'Ba da gurasa kadai mutum zai rayu ba, sai dai da
kowace magana da ta ke fitowa daga wurin Allah.''' 5
Sa'an nan Ibilis ya kai shi tsattsarkan birni ya dora
shi can kan kololuwar ginin haikali, 6 ya ce masa,
“In kai Dan Allah ne, to dira kasa. Domin a rubuce
yake cewa, 'Zai ba mala'ikunsa umarni game da kai,'
kuma, 'Za su daga ka da hannuwansu, domin kada ka
yi tuntube da dutse.''' 7 Yesu ya ce masa, “kuma a
rubuce yake, 'Kada ka gwada Ubangiji Allahnka.''' 8
Kuma, sai Ibilis ya kai shi kan wani dutse mai tsawo
kwarai, ya nuna masa dukan mulkokin duniya da
darajarsu. 9 Ya ce masa, “Dukan wadannan zan baka
idan ka rusuna ka yi mani sujada.'' 10 Sai Yesu ya
ce masa, “Tafi daga nan, Shaidan! Domin a rubuce
yake, 'Ka yi wa Ubangiji Allahnka sujada, shi kadai
za ka bauta wa.''' 11 Sa'an nan Ibilis ya rabu da shi,
sai kuma mala'iku suka zo suka yi masa hidima. 12
To, da Yesu ya ji an kama Yahaya, sai ya tashi zuwa
kasar Galili. 13 Ya bar Nazarat, ya koma Kafarnahum

da zama, can bakin tekun Galili, kan iyakar kasar
Zabaluna da Naftali. 14 Wannan ya faru domin a cika
fadar annabi Ishaya cewa, 15 "Kasar Zabaluna da
kasar Naftali, ta bakin teku, da hayin Kogin Urdun,
Galili ta al'ummai! 16 Mutane mazauna duhu suka ga
babban haske, sannan ga wadanda ke zaune a yankin
da inuwar mutuwa, haske ya keto masu." 17 Daga
lokacin nan, Yesu ya fara wa'azi, yana cewa, "Ku tuba
domin mulkin sama ya kusa." 18 Yana tafiya a bakin
tekun Galili, sai ya ga wadansu 'yan'uwa biyu, Saminu
da ake kira Bitrus, da dan'uwansa Andarawas, suna
jefa taru a teku, domin su masunta ne. 19 Yesu ya ce
masu, "Ku zo, ku biyo ni, zan mai da ku masuntan
mutane." 20 Nan da nan sai suka bar tarunsu, suka
bi shi. 21 Da Yesu ya ci gaba da tafiya, sai ya ga
wadansu mutum biyu, su kuma 'yan'uwa ne, Yakubu
dan Zabadi, da dan'uwansa Yahaya, suna cikin jirgi
tare da mahaifinsu Zabadi, suna gyaran tarunsu. Sai
ya kira su. 22 Nan take suka bar mahaifinsu da jirgin,
suka bi shi. 23 Yesu ya zazzaga dukan kasar Galili,
yana koyarwa a majami'unsu, yana shelar bisharar
mulkin, yana kuma warkar da kowace cuta da rashin
lafiya a cikin mutane. 24 Labarinsa ya bazu a cikin
dukan kasar Suriya, kuma mutanen suka kakkawo
masa dukan marasa lafiya, masu fama da cuta iri iri,
da masu shan azaba, da kuma masu aljannu, da masu
farfadiya, da shanyayyu. Yesu ya warkar da su. 25 Taro
masu yawa suka bi shi daga kasar Galili, da Dikafolis,
da Urushalima, da kasar Yahudiya, har ma daga hayin
Urdun.

5 Da Yesu ya ga taron jama'ar, sai ya hau saman dutse.
Sa'adda ya zauna, almajiransa suka zo wurinsa. 2
Ya bude bakinsa kuma ya koyar da su, yana cewa, 3
"Albarka ta tabbata ga masu talauci a ruhu, domin
mulkin sama nasu ne. 4 Albarka ta tabbata ga masu
makoki, domin za a ta'azantar da su. 5 Albarka ta
tabbata ga masu tawali'u, domin za su gaji duniya. 6
Albarka ta tabbata ga masu yunwa da kishin adalci,
domin za a kosar da su. 7 Albarka ta tabbata ga masu
jinkai, domin za su samu jinkai. 8 Albarka ta tabbata ga
masu tsabtar zuciya, domin za su ga Allah. 9 Albarka
ta tabbata ga masu kawo salama, domin za a ce da
su 'ya'yan Allah. 10 Albarka ta tabbata ga wadanda
ake tsananta masu saboda adalci, domin mulkin sama
nasu ne. 11 Masu albarka ne ku sa'adda mutane suka
zage ku, suka kuma tsananta maku, ko kuwa suka
zarge ku da dukan miyagun abubuwa iri iri na karya,
saboda ni. 12 Ku yi murna da matukar farin ciki,
domin sakamakonku mai yawan gaske ne a sama. Ta
haka ne mutane suka tsananta wa annabawa da suka
yi rayuwa kafin ku. 13 Ku ne gishirin duniya, amma
idan gishiri ya sane yaya za a mai da dandanonsa?
Ba zai kara anfani ga komai ba, sai ko a zubar da
shi, a tattake a karkashin kafafun mutane. 14 Ku ne
hasken duniya, birnin da ke kan tudu ba shi boyuwa.
15 Mutane ba za su kunna fitila su sa ta karkashin
kwando ba, sai ko a dora ta a mazaunin ta, domin ta
ba da haske ga kowa da ke gidan. 16 Bari hasken ku
ya haskaka gaban mutane yadda za su ga kyawawan
ayyukanku su kuma yabi Ubanku da ke cikin sama.
17 Kada ku yi tsammanin na zo ne domin in rushe
shari'a ko annabawa. Ban zo domin in rushe su ba,
amma domin in cika su. 18 Domin gaskiya ina gaya
maku, har sama da kasa su shude, amma digo ko
wasali daya ba za ya shude ba a cikin shari'ar, sai
an cika dukan al'amura. 19 Saboda haka duk wanda
ya karya mafi kankanta daga cikin dokokin nan ko
kuwa ya koya wa wasu su yi haka, za a kira shi mafi
kankanta a cikin mulkin sama. Amma dukan wanda
ya kiyaye su ko kuwa ya koyar da su, za a kira shi mafi
girma a cikin mulkin sama. 20 Gama ina gaya maku
cewa idan adalcin ku bai zarce adalcin marubuta da
Farisawa ba, babu yadda za ku shiga mulkin sama. 21
Kun ji dai an ce wa mutanen da, 'Kada ka yi kisan kai,'
kuma 'Duk wanda ya yi kisan kai yana cikin hatsarin
hukunci.' 22 Amma ina gaya muku, duk wanda ya yi
fushi da dan'uwansa, yana cikin hatsarin hukunci.
Kuma duk wanda ya ce da dan'uwansa, 'Kai mutumin
banza!' yana cikin hatsarin tsayawa gaban majalisa,
kowa kuma ya ce da dan'uwan sa 'Kai wawa!' yana
cikin hatsarin shiga wutar jahannama. (Geenna g1067)
23 Saboda haka idan za ka yi baiko a bagadi sai ka
tuna cewa dan'uwanka yana da damuwa da kai, 24 ka
bar baikon ka a gaban bagadin, ka yi tafiyarka. Da
farko dai, ka sasanta da dan'uwanka kafin ka zo ka
mika baikon. 25 Ka yi sulhu da mai karar ka tun kana
hanyar zuwa gaban shari'a, domin kada mai karar
ka ya mika ka ga alkali, alkali kuwa ya mika ka ga
dogarai, za a kuwa jefa ka a kurkuku. 26 Gaskiya ina
gaya maka, ba za ka taba fita daga can ba sai ko ka
biya dukan kudin da ya ke binka. 27 Kun dai ji an
ce, 'Kada ka yi zina'. 28 Amma ina gaya maku, duk
wanda ya dubi mace, da muguwar sha'awa, ya riga ya

yi zina da ita a zuciyarsa. 29 Idan idonka na dama
zai sa ka tuntube, kwakule shi ka jefar daga gareka.
Don gara daya daga cikin gabobinka ya halaka, da a
jefa dukan jikin ka a jahannama. (Geenna g1067) 30 Ko
kuwa idan hannunka na dama zai sa ka tuntube, ka
yanke shi ka jefar daga gare ka. Domin gara daya daga
cikin gabobin ka ya halaka, da a jefa dukan jikinka a
jahannama. (Geenna g1067) 31 An sake fada, 'Duk wanda
ya kori matarsa, sai ya ba ta takaddar saki.' 32 Amma
ina gaya maku ko wa ya saki matarsa, idan ba a kan
laifin lalata ba, ya mai da ita mazinaciya kenan. Kuma
duk wanda ya aure ta bayan sakin, ya yi zina kenan.
33 Kun sake ji an ce wa wadan da suke a zamanin da,
'Kada ku yi rantsuwar karya, amma ku yi rantsuwar
ku ga Ubangiji.' 34 Amma ina gaya maku, kada ku
yi rantsuwa sam, ko da sama domin kursuyin Allah
ne; 35 ko kuwa da duniya, domin mazaunin kafafunsa
ne, ko da Urushalima, domin birnin babban sarki
ne. 36 Ko ma ace ku yi rantsuwa da kanku, domin
ba za ku iya mai da gashin kanku baki ko fari ba. 37
Amma bari maganarku ta zama 'I, I', ko kuwa 'A'a,
a'a.' Duk abin da ya wuce wannan, daga mugun yake.
38 Kun dai ji an ce, “Ido a maimakon ido, hakori
kuma a maimakon hakori.' 39 Amma ina gaya maku,
kada ku yi jayayya da wanda ke mugu, a maimakon
haka, ko wa ya mare ku a kuncin dama, ku juya masa
dayan ma. 40 Idan wani yana da niyyar kai kararku
gaban shari'a saboda ya karbi rigarku, ku ba wannan
mutumin mayafinku ma. 41 Duk wanda ya tilasta ku
ga tafiyar mil daya, ku je da shi biyu. 42 Ku ba kowa
da ya tambaye ku, kuma kada ku hana kowa da ke
neman rance a wurinku. 43 Kun ji abin da aka fada,
'Za ka kaunaci makwabcin ka ka ki magabcin ka.' 44
Amma ina gaya maku, ku kaunaci magabtan ku, ku
yi addu'a domin masu tsananta maku, ku albarkaci
wadanda suka la'ance ku, ku yi alheri ga wadanda
suke kin ku, 45 domin ku zama 'ya'yan Ubanku da ke
cikin sama. Domin yakan sa rana ta haskaka wa mugu
da mutumin kirki, kuma yakan aiko da ruwan sama
ga adali da azzalumi. 46 Domin idan kuna kaunar
wadanda suke kaunarku, wanne lada kuka samu? Ba
haka masu karban haraji ma suke yi ba? 47 Kuma
in kun gaida 'yan'uwanku kadai, me kuke yi fiye da
sauran? Ba hakanan al'ummai ma suke yi ba? 48
Saboda haka, lalle ne ku zama cikakku, kamar yadda
Ubanku na sama yake cikakke.

6 Ku yi hankali kada ku yi ayyukan adalcinku gaban
mutane domin su ganku, idan kun yi haka, ba za
ku sami sakamako a wurin Ubanku da yake sama ba. 2
Saboda haka, in za ku yi sadaka, kada ku busa kaho
yadda munafukai suke yi a majami'u da kuma akan
tituna domin mutane su yabesu. Gaskiya ina gaya
maku, sun samu ladansu. 3 Amma in za ku yi sadaka,
kada hannunku na hagu ya san abin da hannunku na
dama yake yi, 4 domin sadakarku ta zama a asirce.
Ubanku kuwa da yake ganin abin da ake yi a asirce,
zai saka maku. 5 Sa'adda za ku yi addu'a kuma, kada
ku zama kamar munafukai, domin sun cika son yin
addu'a a tsaye a majami'unsu da kuma a gefen tituna,
domin mutane su gansu. Gaskiya ina gaya maku, sun
sami ladarsu kenan. 6 Amma ku, idan za ku yi addu'a,
sai ku shiga cikin daki. Ku rufe kofa, ku yi addu'a
ga Ubanku wanda yake a asirce, Ubanku kuwa da ke
ganin abin da ake yi a asirce, zai saka maku. 7 Idan za
ku yi addu'a, kada ku yi ta maimaici marar anfani,
kamar yadda al'ummai suke yi, domin a tunanin su za
a saurare su saboda yawan maganganunsu. 8 Domin
haka, kada ku zama kamarsu, domin Ubanku ya san
bukatar ku tun kafin ku roke shi. 9 Saboda haka
sai ku yi addu'a kamar haka: 'Ubanmu da ke sama,
bari a tsarkake sunanka. 10 Bari mulkinka shi zo.
Bari nufinka ya yiwu a duniya kamar yadda ake yi a
sama. 11 Ka ba mu yau abincinmu na kullum. 12 Ka
gafarta mana basussukanmu, kamar yadda mu ma
muke gafarta ma wadanda muke bi bashi. 13 Kuma
kada ka kawo mu cikin jaraba, amma ka kubutar da
mu daga Mugun.' [Gama mulki da iko da daukaka
naka ne har abada. Amin] 14 Domin in kun yafe wa
mutane laifuffukansu, Ubanku na Sama shima zai yafe
maku. 15 In kuwa ba ku yafe wa mutane laifuffukansu
ba, Ubanku ma ba zai yafe muku laifuffukanku ba.” 16
Haka kuma, in za ku yi azumi, kada ku zama da fuska
kamar masu makoki yadda munafukai ke yi, domin
sukan yankwane fuskokinsu, domin su bayyana ga
mutane kamar suna azumi. Gaskiya, ina gaya maku,
sun sami ladansu ke nan. 17 Amma in kuna azumi, ku
shafa mai a ka, ku kuma wanke fuska, 18 don kada
mutane su gane kuna azumi, sai dai Ubanku da yake a
asirce. Kuma Ubanku da ke ganin abinda ke a asirce,
zai saka maku.” 19 “Kada ku tara wa kanku dukiya
a duniya, inda asu da tsatsa ke batawa, inda barayi
kuma ke fasawa su yi sata. 20 Maimakon haka, ku tara
wa kanku dukiya a sama, inda babu asu da tsatsa da

za su bata, inda kuma ba barayi da za su fasa su yi
sata. 21 Domin inda dukiyar ka take, a nan zuciyar ka
ma take. 22 Ido shi ne fitilar jiki. Saboda haka, idan
idonka na da kyau, dukan jiki na cike da haske. 23
Amma in idonka na da lahani, dukan jiki na cike da
duhu. Saboda haka, in hasken da yake cikinka duhu
ne, ina misalin yawan duhun! 24 Ba mai iya bauta wa
iyayengiji biyu, ko dai ya ki daya, ya so daya, ko kuma
ya amince wa dayan ya raina dayan. Ba dama ku bauta
wa Allah da kuma dukiya. 25 Saboda haka ina gaya
maku, kada ku damu a kan rayuwarku, game da abin
da za ku ci, da abin da za ku sha- ko kuwa jikinku,
abin da za ku yi tufafi da shi. Ashe rai bai fi abinci
ba, jiki kuma bai fi tufafi ba? 26 Ku dubi tsuntsayen
da ke sararin sama. Ai, ba su shuka, balle girbi, ba
su kuma tarawa a cikin rumbuna, amma Ubanku na
Sama na ciyar da su. Ashe, ba ku fi su martaba ba?
27 Kuma wanene a cikinku, don damuwarsa, zai iya
kara ko taki ga tsawon rayuwarsa? 28 To, don me kuke
damuwa a kan tufafi? Ku dubi furannin jeji, yadda
suke girma. Ba su aiki, kuma ba su sakar kaya. 29
Duk da haka ina gaya maku, ko Sulaimanu ma, cikin
dukan daukakar sa bai yi ado kamar daya daga cikin
wadannan ba. 30 Idan Allah yayi wa ciyawar jeji ado,
wadda yau tana wanzuwa, gobe kuwa a jefa ta cikin
murhu, ina misalin adon da za ya yi maku, ya ku masu
karancin bangaskiya? 31 Don haka kada ku damu,
kuna cewa, 'Me za mu ci? ko, Me za mu sha?' ko
kuwa, 'Wadanne tufafi za mu sa?' 32 Ai, al'ummai ma
suna neman dukan irin wadannan abubuwa, Ubanku
na sama kuwa ya san kuna bukatarsu. 33 Amma ku
nemi mulkinsa da farko da adalcinsa, kuma dukan
wadannan abubuwa za a baku. 34 "Saboda haka kada
ku damu don gobe, ai, gobe za ta damu da kanta.
Kowace rana ta na cike da wahalarta".

7 Kada ku yi hukunci, domin ku ma kada a hukunta
ku. Domin da irin hukuncin da ku kan hukunta
da shi za a hukunta ku. 2 Mudun da kukan auna,
da shi za a auna maku. 3 Don me kake duban dan
hakin da ke idon dan'uwanka, amma ba ka kula da
gungumen da ke naka idon ba? 4 Ko kuwa yaya za
ka iya ce wa dan'uwanka, 'Bari in cire maka dan
hakin da ke idon ka,' alhali ga gungume a cikin naka
idon? 5 Kai munafiki! Ka fara cire gungumen da ke
idonka, sa'annan za ka iya gani sosai yadda za ka
cire dan hakin da ke idon dan'uwanka. 6 Kada ku ba
karnuka abin da ke tsattsarka. Kada kuma ku jefa wa
aladu, lu'u lu'anku. Idan ba haka ba za su tattake su
a karkashin sawunsu, su kuma juyo su kekketa ku.
7 Roka, kuma za a ba ku. Nema, kuma za ku samu.
Kwankwasa kuma za a bude maku. 8 Ai duk wanda ya
roka, zai karba, kuma duk wanda ya nema zai samu,
wanda ya kwankwasa kuma za a bude masa. 9 Ko,
kuwa wane mutum ne a cikin ku, dan sa zai roke shi
gurasa, ya ba shi dutse? 10 Ko kuwa in ya roke shi kifi,
zai ba shi maciji? 11 Saboda haka, idan ku da ku ke
miyagu, kun san yadda za ku ba da kyautai masu kyau
ga 'ya'yanku, ina kimanin yadda Ubanku na sama
zai ba da abubuwa masu kyau ga duk wadanda suke
rokon sa? 12 Saboda haka, duk abinda ku ke so mutane
su yi maku, ku ma sai ku yi masu, domin wannan shi
ne dukan shari'a da koyarwar annabawa. 13 Ku shiga
ta matsattsiyar kofa, don kofar zuwa hallaka na da
fadi, hanyar ta mai saukin bi ce, masu shiga ta cikin
ta suna da yawa. 14 Domin kofar zuwa rai matsattsiya
ce, hanyar ta mai wuyar bi ce, masu samun ta kuwa
kadan ne. 15 Ku kula da annabawan karya, wadanda
su kan zo maku da siffar tumaki, amma a gaskiya
kyarketai ne masu warwashewa. 16 Za ku gane su ta
irin ''ya'yansu. Mutane na cirar inabi a jikin kaya,
ko kuwa baure a jikin sarkakkiya? 17 Haka kowanne
itace mai kyau yakan haifi kyawawan 'ya'ya, amma
mummunan itace kuwa yakan haifi munanan 'ya'ya.
18 Kyakkyawan itace ba zai taba haifar da munanan
'ya'ya ba, haka kuma mummunan itace ba zai taba
haifar da kyawawan 'ya'ya ba. 19 Duk itacen da ba ya
ba da 'ya'ya masu kyau, sai a sare shi a jefa a wuta. 20
Domin haka, ta irin 'ya'yansu za a gane su. 21 Ba duk
mai ce mani, 'Ubangiji, Ubangiji,' ne, zai shiga mulkin
sama ba, sai dai wanda ya yi nufin Ubana da yake cikin
sama. 22 A ranar nan da yawa za su ce mani, 'Ubangiji,
Ubangiji,' ashe ba mu yi annabci da sunanka ba, ba mu
fitar da aljanu da sunanka ba, ba mu kuma yi manyan
ayyuka masu yawa da sunanka ba?' 23 Sa'annan zan
ce masu 'Ni ban taba saninku ba! Ku rabu da ni, ku
masu aikata mugunta!' 24 Saboda haka, dukan wanda
yake jin maganata, yake kuma aikata ta, za a kwatanta
shi da mutum mai hikima, wanda ya gina gidan sa
a bisa dutse. 25 Da ruwa ya sauko, ambaliyar ruwa
ta zo, iska ta taso ta buga gidan, amma bai fadi ba,
domin an gina shi bisa dutse. 26 Amma duk wanda ya
ji maganar nan tawa, bai aikata ta ba, za a misalta shi
da wawan mutum da ya gina gidansa a kan rairayi.

27 Ruwa ya sauko, ambaliyar ruwa ta zo, sai iska ta
taso ta buga gidan. Sai kuma ya rushe, ya kuwa yi
cikakkiyar ragargajewa.'' 28 Ya zama sa'adda Yesu ya
gama fadin wadannan maganganu, sai taro suka yi
mamakin koyarwarsa, 29 Domin yana koya masu da
iko, ba kamar marubuta ba.

8 Da Yesu ya sauko daga dutsen, sai taro masu yawa
suka bi shi. 2 Sai wani kuturu ya zo gunsa ya yi
masa sujada, ya ce, "Ubangiji, in dai ka yarda, za ka
iya tsarkake ni." 3 Yesu ya mika hannunsa ya taba
shi, ya ce, "Na yarda, ka tsarkaka." Nan da nan aka
tsarkake shi daga kuturtarsa. 4 Yesu ya ce masa, 'Ka
tabbata, ba ka gaya wa kowa komai ba. Sai dai ka
je ka nuna kan ka ga firist, ka kuma bayar da baiko
da Musa ya umarta domin shaida garesu? 5 Da Yesu
ya shiga kafarnahum, sai wani hafsa ya zo gunsa
ya roke shi, 6 Ya ce, Ubangiji, bawana na kwance
shanyayye a gida, yana shan azaba kwarai." 7 Yesu ya
ce masa, "Zan zo in warkar da shi." 8 Sai hafsan, ya
ce, "Ubangiji, ban isa har ka zo gida na ba, amma sai
ka yi magana kawai, bawana kuwa zai warke. 9 Domin
ni ma ina karkashin ikon wani ne, ina kuma da sojoji a
karkashina, sai in ce wa wannan, 'je ka,' sai ya je, wani
kuma in ce masa, 'zo,' sai ya zo, in ce wa bawa na, 'yi
abu kaza,' sai ya yi," 10 Da Yesu ya ji haka, sai ya yi
mamaki, har ya ce wa mabiyansa, "Gaskiya, ina gaya
maku, ko a cikin isra'ila ban taba samun bangaskiya
mai karfi irin wannan ba. 11 Na gaya maku, da yawa
za su zo daga gabas da yamma, su zauna cin abinci
tare da Ibrahim da Ishaku, da Yakubu a cikin mulkin
sama. 12 Amma 'ya'yan mulkin kuwa sai a jefa su
cikin matsanancin duhu. Can za su yi kuka da cizon
hakora." 13 Yesu ya ce wa hafsan, "Je ka! Bari ya zamar
maka gwargwadon bangaskiyar da ka yi," A daidai
wannan sa'a bawansa ya warke. 14 Da Yesu ya shiga
gidan Btrus, sai ya ga surukar Bitrus tana kwance
da zazzabi. 15 Yesu ya taba hannunta, zazzabin ya
sake ta, ta kuma tashi ta fara yi masa hidima. 16 Da
maraice ya yi, sai mutanen suka kakkawo wa Yesu
masu aljanu da yawa. Da magana kawai ya fitar da
aljanun, ya kuma warkar da dukan marasa lafiya. 17
Ta haka kuwa maganar annabi Ishaya ta samu cika
cewa, "Shi da kansa ya debe rashin lafiyar mu, ya
dauke cututtukan mu." 18 Sa'adda Yesu ya ga taro
masu yawa kewaye da shi, sai ya ba da umarni su tafi
su koma wancan hayi na tekun Galili. 19 Sai wani
marubuci ya zo ya ce masa, "Malam, zan bi ka duk
inda za ka je." 20 Yesu ya ce masa, "Yanyawa suna da
ramukansu, tsuntsayen sama kuma da shekunan su,
amma Dan mutum ba shi da wurin da zai kwanta." 21
Wani cikin almajiran ya ce masa, "Ubangiji, ka bar
ni tukuna in je in binne mahaifina." 22 Amma Yesu
ya ce masa, "Bari matattu su binne matattunsu." 23
Da Yesu ya shiga jirgi, almajiransa suka bi shi. 24 Sai
ga wata babbar iska ta taso a tekun, har rakuman
ruwa suka fara shan kan jirgin. Amma Yesu yana
barci. 25 Sai almajiran sa suka je suka tashe shi, suka
ce, "Ubangiji, ka cece mu, za mu hallaka!" 26 Yesu
ya ce masu, "Don me kuka firgita haka, ya ku masu
karancin bangaskiya?" Sa'annan ya tashi, ya tsauta
wa iskar da tekun. Sai wurin gaba daya ya yi tsit. 27
Mutanen suka yi al'ajibi, suka ce, "Wanne irin mutum
ne wannan, wanda har iska da teku ma suke masa
biyayya?". 28 Da Yesu ya zo daga wancan hayin a kasar
Garasinawa, mutane biyu masu al'janu suka fito suka
same shi. Suna fitowa daga makabarta kuma suna da
fada sosai, har ma ba mai iya bin ta wannan hanya. 29
Sai suka kwala ihu suka ce, "Ina ruwanka da mu, kai
dan Allah? Ka zo nan ne ka yi mana azaba tun kafin
lokaci ya yi?" 30 To akwai wani garken aladu masu
yawa na kiwo, babu nisa da su. 31 Sai al'janun suka
roki Yesu suka ce, "In ka fitar da mu, tura mu cikin
garken aladun nan." 32 "Yesu ya ce masu, "To, ku
je." Sai aljanun suka fita, suka shiga cikin aladun. Sai
kuwa duk garken suka rugungunta ta gangaren, suka
fada cikin tekun, suka hallaka a ruwa. 33 Mutanen
masu kiwon aladun suka gudu, suka shiga gari, suka
yi ta ba da labarin komai da komai, musamman abin
da ya faru da masu al'janun. 34 Sai duk jama'ar gari
suka fito su sami Yesu. Da suka gan shi, suka roke shi
ya bar kasarsu.

9 Yesu ya shiga jirgi ya haye ya je birninsa. 2 Sai
gashi, sun kawo masa wani mutum shanyayye
kwance a tabarma. Da Yesu ya ga bangaskiyarsu, sai
ya ce wa shanyayyen, ''Da, ka yi farin ciki. An gafarta
maka zunuban ka.'' 3 Sai wadansu marubuta suka ce a
tsakaninsu, ''Wannan mutum sabo yake yi.'' 4 Yesu
kuwa da yake ya san tunaninsu, yace, ''Don me kuke
mugun tunani a zuciyarku? 5 Wanne ya fi sauki, a ce,
'An gafarta maka zunubanka,' ko kuwa a ce, 'Tashi
ka yi tafiya'? 6 Amma domin ku sani Dan mutum
yana da ikon gafarta zunubai a duniya...'' Sai ya ce

wa shanyayyen, ''Tashi, ka dauki shimfidarka ka tafi
gida.'' 7 Mutumin kuwa ya tashi ya tafi gida. 8 Da
taron suka ga haka sai suka yi mamaki, suka daukaka
Allah, wanda ya ba mutane irin wannan iko. 9 Da
Yesu ya yi gaba, ya ga wani mutum mai suna Matiyu a
zaune, yana aiki a wurin karbar haraji. Yace masa,
''Ka biyo ni.'' Ya tashi ya bi shi. 10 Sa'adda kuma Yesu
yake cin abinci a gida, sai ga masu karbar haraji da
masu zunubi da yawa sun zo, sun zauna tare da shi da
almajiransa. 11 Da Farisawa suka ga haka, sai suka ce
wa almajiransa, ''Don me malamin ku ya ke ci tare da
masu karbar haraji da masu zunubi?'' 12 Amma da
Yesu ya ji haka ya ce, ''Ai, lafiyayyu ba ruwansu da
likita, sai dai marasa lafiya. 13 Sai ku fahimci ma'anar
wannan tukuna, 'Ni kam, ina bukatar jinkai ba hadaya
ba.' Ba domin in kira masu adalci su tuba na zo ba,
sai dai masu zunubi. 14 Sai almajiran Yahaya suka zo
wurinsa, suka ce, ''Don me mu da Farisawa mu kan yi
azumi a kai a kai, amma naka almajiran ba su yi?''
15 Sai Yesu ya ce masu, ''Masu hidimar buki za su yi
bakin ciki tun ango yana tare da su? Ai, lokaci yana
zuwa da za a dauke masu angon. A sa'annan ne fa za
su yi azumi.'' 16 Babu mutumin da zai sa sabon kyalle
a kan tsohuwar tufa, domin kyallen zai yage daga
tufar, har ma yagewar ta fi ta da. 17 Mutane kuma ba
su dura sabon ruwan inabi a tsofaffin salkuna. Idan
sun yi haka, sai salkunan kuma su fashe inabin ya
tsiyaye, sai salkunan su lalace. A maimakon haka,
ana sa sabon inabi cikin sababbin salkuna, ta haka
an tsirar da duka biyun kenan.'' 18 Yesu kuwa yana
cikin yi masu magana sai ga wani shugaban jama'a
ya zo ya yi masa sujada, ya ce, ''Yanzun nan 'yata ta
rasu, amma ka zo ka dora mata hannu, za ta rayu.'' 19
Sai Yesu ya tashi ya bi shi tare da almajiransa. 20 Sai
ga kuma wata mace wadda ta yi shakaru goma sha
biyu tana zubar da jini sosai, ta rabo ta bayan Yesu, ta
taba gezar mayafinsa. 21 Domin ta ce a ran ta, ''Ko da
mayafinsa ma na taba, sai in warke.'' 22 Sai Yesu ya
juya, ya gan ta ya ce, '''Yata, ki karfafa. Bangaskiyarki
ta warkar da ke.'' Nan take matar ta warke. 23 Da
Yesu ya isa gidan shugaban jama'ar, ya kuma ga masu
busar sarewa da taro suna ta hayaniya sosai. 24 Sai ya
ce, ''Ku ba da wuri, ai, yarinyar ba matacciya take
ba, barci ta ke yi.'' Sai suka yi masa dariyar raini. 25
Sa'adda aka fitar da taron waje, ya shiga ya kama
hannunta, sai kuwa yarinyar ta tashi. 26 Labarin kuwa
ya bazu a duk yankin. 27 Da Yesu ya yi gaba daga
nan, sai wadansu makafi biyu suka bi shi, suna daga
murya suna cewa, ''Ya Dan Dauda, ka ji tausayinmu.''
28 Da Yesu ya shiga wani gida sai makafin suka zo
gareshi. Yesu ya ce masu, “Kun gaskata ina da ikon
yin haka?'' Sai suka ce masa. ''I, ya Ubangiji.'' 29
Sai Yesu ya taba idanunsu, ya ce, ''Ya zama maku
gwargwadon bangaskiyarku.'' 30 Sai idanunsu suka
bude. Amma Yesu ya umarce su kwarai, ya ce, ''Kada
fa kowa ya ji labarin nan.'' 31 Amma suka tafi suka yi
ta baza labarinsa a duk yankin. 32 Da makafin biyu
suka tafi, sai aka kawo wa Yesu wani bebe mai aljani.
33 Bayan da an fitar da aljanin, sai beben ya yi magana,
taron kuwa suka yi mamaki, su ka ce, ''Kai, ba a taba
ganin irin wannan a cikin Isra'ila ba!'' 34 Amma sai
Farisawa suka ce, ''Ai, da ikon sarkin aljanu ya ke fitar
da aljanu.'' 35 Sai Yesu ya zazzaga dukan garuruwa
da kauyuka, yana koyarwa a majami'unsu, yana yin
bisharar mulkin Allah, yana kuma warkar da kowace
irin cuta da rashin lafiya. 36 Amma da ya ga taro masu
yawa sai ya ji tausayinsu, domin suna shan wahala
kuma sun karaya. Suna nan kamar tumaki da babu
makiyayi. 37 Sai ya ce wa almajiransa, ''Girbin yana da
yawa, amma ma'aikatan kadan ne. 38 Saboda haka sai
ku yi sauri ku roki Ubangijin girbin ya turo ma'aikata
cikin girbinsa.''

10 Yesu ya kira almajiransa goma sha biyu, ya kuma
ba su ikon fitar da kazaman ruhohi, su warkar
da kowacce irin cuta da rashin lafiya. 2 To yanzu ga
sunayen manzanin nan goma sha biyu. Na farkon
shine, Saminu, wanda ake kira Bitrus, da dan'uwansa
Andarawas, da Yakubu dan Zabadi, da dan'uwansa
Yahaya; 3 Filibus, da Bartalamawus, da Toma da
Matiyu mai karbar haraji da Yakubu dan Halfa, da
Taddawus; 4 Saminu Bakairawane, da kuma Yahuza
Iskariyoti wanda ya bashe shi. 5 Sha biyun nan su ne
Yesu ya aika, ya yi masu umarni ya ce, ''Kada ku shiga
wajen al'ummai, ko kuma kowane garin Samariyawa.
6 Sai dai ku je wurin batattun tumaki na gidan Isra'ila.
7 Sa'adda kuna tafiya, kuna wa'azi, kuna cewa, 'Mulkin
Sama ya kusato'. 8 Ku warkar da marasa lafiya, ku tada
matattu, ku tsarkake kutare, ku kuma fitar da aljanu.
Kyauta kuka samu ku ma ku bayar kyauta. 9 Kada ku
rike zinariya, ko azurfa, ko tagulla a jakarku. 10 Kada
kuma ku dauki zabira a tafiyarku, ko taguwa biyu, ko
takalma, ko sanda, don ma'aikaci ya cancanci abincin
sa. 11 Kowanne birni, ko kauyen da kuka shiga, ku

nemi mai mutunci a cikinsa, ku kuma zauna a wurin
har lokacin da za ku tashi. 12 In za ku shiga gida ku
ce, salama a gareku. 13 Idan gidan akwai dan salama,
salamarku za ta ta tabbata a gare shi. Idan kuwa babu,
salamarku za ta komo maku. 14 Ga wadanda su ka
ki karbar ku ko sauraron ku, idan za ku fita garin
ko gidan, sai ku karkade kurar kafafunku. 15 Hakika,
ina gaya maku, a ranar shari'a za a fi rangwanta wa
kasar Saduma da ta Gwamrata a kan wannan birni. 16
''Duba, na aike ku kamar tumaki a tsakiyar kyarketai,
don haka sai ku zama masu wayo kamar macizai, da
kuma marasa barna kamar kurciyoyi. 17 Ku yi hankali
da mutane, don za su kai ku gaban majalisa, su kuma
yi maku bulala a majami'unsu. 18 Za su kuma kai ku
gaban mahukunta da sarakuna saboda ni, domin ku
bada shaida a gabansu, da kuma gaban al'ummai. 19
Idan har sun bada ku, kada ku damu da yadda za ku yi
magana, ko kuwa abin da za ku fada, domin za a ba
ku abin da za ku fada a lokacin. 20 Domin ba ku ne
kuke magana ba, Ruhun Ubanku ne yake magana ta
bakinku. 21 Dan'uwa zai ba da dan'uwansa a kashe shi,
uba kuwa dansa. 'Ya'ya kuma za su tayarwa iyayensu,
har su sa a kashe su. 22 Kowa kuma zai ki ku saboda
sunana. Amma duk wanda ya jure har karshe, zai
tsira. 23 In sun tsananta maku a wannan gari, ku
gudu zuwa na gaba. Hakika ina gaya maku, kafin ku
gama zazzaga dukan garuruwan Isra'ila, Dan Mutum
zai zo. 24 Almajiri ba ya fin malaminsa, bawa kuma
ba yafin ubangijinsa. 25 Dai dai ne almajiri ya zama
kamar malaminsa, bawa kuma kamar ubangijinsa. In
har sun kira mai gida Ba'alzabuba, za su kuma bata
mutanen gidansa! 26 Don haka kada kuji tsoron su,
domin ba abin da yake boye da ba za a bayyana ba.
27 Abin da nake fada maku a asirce, ku fada a sarari.
Abin da kuma kuka ji a cikin rada, ku yi shelarsa daga
kan soraye. 28 Kada ku ji tsoron masu kisan jikin
mutum, amma ba sa iya kashe rai. Sai dai ku ji tsoron
wannan da yake da ikon kashe jiki ya kuma jefa rai
cikin jahannama. (Geenna g1067) 29 Ba 'yan tsuntsaye
biyu ake sayarwa akan kobo ba? Ba ko daya a cikin
su da zai fadi kasa ba tare da yardar Ubanku ba. 30
Ai, ko da gashin kan ku ma duk a kidaye yake. 31
Kada ku ji tsoro. Gama darajarku ta fi ta tsuntsaye
masu yawa. 32 ''Saboda haka duk wanda ya shaida
ni a gaban mutane, ni ma zan yi shaidar sa a gaban
Ubana wanda ya ke cikin Sama. 33 Amma duk wanda
ya yi musun sani na a gaban mutane, ni ma zan yi
musun sanin sa a gaban Ubana da yake cikin Sama.''
34 ''Kada ku zaci na zo ne in kawo salama a duniya.
Ban zo domin in kawo salama ba, sai dai takobi. 35
Domin na zo ne in hada mutum da ubansa gaba, 'ya
da uwatarta, mata da kuma surukarta. 36 Zai zama na
kuma magabtan mutum su ne mutanen gidansa. 37
Dukan wanda ya fi son mahaifinsa ko mahaifayarsa
fiye da ni, bai cancanci zama nawa ba. Wanda kuma
ya fi son dansa ko 'yarsa fiye da ni, bai cancanci zama
nawa ba. 38 Wanda kuma bai dauki gicciyensa ya biyo
ni ba, bai cancanci zama nawa ba. 39 Dukan mai son ya
ceci ransa, zai rasa shi. Duk kuwa wanda ya rasa ransa
saboda ni, yana ceton sa ne. 40 ''Wanda ya marabce
ku, ya marabce ni ke nan. 41 Wanda ya marabce ni
kuwa, ya marabci wanda ya aiko ni. Wanda ya marabci
annabi domin shi annabi ne, zai karbi lada kamar na
annabi. Wanda kuma ya marabci mai adalci saboda
shi mai adalci ne, zai sami lada kamar na mai adalci.
42 Kowa ya ba daya daga cikin 'yan kananan nan, ko
da kofin ruwan sanyi ya sha, domin shi almajirina ne,
hakika, Ina gaya maku, ba zai rasa ladarsa ba.''

11 Bayan Yesu ya gama yi wa almajiransa gargadi,
sai ya bar wannan wuri, ya tafi biranensu domin
yayi koyorwa, da wa'azi. 2 Da Yahaya mai baftisma ya
ji daga kurkuku irin ayyukan da Yesu ke yi, sai ya aika
sako ta wurin almajiransa. 3 Ya ce masa. “Kai ne mai
zuwa”? ko mu sa ido ga wani. 4 Yesu ya amsa ya ce
masu, “Ku je ku gaya wa Yahaya abin da ku ka gani
da abin da ku ka ji. 5 Makafi suna samun ganin gari,
guragu na tafiya, ana tsarkake kutare, kurame na jin
magana kuma, ana tada matattu, mabukata kuma
ana ba su bishara. 6 Kuma mai albarka ne wanda
baya tuntube sabili da ni. 7 Bayan wadannan sun tafi,
sai Yesu ya fara wa jama'a jawabi game da Yahaya
mai baftisma, yana cewa, “Me ake zuwa gani a jeji -
ciyawa ce da iska ke busawa? 8 Shin menene kuke
zuwa gani a jeji - mutum mai sanye da tufafi masu
laushi? Hakika, masu sa tufafi masu laushi suna zaune
ne a fadar sarakuna. 9 Amma me ku ke zuwa gani,
annabi? Hakika ina fada maku, fiye ma da annabi. 10
Wannan shine wanda aka rubuta game da shi, 'Duba,
ina aika manzona, wanda za ya ya tafi gabanka domin
ya shirya maka hanya inda za ka bi'. 11 Ina gaya
maku gaskiya, cikin wadanda mata suka haifa, babu
mai girma kamar Yahaya mai baftisma. Amma mafi
kankanta a mulkin sama ya fi shi girma. 12 Tun daga

kwanakin Yahaya mai baftisma zuwa yanzu, mulkin
sama yana shan gwagwarmaya, masu husuma kuma
su kan kwace shi da karfi. 13 Gama dukan annabawa
da shari'a sun yi annabci har zuwa lokacin Yahaya.
14 kuma in zaku karba, wannan shine Iliya wanda
za ya zo. 15 Wanda ke da kunnuwan ji, ya ji. 16 Da
me zan kwatanta wannan zamani? Ya na kamar yara
masu wasa a kasuwa, sun zauna suna kiran juna 17
suna cewa mun busa maku sarewa baku yi rawa ba,
mun yi makoki, baku yi kuka ba. 18 Gama Yahaya
ya zo, baya cin gurasa ko shan ruwan inabi, sai aka
ce, "Yana da aljannu". 19 Dan mutum ya zo yana ci
yana sha, sai aka ce, 'Duba, ga mai hadama, mashayi
kuma, abokin masu karbar haraji da masu zunubi!'
Amma hikima, ta wurin aikin ta ake tabbatar da ita. 20
Sannan Yesu ya fara tsautawa biranen nan inda ya yi
yawancin ayukansa, domin ba su tuba ba. 21 "Kaiton
ki Korasinu, kaiton ki Batsaida! In da an yi irin ayuka
masu ban mamaki a Taya da Sidon! Yadda aka yi a
cikinku, da tuni sun tuba suna sanye da tsumma da
yafa toka. 22 Amma zai zama da sauki a kan Taya da
Sidon a ranar shari'a fiye da ku. 23 Ke kafarnahum,
kina tsammani za a daukaka ki har zuwa sama? A'a za
a saukar da ke kasa zuwa hades. Gama in da an yi irin
al'ajiban da aka yi a cikin ki a Sodom, da tana nan har
yanzu. (Hadēs g86) 24 Amma ina ce maku, za a saukaka
wa Sodom a ranar shari'a fiye da ku." 25 A wannan
lokaci Yesu ya ce, "Ina yabon ka, ya Uba, Ubangijin
sama da kasa, domin ka boye wa masu hikima da
fahimta wadannan abubuwa, ka bayyana wa marasa
sani, kamar kananan yara. 26 I, ya Uba gama wannan
shine ya yi daidai a gare ka. 27 An mallaka mani dukan
abu daga wurin Ubana. Sannan babu wanda ya san
Dan, sai Uban, babu kuma wanda ya san Uban, sai
Dan, da duk wanda ya so ya bayyana masa. 28 Ku zo
gare ni, dukanku masu wahala da fama da nauyin
kaya, ni kuma zan ba ku hutawa. 29 Ku dauki karkiya
ta ku koya daga gare ni, gama ni mai tawali'u ne da
saukin hali a zuciya, sannan zaku sami hutawa ga
rayukanku. 30 Gama karkiyata mai sauki ce, kaya na
kuma ba shi da nauyi."

12 A wannan lokaci, Yesu ya tafi a ranar Asabaci, ya
bi cikin gonar hatsi. Almajiransa na jin yunwa,
sai suka fara zagar hatsi suna ci. 2 Amma da Farisawa
suka gan su, sai su ka ce wa Yesu. "Duba, almajiranka
su na yin abin da doka ta haramta a ranar Asabaci." 3
Amma Yesu ya ce masu, "Baku karanta abin da Dauda
ya yi ba, lokacin da ya ke jin yunwa, tare da mazan
da ke tare da shi? 4 Yadda ya shiga gidan Allah, ya
ci gurasar alfarwa da doka ta hana shi ko mazan da
ke tare da shi su ci, sai dai Firistoci ne kawai doka
ta basu damar ci? 5 Sa'annan ba ku karanta cikin
shari'a cewa, a ranar Asabaci, Firistoci da ke cikin
haikali na sabawa ranar Asabaci, amma kamar ba su
yi laifi ba? 6 Amma ina tabbatar maku da cewa, wani
wanda ya fi haikali girma yana nan. 7 In da kun san
ma'anar wannan 'Na fi son jinkai fiye da hadaya,' da
baku shari'anta wa marar laifi ba. 8 Gama Dan mutum
shine Ubangijin Asabaci." 9 Sa'annan Yesu ya bar
wannan wuri, ya shiga majami'ar su. 10 Sai ga wani
mutum wanda hannun sa ya shanye, sai Farisawa suka
tambayi Yesu, cewa, "Doka ta halarta a yi warkarwa a
ranar Asabaci?" Domin su zarge shi a kan zunubi. 11
Yesu ya ce masu, "Wanene a cikin ku, wanda idan
ya na da tunkiya guda, sa'annan tunkiyar nan ta
fada a rami mai zurfi a ranar Asabaci ba zai kamo
ta ya fitar da ita ba? 12 Yaya za a kwatanta darajar
mutum da tunkiya! Saboda haka ya halarta a yi alheri
ranar Asabaci." 13 Sai Yesu ya ce wa mutumin nan
"Mika hannun ka." Ya mike hannunsa, sai hannun nan
ya dawo lafiyaye kamar dayan hannunsa. 14 Amma
Farisawa su ka fita waje su ka fara mugun shiri domin
sa. Su na neman hanyar da za su kashe shi. 15 Da
Yesu ya fahimci wannan, sai ya janye kan sa daga nan.
Mutane da dama su ka bi shi, ya warkar da su duka.
16 Ya dokace su da kada su bayyana shi ga kowa, 17
domin ya zama gaskiyar abin da aka fada ta wurin
annabi Ishaya, cewa, 18 "Dubi, bawa na zababbe;
kaunatacce na, wanda ya ke faranta mani raina sosai.
Zan sa Ruhu na bisan sa, za ya furta hukunci zuwa
al'ummai. 19 Ba za ya yi jayayya ko tada murya ba,
babu wanda za ya ji muryar sa a karabku. 20 Ba zai
karya kara da ya tankwashe ba; ba zai kashe fitilar da
ta kusa mutuwa ba; sai ya kawo hukunci ga nasara.
21 Sa'annan al'ummai za su dogara a ga sunansa. 22
Sa'annan wani mutum, makaho ne, kurma kuma,
aljannu kuma na cikinsa, an kawo shi wurin Yesu. Ya
warkar da shi, ya sami ganin gari ya kuma yi magana.
23 Jama'a su ka yi mamaki kwarai, su na cewa, "Ko
wannan ne Dan Dawuda?" 24 Amma da Farisawa su
ka ji wannan al'ajibi, sai su ka ce, "Mutumin nan
yana fitar da aljannu ta wurin Bahalzabuba sarkin
aljannu ne." 25 Amma Yesu ya san tunanin su, sai ya

ce. “Duk mulkin da ya rabu gaba da kan sa, ba zaya
tsaya ba, duk wani birni da ya rabu ba zai tsaya ba,
ko gida da ya tsage, za ya rushe. 26 Idan Shaidan ya
fitar da Shaidan, ya rabu gaba da kansa. Yaya mulkin
sa za ya tsaya? 27 Idan Ina fitar da aljannu da ikon
Ba'alzabuba, ta wurin wa masu bin ku su ke fitar da
su? Saboda haka, su za su shari'anta ku. 28 Amma
idan ina fitar da aljannu da Ruhun Allah ne, hakika
mulkin Allah ya zo gare ku. 29 Kuma ta yaya mutum
za ya shiga gidan mai karfi ya kwashe masa kaya
ba tare da ya fara daure shi ba? Sa'annan ne za ya
iya satar masa kaya daga gidansa. 30 Wanda baya
tare da ni yana gaba da ni ke nan, wanda kuma baya
tarawa tare da ni, yana watsarwa ne. 31 Saboda haka
ina ce maku, kowanne zunubi da sabo, za a gafarta
wa mutum, amma sabon Ruhu Mai Tsarki, ba za a
gafarta shi ba. 32 Duk wanda yayi batanci ga Dan
Mutum, za a gafarta masa. Amma duk wanda yayi
batanci game da Ruhu Mai Tsarki ba za a gafarta masa
ba, a nan duniya da har abada. (aiōn g165) 33 Ko dai a
mai da itace mai kyau 'ya'yansa kuma su yi kyau, ko
a mai da itace marar kyau 'ya'yansa kuma marasa
kyau, gama ana sanin itace ta wurin 'ya'yansa. 34 Ku
'ya'yan macizai, tun da ku miyagu ne, yaya za ku iya
fadin abubuwa nagari? Gama daga cikar zuciya baki
ke magana. 35 Mutumin kirki daga ajiyar zuciyarsa
ya kan fitar da abubuwa masu kyau, mugun mutum
kuma daga mummunar ajiyar zuciyarsa ya kan fitar
da abubuwan mugunta. 36 Sa'annan ina ce maku a
ranar shari'a, mutane za su bada lissafin abubuwan
banza da su ka fadi. 37 Gama ta wurin maganganun
ku, za a 'yantar da ku, ta wurin maganganun ku
kuma za a kashe ku.” 38 Sa'annan wadansu Malaman
Attaura, da Farisawa suka amsa suka ce wa Yesu,
“Mallam, muna so mu ga wata alama daga gare ka.”
39 Amma Yesu ya amsa ya ce masu, “Mugun zamani da
mazinaciyar tsara, su na bukutar alama. Amma babu
alamar da za a ba su, sai dai alamar annabi Yunusa. 40
Gama yadda Yunusa ya yi kwana uku da dare uku a
cikin babban kifi, haka ma Dan Mutum zaya yi kwana
uku da dare uku a cikin zuciyar kasa. 41 Mutanen
Nineba za su tsaya a ranar shari'a da wannan zamani
sannan su kashe su. Domin sun tuba da suka ji wa'azin
Yunusa, amma duba wanda ya fi Yunusa yana nan.
42 Sarauniyar Kudu za ta tashi da mutanen wannan
zamani ta kuma kashe su. Ta zo daga karshen duniya
domin ta ji hikimar Sulaimanu, kuma duba, wanda
ya fi Sulaimanu yana nan. 43 Idan kazamin ruhu ya
rabu da mutum, ya kan wuce ya nemi wuraren da
ruwa yake domin ya huta, amma bai samu ba. 44
Sai ya ce, 'zan koma gidana inda na fito'. Bayan ya
dawo, sai ya tarar da gidan nan an share shi ya zama
da tsabta. 45 Sai ya koma ya kawo wadansu ruhohi
guda bakwai, wadanda su ka fi shi mugunta, sa'annan
dukan su su zo su zauna a nan. Sa'annan yanayin
mutumin nan na karshe ya fi na farko muni. Haka
zaya kasance ga wannan mugun zamani. 46 Sa'adda
Yesu ya ke yi wa Jama'a jawabi, sai mahaifiyarsa da
'yan'uwansa su ka zo su ka tsaya a waje, suna neman
su yi magana da shi. 47 Sai wani ya ce masa, “Duba,
mahaifiyarka da 'yan'uwanka suna tsaye a waje, suna
so su yi magana da kai”. 48 Amma Yesu ya amsa ya ce
wa shi wanda ya gaya masa, “Wacece mahaifiyata?
Kuma su wanene 'yan'uwana?” 49 Sai ya mika hannu
ya nuna almajiransa ya ce, “Duba, ga mahaifiyata da
'yan'uwana! 50 Gama duk wanda yake aikata nufin
Ubana wanda ya ke cikin sama, shine dan'uwana, da
'yar'uwata da mahaifiyata.”

13 A waccan rana Yesu ya fito daga gida ya zauna
a gefen teku. 2 Taro mai yawan gaske kuwa suka
kewaye shi, sai ya shiga cikin kwalekwale ya zauna.
Dukan taron kuwa na tsaye a bakin tekun. 3 Sai Yesu
ya fada masu abubuwa da yawa cikin misalai. Ya ce,
“Wani mai shuka, ya tafi yayi shuka. 4 Da yayi shukar,
wadansu irin suka fadi a kan hanya, sai tsunsaye suka
zo suka cinye su. 5 Wadansu irin kuwa suka fadi a kan
duwatsu, wurin da babu kasa. Nan da nan sai suka
tsira, domin kasar babu zurfi. 6 Amma da rana ta
taso, sai suka yankwane domin ba su yi saiwa ba, suka
kuwa bushe suka zube. 7 Wasu irin kuwa suka fada a
cikin kayayuwa. Kayayuwan kuwa suka shake su. 8
Wasu irin kuwa suka fada a wuri mai kyau suka ba
da tsaba, wani ya ba da dari, wasu sitin, wasu kuma
talatin. 9 Duk mai kunnen ji, bari ya ji. 10 Almajiran
suka zo suka ce ma Yesu, “Don me ka ke yi wa taron
magana da misali?” 11 Yesu ya amsa ya ce masu, “An
baku 'yanci ku fahimci asiran mulkin sama, amma
gare su ba a bayar ba. 12 Domin wanda yake da shi, za
a kara masa, zai kuma samu dayawan gaske. Amma
duk wanda ba shi da shi, sai a dauke har ma abin da
yake dashi. 13 Saboda haka na yi masu magana cikin
misalai, amma ko da ya ke sun gani, duk da haka ba
su gani ba. Kuma ko da yake sun ji, hakika ba su ji

ba, balle ma su fahimta. 14 A gare su ne annabcin
Ishaya ya cika, wanda yake cewa, “Game da sauraro
zaku saurara, amma ba za ku fahimta ba. Game da
gani kuma za ku kalla, amma ba za ku gane ba. 15
Domin zuciyar mutanen nan ta duhunta, sun taurare
ga saurare, kuma sun rufe idanunsu domin kada su
gani da idanunsu, ko kuwa su ji da kunnuwansu, ko
kuwa su fahimta da zukatansu, saboda su juyo kuma
in warkar da su'. 16 Amma idanunku masu albarka ne,
domin sun gani, haka ma kunnuwanku, domin sun
ji. 17 Hakika ina gaya muku, annabawa da mutane
dayawa masu aldalci sun yi marmarin ganin abin
da kuka gani, amma ba su sami ganin su ba. Sun yi
marmarin jin abin da kuka ji, ba su kuwa ji su ba. 18
Ku saurari misalin nan na mai shuka. 19 Idan wani
ya ji maganar mulkin sama amma bai fahimce ta
ba, sai mugun nan ya zo ya kwace abinda aka shuka
a zuciyarsa. Wannan shine irin da aka shuka a kan
hanya. 20 Shi wanda aka shuka akan duwatsu, shine
wanda ya ji maganar ya kuma karbe ta da murna nan
da nan. 21 Duk da haka, bai yi karfi cikin ta ba kuma
nan ba da dadaiwa ba. Da wahala da tsanani suka taso
saboda maganar, sai ya yi tuntube nan da nan. 22 Shi
wanda aka shuka a cikin kayayuwa wannan shine
wanda ya ji maganar, amma dawainiyar duniya da
kuma yaudarar dukiya suka shake maganar, sai ya
kasa ba da 'ya'ya. (aiōn g165) 23 Shi wanda aka shuka a
kasa mai kyau, wannan shine wanda ya ji maganar, ya
kuma fahimce ta. Wannan shine wanda ba da 'ya'ya
da gaske; wadansu ribi dari, wadansu sittin, wasu
kuma talatin.” 24 Yesu ya sake ba su wani misali, yana
cewa “Za a kwatanta mulkin sama da wani mutum
wanda ya shuka iri mai kyau a gona. 25 Amma da
mutane suka yi barci, magabcin sa ya zo ya shuka
ciyayi a cikin alkamar, ya kuwa yi tafiyarsa. 26 Sa'adda
suka yi toho suka kuma ba da tsaba, sai ciyayin suka
bayyana. 27 Bayin mai gonar kuwa suka zo suka
ce masa, maigida, ashe ba iri mai kyau ka shuka a
gonarka ba? ya ya aka yi ta kasance da ciyayi? 28 Ya
ce masu, “Magabci ne ya yi wannan”. Sai bayin suka
ce masa, 'kana so mu je mu tuge su ne?' 29 Mai gonar
ya ce, 'A'a, kada a garin tuge ciyayin, ku tuge tare da
alkamar. 30 Bari dukan su su girma tare har lokacin
girbi, a lokacin girbin zan gaya wa masu girbin, “Ku
tuge ciyayin da farko a daura su dami dami sai a kona
su, amma a tara alkamar a kai rumbunana.'” 31 Sai
Yesu ya sake yin magana da su cikin misalai, yana
cewa “Za a kwatanta mulkin sama da kwayar mustad,
wanda wani mutum ya shuka a lambunsa. 32 Wannan
iri shine mafi kankanta cikin dukan iri. Amma bayan
ya yi girma, sai ya fi dukan ganyaye dake lambun.
Ya zama itace, har ma tsuntsayen sama su yi sheka
a rassansa.” 33 Yesu ya sake fada masu wani misali.
“Za a kwatanta mulkin sama da yisti da mace takan
dauka ta kwaba gari da shi mudu uku har sai ya yi
kumburi.” 34 Duk wadannan abubuwa Yesu ya fada
wa taron cikin misalai. Babu abinda ya fada masu da
ba a cikin misali ba. 35 Wannan ya kasance ne domin
abinda annabin ya fada ya zama gaskiya, da ya ce,
“Zan buda bakina da misali. In fadi abubuwan da ke
boye tun daga halittar duniya.” 36 Sai Yesu ya bar
taron ya shiga cikin gida. Amajiransa suka zo wurin sa
suka ce, “Ka fasarta mana misalan nan a kan ciyayin
da ke gonar” 37 Yesu ya amsa kuma ya ce, “Shi wanda
ya shuka iri mai kyau Dan Mutum ne. 38 Gonar kuwa
duniya ce; iri mai kyau kuma sune 'ya'yan mulkin.
Ciyayin kuma sune 'ya'yan mugun, 39 magabcin da
ya shuka su kuma shaidan ne. Girbin shine karshen
duniya, kuma masu girbin sune mala'iku. (aiōn g165)
40 Saboda haka, kamar yadda aka tara ciyayin aka
kona su da wuta, haka ma zai faru a karshen duniya.
(aiōn g165) 41 Dan Mutum zai aiki mala'ikunsa, kuma
su tara dukan abubuwan da ke sa zunubi daga cikin
mulkinsa, da kuma wadanda su ka yi aikin mugunta.
42 Za su jefa su cikin korama ta wuta, inda za a yi kuka
da cizon hakora. 43 Sa'an nan ne mutane masu adalci
za su haskaka kamar rana a mulkin Ubansu. Bari mai
kunnen ji, ya ji. 44 Mulkin sama kamar dukiya ce da
ke boye a gona. Mutum ya samu sai ya boye ta, ya
tafi cikin murna, ya sayar da mallakarsa kuma ya
sayi filin. 45 Haka ma za a kwatanta mulkin sama
da wani attajiri mai neman Lu'ulu'ai masu daraja.
46 Da ya sami lu'ulu'u daya mai darajar gaske, ya je
ya sayar da dukan mallakarsa ya kuma saye shi. 47
Haka kuma, za a kwatanta mulkin sama da taru da
aka jefa cikin teku, ya kuwa tara hallitu iri-iri. 48 Da
ya cika, sai masuntan suka jawo shi bakin tekun. Sai
suka zauna suka tara kyawawan abubuwan a taska,
amma munanan abubuwan, suka watsar da su. 49
Haka zai kasance a karshen duniya. Mala'iku za su zo
su ware miyagu daga cikin masu adalci. (aiōn g165) 50
Za su jefa su cikin korama ta wuta, inda za a yi kuka
da cizon hakora. 51 Kun fahimci dukan wadannan
abubuwa? Amajiran suka ce da shi, “I”. 52 Sai Yesu ya

ce masu, “Saboda haka kowane malamin attaura da
ya zama almajirin mulkin sama, yana kamar mutum
mai gida wanda ya zaro tsoho da sobon abu daga
taskarsa.” 53 Daga nan, sa'adda Yesu ya kammala
ba da wadanan misalai, sai ya tafi ya bar wurin. 54
Sai Yesu ya shiga yankinsa ya koyar da mutane a
masujadarsu. Saboda haka suka yi mamaki suna cewa,
“Daga ina wannan mutumin ya sami hikimarsa da
al'ajibai? 55 Wannan mutumin ba dan masassakin nan
ba ne? Ba kuma sunan mahaifiyarsa Maryamu ba?
Ba Kuma 'yan'uwansa sune, Yakubu da Yusufu da
Saminu da kuma Yahuza ba? 56 Ba 'yan'uwansa mata
na tare da mu ba? To daga ina wannan mutumin ya
sami dukan wadannnan abubuwa? 57 Suka bata rai
saboda shi. Amma Yesu ya ce masu, “Ai annabi bai
rasa daraja sai dai ko a garinsa da kuma cikin iyalinsa.
58 Kuma bai yi al'ajibai dayawa a can ba saboda rashin
bangaskiyarsu.

14 A lokacin nan ne, Hiridus mai mulki ya ji labarin
Yesu. 2 Ya ce wa barorinsa, “Wannan Yahaya
mai baftisma ne; ya tashi daga matattu. Saboda haka
wadannan ikoki na aiki a cikinsa”. 3 Domin Hiridus ya
kama Yahaya, ya daure shi, kuma ya jefa shi a kurkuku
saboda Hirudiya, matar dan'uwansa Filibus. 4 Ya ce
masa, “Bai kamata ka dauke ta a matsayin matarka
ba.” 5 Da Hirudus ya kashe shi, amma yana tsoron
jama'a, domin sun dauke shi a matsayin annabi. 6
Amma da ranar bikin haihuwar Hirudus ta kewayo,
diyar Hirudiya tayi rawa a lokacin har ta burge
Hirudus. 7 Sai ya yi mata alkawari har da rantsuwa
cewa ta roki komenene ta ke so, zai ba ta. 8 Bayan ta
amshi umurni daga wurin mahaifiyarta, ta ce, “Ka
bani kan Yahaya mai baptisma a kan tire. 9 Sarki ya
husata da rokonta, amma domin rantsuwar da ya yi
kuma domin mutanen da ke a wurin bukin tare da
shi, sai ya umurta a yi haka. 10 Ya aika aka yanke kan
Yahaya acikin kurkuku. 11 Sai aka kawo kansa bisa tire,
aka mika wa yarinyar, ta kuwa kai wa mahaifiyarta. 12
Sai almajiransa suka zo, su ka dauki gawar su ka je
su ka yi jana'iza. Bayan haka, su ka je su ka fada wa
Yesu. 13 Sa'adda da Yesu ya ji haka, ya fita daga cikin
kwale-kwale zuwa wani kebabben wuri. Da taron suka
ji haka, suka bi shi da kafa daga biranen. 14 Sai Yesu
ya zo gabansu, ya kuma ga babban taron. Ya tausaya
masu ya kuwa warkar da marasa lafiya dake cikinsu.
15 Da maraice ya yi, almajiransa su ka zo su ka ce
masa, “Wannan wuri jeji ne, dare kuwa ya riga ya yi.
Ka sallami taron domin su je cikin kauyukan nan, su
sayo wa kansu abinci.” 16 Amma Yesu ya ce masu,
“Babu amfanin tafiyar su, ku basu abin da za su ci.” 17
Suka ce masa, “Muna da gurasa guda biyar da kifi biyu
ne kawai.” 18 Yesu ya ce, “Ku kawo mani su.” 19 Sai
Yesu ya umarci taron su zauna akan ciyawa. Ya dauki
gurasa biyar da kifi biyun. Ya dubi sama, ya sa albarka
ya gutsuttsura ya kuma ba almajiran. Almajiran suka
ba taron. 20 Dukansu suka ci suka koshi. Sai suka
dauki gutsattsarin gurasa da kifin, kwanduna goma
sha biyu cike. 21 Wadanda su ka ci kuwa kimanin
maza dubu biyar ne, ban da mata da yara. 22 Nan take
sai ya sa almajiran suka shiga kwale-kwalen su haye
zuwa dayan gefen kafin shi, domin ya sallami taron.
23 Bayan ya sallami taron sun tafi, sai ya haura kan
dutse domin yayi addu'a. Da dare yayi, yana can shi
kadai. 24 Amma yanzu fa kwale-kwalen na tsakiyar
tekun, kuma da wuyar sarrafawa saboda rakuman
ruwa da iska na gaba da su. 25 Da asuba (wajen karfe
uku na dare) Yesu ya nufo su yana tafiya akan teku. 26
Da almajiran suka ganshi yana tafiya akan tekun, sai
suka firgita suna cewa, “Fatalwa ce,” suka yi kururuwa
cikin tsoro. 27 Amma Yesu yayi magana da su nan da
nan yace, “Ku yi karfin hali! Ni ne! Kada ku ji tsoro.”
28 Bitrus ya amsa masa cewa, “Ubangiji, idan kai ne,
ka umarce ni in zo wurin ka bisa ruwan.” 29 Yesu
yace, “Zo” Sai Bitrus ya fita daga jirgin yana tafiya
akan ruwan zuwa wurin Yesu. 30 Amma da Bitrus ya
ga iska, sai ya tsorata. Yayin da ya fara nutsewa, sai ya
tada murya ya ce, “Ubangiji, ka cece ni!” 31 Nan take
Yesu ya mika hannunsa, ya kama Bitrus ya ce masa,
“Kai mai karancin bangaskiya, meyasa ka yi shakka?”
32 Bayan da Yesu da Bitrus suka shiga cikin kwale-
kwalen, sai iska ta daina kadawa. 33 Sai almajiran
dake cikin kwale-kwalen su ka yi wa Yesu sujada suna
cewa, “Hakika kai Dan Allah ne.” 34 Da suka haye, sun
iso kasar Janisarata. 35 Da mutanen wurin suka gane
Yesu, sai suka aika da sako zuwa dukan yankin, kuma
suka kawo masa dukan marasa lafiya. 36 Suka roke shi
don su taba gezar rigarsa, kuma dukan wadanda suka
taba shi sun warke.

15 Sai wadansu Farisawa da malamai suka zo wurin
Yesu daga Urushalima. Su ka ce, 2 “Meyasa
almajiranka suke karya al'adar dattawa? Don ba su
wanke hannayen su kafin su ci abinci.” 3 Yesu ya
amsa masu ya ce, “Kuma don me ku ke karya dokar

Allah saboda al'adunku? 4 Domin Allah ya ce, 'Ka
girmama mahaifinka da mahaifiyarka; 'Shi wanda ya
yi muguwar magana ga mahaifinsa ko mahaifiyarsa,
lallai zai mutu. 5 Amma kun ce, “Duk wanda ya ce
wa mahaifinsa ko mahaifiyarsa, “Kowanne taimako
da za ka samu daga gare ni yanzu baiko ne ga
Allah,'” 6 wannan mutum ba ya bukatar ya girmama
mahaifinsa. Ta wannan hanya kun maida maganar
Allah wofi saboda al'adunku. 7 Ku munafukai, daidai
ne Ishaya ya yi annabci akan ku da ya ce, 8 “Wadannan
mutane girmama ni da baki kawai suke yi, amma
zukatansu nesa suke da ni. 9 Suna mani sujada a banza,
domin suna koyar da dokokin mutane a matsayin
rukunansu.” 10 Sai ya kira taron mutane zuwa gare
shi ya ce masu, “Ku saurara ku fahimta, 11 ba abin da
ke shiga baki ke kazantar da mutum ba. Sai dai, abin
da ke fitowa daga baki, wannan shi ya ke kazantar
da mutum.” 12 Sai al'majiran suka zo suka ce masa,
“Ka san Farisawa ba su ji dadi ba da suka ji maganan
nan?” 13 Yesu ya amsa ya ce, “Kowace shuka wadda ba
Ubana na sama ya shuka ba za a tuge ta. 14 Ku kyale su
kawai, su makafin jagora ne. In makaho ya ja wa wani
makaho gora dukan su za su fada rami.” 15 Bitrus ya
amsa ya ce wa Yesu, “Ka bayyana wannan misali a
garemu,” 16 Yesu ya ce, “Ku ma har yanzu ba ku da
fahimta? 17 Ko baku gani ba duk abin da ke shiga
baki zuwa ciki ta haka yake fita zuwa salga? 18 Amma
abubuwan da ke fita daga baki suna fitowa ne daga
zuciya. Su ne abubuwan da ke kazantar da mutum. 19
Domin daga zuciya mugayen tunani suke fitowa, kisan
kai, zina, fasikanci, sata, shaidar zur, da zage-zage. 20
Wadannan su ne abubuwan da ke kazantar da mutum.
Amma ci da rashin wanke hannu baya kazantar da
mutum.” 21 Sai Yesu ya tafi daga nan ya nufi yankin
biranen Taya da Sidon. 22 Sai wata mace Bakan'aniya
ta zo daga wannan yanki. Ta daga murya ta ce,” Ka
yi mani jinkai, Ubangiji, Dan Dauda; 'yata tana cikin
bakar azaba da aljani.” 23 Amma Yesu bai ce mata
kome ba. Almajiransa suka zo suka roke shi, suna
cewa, “Ka sallame ta, domin tana bin mu da ihu.” 24
Amma Yesu ya amsa ya ce, “Ba a aike ni gun kowa ba
sai dai ga batattun tumakin gidan Isra'ila.” 25 Amma
ta zo ta durkusa a gabansa, tana cewa, “Ubangiji ka
taimake ni.” 26 Ya amsa ya ce, “Ba daidai bane a dauki
gurasar yara a jefa wa kananan karnuka. 27 Ta ce,
“I, Ubangiji, amma ko kananan karnuka suna cin
barbashin da ke fadowa daga teburin maigida.” 28 Sai
Yesu ya amsa ya ce mata, “Mace, bangaskiyarki tana
da girma. Bari ya zamar maki yadda ki ke so.”'Yarta ta
warke a lokacin. 29 Yesu ya bar wurin ya tafi kusa da
tekun Galili. Sai ya hau tudu ya zauna a can. 30 Taro
mai yawa suka zo gunsa. Suka kawo masa guragu,
makafi, bebaye da nakasassun mutane da yawa, da
wadansu marasa lafiya. Suka kawo su gaban Yesu,
sai ya warkar da su. 31 Don haka mutane da yawa
suka yi mamaki a lokacin da suka ga bebaye suna
magana, nakasassu sun warke, guragu suna tafiya,
makafi suna gani. Sai suka daukaka Allah na Isra'ila.
32 Yesu ya kira almajiransa zuwa gun sa sai ya ce, “Ina
jin tausayin taron, sun kasance tare da ni kwana uku
ke nan kuma ba su da abin da za su ci. Bana so in
sallame su ba tare da sun ci abinci ba, domin kada
su suma a hanya.” 33 Almajiran suka ce masa, “A ina
zamu sami isasshiyar gurasa a wannan wuri da babu
kowa har ta ishi babban taron nan.” 34 Yesu ya ce
masu, “Gurasa nawa ku ke da ita?” Suka ce, “Bakwai
da 'yan kifi marasa yawa.” 35 Sai Yesu ya umarci taron
su zauna a kasa. 36 Ya dauki gurasar nan bakwai da
kifin, bayan ya yi godiya, ya kakkarya gurasar ya bada
ita ga almajiran Sai almajiran suka ba taron. 37 Jama'a
duka suka ci suka koshi. Suka tattara gutsattsarin
abincin da ya rage, kwando bakwai cike. 38 Wadanda
suka ci su dubu hudu ne maza, banda mata da yara.
39 Sai Yesu ya sallami taron ya shiga cikin jirgin ruwa
ya tafi yankin Magadan.

**16** Sai Farisawa da Sadukiyawa suka zo su gwada shi
suka roke shi ya nuna masu alama daga sama. 2
Amma ya amsa ya ce masu, “Lokacin da yamma ta yi,
sai ku ce, 'Za a yi yanayi mai kyau, domin sama ta yi
ja,' 3 Kuma da safe ku ce, 'Zai zama yanayi mara kyau
a yau, domin sama ta yi ja ta kuma gama gari, kun
san yadda za ku bayyana kammanin sararin sama,
amma ba ku iya bayyana alamun lokaci ba. 4 Mugun
zamani, maciya amana suna neman alama, amma
babu wata alama da za a nuna sai ta Yunusa.” Daga
nan sai Yesu ya tafi. 5 Almajiran suka zo daga wancan
gefe, amma sun manta su dauki gurasa, 6 Yesu ya
ce masu, “Ku kula ku kuma mai da hankali da yisti
na Farisawa da Sadukiyawa.” 7 Sai almajiran suka
fara magana da junansu suka ce, “Ko saboda bamu
kawo gurasa bane.” 8 Yesu yana sane da wannan sai
ya ce, “Ku masu karancin bangaskiya, don me ku ke
magana a tsakaninku cewa ko don bamu kawo gurasa
bane? 9 Ba ku gane ko tuna da gurasa guda biyar da

aka ciyar da mutum dubu biyar, kuma kwando nawa
kuka tara ba? 10 Ko gurasa bakwai ga mutum dubu
hudu, da kuma kwanduna nawa kuka dauka ba? 11
Yaya kuka kasa fahimta cewa ba game da gurasa nake
yi maku magana ba? Ku yi hankali ku kuma lura da
yistin Farisawa da Sadukiyawa." 12 Sa'annan suka
fahimta cewa ba yana gaya masu su yi hankali da
yistin da ke cikin gurasa ba ne, amma sai dai su yi lura
da koyarwar Farisawa da Sadukiyawa. 13 A lokacin
da Yesu ya zo yankin Kaisariya Filibbi, ya tambayi
almajiransa, cewa, "Wa mutane ke cewa Dan Mutum
yake? 14 Suka ce, "Wadansu suna cewa Yahaya mai
baftisma; wadansu Iliya, saura suna cewa Irmiya, ko
daya daga cikin annabawa." 15 Ya ce masu, "Amma ku
wa kuke ce da ni?" 16 Sai Saminu Bitrus ya amsa ya ce,
"Kai ne Almasihu, Dan Allah mai rai." 17 Yesu ya amsa
ya ce masa, "Mai albarka ne kai, Saminu dan Yunusa,
don ba nama da jini ba ne ya bayyana maka wannan,
amma Ubana wanda ke cikin sama. 18 Ina kuma gaya
maka cewa kai ne Bitrus, a kan wannan dutse zan
gina ikilisiya ta. Kofofin hades ba za su yi nasara da
ita ba. (Hadēs g86) 19 Zan ba ka mabudan mulkin sama.
Duk abin da ka kulla a duniya zai zama abin da an
kulla a cikin sama, kuma duk abinda ka warware a
duniya a warware yake cikin sama," 20 Sai Yesu ya
umarci almajiransa kada su gaya wa kowa cewa shi
ne Almasihu. 21 Daga lokacin nan Yesu ya fara gaya
wa almajiransa cewa dole ne ya tafi Urushalima, ya
sha wahala mai yawa a hannun dattawa, da manyan
firistoci da malaman attaura, a kashe shi, a tashe shi
zuwa rai a rana ta uku. 22 Sai Bitrus ya kai shi a gefe
ya tsauta masa, cewa, "Wannan ya yi nesa da kai,
Ubangiji; wannan ba zai taba faruwa da kai ba." 23
Amma Yesu ya juya ya ce wa Bitrus, "Ka koma bayana,
Shaidan! Kai sanadin tuntube ne gare ni, domin ba
ka damuwa da abubuwan da suke na Allah, amma
sai abubuwan mutane." 24 Sa'annan Yesu ya ce wa
almajiransa, "Duk wanda yake so ya bi ni, lallai ne ya
ki kansa, ya dauki gicciyensa, ya bi ni. 25 Domin duk
wanda yake so ya ceci ransa zai rasa shi. Duk wanda
ya rasa ransa domina zai same shi. 26 Domin wace
riba mutum zai samu in ya sami dukan duniya ya rasa
ransa? Me mutum zai iya bayarwa a maimakon ransa?
27 Domin Dan Mutum zai zo ne cikin daukakar Ubansa
tare da mala'ikunsa. Sa'annan ne zaya biya kowane
mutum bisa ga ayyukansa. 28 Gaskiya ina gaya maku,
akwai wadansun ku da ke tsaye a nan, da ba za su
dandana mutuwa ba sai sun ga Dan Mutum na zuwa
cikin mulkinsa."

17 Bayan kwana shida Yesu ya dauki Bitrus da
Yakubu, da Yahaya dan'uwansa, ya kai su kan
wani dutse mai tsawo su kadai. 2 Kamanninsa ya
canja a gabansu. Fuskarsa ta haskaka kamar rana,
kuma rigunansa suka yi kyalli fal. 3 Sai ga Musa
da Iliya sun bayyana garesu suna magana da shi. 4
Bitrus ya amsa ya ce wa Yesu, "Ubangiji, ya yi kyau
da muke a wurin nan. In kana so, zan yi bukkoki
uku daya dominka, daya domin Musa, daya domin
Iliya." 5 Sa'adda yake cikin magana, sai, girgije mai
haske ya rufe su, sai murya daga girgijen, tana cewa,
"Wannan kaunattacen Dana ne, shi ne wanda yake
faranta mani zuciya. Ku saurare shi." 6 Da almajiran
suka ji haka, suka fadi da fuskokinsu a kasa, saboda
sun tsorata. 7 Sai Yesu ya zo ya taba su ya ce, "Ku
tashi, kada ku ji tsoro." 8 Amma da suka daga kai
ba su ga kowa ba sai Yesu kadai. 9 Yayin da suke
saukowa daga dutsen, Yesu ya umarce su, ya ce, "Kada
ku fadawa kowa wannan wahayin, sai Dan Mutum ya
tashi daga matattu." 10 Almajiransa suka tambaye shi,
suka ce, "Don me marubuta ke cewa lallai ne Iliya ya
fara zuwa?" 11 Yesu ya amsa ya ce, "Hakika, Iliya zai
zo ya maido da dukan abubuwa. 12 Amma ina gaya
maku, Iliya ya riga ya zo, amma ba su gane shi ba. A
maimakon haka, suka yi masa abin da suka ga dama.
Ta irin wanan hanya, Dan Mutum kuma zai sha wuya
a hannunsu. 13 Sa'annan almajiransa suka fahimci
cewa yana yi masu magana a kan Yahaya mai Baftisma
ne. 14 Da suka iso wurin taron, wani mutum ya zo
gunsa, ya durkusa a gaban sa, ya ce, 15 "Ubangiji, ka ji
tausayin yarona, domin yana da farfadiya, kuma yana
shan wuya kwarai, domin sau da yawa yana fadawa
cikin wuta ko ruwa. 16 Na kawo shi wurin almajiran
ka, amma ba su iya su warkar da shi ba." 17 Yesu
ya amsa ya ce, "Marasa bangaskiya da karkataccen
zamani, har yaushe zan kasance tare da ku? Har
yaushe zan jure da ku? Ku kawo shi nan a wurina." 18
Yesu ya tsauta masa, sai aljanin ya fita daga cikinsa.
Yaron ya warke nan take. 19 Sai almajiran suka zo
wurin Yesu a asirce suka ce, "Me ya sa muka kasa
fitar da shi?" 20 Yesu ya ce masu, "Saboda karancin
bangaskiyarku. Domin hakika, ina gaya maku, in kuna
da bangaskiya ko da kamar kwayar mastad, za ku ce
wa wannan dutse, 'Matsa daga nan ka koma can,' zai

kuwa matsa kuma ba abin da zai gagare ku. 21 [Irin
wannan aljanin bashi fita sai tare da addu'a da azumi].
22 Suna zaune a Galili, Yesu ya ce wa almajiransa, “Za
a bada Dan Mutum ga hannun mutane. 23 Kuma za su
kashe shi, a rana ta uku zai tashi.” Sai almajiransa
suka yi bakin ciki kwarai. 24 Da suka iso Kafarnahum,
mutane masu karbar haraji na rabin shekel suka zo
wurin Bitrus suka ce, “Malaminku na ba da rabin
shekel na haraji?” 25 Sai ya ce, “I.” Amma da Bitrus ya
shiga cikin gida, Yesu ya fara magana da shi yace,
“Menene tunaninka Saminu? Sarakunan duniya, daga
wurin wa suke karbar haraji ko kudin fito? Daga
talakawansu ko daga wurin baki?” 26 Sai Bitrus ya ce,
“Daga wurin baki,” Yesu ya ce masa, “Wato an dauke
wa talakawansu biya kenan. 27 Amma don kada mu sa
masu karbar harajin su yi zunubi, ka je teku, ka jefa
kugiya, ka cire kifin da ya fara zuwa. Idan ka bude
bakinsa, za ka sami shekel. Ka dauke shi ka ba masu
karbar harajin nawa da naka.

**18** Daidai wannan lokacin, almajiran suka zo wurin
Yesu suka ce, ''Wanene mafi girma a mulkin
sama?'' 2 Sai Yesu ya kira karamin yaro gunsa, ya sa
shi a tsakaninsu, 3 ya ce, ''Hakika ina gaya maku, idan
baku juya kun zama kamar kananan yara ba, babu
yadda zaku shiga mulkin sama. 4 Saboda haka, duk
wanda ya kaskantar da kansa kamar karamin yaron
nan, shi ne mafi girma a mulkin sama. 5 Duk wanda
ya karbi karamin yaro a suna na, ya karbe ni. 6 Amma
duk wanda ya sa daya daga cikin 'yan yaran nan da
suka gaskanta da ni zunubi, gwamma a rataya dutsen
nika a wuyansa a jefa shi cikin zurfin teku. 7 Kaiton
duniya saboda lokacin tuntube! Lallai ne wadannan
lokuta su zo, amma kaiton mutumin da ta wurinsa
ne wadannan lokutan za su zo! 8 Idan hannunka ko
kafarka ce za ta sa ka tuntube, ka yanke ta, ka yar
daga gare ka. Zai fi maka kyau ka shiga rai da nakasa
ko gurguntaka, da a jefa ka cikin madawwamiyar wuta
tare da hannayenka ko kafafunka. (aiōnios g166) 9 Idan
idonka zai sa ka tuntube, ka kwakule shi, ka yar. Zai fi
maka kyau ka shiga rai da ido daya, da a jefa ka cikin
madawwamiyar wuta da idanu biyu. (Geenna g1067) 10 Ku
kula fa kada ku rena kananan nan. Domin koyaushe
a sama, mala'ikunsu na duban fuskar Ubana da ke
sama. 11 [Dan Mutum ya zo ya ceci abinda ya bata]. 12
Menene tunaninku? Idan mutum na da tumaki dari,
sa'annan daya ta bata, ashe ba zai bar tassa'in da tara
a gefen tudu ya tafi neman wadda ta bata ba? 13 In
ya same ta, hakika ina gaya maku, farin cikinsa na
samun dayan nan da ta bace, zai fi na tassa'in da
taran nan da basu bata ba. 14 Hakanan fa, ba nufin
Ubanku dake sama ba ne da ya daga cikin wadannan
kananan ya hallaka. 15 Idan dan'uwanka yayi maka
laifi, fada masa tsakaninku, kai da shi kadai. Idan ya
saurare ka, ka maido da dan'uwanka kenan. 16 Amma
in ya ki ya saurare ka, ka je da 'yan'uwa biyu ko uku
su zama shaidu, don ta wurin shaidu biyu ko uku
ake tabbatar da kowacce kalma. 17 In kuma ya ki ya
saurare su, ka kai lamarin ga ikklisiya. Idan ya ki ya
saurari ikklisiya, ka maishe shi ba'al'umme da mai
karbar haraji. 18 Hakika ina gaya maku, duk abin da
kuka daure a duniya, a daure yake a sama. Abin da
kuka kwance kuma, a kwance yake a sama. 19 Kuma
ina gaya maku, idan mutum ku biyu zaku yarda akan
duk abin da zaku roka, Ubana wanda ke a sama zai yi
maku shi. 20 Wurin da mutum biyu ko uku suka taru a
cikin sunana, zan kasance tare da su.'' 21 Bitrus ya
zo ya ce wa Yesu, ''Ubangiji, sau nawa ne dan'uwana
zai yi mani laifi in gafarta masa? Har sai ya kai sau
bakwai?'' 22 Yesu ya amsa ya ce masa, ''Ban gaya
maka sau bakwai ba, amma bakwai din ma har sau
saba'in. 23 Saboda haka, za a kwatanta mulkin sama
da wani sarki da yake so ya lisafta dukiyarsa dake
a hannun barorinsa. 24 Da ya fara yin haka, sai aka
kawo masa daya daga cikin barorinsa da yake binsa
talanti dubu goma. 25 Amma tunda ba shi da abin
biya, ubangidansa ya bada umurni a sayar da shi, tare
da matarsa da 'ya'yansa da duk mallakarsa, domin
a biya. 26 Sai baran ya fadi kasa, ya rusuna a gaban
ubangidansa ya ce, “Maigida, kayi mani hakuri, zan
biya duk abin da na karba.” 27 Don haka ubangidansa
yayi juyayi, sai ya ce, ya yafe bashin, a saki baran. 28
Amma bayan an saki wannan baran, ya je ya sami
wani baran kamar sa da yake bi bashin dinari dari.
Ya cafke shi, ya shake shi a wuya, ya ce, 'Ka biya
bashin da nake bin ka.' 29 Amma dan'uwansa bara
ya roke shi ya ce, kayi mani hakuri, zan biya ka duk
abinda na karba.' 30 Amma baran nan na farko ya
ki. A maimakon haka, ya sa aka jefa dan'uwansa
bara a kurkuku sai ya biya bashin nan. 31 Da sauran
barori suka ga abin da ya faru, suka damu kwarai.
Sai suka je suka fada wa ubangidansu yadda abin ya
faru duka. 32 Sai ubangidansa ya kirawo shi, ya ce
masa, ''Kai mugun bawa, na gafarta maka bashin nan

duka, domin ka roke ni. 33 Ashe, bai kamata kaima
ka nuna jinkai ga dan'uwanka bara kamar yadda na
nuna maka jinkai ba?' 34 Ubangidansa yayi fushi, ya
danka shi ga masu azabtarwa, har sai ya gama biyan
dukan bashin da ake binsa. 35 Hakanan Ubana dake a
sama zai yi maku, idan kowannenku bai gafarta wa
dan'uwansa daga zuciya ba.''

19 Sai ya zama sa'adda Yesu ya gama wadannan
maganganu, sai ya bar Galili ya zo kan iyakokin
Yahudiya, ketaren kogin Urdun. 2 Taro mai yawa suka
bi shi, ya kuma warkar da su a wurin. 3 Farisawa suka
zo wurinsa, suna gwada shi, suka ce masa, ''Ya hallata
bisa ga doka mutum ya saki matarsa don kowanne
dalili?'' 4 Yesu ya amsa ya ce, ''Baku karanta ba, cewa
shi wanda ya yi su tun farko ya yi su miji da mace?
5 Shi wanda ya yi su kuma ya ce, "Saboda wannan
dalilin, mutum zai rabu da mahaifinsa da mahaifiyarsa
ya hade da matarsa, su biyun su zama jiki daya?" 6
Su ba biyu ba ne kuma, amma jiki daya. Don haka,
duk abin da Allah ya hada, kada wani ya raba.'' 7
Sai suka ce masa, ''To me yasa Musa ya umarcemu
mu bada takardar saki, mu kuma kore ta?'' 8 Sai ya
ce masu, ''Saboda taurin zuciyarku, shi yasa Musa
ya yarda maku ku saki matanku, amma da farko ba
haka yake ba. 9 Ina gaya maku, duk wanda ya saki
matarsa in ba saboda zina ba, ya kuma auri wata,
yana zina kenan. Wanda kuma ya auri macen da aka
saka, yana aikata zina.'' 10 Almajiran suka ce wa Yesu,
''Idan haka yake game da mutum da matarsa, ba kyau
ayi aure ba.'' 11 Amma Yesu yace masu, ''Ba kowa ne
zai karbi wannan koyarwa ba, amma sai wadanda an
yardar masu su karbe ta. 12 Akwai wadanda aka haife
su babanni. Akwai wadanda mutane ne suka maida
su babanni. Sa'annan akwai wadanda sun mayar da
kansu babanni saboda mulkin sama. Duk wanda zai iya
karbar wannan koyarwa, ya karba.'' 13 Sai aka kawo
masa yara kanana don ya dibiya hannuwansa akansu,
yayi masu addu'a, amma almajiran suka kwabe su. 14
Amma Yesu ya ce masu, ''Ku bar yara kanana, kada
ku hana su zuwa wuri na, domin mulkin sama na
irinsu ne.'' 15 Ya sa hannuwa akan su, sa'annan ya bar
wurin. 16 Sai wani mutum ya zo wurin Yesu, ya ce,
''Malam, wanne ayyuka nagari ne zan yi domin in
sami rai madawwami?'' (aiōnios g166) 17 Yesu ya ce masa,
''Me yasa kake tambaya ta game da abin da ke nagari?
Daya ne kawai ke nagari, amma idan kana so ka shiga
cikin rai, ka kiyaye dokokin.'' 18 Mutumin ya ce masa,
''Wadanne dokokin?'' Yesu ya ce masa, ''Kada kayi
kisa, kada kayi zina, kada kayi sata, kada kayi shaidar
zur, 19 ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka, kuma
ka kaunaci makwabcinka kamar kanka.'' 20 Saurayin
nan ya ce masa, ''Ai na kiyaye duk wadannan. Me nake
bukata kuma?'' 21 Yesu ya ce masa, ''Idan kana so ka
zama cikakke, ka tafi ka sayar da mallakarka, ka kuma
ba matalauta, zaka sami dukiya a sama. Sa'annan ka
zo ka biyo ni.'' 22 Amma da saurayin nan ya ji abin
da Yesu ya fada, ya koma da bakin ciki, domin shi
mai arziki ne kwarai. 23 Yesu ya ce wa almajiransa,
''Hakika ina gaya maku, zai zama da wuya mai arziki
ya shiga mulkin sama. 24 Ina sake gaya maku, zai fi wa
rakumi sauki ya shiga ta kafar allura, da mai arziki ya
shiga mulkin Allah.'' 25 Da almajiran sun ji haka, suka
yi mamaki kwarai da gaske, suka ce, ''Wanene zai sami
ceto?'' 26 Yesu ya dube su, ya ce, ''A wurin mutane
wannan ba zai yiwu ba, amma a wurin Allah, kome
mai yiwuwa ne.'' 27 Sai Bitrus ya amsa ya ce masa,
''Duba, mun bar kome da kome mun bi ka. To me za
mu samu?'' 28 Yesu ya ce masu, ''Hakika ina gaya
maku, ku da kuka bi ni, a sabuwar haihuwa, lokacin
da Dan Mutum ya zauna a kursiyin daukakarsa, ku ma
zaku zauna a kursiyoyi goma sha biyu, kuna shari'anta
kabilu goma sha biyu na Isra'ila. 29 Duk wanda ya
bar gidaje, 'yan'uwa maza, 'yan'uwa mata, mahaifi,
mahaifiya, 'ya'ya, ko gonaki, saboda sunana, zai sami
ninkin su dari, ya kuma gaji rai madawwami. (aiōnios
g166) 30 Amma dayawa dake farko yanzu, za su zama na
karshe, dayawa dake karshe kuma, su zama na farko.

20 Gama mulkin sama yana kama da wani mai gona,
wanda ya fita da asuba ya nemi 'yan kwadago da
za su yi aiki a gonarsa. 2 Bayan sun shirya kudin da
zai biya ma'aikata kimanin dinari daya a kowanne
yini, sai ya aike su gonarsa suyi aiki. 3 Misalin sa'a ta
uku sai ya sake fita, sai ya ga wasu ma'aikata suna
tsaye a bakin kasuwa, babu aiki. 4 Sai ya ce masu,
'Kuzo kuyi aiki a gonar, duk abinda ya wajaba, zan
ba ku,' Sai suka tafi su yi aikin. 5 Sai ya sake fita a
sa'a ta shida ya kuma sake fita a sa'a ta tara, ya sake
yin hakan din. 6 Ya kuma sake yin haka a sa'a ta sha
daya, da ya fita sai ya ga wasu a tsaye da ba sa yin
kome. Sai ya ce masu, 'Me yasa kuke tsaye ba ku yin
kome dukan yini?' 7 Sai suka ce masa, 'Ai babu wanda
ya dauke mu aiki, shi yasa.' Sai ya ce masu, 'ku ma,

kuje cikin gonar. 8 Da yamma ta yi, sai mai gonar ya
ce wa manajansa, 'Ka kira ma'aikatan nan ka biya
su hakkin su, amma ka fara da wadanda suka zo a
karshe, zuwa na farkon.' 9 Sa'adda wadanda suka fara
aiki da yamma suka zo, an biya su daidai yadda ake
biya a yini. 10 Da wadanda suka fara aiki tun safe suka
zo, suna tsammani za a ba su fiye da wadanda sun zo
daga baya, amma aka ba kowannensu dinari daya. 11
Da suka karbi hakkinsu, suka yi gunaguni game da
mai gonar. 12 Suka ce, 'Wadannan da suka zo a karshe,
sa'a guda ce kadai suka yi aiki, amma ka ba su daidai
da mu, mu da muka yi fama da aiki cikin zafin rana.'
13 Amma mai gonar ya amsa wa daya daga cikin su, ya
ce, 'Aboki na, ban yi maku laifi ba. Ai mun shirya zan
biya ku yadda ake biya a yini, ko ba haka ba? 14 Ku
karbi abin da ke na ku, ku tafi. Ganin dama ta ne, in ba
wadannan da suka zo a karshe daidai da ku. 15 Ashe,
ba daidai bane a gare ni, in yi abin da na ga dama da
mallaka ta? Ko kishi ne kuke yi saboda kirki na?' 16
Haka yake, na karshe za su zama na farko, na farko
kuma su zama na karshe.'' [An kira dayawa, amma
kadan ne zababbu]. 17 Da Yesu zai tafi Urushalima, ya
dauki sha-biyun nan a gefe, yayin da suke tafiya, sai
ya ce masu, 18 "Ku duba fa, zamu tafi Urushalima,
kuma za a bada Dan Mutum ga manyan firistoci da
marubuta. Za su kuma yanke masa hukuncin kisa, 19
za su kuma bada shi ga al'ummai don suyi masa ba'a,
su bulale shi, su kuma gicciye shi. Amma a rana ta
uku, za a tada shi.'' 20 Sai uwar 'ya'yan Zabadi ta zo
wurin Yesu tare da 'ya'yanta. Ta rusuna a gabansa
tana neman alfarma a wurinsa. 21 Yesu ya ce mata,
Me kike so in yi maki?'' Sai ta ce masa, ''Ina so ka
ba 'ya'yana izinin zama a mulkinka, daya a hannun
damanka, daya kuma a hannun hagunka. 22 Amma
Yesu ya amsa, ya ce, ''Baku san abin da kuke roko ba.
Ko zaku iya sha daga cikin kokon da zan sha bada
dadewa ba?'' Sai suka ce masa, ''Zamu iya.'' 23 Sai
ya ce masu, ''In dai kokon nan da zan sha ne, lallai
zaku sha. Amma, zama a hannun dama na da kuma
hannun hagu na, ba ni ne mai bayarwa ba, amma na
wadanda Uba na ya shirya domin su ne.'' 24 Sa'anda
sauran almajirai goma suka ji haka, sun yi bacin rai da
'yan'uwan nan biyu. 25 Amma Yesu ya kira su wurin
sa, ya ce, ''Kuna sane da cewa, sarakunan al'ummai
suna gwada masu mulki, manyan-gari kuma na nuna
masu iko. 26 Ba zai kasance haka a tsakanin ku ba. A
maimakon haka, duk wanda ke da marmari ya zama
da girma a tsakanin ku, ya zama baran ku. 27 Wanda
kuma ke da marmari ya zama na farko a cikin ku, ya
zama baran ku. 28 Kamar dai yadda Dan mutum bai zo
don a bauta masa ba, amma yayi bauta, ya kuma bada
ransa fansa domin mutane dayawa.'' 29 Da suka fita
daga Yariko, babban taro suka bi shi. 30 Suka kuma ga
makafi biyu zaune a bakin hanya. Da makafin suka ji
cewa Yesu ne ke wucewa, sai suka tada murya suna
cewa, ''Ya Ubangiji, Dan Dauda, kayi mana jinkai.'' 31
Amma jama'ar suka tsauta masu, suka ce suyi shiru.
Duk da haka, makafin suka kara tada murya fiye da
na da, suka ce, ''Ya Ubangiji, Dan Dauda, kayi mana
jinkai.'' 32 Sai Yesu ya tsaya cik, ya sa aka kira su, sai
ya ce masu, ''Me kuke so in yi maku?'' 33 Sai suka ce
masa, Ya Ubangiji, muna so mu sami ganin gari.'' 34
Sai Yesu yayi juyayi a cikin sa, ya taba idanunsu. Nan
da nan, suka sami ganin gari, suka kuma bi shi.

**21** Yayinda Yesu da almajiransa suka kusato
Urushalima sai suka zo Betafaji wajen dutsen
zaitun, sai Yesu ya aiki almajiransa guda biyu, 2 yace
masu, "Ku shiga kauyen da yake gaban ku zaku iske
wata jaka da aholaki tara da ita. Ku kwance su ku
kawo mani su. 3 Idan wani ya gaya maku wani abu
game da haka, sai ku ce, 'Ubangiji ne yake bukatarsu,'
mutumin kuwa zai aiko ku da su nan da nan." 4
Anyi wannan kuwa domin a cika annabcin anabin.
Yace, 5 "Ku cewa diyar Sihiyona, duba, ga sarkinki
na zuwa wurin ki, mai tawali'u ne, kuma akan jaki
wanda aholaki ne." 6 Sai almajiran suka tafi suka
yi kamar yadda Yesu ya umarce su. 7 Suka kawo
jakar da dan aholakin, suka sa tufafinsu akai, Yesu
kuwa ya zauna akan tufafin. 8 Yawancin jama'a kuwa
suka baza tufafinsu akan hanya, wasu kuma suka
yanko ganye daga bishiyoyi suka shimfida su a hanya.
9 Taron jama'a da suke gabansa da wadanda suke
bayansa, suka ta da murya suna cewa, "Hossana ga
dan Dauda! mai albarka ne shi wanda ke zuwa cikin
sunan Ubangiji. Hossana ga Ubangiji!" 10 Sa'adda
Yesu ya shiga Urushalima sai doki ya cika birnin ana
cewa, "Wanene wannan?" 11 Sai jama'a suka amsa,
"Wannan shine Yesu annabi, daga Nazaret ta Galili."
12 Sai Yesu ya shiga haikalin. Ya kori duk wadanda ke
saye da sayarwa a cikin ikiilisiya. Ya birkice teburan
masu canjin kudi da kujerun masu sayar da tantabaru.
13 Ya ce masu, "A rubuce yake, 'Za a kira gidana gidan
addu'a,' amma kun mayar dashi kogon 'yan fashi."

14 Sai makafi da guragu suka zo wurin sa a haikalin,
ya warkar da su. 15 Amma da manyan firistoci da
malaman attaura suka ga abubuwan banmamaki da
yayi, kuma sa'adda suka ji yara suna tada murya a
cikin haikalin suna cewa, “Hossana ga dan Dauda,”
sai suka ji haushi. 16 Suka ce masa, kana jin abinda
wadannan mutanen ke fadi?'' Yesu ya ce masu, “I!
Amma ba ku taba karantawa ba, 'daga bakin jarirai da
masu shan mama ka sa yabo'?” 17 Sai Yesu ya bar su,
ya fice daga birnin zuwa Betaniya ya kwana a wurin.
18 Washegari da safe yayin da yake komawa birnin, sai
yaji yunwa. 19 Da ya ga bishiyar baure a bakin hanya,
sai yaje wurin amma bai sami kome ba sai dai ganye.
Sai ya ce mata, “Kada ki kara yin 'ya'ya har abada.”
Sai nan take bishiyar bauren ta bushe. (aiōn g165) 20 Da
almajiran suka ga haka, sai suka yi mamaki suka ce,
“Kaka bishiyar bauren ta bushe nan da nan?” 21 Yesu
ya amsa yace masu, “Hakika ina ce maku, in dai kuna
da bangaskiya ba ku yi shakka ba, ba abinda aka yi
wa bauren nan kadai za kuyi ba har ma za ku cewa
tsaunin nan, “Ka ciru ka fada teku,' sai kuwa haka
ta kasance. 22 Kome kuka roka cikin addu'a, in dai
kun gaskanta, za ku samu.” 23 Sa'adda Yesu ya shiga
haikalin, sai manyan fristocin da shugabannin jama'a
suka zo suka same shi yayin da yake koyarwa, suka ce,
“Da wane iko kake yin wadannan abubuwa?” 24 Yesu
ya amsa yace masu, “Ni ma zan yi maku tambaya
daya. In kun fada mani, ni ma zan fada maku ko da
wane iko nake yin wadannan abubuwa. 25 Daga ina
baftismar Yahaya ta fito, daga sama ko kuma daga
mutune?” Sai suka yi shawara a tsakanin su, suka
ce, “In munce, 'daga sama,' zai ce mana, 'don me
bamu gaskanta dashi ba?' 26 Amma in munce, ' daga
mutune,' muna tsoron jama'a, saboda sun san Yahaya
annabi ne.” 27 Sai suka amsa ma Yesu suka ce, ''Bamu
sani ba.” Shi ma yace masu, “Nima bazan gaya maku
ko da wane iko nake yin abubuwan nan ba. 28 Amma
me kuke tunani? Wani mutum yana da 'ya'ya biyu.
Ya je wurin na farkon yace, 'Da, je ka kayi aiki yau
a cikin gona.' 29 Yaron ya amsa yace, 'bazan yi ba,'
amma daga baya ya canza tunaninsa ya tafi. 30 Sai
mutumin ya je wurin da na biyun ya fada masa abu
guda. Wannan dan ya amsa ya ce, 'zanje, baba,' amma
bai je ba. 31 Wanene a cikin 'ya'ya biyun nan yayi
nufin ubansa?” Suka ce, “na farkon.” Yesu ya ce masu,
“Hakika ina gaya maku, masu karbar haraji da karuwai
za su shiga mulkin Allah kafin ku. 32 Gama Yahaya
ya zo maku a hanyar adalci, amma ba ku gaskata da
shi ba, a yayinda masu karbar haraji da karuwai suka
gaskata da shi. Ku kuwa, bayan kun ga abin da ya faru,
baku ma tuba daga baya ba don ku gaskata da shi. 33
Ku saurari wani misalin. Anyi wani mutum, mai gona.
Yayi shuka a gonar, ya shinge ta, ya gina ramin matse
inabi a cikin gonar, ya kuma gina wata hasumiyar
tsaro, sai ya bada hayar gonar ga wadansu manoma.
Sai ya tafi wata kasa. 34 Da kakar inabi ta yi, sai ya aiki
wadansu bayi su karbo masa amfanin gonar. 35 Amma
manoman suka kama bayin, suka doddoki dayan, suka
kashe dayan, suka jejjefe dayan da duwatsu. 36 Sai
mai gonar ya sake aika wadansu bayinsa da suka fi na
farko, amma manoman suka yi masu kamar yadda
suka yi wa sauran. 37 Bayan wannnan, sai mai gonar
ya aika da dansa wurin su yana cewa, 'za su yi wa
dana biyayya.' 38 Amma da manoman suka ga dan, sai
suka ce a tsakanin su, 'wannan shine magajin. Kuzo,
mu kashe shi mu gaji gonar.' 39 Sai suka dauke shi,
suka jefar da shi daga cikin gonar, suka kashe shi. 40
To idan me gonar ya zo, me zai yiwa manoman? 41
Suka ce masa, “Zai hallaka mugayen manoman nan
ta hanya mai tsanani, zai kuma bada gonar haya ga
wadansu manoman, mutanen da za su biya, lokacin
da inabin ya nuna.” 42 Yesu yace masu, “Baku taba
karantawa a nassi ba,'' 'Dutsen da magina suka ki ya
zama dutse mafi amfani. Wannan daga Ubangijine,
kuma abin mamaki ne a idanunmu?' 43 Saboda haka
ina gaya maku, za a karbe mulkin Allah daga wurin
ku a ba wata al'umma da zata bada amfaninsa. 44 Duk
wanda ya fadi akan dutsen nan zai ragargaje. Amma
duk wanda dutsen ya fadawa, zai nike.” 45 Da manyan
firistocin da farisawan suka ji wannan misalin, sai
suka gane da su yake. 46 Da suka nemi kama shi, sai
suka ji tsoron taron, saboda mutanen sun dauke shi
annabi.

**22** Yesu ya sake yi masu magana da misalai, yace,
2 “Mulkin sama yana kama da wani sarki wanda
ya shirya wa dansa liyafar aure. 3 Ya aiki bayinsa
su kira wadanda aka gayyata su zo liyafar auren,
amma suka ki zuwa. 4 Sai sarkin ya sake aiken wasu
bayin, yace, “Ku gaya wa wadanda aka gayyata, “Duba,
na shirya liyafata. An yanka bajimaina da kosassun
'yanmarukana, an gama shirya komai. Ku zo wurin
bikin auren.” 5 Amma mutanen ba su dauki sakon
da mahimmanci ba kuma suka yi tafiyarsu. Wani

ga gonarsa, wani ga kasuwancinsa. 6 Sauran kuma
suka kama bayin sarkin, suka wulakanta su, suka
kuma kashe su. 7 Amma sarkin ya ji haushi. Ya aika
sojojinsa, ku kashe masu kisan kan nan, ku kuma kone
birnin su. 8 Sai ya ce wa bayinsa, 'An gama shirya
bikin, amma wadanda aka gayyata ba su cancanta
ba. 9 Saboda haka ku je bakin hanya ku gayyaci
iyakar yawan mutanen da za ku samu zuwa bukin
auren.' 10 Bayin suka tafi hanya suka tattaro dukan
mutanen da suka samu, da masu kyau da marassa
kyau. Zauren auren kuwa ya cika makil da baki. 11
Amma da sarkin ya zo don ya ga bakin, sai ya ga
wani wanda bai sa kayan aure ba. 12 Sai sarkin ya
ce masa, 'Aboki, ta yaya ka shigo nan ba tare da
kayan aure ba?' Mutumin kuwa ya rasa ta cewa. 13
Sai sarkin ya ce wa bayinsa, 'Ku daure mutumin nan
hannu da kafa, ku jefa shi cikin duhun, inda za ayi
kuka da cizon hakora.' 14 Gama mutane dayawa aka
kira, amma kadan aka zaba.”' 15 Sai Farisawan suka
tafi suka shirya makirci akan yadda zasu kama shi
ta maganarsa. 16 Suka tura masa almajiransu, da
Hirudiyawa. Suka ce ma Yesu, “Mallam, mun san kai
mai gaskiya ne, kuma kana koyar da hanyar Ubangiji
da gaskiya. Ba ka damu da ra'ayin kowa ba, kuma ba ka
nuna bambanci a tsakanin mutane. 17 To gaya mana,
menene tunaninka? Ya halarta a biya haraji ga Kaisar
ko a'a?” 18 Amma Yesu ya gane muguntarsu yace,
“Don me kuke gwada ni, ku munafukai? 19 Ku nuna
mani sulen harajin.” Sai suka kawo masa sulen. 20
Yesu yace masu, “Hoto da sunan wanene wadannan?”
21 Suka ce masa, “Na Kaisar.” Sai Yesu ya ce masu, “To
ku ba Kaisar abubuwan dake na Kaisar, Allah kuma
abubuwan dake na Allah.” 22 Da suka ji haka, suka
yi mamaki. Sai suka bar shi suka tafi. 23 A ran nan
sai wadansu Sadukiyawa, wadanda suka ce ba tashin
matattu, suka zo wurinsa. Suka tambaye shi, 24 cewa,
“Mallam, Musa yace, 'Idan mutum ya mutu, bashi
da 'ya'ya, dole dan'uwansa ya auri matarsa ya kuwa
haifawa dan'uwansa 'ya'ya. 25 Akwai wasu 'yan'uwa
bakwai. Na farkon yayi aure sai ya mutu. Da shike
bai bar 'ya'ya ba. Ya bar wa dan'uwansa matarsa. 26
Sai dan'uwansa na biyu shi ma yayi haka, haka kuma
na ukun, har zuwa dan'uwan na bakwai. 27 Bayan
dukansu, sai matar ta mutu. 28 To a tashin matattu,
matar wa zata zama a cikin su bakwai din? Don duk
sun aure ta.” 29 Amma Yesu ya amsa yace masu, “Kun
bata, domin ba ku san litattafai ko ikon Allah ba. 30
Domin a tashin matattu basu aure, ba kuma a bada
su aure. Maimaikon haka, suna kama da mala'ikun
sama. 31 Amma game da tashin matattu, ba ku karanta
abinda Allah ya fada maku ba, cewa, 32 'Nine Allah na
Ibrahim, Allah na Ishaku, da Allah na Yakubu'? Allah
ba Allah na matattu bane, amma na rayayyu.” 33 Da
taron suka ji haka, sai suka yi mamakin koyarwarsa.
34 Amma da Farisawan suka ji cewa Yesu ya kure
Sadukiyawa, sai suka tattara kansu. 35 Daya daga
cikinsu, masanin shari'a, yayi masa tambaya, yana
gwada shi- 36 “Mallam, wace doka ce mafi girma
a cikin shari'a?” 37 Yesu yace masa, “Ka kaunaci
Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan
ranka, da dukkan hankalinka.' 38 Wannan itace babbar
doka ta farko. 39 Doka ta biyu kuma kamar ta take-
'Ka kaunaci makwabcinka kamar kanka.' 40 Akan
wadannan dokoki ne dukkan shari'a da annabawa
suka rataya.” 41 Yayin da Farisawa suke tattare wuri
daya, Yesu yayi masu tambaya. 42 Yace, “Me kuke
tunani game da Almasihu? Shi dan wanene?” Suka
ce masa, ''Dan Dauda ne.” 43 Yesu yace masu, “To ta
yaya kuma Dauda cikin Ruhu ya kira shi Ubangiji,
yana cewa, 44 “Ubangiji ya cewa wa Ubangijina, zauna
a hannun damana, har sai na mai da makiyanka
matakin sawayenka.” 45 Idan Dauda ya kira Almasihu
'Ubangiji,' ta yaya ya zama dan Dauda?” 46 Ba wanda
ya iya bashi amsa, ba kuma wanda ya kara yi masa
tambayoyi tun daga wannan rana.

23 Sai Yesu yayi wa taron da alamajiransa magana.
2 Ya ce, “Marubuta da Farisawa suna zaune
a mazaunin Musa. 3 Don haka, duk abinda suka
umarceku kuyi, kuyi wadannan abubuwa ku kuma
kiyaye su. Amma kada kuyi koyi da ayyukansu, gama
suna fadar abubuwa amma kuma ba su aikata su. 4 I,
sukan daura kaya masu nauyi, masu wuyar dauka,
daga nan su dauka su jibga wa mutane a kafada.
Amma su kan su baza su mika danyatsa ba su dauka.
5 Duk ayyukan su suna yi ne don mutane su gani,
suna dinka aljihunan nassinsu da fadi, suna fadada
iyakokin rigunansu. 6 Su na son mafifitan wuraren
zama a gidan biki, da mafifitan wuraren zama a
majami'u, 7 da kuma gaisuwar musamman a wuraren
kasuwanci, a kuma rika ce da su 'mallam.' 8 Amma
ba sai an kira ku 'mallam, ba' domin malami daya
kuke da shi, ku duka kuwa 'yan'uwan juna ne. 9 Kada
ku kira kowa 'Ubanku' a duniya, domin Uba daya
ne ku ke da shi, kuma yana sama. 10 Kada kuma a

kira ku malamai, saboda malamin ku daya ne, shi ne
Almasihu. 11 Amma wanda yake babba a cikin ku zaya
zama bawanku. 12 Duk wanda ya daukaka kansa za a
kaskantar dashi. Duk wanda ya kaskantar da kansa
kuma za a daukaka shi. 13 Amma kaiton ku marubuta
da Farisawa, munafukai! Kun toshewa mutane kofar
mulkin sama. Baku shiga ba, kuma ba ku bar wadanda
suke so su sami shiga ba. 14 kaiton ku marubuta da
Farisawa, domin kuna hallaka gwauraya - 15 Kaiton
ku marubuta da Farisawa, munafukai! Kuna tafiya
ketaren tekuna da kasashe domin samun almajiri
daya tak, in kwa kun samu kukan mai da shi biyunku
danwuta. (Geenna g1067) 16 Kaiton ku, makafin jagora,
kuda kuke cewa, Kowa ya rantse da Haikali, ba komai.
Amma duk wanda ya rantse da zinariyar Haikalin,
rantsuwarsa ta daure shi.' 17 Ku wawayen makafi!
wanene yafi girma, zinariyar ko kuwa Haikalin da
yake tsarkake zinariyar? 18 Kuma, 'Kowa ya rantse da
bagadi, ba komai bane. Amma duk wanda ya rantse da
baikon da aka dora a kai, sai rantsuwarsa ta kama
shi.' 19 Ku makafi! Wanene yafi girma, baikon ko kuwa
bagadin da yake kebe baikon ga Allah? 20 Saboda
haka, duk wanda ya rantse da bagadi, ya rantse da
shi da duk abinda ke kansa. 21 Kuma duk wanda ya
rantse da Haikali ya rantse dashi da kuma wanda yake
cikin sa. 22 Kuma duk wanda ya rantse da sama, ya
rantse da kursiyin Allah da kuma wanda yake zaune
akai. 23 Kaiton ku Farisawa da marubuta, munafukai!
Kukan fitar da zakkar doddoya, da karkashi, da lamsur,
amma kun yar da al'amuran attaura mafi nauyi-,
wato, hukunci, da jinkai da bangaskiya. Wadannan ne
ya kamata kuyi, ba tare da kunyi watsi da sauran ba.
24 Makafin jagora, ku kan burtsar da kwaro dan mitsil,
amma kukan hadiye rakumi! 25 Kaiton ku marubuta
da Farisawa, munafukai! kuna wanke bayan moda
da kwano, amma aciki cike suke da zalunci da keta.
26 Kai makahon Bafarise! Sai ka fara tsarkake cikin
modar da kwanon domin bayansu ma su tsarkaka. 27
Kaiton ku marubuta da Farisawa, munafukai! Kamar
kaburburan da aka shafa wa farar kasa kuke, masu
kyaun gani daga waje, daga ciki kuwa sai kasusuwan
matattu da kazanta iri iri. 28 Haka nan kuke a idanun
mutane ku adalai ne, amma a ciki sai munafunci
da mugun aiki. 29 Kaiton ku marubuta da Farisawa,
munafukai! Ku kan gina kaburburan annabawa, kuna
kuma kawata kaburburan adalai. 30 Kuna cewa, 'Da
muna nan a zamanin Ubanninmu, da bamu basu
goyon baya ba wajen zubar da jinin annabawa.' 31
Domin haka kun shaida kanku ku ne 'ya'yan masu
kisan annabawa. 32 Sai kuma kuka cika ma'aunin
ubanninku! 33 macizai, Ku 'ya'yan ganshekai, Yaya
zaku tsere wa hukuncin Gidan wuta? (Geenna g1067) 34
Saboda haka, duba, ina aiko maku da annabawa, da
masu hikima da marubuta. Za ku kashe wadansun
su kuma ku gicciye su. Zaku yiwa wasu bulala a
majami'un ku, kuna bin su gari gari. 35 Sakamakon
hakan alhakin jinin dukkan adalai da aka zubar a
duniya ya komo a kan ku, tun daga jinin Habila adali
har ya zuwa na Zakariya dan Barakiya, wanda kuka
kashe a tsakanin Haikali da bagadi. 36 Hakika, Ina gaya
maku, duk wannan zai auko wa mutanen wannan
zamani. 37 Urushalima, Urushalima, keda kika kashe
annabawa kika kuma jejjefi wadanda aka turo maki da
duwatsu! Sau nawa ne naso in tattaro ki kamar yadda
kaza take tattara 'yan tsakinta cikin fukafukanta,
amma kin ki. 38 Ga shi an bar maku gidan ku a yashe!
39 Ina dai gaya maku, ba za ku kara gani na ba, sai
ran da kuka ce, 'Albarka ta tabbata ga mai zuwa cikin
sunan Ubangiji."'

24 Yesu ya fita daga cikin haikalin ya kama hanyar
sa. Almajiran sa suka zo suna nuna masa ginin
haikali. 2 Amma ya amsa masu yace, "kun ga dukkan
wadannan abubuwan? Ina gaya maku gaskiya, ba ko
dutse daya da za'a bari akan dan'uwansa wanda ba
za'a rushe shi ba." 3 Yayin da ya zauna a kan dutsen
zaitun, almajiran sa suka zo wurin sa a boye suka ce,
"me zai zama alamar zuwanka da kuma na karshen
duniya?" (aiōn g165) 4 Yesu ya amsa yace dasu, "Ku kula
kada wani yasa ku kauce." 5 Gama da yawa za su zo
da sunana. Za su ce, "ni ne almasihu," kuma za su
sa da yawa su kauce. 6 Za ku ji labarin yake-yake
da kuma shelar yake-yake. Ku kula kar ku tsorata,
domin dole abubuwan nan su faru; amma karshen
dai tukunna. 7 Gama al'umma zata tayarwa al'umma,
kuma mulki zai tayarwa mulki. Za'a yi yunwa da
girgizar kasa a wurare dabam dabam. 8 Amma dukkan
wadannan farkon ciwon haihuwa ne kawai. 9 Bayan
haka za'a bada ku ga tsanani a kuma kashe ku. Dukkan
al'ummai za su tsane ku saboda sunana. 10 Daga nan
da yawa za su yi tuntube, kuma su ci amanar juna, su
kuma tsani juna. 11 Annabawan karya da yawa za su
taso kuma susa da yawa su kauce. 12 Domin mugunta
zata ribambanya, kaunar masu yawa zata yi sanyi. 13

Amma duk wanda ya jure har karshe, zai sami ceto.
14 Za'a yi wa'azin wannan bisharar mulkin a dukkan
duniya don ya zama shaida akan dukkan al'ummai.
Daganan karshen zai zo. 15 Don haka, idan kun ga
abin kyama mai lalatarwa, wanda Annabi Daniyel ya
yi maganar sa, Ya tsaya a wuri mai tsarki (bari mai
karatu ya fahimta), 16 bari wadanda ke yahudiya su
gudu zuwa kan duwatsu, 17 Bari wanda yake kan bene
kada ya sauko don daukar wani abu a cikin gidansa,
18 kuma wanda yake gona kar ya dawo gida domin
daukar babbar rigarsa. 19 Amma kaito ga wadanda
suke dauke da yaro, ko masu shayarwa a wannan
kwanakin! 20 Ku yi addu'a kada gudun ku ya zama
lokacin hunturu, ko ranan asabaci. 21 Domin za'ayi
tsanani mai girma, wanda ba'a taba yin irin shi ba,
tun farkon duniya har ya zuwa yau, a'a ba za ayi irin
shi ba kuma. 22 In ba don an rage kwanakin ba, da ba
mahalukin da zai tsira. Amma albarkacin zababbun,
za a rage kwanakin. 23 Sa'annan idan wani yace
maku, duba, “ga Almasihu a nan!” ko, “ga Almasihu
a can!” kar ku gaskata. 24 Gama annabawan karya
da almasihan karya za su zo suna nuna alamu da
al'ajibai, don su yaudari masu yawa zuwa ga bata, in
ya yiwuma har da zababbun. 25 Kun gani, na gaya
maku kafin lokacin ya zo. 26 Saboda haka, idan suka
ce maku, “ga shi a jeji,” kar ku je jejin. Ko, “ga shi
a can cikin kuryar daki,” kar ku gaskata. 27 Yadda
walkiya ke haskakawa daga gabas zuwa yamma, haka
nan zuwan Dan mutum zai zama. 28 Duk inda mushe
yake, nan ungulai suke taruwa. 29 Amma nan da nan
bayan kwanakin tsananin nan, rana za ta duhunta,
wata kuma ba zai ba da haskensa ba, taurari kuma za
su fado daga sama, ikokin sammai za su girgiza. 30
Sa'annan alamar Dan Mutum za ta bayyana a sararin
sama, kuma dukkan kabilun duniya za su yi bakin ciki.
Za su ga Dan Mutun na zuwa a gajimarai da iko da
daukaka mai girma. 31 Zai aiki mala'ikunsa, da karar
kaho mai karfi, kuma za su tattara dukkan zababbu
daga dukkan kusurwoyi hudu, daga karshen sararin
sama har zuwa wani karshen. 32 Kuyi koyi da itacen
baure. Da zaran reshen sa ya yi toho ya fara bada
ganye, za ku sani bazara ta kusa. 33 Haka kuma, idan
kun ga dukkan wadannan abubuwa, ya kamata ku
sani, Ya yi kusa, ya na bakin kofa. 34 Ina gaya maku
gaskiya, wannan zamanin ba zai wuce ba, sai dukkan
wadannan abubuwan sun faru. 35 Sama da kasa za
su shude, amma kalmomina ba za su shude ba. 36
Amma game da ranan nan ko sa'a ba wanda ya sani,
ko mala'ikun sama, ko Dan, sai Uban kadai. 37 Kamar
yadda kwanakin Nuhu suke, haka zai zama game da
zuwan Dan Mutum. 38 A wadannan kwankin kafin
zuwan ruwan tsufana suna ci suna sha, suna aure
suna aurarwa har ranar da Nuhu ya shiga jirgin, 39 ba
su san kome ba har ruwan ya zo ya cinye su haka ma
zuwan Dan Mutun zai zama. 40 Sa'annan mutane biyu
zasu kasance a gona za a dauke daya, a bar daya a
baya. 41 Mata biyu na nika a manika za a dauke daya,
za a bar dayar. 42 Don haka sai ku yi zaman tsaro,
domin baku san ranar da Ubangijinku zai zo ba. 43
Amma ku san wannan, idan maigida ya san lokacin
da barawo zai zo, zai zauna a shirye ba zai bar gidan
sa har a balle a shiga ba. 44 Don haka sai ku shirya,
domin Dan Mutum zai zo a sa'ar da ba ku yi zato
ba. 45 To wanene amintaccen bawannan mai hikima,
wanda maigidan sa ya sa ya kula mar da gida, domin
ya ba su abinci a kan lokaci? 46 Mai albarka ne bawan,
da mai gidan zai same shi a kan aikin sa a lokacin
da ya dawo. 47 Ina gaya maku gaskiya mai gidan zai
dora shi a kan dukkan a binda yake da shi. 48 Amma
idan mugun bawa ya ce a zuciyarsa, “maigida na ya yi
jinkiri,” 49 sai ya fara dukan sauran barorin, ya yi ta
ci da sha tare da mashaya, 50 uban gidan bawan zai
dawo a ranar da bawan bai zata ba, a lokacin da bai
sani ba. 51 Uban gidansa zai datsa shi biyu, karshen sa
zai zama daidai da na munafukai, za a sashi inda a ke
kuka da cizon hakora.

**25** Sa'annan mulkin sama zai zama kamar budurwai
goma da suka dauki fitilunsu domin su taryi
ango. 2 Biyar daga cikin su masu hikima ne biyar
kuma wawaye. 3 Sa'adda wawayen budurwai suka
dauki fitilunsu, ba su dauki karin mai ba. 4 Amma
budurwai masu hikimar suka dauki gorar mai tare
da fitilunsu. 5 To da angon ya makara, dukkan su sai
suka fara gyangyadi sai barci ya dauke su. 6 Amma
da tsakkar dare sai aka yi shela, 'Ga ango ya iso! Ku
fito taryensa. 7 Sai dukka budurwan nan suka tashi
suka gyaggyara fitilunsu. 8 Wawayen su ka ce da
masu hikimar, 'Ku sammana kadan daga manku gama
fitilunmu su na mutuwa.' 9 “Amma masu hikimar
suka ce 'Tun da man ba zai ishe mu tare da ku ba,
sai ku je gun ma su sayarwa ku sayo wa kanku. 10
Sa'adda suka tafi sayan man, sai angon ya shigo,
kuma wadanda suke a shirye su ka shiga tare da shi

bukin auren, sai aka rufe kofar. 11 Bayan dan lokaci
kadan sauran budurwan suka dawo suna cewa, 'Mai
gida, mai gida, bude mana kofar.' 12 Amma ya amsa
ya ce, 'A gaskiya ina gaya maku, ni ban san ku ba.'
13 Don haka sai ku lura, don baku san rana ko sa'a
ba. 14 Domin yana kama da wani mutum da zai tafi
wata kasa. Ya kira barorinsa ya ba su dukiyar sa. 15
Ga wani ya ba shi talanti biyar, ga wani ya ba shi
biyu, ga wani kuma ya ba shi talanti daya. kowa an
bashi gwargwadon iyawarsa, sai wannan mutum ya yi
tafiyar sa 16 nan da nan sai wanda ya karbi talanti
biyar ya sa nasa a jari, ya sami ribar wasu talanti
biyar. 17 Haka ma wanda ya karbi talanti biyu ya sami
ribar wasu biyu. 18 Amma bawan da ya karbi talanti
dayan ya yi tafiyar sa, ya haka rami, ya binne kudin
mai gidansa. 19 To bayan tsawon lokaci sai ubangidan
barorin nan ya dawo, domin yayi lissafin kudinsu.
20 Bawan da ya karbi talanti biyar, ya kawo nasa da
ribar wasu biyar. Yace, 'Maigida, ka bani talanti biyar,
gashi na samo ribar karin talanti biyar.' 21 Maigidansa
yace masa, 'Madalla, bawa na gari mai aminci! Ka
yi aminci akan abu kadan. Zan sa ka akan abubuwa
masu yawa. Ka shiga cikin farincikin maigidanka.' 22
Bawan da ya karbi talanti biyun, ya zo yace, 'Maigida,
ka ba ni talanti biyu. Gashi kuwa na sami karin ribar
wasu biyun.' 23 Ubangidansa yace masa, 'Madalla, kai
bawa na gari mai aminci! Ka yi aminci akan abubuwa
kadan. Zan saka akan abubuwa masu yawa. Ka shiga
cikin farincikin maigidanka.' 24 Sai bawan da ya karbi
talanti daya ya zo yace, 'Maigida, na san kai mai
tsanani ne. Kana girbi inda baka yi shuka ba, kuma
kana tattarawa inda ba ka watsa ba. 25 Na ji tsoro,
don haka sai na je na boye talantinka a rami. Duba, ga
abinda yake naka.' 26 Amma ubangidansa ya amsa
yace, kai mugu malalacin bawa, ka san cewa ni mai
girbi ne inda ban shuka ba kuma ina tattarawa inda
ban zuba ba. 27 To da ba sai ka kai kudina a banki
ba, da bayan na dawo da sai in karbi abina da riba.
28 Saboda haka ku kwace talantin daga gare shi ku
baiwa mai talanti goman nan. 29 Gama ga wanda yake
da shi za'a kara masa har ma a yalwace za'a kara
bashi. Amma ga wanda bashi da komai abinda ke
nasa ma za'a kwace. 30 Ku jefa wannan mugun bawan
marar amfani, cikin duhu mai zurfi, inda ake kuka
da cizon hakora.' 31 Sa'adda Dan mutum zai zo cikin
daukakarsa da dukan Mala'iku tare da shi, sa'annan zai
zauna kursiyinsa na daukaka. 32 A gabansa za'a tattara
dukkan al'ummai, zai rarraba mutanen daya'daya,
kamar yadda makiyayi yake rarraba tumaki daga
awaki. 33 Zai sa tumakin a hannunsa na dama, amma
awakin a hannunsa na hagu. 34 Sa'annan sarkin zai
ce wa na hannun damarsa, 'Ku zo ku da Ubana ya
albarkata, ku gaji mulkin da aka shirya maku kafin a
kafa duniya. 35 Gama na ji yunwa kuka bani abinci;
Na ji kishi kuka bani ruwa; Na yi bakunci kun bani
masauki; 36 Na yi huntanci kuka tufasar dani; Na yi
ciwo kuka kula dani; Ina kurkuku kuka ziyarceni.' 37
Sa'annan masu adalcin za su amsa su ce, 'Ubangiji,
yaushe muka ganka kana jin yunwa muka baka abinci?
Ko kana jin kishi muka baka ruwan sha? 38 Kuma
yaushe muka ganka kana bakunci har muka baka
masauki? Ko kuma kana huntanci da muka tufatar
da kai? 39 Yaushe kuma muka ganka kana ciwo ko a
kurkuku har muka ziyarce ka?' 40 Sa'annan Sarkin zai
amsa masu yace, 'Hakika Ina gaya maku, duk abinda
kuka yi wa daya mafi kakanta daga cikin 'yan'uwana a
nan ni kuka yi wa.' 41 Sa'annan zai cewa wadanda suke
hannunsa na hagu, 'Ku rabu da ni, ku la'anannu, ku
tafi cikin wutar jahannama da aka shirya wa Shaidan
da aljannunsa, **(aiōnios g166, questioned)** 42 domin ina jin
yunwa baku bani abinci ba; ina jin kishi ba ku bani
ruwa ba; 43 Ina bakunci amma baku bani masauki
ba; ina huntanci, baku tufasar da ni ba; ina ciwo
kuma ina kurkuku, baku kula da ni ba.' 44 Sa'annan
suma zasu amsa su ce, 'Ubangiji, yaushe muka ganka
kana jin yunwa, ko kishin ruwa, ko kana bakunci, ko
kana huntanci, ko ciwo, kuma a kurkuku, da bamu yi
maka hidima ba?' 45 Sa'annan zai amsa ya ce masu,
'Ina gaya maku hakika abin da baku iya yiwa mafi
karanta daga cikin wadannan ba, ba ku yi mani ba.' 46
Wadannan kuwa zasu tafi cikin madawwamiyar azaba
amma adalai zuwa rai madawwami.” **(aiōnios g166)**

26 Yayin da Yesu ya gama fadi masu wadannan
maganganu, sai ya cewa almajiransa, 2 “Kun sani
sauran kwana biyu idin ketarewa ya zo, kuma za'a
bada Dan mutum domin a gicciye shi. 3 Sa'annan
manyan firistoci da dattawan jama'a suka taru a fadar
babban firist, mai suna Kayafa. 4 Suka shirya yadda
zasu kama Yesu a boye su kuma kashe shi. 5 Amma
suna cewa, “Ba a lokacin idin ba, domin kada tarzoma
ta tashi daga cikin mutane.” 6 Sa'adda Yesu yake
Baita'anya a gidan Saminu Kuturu, 7 daidai lokacin da
ya zauna a gefen teburin cin abinci, sai wata mata ta

shigo da kwalbar mai, mai tsada, ta zuba wa Yesu a
kansa. 8 Amma da almajiransa suka ga haka, sai suka
ji haushi suka ce, “Ina dalilin yin irin wannan asara?
9 Ai da an sayar da wannan mai da kudi mai yawa
a rabawa talakawa.” 10 Amma da yake Yesu ya san
tunaninsu, sai yace masu, “Don me kuke damun matar
nan? Ta yi abu mai kyau domina. 11 Kuna da talakawa
tare da ku koyaushe, amma ni ba zan kasance da ku ba
koyaushe. 12 Don a sa'adda ta zuba man nan a jikina,
ta yi haka ne don jana'iza ta. 13 Hakika Ina gaya maku,
duk inda za ayi wannan bishara a dukan duniya,
abin da matar nan tayi za'a rika ambatar da shi don
tunawa da ita.” 14 Sai daya daga cikin sha biyun,
mai suna Yahuza Iskariyoti, ya tafi wurin manyan
firistocin, 15 yace, ''Me kuke da niyyar bani idan na
mika maku shi?” Suka auna masa azurfa talatin. 16
Daga wannan lokacin yayi ta neman zarafi da zai bada
shi a wurinsu. 17 To a rana ta fari na idin ketarewa
almajiran suka zo wurin Yesu suka ce, ''Ina kake so
mu shirya maka da zaka ci abincin idin ketarewa?” 18
Yace, “Ku shiga cikin birnin zaku sami wani mutum
sai kuce masa, 'Mallam yace, “lokaci na ya kusa.
Zan ci idin ketarewa a gidanka, da almajiraina.”''' 19
Almajiran suka yi kamar yadda Yesu ya umarce su,
suka shirya abincin idin ketarewar. 20 Da yamma ta yi,
sai ya zauna domin ya ci tare da almajiransa goma sha
biyu. 21 Sa'adda suke ci, yace, “Hakika ina gaya maku,
daya daga cikin ku zai bada ni.” 22 Suka yi bakin ciki,
suka fara tambayarsa daya bayan daya, ''Na tabbata
ba ni bane ko, Ubangiji?” 23 Sai ya amsa, “Wanda ke
sa hannu tare da ni cikin kwano daya shi ne zai bada
ni. 24 Dan mutum zai tafi, kamar yadda aka rubuta
akan sa. Amma kaiton mutumin da ta wurin sa za'a
bada Dan mutum! Gwamma da ba'a haifi mutumin
nan ba.” 25 Yahuza da zai bada shi yace, “Mallam ko
ni ne?” Yace masa, “Ka fada da kanka.” 26 Yayin da
suke ci, sai Yesu ya dauki gurasa, ya sa albarka, ya
karya. Ya ba almajiran yace, “Ku karba, ku ci, wannan
jiki nane.” 27 Sai ya dauki kokon yayi godiya, Ya ba su
yace, “Ku sha, dukanku. 28 “Gama wannan jinina ne
na alkawari wanda aka zubar domin gafarar zunuban
mutane da yawa. 29 Amma ina gaya maku, ba zan kara
shan ruwan inabin nan ba, sai ranar da zan sha shi
sabo tare da ku a cikin mulkin Ubana.” 30 Da suka
raira waka, sai suka ka tafi dutsen zaitun. 31 Sai Yesu
yace masu, “Dukan ku zaku yi tuntube a wannan dare
sabili da ni, gama a rubuce yake, ''Zan bugi makiyayin,
garken tumakin kuma za su watse.' 32 Amma bayan
an tashe ni, zan riga ku zuwa Galili.” 33 Amma Bitrus
yace masa, “Ko dama duka zasu fadi sabili da kai, ni
kam bazan fadi ba.” 34 Yesu yace masa, ''Hakika ina
gaya maka, a wannan daren kafin carar zakara, za
ka yi musun sani na sau uku.” 35 Bitrus yace masa,
koda zan mutu tare da kai, bazan yi musunka ba.”
Sai sauran almajiran suma suka fadi haka. 36 Sa'anna
Yesu ya tafi tare da su, wurin da ake kira Getsaimani
sai yace wa almajiransa, ''Ku zauna a nan ni kuma
zan je gaba in yi addu'a.” 37 Ya dauki Bitrus da kuma
'ya'ya biyu na Zabadi tare da shi, sai ya fara damuwa
da juyayi. 38 Sai yace masu, “Raina na cikin damuwa
sosai har ga mutuwa. Ku kasance anan kuna tsaro
tare da ni.” 39 Ya dan taka zuwa gaba kadan, sai ya
fadi a fuskarsa, yayi addu'a. Yace, “Ya Ubana, in zai
yiwu, bari kokon nan ya wuce ni. Duk da haka, ba
nufina za'a bi ba, amma naka nufin.” 40 Ya koma
wurin almajiran ya same su suna barci, sai ya cewa
Bitrus, “Kai, ba zaku yi tsaro tare da ni ba koda sa'a
daya? 41 Ku yi tsaro kuma, kuyi addu'a domin kada ku
fada cikin jaraba. Ruhu dai ya yarda amma, jiki ba
karfi.” 42 Sai ya koma karo na biyu yayi addu'a, Yace,
“Ya Ubana, in wannan kokon ba zai wuce ba sai na
sha shi, bari nufinka ya kasance.” 43 Ya sake dawowa,
ya same su suna barci, domin idanunsu sun yi nauyi.
44 Sai ya sake barinsu ya tafi. Ya koma karo na uku
yana addu'a yana fadin kalmomi iri daya. 45 Sai Yesu
ya koma wurin almajiran yace masu, “Har yanzu barci
kuke kuna hutawa? Duba, lokaci ya kusato, kuma
an bada Dan mutum ga hannun masu zunubi. 46 Ku
tashi mu tafi. Duba, wanda zai badani ya kusato.” 47
Sa'adda yana cikin magana Yahuza, daya daga cikin
sha biyun, ya zo. Babban taro ya zo tare da shi daga
wurin manyan firistoci da dattawan jama'a. Suna rike
da takubba da kulake. 48 To mutumin da zai bada
Yesu ya rigaya ya basu alama, cewa, ''Duk wanda na
sumbata, shine. Ku kama shi.'' 49 Nan da nan ya kaiga
Yesu ya ce, “Gaisuwa, Mallam!” sai ya sumbace shi. 50
Yesu kuwa yace masa, “Aboki, kayi abin da ya kawo
ka.” Sai suka iso suka sa hannuwansu kan Yesu suka
kama shi. 51 Nan take, daya daga cikin wadanda suke
tare da Yesu ya mika hannunsa, ya zare takobinsa, ya
sare wa bawan babban firist din kunne. 52 Sai Yesu
yace, masa, “Ka maida takobinka cikin kubensa, domin
duk wadanda suka dauki takobi su ma ta wurin takobi
za su hallaka. 53 Ko kana tunanin ba zan iya kiran

Ubana ba, ya kuma aiko da rundunar Mala'iku fiye da
goma sha biyu? **54** Amma to tayaya za'a cika nassi,
cewa dole wannan ya faru?'' **55** A wannan lokacin
Yesu yace wa taron, "Kun zo da takubba da kulake ku
kama ni kamar dan fashi? Ina zaune kowace rana a
haikali ina koyarwa, amma baku kama ni ba. **56** Amma
duk wannan ya faru ne don a cika abinda annabawa
suka rubuta." Bayan haka sai dukkan almajiran suka
bar shi suka gudu. **57** Wadanda suka kama Yesu, suka
kai shi wurin Kayafa babban firist, inda marubuta
da duttawan jama'a suka taru. **58** Amma Bitrus ya bi
shi daga nesa, har zuwa farfajiyar babban firist din.
Ya shiga ya zauna da masu tsaro domin ya ga abinda
zai faru. **59** A wannan lokaci manyan firistoci da duk
'yan majalisar suka fara neman shaidar karya akan
Yesu, domin su samu su kashe shi. **60** Amma ba su
samu ko daya ba, ko dayake an samu shaidun karya
dayawa da suka gabata. Amma daga baya sai wasu
su biyu suka fito **61** sukace ''Wannan mutum yace
zan iya rushe haikalin Allah, in kuma gina shi cikin
kwana uku.''' **62** Babban Firist din ya tashi tsaye yace
masa, "Ba zaka ce komai ba? Wace irin shaida ce ake
yi akanka?" **63** Amma Yesu yayi shiru. Babban Firist
ya ce, "Na umarce ka da sunan Allah mai rai, ka gaya
mana ko kai Almasihu ne, Dan Allah.'' **64** Yesu ya amsa
masa, "Ka fada da bakin ka. Amma ina gaya maka,
daga yanzu zaka ga Dan mutun na zaune a hannun
dama na iko, ya na zuwa akan gizagizai na sama." **65**
Sai babban firist din ya yayyaga rigarsa, yana cewa,
"Yayi sabo! don me ku ke neman wata shaida kuma?
Duba, yanzu kun ji sabon. **66** Menene tunaninku?"
Suka amsa sukace, "Ya cancanci mutuwa." **67** Sai suka
tofa masa yawu a fuska, suka kuma yi masa duka, suka
kuma mammare shi da tafin hannuwansu, **68** sukace,
''Ka yi mana anabci, kai Almasihu. Wanene wanda ya
dokeka. **69** To Bitrus kuwa na zaune a farfajiyar, sai
wata yarinya baiwa ta zo wurinsa tana cewa, "Kaima
kana tare da Yesu na Galili." **70** Amma ya yi musun
haka a gaban su duka, yace, "Ban ma san abinda kike
magana akai ba." **71** Da ya fita zuwa bakin kofa, nan
ma wata yarinyar baiwa ta gan shi tace wa wadanda
suke wurin, "Wannan mutumin ma yana tare da Yesu
Banazare." **72** Sai yayi musun haka kuma, har da
rantsuwa, yace, "Ban san mutumin nan ba." **73** Bayan
dan lokaci kadan wadanda suke a tsaye suka zo wurin
Bitrus suka ce masa, "Hakika kai daya daga cikin
su ne, gama harshen ka ya tonaka." **74** Sai ya fara
rantsuwa irin ta la'ana, yana cewa, ''Ban san wannan
mutumin ba," nan da nan zakara yayi cara. **75** Bitrus
ya tuna da maganar da Yesu ya fada, "Kafin carar
zakara zaka yi musun sani na sau uku." Sai ya fita
waje yayi kuka mai zafi.''

**27** Da gari ya waye, duk manyan firistoci da dattawan
jama'a suka shirya yadda zasu kulla makirci
domin su kashe shi. **2** Suka daure shi, suka mika shi
ga gwamna Bilatus. **3** Sa'adda Yahuza, wanda ya bashe
shi, ya ga an zartarwa Yesu hukuncin kisa, ya nemi
tuba ya kuma mayar da azurfar talatin ga manyan
firistocin da dattawan, **4** yace, "Na yi zunubi ta wurin
cin amanar mara laifi." Amma sukace, "Ina ruwan mu?
Ka ji da shi da kanka?" **5** Sai ya jefar da kwandalolin
azurfar a kasa cikin haikalin ya kuma bar su, ya tafi ya
rataye kansa. **6** Sai babban firist ya dauki kwandalolin
azurfar ya ce, "Ba daidai bane bisa ga shari'a musa
wannan cikin ma'aji, saboda kudin jini ne." **7** Sai suka
tattauna al'amarin a tsakanin su, kudin kuma suka
sayi filin maginin tukwane domin makabatar baki. **8**
Dalilin wannan ne ake kiran wurin, "Filin jini" har
yau. **9** Sai abin da aka fada ta bakin annabi Irmiya
ya cika, cewa, "Suka dauki tsabar azurfa talatin na
farashin da mutanen Isra'ila suka sa a kansa, **10** suka
bayar domin sayen filin mai tukwane, kamar yadda
Ubangiji ya umarce ni." **11** Sai Yesu ya tsaya a gaban
gwamna, gwamna ya kuma tambaye shi, "Kai sarkin
Yahudawa ne?" Yesu ya amsa, "Haka ka fada." **12**
Amma da manyan firistocin da dattawan suka zarge
shi, bai ce komai ba. **13** Sai Bilatus yace masa, "Baka ji
dukan zarge-zargen da ake yi maka ba?" **14** Amma bai
ce masa ko kalma guda ba, sai gwamna yayi matukar
mamaki. **15** To lokacin bikin idi, al'adar gwamna ne
ya saki mutum guda wanda jama'a suka zaba. **16** A
wannan lokacin suna da wani sanannen dan kurkuku
mai suna Barabbas. **17** To da suka tattaru, sai Bilatus
yace masu, "Wa kuke so a sakar maku? Barabbas, ko
Yesu wanda ake kira Almasihu?" **18** Saboda ya san
sun kawo shi ne domin kishi. **19** Da yake zaune a
kujerar shari'a, matarsa ta aika masa cewa, "Ka fita
sha'anin mutumin nan marar laifi. Saboda na sha
wahala sosai a yau cikin mafarki saboda shi." **20** A
lokacin nan manyan firistoci da dattawa suka rinjayi
ra'ayin jama'a suce a sakar masu da Barabbas, a kashe
Yesu. **21** Sai gwamna ya tambayesu, "Wa kuke so a
sakar maku?" Sukace, "Barabbas." **22** Bilatus yace

masu, "Me zan yi da Yesu wanda ake kira Almasihu?"
Sai duka suka amsa, "A gicciye shi." 23 Sai yace, "Don
me, wane laifi ya aikata?" Amma suka amsa da babbar
murya, "A gicciye shi" 24 Amma da Bilatus ya ga ba zai
iya komai ba don hargitsi zai iya barkewa, ya dauki
ruwa ya wanke hannuwansa a gaban jama'a, yace,
"Ba ni da laifi ga jinin mutumin nan marar laifi. Ku
yi abin da kuka ga dama." 25 Duka mutanen sukace,
"Bari jininsa ya kasance a kan mu da 'ya'yan mu." 26
Sai ya sakar masu da Barabbas amma yayi wa Yesu
bulala ya mika shi garesu domin su gicciye shi. 27
Sai sojojin gwamna suka dauki Yesu zuwa farfajiya
suka kuma tara dukan rundunar sojoji. 28 Suka yi
masa tumbur sa'annan suka sa masa jar alkyabba.
29 Sai suka yi masa rawanin kaya suka sa a kansa,
suka kuma bashi sanda a hannunsa na dama. Suka
rusuna a gabansa suna masa ba'a, suna cewa, "Ranka
ya dade, Sarkin Yahudawa!" 30 Suka kuma tofa masa
yawu, suka kwace sandar suka buga masa a ka. 31
Bayan sun gama masa ba'a, suka cire masa alkyabbar
suka sa masa kayansa, suka jagorance shi zuwa wurin
da za a gicciye shi. 32 Da suka fito waje, sai suka
iske wani Bakurame mai suna Saminu, wanda suka
tilasta ya tafi tare dasu domin ya dauki gicciyen. 33
Suka iso wani wuri da ake kira Golgotta, wanda ke
nufin,"Wurin kwalluwa." 34 Suka bashi ruwan inabi
da aka gauraya da wani abu mai daci. Amma da ya
'dan-'dana shi sai ya ki sha. 35 Bayan da suka gicciye
shi, suka kada kuri'a a kan rigarsa. 36 Suka kuma
zauna suna kallonsa. 37 A sama da kansa suka sa
abinda ake tuhumarsa da ita a rubuce, "Wannan shine
sarkin Yahudawa." 38 An gicciye shi da 'yanfashi guda
biyu, daya ta damansa dayan kuma ta hagunsa. 39
Wadanda suke wucewa suna zaginsa, suna girgiza kai,
40 suna kuma cewa, "Kai da kace zaka rushe haikali ka
kuma gina shi a kwana uku, ka ceci kanka mana! In
dai kai Dan Allah ne, ka sauko daga gicciyen!" 41 Ta
haka ma manyan firistocin suka rika yi masa ba'a,
tare da marubuta da shugabannin, suna cewa, 42 "Ya
ceci wasu amma ya kasa ceton kansa. Shi ne sarkin
Isra'ila. Ya sauko mana daga kan gicciyen, sai mu
ba da gaskiya gareshi. 43 Tun da ya yarda da Allah.
Bari Allahn ya cece shi mana, saboda yace, "Ni dan
Allah ne." 44 Hakan nan ma 'yanfashin guda biyu da
aka gicciye su tare suka zage shi. 45 To tun da tsakar
rana sai duhu ya rufe kasar gaba daya har karfe uku
na yamma. 46 Wajen karfe uku, Yesu ya tada murya
mai karfi yace, "Eli, Eli lama sabaktani?" wanda ke
nufin, "Allahna, Allahna, don me ka yashe ni?" 47 Da
wadanda suke tsaye kusa suka ji haka, sai sukace,
"Yana kiran Iliya." 48 Nan take wani ya ruga da gudu
ya dauki soso ya tsoma cikin ruwan inabi mai tsami
ya soka kan sandar kara ya mika masa ya sha. 49 Sai
sauran sukace, "Rabu da shi mu gani ko Iliya zai zo ya
cece shi." 50 Sai Yesu ya ta da murya mai karfi yayi
kuka sai ya saki ruhunsa. 51 Sai labullen haikali ya
yage gida biyu daga sama zuwa kasa. Kasa kuma ta
girgiza, duwatsu suka farfashe. 52 Kaburbura suka
bude, tsarkaka kuwa wadanda suke barci da yawa suka
tashi. 53 Suka fito daga kaburbura bayan tashinsa,
suka shiga birni mai tsarki suka bayyana ga mutane
da yawa. 54 Da hafsan sojan da wadanda suke kallon
Yesu suka ga girgizar kasar da abinda ya faru, suka
ji tsoro kwarai sukace, "Hakika wannan Dan Allah
ne" 55 Mata dayawa da suka bi Yesu daga Galili domin
su lura da shi suka tsaya suna kallo daga nesa. 56
A cikin su akwai Maryamu Magadaliya, Maryamu
uwar Yesu da Yusufu, da uwar 'ya'yan Zabadi. 57 Da
yamma sai wani attajiri mutumin Armatiya ya zo,
mai suna Yusufu wanda shi ma almajirin Yesu ne.
58 Ya je wurin Bilatus ya roka a bashi jikin Yesu. Sai
Bilatus ya umarta a bashi. 59 Yusufu ya dauki jikin,
ya rufe shi da likafani mai tsabta, 60 sai ya sa shi a
cikin sabon kabarinsa da ya sassaka cikin dutse. Sai ya
mirgina babban dutse a bakin kofar kabarin ya tafi. 61
Maryamu Magadaliya da dayan Maryamun suna nan
zaune akasin kabarin. 62 Washegari, wato bayan ranar
Shiri, Sai manyan firistoci da Farisawa suka taru tare
da Bilatus. 63 Sukace, "Mai gida, mun tuna lokacin
da mayaudarin nan yake da rai, yace, "Bayan kwana
uku zan tashi." 64 Saboda haka, ka bada umarni a
tsare kabarin na kwana uku. In ba haka ba almajiransa
zasu zo su sace shi, kuma su ce wa mutane, "Ya tashi
daga mattatu." Kuma yaudarar karshe zata fi ta farko
muni." 65 Bilatus yace masu, "Ku dauki masu tsaro.
Kuyi tsaro iyakar karfin ku." 66 Sai suka tafi suka tsare
kabarin, suka hatimce dutsen, suka sa masu tsaro.

28 Da daddare ranar Asabaci, rana ta fari ga mako
ta fara gabatowa, Maryamu Magadaliya da daya
Maryamun suka zo don su ziyarci kabarin. 2 Sai aka yi
girgizar kasa mai karfi, saboda mala'ikan Ubangiji ya
sauko daga sama ya kuma murgine dutsen ya zauna a
kai. 3 Kamanninsa kamar walkiya, tufafinsa kuma fari

fat kamar suno. 4 Masu tsaron suka razana don tsoro
suka zama kamar matattun mutane. 5 Mala'ikan ya yi
wa matan magana cewa, “Kada ku ji tsoro, nasan kuna
neman Yesu wanda aka gicciye. 6 Baya nan, amma ya
tashi kamar yadda ya fada. Ku zo ku ga wurin da aka
kwantar da shi. 7 Ku hanzarta ku gaya wa almajiransa,
'Ya tashi daga matattu. Duba, ya tafi Galili, can zaku
same shi.' Gashi ni kuwa na fada maku.” 8 Matan
suka yi hanzari suka bar kabarin da tsoro da murna,
suka ruga domin su sanar wa almajiransa. 9 Sai
ga Yesu ya tare su, yace masu, “A gaishe ku.” Sai
matan suka kama kafar sa, suka kuma yi masa sujada.
10 Sai Yesu yace masu, “Kada ku ji tsoro. Ku je ku
fada wa 'yan'uwana su je Galili. Can zasu ganni.” 11
Sa'adda matan suke tafiya, sai wadansu masu tsaro
suka shiga gari suka fada wa Shugabanin Firistoci
dukan abin da ya faru. 12 Firistocin suka hadu da
dattawa suka tattauna al'amarin, sai suka bada kudi
masu yawa ga sojojin 13 Sukace masu, “Ku gaya wa
sauran cewa, “Almajiran Yesu sun zo da daddare sun
sace gangar jikinsa lokacin da muke barci.” 14 Idan
wannan rahoto ya isa wurin gwamna, za mu lallashe
shi mu ja hankalinsa mu raba ku da damuwa.” 15 Sai
sojojin suka karbi kudin suka yi abinda aka umarcesu.
Wannan rahoto ya bazu a tsakanin Yahudawa, ya ci
gaba har zuwa yau. 16 Amma almajiran sha daya suka
tafi Galili, kan dutsen da Yesu ya umarcesu. 17 Da
suka gan shi, suka yi masa sujada, amma wadansu
suka yi shakka. 18 Yesu ya zo wurin su ya yi masu
magana, yace, “Dukan iko dake sama da kasa an ba
ni. 19 Sai kuje ku almajirantar da dukan al'ummai.
Kuna yi masu baftisma cikin sunan Uba da na Da da
na Ruhu Mai Tsarki. 20 Ku koya masu su kiyaye dukan
abin da na umarce ku. Duba, ni kuma kullum ina tare
da ku har karshen zamani.” (aiōn g165)

# Markus

1 Wannan itace farkon bisharar Yesu Almasihu, Dan
Allah. 2 kamar yadda aka rubuta cikin littafin
annabi Ishaya. Duba, ina aika manzona, a gabanka,
wanda zai shirya maka hanya. 3 Akwai murya mai
kira a jeji, tana cewa ka shirya hanyar Ubangiji. ka
daidaita ta. 4 Yahaya ya zo, yana baptisma acikin
jeji yana wa'azin tuba, domin gafarar zunubai. 5
Dukan kasar Yahudiya da mutanen Urshalima suka
zo wurin sa, a ka kuma yi masu baptisma a kogin
urdun. suna furta zunubansu. 6 Yahaya yana saye
da tufa ta gashin rakumi, yana kuma da damara ta
fata a kugunsa, abincinsa fara ce da zuma. 7 Yana
wa'azi, ya ce "akwai mai zuwa a bayana wanda ya ke
da iko fiye da ni. wanda ko maballin takalminsa ban
isa in kwance ba. 8 Ni ina yi maku baptisma da ruwa,
amma mai zuwa a bayana zai yi maku baptisma da
Ruhu Mai Tsarki". 9 Sai ya kasance a kwanakin nan
Yesu ya zo daga Nazarat ta Galili, sai Yahaya ya yi
masa baptisma a kogin urdun. 10 Sa'adda Yesu ya fito
daga ruwan, sai sama ta bude, sai Ruhu ya sauko a
bisansa da kamanin kurciya. 11 Sai wata murya ta zo
daga sama, tana cewa, "Kai kaunataccen Dana ne.
zuciyata ta na murna da kai kwarai". 12 Sai Ruhu
ya iza shi zuwa jeji. 13 Yana a jeji kwana arba'in,
Shaidan yana jarabtar sa. Yana cikin jeji da dabobi,
sai malaiku su ka yi masa hidima. 14 Bayan da aka
kama Yahaya, Yesu ya shiga kasar Galili yana wa'azin
bisharar Allah. 15 Yana cewa, "Lokaci ya yi, gama
mulkin Allah ya kusato. Ku tuba ku bada gaskiya ga
bishara". 16 Sa'adda ya ke wucewa a gefen takun
Galili, sai ya ga Saminu da Andarawus, dan'uwansa
suna jefa taru a teku, domin su masunta ne. 17 Yesu
ya ce masu ku zo, ku biyo ni, ni kuwa sai in maisheku
masuntan mutane". 18 Nan da nan suka bar tarun
su, suka bi shi. 19 Sa'adda Yesu ya yi tafiya kadan,
sai ya ga Yakubu dan Zabadi da Yahaya dan'uwansa;
suna gyaran tarunsu a jirgin ruwa. 20 Sai ya kira su,
su kuwa suka bar mahaifinsu Zabadi a jirgin ruwan da
ma'aikatansu, sai su ka bi shi. 21 Da su ka shigo cikin
kafanahum, a ranar asabar, Yesu ya shiga majami'a ya
koya masu. 22 Su ka yi mamakin koyarwarsa, domin
ya na koya masu da iko ba kamar marubuta ba. 23 A
nan cikin majami'a akwai wani mutum mai kazamin
ruhu, sai ya yi ihu da karfi. 24 Yana cewa Ina ruwan
mu da kai, Yesu Banazarat? Ka zo ne domin ka halakar
da mu? Na san wanene kai. Kai ne Mai Tsarki na
Allah". 25 Sai Yesu ya tsauta wa kazamin ruhun ya
ce, "Ka yi shiru ka fita daga cikinsa". 26 Bayan da
kazamin ruhun ya buga shi kasa, sai kazamin ruhun
ya yi ihu sa'annan ya fita daga jikinsa. 27 Sai dukan
mutanen su ka yi mamaki kwarai, suna tambayar
junansu menene wannan? wace sabuwar koyarwa ce
da iko haka? har yana umartar kazaman ruhohi suna
kuwa yi masa biyayya!" 28 Nan da nan labarinsa ya
bazu ko'ina a dukkan kewayen kasar Galili. 29 Bayan
da suka bar majami'a, sai su ka shiga gidan Saminu da
Andarawus, suna kuma tare da Yakubu da Yahaya. 30
Surikar Saminu tana kwance ba lafiya tana fama da
zazzabi. Sai suka gaya wa Yesu game da ita. 31 Sai ya
zo, ya kama hannunta, ya daga ta, sai zazzabin ya sake
ta, ta fara yi masu hidima. 32 Da yamman nan, bayan
da rana ta fadi, sai su ka kawo masa dukan marasa
lafiya da masu fama da aljanu. 33 Dukan mutanen
garin su ka taru a bakin kofa. 34 ya warkar da masu
ciwo da yawa da masu chututtuka iri-iri, ya kuma
fitar da bakaken aljanu, amma bai yarda aljanun su yi
magana ba domin sun san shi. 35 Ya tashi da sassafe,
tun da sauran dare, ya tafi wurin da ba kowa, a can ya
yi add'ua. 36 Saminu da wandanda suke tare da shi
suka neme shi. 37 Suka sa me shi, sai su ka ce masa,
"kowa yana nemanka". 38 Ya ce, bari mu tafi wani
wuri, zuwa wadansu garuruwan da ke kewaye, Saboda
in yi wa'azi a can kuma. Wannan shi yasa na zo nan".
39 Ya tafi dukan kasar Galili, yana wa'azi a majimi'un
su yana kuma fitar da aljanu. 40 Wani kuturu ya zo
wurinsa. Yana rokonsa, ya durkusa. Ya ce masa, "in ka
yarda kana iya warkar da ni. 41 Sai ya yi juyayi, Yesu
ya mi ka hannun sa ya ta ba shi ya na ce masa "Na
yarda. Ka sarkaka". 42 Nan da nan kuturtar ta barshi,
ya kuma sa mu tsarkakewa. 43 Yesu ya yi masa gargadi
sosai, ya salame shi. 44 Ya ce masa "ka tabbata fa kada
ka gayawa kowa, amma ka tafi ka nuna kanka ga firist,
sai ka je ka yi hadaya domin tsarkakewa kamar yadda
Musa ya umurta, domin shaida. 45 Amma da ya fita
sai ya fara gaya wa kowa, ya baza maganar a ko'ina,
har Yesu bai iya tafiya a sake a garin ba. Ya tafi ya
tsaya a wuraren da ba kowa, mutane kuwa su ka zo
wurinsa daga ko'ina.

2 Da ya dawo Kafarnahum bayan yan kwanaki kadan,
aka ji cewa yana gida. 2 Da yawa suka taru a can,
ba wuri har kofa, sai Yesu ya yi masu magana. 3 Sai

wadansu mutane su ka zo wurinsa dauke da wuni
mutum shanyayye, mutane hudu na dauke da shi.
4 Lokacin da ba su iya zuwa kusa da shi ba domin
yawan jama'a, sai su ka daye jinkar dakin daidai da
inda ya ke. Bayan da suka huda ramin suka saukar da
gado wanda shanyayyen ke kwance a kai. 5 Da ganin
bangaskiyarsu, Yesu ya ce wa shanyayyen mutumin,
"Da, an gafarta maka zunuban ka". 6 Amma wadansu
marubuta da ke zaune a nan, suka yi tunani aransu.
7 Yaya wannan mutum zai yi magana haka? Ya yi
sabo! wa ke iya gafarta zunubi "sai Allah kadai?"
8 Nan da nan Yesu ya sani a ruhunsa, abinda suke
tunani a tsakaninsu. Ya ce masu, "Me ya sa kuke
tunanin wannan a zuciyarku? 9 Me yafi sauki a cewa
shanyayyen mutumin, 'An gafarta maka zunuban
ka' ko kwa a ce masa, 'tashi, ka dauki shinfidarka,
ka yi tafiyarka'? 10 Amma domin ku san cewa Dan
mutum na da ikon gafarta zunubi a duniya, ya ce wa
shanyayyen, 11 ''Na ce maka, tashi, dauki tabarmanka,
ka tafi gidan ka." 12 Sai nan da nan ya tashi ya dauki
tabarmarsa, ya fita gidan a gabansu, dukansu su ka
yi mamaki, su ka girmama Allah, ''suka ce ba mu
taba ganin abu irin wannan ba." 13 Ya sake fita gefen
tafki, dukan taron jama'a suka zo wurinsa, sai ya
koya masu. 14 Sa'adda ya na wucewa, ya ga Levi dan
Halfa yana zaune a wurin karbar haraji, sai ya ce
masa, "Ka biyo ni." Ya tashi, ya bi shi. 15 Sa'adda
Yesu ya shiga gidan Levi yana cin abinci, masu karbar
haraji da masu zunubi da yawa su ka zo wurinsa
da almajiransa, jama'a masu yawan gaske suka ka
bi shi. 16 Da Marubuta wadanda su ke Farisawa,
sun ga cewa Yesu na cin abinci da masu zunubi
da masu karbar haraji, sai su ka ce wa almajiransa,
"Me ya sa ya ke ci da masu karbar haraji da mutane
masu zunubi?" 17 Da Yesu ya ji wannan ya ce masu,
"Mutane wadanda ke da lafiya a jiki ba su bukatar
likita; sai dai ko marasa lafiya ke bukatarsa. Ban zo
domin in kira mutane masu a dalci ba, amma mutane
masu zunubi." 18 Almajiran Yahaya da Farisawa suna
azumi, sai wadansu mutane suka zo suka ce, "Don
me almajiran Yahaya da almajiran Farisawa na azumi
amma na ka almajiran ba su yi?" 19 Sai Yesu yace
masu, "Abokan ango, za su yi azumi sa'adda ango
yake tare da su? muddin suna tare da ango ba za su yi
azumi ba. 20 Amma kwanaki za su zo da za a dauki
angon daga gare su, a wadancan kwanakin ne, za su
yi azumi. 21 Babu wanda zai dinka sabuwar riga ya
hada ta da tsohuwar riga, sai rigar ta yage, kuma ta
yi mummunar yagewa. 22 Babu wanda zai sa sabon
ruwan inabi a cikin tsohuwar salka, ai sai salkar ta
fashe kuma ruwan inabin ya zube. duka biyu ruwan
inabin da salkar arasa su. A maimakon haka, sai ka
sanya sabon ruwan inabi cikin sabuwar salka." 23
A ranar asabar Yesu ya tafi cikin gonakin hatsi, sai
almajiransa su ka fara zagar hatsi, 24 Sai Farisawa su
ka ce masa, "Duba, don me suke yin abin da bai dace a
yi ranar Asabar ba?" 25 Yace masu, Ba ku karanta ba
abinda Dauda ya yi sa'adda yake jin yunwa, shi da
mutanen da ke tare da shi? 26 Yadda ya shiga gidan
Ubangiji, sa'adda Abiyata ya ke babban firist, ya ci
gurasa da ke ta firist wadda bai dace wani ya ci ba sai
Firistoci. Har kuma ya ba wadanda ke tare da shi." 27
Yesu yace, "Asabar an yi ta don mutum ne, ba a yi
mutum don Asabar ba. 28 Saboda haka, Dan Mutum
Ubangiji ne, har da na Asabar."

3 Sai kuma ya sake tafiya cikin Majami'a sai ga
wani Mutum mai shanyayyen hannu. 2 Wadansu
mutane suna kallonsa sosai, su gani ko zai warkar
da shi a ranar Asabar. don su zarge shi. 3 Yesu ya
ce wa mai shanyayyen hanun "Ka tashi ka tsaya a
tsakiyar kowa." 4 Sai ya ce wa mutane, "Ya dace a
yi abu mai kyau aranar Asabar ko a yi mugunta; a
ceci rai, ko a yi kisa? "Amma suka yi shiru. 5 Sai ya
dube su cikin fushi, yana bakin ciki da taurin zuciyar
su, ya ce wa mutumin ka mikar da hanunka, sai ya
mikar da hanunsa Yesu kuwa ya warkar da shi. 6 Sai
Farisiyawa suka fita da sauri zuwa wurin mutanen
Hirudus suka shirya yadda za su kashe shi. 7 Sai
Yesu da almajiransa, suka tafi bakin teku. sai mutane
dayawa suka bi shi, daga Galili da Yahudiya 8 Daga
Urushalima da Edom gaba da Urdun da kewayan Taya
da Sidon, da baban taro, ya ji abinda yake yi. suka zo
wurinsa. 9 Ya tambayi almajiransa su shirya masa
karamin jirgin ruwa domin yawan mutane, domin
kada su murkushe shi. 10 Ya warkar da mutane da
yawa, yadda duk wadanda suke da cuttutuka suna
kokari su taba shi. 11 Duk sa'adda kazaman ruhohin
suka ganshi, sai su durkusa a gabansa su yi ihu da
karfi su ce, kai Dan Allah ne." 12 Ya umarce su da
karfi kada su sa a san shi. 13 Ya hau saman dutsen,
ya kira wadanda yake bukar su, su zo wurinsa. 14
Ya zabi guda goma sha biyu (ya kira su manzanni).
Wadanda zasu kasance tare da shi, ya kuma aike su,

su yi wa, azi, 15 Ya kuma basu Ikon fitar da aljanu.
16 Ya zabi guda goma sha biyu wato Saminu kuma
yaba shi suna Bitrus. 17 Yakubu dan Zabadi da Yahaya
dan-uwan Yakubu wanda ya basu sunan Buwanarjis
watau 'ya'yan tsawa, 18 da Andarawus da Filibus da
Bartalamawus da Matta da Toma da Yakubu dan Halfa,
da Taddawus da Saminu Ba-kananiye, 19 da Yahuza
Iskariyoti wanda zai bashe shi. 20 Sa'adda ya shiga
gida, Taron kuwa ya sake haduwa, har ya hana su cin
abinci, 21 Da iyalansa suka ji haka, sai suka fito sun
kamo shi, saboda sun ce, "Ai, baya cikin hankalinsa "
22 Marubutan da suka zo daga Urushalima suka ce
"Ai Ba'alzabuba ne ya hau shi, da ikon sarkin aljannu
kuma yake fitar da aljannu." 23 Yesu ya kirawo su
wurinsa ya ce da su cikin misalai, "Yaya shaidan zai
iya fitar da shaidan? 24 idan mulki ya rabu gida biyu
ba zai tsayawa ba. 25 Haka in gida ya rabu kashi biyu,
gaba da kansa bai zai tsaya ba. 26 Shaidan kuma in ya
tayar wa kansa ya rabu, ba zai iya tsayawa ba, gama
karshen sa ya zo kenan. 27 Amma ba mai iya shiga
gidan kakkarfan mutum ya kwace kayansa, ba tare
da ya fara daure kakkarfan mutumin ba, sa'an nan
kuma ya kwashe kayan gidansa. 28 Hakika, ina gaya
maku, dukan zunuban da mutane suka yi za a gafarta
masu, da kowane irin sabon da suka furta, 29 amma
fa duk wanda yayi sabon Ruhun Mai Tsarki baza a
gafarta masa ba ko kadan, ya zama mai zunubi har
abada." (aiōn g165, aiōnios g166) 30 "Yesu ya fadi wadannan
abubuwa domin suna cewa yana da ba kazamin ruhu,"
31 Sa'an nan uwatasa, da "Yan'uwansa suka zo suna
tsaye a waje. sai suka aika masa, suna kuma umurtar
sa ya zo. 32 Taro kuwa na zaune kewaye da shi, sai
suka yi magana da shi da cewa, ga uwarka da yan-
uwanka suna nan a waje, suna nemanka." 33 Ya amsa
masu, "Dacewa su wanene uwa-ta da "yan'uwa na? "
34 Sai ya waiwayi wadanda suke zaune kewaye da shi,
yace, "Ga uwa-ta da yan-uwana anan! 35 Gama duk
wanda ke yin abin da Allah yake so, shine dan'uwana
da yar, uwata, da kuma uwa-ta."

4 Ya kuma fara koyarwa a bakin teku. Akwai babban
taro kewaye da shi, sai ya shiga cikin jirgin ruwa
a cikin tekun, ya kuwa zauna. Duk taron kuwa na
kan tudu a bakin tekun. 2 Ya koya masu abubuwa
da yawa da misalai, a cikin koyawarsa ya ce masu, 3
"ku saurara! wani mai shuka ya tafi shuka. 4 Yana
cikin yafa iri, sai wadansu iri suka fadi a kan hanya,
tsuntsaye kuma suka zo suka tsince su. 5 Wadansu
kuma suka fadi a kan dutse inda ba kasa dayawa. Nan
da nan kuwa suka tsiro saboda rashin zurfin kasa. 6
Da rana fa ta daga, sai suka yankwane da yake ba su da
saiwa sosai, sai suka bushe. 7 Wadansu kuma suka fadi
cikin kayayuwa su ka yi girma sai kayayuwan suka
shake su, ba su yi tsaba ba. 8 Wadansu kuma suka fadi
a kasa mai kyau, suka yi yabanya, suka yi tsaba, suka yi
girma, wadansu ribi talattin wadansu sittin, wadansu
kuma dari". 9 Sai ya ce, Duk mai kunnen ji, ya ji," 10
Sa'adda Yesu yake shi kadai, wadanda suke kusa dashi
tare da sha biyun suka tambaye shi ma'anar misalan.
11 Sai ya ce masu, "ku an yardar maku, ku san asirin
mulkin Allah, amma ga wadanda ba su cikinku, komai
sai a cikin Misalai, 12 don gani da ido sun gani, amma
ba su gane ba. ji kuma, sun ji, amma ba su fahimta
ba, don kada su juyo a gafarta masu," 13 Ya ce masu,
"Ashe, ba ku fahimci wannan misalin ba? yaushe za
ku fahimci sauran? 14 Mai shukan nan fa maganar
Allah yake shukawa. 15 Wadanda suka fadi a hanyar
kuwa, su ne kwatancin wadanda. a aka shuka mganar
a zuciyarsu, Da suka ji, nan da nan sai shaidan ya zo
ya dauke Maganar da aka shuka a zuciyarsu. 16 Haka
kuma wadanda aka shuka a wuri mai duwatsu, sune
wadanda da zarar sun ji Maganar sai su karba da farin
ciki. 17 Su kuwa basu da tushe, ba su da karfi, idan
kunci ko tsanani ya zo saboda kalmar, nan da nan
sai su yi tuntube. 18 Wadansu kuma su ne kwatacin
wadanda suka fadi cikin kayayuwa, sune wadanda
suka ji Maganar, 19 amma abubuwan duniya, da rudin
dukiya da kuma kwadayin wadansu abubuwa, sukan
shiga su shake Maganar, har ta zama marar amfani.
(aiōn g165) 20 Wadanda aka shuka a kasa mai kyau
kuwa, sune kwatancin wadanda suke jin Maganar, su
karba, su kuma yin amfani da ita wadansu ribi talatin,
wadansu sittin, wadansu dari." 21 ya ce masu, "Shin,
ana kawo fitila a cikin gida don a rufe ta da kwando
ko a ajiye ta a karkashin gado? ku kan kawo ta ne
don ku dora ta a kan madorinta. 22 Ba abin da yake
boye, da baza a sani ba ko kuma ba abinda ke asirce
da bazaya bayyana a fili ba. 23 Bari mai kunnen ji,
ya ji!'' 24 Sai ya ce masu, ku mai da hankali a kan
abin da kuka ji, Mudun da ka auna, da shi za a auna
maka, har ma a kara maka. 25 Domin mai abu akan
karawa, marar abu kuma za a karba daga wurinsa a
kuma karawa mai shi." 26 Sai ya ce, "Mulkin Allah
kamar mutum yake mai yafa iri a kasa. 27 A kwana a

tashi har irin ya tsiro, ya girma bai kuwa san ta yaya
aka yi ba. 28 Kasa da kanta, takan ba da amfani, tsiro
shine ne na farko, 29 Sai kai, sa'anan sai kwaya mai
kwari. Sa, adda amfani ya nuna, sai ya sa lauje ya
yanke nan da nan, wato kaka ta yi kenan." 30 Ya kuma
ce, "Da me za mu kwatanta Mulki Allah? ko kuwa
da wane misali za mu misalta shi? 31 Kamar kwayar
zarra yake wadda, in an shuka ta, ko da yake ita ce
mafi kankanta cikin kwayoyi a duniya. 32 Duk da haka
in an shuka ta, sai ta yi girma fiye da duk sauran ita-
tuwan da ke a jeji tayi manyan rassa, har tsuntsaye su
iya yin sheka arassanta." 33 Da misalai da yawa, irin
wadannan ya yi masu Magana, dadai gwargwadon
ganewarsu, 34 ba ya fada masu kome sai da misali,
amma a kebe, yakan bayyana wa almajiransa dukan
abu. 35 A ranan nan da yama ta yi yace masu "Mu
haye wancan ketaren." 36 Sai suka bar taron, suka
tafi tare da shi acikin cikin jirgin. wadansu jirage
kuma na tare da shi. 37 Sai babban hadari da iska mai
karfi ya taso, rakuman ruwa kuma na ta girgizawa
cikin jirgin, har jirgin ya cika. 38 Yesu kuwa na daga
karshen bayan jirgin a kan kujera, yana barci, sai suka
tashe shi, suka ce masa "Malam za mu hallaka ba
ka kula ba?" 39 Sai ya farka, ya tsawata wa Iskar. Ya
kuma ce wa ruwan tekun, "Ka natsu! ka yi shiru!"
Sai Iskar ta kwanta, wurin duk ya yi shiru. 40 Ya ce
masu, "Don me kuka firgita haka? Har yanzu baku da
bangaskiya ne?" 41 Sai suka tsorata kwarai suka ce wa
juna, "wanene wannan kuma, wanda har Iska da teku
ma suke yi masa biyayya?"

**5** Da su ka zo daya ketaren tekun, wanda ya ke cikin
yankin Garasinawa. 2 Sa'adda Yesu ya sauko daga
cikin jirgin ruwan sai wani mutum mai aljanu ya fito
daga cikin kaburbura ya tarbe shi. 3 Mutumin yana
zama a cikin kaburbura. An daure shi da sarkoki da
mari 4 An daure shi da sarkoki da mari sau da yawa,
amma ya tsuntsunke sarkoki da marin. har ma ba
wanda zai iya daure shi kuma. 5 Dare da rana a cikin
kabarbarun da duwatsu mutumin ya na ihu ya na
yaiyage jikinsa da duwatsu masu kaifi. 6 Sa'adda ya
hango Yesu daga nesa, sai ya tarbi Yesu ya durkusa a
gabansa. 7 Ya tada muryarsa da karfi ya ce, ina ruwa
na da kai? Yesu Dan Allah Madaukaki Ina rokon ka da
sunan Allah kada ka bani wahala, 8 Gama Yesu ya ce
masa kai aljani ka fito daga cikinsa." 9 Ya tambaye
shi, "Yaya sunanka? Ya ce suna na tari gama muna da
yawa. 10 Ya yi ta rokonsa kada ya raba su da wannan
yankin kasar. 11 Akwai babban garken aladu a wurin
suna kiwo a gindin tsauni. 12 Sai suka roke shi ya
bar su su shiga cikin wadannan aladun. 13 Shi kuma
ya yardar masu. Aljanun suka fita suka shiga cikin
aladun su kimanin dubu biyu. Aladun dubu biyu suka
gangaro daga gindin tsaunin suka fada cikin ruwa. 14
Mutanen da ke kiwon aladun su ka shiga cikin gari da
kewaye suka bada labarin abin da ya faru. Mutane
da yawa suka je su ga abin da ya faru 15 Sai suka zo
wurin Yesu suka ga mutumin mai aljanun a zaune,
cikin hankalinsa, saye da tufafi, sai suka tsorata. 16
Wadanda suka zo su ka ga abin da ya faru da mutumin
mai aljanun, suka je suka fada wa mutane abin da
suka gani game da aladun. 17 Mutanen suka roke
shi ya fita daga yankin kasarsu. 18 Shi mutumin da
aljanu ke iko da shi, sa'adda ya ga Yesu zai shiga cikin
jirgin ruwa ya tafi, ya roki Yesu da ya bi shi. 19 Amma
Yesu bai yarda masa ba. Ya ce masa ka tafi gidanku,
wurin mutanenka ka gaya ma su alherin da Ubangiji
ya yi maka. 20 Mutumin ya shiga cikin Dikafolis yana
shaidar babban abin da Yesu ya yi masa, dukansu
suka cika da mamaki. 21 Sa'adda Yesu ya sake ketaren
kogin zuwa daya gefen, acikin jirgin, sai taron jama'a
suka keweye shi, a gefen tekun. 22 Sai wani daya daga
cikin shugabannin Majami'a mai suna Yayirus, ya zo,
wurinsa sa'adda ya ganshi ya durkusa a gabansa. 23
Ya yi ta rokonsa, yana cewa, "Diya ta ba ta da lafiya
har ma ta kusa mutuwa. Ina rokonka mu je gida na ka
dora ma ta hannu domin ta warke. ta rayu." 24 Sai ya
tafi tare da shi, babban taro suka biyo shi har ma suna
matse shi. 25 Akwai wata mace wadda ta ke zubar
jini ta kai tsawon shekara goma sha biyu. 26 Ta sha
wahala kwarai da gaske ta je wurin likitoci da yawa
ta kashe kudi sosai, amma ba ta warke ba abin ma
sai karuwa ya ke yi. 27 Ta ji labarin Yesu. Sai ta biyo
bayansa yana tafiya cikin taro, ta taba habar rigarsa.
28 Domin ta ce "Idan dai na taba ko da habar rigarsa
zan warke." 29 Da dai ta taba shi sai zubar jinin ta
ta tsaya, ta ji a jikin ta ta warke, daga damuwarta.
30 Nan da nan, Yesu ya ji iko ya fita daga gare shi
sai ya ce "wanene ya taba rigata?" 31 Almajiransa
suka ce, "a cikin wannan taron mutane da yawa ka ce
wanene ya taba ni?" 32 Amma Yesu ya waiga ya ga ko
wanene ya taba shi. 33 Matar ta san abin da ya faru
sai ta zo cikin tsoro da rawar jiki ta durkusa a gaban
Yesu ta fada masa gaskiya. 34 Sai ya ce da ita, "Diya

bangaskiyarki ta warkar da ke, ki tafi lafiya kin sami
warkewa daga cutarki". 35 Sa'adda ya ke magana da
ita sai ga mutane daga gidan shugaban majami'a suka
ce "Diyarka ta mutu me ya sa za ka dami malam?" 36
Amma sa'adda Yesu ya ji abin da suka ce, sai ya ce da
shugaban majami'ar, "kada ka ji tsoro ka ba da gaskiya
kawai." 37 Bai bari kowa ya kasance tare da shi ba sai
Bitrus da Yakubu da Yahaya dan'uwan Yakubu. 38
Suka zo gidan shugaban majami'ar ya ga mutane suna
bakin ciki, suna kuka sosai. 39 Sa'adda ya shiga gidan
ya ce da mutane "Me ya sa kuke damuwa da kuka?"
Yarinyar ba ta mutu ba barci ta ke yi. 40 Sai su kayi
masa dariya. Amma ya fitar da su waje su duka. Ya
kira baban yarinyar da mamar ta da wadansu da ke
tare da shi su ka shiga wurin da yarinyar ta ke. 41 Ya
kama hannun yarinyar ya ce da ita "Tilatha koum"
wato yarinya na ce ki tashi" 42 Nan da nan yarinyar ta
tashi ta yi tafiya [gama shekarun ta sun kai goma sha
biyu]. Nan da nan mutanen suka yi mamaki kwarai da
gaske. 43 Ya ummurce su da gaske kada kowa ya sani.
Ya ce da su su ba ta abinci ta ci.

**6** Ya bar su ya zo garinsu, almajiransa su ka biyo
shi. 2 Sa'adda ranar Asabar tazo ya shiga cikin
masujada ya yi koyarwa. Mutane da yawa da su ka
ji koyarwarsa su ka yi mamaki, suka ce daga ina ya
sami irin wannan koyarwar? Wacce irin hikima ce
Allah ya ba shi haka? Wadanne irin ayyukan al'ajibi
ya ke yi da hannuwansa? 3 Wannan ba kafintan nan
ba ne dan Maryamu, dan'uwan Yakubu da Yosi da
Yahuza da Saminu? Ba ga 'yan'uwan sa 'yan mata
mu na tare da su ba? Ba su ji dadi ba a ransu saboda
Yesu. 4 Yesu ya ce, "Annabi ba ya rasa daraja sai a
gidansa da garinsa da cikin danginsa." 5 Bai iya yin
wani aikin al'ajibi a wurin ba sai dai mutane kadan
marasa lafiya ya dorawa hannu ya warkar da su. 6
Rashin bangaskiyarsu ya ba shi mamaki. Sai ya tafi
cikin kauyuka na kewaye da su ya yi ta koyarwa.
7 Ya kira almajiransa su goma sha biyu, ya aike su
biyu-biyu, ya ba su iko a kan aljanu, 8 ya dokace
su kada su dauki komai tare da su domin wannan
tafiya, sai dai sanda kadai. Kada su dauki abinci ko
jaka ko kudi a cikin aljihunsu, 9 sai dai su sa takalmi
kadai, kada su sa taguwa biyu a jikinsu. 10 Ya ce
da su, idan ku ka shiga wani gida sai ku zauna a
gidan har lokacin da za ku tashi. 11 Idan ku ka je
wani gari aka ki karbar ku, ku karkabe kurar da ke
kafufunku ta zama shaida kan mutanen garin. 12
Sai suka tafi suka yi ta shela ga mutane cewa su
tuba daga zunubansu. 13 Sun fitar da aljanu da yawa,
suka shafawa mutane da yawa mai suka warkar da
su. 14 Sarki Hirudus ya ji wannan, gama sunan Yesu
ya zama sananne a wurin kowa da kowa. Wadansu
suna cewa Yahaya mai yin baftisma ne ya tashi daga
matattu shi ya sa ake yin wadannan ayyukan al'ajibi
ta wurinsa. 15 Wadansu kuma suna cewa, "Iliya," Har
yanzu wadansu suna cewa daya "daga cikin annabawa
ne na da can." 16 Sa'adda Hirudus ya ji wannan sai
ya ce, "Yahaya wanda na fillewa kai shine ya tashi."
17 Saboda Hirudus ne ya sa aka kama Yahaya aka
kulle shi a kurkuku saboda Hirodiya( matar Filibus
dan'uwansa), domin ya aure ta. 18 Saboda Yahaya
ya gaya wa Hirudus cewa bai halarta ya auri matar
dan'uwansa ba. 19 Sai ita Hirodiya ta yi kudurin ta
kashe Yahaya amma bai yiwu ba. 20 Domin Hirudus
yana jin tsoron Yahaya, domin ya sani shi mai adalci
ce, mai tsarki kuma. Domin haka Hirudus bai so
wani abu ya faru da Yahaya ba, amma ya kan fusata
idan ya ji wa'azin yahaya. Duk da haka da fari ciki
yakan saurare shi. 21 Amma sai dama ta samu inda
Hirodiya za ta iya yin abin da ta ke so ta yi. A lokacin
kewayowar ranar haihuwar sa, sai Hirudus ya shirya
liyafa domin manyan da ke aiki tare da shi a cikin
gwamnatin sa, da shugabannin da ke cikin Galili. 22
Diyar Hirodiya ta zo ta yi masu rawa, rawarta kuwa
tagamshi Hirudus da bakinsa. Sarki ya ce da yarinyar,
"ki tambayi duk abin da ki ke so ni kuwa zan ba ki
shi". 23 Ya rantse mata da cewa"Ko menene ki ka ce
ki na so, ko da rabin mulkina ne" 24 Sai ta fita ta je ta
tambayi mamarta, "me zan ce ya bani?" Sai ta ce kan
Yahaya Mai Yin Baftisma. 25 Sai ta dawo da sauri cikin
dakin taro wurin sarki ta ce da shi, "Ina so ka ba ni
kan Yahaya Mai Yin Baftisma a cikin tire." 26 Sarki ya
damu kwarai, amma saboda ya yi alkawari ga kuma
ofisoshinsa, ba dama ya ce a'a. 27 Sai sarki ya aiki wani
soja ya ba shi ummurni ya je ya kawo kan Yahaya.
Sojan ya je ya fillo kan sa daga cikin kurkuku. 28 Ya
kawo kan a cikin tire ya ba yarinyar, yarinyar kuma ta
kai wa mamarta. 29 Da almajiran su ka ji labari, suka
zo suka dauki gawarsa suka rufe a cikin kabari. 30
Almajiran suka zo wurin Yesu, suka fada masa dukkan
abin da suka yi da abin da suka koyar. 31 Sai ya ce da
su "ku je cikin kebabben wuri domin ku huta kadan,"
domin mutane suna ta kaiwa da komowa, ba su sami

damar hutawa ba balle su ci abinci 32 Sai suka tafi
kebabben wuri a cikin jirgin ruwa su kadai. 33 Amma
mutane da yawa sun gansu suna tafiya sun kuma gane
su, sai suka fito daga cikin dukan garuruwa da gudu
har su ka kai wurin kafin su zo. 34 Sa'adda suka zo
bakin gaba Yesu ya ga taron mutane da yawa sai ya
ji tausayinsu domin sun yi kamar tumakin da ba da
mai kiwo. Sai ya cigaba da koya masu abubuwa da
yawa. 35 Sa'adda yamma ta yi, almajiran sa suka zo
suka ce da shi, “wurinnan kebabben wuri ne kuma ga
lokaci ya tafi. 36 Ka sallami mutanen nan domin su
shiga cikin garuruwa da kauyuka da ke kusa domin
su sayi abin da zasu ci. 37 Amma sai ya ba su amsa
ya ce,”Ku ku basu abinci su ci mana”. Sai suka ce da
shi, “ma iya zuwa mu sawo gurasa ta sule dari biyu
mu basu su ci?” 38 Sai ya ce dasu, “Dunkulen gurasa
guda nawa kuke dasu? Kuje ku gani.” Dasuka gano sai
suka ce da shi, dunkule biyar ne da kifi guda biyu.” 39
Sai ya ba da umarni mutanen su dukka su zauna a
kan danyar ciyawa. 40 Suka zauna kungiya kungiya
wadansu su dari wadansu hamsin. 41 Sai ya dauki
dunkulen gurasa guda biyar da kifi guda biyu, ya ta
da kansa sama, yasa albarka, ya kakkarya dunkulen
gurasan, ya ba almajiran domin su rabawa taron
jama'a duka. 42 Dukansu suka ci suka koshi. 43 Suka
tattara gutsattsarin gurasar suka cika kwanduna guda
goma sha biyu da gutsattsarin da kuma gutsattsarin
kifin. 44 Mutanen da suka ci gurasar sun kai mutum
dubu biyar. 45 Nan da nan ya ce almajiran sa su hau
jirgin ruwa su yi gaba kafin ya zo, su je Baitsaida. Shi
kuma ya tsaya domin ya sallami taron mutanen. 46
Bayan da suka tafi shi kuma ya hau kan dutse domin
ya yi addu'a. 47 Har yamma ta yi jirgin ruwan ya na
tsakiyar rafi shi kuma yana kan tudu shi kadai. 48
Ya gansu suna wahala gama iska ta hana su tafiya.
Wajan karfe hudu na asuba sai ya tawo wurin su
yana tafiya a kan ruwa, yana so ya wuce gaban su. 49
Sa'adda suka gan shi ya na tafiya a kan ruwa suka yi
tsammani fatalwa ce, suka yi ihu, 50 gama su duka
sun gan shi, tsoro ya kama su. Sai nan da nan ya
yi magana dasu ya ce, “Ku karfafa ni ne! kada ku ji
tsoro!'' 51 Ya shiga cikin jirgin ruwan tare dasu, sai
iska ta dena bugawa. Sai suka yi mamaki kwarai. 52
Gama basu gane batun dunkulen ba. Maimakon haka,
sai zukatansu suka taurare. 53 Sa'adda suka haye su
zo kasar Janisarita suka sa wa jirgin sarka. 54 Su na
fitowa daga cikin jirgin kenan, mutane suka gane
cewa Yesu ne. 55 Mutane suka ruga cikin yankin su,
suka kawo marasa lafiya a bisa shinfidun su zuwa
wurinsa, dukan inda suka ji yana zuwa. 56 Ko ina ya
shiga birni da kauye, ko a cikin kasar sukan kawo
marasa lafiya a kasuwanni suna rokonsa su taba ko da
habar rigarsa, dukan wadanda suka taba kuwa suka
warke.

7 Farisawa suka taru wurin Yesu tare da wadansu
marubuta wadda suka zo daga Urushalima. 2 Sun
ga cewa wasu daga cikin almajiransa sun ci gurasa
da hannuwa marasa tsabta, wato, basu wanke hannu
ba, 3 (Domin Farisawa da dukan Yahudawa ba su
cin abinci sai dole sun wanke hannu da kyau domin
suna kiyaye al'adun dattawa. 4 Idan Farisawa suka
dawo daga kasuwa, wajibi ne su yi wanka kamin su ci
abinci. Akwai sauran al'adun da suke kiyayewa, kamar
wanke moda, tukwane, da wasu santula na dalma, har
da dakin cin abinci.) 5 Farisawa da Marubuta suka
tambaye Yesu, “Don me almajiran ka basu kiyaye
al'adun dattawa, domin suna cin abinci ba tare da
sun wanke hannu ba?” 6 Amma ya amsa masu cewa,
“Ishaya ya yi anabci akan ku masu bautan ganin ido,
da ya rubuta cewa 'wadanan mutane suna girmama
ni a baka amma zuciyar su tana nesa da ni. 7 Sujadar
wofi suke mani suna koyar da ka'idodi na mutane a
matsayin rukunansu'”. 8 Kun watsar da dokar Allah
sai kuka rungumi al'adun mutane. 9 Sai yace masu,
kun yi nasara wurin kau da dokokin Allah domin ku
kiyaye al'adun ku na mutane. 10 Koda shike Musa ya
rubuta cewa, “ka girmama Ubanka da Uwarka”, kuma,
“duk wanda ya zagi Ubansa ko Uwatasa, ya cancanci
mutuwa nan take”. 11 Amma kun ce, 'idan mutum
ya ce wa iyayensa, “duk taimakon da ya cacanci ku
samu daga guna ya zama kebabbe (wato, 'na mika wa
Allah)”'. 12 Sabo da haka, kun ba shi izini kada ya yi
wa Ubansa ko Uwatasa wani abu. 13 Kuna mayar da
dokan Allah abin banza, sabili da al'adun ku da kuka
mika masu. Wannan, da wasu abubuwa kamar haka
kuke yi.” 14 Ya kara kiran taron jama'ar yace masu,
“ku kasa kunne gareni, kuma ku gane. 15 Babu wani
abu daga wajen mutum da zai iya gurbatar da shi
har idan ya shiga cikinsa. Amma, abinda ya fita daga
cikinsa shike gurbatar da shi” 16 Bari mai kunnen ji,
ya ji. 17 Da Yesu ya bar taron jama'ar, ya shiga gida,
sai almajiransa suka tambaye shi ma'anar wannan
misali. 18 Sai Yesu yace, 'ashe baku da ganewa? ko

baku sani cewa abin da ya shiga cikin mutum daga
waje ba zai iya gurbatar da shi ba, 19 domin ba zai
iya kai wa cikin zuciyarsa ba, sai dai ya shiga cikin
sa ya kuma fita a matsayin bayan gari a salga". Da
wannan magana, Yesu ya mayar da dukan abinci ya
zama da tsabta. 20 Ya ce, abinda ke cikin mutum shike
gurbatar da shi 21 Domin daga cikin mutum, kuma
daga cikin zuciyarsa ne, mugun tunani, lalata, sata,
kisa, 22 zina, kwadayi, mugunta, hai'inci, mugun guri,
kishi, zargi, girmankai, wawanci. 23 Duk wadannan
miyagun abubuwa suna fitowa ne daga cikin mutum,
kuma suke gurbatar da shi." 24 Ya tashi daga nan ya
tafi shiyyar Sur da Sida. Ya shiga wani gida don baya
son wani ya sani cewa yana nan, amma bai iya boyuwa
ba. 25 Amma nan da nan wata mace, wadda diyarta
ke da mugun ruhu-wannan mace kuwa ta ji game da
Yesu sai ta zo ta durkusa a gabansa. 26 Matar yar kasar
Girka ce, kuma asalinta daga Fonishiya take. Ta roke
shi da ya fitar da mugun ruhun nan daga diyarta. 27
Sai ya ce mata, "Bari a ciyar da 'ya'ya tukuna. Domin
bai kamata a dauki abincin yaya a ba karnuka ba". 28
Sai ta amsa masa cewa, "I, Ubangiji, Karnukan ma
sukan ci abincin da ke fadowa daga teburin 'ya'yan."
29 Ya ce mata, "domin kin fadi haka, kina iya ki tafi
domin aljani ya fita daga diyarki." 30 Ta koma gida sai
ta iske diyarta na kwance akan gado, aljanin ya fice
daga jikinta. 31 Ya sake fita daga shiyar Sur, ya biyo
ta Sidon, har zuwa tekun Galili a shiyar Dikafolis. 32
Sun kawo masa wani kurma, kuma bebe ne shi, suna
rokansa ya dora hanuwansa a bisansa. 33 Sai ya jawo
shi daga taron jama'ar, zuwa gefe, sai ya sa hanunsa a
kunuwan beben bayan ya tufa yawunsa, sannan ya
taba harshensa. 34 Ya dubi sama, ya ja numfashi ya ce
masa, "Ifatha", wato, "bude!" 35 Nan da nan ya mayar
masa da jinsa. abinda ya daure harshensa ya sake shi,
sai ya fara magana da kyau. 36 Ya umarce su da kada
su gaya wa wani. Amma duk da umarnin da yake basu,
suna ta shaida shi ko'ina. 37 kuma suna ta mamaki
cewa, "Yayi kowanne abu da kyau, har ya sa kurame
suna jin magana, da kuma bebaye na magana."

8 A kwanakin nan, akwai wani gagaruman taron
mutane, kuma basu da abincin ci. Yesu ya kirawo
almajiransa yace masu, 2 "Ina tausayin taron mutanen
nan domin kwana uku kenan suna nan tare da ni
babu abinci. 3 Idan na salame su su koma gidajensu
ba tare da sun ci abinci ba, za su galabaita a hanya
domin gidajensu na da nisa." 4 Almajiransa suka
amsa masa cewa, "A ina za mu iya samu gurasa a
wannan jeji da zai ishi wadannan mutane haka?" 5
Ya tambaye su, "gurasa nawa kuke da su?" Sai suka
ce, "Bakwai." 6 Ya umarci mutanen da su zauna.
Ya dauki gurasar bakwai, bayan da ya yi godiya, ya
kakarya gurasar, sa'annan ya umarci almajiransa da
su raba wa mutanen. Su kuwa suka raba masu. 7 Suna
kuma da kananan kifaye kadan. Bayan da ya yi godiya
akan su, ya umurci almajiran su rabawa mutanen. 8
Sun ci sun koshi. Suka tattara ragowar, har sun cika
kwanduna bakwai. 9 Akwai maza kimanin dubu hudu
a wurin. Yesu ya sallame su. 10 Nan take, ya shiga
jirgin ruwa da almajiransa zuwa shiyyar Dalmanuta.
11 Sai Farisawa suka zo suka fara gardama da shi.
Suna nema ya nuna masu alama daga sama, domin su
gwada shi. 12 Ya ja numfashi a ruhunsa yana cewa,
"Don me wannan tsarar tana neman alama. Hakika
ina gaya maku, babu wata alama da za a ba wannan
tsarar." 13 Sai ya bar su ya sake shiga jirgin zuwa
hayin tafkin. 14 A lokacin nan, almajiransa sun manta
su dauki gurasa. Domin gurasa daya ce tak a garesu
cikin jirgin ruwan. 15 Ya gargade su, "ku yi hattara da
yisti na Farisawa da Yisti na Hirudus." 16 Almajiran
suka fara tattaunawa a tsakaninsu, "Saboda ba mu da
gurasa ne." 17 Yesu yana sane da wannan, sa'annan
ya ce masu, "Don me kuke tattaunawa akan rashin
gurasa? Har yanzu baku gane ba? Har yanzu ba ku da
sane? Ko zuciyar ku ta duhunta ne?" 18 Kuna da idanu,
ba ku gani? Kuna da kunnuwa, ba ku ji? Ba ku tuna
ba? 19 Da na kakkarya gurasar a cikin mutane dubu
biyar, kwanduna nawa kuka samu ragowa? Suka ce
masa, "Goma sha biyu." 20 Kuma da na kakarya gurasa
bakwai a cikin mutane dubu hudu, kwanduna nawa
kuka dauka cike da ragowar? Suka ce masa, "bakwai."
21 Ya ce masu, "har yanzu baku gane ba?" 22 Sun
zo Baitsaida. Mutanen wurin suka kawo masa wani
makaho, sai suka roke shi ya taba shi. 23 Yesu ya rike
hanun makahon, ya jagorance shi zuwa bayan kauyen.
Da ya tofa yawunsa a idon mutumin, kuma ya dora
hanunsa akan mutumin, sai ya tambaye shi "kana
ganin wani abu kuwa?" 24 Ya daga ido sai ya ce, "ina
ganin mutane na tafiya kamar itatuwa." 25 Ya sake
dora masa hannu a idanuwansa, mutumin ya bude
idanuwansa, sai ya fara ganin gari da kyau. 26 Yesu
ya sallame shi zuwa gidansa nan take, ya ce masa,
"kada ka shiga cikin garin" 27 Yesu da almajiransa

sun shiga kauyukan kaisariya ta Filibi. Da suke kan
hanya, sai ya tambaye su, “Shin wanene mutane ke
ce da ni?” 28 Suka amsa masa suka ce, Yahaya mai
Baftisma. Wasu suka ce, “Iliya”. wadansu kuma, 'Daya
daga cikin anabawa”. 29 Ya tambaye su, “Amma me ku
ke ce da ni?” Bitrus ya ce, “Kai ne Almasihu.” 30 Yesu
ya umarce su kada su gaya wa kowa game da shi. 31
Sai ya fara koya masu cewa, dole ne Dan Mutum ya
sha wahala, dattawa da marubuta da manyan Firistoci
zasu ki shi, a kuma kashe shi. Bayan kwana uku, zai
tashi daga matattu. 32 Ya fadi wannan afili. Sai Birus
ya ja shi gefe ya fara tsauta masa. 33 Amma Yesu ya
juya ya dubi almajiransa sa'annan ya tsautawa Bitrus
yana cewa, “Ka koma bayana Shaidan, domin kana
kula da abubuwan mutane ne kawai, ba na Allah ba.”
34 Sai ya kira taron jama'ar da almajiransa a wuri
daya, ya ce masu, “Duk wanda yake so ya bini, dole
ne ya musunci kansa, ya dauki giciyensa ya biyo ni.
35 Domin duk wanda yake so ya ceci ransa zai rasa
shi, amma duk wadda ya rasa ransa domina da kuma
bishara zai cece shi. 36 Me zai amfani mutum idan
ya sami dukan duniya sannan ya rasa ransa. 37 Me
mutum zai bayar amaimakon ransa? 38 Duk wanda ke
jin kunyata ko maganata a wannan mazinaciyar tsara
mai zunubi, Dan Mutum ma zai ji kunyarsa a lokacin
da ya dawo cikin daukakar Ubansa da Malaiku masu
tsarki.”

9 Sai ya ce masu, “Hakika, ina gaya maku, akwai
wasun ku anan da ba za su mutu ba, sai sun ga
mulkin Allah ya bayyana da iko.” 2 Bayan kwana shida
Yesu ya dauki Bitrus, da Yakubu, da Yahaya, ya kai su
kan wani dutse mai tsawo, su kadai. Sai kamaninsa ya
sake a gabansu. 3 Sai tufafinsa ya zama fari fat, yadda
ba mai rinin da zai iya rininsa haka a duniya. 4 Sai
Iliya da Musa suka bayyana gare su, suna magana da
Yesu. 5 Sai Bitrus ya amsa ya ce, malam, bari mu da
muke anan mu kafa bukka uku, daya ta ka, daya ta
Musa, da ta Iliya, 6 Ya rasa abin da zai fada ne, don
sun tsorota kwarai.) 7 Sai ga wani gajimare ya zo ya
rufe su, aka kuma ji wata murya daga gajimaren, “ta
ce Wannan shine kaunataccen Dana, Ku saurare shi. 8
Nan take da suka duba, ba su ga kowa ba, sai Yesu shi
kadai. 9 Suna cikin gangarowa daga dutsen, sai ya
kwabe su kada su gaya wa kowa abin da suka gani, sai
bayan da Dan Mutum ya tashi daga mattatu. 10 Sai
suka bar zancen a tsakaninsu, amma suka tamabayi
junansu “mene ne tashin matattu” ke nufi. 11 Suka
tambaye shi yaya malaman attaura suka ce Iliya zai
fara zuwa?” 12 Ya ce masu, laile ne Iliya ya fara zuwa
ya raya dukan abubuwan. Don me a ka rubuta cewa
Dan Mutum, zai sha wuya iri iri a kuma ki shi? 13
Amma ina gaya muku Iliya ya riga, ya zo, amma sun
yi masa abin da suke so su yi kamar yadda littatafai
suka yi magana a kansa.” 14 Sa'adda suka dawo wurin
sauran almajiran, suka ga taron jama'a masu yawa
suna ta muhawara tare da manyan malaman attaura.
15 Da ganin sa, sai dukan taron yayi mamaki kwarai
da gaske, suka dungumo wurinsa a guje, suna gaishe
shi. 16 Ya tambayi almajiransa, “Wacce muhawara
ce kuke yi da su?” 17 Daya daga cikin taron ya amsa
masa”malam, ga shi na kawo maka dana don yana
da beben aljani. 18 Duk lokacin da ya tasar masa
yakan buga shi har kasa, na kuma yi wa almajiranka
magana su fitar sun kasa. 19 Ya amsa masu ya ce ya ku
mutanen zamaninnan marasa bangaskiya, har yaushe
zan kasance tare da ku ina jimrewa? ku dai kawo mini
shi. 20 Sai suka kawo masa yaron. Da ruhun ya ga
Yesu, nan da nan ya buge yaron jikinsa na rawa. Sai
yaron ya fadi yana ta birgima, bakinsa yana kumfa. 21
Yesu ya tambayi mahaifin yaron, Tun yaushe wannan
abu ya same shi? Mahaifin yaron ya ce tun yana
karami. 22 Ya kuwa sha jefa shi a ruwa da wuta, don
ya halakar da shi. Idan zaka iya yin wani abu, ka ji
tausayinmu ka taimakemu. 23 Yesu ya ce masa, “In
zan iya? Ai dukan abu mai yiwuwa ne, ga duk wanda
ya gaskata. 24 Nan da nan mahaifin yaron ya daga
murya ya ce, Na ba da gaskiya. A kore mini rashin
bangaskiyata. 25 Da Yesu ya ga taron na dungumowa
a guje, sai ya tsawata wa bakin aljanin ya ce masa,
“kai, beben aljani na umarce ka, ka fita daga wannan
yaron kar ka sake shigar sa. 26 Sai wannan aljanin ya
daga murya ya fita ya rabu da wannan yaron. Sai yaro
ya zama kamar mattacce, sai sauran mutanen suka ce,
“Ai, yaron ya mutu. 27 Yesu ya kama hannunsa, ya
daga shi, sai yaron ya mike tsaye. 28 Da Yesu ya shiga
gida, sai almajiransa suka tambaye shi a kadaice, me
ya sa muka kasa fitar da shi?” 29 Ya ce masu, “Ai, irin
wannan ba ya fita sai da addu'a.” 30 Sai suka ratsa
cikin Galili, amma ba ya son kowa ya san inda suke. 31
Da yake koyar da almajiransa, ya ce masu lokaci na
zuwa da za'a ba da Dan mutum a hannun mutane,
za su kuwa kashe shi, sa'adda aka kashe shi kuma,
bayan kwana uku zai tashi. 32 Amma fa ba su fahimci

maganar ba, suna kuma jin tsoron tambayarsa. 33 Sai
suka zo kafarnahum. A lokacin da ya ke cikin gida, ya
tambayi Al'majiransa, Menene ku ke magana a kansa
a hanya? 34 Amma suka yi shiru. don suna gardama
da junansu akan hanya, a kan wane ne mafi girma.
35 Sai ya zauna, ya kira al'majiransa goma sha biyu,
yace masu duk wanda ya ke so ya zama na fari, dole
ya kankantar da kansa, sa'annan ya bautawa sauran
duka. 36 Sai ya dauko karamin yaro a hannunsa ya sa
shi a tsakiyarsu. Ya rumgome shi a kafadarsa ya ce
masu. 37 Dukan wanda ya karbi dan karamin yaron
nan a cikin sunana ni ya karba, kuma dukan wanda ya
karbi wani, ni ya karba, bai kuma karbeni ni kadai ba,
duk da wanda ya aiko ni." 38 Sai Yahaya ya ce masa,
Malam mun ga wani yana fitar da aljanu da sunanka
mun yi kokari mu hana shi domin ba ya tare da mu.
39 Sai Yesu ya ce masu ku kyale shi domin babu wanda
zai yi irin wannan babban aikin, sa'annan ya fadi wasu
maganganu mara sa kyau a kanmu. 40 Duk wanda ba
ya gaba da mu, na mu ne. 41 Duk wanda ya ba ku ruwa
ku sha domin kuna na Almasihu, gaskiya nake fada
maku ba za ya rasa ladansa ba. 42 Amma duk wanda
ya sa kananan nan tuntube, ya fi kyau a rataya masa
dutsen nika a jefa shi a cikin teku. 43 Idan har hannun
ka zai sa ka yi tuntube, zai fi kyau ka yanke shi. Domin
zai fi kyau ka shiga aljanna da hannu daya da ka
shiga jahannama da hannu biyu. (Geenna g1067) 44 (Inda
tsutsotsi basu mutuwa, wutar kuma bata mutuwa). 45
Idan kafarka za ta sa ka yi tuntube, ka yanke ta ka
yar. Zai fi kyau ka shiga aljanna da kafa daya da ka
shiga jahannama da kafa biyu. (Geenna g1067) 46 (Inda
tsutsotsi basu mutuwa, wutar kuma bata mutuwa).
47 Idan idonka zai sa ka yi tuntube, ka kwakule shi
ka yar, domin gwamma ka shiga mulkin Allah da ido
daya, da a jefa ka cikin wuta da idanu biyu. (Geenna
g1067) 48 Inda tsutsotsi basu mutuwa, wutar kuma bata
mutuwa. 49 Domin da wuta za a tsarkake kowa. 50
Gishiri yana da kyau, amma idan ya rasa zakinsa, ta
ya ya za ka sa shi yayi zaki kuma? Ku kasance da zaki,
kuma ku yi zaman lafiya da kowa.

**10** Yesu ya bar wannan wurin, ya tafi yankin
Yahudiya, wajen hayin kogin Urdun. Sai jama'a
suka je wurinsa. Ya ci gaba da koya masu, kamar yadda
ya zama al'adarsa. 2 Sai Farisawa su ka zo wurinsa, su
ka ce, '' dai dai ne mutum ya saki matarsa?'' Wannan
tambaya sun yi ta ne domin su gwada shi. 3 Ya amsa
ya ce, menene Musa ya umarce ku? 4 Suka ce, ''Musa
ya yarda mutum ya rubuta takardar saki ga matarsa,
ya sallameta ta fita.'' 5 "Domin taurin zuciyarku ne
ya rubuta maku wannan dokar," Yesu ya ce masu.
6 Amman tun daga farkon halitta, 'Allah ya halicci
namiji da ta mata.' 7 Domin wannan dalilin ne mutum
zai rabu mahaifinsa da mahaifiyarsa ya mannewa
matarsa. 8 Su biyu kuwa sun zama jiki daya, ba biyu
ba, 9 Saboda haka abinda Allah ya hada kada mutum
ya raba." 10 Lokacin da suke cikin gida, sai almajiransa
suka sake tambayarsa akan wannan magana. 11 Ya ce
da su. Dukan wanda ya saki matarsa ya kuma auro
wata matar yayi zina da ita kenan. 12 Haka nan duk
matar da ta saki mijinta ta auri wani ta yi zina da
shi kenan." 13 Mutane suka kawo masa 'ya'yansu
kanana don ya taba su, sai almajiransa suka kwabe
su. 14 Da Yesu ya gani, ya ji haushi, ya ce masu.
Ku bar yara kanana su zo wurina, kada ku hana su
domin mulkin Allah na irinsu ne. 15 Gaskiya na ke
fada maku duk mutumin da bai karbi mulkin Allah
kamar karamin yaro ba, babu shakka ba zai shiga
mulkin Allah ba. 16 Sai ya rungume su ya sa masu
albarka. 17 Lokacin da ya fara tafiya, sai wani mutum
ya rugo wurinsa, ya durkusa a gabansa. Ya tambaye
shi, yace ya ''Malam managarci, me zan yi domin in
sami rai na har abada?'' (aiōnios g166) 18 Amma Yesu
ya ce masa. Don me ka ke kira na managarci? Babu
wani managarci sai dai Allah kadai. 19 Kasan dokokin.
Kada ka yi kisan kai, kada ka yi zina, kada ka yi sata,
kada ka yi shaidar zur, kada ka yi zamba, ka girmama
mahaifinka da mahaifiyarka." 20 Sai mutumin ya ce
masa Malam ai na kiyayye duk wadannan abubuwa
tun ina yaro. 21 Yesu ya dube shi duban kauna ya
ce masa. Abu daya ka rasa. Shi ne ka je ka sayar da
duk mallakarka ka ba mabukata, za ka sami wadata a
sama. Sa'annan ka zo ka bi ni. 22 Da ya ji haka sai
ransa ya baci, ya tafi yana bakin ciki, don shi mai
arziki ne kwarai. 23 Yesu ya dubi almajiransa ya ce.
''Yana da wuya masu arziki su shiga mulkin Allah!'' 24
Almajiransa suka yi mamakin maganarsa. Sai Yesu ce
masu, ya ku ya'ya'na yana da wuya kamar me a shiga
mulkin Allah. 25 Zai zama da sauki ga rakumi yabi ta
kafar allura da mai arziki ya shiga mulkin Allah. 26 Sai
suka cika da mamaki sosai, su kace wa juna, ''to idan
haka ne wanene zai iya tsira kenan?'' 27 Yesu ya dube
su ya ce masu. Ga mutane a bu ne mai wuyar gaske,
amma a wurin Allah komai yiwuwa ne. 28 Bitrus ya ce

masa, ''to gashi mu mun bar kome, mun bika''. 29 Yesu
ya ce. Gaskiya na ke fada maku, babu wanda zai bar
gidansa, da yan'uwansa maza da mata, da mahaifiya
ko mahaifi, ko 'ya'ya ko gona, saboda da ni da kuma
bishara, 30 sa'annan ya rasa samun nikinsu dari a
zamanin yanzu, na gidaje, da yan'uwa mata da maza'
da iyaye mata da 'ya'ya da gonaki, game da tsanani, a
duniya mai zuw kuma ya sami rai madawwami. (aiōn
g165, aiōnios g166) 31 Da yawa wadanda suke na farko
za su koma na karshe, na karshe kuma za su zama
na farko. 32 Suna tafiya Urushalima, Yesu kuwa na
gabansu. Almajiransa sun yi mamaki, mutane da ke
biye da su kuwa sun tsorata. Yesu kuwa ya sake kebe
sha biyun nan, ya fara fada masu abin da zai same shi.
33 "Kun ga, za mu Urushalima za a bada Dan mutum
ga manyan Firistoci da malan Attaura, za su kuma yi
masa hukuncin kisa su kuma bada shi ga al'ummai.
34 Za su yi masa ba a, su tofa masa yau, su yi masa
bulala, su kashe shi, bayan kwana uku kuwa zai tashi."
35 Yakubu da Yahaya, 'ya'yan Zabadi, suka zo wurin sa,
suka ce, ''Malam muna so kayi mana duk abin da mu
ka roke ka'' 36 Ya ce masu. ''Me ku ke so in yi maku?''
37 Suka ce, ''ka yardar mana, a ranar daukakarka, mu
zauna daya a damanka, daya kuma a hagunka.'' 38
Yesu ya ce masu. ''Ba ku san abinda ku ke roka ba.
Kwa iya sha daga kokon da zan sha? Ko kuma za a yi
maku baftismar da za a yi mani?'' 39 Suka fada masa,
''Zamu iya.'' Yesu ya ce masu, '' kokon da zan sha, da
shi zaku sha, baftismar da za ayi mani kuma da ita za
a yi maku.'' 40 Amma zama a damata, ko a haguna, ba
na wa ba ne da zan bayar, ai na wadanda a ka shiryawa
ne." 41 Da sauran almajiran nan goma suka ji, suka
fara jin haushin Yakubu da Yahaya. 42 Yesu kuma ya
kira su wurinsa ya ce masu, '' kun sani wadanda aka
san su da mulkin al'ummai sukan nuna masu iko,
hakimansu kuma sukan gasa masu iko. 43 Amma ba
haka zai kasance a tsakaninku ba. Duk wanda ya ke
son zama babba a cikinku, lalle ne ya zama baranku.
44 Duk wanda ya ke so ya shugabance ku lalle ne ya
zama bawan kowa. 45 Saboda haka ne Dan mutum ya
zo ba domin a bauta masa ba, sai dai domin shi yayi
bautar, ya kuma ba da ransa fansa saboda da mutane
da yawa." 46 Sa'adda suka iso Yariko, yana fita daga
Yariko kenan, shi da almajiransa, da wani babban taro,
sai ga wani makaho mai bara, mai suna Bartimawas
dan Timawas yana zaune a gefen hanya. 47 Da ya ji
Yesu Banazare ne, ya fara daga murya yana cewa, ''Ya
Yesu, Dan Dauda, kaji tausayina'' 48 Mutane da yawa
suka kwabe shi, cewa yayi shiru. Sai ya kara daga
murya kwarai da gaske, yana cewa, Ya Dan Dauda ka
yi mani jinkai, ka ji tausayina!" 49 Yesu ya tsaya ya ce,
ku kirawo shi. Su kuwa suka kirawo makahon suka ce
masa. ''Albishrinka, ta so! Yana kiranka.'' 50 Makahon
ya yar da mayafinsa, ya zaburo wurin Yesu. 51 Yesu
ya tambaye shi, ya ce, '' me ka ke so in yi maka?''
Makahon ya ce, ''Malam in sami gani.'' 52 Yesu ya ce
masa. ''Yi tafiyarka, bangaskiyarka ta warkar da kai.''
Nan take idanunsa suka bude, ya bi Yesu, suka tafi
tare.

11 Da suka kusa Urushalima, kusa da Betafaji, da
Betanya, wajen dutsen zaitun, sai Yesu ya aiki
almajiransa biyu 2 ya ce masu, "ku shiga kauyen can
kusa da mu. Da zarar kun shiga za ku ga aholaki a
daure, wanda ba a taba hawa ba. Ku kwance shi, ku
kawo mani. 3 In wani ya ce maku, "Don me kuke
haka? ku ce, 'Ubangiji ne yake bukatarsa, zai kuma
komo da shi nan da nan."' 4 Sai suka tafi, suka tadda
aholakin a daure a kofar gida a bakin hanya, suka
kwance shi. 5 sai wadanda suke tsaye a gun suka
ce masu, "Don me kuke kwance aholakin nan? 6
Suka fada masu abinda Yesu yace, sai suka kyale su
suka tafi. 7 Almajiran nan biyu suka kawo wa Yesu
aholakin, suka shimfida mayafansu a kai, sai ya hau.
8 Sai mutane da yawa suka shimfida mayafansu a
hanya, wadansu kuma suka baza ganyen da suka
yanko daga filayen. 9 Wadanda suke gaba da shi da
wadanda ke bin bayansa suka yi sowa suna cewa,
"Hosanna! Albarka ta tabbata ga mai zuwa cikin sunan
Ubangiji. 10 Albarka ta tabbata ga mulkin nan mai
zuwa na Ubanmu Dawuda! Dukaka a cikin sama!" 11
San nan Yesu ya shiga Urushalima, ya shiga Haikalin.
Sai ya dudduba komai, da magariba ta yi, ya fita ya
tafi Betanya tare da goma sha biyu nan. 12 Kashe gari,
suka tashi daga Betanya, sai ya ji yunwa. 13 Da ya
hango itacen baure mai ganye daga nesa sai ya je ya
ga ko za sami 'ya'ya. Da ya iso wurinsa bai ga komai ba
sai ganye, don ba lokacin 'ya'yan baure ba ne. 14 Sai ya
ce wa bauren, "Kada kowa ya kara cin ''ya'yanka har
abada!" Almajiransa kuwa sun ji maganar. (aiōn g165) 15
Suka iso Urushalima, da shigar su, ya kori masu saye
da sayarwa, ya watsar da taburan 'yan canjin kudi, da
kujerun masu sayar da tantabaru. 16 Ya hana kowa ya
dauki wani abu da za a i ya sayarwa a cikin haikalin. 17

Sai ya koyar da su cewa, “Ashe ba rubuce yake ba, “Za
a kira gidana gidan addu'a na dukan al'ummai? Amma
ku kun mayar da shi kogon yan fashi”. 18 Da mayan
Faristoci da marubutan attaura suka ji maganar da ya
yi, sai suka nami hanyar da za su kashe shi. Amma
suka ji tsoronsa domin dukkan taron na mamakin
koyarwarsa. 19 Kowace yamma kuma, sukan fita gari.
20 Da safe suna wucewa, sai suka ga bauren nan ya
bushe. 21 Bitrus kuwa ya tuna ya ce “Malam, dubi!
Baurenan da ka la'anta ya bushe.” 22 Yesu ya amsa
masu ya ce, “ku gaskata da Allah.” 23 Hakika, ina gaya
maku, duk wanda ya ce wa dutsen nan tashi ka fada
cikin tekun', bai kuwa yi shakka a zuciyarsa ba, amma
ya gaskata haka kuwa zai faru, haka kuwa Allah zai
yi. 24 Saboda haka ina dai gaya maku, komai kuka
yi addu'a kuka roka, ku gaskata cewa samamme ne,
zai kuma zama naku. 25 Duk sa'add da kuke addu'a
ku gafarta wa wadanda suka yi maku laifi, domin
Ubanku shima zai gafarta maku naku laifi.” 26 (Amma
in baku gafartawa mutane laifofinsu ba, Ubanku ma
da ke sama ba zai gafarta maku ba.) 27 Da suka sake
dawowa Urushalima. Yasu na tafiya cikin haikali, sai
manyan firistoci, da marubuta, da dattawa suka zo
wurinsa, 28 suka ce masa, “Da wanne iko kake yin
wadanan abubuwa? Ko kuwa wa ya ba ka ikon yinsu?
“ 29 Sai Yesu ya ce masu, “Zan yi maku wata tambaya.
ku ba ni amsa, ni kuwa zan gaya maku ko da wanne
iko ne nake yin wadannan abubuwan. 30 Baftismar da
Yahaya yayi, daga sama take ko kuwa daga mutum
take? ku bani amsa”. 31 Sai suka yi mahuwara da
juna, suka ce, “in kuwa muka ce, 'daga sama take,'
za ya ce, “To, don me ba ku gaskata shi ba? 32 In
kuwa muka ce, “amma in muka ce ta mutum ce zasu
jejjefemu domi suna jin tsoron jama'a, don duk kowa
ya tabbata, cewa Yahaya annabi ne. 33 Sai suka amsa
wa Yesu suka ce, “Ba mu sani ba” Yesu ya ce masu,
“Haka ni kuma ba zan fada muku ko da wanne iko
nake yin abubuwan nan ba.”

12 Sai Yesu ya fara koyar da su da misalai. “Wani
mutum ne ya yi gonar inabi ya shingen ta, ya
haka ramin matse inabin, ya kuwa gina hasumayar
tsaro. Ya ba wandansu manoma jinginar gonar, sa'an
nan ya tafi wata kasa mai nisa. 2 Da lokaci ya yi, sai
ya aika masu wani bawansa domin ya karbi wadansu
daga cikin amfanin gonar. 3 Amma manoman suka
kama shi, suka yin masa duka, suka kore shi hannu
banza. 4 Ya sake aikar wani bawan. Shi kuma suka
raunata shi aka, suka wulakanta shi. 5 Ya sake aiken
wani. Shi kam, suka kashe shi. Haka fa aka yi ta yi da
wadansu da yawa, sun dodoki wadansu, suka kuma
kashe wadansu. 6 Yanzu dai yana da sauran daya
tak, shine kaunatacen dansa. Daga karshe ya aike shi
wurinsu, yana cewa, ai za su bashi girma. 7 Amma
manoman nan suka ce wa juna, “ai, wannan shine
magajinsa, 'ku zo mu kashe shi, gadon ya zama namu.”
8 Sai suka kamo shi, suka kashe shi, suka jefar da shi
bayan shinge. 9 To, me mai gonar inabin zai yi? Sai ya
zo ya hallaka manoman nan, ya ba wadansu gonar. 10
Ashe, ba ku karanta wannan nassi ba? cewa, ' Dutsen
da magina suka ki, shi ne ya zama mafi mahmimanci.
11 Wannan daga Ubangiji ne, kuma ya yi dai dai a
idanunmu.”' 12 Sai suka nemi su kama shi, don sun
lura a kansu ne ya yi masalin, amma suka ji tsoron
jama'a. Don haka suka kyele shi, suka tafi. 13 Suka aika
masa da wadansu farisiyawa da Heridiyawa, don su sa
masa tarko da kalamai cikin maganarsa. 14 Da suka zo,
suka ce masa, “Malam, gaskiya kana koyar da maganar
Allah sosai, ba ka nuna bambanci tsakani mutane,
sai koyar da tafarkin Allah kake yi sosai. “Shin, mu
biya haraji ga Kaisar, ko a a?” 15 AmmaYesu ya gane
munafuncinsu, ya ce masu, “Don me kuke gwada ni?
ku kawo mani dinarin in gani.” 16 Suka kawowa Yesu
daya. Ya ce masu, “Kamar waye da kuma rubutun
wanene? suka ce masa, “Na Kaisar ne.” 17 Yesu ya ce,
“to, ku ba Kaisar abinda yake na Kaisar, ku kuma ba
Allah abin da yake na Allah. Sai suka yi mamakinsa
kwarai. 18 Sai Sadukiyawa suka zo wurinsa, su dake
cewa babu tashin matattu. Suka tambaya shi suka
ce, 19 “Malam, Musa dai ya rubuta mana, cewa idan
dan'uwan mutum ya mutu, ya bar matarsa ba da,
lallai ne dan'uwan mutumin ya auri matar, ya haifa
wa dan'uwansa 'ya'ya.' 20 To an yi wadansu 'yan'uwa
maza guda bakwai, na farko ya yi aure, ya mutu bai
bar 'ya'ya ba. 21 Na biyu kuma ya aure ta, shi ma ya
mutu, ba 'ya'ya. Na ukun ma haka. 22 Haka dai duk
bakwai din, ba wanda ya bar 'ya'ya. A karshe kuma
ita matar ta mutu. 23 To, a tashin matattu, matar wa
za ta zama a cikinsu? Don duk bakwai din nan sun
aure ta”. 24 Sai Yesu ya ce, “Ba saboda wannan dalili
ne kuka yi kuskure ba, wato don ba ku san littafin
ba, kuma ba ku san ikon Allah ba? 25 Domin in an
tashin daga matattu, ba a aure, ba a auraswa, amma
sun zama kamar malaiku a sama. 26 Amma game da

mattattun da suka tashi, ashe, ba ku taba karantawa
a littafin Musa ba, yadda Allah ya ce masa? “Ni ne
Allah na Ibrahim, da Ishaku, da kuma Yakubu'? 27 Ai,
shi ba Allahn mattatu bane, amma na rayyayu ne.
Hakika kun yi kuskure “. 28 Sai wani malamin attuara
ya zo ya ji suna muhawara da juna. Da dai ya ga Yesu
yana ba su kyakkyawar amsa, sai ya tambaye shi,
“Wanne Umarni ne mafi girma dukka?” 29 Yesu ya
amsa yace, “mafi girma shine, 'ku saurara ya Isra'ila,
Ubangiji Allahnmu, Ubangiji daya ne. 30 Sai ka kaunaci
Ubangiji Allah da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka
da dukkan tunaninka, da dukkan karfinka. 31 ta biyu
itace, 'ka kaunaci makwabcinka kamar kanka, Ba wata
doka da ta fi wadannan.'' 32 Sai malamin attaura
ya ce masa, “Hakika gaskiyarka malam, Allah daya
ne, ba kuma wani sai shi. 33 A kaunace shi kuma da
dukkan zuciya, da dukkan hankali, da dukkan karfi, a
kuma kaunaci makwabci kamar kanka, ai ya fi dukkan
hadayu na konawa.” 34 Da Yesu ya ga ya yi masa
magana da hikima, sai ya ce masa, “Ba ka nesa da
mulkin Allah.” Bayan wannan kuma ba wanda ya sake
tambayarsa wani abu. 35 Yesu ya amsa a lokacin da
yake koyarwa a Haikali, ya ce “Yaya malaman attaura
suke ce wa Kristi dan Dauda ne? 36 Domin Dauda
kansa, ta ikon Ruhu Mai Tsarki ya ce, “Ubangiji ya ce
wa Ubangijina, zauna a hannun damana, har sai na
kaskantar da makiyanka'. 37 Dauda da kansa ya kira
shi 'Ubangiji; To, ta yaya ya Almasihu zai zama Dan
Dauda?” Babban taron jama'ar suka saurare shi da
murna. 38 A koyarwa sa Yasu ya ce, “ku yi hankali da
malaman attaura, masu son yawo da manyan riguna,
suna so a gaishesu a kasuwa, 39 da kuma son wuraren
zama masu daraja a haikali, da wurin bukukuwa. 40
Sun kuma kwace gidajen gwauraye, da yin doguwar
addu'a, don mutane su gani. Wadanan mutanen zasu
sami hukunci mai tsanani.” 41 Sai ya zauna a gaban
akwatin baiko a Haikalin, yana duban yadda jama'a
suke zuba kudi a ciki. 42 Wadansu masu arziki da
yawa suna zuba kudi masu tsoka. Sai gwauruwa mara
abin hanu ta saka anini biyu a ciki akwatin baikon. 43
Ya kira almajiransa, ya ce masu, “Hakika, ina gaya
maku, abinda gwauruwa nan ta saka a akwatin baikon
nan ya fi na sauran dukka. 44 Su duk sun bayar daga
yalwa tasu ne, ita kuwa daga cikin rashinta ta bada
duk abinda take da shi.”

13 da Yesu ke fita daga Haikalin, sai daya daga cikin
almajirnsa ya ce masa “malam, dubi kyawawan
duwatsunnan da kyawawan gine-ginnenan!” 2 Ya ce
masa, ka ga wadannan kyawawan gine- ginen? babu
wani dutsen da za a bar shi akan dan'uwansa, da ba
za a rushe shi ba.” 3 Yana zaune a kan dutsen zaitun
wanda yake kusa da Haikali, sai Bitrus, da Yakubu, da
Yahaya, da Andarawus suka tambaye shi a asirce, suka
ce. 4 Gaya mana yaushe za a yi wadannan abubuwa?
mecece zata zama alamar faruwar wadanna abubuwa
da zasu faru?'' 5 Yesu ya ce masu, “ku kula, kada kowa
ya rudeku. 6 Da yawa za su zo da sunana, suna cewa
nine shi, har su bad da mutane da yawa. 7 In kuka
ji labarin yake- yake, da jita-jitarsu kada ku damu,
wannan zai faru, amma karshen duniya bai gabato ba.
8 Al'umma za ta tasarwa al'umma, mulki ya tasarwa
mulki. Za a yi girgizar kasa awurare dabam-dabam, da
kuma yunwa, amma fa dukkan wadanna abubuwan
mafarin azaba ne. 9 Amma, ku zauna a fadake. Don
za su kai ku gaban majalisa. za a yi maku duka a
cikin majami'u. Su kuma kai ku gaban masu mulki da
sarakuna, saboda sunana, domin ku ba da shaida a
gare su. 10 Amma lallai sai an fara yi wa dukkan al,
ummai bishara. 11 Sa'ad da suka kai ku gaban shari'a
suka mika ku, kada ku damu a wannan lokacin, za
a baku abin da zaku fada, Amma duk abin da aka yi
muku a wannn lokacin, shi za ku fada, domin ba ku
ne kuke magana ba, Ruhu mai tsarki ne. 12 Dan'uwa
zai bada dan'uwarsa akashe shi, uba kuwa dansa.
Yara kuma zasu tayar wa iyayensu har su sa akashe
su. 13 Za a ki ku saboda sunana, amma duk wanda
ya jumre har karshe zai cetu. 14 Sa'adda kuka ga an
kafa mummunan aikin sabo mai ban kyama a wurin
da bai kamata ba (bari mai karatu ya fahimta), to,
bari wadanda suke kasar Yahudiya, su gudu zuwa
dutse. 15 Wanda yake tudu kuma kada ya sauko ya
shiga gida garin daukar wani abu. 16 Wanda yake
gona kuma kada ya koma garin daukar mayafinsa. 17
Amma, kaiton masu juna biyu da masu goyo a wannan
lokacin. 18 Ku yi addu, a kada abin ya faru da damina.
19 A lokacin za ayi wata matsanaciyar wahala, wadda
bata taba faruwa ba, tun farkon halittar da Allah ya yi
har zuwa yau, ba kuwa za a taba yi ba har abada. 20 In
da ba ubangiji ya rage kwanakin nan ba, da ba Dan
adam din zai tsira. Amma saboda zabbabunan da ya
zaba, ya rage kwanakin. 21 To, in wani ya ce maku,
kun ga Almasihu nan!' ko, 'kun gan shi can, kada ku

gaskata. 22 Gama almasihan karya, da annabawan
karya zasu bayyana kuma, zasu yi abubuwan al'ajibai
masu ban mamaki. 23 Amma ku zauna a fadake, Na
dai fada maku wadannan abubuwan kafin lokacin.
24 Amma, bayan matsanaciyar wahalannan, rana
zata duhunta, wata kuma ba zai bada haske ba. 25
Taurari za su fado daga sararin sama, za a kuma
girgiza manyan abubuwan da suke a sararin sama.
26 Sa' annan zasu ga Dan mutum na zuwa a cikin
gajimare, da iko mai girma da daukaka. 27 Zai aiko da
mala'ikunsa su tattaro zabbabunsa daga kusuwoyi
hudu na duniya(watau Gabas da Yamma, kudu da
Arewa) har zuwa karshen sama. 28 "Ku yi koyi da
itacen baure. Da zarar rassansa sun fara taushi yana
kuma fitar da toho, kun san damina ta yi kusa ke nan.
29 Sa'adda kuka ga wadannan abubuwa suna faruwa,
ku dai sani ya kusato, a bakin kofa ma ya ke. 30 Hakika
ina gaya maku, zamanin nan ba zai shude ba sai dukan
abubuwan nan sun faru. 31 Sararin sama da kasa za su
shude, amma maganata ba za ta shude ba. 32 Amma
wannan rana ko sa'a ba wanda ya sani, ko mala'ikun
sama, ko Dan, sai dai Uban kadai. 33 Ku kula, ku zauna
a fadake, kuna addu'a don baku san ranar da lokacin
zai yi ba. 34 Kamar yadda mutum mai tafiya, in ya
bar gida ya wakilta bayinsa kan gidansa, kowanne da
aikinsa, ya kuma umarci mai gadi ya zauna a fadake.
35 To, ku zauna a fadake don ba ku san lokacin da
maigidan zai zo ba, ko da yamma ne, ko da tsakar
dare ne, ko da carar zakara ne, ko da safe ne. 36 Kada
ya zo ba zato, ya samu kuna barci. 37 Abinda na gaya
maku, ina gaya wa kowa, shine ku zauna a fadake!"

14 Idin Ketarewa da bukin gurasa mara yisti sauran
kwana biyu kenan, sai shugabanin firistoci da
malaman attaura suka nemi yadda zasu kama Yesu a
asirce domin su kashe shi. 2 Suna cewa amma "Ba
a lokacin idin ba, domin kada su haddasa hargitsi
a tsakanin mutane". 3 Yesu yana Betanya a gidan
Saminu kuturu, yana shirin liyafa kenan sai ga wata
mace dauke da kwalbar turare mai tamanin kwarai, ta
shafa masa a kansa. 4 wasu dake tare da Yesu suka
husata, suna kwalbarta da cewa 5 "Ai wannan turare
ne mai tsada, ina laifin a sayar a raba wa talakawa
kudin? ina dalilin wannan almubazaranci? 6 Sai Yesu
yace masu "Ku kyaleta, don me kuke tsauta mata, 7 ai
Idan kuna da niyyar taimakon talakawa ko matalauta,
suna nan tare da ku ko a yaushe amma ni bazan
kasance da ku kullum ba. 8 Macen nan tayi aiki nagari
domin shirya jikina ga jana'iza. 9 hakika, Ina gaya
maku, duk inda za'a yi bishara a duniya baza a mance
da matan nan da hidimar da ta tayi mini ba." 10 Da jin
haka sai Yahuza Iskariyoti, daya daga cikin manzannin
ya ruga zuwa wurin baban firist domin ya bashe shi
a garesu, 11 Da mayan firistoci suka ji haka suka yi
murna matuka tare da alkawarin kudi ga Yahuza, shi
kuwa sai ya fara neman zarafin da zai mika Yesu a
gare su. 12 A ranar farko ta bukin gurasa marar yisti
da kuma hadayar ragon Idin ketarewa, almajiransa
suka ce masa "Ina zamu shirya liyafar domin idin
ketarewa? 13 Ya aiki biyu daga cikin almajiransa
da cewa "Ku shiga cikin birnin, zaku tarar da wani
mutum dauke da tullun ruwa. 14 Duk gidan da ya
shiga ku bishi, sai ku cewa mai gidan, malam yace
"ina bukatar masauki domin hidimar idin ketarewa
tare da almajiraina?"' 15 Zai kuwa nuna maku babban
bene gyararre. Sai ku yi mana shiri a can." 16 Da
shigar almajiran cikin birnin, sai kome ya kasance
yadda ya fada, su kuwa suka yi shirye shiryen idin
ketarewar. 17 Da maraice ta yi, sai ya tare da sha
biyun. 18 Yayin da suke zazzaune a teburin suna
cin abincin, sai Yesu ya ce "Hakika ina gaya maku
wani da ke ci tare da ni a nan zai bashe ni". 19 Sai
suka damu suka tambaye shi daya bayan daya suna
cewa "Hakika bani bane ko?" 20 Yesu ya amsa masu
da cewa "Daya daga cikin sha biyu ne, wanda ke sa
hannu tare da ni yanzu cikin tasar". 21 Dan Mutum
zai tafi ne yadda nassi ya umarta game da shi amma
kaiton wanda zai bashe shi! "zai, fiye masa, dama
ba a haife shi ba". 22 Lokacin da suke cin abincin,
Yesu ya dauki gurasa ya sa albarka, ya gutsuttsura
ta, sai ya basu yana cewa "Wannan jikinana ne". 23
Ya kuma dauki koko, yayi godiya, ya basu, su kuwa
suka sha daga kokon. 24 Ya ce "Wannan jinina ne
na alkawari da an zubar ga yawancin mutane". 25
Hakika, bazan kara sha daga wannan ruwan inabi ba
sai a ranar da zan sha sabo cikin mulkin Allah." 26
Bayan sun raira wakar yabo ga Allah, sai suka tafi
wurin dutsen zaitun. 27 Yesu ya ce masu dukkan ku
zaku yi tuntube harma ku fadi saboda ni gama rubuce
take cewa "Zan buge makiyayin, tumakin kuwa za su
watse; 28 Amma bayan tashina, zai yi gaba in riga ku
zuwa Galili. 29 Bitrus ya ce masa "ko dukkansu sun
fadi, faufau banda ni". 30 Yesu yace masa "Hakika
ina gaya maka, cikin wannan dare kafin carar zakara

ta biyu zaka yi musun sani na sau uku". 31 Amma
Bitrus ya sake cewa "Koda za'a kasheni tare da kai ba
zan yi musun sanin ka ba". Dukkan su kuwa suka yi
wannan Alkawari. 32 Suka isa wani wuri da ake kira
Getsamani, sai Yesu ya ce wa almajiransa "Ku dakata
anan domin zan je inyi addu'a". 33 Sai ya dauki Bitrus,
da Yakubu, da Yahaya. Ya fara jin wahala mutuka tare
da damuwa kwarai. 34 Sai ya ce masu "Raina na shan
wahala harma kamar in mutu. Ku dakata a nan, ku
zauna a fadake". 35 Da Yesu yayi gaba kadan, sai ya
fadi kasa yayi addu'a yana cewa idan mai yiwuwa ne
"A dauke masa wannan sa'a daga gare shi. 36 Ya ce
"Ya Abba Uba, kome mai yuwane gare ka, ka dauke
mini kokon wahalan nan, duk da haka ba nufina ba
sai dai naka". 37 Da komowarsa ya same su suna barci,
sai ya ce wa Bitrus, Siman barci kake? Ashe, ba za ka
iya zama a fadake ko da sa'a daya ba? 38 Ku zauna a
fadake, kuyi addu'a kada ku fada cikin jaraba. Lalle
ruhu na da niyya amma jiki raunana ne. 39 Sai ya sake
komawa, yayi addu'a, yana maimaita kalmominsa na
farko. 40 Har wa yau kuma ya sake dawowa, ya same
su suna barci don barci ya cika masu idanu kwarai,
sun kuwa kasa ce masa kome. 41 Ya sake komowa
karo na uku yace masu "har yanzu barci kuke yi kuna
hutawa? Ya isa haka! Lokaci yayi, an bada Dan Mutum
ga masu zunubi". 42 Ku tashi mutafi kun ga, ga mai
bashe ni nan ya kusato." 43 Nan da nan, kafin ya rufe
baki sai ga Yahuza, daya daga cikin sha biyun da taron
jama'a rike da takkuba da kulake. Manyan firistoci
da malaman attaura da shugabanni suka turo su. 44
Mai bashe shi din nan ya riga ya kulla da su cewa
"Wanda zan yi wa sumba shine mutumin, ku kama shi
ku tafi da shi a tsare. 45 Da isowarsa kuwa, sai ya zo
wurin Yesu ya ce "Ya malam!". Sai ya sumbace shi. 46
Su kuwa suka kama shi, suka tafi da shi. 47 Amma
daya daga cikin na tsaye ya zaro takobinsa ya kai wa
bawan babban firist sara, ya yanke masa kunne. 48
Sai Yesu ya ce "kun fito kamar masu kama yan fashi
da takkuba da kulake, domin ku kama ni? 49 Lokacin
da nake koyarwa a Haikali, kowace rana da ku, baku
kama ni ba. Amma anyi haka ne domin a cika abinda
Nassi ya fada." 50 Daga nan duk wadanda suke tare da
Yesu suka yashe shi, suka tsere. 51 Wani saurayi, daga
shi sai mayafi ya bi shi, suka kai masa cafka. 52 Shi
kuwa ya bar masu mayafin ya gudu tsirara. 53 Daga
nan suka tafi da Yesu wurin babban firist. a can suka
tara dattawa duk da manyan firistoci da shugabanni
da marubuta, suka taru a wurinsa. 54 Bitrus kuwa
ya bi shi daga nesa har cikin gidan babban firist.
Ya zauna tare da dogaran Haikalin, yana jin dumin
wuta. 55 Sai, manyan firistoci da duk 'yan majalisa
Yahudawa suka nemi shaidar da za a tabbatar a kan
Yesu, don su samu su kashe shi. Amma basu samu ba.
56 Da yawa kuma suka yi masa shaidar Zur (Karya),
amma bakin su bai zama daya ba. 57 Sai wadansu
kuma suka taso suka yi masa shaidar zur (karya) suka
ce. 58 "Mun ji ya ce, wai zai rushe haikalin nan da
mutane suka gina, ya sake gina wani cikin kwana
uku, ba kuwa ginin mutum ba". 59 Duk da haka, sai
shaidar tasu bata zo daya ba. 60 Sai babban firist ya
mike a tsakanin su, ya tambayi Yesu yace "Ba ka da
wata amsa game da shaidar da mutanen nan suke yi a
kanka? 61 Amma yayi shiru abinsa, bai ce kome ba.
Sai babban firist din ya sake tambayarsa "To, ashe kai
ne Allmasihu Dan Madaukaki? 62 Yesu ya ce "Nine. Za
ku kuwa ga Dan Mutum zaune dama ga mai iko, yana
kuma zuwa cikin gajimare". 63 Sai babban firist ya
kyakketa tufafinsa yace "Wacce shaida kuma zamu
nema? 64 Kun dai ji sabon da yayi! Me kuka gani? Duk
suka yanke masa hukunci akan ya cancanci kisa. 65
Wadansu ma suka fara tottofa masa yau, suka daure
masa idanu, suka bubbuge shi suna cewa "Yi annabci"
Dogaran kuma suka yi ta marinsa. 66 Bitrus kuwa na
kasa a filin gida, sai wata baranyar babban firist ta zo.
67 Da ta ga Bitrus na jin dumi, ta yi masa kallon gaske
ta ce "Kaima ai tare kake da banazaren nan Yesu".
68 Amma ya musa ya ce "Ni ban ma san abinda kike
fada ba balle in fahimta". Sai ya fito zaure. Sai zakara
yayi cara. 69 Sai baranyar ta ganshi, ta sake ce wa
wadanda ke tsaitsaye a wurin, "Wannan ma daya daga
cikinsu ne". 70 Amma ya sake musawa, jim kadan sai
na tsaitsayen suka ce wa Bitrus "Lalle kai ma dayansu
ne don ba Galile ne kai". 71 Sai ya fara la'anta kansa
yana ta rantsuwa yana ce wa "Ban ma san mutumin
nan da kuke fada ba". 72 Nan da nan sai zakara ya yi
cara ta biyu, Bitrus kuwa ya tuna da maganar Yesu a
gare shi cewa "Kafin zakara ya yi cara ta biyu, za ka yi
musun sani na sau uku". Da ya tuno haka, sai ya fashe
da kuka.

15 Da sassafe, sai manyan firistoci suka hadu da
dattawa da manyan malamai, da majalisa suka
daure Yesu, suka sa shi gaba suka mika shi ga Bilatus.
2 Bilatus ya tambaye shi, kaine sarkin Yahudawa?
ya amsa ya ce "haka ka ce" 3 Sai manyan firistochi

suka kawo zargi iri iri a kan Yesu. 4 Bilatus ya sake
tambayarsa, ba ka da abin cewa? ka lura da yawan
zargi da ake yi maka. 5 Amma Yesu baya sake yi masa
magana ba. wannan ya ba shi mamaki. 6 A lokacin
idi, Bilatus ya kan sakar masu da dan bursuna wanda
jama'a suka bukaci a saka, 7 A cikin gidan yari, in da
aka tsare wadansu yan tawaye, da masu kisan kai,
akwai wani mai kisan kai, ana ce da shi Barrabbas. 8
Sai Jama'a suka zo wurin Bilatus ya yi masu kamar
yadda ya saba yi. 9 Bilatus ya amsa masu ya ce, kuna
so in sakar maku sarkin Yahudawa? 10 Yayi wannan
domin ya sani cewa Firistoci sun bada shi ne domin
suna kishin sa, 11 Sai Firistochi suka zuga jama'a, sai
suka yi kuwwa suna cewa, a sakar masu Barrabbas
amaimakon Yesu. 12 Bilatus ya sake yi masu tambaya
“Yaya zan yi da Sarkin Yahudawa?” 13 sai suka amsa
da kuwwa” a “giciye shi!” 14 Bilatus ya ce masu
menene laifinsa sai suka kara ihu, “a giciye shi.” 15
Bilatus don yana son ya farantawa jama'a zuciya sai
ya sakar masu da Barrabbas sai ya yi wa Yesu bulala,
sannan ya mika shi a giciye shi. 16 Sojoji suka kai
shi cikin kagara, suka tara rundunan soja, 17 Suka
sa masa tufafin shulaiya suka nada masa rawanin
kaya, 18 Suna masa kirari na ba'a suna cewa, “A gaida
sarkin Yahudawa!” 19 Sai suka buge shi a kai da kulki
suka kuma tofa masa yau a fuska, suka kuma durkusa
suna yi masa sujadar ba'a. 20 Bayan sun gama yi
masa ba'a sai suka cire masa tufafin shunnaiya, sai
suka maida masa tasa tufafinsa, sai suka fitar dashi
don su giciye shi. 21 Suna cikin tafiya sai suka hadu
da wani, mai suna Saminu Bakairawani (wato uban
Alizanda da Rufus); suka tillasta shi ya dauki gijiyen
Yesu. 22 Sojojin suka kawo Yesu wurin da ake kira
Golgota (wato kokon kai) 23 Suka bashi ruwan inabi
hade da mur, amma ya ki ya sha. 24 Sai suka giciye
shi, suka kuma raba tufafinsa suka kuma jefa kuri'a
domin kowanne soja ya sami rabonsa. 25 A sa'a ta
uku aka giciye shi. 26 Sai aka rubuta alamar zargi
da take cewa “Ga Sarkin Yahudawa” 27 Suka kuma
giciye shi tare da wadansu yan fashi guda biyu. 28
Daya a hannun damansa daya a hannun hagunsa.
Domin a cika abinda nassi ya fada. 29 suke wucewa
suna zaginsa suna kada kai suna cewa, “Aha! kai da
zaka rushe haikali ka kuma gina shi cikin kwana uku,
30 ka ceci kanka mana, ka sauka daga giciye!” 31 Haka
ma manyan firistoci da malamai, suka yi masa ba'a
suna cewa “Ya ceci wadansu amma bai iya ceci kansa
ba” 32 Bari Almasihu Sarkin Yahudawa ya sauka daga
giciye. Domin mu gaskata shi, sai wadanda aka giciye
shi tare dasu, suma suka yi masa ba'a. 33 sa'a ta shida
zuwa sa'a ta tara, duhu ya rufe ko'ina, 34 A sa'a ta
tara, Yesu ya tada murya da karfi ya ce Eloi, Eloi
lamathsabathani?” Ma'ana Ya Allahna Ya Allahna,
me ya sa ka yashe ni?” 35 Wasu daga cikin na tsaye,
da suka ji shi, sai suka ce, “Duba, yana kiran Iliya.”
36 Sai wani ya hanzarta, ya dauki soso ya tsoma a
ruwan inabi mai tsami, ya soka agora ya mika masa
don yasha. Mutumin yace bari mu gani ko Iliya zai
zo ya saukar da shi. 37 Sai Yesu yayi kuka da babban
murya da karfi sannan ya rasu. 38 Sai labulen haikalin
ya rabu kashi biyu daga sama har kasa. 39 Sa'adda
da jarumin sojan da ke tsaye yana fuskantar Yesu
ya ga yadda ya mutum, Sai ya ce “hakika, wannan
mutum Dan Allah ne.” 40 Akwai kuma mata wadanda
ke dubawa daga nesa. Daga cikinsu akwai Maryamu
Magadala, da Maryamu( Uwar Yakubu da Yusufu) da
Salome. 41 Wadannan matan sune suka bishi sa'adda
da yake Galilee suna yi masa hidima. Da wadansu
mata da yawa suka zo Urushalima tare da shi. 42
Da maraice an shiga shirye shirye domin kashe gari
asabbaci ce. 43 Sai Yusufu daga garin Arimatiya ya
zo, mutumin kirki, mai girma kuma dan majalisar
dattawa, mai sauraron mulkin Allah, da gaba gadi
ya tafi wurin Bilatus ya bukaci a bashi jikin Yesu. 44
Bilatus ya yi mamakin mutuwar Yesu cikin lokaci
kadan, sai ya kira jarumin ya tabbattar koYesu ya
mutu. 45 Bayan ya tabbattar daga wurin jarumin soja
cewa Yesu ya mutu, sai ya bada jikin ga Yusufu. 46
Yusufu ya sayo likafani. ya saukar da shi daga giciye,
ya kawo likafanin nan ya lulube jikin Yesu dashi. Ya
kai shi kabarin da aka sassaka da dutse, wadda ya
shirya shi domin kansa. Ya kawo dutse ya rufe bakin
kabarin da shi. 47 Maryamu Magadaliya da Maryamu
Uwar Yusufu sun ga wurin da aka yi jana'izar Yesu.

16 Bayan ranar assabaci, Maryamu Magadaliya da
Maryamu uwar Yakubu da Salomi, suka sayo man
shafawa mai kamshi domin shafe jikin Yesu saboda
jana'iza. 2 Da safiyar ranar farko ta mako sai suka
tafi kabarin a dai dai fitowar rana. 3 Suna magana a
tsakaninsu suna cewa, wanene zai gangarar da dutsen
da aka rufe bakin kabarin da shi?” 4 Da suka daga
ido, sai suka ga an riga an gangarar da dutsen, domin
yana da girma. 5 Da suka shiga cikin kabarin sai ga
wani saurayi saye da farar tufa, yana zaune a hannun

dama, suna mamaki. 6 Sai ya ce masu, “Kada ku ji
tsoro. Kuna neman Yesu banazare, wanda aka giciye.
Ya tashi! Baya nan. Ku duba wurin da aka kwantar
dashi. 7 Sai ku je, ku gaya wa almajiransa da Bitrus
cewa ya rigaya ya yi gabanku zuwa Galili. A can zaku
ganshi, kamar yadda ya fada maku.” 8 Suka fita daga
cikin kabarin da gudu suna rawar jiki da mamaki, ba
su cewa kowa komai ba domin suna jin tsoro. 9 **(note:
The most reliable and earliest manuscripts do not include Mark 16:9-20.)**
Da safiyar ranar farko ta mako ya fara bayyana kansa
ga Maryamu Magadaliya wadda ya kori aljannu guda
bakwai daga cikinta. 10 Sai ta tafi ta shaida wadanda
suke tare da shi suke makoki da kuka. 11 Sai suka ji
cewa ya tashi kuma ta ganshi, amma basu gaskata ba.
12 Bayan wadannan al'amura ya bayana kansa ta wata
siffa ga mutum biyu sa'ilin da suke tafiya akan hanya.
13 Sai suka tafi suka gaya wa sauran almajiransa,
duk da haka basu gaskata ba. 14 Bayan wani lokaci,
Yesu ya bayyana kansa ga almajiransa su goma sha
daya, ya tsauta masu saboda rashin gaskatawa da
taurin zuciya, bayansun ji daga wadanda suka ganshi
bayan ya tashi daga matattu. 15 Sai ya umarcesu
cewa “Ku tafi cikin duniya ku yi bishara ga dukan
halitta. 16 Wanda ya ba da gaskiya aka kuma yi masa
baftisma, zaya sami ceto, wanda baya bada gaskiya ba
za ya hallaka. 17 Wadannan alamu za su kasance da
wadanda suka gaskata; a cikin sunana, za su fidda
aljannu, za su yi magana da sabbin harsuna. 18 Za su
dauki macizai da hannayesu, idan sun sha guba ba ta
cutar dasu ba, za su dibiya hannayensu ga marasa
lafiya, za su sami warkaswa.” 19 Bayan Ubangiji ya
gama magana da su, sai aka dauke shi zuwa sama in
da zai zauna a hannun dama na Allah. 20 Almajiransa
kuma suka tafi ko'ina suna sheilar bishara. Ubangiji
kuma yayi aiki tare da su, yana tabbatar da kalma ta
wurin ayukan al'ajiba tare da su.

# Luka

1 Mutane da dayawa sun yi kokarin rubutu akan
abubuwan da suka cika a tsakaninmu, 2 kamar
yanda suka danka mana su, wadanda tun daga farko
suka zama shaidu da idanunsu kuma manzanni ne na
sakon. 3 Sabili da haka, ni ma, bayan da na yi bincike
da kyau akan yanayin wadannan abubuwa tun da
farko na ga ya yi kyau in rubuta wadannan abubuwa
bi da bi ya mafi girmaTiyofilas. 4 Ya zama haka domin
ka san gaskiyar abin da aka koya maka ne. 5 A cikin
zamanin Hirudus, Sarkin Yahudiya, akwai wani firist
mai suna Zakariya, daga yankin Abija. Matarsa daga
cikin yaya mata na zuriyar Haruna ce, kuma sunan ta
Alisabatu ne. 6 Dukan su biyu masu adalci ne a gaban
Allah; marasa zargi a tafiyarsu cikin dukan dokoki da
farilan Ubangiji. 7 Amma ba su da da, domin Alisabatu
ba ta haihuwa, kuma a wannan lokacin dukansu sun
tsufa kwarai. 8 Ya zama kuma a lokacin da Zakariya
yana gaban Allah, yana yin hidimar sa ta firist bisa ga
tsari da ka'idar aikinsa. 9 Bisa ga al'adar zaben firist da
zai yi hidima, an zabe shi ta wurin kuri'a ya shiga cikin
haikalin Ubangiji domin ya kona turare. 10 Dukan
taron Jama'a suna addu'a a waje a sa'adda ake kona
turaren. 11 A lokacin, mala'ikan Ubangiji ya bayana a
gare shi yana tsaye a gefen daman bagadi na turaren.
12 Zakariya ya firgita sa'adda ya gan shi; tsoro ya kama
shi. 13 Amma mala'ikan ya ce masa, "Kada ka ji tsoro,
Zakariya, domin an ji addu'ar ka. Matar ka Alisabatu
za ta haifa maka da. Za ka kira sunansa Yahaya. 14
Za ka yi murna da farin ciki, kuma da yawa za su yi
murna da haifuwarsa. 15 Domin zai zama mai girma a
gaban Ubangiji. Ba zai sha ruwan inabi ba ko wani
abu mai sa maye, kuma zai cika da Ruhu Mai Tsarki
tun daga cikin cikin mahaifiyarsa. 16 Kuma mutanen
Isra'ila da yawa za su juya zuwa ga Ubangiji Allahnsu.
17 Zai yi tafiya a gaban Unbangiji a cikin ruhu da
ikon Iliya. Zai yi haka domin ya juya zuciyar Ubanni
zuwa ga 'ya'yansu, domin marasa biyayya su yi tafiya
a cikin tafarkin adalai. Don ya shirya wa Ubangiji
mutanen da aka shirya dominsa." 18 Zakariya ya ce wa
mala'ikan, "Ta yaya zan san wannan? Ga shi na tsufa
kuma matata tana da shekaru da yawa." 19 Mala'ikan
ya amsa ya ce masa, "Nine Jibra'ilu, wanda ke tsaye a
gaban Allah. An aiko ni in gaya maka wannan labari
mai dadi. 20 Kuma duba, za ka zama bebe, ba za ka iya
magana ba, sai ran da wadannan abubuwa suka cika.
Ya zama haka domin ba ka gaskanta da kalmomina
ba, wadanda za su cika a daidai lokacin." 21 Sa'adda
mutane suke jiran Zakariya. Sun yi mamaki yadda ya
dauki lokaci sosai a cikin haikali. 22 Amma da ya fita,
bai iya yin magana da su ba. Sun gane da cewa ya
ga wahayi lokacin da yake cikin haikali. Ya ci gaba
da yi masu alamu, ba ya magana. 23 Ya zama bayan
da kwanakin hidimarsa suka kare, ya tafi gidansa. 24
Bayan kwanakin nan, matarsa Alisabatu ta samu juna
biyu. Ta boye kanta har na watani biyar. Ta ce, 25
"Wannan shi ne abin da Allah ya yi mani da ya dube
ni domin ya dauke kunyata a gaban jama'a." 26 A cikin
watan ta na shidda, an aiki Mala'ika Jibra'ilu daga
wurin Allah zuwa wani birni a Galili mai suna Nazarat,
27 zuwa ga wata budurwa wanda aka ba da ita ga wani
mutum mai suna Yusufu. Shi dan zuriyar Dauda ne,
kuma ana kiran budurwar Maryamu. 28 Ya zo wurin
ta ya ce, "A gaishe ki, ke da ki ke da tagomashi sosai!
Ubangiji yana tare da ke. 29 Amma ta damu kwarai
da wadannan kalmomi sai ta yi tunani ko wacce irin
gaisuwa ce wannan. 30 Mala'ikan ya ce mata, "Kada ki
ji tsoro, Maryamu, domin kin samu tagomashi a wurin
Allah. 31 Duba, za ki sami juna biyu, za ki haifi da. Za
ki kira sunansa 'Yesu'. 32 Zai zama mai girma, kuma
za a ce da shi Dan Allah Madaukaki. Ubangiji Allah zai
ba shi kursiyin ubansa Dauda. 33 Zai yi mulkin dukkan
gidan Yakubu har abada, kuma mulkinsa ba shi da
iyaka." (aiōn g165) 34 Maryamu ta ce wa mala'ikan, "Yaya
wannan zai faru, tun da shike ni ban san namiji ba?"
35 Mala'ikan ya amsa ya ce mata, "Ruhu Mai-tsarki zai
sauko a kan ki, kuma ikon Madaukaki zai lullube ki.
Sabili da haka, za a kira mai tsarkin da za ki haifa Dan
Allah. 36 Ki kuma duba, ga 'yar'uwarki Alisabatu ta
samu juna biyu a tsufanta. Watannin ta shida kenan,
ita wadda aka kira ta bakarariya. 37 Gama babu abin
da ba shi yiwuwa a wurin Allah." 38 Maryamu ta ce,
"To, ni baiwar Ubangiji ce. Bari ya faru da ni bisa ga
sakonka." Sai mala'ikan ya bar ta. 39 Sai Maryamu ta
tashi da sauri a cikin kwanakin nan, zuwa kasa mai
duwatsu, zuwa wani birni a Yahudiya. 40 Ta shiga
gidan Zakariya ta kuma gai da Alisabatu. 41 Ya zama
sa'adda Alisabatu ta ji gaisuwar Maryamu, sai dan da
ke cikinta ya yi tsalle, an cika Alisabatu kuma da Ruhu
Mai Tsarki. 42 Ta daga murya, ta ce, "Mai albarka kike
a cikin mata, kuma mai albarka ne dan cikinki. 43
Kuma don me ya faru da ni da uwar Ubangijina ta
ziyarce ni? 44 Kuma duba, da na ji karar gaisuwan ki

sai dan ciki na ya yi tsalle domin murna. 45 Kuma
mai albarka ce wadda ta gaskanta cewa abubuwan
da aka alkawarta mata daga wurin Ubangiji za su
cika. 46 Maryamu ta ce, “Zuciyata ta yabi Ubangiji, 47
kuma ruhu na ya yi murna da Allah mai ceto na.”
48 Domin ya dubi kaskancin baiwarsa. Duba, daga
yanzu, dukkan tsararraki za su ce da ni mai albarka.
49 Domin shi madaukaki ya yi mani manyan abubuwa,
kuma sunansa Mai Tsarki ne. 50 Jinkansa ya tabbata
daga tsara zuwa tsara wadanda suke girmama shi.
51 Ya nuna karfinsa da hannuwansa; ya warwatsa
ma su girman kai game da tunanin zuciyarsu. 52 Ya
nakasar da magada daga kursiyoyinsu, ya kuma fifita
nakasassu. 53 Ya ciyar da mayunwata da abubuwa
masu kyau, amma ya aiki attajirai wofi. 54 Ya ba da
taimako ga bawan sa Isra'ila, domin ya tuna ya kuma
nuna jinkai 55 (kamar yanda ya fada wa ubaninmu) ga
Ibrahim da zuriyarsa har abada.” (aiōn g165) 56 Maryamu
ta zauna da Alisabatu tsawon watanni uku sai ta
koma gidanta. 57 Da lokaci yayi da Alisabatu za ta
haifi danta, ta kuma haifi da namiji. 58 Makwabtanta
da 'yan'uwanta sun ji cewa Ubangiji ya ribanbanya
jinkansa akanta, sai suka yi murna tare da ita 59 Ya
zama akan rana ta takwas, sun zo domin a yi wa yaron
kaciya. Da sun kira sunansa “Zakariya” kamar sunan
ubansa, 60 amma mahaifiyarsa ta amsa ta ce, “A'a, za a
kira shi Yahaya.” 61 Suka ce mata, “Babu wani a cikin
danginku wanda ake kira da wannan suna.” 62 Sun
nuna alama ga ubansa bisa ga yanda ya ke so a rada
masa suna. 63 Ubansa ya nemi a ba shi allon rubutu,
sai ya rubuta, “Sunansa Yahaya.” Dukan su suka yi
mamaki kwarai da wannan. 64 Nan take, sai bakinsa
ya bude kuma harshensa ya saki. Ya yi magana ya
kuma yabi Allah. 65 Tsoro ya kama dukan wadanda
suke zama kewaye da su. Sai labarin ya bazu cikin
dukan kasar duwatsu ta Yahudiya. 66 Kuma dukan
wadanda suka ji su, sun ajiye su a cikin zuciyarsu,
suna cewa, “To me wannan yaro zai zama ne?” Domin
hannun Ubangiji yana nan tare da shi. 67 Ruhu Mai-
tsarki ya cika mahaifinsa Zakariya sai ya yi anabci
cewa, 68 “Yabo ga Ubangiji, Allah na Isra'ila domin
ya zo ya taimaki mutanen sa kuma ya yi aikin ceto
domin su.” 69 Ya ta da kahon ceto dominmu daga
gidan bawansa Dauda, daga zuriyar Dauda bawansa, 70
kamar yadda ya fada ta bakin annabawansa tsarkaka
tun zamanin zamanai. (aiōn g165) 71 Zai kawo mana ceto
daga magabtan mu da kuma daga hannun makiyanmu.
72 Zai yi haka domin ya nuna jinkai ga ubaninmu ya
kuma tuna da alkawarinsa mai tsarki, 73 rantsuwar da
ya fada wa ubanmu Ibrahim. 74 Ya rantse zai yardar
mana, bayan da an kubutar da mu daga hannun
makiyanmu, mu bauta masa ba tare da tsoro ba, 75
a cikin tsarki da adalci a gabansa dukan kwanakin
ranmu. 76 I, kai kuma, yaro, za a kira ka annabi na
Madaukaki, domin za ka tafi gaban fuskar Ubangiji ka
shirya hanyoyinsa, ka shirya mutane domin zuwansa,
77 domin ba mutanensa ilimin ceto ta wurin gafarar
zunubansu. 78 Wannan zai faru ne domin girman
jinkan Allahnmu, sabili da hasken rana daga bisa za
ya zo wurinmu, 79 domin haskakawa akan wadanda
ke zaune a cikin duhu da kuma cikin inuwar mutuwa.
Zai yi hakan nan domin ya kiyaye kafafunmu zuwa
hanyar salama. 80 Yaron ya yi girma ya kuma zama
kakkarfa a cikin ruhu, yana kuma cikin jeji sai ranar
bayyanuwarsa ga Isra'ila.

**2** Ananan cikin kwanakin, sai Kaisar Augustas ya
yi shela ya umarta a kidaya dukan mutane da ke
zaune a cikin duniya. 2 Wannan itace kidaya ta farko
da aka yi lokacin da Kiriniyus yake mulkin Suriya. 3
Sabili da haka, kowa ya koma garinsa domin a yi masa
rijista domin kidayan. 4 Yusufu kuma ya tashi ya bar
birnin Nazarat zuwa garin Baitalami da ke Yahudiya,
wanda ake kuma kira birnin Dauda, domin shi daga
zuriyar iyalin Dauda ne. 5 Ya je can ya yi rijista tare da
Maryamu, wadda yake tashi tana kuma da juna biyu.
6 Ya zama sa'adda suke can, lokaci ya yi da za ta haifi
danta. 7 Ta haifi da, dan farinta kuwa, ta nade shi da
kyau da 'yan tsummoki. Ta sa shi cikin wani kwami
na dabbobi, gama babu daki dominsu a masaukin. 8 A
cikin wannan yankin, akwai makiyaya wadanda suke
zama a sarari suna tsaron garken tumakinsu da dare.
9 Nan da nan, sai mala'ikan Ubangiji ya bayyana gare
su, daukakar Ubangiji kuma ta haskaka kewaye da su,
sai suka figita kwarai. 10 Sai mala'ikan ya ce masu,
“Kada ku ji tsoro, domin na kawo maku labari mai
dadi da zai kawo murna da yawa ga dukan mutane.
11 Yau an haifi maku mai ceto a cikin birnin Dauda!
Shine Almasihu Ubangiji! 12 Wannan itace alama
da za a ba ku. Za ku ga dan jariri nade cikin 'yan
tsummoki kwance cikin kwamin dabbobi.” 13 Nan
take, sai ga babban taro daga sama tare da mala'ikan
suna yabon Allah, suna cewa, 14 “Daukaka ga Allah
daga bisa, bari salama ta kasance a duniya tsakanin

mutanen da ya ke jin dadinsu." 15 Ya zama sa'adda
mala'iku suka bar su zuwa cikin sama, sai makiyayan
su ka ce wa junansu, "Bari mu je Baitalami mu ga
wannan abin da ya faru, wanda Ubangiji ya nuna
mana." 16 Su ka yi hamzari suka tafi can sun iske
Maryamu da Yusufu, suka ga jaririn kuwa kwance a
cikin kwamin dabbobin. 17 Bayan da sun ga wannan,
suka gaya wa mutane abinda aka gaya masu game
da wannan yaro. 18 Dukan wadanda su ka ji, su ka
yi mamaki kwarai game da abin da makiyayan su ka
gaya masu. 19 Amma ita Maryamu ta ci gaba da tunani
akan wadanan abubuwa da ta ji, tana tunani mai zurfi
a cikin zuciyarta. 20 Makiyayan suka koma suna ta
daukaka da yabon Allah domin dukan abubuwan da
suka ji, suka kuma gani, dadai da yadda aka gaya
masu. 21 Da ya kai kwana takwas, lokacin da za a
yi wa jaririn kaciya, sai aka rada masa suna Yesu,
sunan da mala'ikan ya bashi kamin a yi cikinsa. 22 Da
kwanakin tsarkakewar su ya wuce bisa ga shari'ar
Musa, Yusufu da Maryamu suka kawo shi cikin haikali
a Urushalima dominsu mika shi ga Ubangiji. 23 Kamar
yadda aka rubuta a dokokin Ubangiji, "Za a kira duk
da na fari kebabbe ga Ubangiji." 24 Suka kuma zo
su mika hadaya bisa ga yadda aka fada a shari'ar
Ubangiji, "Kurciyoyi biyu ko 'yan tantabaru biyu." 25
Ga shi akwai wani mutum a Ushalima mai suna Siman.
Wannan mutum adali ne kuma mai ibada. Yana jiran
mai ta'aziyar Isra'ila, kuma Ruhu Mai-sarki na bisansa.
26 An kuma bayyana masa ta wurin Ruhu Mai-tsarki
cewa ba zai mutu ba sai ya ga Kristi na Ubangiji. 27
Wata rana Siman ya zo cikin haikali ta wurin jagorar
Ruhu Mai-tsarki. Da iyayen suka kawo yaron ciki,
wato Yesu, domin su cika sharudan da shari'ar ke
bukata, 28 sai Siman ya karbe shi cikin hanuwansa, ya
yabi Allah ya ce, 29 "Yanzu bari bawanka ya tafi da
salama, Ubangiji, bisa ga kalmarka. 30 Domin idanuna
sun ga cetonka, 31 wanda ka shirya a gaban dukan
mutane: 32 Haske ne na wahayi ga al'ummai, kuma
daukakar mutanenka Isra'ila." 33 Mahaifin yaron da
Mahaifiyarsa, sun yi mamaki kwarai domin abubuwan
da aka fada akansa. 34 Sai Siman ya albarkace su ya ce
wa uwatasa Maryamu, "Ki ji da kyau, wannan yaro zai
zama sanadiyar faduwa da tashin mutane dayawa a
Isra'ila, kuma alama wadda ake kushen ta. 35 Kuma
takobi zai tsaga zuciyar ki yadda tunanin mutane za
ya bayyana." 36 Wata annabiya mai suna Annatu ta na
nan wurin. Ita diyar Fanuyila ce daga kabilar Ashiru.
Ta riga ta manyanta a shekaru sosai. Ta kasance da
maigidanta shekaru bakwai bayan auren ta, 37 sannan
ta yi zama gwambranci na shekaru tamanin da hudu.
Ba ta taba barin haikali ba, tana ci gaba da yi wa
Ubangiji sujada, dare da rana. 38 A dadai lokacin nan,
ta hau zuwa wurinsu ta fara yi wa Allah godiya. Ta
gaya wa dukan wadanda ke jiran fansar Urushalima.
39 Da su ka gama komai da aka bukace su suyi bisa
ga tafarkin shari'ar Ubangiji, sai suka koma Galili,
zuwa birninsu, Nazarat. 40 Yaron kuma ya yi girma
ya zama da karfi, yana karuwa da hikima, alherin
Ubangiji kuma yana kansa. 41 Iyayensa sukan tafi
Urushalima kowacce shekara domin idin ketarewa. 42
Da yana shekara goma sha biyu, suka sake haurawa
daidai lokacin idin a al'adance. 43 Bayan da sun cika
dukan kwanakin idin, sun fara dawowa gida. Amma
dan yaron Yesu ya jinkirta ya zauna a Urushalima,
kuma iyayensa basu sani ba. 44 Suna tsammani yana
tare da sauran mutane da suke tafiya tare, sai suka
yi tafiya na kwana daya. Suka fara neman sa a cikin
danginsu da abokansu. 45 Da ba su gan shi ba, sai suka
koma Urushalima suna cigiyar sa a can. 46 Ya zama
bayan kwanaki uku, su ka same shi a cikin haikali,
yana zama a tsakiyar malamai, yana sauraron su yana
kuma yi masu tambayoyi. 47 Dukan wadanda suka ji
shi suna ta mamakin fahimtar sa da amsoshin sa. 48
Da suka gan shi, suka yi mamaki kwarai. Mahaifiyarsa
ta ce masa, "Da na, don me ka yi mana haka? Ka
ji, mahaifinka da ni muna ta neman ka rai a bace."
49 Ya ce masu, "Don me kuke nema na? Ba ku sani
cewa dole in kasance a gidan Ubana ba?" 50 Amma
ba su gane abin da yake nufi da kalmomin nan ba.
51 Sa'annan ya koma gida tare da su zuwa Nazarat
yana kuma masu biyayya. Mahaifiayarsa kuma ta ajiye
dukan wadannan abubuwa a zuciyarta tana yin tunani
akansu. 52 Amma Yesu ya ci gaba da hikima da girma,
ya kuma karu da tagomashi wurin Allah da mutane.

3 A cikin shekara ta goma sha biyar da Tibariyus
Kaisar ke mulki, Bilatus Babunti kuma ke jagorar
Yahudiya, Hirudus yana sarautar Galili, dan'uwansa
Filibus yana sarautar yankin Ituriya da Tirakonitis,
Lisaniyas kuma na sarautar yankin Abiliya, 2 kuma
zamanin da Hanana da Kayafa suke manyan firistoci,
maganar Allah ta zo wurin Yahaya dan Zakariya, a
cikin jeji. 3 Ya yi tafiya cikin dukan yankuna da ke
kewaye da Kogin Urdun, yana wa'azin baftismar tuba
domin gafarar zunubai. 4 Kamar yadda aka rubuta a

cikin littafin annabi Ishaya, “Ga muryan wani yana
kira a cikin jeji, 'Shirya hanyar Ubangiji, ka daidaita
tafarkunsa! 5 Za a cika kowani kwari, za a fasa kowani
dutse a kuma baje kowani tudu, za a mike karkatattun
hanyoyi, za a cike hanyoyi masu gargada, 6 kuma
dukan mutane za su ga ceton Allah.” 7 Sai Yahaya ya
kara fada wa taron jama'ar da ke zuwa domin ya yi
masu baftisma, “Ku 'ya'yan macizai masu dafi, wa
ya gargadeku ku guje wa fushin nan mai zuwa? 8
Ku ba da 'ya'ya da sun cancanci tuba, kada ku kuma
fara cewa a cikinku, 'Muna da Ibrahim a matsayin
Ubanmu', domin ina gaya maku, Allah yana iya ta da
wa Ibrahim 'ya'ya daga cikin wadannan duwatsu. 9
Yanzu kuwa, an rigaya an sa gatari a gindin itatuwa.
Sabili da haka, duk itacen da bai ba da 'ya'ya masu
kyau ba za a sare shi kasa a kuma jefa shi cikin wuta.”
10 Sai mutanen da ke cikin taron jama'ar suka tambaye
shi cewa, “To me za mu yi?” 11 Ya amsa ya ce masu,
“Idan wani yana da taguwa biyu, sai ya ba wanda
bashi da ita daya, kuma wanda yake da abinci ya yi
haka nan.” 12 Masu karban haraji ma suka zo domin a
yi masu baftisma, suka ce masa, “Malam, me za mu
yi?” 13 Ya ce masu, “Kada ku karba kudi fiye da yadda
aka umarce ku.” 14 Wasu sojoji ma suka tambaye shi
cewa, “To, mu fa? Yaya za mu yi?” Ya ce masu, “Kada
ku kwace wa wani kudi, kada ku kuma yi wa wani
zargin karya. Ku dogara ga albashinku.” 15 Ana nan
da mutane ke sauraron zuwan Almasihu, kowa yana
ta tunani a zuciyar sa game da Yahaya, ko shi ne
Almasihu. 16 Yahaya ya amsa ya ce masu duka, “Game
da ni dai, na yi maku baftisma da ruwa, amma akwai
wani tafiye wanda ya fi ni iko, ban ma isa in kwance
maballin takalmansa ba. Shi zai yi maku baftisma da
Ruhu Mai Tsarki da kuma wuta. 17 Kwaryar shikarsa
na hanun sa domin ya share masussukarsa da kyau
ya kuma tara alkama a cikin rumbunsa. Amma zai
kona buntun da wuta marar mutuwa. 18 Da gargadi
masu yawa ya yi wa mutanen wa'azin bishara. 19
Yahaya kuma ya tsauta wa sarki Hirudus domin ya
auri matar dan'uwansa, Hiruduya, da kuma sauran
abubuwan da Hirudus ya yi. 20 Amma Hirudus ya
kara yin wani mugun abu. Ya sa an kulle Yahaya
a cikin kurkuku. 21 Ana nan, lokacin da ake yiwa
dukan mutane baftisma, aka yiwa Yesu mai baftisma.
Lokacin da yake yin addu'a, sai sama ta bude, 22 kuma
Ruhu Mai Tsarki ya sauko masa a kamanin kurciya, sai
wata murya ta fito daga sama, “Kai ne kaunataccen
Da na. Ina jin dadin ka.” 23 Ana nan Yesu da kansa,
da ya fara, yana kimanin shekara talatin. Shi dan
(kamar yadda ake tsammani) Yusufu ne, dan Heli,
24 dan Matat, dan Lawi, dan Malki, dan Yanna, dan
Yusufu, 25 dan Matatiya, dan Amos, dan Nahum, dan
Hasli, dan Najjaya, 26 dan Ma'ata, dan Matatiya, dan
Shimeya, dan Yuseka, dan Yoda, 27 dan Yowana, dan
Resa, dan Zarubabila, dan Shiyaltiyel, dan Niri, 28
dan Malki, dan Addi, dan Kosama, dan Almadama,
dan Er, 29 dan Yosi, dan Aliyeza, dan Yorima, dan
Matat, dan Lawi, 30 dan Saminu, dan Yahuda, dan
Yusufu, dan Yonana, dan Aliyakima, 31 dan Malaya,
dan Mainana, dan Matata, dan Natan, dan Dauda, 32
dan Yesse, dan Obida, dan Bu'aza, dan Salmon, dan
Nashon, 33 dan Amminadab, dan Adimi, dan Arama,
dan Hezruna, dan Feresa, dan Yahuda, 34 dan Yakubu,
dan Ishaku, dan Ibrahim, dan Tera, dan Nahor, 35 dan
Serug, dan Reyu, dan Feleg, dan Abiru, dan Shela, 36
dan Kainana, dan Arfakshada, dan Shem, dan Nuhu,
dan Lamek, 37 dan Metusela, dan Anuhu, dan Yaret,
dan Mahalel, dan Kainana, 38 dan Enosh, dan Shitu,
dan Adamu, dan Allah.

4 Sai Yesu, cike da Ruhu Mai Tsarki, ya dawo daga
kogin Urdun, sai Ruhu Mai Tsarki ya bishe shi zuwa
cikin jeji 2 kwana arba'in, shaidan kuma ya jarabce
shi. A kwanakin nan, bai ci abinci ba, kuma yunwa
ta kama shi bayan karshen lokacin. 3 Shaidan ya ce
masa, “Idan kai Dan Allah ne, ka umarci wannan dutse
ya zama gurasa.” 4 Yesu ya amsa masa, “A rubuce
yake, 'Ba da gurasa kadai Mutum zai rayu ba.'” 5
Sai shaidan ya kai shi zuwa wani tudu mai tsawo,
ya kuma nuna masa dukan mulkokin duniyan nan a
dan lokaci. 6 Shaidan ya ce masa, “Zan ba ka iko ka
yi mulkin dukan wadannan, da dukan daukakarsu.
Zan yi haka domin an ba ni su duka in yi mulkinsu,
kuma ina da yanci in ba dukan wanda na ga dama. 7
Saboda da haka, idan ka rusuna ka yi mani sujada,
dukansu za su zama naka.” 8 Amma Yesu ya amsa ya
ce masa, “A rubuce yake, 'Dole ne Ubangiji Allahnka
za ka yi wa sujada, shi kadai kuma za ka bauta wa.” 9
Sai shaidan ya kai Yesu Urushalima, ya tsayadda shi
a bisan kololuwar haikali, kuma ya ce masa, “Idan
kai Dan Allah ne, ka jefas da kanka kasa daga nan. 10
Domin a rubuce yake, 'Zai ba mala'ikunsa umarni su
kiyaye ka, su kuma tsare ka,' 11 kuma, 'Za su daga
ka sama a hannunsu, don kada ka yi tuntube a kan

dutse.” 12 Yesu ya amsa masa cewa, “An fadi, 'Kada ka
gwada Ubangiji Allahnka.'” 13 Da shaidan ya gama yi
wa Yesu gwaji, sai ya kyale shi sai wani lokaci. 14 Sai
Yesu ya koma Galili cike da ikon Ruhu, kuma labarinsa
ya bazu cikin dukan wuraren dake wannan yankin. 15
Ya yi ta koyarwa a cikin majami'unsu, sai kowa na
ta yabon sa. 16 Wata rana ya zo Nazarat, birnin da
aka rene shi. Kamar yadda ya saba yi, ya shiga cikin
majami'a a nan ranar Asabaci, ya kuma tashi tsaye
domin ya karanta Nassi. 17 An mika masa littafin anabi
Ishaya, ya bude littafin ya kuma ga inda an rubuta, 18
“Ruhun Ubangiji yana kai na, domin ya shafe ni in yi
wa'azin Bishara ga matalauta. Ya aike ni in yi shelar
yanci ga daurarru, da kuma budewar idanu ga makafi,
in 'yantar da wadanda su ke cikin kunci, 19 in kuma
yi shelar shekarar tagomashi na Ubangiji.” 20 Sai ya
rufe littafin, ya mai da shi ga ma'aikacin majami'ar,
sai ya zauna. Dukan wadanda suke cikin majami'ar
suka zura Idanuwansu a kansa. 21 Sai ya fara masu
magana, “Yau wannan Nassi ya cika a kunuwanku.”
22 Dukan wadanda ke wurin sun shaida abin da ya fadi
kuma dukansu sun yi ta mamakin kalmomin alheri
da suke fitowa daga bakinsa. Suna cewa, “Wannan ai
dan Yusufu ne kawai, ko ba haka ba?” 23 Yesu ya ce
masu, “Lallai za ku fada mani wannan karin magana,
'Likita, ka warkar da kanka. Duk abin da mun ji wai ka
yi a Kafarnahum, ka yi shi a nan garinka ma.'” 24 Ya
sake cewa, “Hakika na fada maku, annabi baya samun
karbuwa a garinsa. 25 Amma na gaya maku gaskiya
akwai gwauraye da yawa cikin Isra'ila a zamanin Iliya,
lokacin da an rufe sammai shekaru uku da rabi babu
ruwa, lokacin da anyi gagarumar yunwa a duk fadin
kasar. 26 Amma ba a aiki Iliya zuwa wurin waninsu ba,
sai wurin gwauruwa da ke a Zarifat can kusa da Sidon.
27 Akwai kutare da yawa kuma a Isa'ila a zamanin
anabi Elisha, amma babu wanda aka warkar sai dai
Na'aman mutumin Suriya kadai. 28 Dukan mutanen
da ke cikin majami'a suka fusata kwarai sa'adda suka
ji wadannan zantattuka. 29 Suka tashi suka tura shi
zuwa wajen birnin, suka kai shi bakin dutsen da
aka gina garinsu a kai dominsu jefar da shi kasa. 30
Amma ya ratsa tsakaninsu ya yi gabansa. 31 Sannan
ya gangara zuwa Kafarnahum, wani birni a Galili.
Wata Asabaci yana koya wa mutane a cikin majami'a.
32 Sun yi mamaki kwarai da koyarwan sa, domin
maganarsa na da iko. 33 A wannan lokacin akwai wani
mutum a cikin majami'a mai kazamin ruhu, sai ya
yi kara da babbar murya, 34 “Ina ruwan mu da kai,
Yesu Banazarat? Ka zo domin ka hallaka mu ne? Na
san ko kai wanene! Kai ne Mai Tsarki na Allah!” 35
Yesu ya tsauta wa aljanin yana cewa, “Yi shiru ka fita
daga cikinsa!” Da aljanin ya jefar da mutumin kasa
a tsakiyarsu, ya fita daga cikinsa ba tare da yi masa
rauni ba. 36 Dukan mutanen suka yi mamaki, kuma
suna ta zancen wannan abu a tsakaninsu. Sun ce,
“Wanda irin maganganu kenan? Ya umarce kazaman
ruhohin da karfi da iko kuma sun fita.” 37 Saboda da
haka, an fara yada labarinsa zuwa dukan kewayen
yankin. 38 Sai Yesu ya bar majami'ar ya shiga gidan
Siman. A wannan lokacin, surukar Siman tana fama
da zazzabi mai zafi, sai suka roke shi dominta. 39 Sai
ya tsaya a kanta, ya tsautawa zazzabin, kuma ya rabu
da ita. Nan take, ta tashi ta fara yi masu hidima. 40
Da faduwar rana, mutane suka kawo wa Yesu dukan
wadanda suke ciwo da cuttuttuka dabam dabam. Ya
dora masu hannuwansa ya warkar da su. 41 Aljanu
kuma sun fita daga wadasunsu da dama, suna kuka
cewa, “Kai ne Dan Allah!” Yesu ya tsauta wa aljannun
ya kuma hana su magana, domin sun sani cewa shine
Almasihu. 42 Da safiya ta yi, ya kebe kansa zuwa wani
wurin da babu kowa. Jama'a da dama suna neman sa
suka zo inda yake. Sun yi kokari su hana shi barin
su. 43 Amma ya ce masu, “Dole in yi bisharar Allah a
wasu birane da dama, domin dalilin da aka aiko ni
nan kenan.” 44 Sai ya ci gaba da wa'azi cikin majami'u
dukan fadin Yahudiya.

5 Ya zama sa'adda mutane sun taru a wurin Yesu
suna sauraron maganar Allah, yana kuma yana
tsaye a bakin tabkin Janisarata. 2 Ya ga jiragen ruwa
biyu tsaye a bakin tabkin. Masu kamun kifin kuwa sun
fita daga cikin jiragen suna wanke tarunsu. 3 Yesu ya
shiga daya daga cikn jiragen wanda shike na Bitrus
ne, sai ya umarce shi ya dan zakuda da jirgin daga
bakin tabkin kadan zuwa cikin ruwa. Sai ya zauna ya
kuma koya wa mutane daga cikin jirgin. 4 Da ya gama
magana, ya ce wa Siman, “Zakuda jirgin zuwa wuri
mai zurfi sa'annan ka zuba tarunka domin kamu.” 5
Siman ya amsa ya ce, “Ubangiji, mun yi aiki dukan
dare bamu kama komai ba, amma bisa ga maganarka,
zan jefa tarun.” 6 Da sun yi haka, suka kama kifaye da
yawan gaske, har tarunsu suna yagewa. 7 Sai suka
roki abokan aikinsu da ke a dayan jirgin su zo su
taimake su. Suka zo sun cika jiragen biyu da kifaye,

har suka fara nutsewa. 8 Amma Siman Bitrus, da ya
ga haka, ya russuna a gaban Yesu, yana cewa, “Ka
rabu da ni Ubangiji, gama ni mai zunubi ne.” 9 Domin
ya yi mamaki, da dukan wadanda suke tare da shi,
sabili da yawan kifaye da suka kama. 10 Wannan ya
hada da Yakubu da Yahaya 'ya'yan Zabadi abokan
aikin Siman. Sai Yesu ya ce wa Siman, “Kada ka ji
tsoro, domin daga yanzu, za ka kama mutane.” 11 Da
sun kawo jiragensu waje kan kasa, suka bar komai
suka kuma bi shi. 12 Sa'adda yana daya daga cikin
biranen, wani mutum dauke da kuturta yana nan
wurin. Da ya ga Yesu, ya fadi bisa fuskarsa kasa yana
rokansa, yana cewa, “Ubangji, idan ka yarda, za ka iya
tsarkake ni.” 13 Yesu ya mika hanunsa ya taba shi,
yana cewa, “Na yarda. Ka tsarkaka.” Sai nan da nan,
kuturtar ta rabu da shi. 14 Ya umarce shi kada ya gaya
wa kowa, amma ya ce ma sa, “Tafi ka nuna kanka ga
firist sa'annan ka mika hadaya domin tsarkakewarka,
kamar yadda Musa ya umarta, a matsayin shaida
a garesu.” 15 Amma labarinsa ya bazu nesa, taron
mutane da yawa kuma suka zo wurinsa domin su ji
shi, su kuma samu warkarwa daga cututtukansu. 16
Amma ya kan janye zuwa wuraren da babu kowa ya yi
addu'a. 17 Ya zama daya a cikin kwanakin da yake
koyarwa, akwai Farisawa da malaman attaura da ke
zaune a wurin wandanda suka zo daga kauyukan da
suke kewaye da Galili da Yahudiya da kuma birnin
Urushalima. Ikon Ubangiji yana tare da shi domin
warkarwa. 18 A lokacin nan, wasu mutane suka zo
dauke da wani mutum shanyayye a kan tabarma, suka
kuma nemi yadda za su shigar da shi ciki, su kwantar
da shi a gaban Yesu. 19 Ba su iya samun hanyar da
za su shigar da shi ba saboda taron, sai suka hau
saman gidan, suka saukar da shi daga rufin, a kan
tabarman sa, zuwa tsakiyar mutanen, dai dai a gaban
Yesu. 20 Da ya ga bangaskiyarsu, Yesu ya ce, “Maigida,
an gafarta zunubanka.” 21 Marubuta da Farisawa suka
fara sukar wannan, suna cewa, “Wanene wannan da
ke sabo? Wa zai iya gafarta zunubi, idan ba Allah
kadai ba?” 22 Amma da Yesu ya fahimci abin da suke
tunani, sai ya amsa ya ce masu, “Don me kuke sukar
wannan a zuciyarku? 23 Wanne ne ya fi sauki a ce, 'An
yafe zunubanka' ko kuwa a ce, 'Tashi ka yi tafiya?”
24 Amma domin ku sani cewa Dan Mutum yana da
yancin gafarta zunubai a duniya, na ce maka, 'Tashi,
dauki tabarmanka, ka tafi gidanka.'” 25 Nan take, ya
tashi a gabansu ya dauki tabarma da yake kwance; sai
ya koma gidansa, yana daukaka Allah. 26 Kowa yana
ta mamaki kuma suka daukaka Allah. Suna cike da
tsoro, suna cewa, “Yau mun ga abubuwan al'ajibi.” 27
Bayan wadannan abubuwa sun faru, Yesu ya fito daga
can sai ya ga wani mai karban haraji mai suna Lawi
yana zama a wurin karban haraji. Ya ce masa, “Ka
biyo ni.” 28 Sai Lawi ya bar komai, ya tashi, ya bi shi.
29 Lawi kuma ya shirya gagarumar liyafa a gidansa,
kuma akwai masu karban haraji da yawa a nan, da
wasu mutane da ke zama a gaban teburin liyafar suna
cin abinci tare da su. 30 Amma Farisawa da Marubuta
suka fara korafi ga almajiransa, suna cewa, “Don
menene kuna ci da sha tare da masu karban haraji da
mutane masu zunubi?” 31 Yesu ya amsa masu, “Masu
lafiya basu bukatar likita, wadanda ke marasa lafiya
kadai ke bukatar likita. 32 Ban zo domin kiran masu
adalci ba, amma na zo ne domin kiran masu zunubi
zuwa ga tuba.” 33 Sun ce masa, “Almajiran Yahaya
sukan yi azumi da addu'a, kuma almajiran Farisawa
ma sukan yi haka. Amma almajiranka suna ci suna
sha?” 34 Yesu ya ce masu, “Akwai wanda zai sa abokan
ango su yi azumi, a lokacin da shi ango yana tare da
su? 35 Amma kwanaki na zuwa wadanda za a dauke
ango daga wurinsu, a kwanakin za su yi azumi.” 36 Sai
Yesu ya sake fada masu wani misali. “Babu wanda zai
yage kyalle daga sabuwar tufa, ya kuma yi amfani
da ita ya dinka tsohuwar tufa. Idan ya yi hakannan,
zai yage sabuwar tufar, kuma kyallen daga sabuwar
tufar ba zai dace da kyallen tsohuwar tufar ba. 37
Kuma, babu mutum da zai sa sabon ruwan inabi a
cikin tsofafin salkuna. Idan ya yi haka, sabon ruwan
inabin zai fasa salkunan, kuma ruwan inabin din zai
zube, salkunan kuma za su lallace. 38 Amma dole ne
a sa sabon ruwan inabi a sabobin salkuna. 39 Babu
wanda zai yi marmarin sabon ruwan inabi bayan da
ya sha tsohon, gama zai ce, “Tsohon ya fi sabon.”

**6** Ana nan wata Asabaci Yesu yana ratsawa cikin
gonar hatsi, almajiransa kuma na karyar zangarkun
hatsin, suna murtsukawa a hanayensu suna ci. 2
Amma wasu daga cikin Farisawa suka ce, “Saboda
me kuke yin abin da bai halatta a yi a ranar Asabaci
ba?” 3 Yesu ya amsa masu, ya ce, “Ba ku karanta
abin da Dauda ya yi a lokacin da yake jin yunwa
ba, shi da mutanen da ke tare da shi? 4 Ya je cikin
gidan Allah, ya dauki gurasar alfarwa ya kuma ci
daga ciki, ya kuma ba mazajen da ke tare da shi su

ci, ko da shike ya halarta ga Firistoci ne kadai su
ci.” 5 Sai ya ce masu, “Dan Mutum shi ne Ubangijin
asabaci.” 6 Ya kasance a wata ranar Asabaci ya shiga
cikin majami'a ya kuma koya wa mutane a can. Wani
mutum na can wurin wanda hannun damansa ya
shanye. 7 Marubuta da Farisawa na kallonsa su ga
ko zai warkar da wani a ranar Asabaci, domin su
samu dalilin zarginsa da yin abin da bai cancanta
ba. 8 Amma ya san abin da suke tunani, sai ya ce
wa mai shanyeyen hannun, “Tashi, ka tsaya a nan
tsakiyar jama'a.” Sai mutumin ya tashi ya tsaya a nan.
9 Yesu ya ce masu, “Ina tambayar ku, ya halatta a
ranar Asabaci a yi nagarta ko mugunta, a ceci rai ko a
hallaka shi? 10 Sai ya dube su duka, ya kuma ce wa
mutumin, “Mika hannunka.” Ya yi haka, sai hannunsa
ya koma lafiyayye. 11 Amma suka fusata kwarai, suka
yi shawara da junansu game da abin da za su yi da
Yesu. 12 Ya zama a kwanakin nan, ya hawo bisan
dutse domin ya yi addu'a. Ya ci gaba dukan dare yana
addua'a ga Allah. 13 Da safiya ta yi, ya kira almajiransa
zuwa wurinsa, ya kuma zabi goma sha biyu daga
cikinsu, wadanda ya kira su “Manzanni.” 14 Sunayen
Manzannin sune Siman (wanda ya kuma kira Bitrus)
da dan'uwansa, Andrawus, Yakubu, Yahaya, Filibus,
Bartalamawus, 15 Matta, Toma, Yakubu dan Halfa,
Siman, wanda ake kira Zaloti, Yahuda dan Yakubu,
16 da Yahuda dan Iskariyoti, wanda ya zama maci
amana. 17 Sai Yesu ya gangaro daga dutsen tare da su,
suka kuma tsaya a sarari. Almajiransa da yawa na nan
a wurin, tare da mutane da yawa daga Yahudiya da
Urushalima, da kuma bakin tekun Taya da Sidon. 18
Sun zo domin su ji shi, da kuma su sami warkarwa
daga dukan cututukansu. Mutane waddan da ke fama
da kazaman ruhohi ma sun sami warkarwa. 19 Dukan
taron jama'ar suna kokarin su taba shi domin ikon
warkarwa yana fitowa daga wurinsa, ya kuma warkar
da su duka. 20 Sai ya dubi almajiransa ya ce, “Masu
albarka ne ku matalauta, gama Mulkin Allah naku
ne. 21 Masu albarka ne ku masu yunwa yanzu, domin
za a kosar da ku. Masu albarka ne ku masu kuka a
yanzu, domin za ku yi dariya. 22 Masu albarka ne ku
idan mutane sun ki ku, suka nuna maku wariya suna
mai da sunayen ku na mugunta, domin Dan Mutum.
23 Za ku yi farin ciki a ranan nan kuna tsalle domin
murna, domin hakika za ku samu lada mai girma a
sama, domin haka kakannin-kakannin su suka yi wa
annabawa. 24 Amma kaitonku mawadata! Domin kun
rigaya kun samu ta'aziyar ku. 25 Kaitonku kosassu
a yanzu! Domin za ku ji yunwa nan gaba. Kaitonku
masu dariya yanzu! Domin za ku yi makoki kuna kuka
nan gaba. 26 Kaiton ku idan kowadanne mutane suna
yabon ku! Domin haka kakannin-kakanninsu suka
yi wa annabawan karya. 27 Amma ina ce maku ku
masu saurare na, ku kaunaci magabtanku, ku kuma
aikata nagarta ga wadanda suke kinku. 28 Ku albarkaci
masu zaginku, ku kuma yi addu'a ga wadanda suke
wulakanta ku. 29 Wanda ya mare ku a wannan kunci,
ku juya masa dayan. Idan wani ya dauki mayafinka,
kada ka hana masa taguwarka. 30 Ku bayar ga duk
wanda ya roke ku. Idan wani ya dauki wani abu da
ke naku, kada ku bidi ya mayar da shi. 31 Duk abin
da kake so mutane su yi maka, ka yi masu hakan
nan. 32 Idan ka kaunaci masoyan ka ne kadai, me
wannan zai amfane ka? Ko masu zunubi ma na kaunar
masoyan su. 33 Idan kuna nuna alheri ga wadan da
ke maku alheri kadai, menene ladan ku a nan? Ko
masu zunubi ma na yin hakan nan. 34 Idan kun ba da
rancen abubuwa ga mutanen da kuna sa zuciya zasu
mayar maku ne kadai, menene ribar ku a nan? Ko
masu zunubi suna ba masu zunubi rance, suna kuma
sa zuciya a mayar masu dadai gwargwado. 35 Amma
ku kaunaci magabtan ku, ku kuma nuna masu alheri.
Ku basu rance, kada ku sa zuciya a maido maku,
kuma sakamakon ku zai zama da girma. Za ku zama
yayan Mafifici, domin shi da kansa yana nuna jinkai
ga marasa godiya da miyagun mutane. 36 Ku zama
masu jinkai, domin Ubanku mai jinkai ne. 37 Kada ku
shari'anta, kuma ba za a shari'anta ku ba. Kada ku
kayar, ku ma ba za a kashe ku ba. Ku yafe wa wasu,
kuma za a yafe maku. 38 Ku bayar ga wasu, ku ma za a
ba ku da yawa. Magwaji dankararre, girgizajje har ya
cika yana zuba, za su zuba har cinyarku. Domin duk
ma'aunin da ku ka yi amfani da shi, da shi za a auna
maku. 39 Sai ya sake basu wani misali, “Makaho yana
iya yi wa makaho jagora? Idan ya yi haka, dukansu
biyu za su fada cikin rami, ko ba haka ba? 40 Almajiri
baya fin Malaminsa, amma duk wanda ya samu horo
sosai zai zama kamar malaminsa. 41 Don me kake
duba dan hakin da ke a idon dan'uwanka, amma
ba ka iya ganin gungumen da ke a idonka ba? 42
Don me za ka ce wa dan'uwanka, 'Dan'uwa, bari in
cire dan hakin da ke a idonka', bayan kai da kanka
ba ka iya ganin gungumen da ke a idonka ba? Kai
munafuki! Ka fara cire gungumen da ke a idonka,

sa'annan za ka gani da kyau yadda zaka cire hakin da
ke a idon dan'uwanka. 43 Domin babu itace mai kyau
da ke haifar rubabbun 'ya'ya, ko rubabben itace da
zai haifi kyawawan 'ya'ya. 44 Domin ana iya sanin
ko wani itace ta wurin 'ya'yan da yake bayarwa.
Domin mutane basu kan tsinki 'ya'yan baure a jikin
kaya, ko kuwa su dibi inabi daga jikin sarkakkiya. 45
Mutumin kirki, daga wadatar zuciyarsa ya kan ba da
yaya masu kyau, kuma mugu daga cikin muguwar
ajiyar zuciyarsa yake aikata mugunta. Domin daga
cikar zuciyarsa ne bakinsa yakan yi magana. 46 Don
me kuke ce da ni, 'Ubangiji, Ubangiji', amma ba ku
yin biyayya da magana ta? 47 Duk wanda ya zo wurina
ya ji kalmomina ya kuma yi biyayya da su, zan gaya
maku yadda yake. 48 Yana kama da mutum da ke
gina gida, wanda ya haka da zurfi zuwa cikin kasa
ya kuma gina harshashin gidan sa a kan dutse. Da
rigyawa ta zo, sai ruwa ya buga gidan, amma bai iya
girgiza shi ba, domin an gina shi da kyau. 49 Amma
duk mutumin da ya ji kalmomina ya kuma ki biyayya
da su, yana kamar mutum wanda ya gina gidansa a
kan kasa, babu harshashi. Amma da ambaliyan ruwa
ta buga gidan, nan take ya rushe, ragargajewar gidan
kuma da girma take.

7 Bayan da Yesu ya gama fadar dukan abubuwan
da zai fadi a jin kunnen dukan mutanen, sai ya
shiga Kafarnahum. 2 Bawan wani jarumi, wanda yake
kauna, ba shi da lafiya har ma ya kusa mutuwa. 3
Amma da ya ji labarin Yesu, jarumin ya aiki wadansu
dattawan Yahudawa, ya ce a roki Yesu ya zo ya ceci
bawansa daga mutuwa. 4 Sa'adda su ka zo kusa da
Yesu, su ka roke shi da gaske, cewa, “Wannan ya isa
ka yi masa haka, 5 saboda shi mai kaunar kasar mu
ne, kuma shi ne ya gina mana majami'a. 6 Sai Yesu ya
tafi tare da su. Amma sa'adda ya zo kusa da gidan
mutumin, jarumin ya aiki abokansa su ka ce da shi,
“Ubangiji kada ka damu domin ni ban isa ka zo gida
na ba. 7 Shi ya sa na ga ban isa in zo wurinka ba, ka
yi magana kadai bawa na kuwa zai warke. 8 Gama
ni ma mutum ne mai iko, ina da sojoji karkashina.
Ina iya cewa da wannan, 'Ka je' sai ya tafi, in kuma
ce da wani 'ka zo' sai ya zo, in kuma ce da bawa na,
'Yi kaza,' sai ya yi.” 9 Sa'adda Yesu ya ji haka, ya yi
mamakin mutumin, ya juya wajen taron da su ke
biye da shi, ya ce, “Na gaya maku, ko a cikin Isra'ila
ban sami wani mai bangaskiya irin wannan ba” 10
Daga nan wadanda a ka aika, suka dawo gida suka
tarar da bawan cikin koshin lafiya. 11 Wani lokaci
bayan wannan, ya zama Yesu yana tafiya wani gari
da ake kira Na'im. Almajiransa su na tare da shi, da
kuma taron mutane masu yawa. 12 Sa'adda ya kusa
da kofar garin, sai ga wani matacce ana dauke da
shi. Kuma shi kadai ne da a wurin mahaifiyarsa. Ita
kuwa gwauruwa ce, mutane da dama daga cikin gari
suna tare da ita. 13 Da ganin ta, sai Ubangiji ya cika
da tausayi a game da ita ya ce da ita, “Kada ki yi
kuka.” 14 Sai ya zo ya taba makarar, sai masu dauke
da shi su ka tsaya. Ya ce 'Saurayi na ce ma ka ka
tashi.” 15 Sai mataccen ya tashi ya fara yin magana.
Sai Yesu ya ba mahaifiyar danta. 16 Sai tsoro ya kama
su duka. Su ka kama yabon Allah, su na cewa, “An ta
da wani annabi mai girma a cikinmu” kuma “Allah
ya dubi mutanensa.” 17 Wannan labari na Yesu, ya
ba zu a cikin dukan Yahudiya da yankuna da su ke
kewaye. 18 Almajiran Yahaya suka gaya masa dukan
wadannan abubuwa. 19 Sai Yahaya ya kira biyu daga
cikin almajiransa, ya aike su wurin Ubangiji, suka ce
da shi, “Kai ne mai zuwan nan, ko akwai wani wanda
za mu saurari zuwansa?” 20 Sa'adda suka zo kusa da
Yesu, sai mutanen suka ce, “Yahaya Mai Baftisma,
ya aiko mu, mu tambaya, “Kai ne mai zuwan nan, ko
akwai wani wanda za mu saurari zuwansa?” 21 A cikin
wannan lokaci, ya warkar da mutane da yawa daga
cututtuka da matsaloli da miyagun ruhohi. Makafi
da yawa sun sami ganin gari. 22 Yesu, ya amsa ya
ce masu, “Bayan kun tafi, ku ba Yohanna rahoton
abin da ku ka ji da abin da ku ka gani. Makafi suna
ganin gari, guragu suna tafiya, ana kuma tsarkake
kutare. Kurame suna ji, ana tayar da matattu, ana
gaya wa matalauta labari mai dadi. 23 Mai albarka
ne mutumin da ya tsaya a kan ba da gaskiya gare ni
saboda ayukan da na ke yi.” 24 Bayan da mutanen
da Yahaya ya aiko suka tafi, Yesu ya fara yi wa taron
magana game da Yahaya. “Me ku ka tafi ku gani a
cikin hamada, ciyawa wadda iska ta ke girgizawa? 25
Amma me ku ka tafi domin ku gani, mutum mai saye
da tufafi masu taushi? Duba mutanen da su ke saye
da tufafi masu daraja, kuma suna rayuwa cikin jin
dadi suna fadar sarakuna. 26 Amma me ku ka tafi
domin ku gani, annabi ne? I, ina gaya ma ku, ya ma fi
annabi. 27 Wannan shine wanda aka rubuta a kansa,
“Duba, ina aika manzo na a gabanka, wanda za ya
shirya maka hanya a gabanka. 28 Ina gaya maku, a

cikin wadanda mata suka haifa, ba wanda ya fi Yahaya
girma. Duk da haka, wanda ya fi kankanta a mulkin
Allah, ya fi shi girma. 29 Sa'anda dukan mutane suka
ji haka, har da ma su karbar haraji, suka shaida Allah
mai adalci ne. Su na cikin wadanda Yahaya ya yi
wa baftisma. 30 Amma Farisawa da wadanda su ke
kwararru a cikin shari'ar Yahudawa, wadanda ba shi
ne ya yi masu baftisma ba, suka yi watsi da hikimar
Allah don kansu. 31 Sa'annan Yesu ya ce, "Da me zan
kamanta mutanen wannan zamani? Da me suka yi
kama? 32 Suna kama da yaran da suke wasa a kasuwa,
wadanda suke magana da junansu suna cewa, "Mun
yi maku busa, ba ku yi rawa ba. Mun yi makoki, ba ku
yi kuka ba." 33 Haka, Yahaya ya zo, bai ci gurasa ba,
bai sha ruwan inabi ba, amma ku ka ce, 'Aljani ne
yake mulkinsa. 34 Dan Mutum, ya zo, yana ci, yana
sha, amma, kuka ki shi, kuna cewa dubi mutum mai
hadama, mai shan ruwan inabi da yawa, abokin masu
karbar haraji da masu zunubi! 35 Amma hikimar Allah
tana shaidar dukan 'yayanta." 36 Wata rana wani
Bafarise, ya roki Yesu ya je ya ci abinci tare da shi.
Bayan da Yesu ya shiga gidan Bafarisen, ya zauna a
teburi domin ya ci abinci. 37 Sai ga wata mace mai
zunubi, ta fito daga cikin birni. Sa'anda ta ji labari
Yesu yana gidan Bafarisen, domin ya ci abinci. Ta
dauki tandun mai na alabastar mai kamshi. 38 Ta
tsaya kusa da Yesu tana kuka. Ta fara jika kafafunsa
da hawayenta, tana shafe kafafunsa da gashin kanta.
Tana yi wa kafafunsa sumba, tana shafe su da turare.
39 Sa'anda Bafarisen da ya gaiyaci Yesu, ya ga haka,
sai ya yi tunani a cikin ransa, da cewa, "In da wannan
mutum annabi ne, da ya gane ko wacce irin mace ce,
wannan da take taba shi, ita mai zunubi ce." 40 Yesu
ya amsa ya ce masa, "Siman, ina so in gaya maka wani
abu." Ya ce, "malam sai ka fadi!" 41 Yesu ya ce, "wani
mutum mai ba da bashi yana bin wadansu mutane
su biyu kudi, yana bin dayan sule dari, dayan kuma
yana bin sa sule hamsin. 42 Da yake ba su da kudin da
za su iya biyan sa, sai ya yafe masu, su duka biyu. A
cikin su biyu, wanne ne zai fi nuna kauna ga wannan
mutum?" 43 Siman ya amsa ya ce, "Ina tsammani
wanda ya yafe wa kudi da yawa." Yesu ya amsa ya ce
masa, "Ka shari'anta dai dai." 44 Yesu ya juya wajen
matar, ya ce da Siman, "Ka ga matan nan. Na shiga
gidanka. Ba ka ba ni ruwa domin kafafuna ba, amma
ita ta ba ni, da hawayenta ta wanke kafafuna, ta kuma
shafe su da gashin kanta. 45 Kai ba ka yi ma ni sumba
ba, amma ita ta yi, tun sa'adda na shigo nan ba ta
dena sumbatar kafafuna ba. 46 Kai ba ka shafe kai na
da mai ba, amma ita ta shafe kafafuna da turare. 47
Saboda haka, ita wadda ta ke da zunubi da yawa ta
bayar da mai yawa, ta kuma nuna kauna mai yawa.
Amma shi wanda aka gafarta wa kadan, ya kuma nuna
kauna kadan." 48 Daga nan sai ya ce mata, "An gafarta
zunubanki." 49 Wadanda su ke a nan zaune tare da
shi suka fara magana da junansu, "Wanene wannan
wanda har yake gafarta zunubai? 50 Sai Yesu ya ce da
matar, "Bangaskiyarki ta cece ki. Ki tafi da salama."

**8** Bayan haka, Yesu da almajiransa goma sha biyu, su
ka zagaya cikin birane da kauyuka dabam dabam,
suna wa'azi da shelar labari mai dadi game da mulkin
Allah, 2 mata da yawa wadanda Yesu ya warkar
daga aljanu da cututtuka iri iri suna tafiya tare da
su. A cikinsu akwai Maryamu wadda a ke ce da ita
Magadaliya, wadda ya fitar da aljanu bakwai daga
cikinta, 3 da Yuwana matar Kuza wakilin Hirudus,
da Suzanatu da kuma wasu mata da yawa. Daga
abin hannunsu suka tanada masu. 4 Wata rana aka
tara taron mutane da yawa, saboda mutane su na
zuwa daga birane da yawa domin su ga Yesu. Ya yi
magana dasu cikin misali. 5 "Wani mai shuka ya tafi
domin ya shuka iri. Sa'adda ya ke yafa iri, wadansu iri
suka fada a kan hanya. Sai mutane suka tattake su,
tsuntsaye kuma suka tsince wadansu suka cinye. 6
Wadansu kuma suka fada a kan duwatsu inda babu
kasa da yawa. Da suka tsaro suka fara girma, sai nan
da nan suka bushe saboda babu laima a wurin. 7
Wadansu irin kuma suka fada inda yake da kayayuwa.
Tsiretsiren kayayuwan suka fito tare da irin da aka
shuka, suka shake su yadda basu iya yin girma ba. 8
Amma wadansu irin suka fada a kan kasa mai kyau,
suka yi girma sosai suka ba da anfani da yawa, har rubi
dari." Bayan da Yesu ya fadi wadannan abubuwan, sai
ya yi kira gare su, "Duk mai kunnen ji, bari ya ji." 9
Sai almajiran Yesu suka tambaye shi ya gaya ma su
ma'anar labarin. 10 ya ce da su, "Ku aka ba dama ku
gane boyayyun abubuwa, na mulkin Allah. Amma ga
sauran mutane ina yi masu magana cikin misalai,
'Domin ko da sun gani ba za su gane ba, kuma ko da
sun ji ba za su fahimta ba." 11 To ga ma'anar misalin.
Irin shi ne maganar Allah. 12 Irin da ya fada a kan
hanya sune mutanen da suka ji maganar Allah amma
daga baya sai shedan ya zo ya dauke maganar daga

cikin hankulansu, domin kada su bada gaskiya su tsira.
13 Sa'annan, wadanda suka fada kan duwatsu sune
mutanen da, da zarar sun ji maganar, sukan karbe ta
da murna, amma ba su da sauyu; su kan bada gaskiya
na dan lokaci kadan kawai, da zaran gwaji ya same su
sai su ridda. 14 Irin da suka fada cikin kayayuwa, sune
mutanen da suka ji maganar, amma da suka ci gaba da
rayuwa, sai suka bari matsalolin rayuwa kamar dukiya
da jin dadin rayuwa suka fi karfinsu, sai ya zama ba
su iya bada 'ya'yan da suka yi girma ba. 15 Amma irin
da suka fada a kan kasa mai kyau, wadannan sune
mutanen da suka ji maganar, suka karbe ta da gaskiya
da zuciya daya, sun rike ta kam-kam, suna jimrewa
wurin ba da 'ya'ya. 16 Ba mai kunna fitila, ya rufe ta
da kasko, ko su sa ta a karkashin gado. Amma sai a
sa ta a wurin zaman ta domin duk wanda ya shigo
ya iya ganin hasken ta. 17 Babu abin da yake a boye
wanda ba za a tone shi ba, ko wani asiri da ba za ya
fito fili a san shi ba. 18 Ku yi hankali da yadda kuke ji,
domin duk mai abu, shi za a kara wa, kuma duk mara
abu, dan kadan da yake tunani yana da shi ma, za a
dauke." 19 Sai mahafiyar Yesu da 'yan'uwansa, su ka
zo wurinsa, amma ba su iya zuwa ko kusa da shi ba
saboda taron jama'a. 20 Sai wani ya gaya masa, "Ga
mahaifiyarka da 'yan'uwanka, su na tsayuwa a waje,
su na son ganin ka." 21 Amma Yesu ya amsa ya ce ma
su, "Mahaifiyata da 'yan'uwana sune wadanda suke
jin maganar Allah, suke yin biyayya da ita." 22 Wata
rana kuma Yesu ya shiga cikin jirgin ruwa, shi da
almajiransa. Ya ce masu, "Ina so mu je dayan ketaren
tafkin." Sai su ka fara tafiya domin su ketare tafkin.
23 Amma sa'adda su ke tafiya sai Yesu ya yi barci, sai
wata iska mai karfi ta taso cikin tafkin, nan da nan sai
jirgin ya fara cika da ruwa, kuma su na cikin hatsari.
24 Sai almajiran Yesu su ka zo su ka tashe shi daga
barci. Suka ce da shi, "Ya Shugaba! Ya Shugaba! Za
mu mutu!" Sai ya tashi ya umarci iskar, sai iskar mai
hauka da tumbatsar ruwan sun tsaya tsit. 25 Daga
nan sai ya ce da su, "Ina bangaskiyar ku?" Almajiran
suka tsorata suka yi mamakin abin da ya faru nan
take. Suka ce wa junansu, "Wanene wannan wanda
har zai ba iska da ruwa umarni kuma su yi masa
biyayya?" 26 Suka zo yankin Garasinawa, wanda ke
kusa da Gallili. 27 Sa'adda Yesu ya sauka kasa, sai wani
mutum daga wannan yankin ya tarbe shi. Wannan
mutum kuwa yana da aljanu. Mutumin ya dade ba ya
sa tufafi, kuma ba ya zama a gida. Maimakon haka,
sai a cikin kabarbura ya ke zama. 28 Sa'adda ya ga
Yesu, mutumin ya yi ihu da karfi, ya rusuna a gabansa
da babban murya ya ce, "Me zan yi da kai, Yesu,
Dan Allah Madaukaki? Ina rokonka, kada ka ba ni
azaba!" 29 Domin Yesu ya umarci aljanun su fita daga
cikinsa, domin sau da dama aljanun sukan kama shi.
Ko an daure mutumin da sarkoki an kuma tsare shi,
yakan tsuttsunke su, kazaman ruhohin sukan kora
shi cikin jeji. 30 Sa'annan Yesu ya tambaye shi, "Yaya
sunanka?" Sai ya ba da amsa, "Suna na dubbai." Ya
ce haka ne domin aljanu da yawa sun shiga wannan
mutum. 31 Aljanun suka yi ta rokon Yesu kada ya
ummarce su su shiga cikin rami mai zurfi. (Abyssos g12)
32 Akwai babban garken aladu su na kiwo a kan tsauni
kusa da wurin. Aljanun suka roki Yesu da ya barsu
su shiga cikin aladun, shi kuwa ya yarda masu. 33
Aljanun suka bar mutumin suka shiga cikin aladun,
sai garken aladun suka gangara kwari suka fada cikin
tafkin, suka nutse. 34 Lokacin da mutanen da su ke
kiwon aladun suka ga abin da ya faru, sai suka gudu!
Suka ba da rahoton abin da ya faru ga mutanen cikin
gari da na wannan kewayen. 35 Don haka, mutanen
da suka ji haka suka tafi domin su ga abin da ya faru,
suka zo wurin da Yesu yake, suka ga mutumin wanda
aljanu suka fita daga cikinsa. Suka ga ya na sanye da
tufafi, kuma ya na cikin hankalinsa, sai tsoro ya kama
su. 36 Mutanen da suka ga abin da ya faru, suka gaya
wa wadansu yadda aka warkar da mutumin da aljanu
suke iko da shi. 37 Sai dukan mutane wadanda suke
cikin yankin Garasinawa da wadanda suke kewaye,
suka roki Yesu da ya fita daga cikin yankin kasarsu
domin sun ji tsoro kwarai da gaske. Daga nan Yesu da
almajiransa suka shiga cikin jirgin ruwa suka koma.
38 Mutumin wanda aljanu suka fita daga cikinsa, ya
roki Yesu cewa, "Ka barni in tafi tare da kai!" Amma
Yesu ya sallame shi cewa, 39 "Ka koma gida ka gaya
wa mutanen ka abubuwa masu girma wadanda Allah
ya yi maka." Daga nan sai mutumin ya tafi yana ta
gayawa dukan mutanen birnin game da abubuwan da
Yesu ya yi masa. 40 Sa'adda Yesu ya dawo, mutanen
suka marabce shi, gama, dukansu suna jiransa. 41 Sai
ga wani mutum mai suna Yayirus, daya daga cikin
shugabannin majami'a, ya zo kusa da Yesu ya rusuna
da kansa a kasa. Ya roke shi domin ya zo gidansa, 42
saboda diyarsa mai kimanin shekara goma sha biyu
ta na bakin mutuwa, kuma ita kadai ce diya a gare
shi. Amma sa'adda yake tafiya, taron mutane da yawa

suna matsa shi. 43 Akwai wata mace a nan wadda
take zubar jini har shekara goma sha biyu. Ta kashe
kudinta duka a wurin likitoci, domin su warkar da ita
amma ba wanda ya iya warkar da ita. 44 Sai ta biyo ta
bayan Yesu ta taba habar rigarsa. Nan take sai zubar
jinin ya tsaya. 45 Yesu ya ce, “Wanene ya taba ni?”
Wadanda suke kewaye da shi, kowa ya ce bai taba shi
ba, Bitrus ya ce, “Shugaba, mutane da yawa suna ta
taruwa kewaye da kai suna ta matsowa kusa da kai.”
46 Amma Yesu ya ce, “Na sani, wani ya taba ni, domin
iko ya fita daga wurina.” 47 Sa'adda matar ta gane
cewa ba za ta iya boyewa ba, sai ta zo wurinsa cikin
tsoro. Ta durkusa a gaban Yesu, ta fada a gaban dukan
jama'a dalilin da ya sa ta taba shi kuma nan da nan
ta warke. 48 Sai ya ce da ita, “Diya, bangaskiyarki ta
warkar da ke. Tafi cikin salama.” 49 Yana cikin yin
magana, wani daga cikin gidan shugaban majami'ar
ya zo, ya ce, “Diyarka ta riga ta mutu, kada ka dami
malam.” 50 Amma sa'adda Yesu ya ji haka, sai ya ce da
shi, “Kada ka ji tsoro. Ka bada gaskiya za ta rayu.”
51 Sa'adda ya zo gidan, bai bar kowa ya shiga gidan
tare da shi ba sai Bitrus da Yahaya da Yakubu, da
mahaifiyar yarinyar da babanta. 52 Dukan mutane
a wurin, suna ta kuka da karfi saboda sun damu da
yarinyar ta mutu. Amma Yesu ya ce da su, “Ku dena
kuka! Ba mutuwa ta yi ba! Barci ta ke yi kawai!” 53
Mutanen suka yi ma sa dariyan reni, saboda sun sani
yarinyar ta mutu. 54 Amma ya kama hannun ta yayi
kira cewa, “Yarinya, na ce ki tashi!” 55 Nan da nan
ruhun ta ya dawo jikin ta sai ta tashi. Ya ce masu
su ba ta wani abu ta ci. 56 Iyayenta suka yi mamaki,
amma Yesu ya ce da iyayen kada su gaya wa kowa
abin da ya faru.

9 Ya kira almajiransa goma sha biyu, ya ba su iko
su fitar da kowanne irin aljani, su kuma warkar da
cututtuka daga mutane. 2 Ya aike su, su yi wa'azin
mulkin Allah, su kuma warkar da marasa lafiya. 3
Ya ce masu, “Kada ku dauki komi tare da ku domin
wannan tafiya. Kada ku dauki sanda, ko jakar matafiyi,
ko gurasa, ko kudi - Kada ma ku dauki taguwa biyu. 4
Dukan gidan da ku ka shiga, ku zauna a gidan har
zuwa lokacin da za ku tafi daga wannan yankin. 5
Dukan wadanda ba su marabce ku ba, sa'adda ku ke
barin wannan gari, ku karkabe kurar kafufunku a
matsayin shaida a kansu.” 6 Daga nan sai almajiran
suka tafi zuwa cikin kauyuka, suka yi ta shelar bishara,
su na warkar da mutane a ko'ina. 7 Ana nan Hirudus,
mai mulki, ya ji labarin dukan abubuwan da su ke
faruwa. Ya yi mamaki saboda wadansu mutane suna
cewa Yahaya mai yin Baftisma ne ya sake dawowa
da ransa. 8 Wadansu kuma suna cewa, annabi Iliya
ne ya sake bayyana, wadansu kuma suna cewa daya
daga cikin annabawa na da can ne ya sake bayyana
da rai. 9 Hirudus ya ce, “Ba zai yiwu Yahaya ne ba,
domin na datse masa kai. To, wanene wannan da
ni ke jin wadannan abubuwa a kansa?” Daga nan
sai ya cigaba da neman hanyar da zai ga Yesu. 10
Sa'adda manzannin suka dawo daga tafiyarsu, suka
gaya wa Yesu dukan abubuwan da suka yi. Daga
nan sai ya dauke su domin su tafi tare da shi zuwa
garin Baitsaida. 11 Amma sa'adda taron suka ji inda
Yesu ya tafi, sai suka bi shi can. Ya marabce su ya yi
masu jawabi a kan mulkin Allah, kuma ya warkar da
wadanda su ke bukatar warkarwa. 12 Da yake yamma
ta fara yi, sai almajiransa goma sha biyu suka zo suka
ce da shi, “Idan ka yarda ka sallami wannan babban
taron mutane dominsu shiga cikin kauyuka, da ke
kewaye da gonaki, dominsu sami abinci da wuraren
da za su kwana, da yake mu na nan a wurin da ba
kowa.” 13 Amma sai ya ce da su, “Ku ba su abin da za
su ci.” Suka amsa masa, “Dukan abin da muke da shi
shine, 'Yan dunkulen gurasa biyar da 'yan kifaye guda
biyu, ba za mu iya zuwa mu sawo abincin da zai ishi
mutanen nan su duka ba.” 14 Mutanen da suke wurin
sun kai kimanin mazaje dubu biyar. Sai Yesu ya ce
da almajiran, “Ku ce da mutanen su zauna kungiya-
kungiya, mutane hamsin a kowacce kungiya.” 15 Sai
almajiran suka yi haka, dukan mutanen suka zauna.
16 Ya dauki dunkulen gurasan guda biyar, da kifin
guda biyu, yana dubawa zuwa sama ya albakarce su,
sa'annan ya gutsuttsura, ya ba almajiran domin su
rarraba wa mutane. 17 Dukansu suka ci kowa ya koshi.
Daga nan almajiran suka tattara sauran abin da ya
rage, har kwanduna goma sha biyu suka cika! 18 Wata
rana Yesu yana yin addu'a shi kadai, sai almajiransa
suka zo sai ya tambaye su, “Wa mutane suke cewa
da ni?” 19 Suka amsa, “Wadansu suna cewa, Yahaya
mai yin Baftisma, wadansu suna cewa kai annabi Iliya
ne, har yanzu wadansu suna cewa kai wani cikin
annabawa na da can ne ya dawo da rai.” 20 Ya tambaye
su, “Ku fa? Wa kuke cewa da ni?” Bitrus ya amsa, “Kai
Almasihu ne wanda ya zo daga wurin Allah.” 21 Sai
Yesu ya gargade su da karfi, kada su gayawa kowa

haka tukuna. 22 Sa'annan ya ce, “Dan Mutum dole
ya sha wahalar abubuwa da yawa; dattawa za su ki
shi da manyan fristoci da marubuta, sa'annan za a
kashe shi. Bayan kwana uku, za a tashe shi da rai.”
23 Sai ya ce da su duka, “Dukan wanda ya ke so ya
biyo ni, dole ne ya yi musun kansa, ya dauki gicciyen
sa kulluyomin, ya biyo ni. 24 Dukan wanda yake so
ya ceci ransa, za ya rasa shi, amma dukan wanda ya
ba da ransa domina, za ya cece shi. 25 Wacce riba
mutum zai samu idan ya sami duniya duka, amma
ya rasa ransa? 26 Dukan wanda yake jin kunya ta da
magana ta, Dan Mutum ma zai ji kunyarsa, sa'adda ya
dawo cikin darajarsa da darajar Uba da ta mala'iku
masu tsarki. 27 Amma ina gaya maku wannan tabbas,
wadansu cikinku da ke nan tsaye, ba za su mutu ba
sai sun ga mulkin Allah.” 28 Kwana takwas bayan
Yesu ya fadi wadannan kalmomi, sai ya dauki Bitrus
da Yahaya da Yakubu, ya hau kan dutse domin ya yi
addu'a a can. 29 Sa'anda ya ke yin addu'a sai yanayin
fuskar sa ya canza sosai, tufafinsa kuma suka yi sheki
da haske kamar walkiya. 30 Nan da nan sai ga mutane
biyu suna magana da shi, wato Musa da Iliya. 31 Suka
bayyana da daraja kewaye da su, suka yi magana da
Yesu a kan tafiyarsa wadda za ta zo ba da dadewa ba
a cikin Urushalima. 32 Bitrus da almajiran da suke
tare da shi barci mai nauyi ya dauke su. Sa'adda suka
farka sai su suka ga daukakar Yesu; kuma suka ga
mutanen su biyu da ke tsaye tare da shi. 33 Sa'adda
Musa da Iliya suke shirin su bar wurin Yesu, sai Bitrus
ya ce, “Ya shugaba, ya yi kyau da muke a nan. Zai yi
kyau mu yi runfuna uku, daya dominka, daya domin
Musa, daya kuma domin Iliya.” Amma hakika bai san
abin da ya ke fadi ba. 34 Sa'adda yake fadin haka sai
wani girgije ya zo ya rufe su. Sai suka ji tsoro sa'adda
girgijen ya kewaye su. 35 Sai ga wata murya daga
cikin girgijen tana cewa, “Wannan Dana ne wanda na
zaba, ku ji shi.” 36 Sa'adda muryar ta gama magana,
Yesu yana nan shi kadai. Suka yi shiru ba su iya cewa
kome ba a kan abin da suka gani a kwanakin nan. 37
Washe gari, da suka sauko daga kan dutsen, sai taron
mutane da yawa suka zo wurinsa. 38 Nan da nan, wani
mutum daga cikin taron mutanen ya yi magana da
karfi, “Mallam, kayi wani abu dominka taimaki da
na, shi kadai ne gare ni. 39 Mugun ruhu ya kan hau
kansa, ya sa shi ya yi ta magowa. Ya kan girjiza shi
da karfi ya sa bakinsa ya yi ta kumfa. Da kyar ya ke
rabuwa da shi, kuma ya kan ji masa ciwo ba kadan
ba bayan da ya bar shi. 40 Na roki almajiran ka su
umurci mugun ruhun ya fita daga cikinsa, amma ba
su iya ba!” 41 Yesu, ya amsa, ya ce, “Ku karkatattun
tsara marasa bangaskiya, har yaushe zan zauna da
ku ina jimrewa da ku? “Kawo yaronka anan.” 42
Sa'adda yaron yake zuwa, sai mugun ruhun ya fyada
yaron a kasa, ya jijjiga shi sosai. Amma Yesu ya tsauta
wa mugun ruhun, ya warkar da yaron. Sa'annan ya
mika yaron wurin mahaifinsa. 43 Dukansu suka yi
mamaki da girman ikon Allah. Amma sa'anda suke ta
yin mamaki a kan dukan al'ajiban da ya yi, ya ce da
almajiransa, 44 “Ku saurara da kyau a kan abin da zan
gaya maku, ba da dadewa ba za a bada Dan Mutum
ga mutane.” 45 Amma almajiran ba su gane abin da
yake nufi da haka ba, an hana su fahimta, domin
kada su gane abin da ya ke nufi tukuna, kuma suna
jin tsoron su tambaye shi. 46 Wani lokaci, almajiran
suka fara gardama a tsakaninsu game da wanene za
ya zama mafi girma a cikinsu. 47 Amma Yesu ya san
abin da suke tunani a zuciyarsu, sai ya kawo dan
karamin yaro ya tsaya a kusa da shi, 48 sai ya ce da su,
“Idan wani ya karbi dan karamin yaro kamar wannan
saboda ni, dai dai yake da ya karbe ni. Idan kuma
wani ya karbe ni, ya karbi wanda ya aiko ni kenan.
Wanda yake mafi kankanta a cikinku, shi ne mafi
mahimmanci.” 49 Yahaya ya amsa yace, “Ya shugaba,
mun ga wani mutum yana ba miyagun ruhohi umarni
su fita daga cikin mutane da sunanka. Sai muka ce
da shi ya dena yin haka saboda baya tare da mu.” 50
Amma Yesu ya ce, “Kada ku hana shi yin haka, domin
dukan wanda ba ya gaba da ku, yana tare da ku.” 51
Sa'adda rana ta kusato da zai hawo zuwa sama, ya
kudurta sosai zai tafi Urushalima. 52 Ya aiki wadansu
manzanni su shirya wuri dominsa kafin ya zo. Suka
shiga wani kauye a cikin kauyen Samariya domin su
shirya masa wuri a can. 53 Amma mutanen can ba
su karbe shi ba tun da ya ke Urushalima zai tafi. 54
Sa'adda biyu daga cikin almajiransa, wato Yakubu da
Yahaya suka ga haka, suka ce, “Ubangiji, kana so mu
umarci wuta ta sauko daga sama, ta hallaka su?” 55
Amma, ya juya ya tsauta masu. 56 Sai suka tafi wani
kauye dabam. 57 Da suna cikin tafiya a kan hanya, sai
wani mutum ya ce da shi, “Zan bi ka dukan inda za ka
tafi.” 58 Yesu ya amsa masa, “Dila suna da ramuka a
kasa inda za su shiga, tsuntsaye kuma suna da sheka,
amma Dan Mutum ba shi da inda zai kwanta.” 59 Yesu,
ya ce da wani mutumin kuma, “Ka biyo ni.” Amma

mutumin ya ce, “Ubangiji, ka bari in koma gida in
bizine mahaifina tukuna.” 60 Amma Yesu ya ce masa,
“Ka bar matattu su bizine matattunsu; amma kai ka
tafi ka yi wa mutane shelar mulkin Allah a ko'ina.” 61
Wani kuma ya ce, “Ubangiji zan tafi tare da kai, amma
bari in je gida inyi ban kwana da mutanena tukuna.”
62 Yesu ya ce da shi, “Dukan wanda ya fara huda a
gonarsa idan ya dubi baya, bai isa ya shiga mulkin
Allah ba.”

10 Bayan wadannan abubuwa, Ubangiji ya sake
nada wadansu saba'in ya aike su biyu biyu,
domin su tafi kowanne birni da wurin da yake niyyan
zuwa. 2 Ya ce da su, “Girbin yana da yawa, amma
ma'aikatan sun yi kadan. Saboda haka kuyi addu'a
sosai ga Ubangijin girbin, domin ya aiko da ma'aikata
cikin gonarsa. 3 Ku tafi, duba na aike ku kamar 'yan
raguna cikin kyarkyetai. 4 Kada ku dauki jakan kudi,
ko jakar matafiyi, ko takalma, kada ku gai da kowa
a kan hanya. 5 Dukan gidan da ku ka shiga, ku fara
cewa, 'Bari salama ta kasance a wannan gida.' 6 Idan
akwai mutum mai salama a gidan, salamar ku za ta
kasance a kansa, amma idan babu, salamar ku za ta
dawo wurinku. 7 Ku zauna a wannan gidan, ku ci
ku sha abin da suka tanada maku. Gama ma'aikaci
ya wajibci ladansa. Kada ku bi gida gida. 8 Dukan
birnin da ku ka shiga kuma sun karbe ku, ku ci abin
da suka sa a gabanku. 9 Ku warkar da marasa lafiyar
da ke wurin. Ku ce da su, 'Mulkin Allah ya zo kusa da
ku.' 10 Amma dukan birnin da ku ka shiga, idan ba
su karbe ku ba, ku tafi cikin titunansu, ku ce, 11 'Ko
kurar birninku da ta like a kafafunmu, mun karkabe
maku ita a matsayin shaida a kanku! Amma ku sani
mulkin Allah ya zo kusa da ku.' 12 Na gaya maku, a
ranar shari'a Saduma za ta fi wannan birni samun
sauki. 13 Kaiton ki, Korasinu! Kaiton ki, Baitsaida!
Ayyuka masu girma da aka yi a cikinku, da an yi su
a cikin Taya da Sidon, da sun tuba tuntuni a zaune
cikin toka da tufafin makoki. 14 Amma a ranar shari'a
Taya da Sidon za su fi ku samun sauki. 15 Ke kuma
Kafarnahum, kina tsammani har zuwa sama za a
daukaka ki? Babu, za a gangarar dake har zuwa hadas.
(Hadēs g86) 16 Wanda ya saurare ku ya saurare ni, wanda
ya ki ku, ya ki ni, kuma wanda ya ki ni, ya ki wanda
ya aiko ni.” 17 Su saba'in din suka dawo da murna,
suna cewa, “Ubangiji, har ma aljanu suna yi mana
biyayya, a cikin sunanka.” 18 Sai Yesu ya ce masu, “Na
ga Shaidan yana fadowa daga sama kamar walkiya. 19
Duba, na ba ku iko ku taka macizai da kunamai, da
kuma kan dukan ikon magabci, kuma ba zai iya yin
illa a gareku ba ko kadan. 20 Amma duk da haka kada
ku yi murna a kan wannan kadai cewa ruhohi suna yi
maku biyayya, amma ku yi murna domin an rubuta
sunayenku a cikin sama.” 21 Cikin wannan lokacin,
ya yi farin ciki kwarai cikin Ruhu Mai Tsarki, ya ce,
“Na ba ka girma, ya Uba, Ubangijin sama da kasa.
Domin ka rufe wadannan abubuwa daga masu hikima
da ganewa, ka bayyana su ga wadanda ba koyayyu
ba ne, kamar kananan yara. I, Uba gama haka ne ya
gamshe ka.” 22 Dukan abu, Ubana ya damka su gare
ni, kuma babu wanda ya san Dan, sai Uban, kuma ba
wanda ya san Uban, sai Dan. Sai kuma wanda Dan
ya yi niyyar ya bayyana Uban a gareshi.” 23 Ya juya
wajen almajiran, ya ce da su a kadaice, “Masu albarka
ne su wadanda suka ga abin da kuke gani. 24 Na fada
maku, annabawa da yawa, da sarakuna da yawa sun
so da sun ga abubuwan da kuke gani, amma ba su
gani ba. Kuma sun so da sun ji abubuwan da kuke ji,
amma ba su ji su ba.” 25 Sai ga wani malamin shari'ar
Yahudawa, ya zo ya gwada shi da cewa, “Malam, me
zan yi domin in gaji rai na har abada?” (aiōnios g166) 26
Sai Yesu ya ce masa, “Yaya kake karanta abin da aka
rubuta cikin shari'a?” 27 Ya amsa ya ce,”Dole ne ka
kaunaci Ubangiji Allah da dukan zuciyarka, da dukan
ranka da dukan karfinka, da dukan lamirinka. Ka
kuma kaunaci makwabcinka kamar kanka.” 28 Yesu ya
ce ma sa, “Ka amsa daidai, idan ka yi haka za ka rayu.”
29 Amma, malamin ya na so ya 'yantar da kansa, sai ya
ce da Yesu, “To, wanene makwabcina?” 30 Ya amsa
ya ce, “Wani mutum yana tafiya daga Urushalima za
shi Yariko. Sai ya fada hannun mafasa, suka tube shi,
suka kwace dukan abin da ya ke da shi, suka yi masa
duka, suka bar shi kamar matacce. 31 Ya zama sai ga
wani firist ya na bin wannan hanya, da ya gan shi sai
ya bi ta gefe daya ya wuce. 32 Haka kuma sai ga wani
Balawi, sa'adda ya zo wurin, ya gan shi sai ya bi ta
wani gefe ya wuce shi. 33 Amma wani Basamariye,
ya na tafiya sa'adda ya zo wurin da mutumin yake,
sa'adda ya ga mutumin sai tausayi ya kama shi. 34 Ya
zo inda mutumin yake, ya daure masa raunukan da
aka ji masa, yana shafa masu mai da ruwan inabi. Ya
dora shi a kan dabbarsa ya kawo shi wurin kwana, ya
kula da shi 35 Washegari ya kawo dinari biyu, ya ba
mai wurin kwanan ya ce 'Ka kula da shi, idan ma ka
kashe fiye da haka, idan na dawo zan biya ka.' 36 A

cikinsu ukun nan, wanene kake tsammani makwabcin
wannan mutum da ya fada hannun 'yan fashi?" 37 Sai
malamin ya ce, "Wannan da ya nuna masa jinkai"
Sai Yesu yace masa, "Ka je kai ma ka yi haka." 38
Sa'adda suke tafiya, sai ya shiga cikin wani kauye, sai
wata mata mai suna Marta ta marabce shi a gidanta.
39 Tana da 'yar'uwa mai suna Maryamu, wadda ta
zauna a kafafun Ubangiji tana jin abin da yake fadi.
40 Amma ita Marta ta na ta kokari ta shirya abinci.
Sai ta zo wurin Yesu ta ce, "Ubangiji, ba ka damu ba
'yar'uwata ta bar ni ina ta yin aiki ni kadai? Ka ce da
ita ta taya ni." 41 Amma Ubangiji ya amsa ya ce da ita,
"Marta, Marta, kin damu a kan abubuwa da yawa, 42
amma abu daya ne ya zama dole. Maryamu ta zabi
abu mafi kyau, wanda ba za a iya kwace mata ba."

11 Wani lokaci, Yesu yana yin addu'a a wani wuri,
sai daya daga cikin almajiransa yace da shi,
"Ubangiji, ka koya mana yin addu'a kamar yadda
Yahaya ya koya wa almajiransa." 2 Yesu ya ce ma
su, "Sa'anda ku ke yin addu'a ku ce, 'Uba a tsarkake
sunanka. Mulkin ka ya zo. 3 Ka ba mu abin da za
mu ci a kowacce rana. 4 Gafarta mana zunubanmu,
kamar yadda muke gafarta ma wadanda suke mana
laifi. Kada ka kai mu cikin jaraba.'" 5 Yesu ya ce
masu, "Wanene a cikinku idan yana da aboki, za ya je
wurinsa da tsakar dare ya ce masa, ''Aboki, ka ba ni
rancen dunkulen gurasa guda uku, 6 da ya ke wani
abokina ya iso yanzu daga tafiya, kuma ba ni da abin
da zan ba shi ya ci,' 7 Sai wanda yake ciki, ya amsa, ya
ce, 'Kada ka dame ni. Na riga na rufe kofa ta, kuma
ni da yarana mun riga mun kwanta. Ba zan iya tashi
in ba ka gurasa ba.' 8 Na fada maku, ko da bai tashi
ya ba ka gurasar ba, a matsayin abokinsa, ba ka ji
kunya ba, ka nace da rokonsa, za ya tashi ya ba ka
dukan yawan gurasar da kake bukata. 9 Ni kuma ina
ce maku, ku roka za a ba ku; ku nema za ku samu; ku
kwankwasa za a bude maku. 10 Domin dukan wanda
yake roko ya na karba; dukan wanda ya ke nema kuma
yana samu; kuma wanda yake kwankwasawa, za a
bude masa. 11 Wanne uba ne a cikinku, idan dansa ya
tambaye shi kifi, zai ba shi maciji a maimakon kifi?
12 Ko kuwa idan ya tambaye shi kwai, za ya ba shi
kunama? 13 To, da yake ku da kuke masu mugunta
kun san ku ba 'yanyan ku abu mai kyau. Yaya fa ga
Ubanku wanda yake cikin sama, za ya ba da Ruhu Mai
Tsarki ga wadanda suka roke shi?" 14 Wani lokaci,
Yesu yana fitar da wani beben aljani. Sa'adda aljanin
ya fita, sai mutumin da yake bebe ya yi magana. Sai
taron mutanen suka yi mamaki! 15 Amma, wadansu
daga cikin mutanen suka ce, "Da ikon Ba'alzabuba
sarkin aljanu ne yake fitar da aljanu." 16 Wadansu
suka gwada shi, suka nemi ya nuna masu wata alama
daga sama. 17 Amma Yesu da yake ya san tunaninsu,
ya ce da su, "Dukan mulkin da ya rabu biyu, gaba
da kansa, ya rushe kenan, kuma idan gida ya rabu
biyu, gaba da kansa za ya fadi. 18 Idan Shaidan ya
rabu biyu gaba da kansa, ta yaya mulkinsa zai iya
tsayawa? Gama kun ce ina fitar da aljanu ta wurin
Ba'alzabuba. 19 Idan ni na fitar da aljanu ta wurin
Ba'alzabuba, ta wurin wa wadanda suke bin ku suke
fitar da aljanu? Saboda haka, su ne zasu zama masu yi
maku shari'a. 20 Amma idan daga wurin Allah na ke
fitar da aljanu, to, ya zama ke nan mulkin Allah ya zo
wurinku. 21 Idan mutum mai karfi, mai kayan fada
ya tsare gidansa, kayansa za su tsira. 22 Amma idan
wani mutum wanda ya fi shi karfi ya zo ya ci nasara a
kansa, zai dauke kayan fadan daga wurin mutumin,
kuma ya kwashe kayansa. 23 Wanda ba ya tare da ni,
gaba da ni ya ke yi, kuma wanda ba ya tattarawa tare
da ni, watsarwa yake yi. 24 Idan kazamin ruhu ya
fita daga cikin mutum, ya kan bi ta wurin busassun
wurare yana neman wurin da zai huta. Idan bai samu
ba sai ya ce, 'Bari in koma gidana inda na baro. 25
Sa'adda ya dawo, ya tarar an share gidan, an kuma
gyara shi tsaf. 26 Sai ya je ya dauko wadansu aljanu
guda bakwai wadanda su ka fi shi mugunta, su zo
su zauna a wurin. Sai karshen mutumin nan ya fi
farkonsa muni." 27 Ya zama, lokacin da ya ke fadin
wadannan abubuwa, wata mace ta tada muryarta a
cikin taron mutanen ta ce da shi, "Mai albarka ne
cikin da ya haife ka, da maman da ka sha." 28 Sai
shi kuma ya ce, "Masu albarka ne wadanda suke jin
maganar Allah suke yin biyayya da ita." 29 Lokacin da
mutane suke kara taruwa, sai ya fara cewa, "Wannan
tsara, muguwar tsara ce. Ta na neman alama, Ko da
yake ba wata alamar da za a bata sai irin ta Yunusa.
30 Domin kamar yadda Yunusa ya zama alama ga
mutanen Neneba, haka kuma Dan Mutum za ya zama
alama ga wannan tsara. 31 Sarauniyar Kudu, za ta
tsaya ta yi shari'a da mutanen wannan tsara, kuma za
ta kashe su, gama ta zo daga wuri mai nisa domin ta
saurari hikimar Sulaimanu. Kuma ga wani wanda ya fi
Sulaimanu a nan. 32 Mutanen Neneba, za su tsaya

shari'a da matanen wannan tsara, kuma za su kashe
su. Gama sun ji wa'azin Yunusa sun tuba. Kuma ga
wani wanda ya fi Yunusa a nan. 33 Ba wanda zai kunna
fitila ya boye ta, ko kuwa ya sa ta a karkashin kasko,
amma zai sa ta a mazaunin ta domin dukan wanda
ya shiga dakin ya ga haske. 34 Idon ku shine fitilar
jikinku. Idan idonku yana gani sosai, jikinku zai cika
da haske. Amma idan idonku ba ya gani sosai, jikinku
zai cika da duhu. 35 Ku yi hankali fa, domin kada
hasken da ya ke wurinku ya zama duhu. 36 Idan dukan
jikinku yana cike da haske, babu duhu ko kadan, to
sai dukan jikinku ya zama kamar fitilar da take bada
haskenta a bisanku." 37 Sa'adda ya gama jawabi, sai
wani Bafarise ya ce da shi ya zo gidansa ya ci abinci,
sai Yesu ya shiga ya zauna. 38 Sai Bafarisen ya yi
mamaki da ganin bai wanke hannu kafin ya ci abinci
ba. 39 Amma sai Ubangiji ya ce da shi, "Ku Farisawa
kuna tsabtace bayan kofi da bangaji, amma cikin yana
cike da kazamta da mugunta. 40 Ku mutane marasa
tunani, wanda ya yi wajen, ba shine ya yi cikin ba? 41
Ku bayar da abin da ke ciki ga matalauta, kuma dukan
abu zai zamar maku da tsafta. 42 Amma kaitonku
Farisawa, gama kuna karbar zakka da daddoya da
karkashi da kowanne irin ganye na lambu, amma
kun watsar da adalci da kaunar Allah. Dole ne a yi
adalci, a kaunaci Allah, a yi sauran abubuwan kuma.
43 Kaitonku Farisawa, domin kuna so a ba ku wuraren
zama masu kyau a cikin masujadai, a kuma yi maku
gaisuwar bangirma a cikin kasuwanni. 44 Kaiton ku,
gama kuna kama da kabarbarun da ba yi masu shaida
ba, mutane kuwa suna tafiya akansu ba tare da saninsu
ba." 45 Wani malami a cikin shari'ar Yahudawa ya
amsa masa ya ce, "Malam, abin da ka ce ya bata mana
rai mu ma." 46 Sai Yesu ya ce, "Kaitonku malaman
shari'a! Gama kun dora wa mutane kaya mai nauyi
wanda ya fi karfinsu dauka. Amma ku, ko da dan yatsa
ba ku taba kayan ba. 47 Kaiton ku, gama kuna gina
abubuwan tunawa a kabuburan annabawa, alhali kuwa
kakanni-kakanninku ne suka kashe su. 48 Ya zama
kenan kuna sane da ayyukan kakanni-kakanninku,
domin sune suka kashe annabawan da kuke tunawa
da su. 49 Saboda wannan daliline hikimar Allah ta ce,
''Zan aika manzanni da annabawa a wurinsu, kuma
za su tsananta masu har ma za su kashe wadansu
daga cikinsu.' 50 Wannan tsarar, za ta dauki alhakin
jinin dukan annabawan da aka kashe tun kafuwar
duniya. 51 Tun daga jinin Habila, har zuwa jinin
Zakariya wanda aka kashe tsakanin bagadi da wuri
mai tsarki. I, na gaya ma ku za a nemi hakin su a
wurin wannan tsarar 52 Kaitonku malaman shari'a
na Yahudawa, domin kun dauke mabudin sani, ku da
kanku ba ku shiga ba, kuma kun hana masu shiga su
shiga." 53 Bayan da Yesu ya bar nan wurin, Marubuta
da Farisawa suka yi gaba da shi, suka yi jayayya da shi
a kan abubuwa da yawa, 54 suna kokari su kafa masa
tarko domin su kama shi a cikin kalmomin da yake
fadi.

12 Da jimawa kadan, bayan da mutane da yawa suka
taru kwarai har suna tattaka junansu. Sai ya fara
yin magana da almajiransa. "Ku yi lura da yisti na
Farisawa, wanda shine manufunci. 2 Amma ba abin da
ke rufe wanda ba za a tone ba, ba kuma abin da ke
boye wanda ba za a sani ba. 3 Saboda haka ba abin da
za ku fadi a asirce wanda ba za a ji shi a cikin sarari
ba. Abin da ku ka fadi da rada cikin lungu, za a yi
shelarsa a ko'ina. 4 Ina gaya maku abokaina, kada
ku ji tsoron wanda da za su kashe jiki. Bayan haka
kuma ba abin da za su iya yi. 5 Bari in gargade ku a
kan wanda za ku ji tsoronsa. Ku ji tsoron shi wanda
bayan ya kashe zai iya jefa ku cikin jahannama. I, ina
ce maku ku ji tsoronsa. (Geenna g1067) 6 Ba a kan sayar
da 'yan tsuntsaye biyar a kan anini biyu ba? Duk da
haka, Allah ba zai manta da ko daya daga cikinsu ba.
7 Har ma gashin da ke kan ku ya san yawan su. Kada
ku ji tsoro, ku kun fi tsuntsaye daraja a wurinsa. 8
Ina gaya maku, dukan wanda za ya shaida ni a gaban
mutane, Dan Mutum kuma za ya shaida shi a gaban
mala'kun Allah. 9 Kuma dukan wanda ya ki ni a gaban
mutane, za a ki shi a gaban mala'ikun Allah. 10 Dukan
wanda ya yi magana gaba da Dan Mutum, za a gafarta
masa. Amma shi wanda ya yi sabon Ruhu Mai Tsarki,
ba za a gafarta masa ba. 11 Idan suka kawo ku gaban
majami'a, ko gaban masu shari'a, ko gaban masu iko,
kada ku damu da abin da za ku fada domin ku kare
kanku. Ko kuwa abin da za ku ce. 12 Gama Ruhu Mai
Tsarki zai koya maku abin da za ku fadi a wannan
lokaci." 13 Sai wani a cikin taron ya ce masa, "Malam,
ka yi wa dan'uwana magana ya raba gado da ni 14
Yesu ya ce masa, "Kai, wanene ya sa ni in zama alkali,
ko matsakanci a kanku?" 15 Sai kuma ya ce masu, "Ku
yi lura kada ku zama masu hadama, gama ba abin
da mutum ya mallaka ne ya fi mahimmanci a cikin
rayuwar sa ba." 16 Sa'annan Yesu ya fada masu wani

misali, ya ce, “Gonar wani mutum ta bada amfani
sosai, 17 ya yi tunani, ya ce, 'Me zan yi, domin ba
ni da wurin da zan iya ajjiye amfanin gonata?' 18
Sai ya ce, na san abin da zan yi. Zan rushe rumbuna
na in gina wadansu manya-manya, a nan zan ajjiye
hatsi na da dukan abubuwa. 19 Sai in ce da raina, “Ya
raina, kana da abu da yawa da aka ajjiye dominka,
sai ka huta, ka ci, ka sha, ka yi murna.” 20 Amma
sai Allah ya ce da shi, 'Wawan mutum, a cikin daren
nan ana son ranka daga wurinka. Kayan da ka tara ka
shirya wa kanka, na wa za su zama?' 21 Haka wanda
ya tara wa kansa dukiya yake, idan ba shi da dukiya a
wurin Allah.” 22 Yesu, ya ce da almajiransa, “Saboda
haka ina cewa da ku, kada ku damu da rayuwarku,
wato, abin da za ku ci, ko abin da za ku sa a jikinku.
23 Gama rai ya fi abinci, jiki kuma ya fi tufafi. 24 Ku
dubi hankaki wadanda ba sa yin shuka, ba sa yin
girbi. Ba su da rumbuna ko dakunan ajjiya, amma
Allah ya na ciyar da su. Ku fa kun fi tsuntsaye daraja!
25 Wanene a cikinku ta wurin sha'awarsa za ya iya
karawa kansa kwanaki? 26 Idan ba ku iya yi wa kanku
dan karamin abu ba, me ya sa za ku damu da sauran
abubuwa? 27 Ku dubi furanni a daji - yadda suke yin
girma. Ba su kan yi aiki ba, ba su kan yi kadi ba. Ina
gaya maku, ko Sulaimanu, a cikin darajarsa, bai sa
tufafin da suka fi nasu kyau ba. 28 Idan Allah ya sa wa
ciyawa tufafi masu kyau haka, wadda yau tana nan,
gobe kuma a sa ta a wuta, ta yaya zai kasa sa maku
tufafi, ku masu kankantar bangaskiya! 29 Kada ku
damu da abin da za ku ci, ko abin da za ku sha, kuma
kada ku yi alhini. 30 Gama dukan al'umman duniya
suna neman wadannan abubuwa, kuma Ubanku ya
san kuna bukatar wada nan abubuwan. 31 Amma ku
bidi mulkinsa, wadannan abubuwa kuma za a kara
maku su. 32 Kada ku ji tsoro, ku 'yan kanana, domin
da murna Ubanku zai ba ku mulkin. 33 Ku sayar da
abin da ku ke da shi ku ba matalauta. Kuyi wa kanku
jakukkuna wadanda ba za su lalace ba, ku yi ajjiya
cikin sama inda abin ba ya karewa, inda barayi ba
za su iya zuwa ba, kwari kuma ba za su iya lalatawa
ba. 34 Domin inda dukiyarka take, can zuciyarka za
ta kasance kuma. 35 Ku rage tsawon tufafinku, ku yi
dammara, ya zama fitilarku tana ci koyaushe, 36 ku
kuma zama kamar wadanda suke jiran mai gidansu ya
dawo daga gidan buki, domin duk sa'adda ya zo ya
kwankwasa kofa, nan da nan za su bude masa. 37 Masu
albarka ne wadannan bayi, wadanda ubangijinsu za
ya tarar suna jiran dawowar sa. Gaskiya ni ke gaya ma
ku, zai yi dammara yasa su zazzauna ya ba su abinci
shi da kansa. 38 Ko da ubangijinsu ya zo da dare, ko da
tsakar dare, ya tarar da su a shirye suna jiransa. Masu
albarka ne wadannan bayi. 39 Kuma ku san wannan,
da mai gida ya san lokacin da barawo zai zo, ba zai
bari a fasa masa gida a shiga ba. 40 Sai ku zauna da
shiri fa domin ba ku san lokacin da Dan Mutum zai
dawo ba.” 41 Sai Bitrus ya ce masa, “Ubangiji, mu ka
ke fadawa wannan misali, ko ga kowa da kowa ne?” 42
Sai Ubangiji ya ce, “Wanne shugaba ne, mai aminci,
mai hikima kuma wanda ubangijinsa za ya damka
bayinsa a hannunsa, domin ya kula da su, ya ba su
abincinsu a kan lokaci? 43 Mai albarka ne wannan
bawa, wanda ubangijinsa za ya tarar da shi yana yin
abin da aka sa shi ya yi. 44 Hakika, ina gaya maku,
zai danka dukan malakarsa a gareshi. 45 Amma idan
wannan bawa, ya ce a cikin zuciyarsa, 'Ubangiji na
yayi jinkirin dawowa,' sai ya fara dukan bayin, maza
da mata abokan bautarsa, ya ci ya sha, ya bugu, 46
ubangijin bawan nan zai dawo a lokacin da bawan bai
sa tsammani ba, kuma a cikin lokacin da bai sani ba,
ya daddatsa shi gunduwa-gunduwa, ya kuma hada
shi da marasa aminci. 47 Bawan nan, ya san halin
ubagijinsa, amma bai shirya yayi abin da ubangijinsa
yake so ba. Zai sha duka da bulala da yawa. 48 Amma
shi wanda bai sani ba, kuma yayi abin da ba daidai ba,
ba zai sha duka da bulala da yawa ba. Dukan wanda
aka ba abu da yawa, za a kuma nemi abu da yawa
daga wurinsa. Kuma ga wanda aka ba abu da yawa
amana, za a nemi abu mafi yawa daga gareshi. 49
Na zo domin in sa wuta a duniya, na so da ta riga ta
kama. 50 Amma ni, ina da baftisma wadda za a yi mani
baftisma da ita, kuma na kagara, da an riga an yi ta!
51 Kuna zaton na zo duniya domin in kawo salama?
Na ce maku a'a, amma tsattsaguwa. 52 Daga yanzu za
a sami mutane biyar a cikin gida daya, kuma za su
rarrabu, mutane uku suna gaba da biyu, biyun kuma
suna gaba da ukun. 53 Da da mahaifi za su yi gaba da
juna, dan zai yi gaba da mahaifinsa. Mahaifiya za ta yi
gaba da diyarta, diya kuma gaba da mahafiyarta; uwar
miji za ta yi gaba da matar danta, matar da kuma gaba
da uwar mijinta.” 54 Yesu, ya kuma gaya wa taron,
“Da kun ga hadari ya taso daga yamma, nan da nan
sai ku ce za a yi ruwa, haka kuwa ya kan zama. 55
Idan iska tana busowa daga kudu sai ku ce za a yi zafi
mai tsanani, haka kuwa ya kan faru. 56 Munafukai,

kun iya fasarta yanayin kasa da sama, amma baku iya
fasarta abin da yake faruwa yanzu ba? 57 Me ya sa ba
ku iya gane abin da zai tamake ku? 58 Idan kuna tafiya
wurin shari'a da abokin husumarka, ka yi kokari ku
daidaita tun a kan hanya domin kada ya kai ka wurin
mai shari'a. Domin kada mai shari'a ya mika ka ga
mai tsaron kurkuku, shi kuwa mai tsaron kurkuku ba
zai nuna maka sani a cikin kurkuku ba. 59 Na gaya
maka, ba za ka iya fitowa ba sai ka biya dukan kudin
da a ke binka?

**13** A lokacin, wadansu mutane suka gaya masa
game da galilawa wadanda Bilatus ya gauraye
jininsu da hadayunsu. 2 Sai Yesu ya amsa masu yace
“Kuna tsammani wadannan Galilawa sun fi duk sauran
Galilawan zunubi ne, da suka sha azaba haka? 3 A'a,
ina gaya maku. In ba ku tuba ba, dukanku za ku halaka
kamarsu. 4 Ko kuwa mutane goma sha takwas din nan
da suna Siluwam wadanda hasumiya ta fado a kansu
ta kashe su, kuna tsamani sun fi duk sauran mutanen
Urushalima laifi ne? 5 Ina gaya maku ba haka bane.
Amma duk wanda ya ki tuba, dukanku za su hallaka”
6 Yesu ya fada wannan misali, “Wani mutum yana
da baure wanda ya shuka a garkar inabinsa sai ya
zo neman 'ya'yan itacen amma bai samu ba. 7 Sai
mutumin ya ce wa mai kula da garkar, “ka ga, shekara
uku kenan nake zuwa neman 'ya'yan wannan baure,
amma ban samu ba. A sare shi. Yaya za a bar shi ya
tsare wurin a banza? 8 Sai mai lura da garkar ya amsa
yace, 'Ka dan ba shi lokaci kadan in yi masa kaftu in
zuba masa taki. 9 In yayi 'ya'ya shekara mai zuwa to,
amma in bai yi 'ya'ya ba sai a sare shi!”' 10 Wata rana
Yesu yana koyarwa a wata majami' a ran Asabaci.
11 Sai, ga wata mace a wurin shekarunta goma sha
takwas tana da mugun ruhu, duk ta tankware, ba ta iya
mikewa. 12 Da Yesu ya gan ta, sai ya kira ta ya ce mata,
an warkar da ke daga wannan cuta.” 13 Sai Yesu ya
dora hannunsa a kanta, nan da nan sai ta mike a tsaye
ta fara daukaka Allah. 14 Amma shugaban majami'a
yayi fushi domin Yesu yayi warkarwa a ranar Asabaci.
Sai shugaban ya amsa yace wa jama'a, “Akwai ranaku
shida da ya kamata a yi aiki. Ku zo domin a warkar da
ku amma ba ranar Asabaci ba.” 15 Amma Ubangiji
ya amsa masa ya ce, “Munafukai! Ashe kowannenku
ba ya kwance Jakinsa ko Sa daga turkensa ya kai shi
banruwa ran Asabaci? 16 Ashe wannan 'yar gidan
Ibrahim, wanda shaidan ya daure ta shekara goma sha
takwas, wato ba za a iya kwance ta a ranar Asabaci
kenan ba? 17 Da ya fada wadannan abubuwa, dukansu
da suka yi adawa da shi suka kunyata, duk taron kuwa
suka yi ta farin ciki da abubuwa masu daraja da yayi.
18 Sai Yesu ya ce, “Yaya za a misalta mulkin Allah,
kuma da me zan kwatanta shi? 19 Yananan kamar
kwayar mastad, wanda wani mutum ya dauka ya jefa
ta a lambunsa, ta kuma yi girma ta zama gagarumin
itace, har tsuntsaye suka yi shekarsu a rassanta.” 20
Ya sake cewa, “Da me zan kwatanta mulkin Allah? 21
Yana kamar yisti wanda wata mace ta dauka ta cuda
da mudu uku na garin alkama don ya kumburar da
shi.” 22 Yesu ya ziyarci kowanne birni da kauye, a
hanyar sa ta zuwa Urushalima yana koyar da su. 23
Sai wani ya ce masa, “Ubangiji, wadanda za su sami
ceto kadan ne?” Sai ya ce masu, 24 “Ku yi kokari ku
shiga ta matsatsiyar kofa, domin na ce maku, mutane
dayawa za su nemi shiga amma ba za su iya shiga ba.
25 In dai maigida ya riga ya tashi ya rufe kofa, sannan
za ku tsaya a waje kuna kwankwasa kofar kuna cewa,
'Ubangiji, Ubangiji, bari mu shiga ciki'. Sai ya amsa
yace maku, 'Ni ban san ku ba ko daga ina ku ka fito.'
26 Sannan za ku ce, 'Mun ci mun sha a gabanka, ka
kuma yi koyarwa a kan titunanmu.' 27 Amma zai
amsa ya ce, “Ina gaya maku, ban san ko daga ina ku
ka fito ba, ku tafi daga wurina, dukanku masu aikata
mugunta!' 28 Za a yi kuka da cizon hakora a lokacin
da kun ga Ibrahim, da Ishaku, da Yakubu da dukan
annabawa a mulkin Allah amma ku-za a jefar da ku
waje. 29 Za su zo daga gabas, yamma, kudu, da arewa,
za su ci a teburin abinci a mulkin Allah. 30 Ku san
da wannan, na karshe za su zama na farko, na farko
kuma za su zama na karshe.” 31 Nan take, wadansu
farisiyawa suka zo suka ce masa, “Ka tafi daga nan
domin Hirudus yana so ya kashe ka.” 32 Yesu ya ce,
“Ku tafi ku gaya wa dilan nan cewa, 'Duba, na fitar da
aljanu, ina warkarwa yau da gobe, kuma a rana ta
uku kuwa zan gama aiki na.' 33 Ko da kaka, dole ne in
ci gaba da tafiyata yau, da gobe, da kuma jibi, don
bai dace a kashe annabi nesa da Urushalima ba. 34
Urushalima, Urushalima masu kisan annabawa, masu
jifan wadanda aka aiko gare ku. Sau nawa ne ina so
in tattara 'ya'yanki kamar yadda kaza take tattara
'ya'yanta a cikin fukafukanta, amma ba ki so wannan
ba. 35 Duba, an yashe gidanki. Ina kwa gaya maku ba
za ku kara ganina ba sai ran da kuka ce, 'Albarka ta
tabbata ga mai zuwa da sunan Ubangiji.'”

**14** Wata ranar Asabaci, ya shiga gidan wani daya
daga cikin shugabanin Farisawa domin cin abinci,
mutane kuwa suna sa masa idanu. 2 Sai ga wani a
gabansa mai ciwon fara. 3 Yesu ya tambaye masanan
attaura da Farisawa, “Ya halata a wakar a ranan
Asabaci, ko a'a?” 4 Amma suka yi shiru. Yesu kuwa
ya kama shi, ya warkar da shi, ya kuma sallame shi.
5 Sai yace masu, “Wanene a cikinku in yana da jaki
ko takarkari ya fadi a rijiya ran Asabaci, ba zai fitar
da shi nan da nan ba?” 6 Sai suka kasa ba da amsar
wadannan abubuwa. 7 Sa'adda Yesu ya lura da yadda
wadanda aka gayyato sun zabi mazaunan alfarma,
sai ya ba su misali yana ce masu, 8 “Sa'adda wani ya
gayyace ka zuwa bikin aure, kada ka zauna a wuri
mai daraja, domin yana yiwuwa an gayyaci wani
wanda ya fi ka daraja. 9 Sa'adda wanda ya gayyace ku
duka biyu ya zo, zai ce maka, 'Ka ba mutumin nan
wurinka,' sa'annan a kunyace za ka koma mazauni
mafi kaskanci. 10 Amma idan an gayyace ka biki,
sai ka je ka zauna a wuri mafi kaskanci, domin idan
wanda ya gayyace ka ya zo, yana iya ce maka, 'Aboki,
hawo nan mana'. Sannan za ka sami girma kenan a
gaban dukan wadanda kuke zaune tare a kan teburi.
11 Duk wanda ya daukaka kansa, za a kaskantar da shi,
wanda ya kaskantar da kansa, kuma daukaka shi za
a yi”. 12 Yesu ya ce wa mutumin da ya gayyace shi,
“Idan za ka gayyaci mutum cin abinci ko biki, kada
ka gayyaci abokanka, ko 'yan'uwanka, ko danginka,
ko makwabtanka masu arziki, kamar yadda suna iya
gayyatar ka, sai ya zama an maida maka. 13 Amma
idan za ka kira biki sai ka gayyace matalauta, da
nakasassu, da guragu, da makafi, 14 za ka kuwa sami
albarka da yake ba su da hanyar saka maka. Gama
za a saka maka a ranar tashin masu adalci.” 15 Da
daya daga cikin wadanda ke zama akan teburi da Yesu
ya ji wadannan abubuwa, sai ya ce masa, “Albarka ta
tabbata ga wanda zai ci abinci a mulkin Allah!” 16
Amma Yesu ya ce masa, “Wani mutum ne ya shirya
babban biki ya gayyaci mutane da yawa. 17 Da lokacin
biki ya yi, sai ya aiki bawansa ya ce wa wadanda
aka gayyata, “Ku zo, duk an shirya kome.” 18 Sai
dukansu, suka fara kawo dalilai. Na farko ya ce masa,
'Na sayi gona, lalle ne in je in gan ta. Ina rokonka
ka dauke mani.' 19 Sai wani ya ce, 'Na sayi shanu
garma biyar, ina so in gwada su. Ina ronkan ka, ka
dauke mani.' 20 Wani mutum kuma ya ce, 'Na yi
aure, don haka ba zan iya zuwa ba.' 21 Da bawan ya
zo ya fadi wa maigidansa wadannan abubuwa, sai
maigidan yayi fushi, ya ce wa bawansa, jeka da sauri
ka bi cikin titunan birni da kwararo-kwararo, ka kawo
gajiyayyu, da nakasassu, da makafi, da guragu.' 22 Sai
bawan ya ce, 'Maigida, abin da ka umarta an gama,
amma har yanzu da sauran wuri.” 23 Sai maigidan
ya ce wa bawan, 'Jeka, ka bi kwararo-kwararo da
hanyoyin karkara, ka rinjayi mutane su shigo, don a
cika gidana. 24 Gama ina gaya maku, babu ko daya
daga cikin mutanen da na gayyata da farko da zai
dandana bikina.” 25 Ana nan, taron suna tafiya tare da
shi, sai ya juya ya ce masu, 26 “Duk mai zuwa wurina
amma bai ki mahaifinsa da mahaifiyarsa, da matarsa,
da 'ya'yansa, da 'yan'uwansa maza da mata ba - I, har
da ransa ma, ba zai iya zama almajirina ba. 27 Duk
wanda bai dauki gijiyensa ya biyo ni ba, ba zai iya
zama almajirina ba. 28 Wanene a cikinku wanda yake
niyyar gina bene, da ba zai zauna ya yi lissafin abin da
zai kashe ba tun da farko, ko yana da ishashen kudi
da zai iya kare aikin? 29 Kada ya zama bayan da ya sa
harsashin ginin, ya kasa gamawa, har duk wadanda
suka gani su fara yi masa ba'a, 30 su rika cewa, ga
mutumin nan ya fara gini amma ya kasa gamawa.' 31
Ko kuwa wanne sarki ne, in za shi je yaki da wani
sarki, da ba zai zauna da farko ya yi shawara ya ga ko
shi mai jarumawa dubu goma zai iya karawa da dayan
sarkin mai jarumawa dubu ashirin ba? 32 In kuwa
ba zai iya ba, to tun wancan yana nesa, sai ya aiki
wakili ya kuma tambayo sharudan salama. 33 Haka
ma, ba wani a cikinku wanda bai rabu da duk abin da
ya mallaka ba, da zai iya zama almajirina.” 34 “Gishiri
abu ne mai kyau, amma idan gishiri ya sane, da me za
a dadada shi? 35 Ba shi da wani anfani a kasa, ko ya
zama taki. Sai dai a zubar kawai. Duk mai kunnen ji,
ya ji.”

**15** To sai duk masu karbar haraji da masu zunubi
suna ta zuwa wurin Yesu suna sauraronsa. 2
Dukan Farisawa da Marubuta suna ta gunaguni da
junansu, cewa, “Wannan mutum yana karbar masu
zunubi, har ma tare suke cin abinci.” 3 Yesu ya fadi
wannan misali, ya ce, 4 “Idan waninku yana da tumaki
dari, sai dayarsu ta bace, wato ba zai bar tasa'in da
taran nan a makiyaya, ya bi sawun wadda ta bata
gudan nan har sai ya same shi ba? 5 Idan kuwa ya
same ta, sai ya dauke ta a kafadarsa yana farin ciki. 6
In ya dawo gida, sai ya kira abokansa da makwabta,

yace masu, 'Ku taya ni murna don na samo tunkiyata
da ta bata.' 7 Ina gaya maku, haka kuma za a yi farin
ciki a sama, a kan mai zunubi guda da ya tuba, fiye
da kan masu adalci tassa'in da tara wadanda ba su
bukatar tuba. 8 Ko kuwa wacce mace ce, in tana da
kudi azurfa guda goma, in ta batar da daya, ba za ta
kunna fitila ta share gidan, ta yi ta neman shi har
sai ta same shi ba? 9 In kuwa ta same shi sai ta tara
kawayenta da makwabtanta, ta ce, 'Ku taya ni farin
ciki don na sami kudin nan nawa da ya bace.' 10
Haka nake gaya maku, abin farin ciki ne ga mala'ikun
Allah idan mai zunubi guda ya tuba." 11 Sai Yesu ya
ce, "Akwai wani mutum mai 'ya'ya biyu maza, 12
sai karamin ya ce wa mahaifinsa, 'Baba, bani rabona
daga cikin dukiyarka.' Sai mahaifinsa ya raba masu
dukiyarsa tsakaninsu. 13 Bayan 'yan kwanaki kadan,
sai karamin dan ya tattara duk mallakarsa, ya kama
hanya zuwa wata kasa mai nisa. A can ya batas da
kudinsa, yana sayan abubuwan da ba ya bukata, ya
kuma batas da kudinsa a wajen masha'a. 14 Bayan
da ya batas da duk abin da ya ke da shi, sai aka yi
babbar yunwa a kasar, sai ya shiga fatara. 15 Ya je ya
mika kansa domin aiki ga wani dan kasar, sai ya aike
shi cikin gonakinsa domin ya rika ba aladu abinci.
16 Har yayi marmarin ya ci daga cikin barbashin da
aladu suke ci, domin babu wanda yake ba shi wani
abu ya ci. 17 Amma da hankalinsa ya dawo, ya ce,
'Barorin mahaifina su nawa ne da suke da abinci
isasshe, amma ina nan a nan, ina mutuwa sabili da
yunwa! 18 Zan tashi, in tafi gun mahaifina, in ce masa,
"Baba, na yi wa sama zunubi, na kuma saba maka. 19
Ban cancanci a kara kira na danka ba; ka mai da ni
kamar daya daga cikin barorinka.'" 20 Sai ya tashi, ya
taho wurin mahaifinsa. Amma tun yana daga nesa, sai
mahaifinsa ya hango shi tausayi ya kama shi, ya ruga
a guje, ya rungume shi, ya yi ta sumbatar sa. 21 Dan
kuma ya ce masa, 'Baba, na yi wa sama zunubi, na
kuma saba maka. Ban isa a kara kira na danka ba.' 22
Amma mahaifinsa ya ce wa bayinsa, 'Ku yi hamzari
ku kawo riga mafi kyau, ku yafa masa. Ku sa masa
zobe a hanunsa da takalma a kafafunsa. 23 Sa'annan a
kawo kiwataccen marakin nan, a yanka. Mu yi buki!
24 Gama da na ya mutu a da, amma yanzu yana a raye.
Ya bata a da, amma a yanzu an same shi.' Sai suka fara
liyafa. 25 A wannan lokacin, babban dansa yana gona.
Da ya kai kusa da gida, ya ji ana kade-kade da raye-
raye. 26 Sai ya kira wani bawan gidan, ya tambayi
manufar wadannan abubuwa. 27 Bawan ya ce masa,
'Dan'uwanka ne ya dawo gida, mahaifinka kuma ya
yanka kiwataccen marakin nan, saboda ya dawo gida
lafiya.' 28 Amma dan'uwan ya yi fushi, ya ki ya shiga
ciki, mahaifinsa kuwa ya fito, ya roke shi. 29 Amma
babban dan ya amsa wa ubansa ya ce, 'Duba, duk
yawan shekarun nan da nake bauta maka, ban taba
karya umarnin ka ba, duk da haka ba ka taba bani ko
dan taure da zan yi shagali tare da abokaina ba, 30
amma da dan nan naka ya zo wanda ya fallasar da
dukiyarka a kan karuwai, ka yanka masa kiwataccen
marakin nan. 31 Sai mahaifin ya ce masa, 'Dana, ai
kullum kana tare da ni, duk abin da yake nawa naka
ne. 32 Amma, daidai ne a yi murna da farinciki, don
dan'uwan nan naka da ya mutu, amma yanzu yana da
rai, da ya bata, amma yanzu an same shi.'"

16 Yesu ya kuma ce wa almajiransa, "Akwai wani
mai arziki da yake da wakili, sai aka yi karan sa
da cewa wannan wakili yana fallasar masa da dukiya.
2 Sai mai arziki ya kira shi ya ce masa, 'Labarin me
nake ji game da kai? Kawo lissafin wakilcin ka, don
ba za ka sake zama wakili na ba.' 3 Sai wakilin ya ce
a ransa, 'Kaka zan yi, da yake maigida na zai karbe
wakilci daga hannuna? Gashi, ba ni da karfin noma
ina kuwa jin kunya in yi roko. 4 Na san abin da zan yi
domin idan an fitar da ni daga wakilcin, mutane su
karbe ni a gidajensu. 5 Sai wakilin ya kira kowanne
daya da maigidansa ke bi bashi, yace wa na farkon,
'Nawa maigida na yake bin ka?' 6 Ya ce, 'Garwan
mai dari.' Sai ya ce masa, 'Ga takardarka, maza ka
zauna, ka rubuta hamsin.' 7 Ya kuma ce wa wani,
'Nawa ake binka?' Ya ce, 'Buhu dari na alkama.' Ya
ce masa, 'Ga tarkardarka, ka rubuta tamanin.' 8 Sai
maigida ya yaba wa wakilin nan marar gaskiya saboda
wayonsa. Gama 'ya'yan zamanin nan a ma'ammalar su
da mutanen zamaninsu sun fi 'ya'yan haske wayo. (aiōn
g165) 9 Ina gaya maku ku yi abuta ta dukiya ta rashin
gaskiya, saboda idan ya kare, su karbe ku a gidaje
masu dauwama. (aiōnios g166) 10 Wanda yake da aminci
a karamin abu, mai aminci ne a babban abu, wanda
yake marar gaskiya a karamin abu, marar gaskiya ne a
babban abu. 11 Idan fa ba ku yi aminci da dukiya mara
adalci ba, wa zai amince maku da dukiya ta gaskiya?
12 Idan kuma ba ku yi aminci da kudin wani ba, wa
zai ba ku kudin da ke naku? 13 Ba bawan da zai iya
bauta wa iyayengiji biyu, ko dai ya ki daya, ya so daya

ko kuwa ya amince wa dayan, ya raina dayan. Ba za
ku iya bauta wa Allah ku kuma bauta wa dukiya ba."
14 Da Farisawa da ke da kaunar kudi suka ji dukan
wadannan abubuwa, suka yi masa ba'a. 15 Sai ya ce
masu, "Ku ne masu baratar da kanku a gaban mutane,
amma Allah ya san zuciyarku. Abin da mutane suke
girmamawa kwarai abin kyama ne a gun Allah. 16
Attaura da litattafan annabawa suna nan har zuwan
Yahaya. Tun daga lokacin nan ake yin bisharar mulkin
Allah, kowa kuma yana kokarin kutsawa zuwa cikinta.
17 Duk da haka, zai fi sauki sama da kasa su shude, da
ko digo daya na attaura ya shude. 18 Duk wanda ya
saki matansa ya auri wata ya aikata zina, kuma wanda
ma ya auri sakakkiya ya aikata zina. 19 Akwai wani
mai arziki, mai sa tufafi na alfarma masu tsada yana
shagalin sa kowace rana. 20 Aka ajiye wani gajiyayye a
kofarsa, mai suna liazaru wanda duk jikinsa miki ne,
21 Shi kuwa yana marmarin ya koshi da barbashin
da ke fadowa daga teburin mai arzikin nan har ma
karnuka sukan zo suna lasar mikinsa. 22 Ana nan sai
gajiyayyen nan ya mutu, malaiku kuma suka dauke
shi suka kai shi wurin Ibrahim. Mai arzikin ma ya
mutu, aka kuma binne shi, 23 yana cikin hades yana
shan azaba, sai ya daga kai ya hangi Ibrahim daga
nesa, da Li'azaru a kirjinsa. (Hadēs g86) 24 Sai ya yi kira
ya ce, 'Baba Ibrahim, ka ji tausayi na, ka aiko Li'azaru
ya tsoma dan yatsansa a ruwa ya sanyaya harshena,
don azaba nake sha a cikin wannan wuta.' 25 Amma
Ibrahim ya ce, 'Yaro, ka tuna fa a zamanka na duniya
ka sha duniyarka, ka kuma karba abubuwa masu kyau,
amma Li'azaru kuma sai wahala. Amma yanzu dadi
ake bashi a nan, kai kuwa kana shan azaba. 26 Banda
haka ma, akwai rami mai zurfi, domin wadanda suke
son ketarewa zuwa wurinku kada su iya, kada kuma
kowa ya ketaro zuwa wurinmu daga can.' 27 Sai mai
arziki ya ce, 'To ina rokonka, Baba Ibrahim, ka aike
shi zuwa gidan mahaifina - 28 domin ina da 'yan'uwa
maza biyar, ya je ya yi masu gargadi kada su ma su zo
wurin azaban nan.' 29 Amma Ibrahim ya ce, 'Suna da
Musa da annabawa; bari su saurare su.' 30 Sai mai
arziki ya amsa, 'A'a, Baba Ibrahim, idan wani daga
cikin matattu ya je wurinsu, zasu tuba.' 31 Amma
Ibrahim ya ce masa, 'In dai har basu saurari Musa da
na annabawa ba, ko da wani ya tashi daga matattu
ma, ba za su rinjayu ba.'"

# 17

Sai Yesu ya ce wa almajiransa, 'Babu shakka
akwai sanadodin tuntube da za su sa mu yin
zunubi amma kaiton wanda shine sanadin su! 2 Zai
gwammaci a rataya masa dutsen nika a wuyansa,
a jefar da shi a cikin teku fiye da wanda zai zama
sanadiyar tuntube ga wadannan kananan. 3 Ku kula
da kanku. Idan dan'uwanka ya yi laifi, ka tsauta
masa, in kuwa ya tuba ka yafe masa. 4 Idan ya yi
maka laifi sau bakwai a rana daya sa'annan ya juyo
wurinka sau bakwai ya ce, 'Na tuba,' ya wajabta ka
yafe masa!" 5 Sai Manzannin suka ce wa Ubangiji,
'Ka kara mana bangaskiya.' 6 Ubangiji kuwa ya ce,
"In kuna da bangaskiya kamar kwayar mastad, za ku
ce wa wannan durumin, 'Ka tuge, ka kuma dasu a
cikin teku,' zai yi biyayya da ku. 7 Amma wanene a
cikinku, idan yana da bawa mai yin masa noma ko
kiwon tumaki, da zarar ya dawo daga jeji, zai ce masa,
'Maza zo ka zauna ka ci abinci'? 8 Ba zai ce masa,
'Ka shirya mani wani abu domin in ci ka kuma yi
damara, ka yi mini hidima har in gama ci da sha.
Bayan haka sai ka ci ka sha'? 9 Ba zai yi wa bawan
nan godiya ba domin ya yi biyayya da abubuwan da
aka umarce shi ya yi, ko zai yi haka? 10 Haka kuma,
idan kuka bi duk abin da aka umarce ku, sai ku ce,
'Mu bayi ne marasa amfani. Mun dai yi abin da yake
wajibi ne kurum.'" 11 Wata rana yana tafiya zuwa
Urushalima, sai ya bi iyakar kasar Samariya da Galili.
12 Yayin da yana shiga wani kauye kenan, sai wadansu
kutare maza guda goma suka tarye shi suna tsaye
daga nesa da shi 13 sai suka daga murya suka ce,
"Yesu, Ubangiji, ka yi mana jinkai." 14 Da ya gan su,
ya ce masu, "Ku je ku nuna kanku a wurin firistoci."
Ya zama sa'adda suke tafiya, sai suka tsarkaka. 15
Daya daga cikinsu da ya ga an warkar da shi, ya koma,
yana ta daukaka Allah da murya mai karfi. 16 Ya fadi a
gaban Yesu, yana masa godiya. Shi kuwa Basamariye
ne. 17 Yesu ya amsa ya ce, "Ba goma ne aka tsarkake
ba? Ina sauran taran? 18 Babu wani da ya dawo ya
girmama Allah sai wannan bakon kadai?" 19 Sai ya ce
masa, "Tashi, kayi tafiyarka. Bangaskiyarka ta warkar
da kai." 20 Da Farisawa suka tambaye shi lokacin da
mulkin Allah zai bayyana, Yesu ya amsa masu ya ce,
"Mulkin Allah ba lura ake yi da shi ba. 21 Ba kuwa
za a ce, 'Gashi nan!' Ko kuwa, 'Ga shi can ba!' domin
mulkin Allah yana tsaknaninku." 22 Yesu ya ce wa
almajiran, "Kwanaki na zuwa da za ku yi begen ganin
rana daya cikin ranakun Dan Mutum, amma ba zaku

gani ba. 23 Za su ce maku, 'Duba can! 'Duba nan!'
Amma kada ku je kuna dubawa, ko kuwa ku bi su. 24
Kamar yadda walkiya take haskakawa daga wannan
bangaren sararin sama zuwa wancan bangaren, haka
ma dan mutum zai zama a ranar bayyanuwarsa. 25
Amma lalle sai ya sha wahaloli dabam dabam tukuna,
mutanen zamanin nan kuma su ki shi. 26 Kamar yadda
ya faru a zamanin Nuhu, haka kuma zai faru a lokacin
bayyanar Dan Mutum. 27 Ana ci, ana sha, ana aure,
ana aurarwa, har zuwa ga ranar da Nuhu ya shiga
jirgi - ruwan tufana kuma ya zo, ya hallaka su duka.
28 Haka ma aka yi a zamanin Lutu, ana ci, ana sha, ana
saye, ana sayarwa, ana shuke-shuke da gine-gine. 29
Amma a ranar da Lutu, ya fita daga Saduma, aka zubo
wuta da kibiritu daga sama, aka hallaka su duka. 30
Haka kuma zai zama a ranar bayyanuwar Dan Mutum.
31 A ranar nan fa, wanda yake kan soro kada ya sauka
domin daukan kayansa daga cikin gida. Haka kuma
wanda yake gona kada ya dawo. 32 Ku tuna fa da
matar Lutu. 33 Duk mai son ransa, zai rasa shi, amma
duk wanda ya rasa ransa, zai same shi. 34 Ina gaya
maku, a wannan dare za a sami mutum biyu a gado
daya. Za a dauka daya, a kuma bar dayan. 35 Za a sami
mata biyu suna nika tare. Za a dauka daya a bar daya."
36 ["Za a ga mutum biyu a gona. Za a dauki daya a bar
daya."] 37 Sai suka tambaye shi, "Ina, Ubangiji?" Sai
ya ce masu, "Duk in da gangar jiki yake, a nan ungulai
sukan taru."

**18** Ya kuma ba su wani misali cewa ya kamata
kullum su yi addu'a kada kuma su karaya, 2
yace, "A wani gari an yi wani alkali mara tsoron
Allah, kuma baya ganin darajan mutane. 3 Akwai
wata mace gwauruwa a wannan garin, wadda ta rika
zuwa wurinsa, tana ce masa, 'Ka taimake ni yanda
zan sami adalci a kan abokin gaba na.' 4 An dade
bai so ya taimaka mata, amma daga baya sai ya ce a
ransa, 'ko da yake ba na tsoron Allah, ba na kuma
darajanta mutane, 5 duk da haka saboda gwauruwar
nan ta dame ni, zan taimake ta domin ta sami adalci,
yadda ba za ta gajiyar da ni da zuwanta wurina
ba.'" 6 Sai Ubangiji ya ce, "Ku ji fa abin da alkalin
nan marar gaskiya ya fada. 7 A yanzu Allah ba zai
biya wa zababbunsa da suke yi masa kuka dare da
rana hakkinsu ba? Zai yi jinkiri a wajen taimakonsu
ne? 8 Ina gaya maku, zai biya masu hakkin su da
wuri. Amma sa'adda Dan Mutum ya zo, zai tarar da
bangaskiya a duniya?" 9 Ya sake ba da misalin nan
ga wadansu masu amincewa da kansu, wai su masu
adalci ne, har suna raina sauran mutane, 10 "Wadansu
mutane biyu suka shiga haikali domin yin addu'a -
daya Bafarise, dayan kuma mai karbar haraji ne. 11
Sai Bafarisen ya mike, ya yi addu'a a kan wadannan
abubuwa game da kansa, 'Allah, na gode maka, da
cewa ni ba kamar sauran mutane dake mazambata ba,
ko marasa adalci, ko mazinata, ko kamar wannan mai
karbar harajin. 12 Duk mako ina azumi sau biyu. Nakan
bayar da zakkar dukan abin da na samu.' 13 Amma
mai karbar harajin kuwa yana tsaye daga can nesa, bai
yarda ya daga kai sama ba, sai dai yana bugun kirjin
sa, yana cewa, 'Allah, ka yi mini jinkai, ni mai zunubi.'
14 Ina gaya maku, wannan mutum ya koma gidansa
baratacce, ba kamar dayan ba, domin dukan wanda
ya daukaka kansa, za a kaskantar da shi, amma duk
wanda kaskantar da kansa kuwa daukaka shi za a yi."
15 Sai mutanen suka kawo masa jariransu, domin ya
taba su, da almajiransa suka ga haka, sai suka kwabe
su. 16 Amma Yesu ya kira su wurinsa, ya ce, "Ku bar
yara kanana su zo wurina, kada ku hana su. Ai mulkin
Allah na irin su ne. 17 Gaskiya ina gaya maku, duk
wanda bai karbi mulkin Allah kamar karamin yaro ba,
lallai ba zai shige shi ba." 18 Wani shugaban jama'a ya
tambaye shi ya ce "Malam managarci, me zan yi in
gaji rai Madawwami?" (aiōnios g166) 19 Yesu ya ce masa,
"Don me ka kira ni managarci? Babu wani managarci
sai Allah kadai. 20 Ka dai san dokokin - kada ka yi zina,
kada ka yi kisankai, kada ka yi sata, kada ka yi shaidar
karya, ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka." 21
Sai shugaban ya ce, "Dukan wadannan abubuwa na
kiyaye su tun a kuruciya ta." 22 Da Yesu ya ji haka, ya
ce masa, "Abu daya ne kadai ya rage maka. Dole ne ka
sayar da dukan mallakarka, ka rarraba wa gajiyayyu,
za ka kuma sami wadata a sama - sa'annan ka zo
ka biyoni." 23 Amma da mai arzikin ya ji wadannan
abubuwa, sai yayi bakin ciki kwarai, don shi mai arziki
ne sosai. 24 Yesu kuwa, da ya ga ransa ya baci, sai ya
ce, "Yana da wuya masu dukiya su shiga mulkin Allah!
25 Zai zama da sauki rakumi ya shiga kafar allura,
da mai arziki ya shiga mulkin Allah." 26 Wadanda
suka ji wannan magana suka ce, "Idan hakane wa zai
sami ceto kenan?" 27 Yesu ya amsa, "Abin da ya fi
karfin mutum, mai yiwuwa ne a gun Allah." 28 Sai
Bitrus ya ce, "To, ga shi mun bar mallakarmu, mun bi
ka." 29 Yesu ya ce masu, "Hakika, ina gaya maku, ba
wanda zai bar gida, ko matarsa, ko 'yan'uwansa, ko

iyayensa, ko kuma 'ya'yansa, saboda mulkin Allah, 30
sa'annan ya kasa samun ninkin ba ninkin a duniyan
nan, da rai na har abada a duniya mai zuwa." (aiōn g165,
aiōnios g166) 31 Bayan da ya tara su goma sha biyun nan,
ya ce masu, "Ga shi, muna tafiya zuwa Urushalima,
duk abubuwan da aka rubuta game da Dan Mutum ta
hannun annabawa zasu tabbata. 32 Gama za a bashe
shi ga al'ummai, a yi masa ba'a, a wulakanta shi, a
kuma tofa masa miyau. 33 Za su yi masa bulala, su
kashe shi, a rana ta uku kuma zai tashi." 34 Amma ba
su fahimci ko daya daga cikin wadannan abubuwa ba,
domin zancen nan a boye yake daga garesu, ba su ma
gane abin da aka fada ba. 35 Da ya kusato Yariko, ga
wani makaho zaune a gefen hanya, yana bara, 36 da
ya ji taro na wucewa, sai ya tambaya ko menene. 37
Suka ce masa Yesu Banazarat ne yake wucewa. 38 Sai
makahon ya ta da murya mai karfi, ya ce, "Yesu, Dan
Dauda, ka yi mani jinkai." 39 Sai wadanda suke gaba
suka kwabe shi, suna gaya masa ya yi shiru. Amma ya
kara daga murya kwarai da gaske, yana cewa, "Dan
Dauda, ka yi mani jinkai." 40 Sai Yesu ya tsaya, ya
umarta a kawo shi wurinsa. Da makahon ya zo kusa,
sai Yesu ya tambaye shi, 41 "Me kake so in yi maka?"
Ya ce, "Ubangiji, ina so in samu gani." 42 Yesu ya
ce masa, "Karbi ganin gari, bangaskiyarka ta warkar
da kai." 43 Nan take ya samu gani, ya bi Yesu, yana
daukaka Allah. Ganin haka, sai duk jama'a suka yabi
Allah.

19 Yesu ya shiga Yariko ya na wucewa cikinta. 2
Sai ga wani mutum a wurin mai suna Zakka.
Shugaba ne na masu karban haraji, kuma mai arziki
ne. 3 Yana kokarin ya ga ko wanene Yesu, amma bai
iya gani ba sabo da yawan jama'a, domin shi gajere
ne. 4 Sai ya ruga gaba ya hau itacen baure domin ya
gan shi, saboda Yesu zai wuce ta wannan hanya. 5
Sa'adda Yesu ya zo wurin, ya kalli sama sai ya ce masa,
"Zakka, ka sauko da sauri, domin yau dole in sauka a
gidanka." 6 Sai ya sauko da sauri, ya karbe shi da farin
ciki. 7 Sa'adda dukansu suka ga wannan, sai suka yi
gunaguni, cewa, "Ya ziyarci mutum mai zunubi." 8
Zakka ya tsaya ya ce wa Ubangiji, "Duba, Ubangiji,
zan ba matalauta rabin arzikina, idan kuma na cuci
wani a kome, zan mai da adadinsa sau hudu." 9 Yesu
ya ce masa, "Yau ceto ya shigo wannan gida, domin
shi ma dan Ibrahim ne. 10 Gama Dan Mutum ya zo ne
domin ya nemi, ya kuma ceci batattun mutane." 11 Da
suka ji wadannan abubuwan, ya cigaba da magana,
sannan ya fada masu wani misali, domin yana kusa da
Urushalima, sai suka yi tsamani mulkin Allah za ya
bayyana nan da nan. 12 Sai ya ce, "Akwai wani mutum
mai sarauta wanda ya tafi wata kasa mai nisa domin
ya karba wa kansa mulki sa'annan ya dawo. 13 Sai ya
kira bayinsa guda goma, ya ba su fam goma, sai ya ce
masu, 'Ku yi kasuwanci da wannan har sai na dawo.'
14 Amma mutanensa suka ki shi sai suka aiki jakadu
bayansa, cewa, 'Ba za mu yarda wannan mutum ya
yi mulki a kanmu ba.' 15 Anan nan sa'adda ya koma
kuma, bayan da ya sami mulkin, sai ya ba da umarni a
kira masa bayin da ya basu kudi, domin ya san ribar
da suka samu wajen kasuwancin da suka yi. 16 Na
farkon ya zo wurinsa, cewa, 'Ubangiji, fam nan na
ka ya yi riban fam goma.' 17 Masaraucin ya ce masa,
'Madalla, bawan kirki. Domin ka yi aminci a karamin
abu, za a baka iko kan birane goma.' 18 Na biyun
ya zo, yana cewa, 'Fam na ka, Ubangiji, ya yi ribar
fam biyar.' 19 Sai masarauncin yace masa, 'Ka dauki
mulkin birane biyar.' 20 Wani kuma ya zo, yana cewa,
'Ubangiji, ga fam naka da na ajjiye shi da kyau cikin
kaya, 21 gama na ji tsoronka, domin kai mutum mai
tsanani ne. Kana daukar abu da baka ajiye ba, kana
kuma girbin abin da ba ka shuka ba.' 22 Masarauncin
ya ce masa, 'Da kalmominka zan shari'antaka, kai
mugun bawa. Ka sani cewa ni mutum mai tsanani
ne, ina daukan abinda ban ajiye ba, ina kuma girbin
abinda ban shuka ba. 23 To don me ba ka kai kudi na
wurin masu banki ba, saboda bayan da na dawo zan
karbe shi da riba?' 24 Masaraucin ya ce wa wadanda
suke a tsaye a wurin, 'Ku karba fam da ke a wurinsa,
ku ba mai fam goman nan.' 25 Suka ce masa, 'Ubangiji,
yana da fam goma.' 26 'Ina ce maku, duk wanda yake
da abu za a kara masa, amma wadda bai da shi, za
a karba sauran da ke wurinsa. 27 Amma wadannan
abokan gabana, wadanda ba sa so in yi mulki bisansu,
a kawo su nan a kashe su a gaba na.' 28 Da ya fadi
wadannan abubuwan, sai ya yi gaba, yana tafiya zuwa
Urushalima. 29 Ananan sa'adda ya zo kusa da Baitfaji
da Baitanya, a kan tudu da a ke kira Zaitun, sai ya
aiki almajiransa guda biyu, cewa, 30 cewa, "Ku tafi
cikin kauye da ke gabanku. Sa'adda ku ka shiga, za
ku same dan aholaki da ba a taba hawansa ba. Ku
kwance sai ku kawo mani shi. 31 Idan wani ya tambaye
ku, 'Don me ku ke kwance shi?' Ku ce, 'Ubangiji ne
ke bukatarsa." 32 Wadanda aka aike su suka je sun
sami aholakin kamar yadda Yesu ya gaya masu. 33

Sa'adda suna kwance aholakin, sai masu shi suka ce
masu, “Don me ku ke kwance aholakin?” 34 Suka ce,
“Ubangiji yana bukatar sa.” 35 Suka kawo wa Yesu,
suka shimfida tufafinsu akan aholakin sai suka dora
Yesu akansa. 36 Da yana cikin tafiya, suka shimfida
tufafinsu akan hanya. 37 Da ya yi kusa da gangaren
tudun Zaitun, sai dukan taron almajiransa suka fara
yin murna suna kuma yabon Allah da murya mai karfi
domin dukan ayukan al'ajibi da suka gani, 38 cewa,
“Albarka ta tabbata ga sarki da ke zuwa cikin sunan
Uba! Salama a sama da daraja mafi daukaka kuma!”
39 Wadansu Farisawa daga cikin taron jama'a suka ce
masa, “Malam, ka tsauta wa almajiranka.” 40 Yesu ya
amsa ya ce, “Ina gaya maku gaskiya, in wadannan
sun yi shiru, duwatsu za su yi shewa.” 41 Sa'adda
Yesu yana kusatowa, sai ya yi kuka akan birnin, 42
cewa, “Da kun san wannan rana, ko ku ma, abubuwan
da ke kawo maku salama! Amma yanzu an boye su
daga idanunku. 43 Gama rana zata ta zo a gareki,
da makiyan ki zasu gina ganuwa a kewaye da ke, su
kuma fada maki daga kowace gefe. 44 Za su sare ki
kasa tare da 'ya'yanki. Ba za su bar wani dutse akan
dan'uwansa ba, domin ba ki lura da lokacin da Allah
ya na kokarin ceton ki ba.” 45 Yesu ya shiga Haikalin
sai ya fara korar masu sayarwa, 46 ya na ce masu, “A
rubuce yake, 'Gida na zai zama wurin addu'a,' amma
kun mayar da shi kogon mafasa.” 47 Yesu yana nan
yana koyarwa kowace rana a cikin haikali. Amma
manyan firistoci da marubuta da shugabanin jama'a
suna so su kashe shi, 48 amma ba su sami hanyar yin
wannan ba, domin mutane suna sauraron sa sosai.

20 Ana nan wata rana, Yesu yana kan koyarwa a
haikali da wa'azin bishara, sai shugaban firistoci
da marubuta suka zo wurinsa da dattawa. 2 Suka yi
magana, su na ce masa, “Gaya mana da wanne iko ne
ka ke yin wadannan abubuwan? Ko wanene ya baka
wannan ikon?” 3 Ya amsa sai ya ce masu, “Ni ma zan
yi maku tambaya. Gaya mani game 4 da baptisman
Yahaya. Daga sama take ko kuwa daga mutane ne?” 5
Sai suka yi mahawara da junansu, suna cewa, “In mun
ce, 'Daga sama,' zai ce, 'To don me ba ku ba da gaskiya
gareshi ba?' 6 Amma in mun ce, 'Daga mutane ne,'
dukan mutane za su jejjefe mu da duwatsu, domin sun
tabbata a ransu Yahaya annabi ne.” 7 Sai suka amsa
cewa ba su san ko daga ina ne take ba. 8 Yesu yace
masu, “To haka ni ma ba zan gaya maku ko da wanne
iko nake yin wadannan abubuwan ba.” 9 Ya gaya wa
mutane wannan misali, “Wani mutum ya dasa gonar
inabi, ya ba wadansu manoma jinginarta, sai ya tafi
wata kasa har ya dade. 10 Da lokacin girbi ya yi sai
ya aiki wani bawansa zuwa wurin manoman, saboda
su bashi daga cikin anfanin gonar. Amma manoman
suka doke shi, sai suka kore shi hannu wofi. 11 Ya aike
wani bawa kuma sai suka daddoke shi, suka kunyatar
da shi, suka kore shi hannu wofi. 12 Ya kuma sake
aike na uku suka yi masa rauni, suka jefar da shi a
waje. 13 Sai mai gonar inabin ya ce, 'Me zan yi? Zan
aiki kaunattacen dana. Watakila zasu ba shi daraja.'
14 Amma sa'adda manoman suka gan shi, suka yi
shawara a tsakaninsu, cewa, 'Wannan ne magajin.
Bari mu kashe shi, saboda gadon ya zama namu.' 15
Suka jefar da shi waje daga gonar, suka kashe shi.
Menene ubangijin gonar inabin zai yi da su? 16 Zai zo
ya halakar da wadannan manoma, sai ya ba wadansu
gonar.” Da suka ji wannan, suka ce, “Allah ya sawake!”
17 Amma Yesu ya kalle su, sai yace, “Menene ma'anar
wannan nassi? 'Dutsen da magina suka ki, an mayar
da shi kan kusurwa'? 18 Duk wanda ya fadi kan dutsen
zai farfashe. Amma duk wanda dutsen ya fadi a kansa,
zai rugurguza shi.” 19 Sai marubutan da manyan
firistocin suka so su kama shi a wannan sa'a, domin
sun sani ya yi wannan misali a kansu ne. Amma sun ji
tsoron mutane. 20 Suna fakonsa, suka aiki magewaya,
wadanda suke kamar masu adalci, saboda su sami
kuskure cikin maganarsa, don su mika shi ga hukumci
da kuma ikon gwamna. 21 Suka tambaye shi, cewa,
“Malam, mun sani da cewa kana fada da koyar da
abin ke daidai, kuma ba wanda yake cusa maka ra'ayi,
amma kana koyar da gaskiya game da hanyar Allah. 22
Wai shin doka ne mu biya haraji ga Kaisar, ko babu?”
23 Amma Yesu ya gane makircinsu, sai ya ce masu, 24
“Nuna mani dinari. Sifar wanene da kuma rubutun
wanene akan sa?” Suka ce, “Na Kaisar ne.” 25 Sai ya
ce masu, “To sai ku ba Kaisar abin da ke na Kaisar, ku
kuma ba Allah, abin da ke na Allah.” 26 Marubutan
da manyan firistocin ba su sami abin zargi cikin
maganarsa, a gaban mutane ba. Suka yi mamakin
amsar sa, ba su kuma ce komai ba. 27 Sa'adda wadansu
Sadukiyawa suka zo wurinsa, wadan da suka ce babu
tashin mattatu, 28 suka tambaye shi, cewa, “Malam,
Musa ya rubuta mana cewa idan dan'uwan mutum ya
mutu, mai mace kuma ba shi da yaro, sai dan'uwansa
ya auri matar, ya samar wa dan'uwansa yaro. 29 Akwai

'yan'uwa guda bakwai kuma na farin ya yi aure, sai ya
mutu babu da, 30 haka ma na biyun. 31 Na ukun ya
aure ta, haka nan na bakwai ma bai bar yaya ba, har
suka mutu. 32 Daga baya sai matar ma ta mutu. 33 To
a ranar tashin mattatu, matar wa za ta zama? Domin
duka bakwai din sun aure ta." 34 Yesu ya ce masu,
"'Ya'yan duniyan nan suna aure, ana kuma ba da su ga
aure. (aiōn g165) 35 Amma wadanda aka ga cancantarsu
a waccan tsara, sun isa su sami tashin mattatu, ba za
suyi aure ko a aurar da su ba. (aiōn g165) 36 Gama ba
za su mutu kuma ba, domin suna daidai da mala'iku
kuma su 'ya'yan Allah ne, da shike su 'ya'yan tashin
matattu ne. 37 Amma batun tashi matattu, ko Musa
ma ya nuna wannan, a cikin jeji, inda ya kira Ubangiji,
Allah na Ibrahim da kuma Allah na Ishaku da Allah na
Yakubu. 38 Yanzu shi ba Allahn matattu ba ne, amma
na masu rai, saboda duka suna raye a wurinsa." 39
Wadansu marubuta suka amsa, "Malam, ka amsa da
kyau." 40 Gama ba su sake yi masa wadansu tambayoyi
ba. 41 Yesu ya ce masu, "Yaya suke cewa Almasihu
dan Dauda ne? 42 Gama Dauda da kansa ya ce a cikin
littafin Zabura, Ubangiji ya ce wa Ubangiji na, 'Zauna
a hannun dama na, 43 sai na maida makiyanka a
karkashin tafin sawunka.' 44 Dauda ya kira Kristi
'Ubangiji', to ta yaya ya zama dan Dauda?" 45 Dukan
mutane suna ji ya ce wa almajiransa, 46 "Ku yi hankali
da marubuta, wadanda suna son tafiya da manyan
riguna, suna kuma son a gaishe su a cikin kasuwanni,
da mayan wuraren zama a cikin majami'u, da kuma
manyan wurare a wurin bukukkuwa. 47 Suna kuma
kwace wa gwamraye gidaje, suna kuma badda kama
ta wurin yin doguwar addu'a. Wadannan za su sha
hukumci mai girma."

21 Yesu ya tada ido sai ya ga mutane masu arziki
wadanda suke saka baikonsu a cikin ma'aji. 2 Ya
ga wata gwauruwa matalauciya tana saka anini biyu
a ciki. 3 Sai ya ce, "Gaskiya ina gaya maku, wannan
matalauciyar gwauruwa ta saka fiye da dukansu. 4
Duka wadannan sun bayar da baikonsu daga cikin
yalwarsu. Amma wannan gwauruwan, daga cikin
talaucin ta, ta saka dukan iyakar kudinta na zaman
gari da take da shi." 5 Kamar yadda wadansu suke
maganan haikali, yadda aka yi masa ado da duwatsu
masu daraja da bayebaye, ya ce, 6 "Game da wadannan
abubuwa da ku ke gani, rana tana zuwa da ba dutse
ko daya da zai zauna kan dan'uwansa da ba za a rushe
kasa ba." 7 Sai suka yi masa tambaya, cewa, "Malam,
yaushe ne wadannan abubuwan zasu faru? Menene
kuma zai zama alama sa'adda wadannan abubuwa
suna shirin faruwa?" 8 Yesu ya amsa, "Ku yi hankali
kada a rude ku. Gama dayawa zasu zo a cikin sunana,
suna cewa, 'Ni ne shi,' kuma, 'Lokaci ya yi kusa.' Kada
ku bi su. 9 Sa'adda ku ka ji game da yakoki da hargitsi,
kada ku firgita, dole ne wadannan abubuwa su faru
tukuna, amma karshe ba zai faru nan da nan ba."
10 Sa'annan ya ce masu, "Al'umma za ta tasar ma
al'umma, mulki kuma za ya tasar wa mulki. 11 Za a yi
babbar girgizan kasa, a wurare dabam dabam kuma
za a yi yunwa da annoba. Za a yi al'amura masu ban
tsoro da manyan alamu daga sama. 12 Amma kafin
abubuwan nan duka, za su kama ku, su kuma tsananta
maku, suna mika ku ga majami'u da kuma gidajen
kurkuku, za su kawo ku gaban sarakuna da gwamnoni
saboda sunana. 13 Zai zamar maku zarafin shaida. 14
Saboda haka ku kudurta a ranku kada ku shirya yadda
za ku amsa, 15 gama ni zan ba ku kalmomi da hikima,
wadda dukan makiyanku ba za su yi tsayayya ko su
karyata ku ba. 16 Amma har da mahaifa da 'yan'uwa
da dangi da abokai za su bashe ku, su kuma kashe
wadansun ku. 17 Kowa zai ki ku saboda sunana. 18
Amma ba ko gashin kanku da zai hallaka. 19 A cikin
hankurin ku za ku ribato rayukanku. 20 Sa'adda ku
ka ga Urushalima tana kewaye da sojoji, sai ku sani
da cewa faduwarta ta yi kusa. 21 Sai wadanda su ke
Yahudiya su gudu zuwa kan tuddai, wadanda suke
tsakiyar gari kuma su tafi, kada su bar wadanda suke
kauyuka su shigo ciki. 22 Gama wadannan ranakun
ramako ne, saboda duka abubuwan da aka rubuta su
cika. 23 Kaiton wadanda suke da juna biyu da masu ba
da mama a wannan kwanakin! Gama za a sha kunci
mai girma a kasan, da fushi kuma zuwa ga mutanen
nan. 24 Za su fadi ta kaifin takobi kuma za a kai su
cikin bauta ga dukan kasashe, al'ummai za su tattake
Urushalima, har ya zuwa lokacin al'ummai ya cika. 25
Za a ga alamomi cikin rana da wata da kuma taurari.
A duniya kuma, al'ummai za su sha kunci, za su rude
saboda rurin teku da rakuman ruwa. 26 Mutane za su
suma da tsoro da kuma da tunanin abubuwa da za su
abko wa duniya. Gama za a girgiza ikokin sammai.
27 Sa'annan za su ga Dan Mutum yana zuwa a cikin
gajimarai da iko da daukaka mai girma. 28 Amma
sa'adda wadannan abubuwa suka fara faruwa, tashi
saye, sai ku daga kanku sama, saboda ceton ku ya

kusato.” 29 Yesu ya bada misali, “Duba itacen baure,
da duka itatuwa. 30 Sa'adda su ke fitar da ganye, za
ku gani da kanku cewa bazara ta yi kusa kuma. 31
Haka kuma, sa'adda ku ka ga wadannan abubuwa
suna faruwa, ku sani cewa mulkin Allah ya yi kusa. 32
Gaskiya, na ke gaya maku, wannan zamani ba za ya
shude ba, sai duka abubuwan nan sun faru. 33 Sama
da kasa za su shude, amma maganata ba za ta shude
ba. 34 Amma ku lura da kanku, domin kada ku nawaita
zuciyarku da tararradin duniya da shayeshaye da
damuwa ta rayuwa. Gama ranar za ta zo babu shiri 35
kamar tarko. Gama zai zo akan kowa da ke rayuwa
a fuskar dukan duniya. 36 Amma ku zama a fadake
kowanne lokaci, kuna addu'a domin ku iya samun
karfin tserewa dukan wadannan abubuwa da za su
faru, da kuma yadda za ku tsaya a gaban Dan Mutum.”
37 Da rana yana koyarwa a cikin haikali, dukan dare
kuma yakan tafi dutsen da a ke kira zaitun. 38 Dukan
mutane suka rika zuwa wurinsa da sassafe domin su ji
shi a haikali.

# 22

Anan nan idin gurasa mara yisti ya yi kusa,
wanda a ke kira Idin ketarewa. 2 Manyan firistoci
da marubuta suka yi shawara yadda za su kashe Yesu,
gama suna jin tsoron mutane. 3 Shaidan ya shiga
Yahuza Iskariyoti, daya daga cikin goma sha biyun. 4
Yahuza ya je ya yi shawara da manyan firistoci da
Jarumawa yadda zai ba da Yesu a garesu. 5 Suka yi
farin ciki, suka yarda su ba shi kudi. 6 Sai ya yarda, sai
ya nimi dama yadda zai ba da shi garesu a lokacin
da babu taro. 7 Ranar idin gurasa mara yisti ya yi,
da dole za a yi hadayan rago na Idin ketarewa. 8
Yesu ya aiki Bitrus da Yahaya, ya ce masu, “Ku je ku
shirya mana abincin Idin ketarewa, domin mu ci.” 9
Suka tambaye shi, “A ina ka ke so mu shirya?” 10 Ya
amsa masu, “Ku ji, sa'adda ku ka shiga birnin, wani
mutum mai dauke da tulun ruwa zai same ku. Ku
bishi zuwa cikin gidan da za ya shiga. 11 Sai ku gaya
wa mai gidan, 'Malam ya ce, “Ina dakin baki, inda
zan ci abincin Idin ketarewa da almajirai na?'” 12
Zai nuna maku babban bene wanda yake a shirye.
Ku shirya a can.” 13 Sai suka tafi, suka sami komai
kamar yadda ya gaya masu. Sai suka shirya abincin
Idin ketarewan. 14 Sa'adda lokacin ya yi, ya zauna
da almajiran. 15 Sai ya ce masu, “Ina da marmari
matuka in ci wannan abincin Idin ketarewa da ku
kamin in sha wahala. 16 Gama na ce maku, ba zan ci
shi kuma ba, sai dai an cika shi a mulkin Allah.” 17 Sai
Yesu ya dauki koko, sa'adda ya yi godiya, sai yace,
“Karba wannan, ku rarraba a tsakaninku. 18 Gama ina
ce maku, ba zan sha wannan ruwan inabi kuma ba,
sai dai mulkin Allah ya zo.” 19 Sai ya dauki gurasa,
sa'adda ya yi godiya, ya kakkarya shi, sai ya ba su,
cewa, “Wannan jikina ne wanda aka bayar dominku.
Ku yi wannan domin tunawa da ni.” 20 Sai ya dauki
kokon kuma bayan jibi, cewa, “Wannan koko sabon
alkawari ne cikin jinina, wanda aka zubar dominku.
21 Amma ku yi lura. Wanda zai bashe ni yana tare da
ni a teburi. 22 Gama Dan Mutum zai tafi lallai kamar
yadda aka kaddara. Amma kaiton wannan mutum da
shine za ya bashe shi!” 23 Sai suka fara tambaya a
tsakaninsu, wanene a cikinmu da zai yi wannan abu.
24 Sai gardama ta tashi a tsakaninsu game da wanene
mafi girma. 25 Ya ce masu, “Sarakunan al'ummai suna
nuna iko akansu, kuma wadanda suke da iko a kansu
ana ce da su masu mulki da daraja. 26 Amma kada ya
zama haka da ku. A maimakon haka, bari wanda ya ke
mafi girma a cikinku ya zama mafi kankanta. Bari
wanda yafi muhimmanci kuma ya zama kamar mai
hidima. 27 Gama wanene yafi girma, wanda ya zauna
a teburi, ko kuwa wanda yake yin hidima? Ba wanda
ya zauna a teburi ba? Duk da haka ina kamar mai
hidima a tsakaninku. 28 Amma ku ne wadanda ku ke
tare da ni a cikin jarabobina. 29 Na baku mulki, kamar
yadda Ubana ya ba ni mulki, 30 domin ku ci ku kuma
sha a teburi na mulkina. Za ku zauna a kan kursiyai
kuna shari'anta kabilun nan goma sha biyu na Israila.
31 Siman, Siman, ka yi hankali, shaidan ya nemi izini a
bada kai domin ya tankade ka kamar alkama. 32 Amma
na yi maka addu'a, saboda kada bangaskiyarka ta fadi.
Bayan da ka juyo kuma, ka karfafa 'yan'uwanka.” 33
Bitrus ya ce masa, “Ubangiji, ina shirye in tafi tare da
kai zuwa cikin kurkuku da zuwa mutuwa.” 34 Yesu
ya amsa masa, “Ina gaya maka, Bitrus, kamin caran
zakara a yau, za ka yi musu na sau uku cewa ba ka
sanni ba.” 35 Sa'annan Yesu ya ce masu, “Lokacin da
na aike ku babu jaka, ko burgami ko takalma, ko kun
rasa wani abu? Sai suka amsa, “Babu.” 36 Ya kuma
ce masu, “Amma yanzu, wanda ya ke da jaka, bari
ya dauka, da kuma burgami. Wanda ba shi da takobi
sai ya sayar da taguwarsa ya sayi guda. 37 Gama ina
ce maku, abin da aka rubuta game da ni dole sai ya
cika, 'An lisafta shi kamar daya daga cikin masu karya
doka.' Gama abinda aka fada akaina ya cika.” 38 Sai

suka ce, "Ubangiji, duba! Ga takuba biyu." Sai ya ce
masu, "Ya isa." 39 Bayan cin abincin yamma, Yesu ya
tafi, kamar yadda ya saba yi, zuwa dutsen Zaitun, sai
almajiran suka bi shi. 40 Sa'adda suka iso, ya ce masu,
"Ku yi addu'a domin kada ku shiga cikin jaraba." 41
Ya rabu da su misalin nisan jifa, sai ya durkusa kasa
ya yi addu'a, 42 yana cewa "Uba, in ka yarda, ka dauke
wannan kokon daga gareni. Ko da yake ba nufina ba,
amma bari naka nufin ya kasance." 43 Sai mala'ika
daga sama ya bayyana a wurinsa, yana karfafa shi. 44
Yana cikin wahala sosai, sai ya dukufa cikin addu'a,
har zufarsa kuma tana diga a kasa kamar gudajen jini.
45 Sa'adda ya tashi daga addu'arsa, sai ya zo wurin
almajiran, ya same su suna barci domin bakin cikinsu,
46 sai ya tambaye su, "Don me kuke barci? Tashi ku yi
addu'a, saboda kada ku shiga cikin jaraba." 47 Sa'adda
yana cikin magana, sai, ga taron jama'a suka bayana,
tare da Yahuza, daya daga cikin sha biyun, ya na
jagabansu. Sai ya zo kusa da Yesu domin ya yi masa
sumba, 48 amma Yesu ya ce masa, "Yahuza, za ka
ba da Dan Mutum da sumba?" 49 Sa'adda wadanda
suke kewaye da Yesu suka ga abin da yake faruwa, sai
suka ce, "Ubangiji, mu yi sara da takobi ne?" 50 Sai
daya daga cikinsu ya kai wa bawan babban firist sara
a kunne, sai ya yanke masa kunnensa na dama. 51
Yesu ya ce, "Ya isa haka." Sai ya taba kunnensa, sai
ya warkar da shi. 52 Yesu yace wa manyan firistoci,
da masu tsaron haikali, da dattawa wadanda suke
gaba da shi, "Kun fito kamar za ku kama dan fashi, da
takuba da sanduna? 53 Sa'adda nake tare da ku kowace
rana a haikali, ba ku kama ni ba. Amma wannan shine
lokacinku, da kuma ikon duhu." 54 Suka kama shi, sai
suka tafi da shi, suka kawo shi cikin gidan babban
firist. Amma Bitrus yana binsa daga nesa. 55 Bayan da
suka hura wuta a tsakiyar gidan da suka zazzauna
tare, Bitrus ya zaune a tsakaninsu. 56 Sai wata baranya
ta ganshi ya zauna a hasken wuta, sai ta zura masa
ido ta ce, "Wannan mutum ma yana tare da shi."
57 Amma Bitrus ya yi musu, yana cewa, "Mace, ban
san shi ba." 58 Bayan dan karamin lokaci sai wani
mutum ya gan shi, sai ya ce, "Kaima kana daya daga
cikinsu." Amma Bitrus ya ce, "Mutumin, ba ni ba ne."
59 Bayan sa'a daya sai wani mutum ya nace da cewa,
"Gaskiya wannan mutum yana tare da shi, gama shi
dan Galili ne." 60 Amma Bitrus ya ce, "Mutumin, ban
san abin da kake fada ba." Sai nan da nan, da yana
cikin magana, sai zakara ta yi cara. 61 Yana juyawa,
sai Ubangiji ya dubi Bitrus. Sai Bitrus ya tuna kalmar
Ubangiji, sa'adda ya ce masa, "Kafin zakara ya yi cara
yau za ka musunce ni sau uku." 62 Da fitowarsa waje,
Bitrus ya yi kuka mai zafi. 63 Sai mutanen da ke tsare
da Yesu suka yi masa ba'a da bulala kuma. 64 Bayan
da suka rufe masa idanu, suka tambaye shi, cewa,
"Ka yi annabci! Wa ya buge ka?" 65 Suka yi wadansu
miyagun maganganu na sabo game da Yesu. 66 Da
gari ya waye, sai dattawa suka hadu tare, da manyan
firistoci da marubuta. Sai suka kai shi cikin majalisa
67 suka ce, "Gaya mana, in kai ne Almasihu." Amma
yace masu, "Idan na gaya maku, ba za ku gaskanta
ba, 68 idan na yi maku tambaya, ba za ku amsa ba.
69 Amma nan gaba, Dan Mutum zai zauna a hannun
dama na ikon Allah." 70 Suka ce masa, "Ashe kai Dan
Allah ne?" Sai Yesu ya ce masu, "Haka kuka ce, nine."
71 Suka ce, "Don me muke neman shaida? Gama mu
da kanmu munji daga bakinsa."

23 Sai duk taron suka tashi, suka kawo Yesu gaban
Bilatus. 2 Suka fara saransa, cewa "Mun same
wannan mutum yana ruda kasarmu, ya haramta a
ba Kaisar haraji, yana kuma cewa shi da kansa ne
Almasihu, sarki." 3 Bilatus ya tambaye shi, cewa "Shin
kaine Sarkin Yahudawa?" Sai Yesu ya amsa masa
ya ce, "Haka ka ce." 4 Sai Bilatus ya ce wa manyan
firistocin da taro mai yawa, "Ban samu ko laifi daya
game da wannan mutumin ba." 5 Amma suka yi
ta cewa, "Yana ta da hankalin mutane da koyarwa
a dukan Yahudiya, ya fara daga Galili har zuwa ga
wannan wuri." 6 Sa'adda Bilatus ya ji wannan, sai ya
tambaya ko mutumin daga Galiline. 7 Sa'adda ya gane
cewa yana karkashin mulkin Hirudus, sai ya tura Yesu
wurin Hirudus, wanda shi da kansa yana Urushalima
a wadannan kwanakin. 8 Sa'adda Hirudus ya ga Yesu,
sai ya cika da farin ciki sosai, saboda ya so ganinsa
tunda dadewa. Tun can ya ji game da shi sai ya yi
begen ganin wadansu al'ajibai da zai yi. 9 Hirudus ya
tambaye Yesu cikin kalmomi masu yawa, amma Yesu
bai amsa masa da komai ba. 10 Sai manyan firistoci da
marubuta suka tsaya, suna ta yi masa zargi mai zafi.
11 Hirudus da sojojinsa suka zarge shi, suka kuma yi
masa ba'a, suka sa masa tufafi masu kyau, sa'annan
ya sake aika Yesu zuwa wurin Bilatus. 12 Sai Hirudus
da Bilatus suka zama abokai a wannan rana (da ma su
abokai gaba ne). 13 Bilatus ya kira manyan firistoci
tare da masu mulki da kuma taron jama'ar, 14 sai ya

ce masu, “Kun kawo mani wannan mutum kamar
wanda yake jagorar mutane ga munanan ayyuka, ku
kuma gani, Ni, na tuhume shi a gabanku, ban sami ko
kuskure daya daga mutumin nan game da abinda ku
ke zarginsa da shi ba. 15 Babu, ko Hirudus ma, ya sake
komar mana da shi, kun gani, babu wani abu wanda
ya yi da ya cancanci mutuwa, 16 saboda haka zan yi
masa horo sa'annan in sake shi.” 17 [Ya zama dole
Bilatus ya sakar wa Yahudawa wani daurarre guda
daya lokacin idin.] 18 Amma dukansu suka yi ihu tare,
cewa, “A tafi da wannan mutumin, sai a sako mana
Barabbas!” 19 Barabbas mutum ne wanda aka sa a
cikin kurkuku saboda wani tada hankali a cikin birni
da kuma kisankai. 20 Bilatus ya sake yi masu magana,
yana so ya saki Yesu. 21 Amma suka yi ihu, cewa, “A
giciye shi, a giciye shi.” 22 Sai ya sake ce masu sau na
uku, “Don me, wace magunta wannan mutum ya yi?
Ban sami wani abu da ya isa sanadin mutuwa game
da shi ba. Saboda haka bayan na hore shi, zan sake
shi.” 23 Amma suka nace da murya mai karfi, suna
so a giciye shi, sai muryarsu ta rinjayi Bilatus. 24 Sai
Bilatus ya yarda ya yi masu bisa ga abin da suke so. 25
Ya sako masu wanda suka tambaya ya ba su wanda aka
sa a kurkuku domin tada hankali da kuma kisankai.
Amma ya ba da Yesu bisa nufinsu. 26 Da suka tafi da
shi, sai suka kama wani mai suna siman Bakurane,
yana zuwa daga karkara, sai suka daura masa giciyen
ya dauka, yana biye da Yesu. 27 Babban taron jama'a,
da na mata da suke makoki da kuka dominsa, suna
binsa. 28 Amma da ya juya wurinsu, Yesu yace, “Yan
matan Urushalima, kada ku yi kuka domina, amma ku
yi kuka domin kanku da 'ya'yanku. 29 Gama ku gani,
kwanaki suna zuwa da za su ce, 'Albarka ta tabbata ga
bakararru da wadanda basu taba haihuwa ba da kuma
wadanda ba a taba shan mamansu ba.' 30 Sa'annan za
su fara ce wa duwatsu, 'Ku fado bisanmu,' da tuddai
ma, 'Ku rufe mu.' 31 Gama idan sun yi wadannan
abubuwan lokacin da itace yana danye, me zai faru
sa'adda ya bushe?” 32 Aka kai wadansu mutum biyu
masu laifi, domin a kashe shi tare da su. 33 Sa'adda
suka zo wurin da a ke kira kwalluwa, nan suka giciye
shi da barayin, daya daga hannun damansa dayan
kuma daga hannun hagu. 34 Yesu yace, “Uba, ka yafe
masu, gama basu san abin da suke yi ba.” Sai suka
jefa kuri'a, suka rarraba tufafinsa. 35 Mutane sun
tsaya suna kallo sa'annan masu mulki suna ta yin
masa ba'a, cewa, “Ya ceci wadansu. Bari ya ceci kansa,
idan shine Almasihu na Allah, zababben nan.” 36
Sojojin ma suka yi masa dariya, suna zuwa wurinsa,
suna mika masa ruwan tsami, 37 suna cewa, “Idan
kai Sarkin Yahudawa ne, ceci kanka.” 38 Akwai wata
alama bisansa, “Wannan shine Sarkin Yahudawa.”
39 Daya daga cikin barayi wanda aka giciye, ya zage
shi, cewa, “Ba kai ne Almasihu ba? Ka ceci kanka da
mu.” 40 Amma dayan ya amsa, ya tsauta masa cewa,
“Ba ka tsoron Allah, da yake shari'arka daya ne da
nasa? 41 Mu kam an yi ma na daidai, gama mun samu
bisa ga abin da muka yi. Amma wannan mutum bai
yi wani abu mara kyau ba.” 42 Sai ya kara, “Yesu, ka
tuna da ni sa'adda ka shiga mulkinka.” 43 Yesu ya ce
masa, “Gaskiya ina ce maka, yau za ka kasance tare
da ni a firdausi.” 44 Anan nan a wajen sa'a na shida,
sai duhu ya mamaye kasar duka har zuwa sa'a na
tara 45 sa'adda rana ya fadi. Sai labulen haikalin ya
rabu a tsakiya zuwa kasa. 46 Da kuka da murya mai
karfi, Yesu yace, “Uba, na mika Ruhu na a hannunka.”
Bayan da ya fadi wannan, sai ya mutu. 47 Sa'adda
jarumin ya ga abin da ya faru, ya daukaka Allah, cewa,
“Lallai wannan mutumin mai adalci ne.” 48 Sa'adda
dukan taro mai yawa wadanda suka zo tare domin
su shaida da idanunsu suka ga abubuwan da suka
faru, suka koma suna bugan kirjinsu. 49 Amma duk
idon sani, da kuma matan da suka bi shi tun daga
Galili, suka tsaya daga nesa, suna duban wadannan
abubuwa. 50 Ga shi kuwa, wani mutum mai suna
Yusufu, shi dan majalisa ne, nagari ne kuma mutum
mai adalci ne 51 (bai yarda da shawarar da kuma abin
da suka aikata ba), daga Arimatiya a kasar Yahudiya,
wanda yake jiran mulkin Allah. 52 Wannan mutum,
ya sami Bilatus, ya tambaya a bashi jikin Yesu. 53 Ya
saukar da shi kasa, sai ya nade shi cikin likafani na
linin mai kyau, ya kwantar da shi cikin kabari da aka
sassaka shi daga dutse, inda ba a taba binne wani
ba. 54 Ranar kuwa, ranar shiri ce, Asabaci kuma ta
kusato. 55 Matan da suka taho da shi tun daga Galili,
suka biyo baya, su ga kabarin da inda aka ajiye shi.
56 Suka koma, sai suka shirya kayan kamshi da mai.
Suka kuma huta a ranar Asabaci bisa ga doka.

**24** Da sassafe a ranar farko ta mako, suka zo kabarin,
suka kawo kayan kamshi wadda suka shirya. 2
Sai suka samu dutsen a mirgine shi daga kabarin.
3 Suka shiga ciki, amma ba su sami jikin Ubangiji
Yesu ba. 4 Ya faru kuwa, yayin da suke a rikice game

da wannan, ba zato, mutane guda biyu suka tsaya
a gabansu da tufafi masu walkiya. 5 Sa'adda matan
suka sunkuyar da kansu kasa domin tsoro, suka ce wa
matan, “Don me kuke neman mai rai ciki matattatu?
6 Baya nan, amma ya tashi! Ku tuna fa yadda ya yi
maku magana tun sa'adda ya ke Galili, 7 cewa za a
ba da Dan Mutum ga mutane masu zunubi su kuma
giciye shi, a rana ta uku, zai tashi kuma” 8 Sai matan
suka tuna da kalmominsa, 9 suka koma daga kabarin
sai suka gaya wa sha dayan wadannan abubuwan da
dukan sauran. 10 Su Maryamu Magadaliya, Yuwana,
Maryamu uwar Yakubu, da sauran matan da ke tare da
su suka ba manzanni rohoton wadannan abubuwan.
11 Amma manzannin suka dauki maganar kamar ba
ta da amfani, kuma ba su bada gaskiya ga matan
ba. 12 Duk da haka Bitrus ya tashi, sai ya gudu zuwa
kabarin, ya sunkuya yana kallon ciki, sai ya gan
likaftani linin kadai. Sa'annan Bitrus ya tafi gidansa,
yana ta mamakin abinda ya faru. 13 A ranan nan, sai
ga biyu daga cikinsu suna tafiya zuwa wani kauye
suna Imawus, wanda nisansa kimanin mil ne daga
Urushalima. 14 Suna tattaunawa da junansu game
da dukan abubuwan da suka faru. 15 Sai ya zama da
cewa, sa'adda su ke tattaunawa tare da tambayoyi, sai
Yesu da kansa ya matsa kusa yana tafiya tare da su. 16
Amma idanunsu basu iya ganewa da shi ba. 17 Yesu ya
ce masu, “Menene ku ke magana akai sa'adda ku ke
tafiya?” Suka tsaya a wurin suna bakin ciki. 18 Daya
daga cikinsu, mai suna Kiliyobas, ya amsa masa, “Kai
ne kadai mutumin da ke Urushalima wanda bai san
abubuwan da suka faru a can a wannan kwanakin ba?”
19 Yesu ya ce masu, “Wadanne abubuwa?” Suka amsa
masa, “Abubuwa game da Yesu ba Nazarat, wanda ya
ke annabi ne, mai manyan ayuka da kalmomi daga
Allah da kuma mutane. 20 Da yadda manyan firistoci
da masu mulkinmu suka bada shi domin a hukunta
shi ga mutuwa a kuma giciye shi. 21 Amma mun yi
begen cewa shine wanda za ya yantar da Isra'ila. I,
bayan wannan kuma, yanzu kwana uku kenan tunda
wadannan abubuwan suka faru. 22 Amma har'ila yau,
wadansu mata da ke tare da mu sun yi mana abin
al'ajabi, da suka kasance a kabarin tunda sassafe. 23
Sa'adda ba su sami jikinsa ba, suka zo, da cewa su ma
sun ga wahayin mala'iku wadanda suka ce masu ya na
da rai. 24 Wasu maza wadanda ke tare da mu suka tafi
kabarin, suka tarar da shi kamar yadda matan suka
fada. Amma ba su ganshi ba.” 25 Yesu ya ce masu,
“Ku mutane masu wauta da marasa ba da gaskiya
ga abin da annabawa suka fada! 26 Bai zama dole ne
Almasihu ya sha wahalan wadannan abubuwan ba, ya
kuma shiga cikin daukakarsa?” 27 Sa'annan da farko
daga Musa da har zuwa dukan annabawa, Yesu ya
fasara masu duka abubuwa da ke game da kansa a
dukan littattafai. 28 Da suka yi kusa da kauyen, inda
suke tafiya, ko da yake Yesu ya yi kamar zai wuce
su. 29 Amma suka tilasta shi, cewa, “Ka zauna da mu,
gama yamma ta yi kusa rana kuma ta kusa karewa.”
Sai Yesu ya tafi ya zauna da su. 30 Ya faru cewa,
sa'adda ya zauna tare da su domin ya ci abinci, sai ya
dauki gurasan, ya albarkace shi, ya kakkarya, sai ya ba
su. 31 Sa'annan idanunsu suka bude, da suka gane
shi, sai ya bace daga garesu, 32 Suka ce wa junansu,
ashe zuciyarmu ba ta yi kuna a cikinmu ba, sa'adda
yake magana da mu a hanya, sa'adda ya bude mana
littattafai?” 33 Suka tashi a wancan sa'a, sai suka
koma Urushalima. Suka sami sha dayan nan tare, da
wadanda suke tare da su, 34 cewa, “Lalle ne Ubangiji
ya tashi, ya kuma bayyana ga Siman.” 35 Sai suka fadi
abubuwan da suka faru a hanya, da yadda aka bayyana
masu Yesu sa'adda ya kakkarya gurasa. 36 Sa'adda
suke fadin wadannan abubuwan, sai Yesu ya tsaya
a sakaninsu, sai ya ce masu, “Salama a gareku.” 37
Amma suka firgita suna cike da tsoro, suna tsammani
sun ga fatalwa. 38 Yesu ya ce masu, don me ku ke
damuwa? Don me tambayoyi ke tasowa a zuciyarku?
39 Duba hannayena da kafafuna, cewa nine da kaina.
Taba ni ku gani. Gama ruhu ba shi da jiki da kashi,
kamar yadda ku ka ga nake da su.” 40 Bayan da ya fadi
wannan, sai ya nuna masu hannayensa da kafafunsa.
41 Sa'adda suke cike da farin ciki, da mamaki, Yesu ya
ce masu, “Kuna da wani abinci?” 42 Sai suka bashi
gasasshen kifi. 43 Yesu ya karba, ya ci a gabansu. 44
Sai ya ce masu, “Sa'adda nake tare da ku na gaya
maku cewa duka abin da aka rubuta a cikin dokokin
Musa da na annabawa da Zabura dole su cika.” 45 Sai
ya bude hankalinsu, saboda su gane littattafai. 46 Ya
ce masu, “A rubuce yake, cewa Almasihu za ya sha
wuya, zai tashi kuma daga matattu a rana ta uku. 47
Ku yi wa'azin tuba da gafarar zunubai a cikin sunansa
ga dukan al'ummai, ku fara daga Urushalima. 48 Ku
shaidu ne ga wadannan abubuwan. 49 Duba, ina aiko
da alkawarin Ubana a kanku. Amma ku jira a birni, sai
an suturta ku da iko daga sama.” 50 Sa'annan Yesu ya
tafi tare da su har sai da suka kai kusa da Betanya. Sai

ya daga hannunsa ya albarkace su. 51 Ya zama sa'adda
yake sa masu albarka, ya bar su sai aka dauke shi zuwa
cikin sama. 52 Sai suka yi masa sujada, suka komo
Urushalima da murna mai yawa. 53 Kullayaumin suna
cikin haikali, suna albarkatar Allah.

# Yohanna

**1** A cikin farko akwai Kalma, Kalmar kuma tana tare
da Allah, wannan Kalma kuwa Allah ne. 2 Shi kuwa
tare da Allah yake tun farko. 3 Dukan abu ta wurinsa
aka yi su, babu abin da aka halitta sai ta wurin sa. 4 A
cikinsa rai ya ke, kuma wannan rai ya zama haske ga
dukan mutane. 5 Hasken ya haskaka a cikin duhu,
kuma duhun bai rinjaye shi ba. 6 Akwai wani mutum
wanda Allah ya aiko, mai suna Yahaya. 7 Ya zo a
matsayin mai ba da shaida game da hasken, domin
kowa ya ba da gaskiya ta wurinsa. 8 Ba Yahaya ne
hasken ba, amma ya zo ne domin ya shaida hasken.
9 Wannan shine haske na gaskiya mai ba da haske
ga dukan mutane, da ke zuwa cikin duniya. 10 Yana
cikin duniya, kuma an halicci duniya ta wurinsa,
amma duniya bata san shi ba. 11 Ya zo wurin nasa,
amma nasa basu karbe shi ba. 12 Amma duk iyakar
wadanda suka karbe shi, suka kuma ba da gaskiya
ga sunansa, ya ba su 'yanci su zama 'ya'yan Allah.
13 Wadanda aka haife su ba ta wurin jini ba, ko ta
wurin nufin jiki, ko nufin mutum, amma ta wurin
Allah. 14 Kalmar kuma ya zama jiki ya zauna cikin
mu. Mun ga daukakarsa, daukaka irin ta makadaici
shi kadai wanda ya zo daga Uban, cike da alheri da
gaskiya. 15 Yahaya ya yi shaida akansa yana kira da
karfi, cewa, “Wannan shine wanda na yi magana a
kansa cewa, 'Shi wanda ke zuwa bayana, ya fi ni,
domin ya kasance kafin ni.'” 16 Domin daga cikarsa
ne muka karbi alheri akan alheri. 17 Gama shari'a
ta zo daga wurin Musa. Alheri da gaskiya sun zo ta
wurin Yesu Almasihu. 18 Babu lokacin da wani ya taba
ganin Allah, shi wanda shi kadai ne Allah, wanda ke
jingine da kirjin Uba, shi ya bayyana shi. 19 Wannan
ita ce shaidar Yahaya sa'adda Yahudawa suka aika da
Firistoci da Lawiyawa zuwa gareshi don su tambaye
shi, “Wanene kai?” 20 Ya fada dalla dalla, kuma bai
musunta ba, yana amsa masu cewa, “ba nine Almasihu
ba.” 21 Sai suka tambaye shi, “To kai wanene? Kai Iliya
ne?” Yace, “Ba ni ba ne.” Suka ce, “Kai ne anabin?”
Ya amsa, “A'a”. 22 Sai suka ce masa, “Kai wanene,
domin mu bada amsa ga wadanda suka aiko mu? Me
kake fadi game da kanka?” 23 Yace, “Ni murya ne,
da ke kira cikin jeji, 'Ku daidaita hanyar Ubangiji,'
kamar yadda annabi Ishaya ya fada.” 24 Su wadanda
aka aika daga wurin Farisawa suke. Sai suka tambaye
shi cewa, 25 “To don me kake baftisma idan kai ba
Almasihu bane, ko Iliya, ko annabin?”. 26 Yahaya ya
amsa masu, cewa, “Ina baftisma ne da ruwa. Amma a
cikinku akwai wani tsaye wanda ba ku sani ba, 27 shi
wanda ke zuwa bayana, wanda ko igiyar takalminsa
ban isa in kwance ba.” 28 Wadannan abubuwa sun
faru ne a Baitanya, a dayan ketaren Urdun, a wurin
da Yahaya ke Baftisma. 29 Washegari, Yahaya ya ga
Yesu yana zuwa wurinsa ya ce, “Duba, ga Dan Ragon
Allah wanda ke dauke zunubin duniya! 30 Wannan
shine wanda na fada maku cewa, “Shi wanda ke zuwa
bayana ya fi ni, domin ya kasance kafin ni.' 31 Ban san
shi ba, amma saboda a bayyana shi ga Isra'ila ne nazo
ina baftisma da ruwa. “ 32 Yahaya ya shaida, cewa,
“Na ga Ruhu yana saukowa kamar kurciya daga sama,
ya kuma zauna a kansa. 33 Ban gane shi ba, amma shi
wanda ya aiko ni in yi baftisma cikin ruwa ya fada
mani cewa, 'duk wanda ka ga Ruhun ya sauka kuma
ya zauna a kansa, shine wanda ke yin baftisma cikin
Ruhu mai tsarki.' 34 Na gani, na kuma shaida cewa
wannan shine Dan Allah.” 35 Kuma, washegari, da
Yahaya na tsaye da biyu daga cikin almajiransa, 36
suka ga Yesu na wucewa, sai Yahaya ya ce, “Duba, ga
Dan rago na Allah!” 37 Sai almajiransa biyu suka ji ya
fadi haka, suka kuwa bi Yesu. 38 Da Yesu ya waiwaya
ya gan su suna bin sa, sai ya ce masu, “Me kuke
so?” Suka amsa, “Rabbi (wato 'Mallam'), ina kake da
zama?” 39 Yace masu, “Zo ku gani.” Sai suka zo suka
ga inda yake zama; suka zauna da shi ranan nan, gama
wajen sa'a ta goma ne. 40 Daya daga cikin wadanda
suka ji maganar Yahaya suka kuma bi Yesu shine
Andarawus, dan'uwan Siman Bitrus. 41 Ya fara neman
dan'uwansa Siman yace masa, “Mun sami Almasihu”
(wanda ake kira 'Kristi'). 42 Ya kawo shi wurin Yesu.
Yesu ya dube shi yace, “Kai ne Siman dan Yahaya.
Za a kira ka Kefas,” (ma'ana, 'Bitrus'). 43 Washegari,
da Yesu yana shirin tafiya zuwa Galili, sai ya sami
Filibus, ya ce masa, “ka biyo ni.” 44 Filibus dan asalin
Baitsaida ne, garin Andarawus da Bitrus. 45 Filibus ya
sami Natana'ilu yace masa, “Mun same shi, shi wanda
Musa ya rubuta shi a cikin attaura, da annabawa: Yesu
Dan Yusufu, Ba-Nazarat.” 46 Natana'ilu ya ce masa,
“za a iya samun wani abu nagari a Nazarat?” Filibus
yace masa, “Zo ka gani.” 47 Yesu ya ga Natana'ilu
yana zuwa wurinsa sai yayi magana game da shi,
“Duba, Ba-Isra'ile na hakika wanda babu yaudara a
cikinsa.” 48 Natana'ilu yace masa, “Ta yaya ka san
ni?” Sai Yesu ya amsa masa yace, “Tun kafin Filibus

ya kira ka, sa'adda kake a gindin baure, na gan ka."
49 Natana'ilu ya amsa, "Rabbi, Kai Dan Allah ne! Kai
Sarkin Isra'ila ne!" 50 Yesu ya amsa masa yace, "Don
na ce maka, 'Na gan ka a gindin Baure', ka gaskanta?
Za ka ga abubuwa da suka fi wannan girma." 51 Sai
yace, 'Hakika, hakika ina gaya maka, zaka ga sammai
a bude, mala'ikun Allah kuma suna hawa suna sauka
akan Dan Mutum."

2 Bayan kwana uku, akwai aure a Kana ta Galili,
mahaifiyar Yesu kuma tana wurin. 2 An gayyaci
Yesu da almajiransa zuwa auren. 3 Da ruwan inabin
ya kare, maihafiyar Yasu tace masa, "basu da ruwan
inabi." 4 Yesu yace mata, "Mace, me yasa kika zo
wurina? Lokaci na bai yi ba tukuna". 5 Maihafiyarsa
tace wa ma'aikatan, "Ku yi duk abin da yace maku." 6
To akwai randunan ruwa na dutse guda shidda a wurin
wadanda Yahudawa ke amfani da su domin al'adansu
na tsarkakewa, kowace zata iya daukar durom guda. 7
Yesu yace masu, "Cika randunan da ruwa". Sai suka
cika randunan makil. 8 Sai yace wa ma'aikatan, "Ku
diba daga ciki ku kai wa shugaban biki." Sai suka
yi hakannan. 9 Shugaban bikin ya dandana ruwan
da ya zama ruwan inabin, amma bai san inda ya
fito ba (amma ma'aikatan wadanda suka jawo ruwan
sun sani). Sai ya kira ango 10 yace masa, "Kowane
mutum yakan raba ruwan inabi mai kyau da farko,
kafin mai arhar bayan an shanye mai kyaun. Amma
kai ka ajiye mai kyaun sai yanzu." 11 Wannan alama
ta farko ce da Yesu yayi a Kana ta Galili, ya kuma
bayyana daukakarsa, almajiransa kuma suka gaskata
da shi. 12 Bayan wannan, Yesu, da mahaifiyarsa, da
'yan'uwansa da almajiransa suka tafi Kafarnahum,
kuma suka zauna can wasu 'yan kwanaki. 13 To idin
ketarewa na Yahudawa ya kusato, Yesu kuwa ya wuce
zuwa Urushalima. 14 Ya iske wadanda suke sayar da
shanu da tumaki da tantabaru, masu canjin kudi kuma
na zaune a wurin. 15 Sai yayi tsumingiya da igiyoyi ya
kore su duka daga cikin haikalin, duk da tumakin da
shanun. Sai ya watsar da sulallan masu canjin kudin
ya birkitar da teburansu. 16 Yace wa masu sayar da
tantabaru, "Ku fitar da wadannan abubuwa daga nan.
Ku daina maida gidan Ubana wurin kasuwanci." 17
Almajiransa suka tuna a rubuce yake, "Himma domin
gidanka za ta cinye ni." 18 Sai shugabannin Yahudawa
suka amsa suka ce masa, "Wace alama za ka nuna
mana, da shike kana yin wadannan abubuwan?" 19
Yesu ya amsa, "Ku rushe wannan haikali, kuma a cikin
kwana uku zan gina shi." 20 Sai shugabanin Yahudawa
suka ce, "An dauki shekaru arba'in da shidda kamin a
gama gina wannan haikalin, za ka dau kwanaki uku
kadai wajen gina shi?" 21 Amma yana nufin haikali na
jikinsa ne. 22 Bayan da aka tashe shi daga matattu,
sai almajiransa suka tuna ya fadi haka, suka kuma
ba da gaskiya ga nassi da wannan kalami da Yesu ya
fada. 23 Kuma, da yana Urushalima a idin ketarewa, a
lokacin idin, mutane da yawa suka gaskata ga sunansa,
sa'adda suka ga alamun da ya yi. 24 Amma Yesu bai
yadda da su ba domin ya san su duka, 25 saboda baya
bukatar wani ya shaida masa game da mutum, domin
ya san abinda ke cikin sa.

3 akwai wani Bafarise da ake kira Nikodimu, shugaba
a cikin Yahudawa. 2 Wannan mutum ya zo wurin
Yesu da dare ya ce masa, "Rabbi, mun sani cewa kai
malami ne da kazo daga wurin Allah, gama ba wanda
zai iya yin wadannan alamu da kake yi sai idan Allah
na tare da shi." 3 Yesu ya amsa masa, "Hakika, hakika,
idan ba a sake haifuwar mutum ba, ba zai iya ganin
mulkin Allah ba." 4 Nikodimu ya ce masa, "Yaya za
a sake haifuwar mutum bayan ya tsufa? Ba zai iya
sake shiga cikin cikin uwarsa kuma a haife shi ba, zai
iya?" 5 Yesu ya amsa, "Hakika, hakika, idan ba a haifi
mutum da ruwa da kuma Ruhu ba, ba zai iya shiga
cikin mulkin Allah ba. 6 Abin da aka haifa ta wurin
jiki, jiki ne, kuma abin da aka haifa ta wurin Ruhu,
Ruhu ne. 7 Kada ka yi mamaki don na ce maka, 'dole
a maya haifuwar ka.' 8 Iska takan hura duk inda ta ga
dama. Ka kan ji motsin ta, amma ba ka san inda ta fito
ko inda za ta tafi ba. Haka duk wanda aka haifa daga
Ruhu." 9 Nikodimu ya amsa yace masa, "Yaya wannan
zai yiwu?" 10 Yesu ya amsa yace masa, "Kai malami ne
a Israila amma ba ka san wadannan al'amura ba? 11
Hakika, hakika, ina gaya maka, muna fadin abubuwan
da muka sani, kuma muna shaida abubuwan da muka
gani. Duk da haka ba ku karbi shaidar mu ba. 12 Idan
na gaya maka abubuwan da ke na duniya amma baka
gaskata ba, to yaya zaka gaskata idan na gaya maka
abubuwa na sama? 13 Babu wanda ya taba hawa zuwa
sama sai dai shi wanda ya sauko daga sama: wato Dan
Mutum. 14 Kamar yadda Musa ya ta da maciji a jeji,
haka ma dole a ta da Dan Mutum 15 domin dukan
wadanda suka bada gaskiya gareshi su sami rai na har
abada. (aiōnios g166) 16 Gama Allah ya kaunaci duniya
sosai, har ya ba da makadaicin Dansa, domin duk

wanda ya bada gaskiya gareshi, kada ya mutu, amma
ya samu rai madawwami. (aiōnios g166) 17 Gama Allah
bai aiko da Dansa cikin duniya domin ya kayar da
duniya ba, amma domin a ceci duniya ta wurin sa. 18
Duk wanda ya bada gaskiya gare shi ba a kayar da shi
ba, amma duk wanda bai bada gaskiya gare shi ba an
riga an kayar da shi, domin bai bada gaskiya ga sunan
wannan da shi kadai ne Dan Allah ba. 19 Wannan shi
ne dalilin shari'ar, domin haske ya zo duniya, amma
mutane suka kaunaci duhu fiye da hasken, sabili da
ayyukan su na mugunta ne. 20 Domin duk wanda
ke mugayen ayyuka ya ki haske, kuma baya zuwa
wurin hasken domin kada ayyukansa su bayyanu. 21
Sai dai duk wanda yake aikata gaskiya kan zo wurin
hasken domin ayyukansa, da ake aiwatarwa ga Allah,
su bayyanu. 22 Bayan wannan, Yesu da almajiransa
suka tafi kasar Yahudiya. A can ya dan zauna tare da
su ya kuma yi Baftisma. 23 Yahaya ma yana Baftisma a
Ainon kusa da Salim domin akwai ruwa da yawa a
can. Mutane na zuwa wurin sa yana masu Baftisma,
24 domin a lokacin ba a jefa Yahaya a kurkuku ba
tukuna. 25 Sai gardama ta taso tsakanin almajiran
Yahaya da wani Bayahude akan al'adun tsarkakewa.
26 Suka je wurin Yahaya suka ce, “Rabbi, wanda yake
tare da kai a dayan ketaren kogin Urdun, kuma ka
shaida shi, duba, yana baftisma, kuma mutane duka
suna zuwa wurin sa.” 27 Yahaya ya amsa, “Mutum ba
zai iya samun wani abu ba sai an ba shi daga sama. 28
Ku da kanku zaku shaida na ce, 'Ba ni ne Almasihu
ba' amma amaimakon haka, 'an aiko ni kafin shi.' 29
Amaryar ta angon ce. Yanzu abokin angon, wanda
ke tsaye yana saurarensa, yana murna sosai saboda
muryan angon. Murnata ta cika domin wannan. 30
Dole shi ya karu, ni kuma in ragu. 31 Shi wanda ya
fito daga sama ya fi kowa. Shi Wanda ya zo daga
duniya, na duniya ne, kuma game da duniya yake
magana. Shi wanda ya fito daga sama yana saman
kowa. 32 Ya shaida abubuwan da ya ji ya kuma gani,
amma babu wanda ya karbi shaidarsa. 33 Duk wanda
ya karbi shaidarsa ya tabbatar Allah gaskiya ne. 34
Domin duk wanda Allah ya aika kan yi magana da
kalmomin Allah. Domin bai bada Ruhun da ma'auni
ba. 35 Uban ya kaunaci Dan, ya kuma ba da dukan
komai a hanunsa. 36 Shi wanda ya bada gaskiya ga
Dan ya na da rai madawwami, amma wanda ya ki
yiwa Dan biyayya ba zai ga rai ba, amma fushin Allah
na kansa. (aiōnios g166)

# 4

Da Yesu ya sani cewa Farisawa sun ji cewa yana
samun almajirai yana kuma yi masu baftisma fiye
da Yahaya 2 (ko da shike ba Yesu da kansa ke yin
baftismar ba, amma almajiransa ne), 3 ya bar Yahudiya
ya koma Galili. 4 Amma ya zamar masa dole ya ratsa
ta Samariya. 5 Ya zo wani birnin Samariya, mai suna
Sika, kusa da filin da Yakubu ya ba dansa Yusufu. 6
Rijiyar Yakubu na wurin. Da Yesu ya gaji da tafiyarsa
sai ya zauna gefen rijiyar. Kusan karfe goma sha biyu
na rana ne. 7 Wata mace, Ba-Samariya ta zo domin
ta dibi ruwa, sai Yesu ya ce mata, “Ba ni ruwa in
sha.” 8 Gama almajiransa sun tafi cikin gari don sayen
abinci. 9 Sai ba-Samariyar tace masa, “Yaya kai da
kake Bayahude kake tambaya ta ruwan sha, ni da
nike 'yar Samariya?” Domin Yahudawa ba su harka da
Samariyawa. 10 Sai Yesu ya amsa yace mata, “In da
kin san kyautar Allah, da shi wanda yake ce da ke,
'Ba ni ruwan sha,' da kin roke shi, sai kuma ya ba ki
ruwan rai.” 11 Matar tace masa, “Mallam, ga shi ba ka
da guga, kuma rijiyar tana da zurfi. Ina za ka samu
ruwan rai? 12 Ai ba ka fi Ubanmu Yakubu ba, ko ka fi
shi, shi wanda ya ba mu rijiyar, shi kansa kuma ya sha
daga cikin ta, haka kuma 'ya'yansa da shanunsa?”
13 Yesu ya amsa yace mata, “duk wanda ya sha daga
wannan ruwan zai sake jin kishi, 14 amma duk wanda
ya sha daga ruwa da zan ba shi ba zai sake jin kishi
ba. Maimakon haka, ruwan da zan bashi zai zama
mabulbular ruwa a cikinsa wanda ke bulbula zuwa rai
madawwami.” (aiōn g165, aiōnios g166) 15 Matar tace masa,
“Mallam, ka ba ni wannan ruwa yadda ba zan kara
jin kishi ba ba kuma sai na zo nan don in dibi ruwa
ba.” 16 Yesu ya ce mata, “Je, ki kira maigidanki ku
zo nan tare.” 17 Matar ta amsa tace masa, “Ba ni da
miji.” Yesu yace, “Kin fadi daidai da kika ce, 'ba ni
da miji,' 18 domin kin auri mazaje har biyar, kuma
wanda kike da shi yanzu ba mijin ki bane. Abinda
kika fada gaskiya ne.” 19 Matar tace masa, “Mallam,
Na ga kai annabi ne. 20 Ubaninmu sun yi sujada a
wannan dutse, amma kun ce Urushalima ce wurin da
ya kamata mutane su yi sujada.” 21 Yesu ya ce mata,
“Mace, ki gaskata ni, cewa lokaci na zuwa wanda ba za
ku yi wa Uban sujada ba ko akan wannan dutse ko a
Urushalima. 22 Ku kuna bauta wa abinda ba ku sani ba.
Mu muna bauta wa abinda muka sani, gama ceto daga
Yahudawa yake. 23 Sai dai, sa'a tana zuwa, har ma ta
yi, wadda masu sujada na gaskiya za su yi wa Uba
sujada a cikin ruhu da gaskiya, domin irin wadannan

ne Uban ke nema su zama masu yi masa sujada. 24
Allah Ruhu ne, kuma mutanen da ke yi masa sujada,
dole su yi sujada cikin ruhu da gaskiya." 25 Matar
ta ce masa, "Na san Almasihu na zuwa (wanda ake
kira Kristi). Sa'adda ya zo, zai bayyana mana kowane
abu. 26 Yesu ya ce mata, "Ni ne shi, wanda ke yi maki
magana." 27 A daidai wannan lokaci, almajiransa suka
dawo. Suna ta mamakin dalilin da yasa yake magana
da mace, amma babu wanda yace, "Me kake so?" Ko
kuma, "Don me ka ke magana da ita?" 28 Sai matar ta
bar tulunta, ta koma cikin gari, tace wa mutanen, 29
"Ku zo ku ga wani mutum wanda ya gaya mani duk
wani abu da na taba yi. Wannan dai ba Almasihun
bane, ko kuwa?" 30 Suka bar garin suka zo wurinsa. 31
A wannan lokacin, almajiransa suna rokansa, cewa,
"Mallam, ka ci." 32 Amma ya ce masu, "ina da abinci
da ba ku san komai akai ba." 33 Sai almajiran suka ce
da junansu, "Babu wanda ya kawo masa wani abu ya
ci, ko akwai ne?" 34 Yesu ya ce masu, "Abincina shine
in yi nufin wanda ya aiko ni, in kuma cika aikinsa. 35
Ba ku kan ce, 'akwai wata hudu tukuna kafin girbi ya
zo ba?' Ina gaya maku, daga idanunku ku ga gonakin,
sun rigaya sun isa girbi. 36 Shi wanda ke girbi yakan
karbi sakamako ya kuma tattara amfanin gona zuwa
rai na har abada, ta haka shi mai shuka da shi mai
girbi za su yi farinciki tare. (aiōnios g166) 37 Gama cikin
wannan maganar take, 'Wani na shuka, wani kuma na
girbi.' 38 Na aike ku ku yi girbin abinda ba ku yi aiki a
kai ba. Wandansu sun yi aiki, ku kuma kun shiga cikin
wahalarsu. 39 Yawancin Samariyawan da ke wannan
birni suka gaskata da shi sabili da labarin matar data
bada shaida, "Ya gaya mani duk abinda na taba yi."
40 To sa'adda Samariyawa suka zo wurinsa, sai suka
roke shi ya zauna tare da su, ya kuwa zauna wurin
kwana biyu. 41 Wasu da dama kuma suka gaskata
domin maganarsa. 42 Suka cewa matar, "Mun bada
gaskiya, ba saboda maganar ki kadai ba, amma mu
kanmu munji, yanzu kuma mun sani cewa wannan
lallai shine mai ceton duniya." 43 Bayan wadannan
kwana biyu, ya bar wurin zuwa Galili. 44 Domin Yesu
da kansa yace, ba a girmama annabi a kasarsa. 45 Da
ya zo Galili, Galiliyawan suka marabce shi. Sun ga
dukan abubuwan da ya yi a Urushalima wurin idin,
domin su ma sun je idin. 46 Kuma ya koma Kana ta
Galili inda ya mayar da ruwa zuwa ruwan inabi. Akwai
wani ma'aikacin fada wanda dansa na rashin lafiya a
Kafarnahum. 47 Da ya ji cewa Yesu ya bar Yahudiya
ya koma Galili, sai ya tafi wurin Yesu ya roke shi ya
sauko ya warka da dansa wanda ke bakin mutuwa. 48
Yesu yace masa, "Idan ba ku ga alamu da mu'ujizai
ba, ba za ku gaskata ba." 49 Ma'aikacin ya ce masa,
"Mallam, ka sauko kafin da na ya mutu." 50 Yesu yace
masa, "Je ka. Dan ka ya rayu." Mutumin ya gaskata
maganar da Yesu ya gaya masa, Sai yayi tafiyarsa. 51
Yayin da yake sauka kasa, bayinsa suka same shi, suna
cewa, danka yana raye. 52 Sai ya tambaye su sa'ar
da ya fara samun sauki. Suka amsa masa, "Jiya a sa'a
ta bakwai zazabin ya bar shi." 53 Sai Uban ya gane
cewa wannan sa'a ce Yesu ya ce masa, "Jeka, danka na
raye." Sabili da haka, shi da dukan gidansa suka bada
gaskiya. 54 Wannan ce alama ta biyu da Yesu ya yi
bayan da ya bar Yahudiya zuwa Galili.

5 Bayan haka akwai idi na yahudawa, kuma Yesu ya
tafi Urashalima. 2 To a cikin Urashilima kusa da
kofar tumaki akwai tabki, wanda ake kira Baitasda da
harshen Ibraniyanci, yana da shirayi biyar. 3 Taron
mutane dayawa masu ciwo da, makafi da guragu da
shanyayyu suna kwance a wurin [suna jira a dama
ruwan]. 4 Gama mala'ikan Ubangiji kan sabko a cikin
tabkin ya dama ruwan, wanda ya fara taba ruwan sai
ya warke komai cutar da yake da ita. 5 Akwai wani
mutum a bakin tabki yana kwance yana da rashin
lafiya har shekara talatin da takwas. 6 Da Yesu ya
gan shi yana kwance a wurin sai ya gane ya dade a
wurin, sai ya ce masa, "Ko kana so ka warke?" 7 Sai
mai rashin lafiyar ya amsa ya ce, "Malam, bani da
kowa da zai sa ni a cikin tabkin idan ruwan ya motsa.
Yayinda na ke kokari sai wani ya riga ni." 8 Yesu ya ce
masa," Ka tashi ka dauki shimfidarka ka tafi." 9 Nan
dan nan Mutumin ya warke, ya dauki shimfidarsa ya
tafi. Ranar kuwa Asabar ce. 10 Sai Yahudawa suka ce
da wanda aka warkar din, "Ai, Asabar ce, bai kuwa
halatta ka dauki shimfidarka ba." 11 Sai ya amsa
ya ce, "Ai wanda ya warkar da ni, shine ya ce mani
'Dauki shimfidarka, ka tafi." 12 Suka tambaye shi,
"wane mutum ne ya ce maka, 'Dauki shimfidar ka yi
tafiya'?" 13 Sai dai, shi wanda aka warka din, ba san
ko wanene ya warkar da shi ba, domin Yesu ya riga
ya tafi aboye, saboda akwai taro a wurin. 14 Bayan
haka, Yesu ya same shi a Haikalin, ya ce masa, "ka ga
fa, ka warke. To, kada ka kara yin zunubi don kada
wani abu da ya fi wannan muni ya same ka." 15 Sai
mutumin ya tafi ya gaya wa Yahuduwa cewa Yesu ne

ya warkar da shi. 16 To saboda haka Yahudawa suka
fara tsanantawa Yesu, don ya yi wadannan abubuwa
ran Asabar. 17 Yesu kuwa ya amsa masu ya ce, “Ubana
yana aiki har yanzu, ni ma ina aiki.” 18 Saboda haka,
Yahudawa suka kara nema su kashe shi ba don ya
keta Asabar kadai ba, amma kuma domin ya ce Allah
Ubansa ne, wato yana maida kansa dai-dai da Allah.
19 Yesu ya amsa masu ya ce, hakika hakika, ina gaya
maku, Dan ba ya yin kome shi kadai, sai abin da ya
ga Uba yana yi. 20 Domin Uban na kaunar Dan, yana
kuma nuna masa dukan abinda shi da kansa yake yi,
kuma zai nuna masa abubuwan da suka fi wadannan,
domin ku yi mamaki. 21 Gama kamar yadda Uba yakan
tada matattu ya kuma basu rai, haka Dan ma yake
bada rai ga duk wanda ya nufa. 22 Gama Uban ba ya
hukunta kowa, sai dai ya damka dukan hukunci ga
Dan, 23 domin kowa ya girmama Dan, kamar yadda
suke girmama Uban. Shi wanda ba ya girmama Dan,
ba ya girmama Uban da ya aiko shi. 24 Hakika, hakika,
duk mai jin Maganata, yana kuma gaskata wanda ya
aiko ni, yana da rai madawwami ba kuma za a kashe
shi ba, domin ya ratse daga mutuwa zuwa rai. (aiōnios
g166) 25 Hakika hakika, ina gaya maku, lokaci na zuwa,
har ma ya yi da matattatu za su ji muryar Dan Allah,
wadanda suka ji kuwa za su rayu. 26 Kammar yada
Uba ya ke da rai a cikinsa, haka ya ba Dan don ya
zama da rai cikin kansa. 27 Uban ya kuma ba Dan ikon
zartar da hukunci, saboda shi ne Dan Mutum. 28 Kada
ku yi mamakin wannan, domin lokaci na zuwa da
duk wadanda suke kaburbura za su ji muryarsa, 29 su
kuma fito: wadanda suka aikata nagarta zawa tashi na
rai, wadanda suka aikata mugunta kuwa zuwa tashi
na hukunci. 30 Ba na iya yin kome ni da kai na. Yadda
na ke ji, haka nake yin hukunci, Hukunci na kuwa na
adalci ne, domin ba nufin kaina nake bi ba, sai dai
nufin wanda ya aiko ni. 31 Idan zan yi shaida game
da kaina, shaidata baza ta zama gaskiya ba. 32 Akwai
wani wanda ya ke bada shaida game da ni, na kuwa
sani shaidar da yake bayarwa game da ni gaskiya
ce. 33 Kun aika zuwa wurin Yahaya, shi kuma ya yi
shaidar gaskiya. 34 Duk da haka shaidar da na karba
bata mutum bace. Na fadi wadanan abubuwa domin
ku sami ceto. 35 Yahaya fitila ne mai ci, mai haske
ne kuma, kun yarda ku yi farinciki da haskensa dan
lokaci kadan. 36 Amma shaidar da ni ke da ita ta fi ta
Yahaya karfi. Domin ayyukan da Uba ya bani ni in yi,
wato ainihin ayyukan da nake yi, su ne suke shaida ta
cewa, Uba ne ya aiko ni. 37 Uba wanda ya aiko ni, shi
da kansa ya shaide ni. Ba ku taba jin muryar sa ba, ko
ganin kamanninsa. 38 Maganarsa kuwa ba ta zaune a
zuciyarku, domin baku gaskata da wanda ya aiko ni
ba. 39 Kuna nazarin littattafai, don a tsammaninku a
cikinsu za ku sami rai Madawwami, alhali kuwa su ne
suke shaidata. (aiōnios g166) 40 kuma baku niyyar zuwa
wurina domin ku sami rai. 41 Ba na karbar yabo daga
wurin mutane, 42 amma na sani baku da kaunar Allah
a zuciyarku. 43 Na zo a cikin sunan Ubana, amma ba
ku karbe ni ba. Idan wani ya zo da sunan kansa, za ku
karbe shi. 44 Ta yaya za ku ba da gaskiya, ku da kuke
karban yabo daga junanku, amma ba ku neman yabon
dake zuwa daga wurin Allah? 45 Kada ku yi tunani
zan zarge ku a wurin Uba. Mai zargin ku shine Musa,
wanda kuka sa begenku a cikin sa. 46 Inda kun gaskata
Musa, da kun gaskata da ni domin ya yi rubutu game
da ni. 47 Idan kuwa ba ku gaskata abin da ya rubuta
ba, ta yaya za ku gaskata maganata?”

## 6

Bayan waddannan abubuwa, Yesu ya ketare tekun
Galili, wanda a ke kira tekun Tibariya. 2 Sai taro
mai yawa suka bi shi domin suna ganin alamu da
yake yi akan marasa lafiya. 3 Sai Yesu ya hau dutse
ya zauna a can tare da almajiransa. 4 (Kuma da idin
Ketarewa, wato idin Yahudawa, ya kusato.) 5 Da Yesu
ya daga kai sai ya ga babban taro yana zuwa wurinsa,
sai ya ce ma Filibus, “Ina za mu sayi gurasar da
Mutanen nan za su ci?” 6 ( Ya fadi haka ne domin ya
gwada shi, saboda shi kansa ya san abin da zai yi.)
7 Filibus ya amsa masa, “gurasar dinari biyu ma ba
zata ishi kowannensu ya samu ko kadan ba.” 8 Daya
daga cikin almajiransa, wato Andarawus, dan'uwan
Siman Bitrus, ya ce masa, 9 “Ga wani dan yaro nan da
dunkule biyar na sha'ir, da kifi biyu. Amma menene
wadannan za su yi wa mutane masu yawa?” 10 Yesu
ya ce, “ku sa mutane su zauna.”( wurin kuwa akwai
ciyawa.) Sai mazajen suka zauna, sun kai wajen dubu
biyar. 11 Sai Yesu ya dauki gurasar, bayan da ya yi
godiya, sai ya rarraba wa wadanda suke zaune. Haka
kuma ya rarraba kifin gwargwadon abin da zai ishe
su. 12 Da Mutanen suka ci suka kuma koshi, sai ya
ce wa almajiransa, ku tattara gutsattsarin da suka
rage, kada ya zama asara.” 13 Sai suka cika kwanduna
goma sha biyu da gutsattsarin gurasar nan biyar da
ya rage bayan da kowa ya ci. 14 Da jama'a suka ga
alamar da ya yi, sai suka ce, “Hakika wannan shi ne

annabin nan mai zuwa cikin duniya. 15 "Da Yesu ya
gane suna shirin zuwa su dauke shi da karfi da yaji
su nada shi sarki, sai ya sake komawa kan dutsen
da kansa. 16 Da yamma ta yi, sai almajiransa suka
gangara teku. 17 Suka shiga cikin jirgi, suka haye teku
zuwa kafarnahum. (A lokacin duhu ya yi, Yesu kuwa
bai riga ya iso wurinsu ba tukuna.) 18 Iska mai karfin
gaske tana kadawa, kuma tekun yana hargowa. 19
Bayan da almajiran suka yi tuki na wajen kimanin mil
ashirin da biyar ko talatin, sai suka hango Yesu yana
tafiya a kan teku ya kuma kusa da jirgin, sai suka
firgita. 20 Amma ya ce masu, "Ni ne! kada ku firgita."
21 Sa'an nan suka yarda suka karbe shi a cikin jirgin,
kuma nan da nan jirgin ya kai gacci. 22 Kashe gari,
sauran taron da suke tsaye a dayan hayin tekun suka
ga cewa babu wani jirgi a wajen sai dayan, Yesu kuma
bai shiga ciki da almajiransa ba, amma almajiransa
suka tafi su kadai. 23 Sai dai, akwai wadansu jirage
da suka zo daga Tibariya kusa da wurin da taron
suka ci gurasa bayan da Ubangiji ya yi godiya. 24
Sa'anda taron suka gane cewa Yesu da almajiransa ba
su wurin, su da kansu su ka shiga cikin jiragen suka
tafi Kafarnahum neman Yesu. 25 Da suka same shi a
hayin tekun, suka ce masa, "Mallam, yaushe ka zo
nan?" 26 Yesu ya amsa masu, da cewa, "hakika, kuna
nema na ne, ba don kun ga alamu ba, amma domin
kun ci gurasar nan kun koshi. 27 Ku daina yin wahala
a kan neman abinci mai lalacewa, sai dai a kan abinci
mai dawwama wanda zai kaiku ga rai madawwami
wanda Dan Mutum zai ba ku, domin Ubangiji Allah
ya sa hatiminsa a kansa." (aiōnios g166) 28 Sai suka ce
Masa, "Me za mu yi, domin mu aikata ayyukan Allah?
29 Yesu ya amsa, "Wannan shi ne aikin Allah: wato
ku gaskata da wanda ya aiko." 30 Sai suka ce masa,
"To wace alama za ka yi, don mu gani mu gaskata
ka? 31 Me za ka yi? Kakanninmu sun ci manna a jeji,
kamar yadda aka rubuta, "Ya ba su gurasa daga sama
su ci." 32 Sa'an nan Yesu ya ce masu, "hakika, hakika,
ina gaya maku ba Musa ne ya ba ku gurasa nan daga
sama ba, amma Ubana ne ya baku gurasa ta gaskiya
daga sama. 33 Gurasar Allah itace mai saukowa daga
sama mai kuma bada rai ga duniya," 34 Sai suka ce
masa, "Mallam, ka rika ba mu irin wannan gurasa
kodayaushe." 35 Yesu ya ce masu, "Ni ne gurasa mai
ba da rai. Wanda ya zo wurina ba zai ji yunwa ba,
wanda kuma ya gaskanta da ni ba zai kara jin kishi ba.
36 Amma na gaya maku cewa, hakika kun gan ni, duk
da haka ba ku ba da gaskiya ba. 37 Duk wanda Uba ya
bani zai zo gare ni, wanda kuwa ya zo gare ni ba zan
kore shi ba ko kadan. 38 Gama na sauko daga sama, ba
domin in bi nufin kaina ba, sai dai nufin wanda ya
aiko ni. 39 Wannan shi ne nufin wanda ya aiko ni,
kada in rasa ko daya daga cikin wadannan da ya bani,
sai dai in tashe su a ranar karshe. 40 Gama wannan shi
ne nufin Ubana, duk wanda yake ganin Dan ya kuma
gaskata da shi zai sami rai madawwami, ni kuma zan
tashe shi a ranar karshe. (aiōnios g166) 41 Sai Yahudawa
suka yi gunaguni akansa, domin ya ce, "Nine Gurasar
da ta sauko daga sama." 42 Suka ce, "Ba wannan ne
Yesu Dan Yusufu, wanda Ubansa da Uwarsa mun san
su ba? Ta yaya yanzu zai ce, 'Na ya sauko daga sama'?
43 Yesu ya amsa, ya ce masu, "Kada ku yi gunaguni a
junanku. 44 Ba mai iya zuwa wurina sai dai in Uba
wanda ya aiko ni ya jawo shi, ni kuwa zan tashe shi
a rana ta karshe. 45 A rubuce yake cikin litattafan
anabawa cewa, 'Dukkansu Allah zai koya masu'. Duk
wanda ya ji ya kuma koya daga wurin Uba, ya kan zo
gare ni. 46 Ba cewa wani ya taba ganin Uban ba, sai
shi wanda yake daga wurin Allah - shine ya ga Uban.
47 Hakika, hakika, wanda ya bada gaskiya, yana da rai
Madawwami. (aiōnios g166) 48 Ni ne Gurasa ta rai. 49
Ubanninku sun ci manna cikin jeji, suka kuma mutu.
50 Ga gurasa da ta sauko daga sama, domin mutum ya
ci daga cikinta ba kuwa zai mutu ba. 51 Ni ne gurasa
mai rai da ya sauko daga sama. Duk wanda ya ci daga
gurasar, zai rayu har abada. Wannan gurasar da zan
bayar jiki na ne don ceton duniya." (aiōn g165) 52 Sai
Yahudawa suka fusata a tsakanin junansu suka kuma
fara gardama, cewa, "Yaya mutumin nan zai iya bamu
naman jikinsa mu ci? 53 Sai Yesu ya ce masu, "hakika,
hakika, in ba ku ci naman jikin Dan mutum ba, ba ku
kuma sha jininsa ba, ba za ku sami rai a cikin ku ba.
54 Dukan wanda ya ci nama na ya kuma sha jinina
yana da rai Madawwami, ni kuwa zan tashe shi a
ranar karshe. (aiōnios g166) 55 Domin namana abinci
ne na gaske, jinina kuma abin sha ne na gaskiya. 56
Duk wanda ya ci namana, ya kuma sha jinina yana
zamne a ciki na, ni kuma a cikinsa. 57 Kamar yadda
rayayyen Uba ya aiko ni, nake kuma rayuwa saboda
Uban, haka ma wanda ya ci namana, zai rayu sabo da
ni. 58 Wannan itace gurasar da ta sauko daga sama, ba
irin wadda Ubanninku suka ci suka mutu ba. Dukan
wanda ya ci gurasar zai rayu har abada." (aiōn g165) 59
Yesu ya fadi wadan nan abubuwa a cikin majami'a

sa'ad da yake koyarwa a Kafarnahum. 60 Da jin haka,
da yawa daga cikin almajiransa suka ce, “Wannan
Magana yana da karfi, wa zai iya jinta?” 61 Yesu,
kuwa da yake ya sani a ransa da cewa almajiransa
suna gunagunin wannan, sai ya ce masu, “Wannan
ya zamar maku laifi? 62 Yaya Ke nan in kun ga Dan
Mutum yana hawa inda yake a da? 63 Ruhu shine mai
bayar da rai; Jiki ba ya amfana komai. Kalmomin da
na fada maku ruhu ne, da kuma rai. 64 Amma fa akwai
wadansun ku da ba su ba da gaskiya ba. Domin tun
farko Yesu ya san wadanda ba su ba da gaskiya ba, da
kuma wanda zai bashe shi. 65 Ya fada cewa, “shiyasa
na gaya maku, ba mai iya zuwa wurina, sai ta wurin
Uban.” 66 Bayan haka, da yawa daga cikin almajiransa
suka koma da baya, ba su kara tafiya tare da shi ba.
67 Sai Yesu ya ce wa goma sha biyun, “ku ba kwa so
ku tafi, ko ba haka ba? 68 Bitrus ya amsa masa ya ce,
“Ya Ubangiji, gun wa za mu je? kai kake da maganar
rai madawwami. (aiōnios g166) 69 Mu kwa mun gaskata
mun kuma sani kai ne mai tsarkin nan na Allah.” 70
Yesu ya ce masu, “Ba ni na zabe ku, goma sha biyu
ba, amma dayanku Iblis ne?” 71 Wato yana magana
akan Yahuda dan Siman Iskariyoti, shi kuwa daya
daga cikin sha-biyun ne, wanda zai ba da Yesu.

7 Bayan wadannan abubuwa Yesu ya zagaya cikin
Gallili, saboda baya so ya shiga cikin Yahudiya
domin Yahudawa suna shirin su kashe shi. 2 To Idin
Bukkoki na Yahudawa ya kusa. 3 Sai 'yan'uwansa
suka ce da shi, “ka tashi ka tafi Yahudiya, domin
almajiranka su ga ayyukan da kake yi su ma. 4 Ba
wanda ya ke yin wani abu a boye idan dai yana so
kowa da kowa ya san shi. Da yake ka na yin wadannan
abubuwa sai ka nuna kan ka a fili ga duniya. 5 Domin
ko 'yan'uwansa ma basu bada gaskiya gare shi ba. 6
Yesu ya ce dasu, “lokaci na bai yi ba tukuna, amma ku
koyaushe lokacin ku ne. 7 Duniya baza ta iya kin ku
ba, amma ta ki ni saboda ina fadin cewa ayyukanta ba
su da kyau. 8 Ku ku je wurin idin, ni ba zan je wurin
idin ba domin lokacina bai yi ba tukuna. 9 Bayan da ya
gaya masu wadannan abubuwa, ya tsaya a cikin Gallili.
10 Amma bayan da 'yan'uwansa su ka tafi wurin idin
shi ma ya tafi, amma a asirce ba a fili ba. 11 Saboda
Yahudawa suna neman sa a wurin idin, su na cewa
“Ina yake?” 12 Akwai maganganu dayawa a kansa
cikin taron. Wadansu suna cewa, “shi mutumin kirki
ne.” Wadansu kuma suna cewa,”A'a yana karkatar da
hankalin jama'a.” 13 Amma duk da haka ba wanda
ya yi magana a fili a kansa saboda suna jin tsoron
Yahudawa. 14 Sa'anda aka kai rabin idin, sai Yesu ya
shiga cikin haikali ya fara koyarwa. 15 Yahudawa suna
mamaki suna cewa,”Yaya aka yi wannan mutum ya
sami ilimi dayawa haka? Shi kuwa bai je makaranta
ba.” 16 Yesu ya ba su amsa ya ce,”Koyarwata ba tawa
ba ce, amma ta wanda ya aiko ni ce.” 17 Idan wani
yana so ya yi nufinsa, za ya gane koyarwannan ko
daga wurin Allah ta zo, ko ko tawa ce ta kaina. 18 Ko
wanene yake maganar kansa, yana neman darajar
kansa kenan, amma ko wanene ya nemi darajar wanda
ya aiko ni, wannan mutum mai gaskiya ne, babu
rashin adalci a cikin sa. 19 Ba Musa ya baku dokoki ba?
Amma duk da haka ba mai aikata dokokin. Me yasa ku
ke so ku kashe ni? 20 Taron suka ba shi amsa, “Ka
na da aljani. Wanene yake so ya kashe ka?” 21 Yesu
ya amsa ya ce masu, “Nayi aiki daya, dukan ku kuna
mamaki da shi. 22 Musa ya baku kaciya, (ba kuwa daga
Musa take ba, amma daga kakannin kakanni ta ke),
kuma a ranar Asabar kukan yi wa mutum kaciya. 23
Idan mutum ya karbi kaciya ranar Asabar, domin kada
a karya dokar Musa, don me kuka ji haushi na saboda
na mai da mutum lafiyayye sarai ranar Asabar? 24
Kada ku yi shari'a ta ganin ido, amma ku yi shari'a
mai adalci.” 25 Wadansun su daga Urushalima suka
ce, “wannan ba shine wannan da suke nema su kashe
ba?” 26 Kuma duba, yana magana a fili, sannan ba
wanda ya ce da shi komai. Ba zai yiwu ba mahukunta
su sani cewa wannan Kristi ne, ko ba haka ba? 27 da
haka, mun san inda wannan mutum ya fito. Amma
sa'anda Kristi za ya zo, ba wanda zai san inda ya
fito.” 28 Yesu yayi magana da karfi a haikali, yana
koyarwa ya na cewa, “Kun san ni kuma kun san inda
na fito. Ban zo domin kaina ba, amma wanda ya aiko
ni mai gaskiya ne, ku kuwa baku san shi ba. 29 Ni
na san shi domin daga wurinsa na fito, kuma shine
ya aiko ni.” 30 Suna kokari su kama shi, amma ba
wanda ya iya sa masa hannu domin sa'arsa ba ta yi ba
tukuna. 31 Duk da haka wadansu dayawa a cikin taron
suka bada gaskiya gare shi suka ce,”Sa'anda Kristi ya
zo, zai yi alamu fiye da wadanda wannan mutum ya
yi?” 32 Farisawa suka ji tattarmukan suna yin rada a
kan wadannan abubuwa game da Yesu, Sai manyan
malamai da Farisawa su ka aika jami'ai su kama shi.
33 Sa'annan Yesu yace ma su,” jimawa kadan ina tare
ku, sa'annan in tafi wurin wanda ya aiko ni. 34 Za ku

neme ni ba za ku same ni ba; inda na tafi, ba za ku iya
zuwa ba." 35 Yahudawa fa su ka cewa junan su, "Ina
wannan mutum zai je inda ba za mu iya samun sa
ba? Ko za ya tafi wurin Helinawa na warwatsuwa ya
koyawa Helinawa? 36 Wace kalma ya ke fadi haka,
'za ku neme ni amma ba za ku same ni ba; inda na
tafi, ba za ku iya zuwa ba'?" 37 To a rana ta karshe,
babbar rana ta idin, Yesu ya mike ya yi magana da
karfi cewa, "Idan kowa yana jin kishi, ya zo wuri na
ya sha. 38 Shi wanda ya bada gaskiya gare ni kamar
yadda nassi ya fadi, daga cikin sa rafukan ruwa na rai
za su bulbulo." 39 Amma ya fadi haka a kan Ruhu,
wanda wadanda suka bada gaskiya gare shi za su
karba; ba a ba da Ruhun ba tukuna, saboda ba a rigaya
an daukaka Yesu ba. 40 Wadansu a cikin taron, sa'anda
suka ji wadannan kalmomi, suka ce, "Wannan lallai
annabi ne." 41 Wadansu suka ce, "Wannan Almasihu
ne." Amma wadansu suka ce, "Almasihu zai fito daga
Gallili ne? 42 Ba nassi ya ce Almasihu zai fito daga
cikin dangin Dauda daga Baitalami ba, daga kauyen da
Dauda ya fito?" 43 Sai aka sami rabuwa a cikin taron
saboda shi. 44 Da wadansun su sun kama shi, amma
ba wanda ya sa masa hannu. 45 Sa'annan jami'an suka
dawo wurin manyan Fristoci da Farisawa, wadanda
suka ce," me yasa ba ku kawo shi ba?" 46 Jami'an
su ka amsa, "Ba mutumin da ya taba yin magana
kamar haka." 47 Farisawa suka amsa masu, "kuma an
karkatar da ku? 48 Ko wani daga cikin mahukunta ya
bada gaskiya gare shi, ko kuwa daga cikin Farisawa? 49
Amma wannan taro da basu san shari'a ba, la'anannu
ne." 50 Nikodimus ya ce masu, (shi wanda ya zo wurin
Yesu da, daya daga cikin Farisawa), 51 "Ko shari'armu
bata hana hukunta mutum ba, sai ta ji daga gare shi
ta kuma san abin da ya aikata ba?" 52 Suka amsa masa
suka ce,"kai ma daga Galili ka fito? Ka yi bincike ka
gani ba annanbin da zai fito daga Galili." 53 Daga nan
sai kowa ya tafi gidansa.

**8** Yesu ya je Dutsen Zaitun. 2 Da sassafe ya dawo
Haikali, dukan mutane kuma suka zo wurin sa;
yazauna koya masu. 3 Sai marubuta da Farisawa suka
kawo mace wadda aka kama ta tana zina. Su ka sa ta a
tsakiya. 4 Sai su ka ce da shi, "Malam, wannan mace
an kama ta tana cikin yin zina. 5 A cikin shari'a, Musa
ya bamu umurni mu jejjefe irin wandannan mutume,
kai me ka ce game da ita?" 6 Sun fadi haka ne domin
su gwada shi su sami abinda za su zarge shi da shi,
amma Yesu ya sunkuya yayi rubutu da yatsansa a
kasa. 7 Sa'adda suka cigaba da tambayar sa, ya mike
tsaye yace masu, "shi wanda ba shi da zunubi a cikin
ku, ya fara jifar ta da dutse." 8 Ya sake sunkuyawa,
ya yi rubutu da yatsansa a kasa. 9 Da suka ji haka,
sai suka fita dai-dai da dai-dai, kama daga babbansu.
A karshe dai aka bar Yesu shi kadai, tare da matar
wadda ta ke a tsakiyar su. 10 Yesu ya tashi tsaye ya
ce da ita, "mace, ina masu zargin ki? Ba wanda ya
kashe ki? 11 Ta ce, "Ba kowa, Ubangiji" Yesu ya ce,
"Ni ma ban kashe ki ba. Ki yi tafiyar ki, daga yanzu
kada ki kara yin zunubi." 12 Yesu ya kara yin magana
da mutanen cewa, "Ni ne hasken duniya, shi wanda
ya biyo ni, ba zai yi tafiya cikin duhu ba, amma za
ya sami hasken rai. 13 Farisawa suka ce masa, "Kana
bada shaida a kan ka, shaidarka ba gaskiya ba ce."
14 Yesu ya amsa ya ce masu, "Ko ma na bada shaida
a kai na, shaidata gaskiya ce, na san daga inda na
fito da inda zan tafi, amma ku baku san daga inda
na fito ba, baku kuma san inda zan tafi ba. 15 Kuna
shari'a ta son kai, ni ko ban yi wa kowa shari'a ba. 16
Ko ma da na yi shari'a, shari'ata gaskiya ce domin
ba ni kadai ba ne, amma ina tare da Uba wanda ya
aiko ni. 17 I, a cikin dokarku an rubuta cewa shaidar
mutum biyu gaskiya ce. 18 Ni ne ni ke shaidar kaina,
kuma Uba wanda ya aiko ni ya na shaida ta. 19 Su ka
ce da shi, "Ina ubanka?" Yesu ya amsa ma su ya ce,
"baku san ni ba balle Ubana, in da kun san ni da kun
san Uba na kuma. " 20 Ya fadi wadannan kalmomi a
kusa da wurin ajiya sa'adda ya ke koyarwa a cikin
haikali, kuma ba wanda ya kama shi saboda sa'arsa
bata yi ba tukuna. 21 Ya kara cewa da su,"Zan tafi, za
ku neme ni ba za ku same ni ba, za ku mutu cikin
zunubinku. Inda ni ke tafiya, ba za ku iya zuwa ba".
22 Yahudawa su ka ce,"Zai kashe kansa ne, da ya ce
inda ni ke tafiya ba za ku iya zuwa ba?" 23 Yesu ya
ce masu ku daga kasa kuke, Ni kuwa daga bisa ni ke.
Ku na wannan duniya ne, Ni kuwa ba na wannan
duniya ba ne. 24 Shiyasa na ce maku za ku mutu
cikin zunubanku. In ba kun bada gaskiya NI NE ba, za
ku mutu cikin zunubanku. 25 Sai kuma suka ce da
shi,"Wanene kai?" Yesu ya ce masu, "Abin da na gaya
maku tun daga farko. 26 Ina da a bubuwa da yawa da
zan gaya maku, in kuma hukunta ku a kai. Duk da
haka, wanda ya aiko ni, mai gaskiya ne, abubuwan da
naji daga wurin sa, wadannan abubuwan su ni ke gaya
wa duniya." 27 Ba su gane ba yana yi masu magana
a kan Uban. 28 Yesu ya ce, "Sa'adda kuka tada Dan

Mutum sama sa'annan za ku gane NI NE, kuma ban yi
komi domin kaina ba. Kamar yadda Uba ya koya mani,
haka nike fadin wadannan abubuwa. 29 Shi wanda ya
aiko ni, yana tare da ni kuma bai bar ni ni kadai ba,
domin kullum ina yin abubuwan da suke faranta masa
rai." 30 Sa'adda Yesu ya ke fadin wadannan abubuwa,
dayawa suka bada gaskiya gare shi. 31 Yesu ya gayawa
wadancan Yahudawa da suka bada gaskiya gare shi,
"Idan kun tsaya a cikin magana ta ku almajiraina ne
na gaskiya, 32 Kuma za ku san gaskiya, gaskiya kuwa
zata 'yantar da ku." 33 Suka amsa masa, "Mu zuriyar
Ibrahim ne kuma bamu taba yin bauta wurin kowa
ba, yaya za ka ce, 'Za a 'yantar da ku'?" 34 Yesu ya ce
masu, "Hakika, hakika, ina ce maku, dukan wanda ya
ke aika zunubi bawan zunubi ne. 35 Bawa kuwa, ba ya
zama a gida dindindin, da yana zama dindindin. (aiōn
g165) 36 Saboda haka, idan Dan ya 'yantar da ku zaku
zama 'yantattu sosai. 37 Na san ku zuriyar Ibrahim ne,
kuna so ku kashe ni saboda kalma ta bata da wurin
zama a cikin ku. 38 Na fadi abubuwan da na gani a
wurin Ubana, ku kuma kuna yin abubuwan da kuka
ji daga wurin ubanku." 39 Suka amsa suka ce masa,
"Ibrahim ne ubanmu" Yesu ya ce masu, "Da ku 'yayan
Ibrahim ne da kun yi ayukan da Ibrahim ya yi. 40
Amma, yanzu kuna so ku kashe ni, mutumin da ya
gaya maku gaskiyar da ya ji daga wurin Allah. Ibrahim
bai yi haka ba. 41 Kuna yin ayyukan ubanku. Suka ce
masa, "mu ba a haife mu cikin fasikanci ba, muna
da Uba daya: Allah." 42 Yesu ya ce masu, "Inda Allah
Ubanku ne, da kun kaunace ni, gama na zo daga wurin
Allah kuma ga ni anan, gama ba domin kaina nazo ba,
shine ya aiko ni. 43 Meyasa baku gane magana ta ba?
Ai saboda ba za ku iya jin maganata ba ne. 44 Ku na
ubanku, shaidan ne, kuma kuna so ku yi nufe-nufe na
ubanku. Shi mai kisan kai ne tun daga farko kuma ba
ya tsayawa gaskiya saboda da babu gaskiya a cikin sa.
Sa'anda yake fadin karya, yana maganar halinsa ne
domin shi dama makaryaci ne da uban karya kuma.
45 Dayake ina fadin gaskiya baku bada gaskiya gare ni
ba. 46 Wanene a cikin ku ya kama ni da zunubi? Idan
na fadi gaskiya don me ba ku gaskanta ni ba? 47 Shi
wanda yake na Allah ya kan ji maganar Allah, ku ba
kwa jin maganar Allah da yake ku ba na Allah bane,"
48 Yahudawa suka amsa suka ce masa, "Bamu fadi
gaskiya ba da muka ce kai Basamariye ne kuma kana
da aljan?" 49 Yesu ya amsa, "Ni ba ni da aljan, ina
girmama Ubana, ku kuma ba kwa girmama ni." 50 Ba
na neman daraja domin kaina, akwai wanda ke nema
yana kuma hukuntawa. 51 Hakika, hakika, iIna ce
maku, dukan wanda ya kiyaye maganata, ba za ya ga
mutuwa ba." (aiōn g165) 52 Sai Yahudawa su ka ce masa,
Yanzu mun sani kana da aljan. Ibrahim da annabawa
sun mutu, amma kai ka ce, 'dukan wanda ya yi biyayya
da maganata ba zai dandana mutuwa ba'. (aiōn g165) 53
Ai baka fi ubanmu Ibrahim girma ba wanda ya mutu,
ko ka fi shi? Annabawa kuma sun mutu. Wa kake
daukar kanka ne?" 54 Yesu ya amsa, "Idan na daukaka
kaina, daukaka ta banza ce, Ubana ne ya daukaka ni.
Wanda kuka ce shi ne Allahnku. 55 Ku kuwa ba ku san
shi ba, amma ni na san shi. Idan na ce ban san shi
ba, na zama kamar ku kenan, makaryaci. Sai dai, Ni
na san shi ina kiyaye maganarsa. 56 Ubanku Ibrahim
ya yi farinciki da ganin rana ta; ya gan ta kuma ya
yi murna." 57 Yahudawa su ka ce masa, "Baka kai
shekara hamsin ba tukuna, ka taba ganin Ibrahim?"
58 Yesu ya ce masu, "Hakika, hakika, ina ce maku,
kafin a haifi Ibrahim, NI NE." 59 Suka dauki duwatsu
za su jefe shi, amma Yesu ya boye kansa, ya fita daga
haikali.

9 Da Yesu yana wucewa, sai ya ga wani mutum
makaho tun daga haihuwa. 2 Sai almajiransa suka
tambaye shi, "Mallam, wa yayi zunubi, mutumin ne
ko iyayensa, har aka haife shi makaho?" 3 Yesu ya
amsa, Ba mutumin ne ko iyayensa suka yi zunubi ba,
amma domin aikin Allah ya bayyana a cikinsa. 4 Dole
mu yi aikin wanda ya aiko ni tunda rana. Dare na
zuwa inda ba mai iya yin aiki. 5 Yayinda ina duniya, ni
ne hasken duniya." 6 Bayan da Yesu ya fadi wadannan
abubuwan, ya tofa yawu a kasa, ya kwaba kasar da
yawunsa, sai ya shafe idanun mutumin da kasar. 7 Ya
ce masa, tafi, ka wanke a tafkin Siloam (ma'anarsa:
aike)." Sai mutumin ya tafi, ya wanke, ya dawo yana
gani. 8 Sai makwabtansa da mutanen da da suka gan
shi tun can yana roko suka ce, "Ba wannan mutum ne
wanda ya ke zaune yana roko ba?" 9 Wadansu suka
ce, "shi ne." Wadansu suka ce, "A'a, amma yana kama
da shi." Amma shi ya ce, "Ni ne wannan mutum."
10 Suka ce masa, "To yaya aka bude maka idanu?"
11 Sai ya amsa, "Mutumin da ake ce da shi Yesu shi
ya kwaba kasa ya shafa mani a idanuna ya ce mani,
'je ka kogin Siluwam ka wanke.' Sai naje na wanke,
sannan na samu gani." 12 Suka ce masa, "Ina yake?"
Ya amsa, "Ban sani ba." 13 Suka kawo mutumnin da

yake makaho a da wurin farisawa. 14 A ranar asabar
ne kwa Yesu ya kwaba kasa ya bude masa idanu. 15
Har yanzu farisawan suka tambaye shi yadda ya sami
ganin gari. Ya ce masu, “Ya sa mani kasa a idanuna, na
wanke, kuma yanzu ina gani.” 16 Wadansu daga cikin
farisawa suka ce, “Wannan mutum ba daga Allah yake
ba domin ba ya kiyaye ranar Asabar. “Wadansu suka
ce, “Yaya mai zunubi zai yi irin wadannan alamu?”
Sai rabuwa ta shiga tsakanin su. 17 Sai suka tambayi
makahon kuma, “Me kake cewa game da shi dashike
ya bude maka idanu?” Makahon ya ce, “shi annabi
ne.” 18 Har yanzu kam Yahudawan basu yarda da
makantarsa ba da da ganin gari da ya samu, sai da suka
kirayo iyayen shi wanda ya sami ganin garin. 19 Su
ka tambayi iyayen, “Wannan shine yaronku da kuka
ce an haife shi makaho? Yaya yanzu ya ke iya gani?”
20 Sai iyayen suka amsa masu, “Mun san wannan
yaronmu ne kuma a makaho aka haife shi. 21 Yadda
ya ke gani yanzu, bamu sani ba, kuma wanda ya
bude masa idanu, bamu sani ba. Ku tambaye shi, ba
yaro ba ne. Zai iya magana don kansa.” 22 Iyayensa
sun fadi wadannan abubuwan, domin suna ji tsoron
Yahudawan. Gama Yahudiyawan sun rigaya sun yarda
duk wanda yace Yesu Almasihu ne, za a fitar dashi
daga majami'a. 23 Domin wannan ne, iyayensa suka
ce, “Ai shi ba yaro ba ne, ku tambaye shi.” 24 Suka sake
kiran mutumin dake makaho karo na biyu, suka ce
masa, “Ka girmama Allah. Mu kam mun sani wannan
mutum mai zunubi ne.” 25 Sai wannan mutum ya
amsa, “Ban sani ba ko shi mai zunubi ne. Abu guda
daya na sani: da Ni makaho ne, amma yanzu ina gani.”
26 Sai su ka ce masa, “Me ya yi maka? Ta yaya ya bude
idanunka?” 27 Ya amsa, “Na rigaya na gaya maku,
amma ba ku ji ba! Don me kuke so ku sake ji? Ko kuma
kuna so ku zama almajiransa, haka ne? 28 Sai suka
kwabe shi suka ce, “kai ne almajirinsa, amma mu
almajiran Musa ne. 29 Mun sani Allah ya yi magana
da Musa, amma wannan mutum, bamu san ko daga
ina ne ya zo ba.” 30 Mutumin ya amsa masu ya ce,
“Tirkashi, baku san inda ya fito ba, duk da haka shi
ya bude mani idanu. 31 Mun san da cewa Allah baya
jin masu zunubi, amma idan wani mai ibada ne yana
kuma yin nufinsa, to yana jin sa. 32 Tunda duniya ta
fara ba a taba jin cewa wani ya bude idanun wanda
aka haifa makaho ba. (aiōn g165) 33 In mutumin nan ba
daga Allah yake ba, ba zai iya yin komai ba.” 34 Suka
amsa suka ce masa, “an haife ka cikin zunubai, yanzu
kana so ka yi mana koyarwa?” Sai suka fitar da shi. 35
Yesu ya ji cewa sun fitar da shi daga majami'a. Da
ya same shi sai ya ce masa, “Kana bada gaskiya ga
Dan Allah?” 36 Sai ya amsa masa yace, “Wanene shi,
Ubangiji, da zan bada gaskiya gare shi?” 37 Yesu yace
masa, “Ai ka gan shi, shine wanda yake magana da
kai.” 38 Mutumin ya ce, “Ubangiji, Na bada gaskiya.”
Sai ya yi masa sujada. 39 Yesu ya ce, “Don hukunci na
zo wannan duniya domin wadanda ba su gani su gani,
saboda kuma wadanda suke gani su zama makafi.”
40 Wadansu Farisawa wadanda suke tare da shi suka
ji wadannan abubuwan, suka tambaye shi, “Muma
makafi ne?” 41 Yesu ya ce masu, “Inda ku makafi ne,
da ba ku da zunubi, amma yanzu kun ce, 'Muna gani',
don haka zunubinku ya tabbata.

10 “Hakika, Hakika, ina ce maku, wanda bai shiga ta
kofa zuwa garken tumaki ba, amma ya haura ta
wata hanya, wannan mutum barawo ne da dan fashi.
2 Wanda ya shiga ta kofa shine makiyayin tumakin.
3 Mai gadin kofar zai bude masa. Tumakin suna jin
muryarsa, ya na kuma kiran tumakinsa da sunayensu,
ya kuma kai su waje. 4 Bayanda ya kawo su duka a
waje, yana tafiya a gabansu, sai tumakin su bi shi,
domin sun san muryarsa. 5 Ba za su bi bako ba amma
sai dai su guje shi, domin basu san muryar baki ba.” 6
Yesu ya yi masu magana da wannan misali, amma
basu gane wadannan abubuwa da yake gaya masu ba.
7 Sai Yesu ya ce masu kuma, “Hakika, Hakika, Ina ce
maku, Ni ne kofar tumaki. 8 Dukan wadanda suka zo
kamin ni barayi ne da yan fashi, amma tumakin ba su
ji su ba. 9 Ni ne kofa, In kowa ya shiga ta wurina, zai
sami ceto, zai shiga ya fita ya kuma sami wurin kiwo.
10 Barawo ba ya zuwa sai don ya yi sata, ya kashe,
ya kuma hallakar. Na zo ne domin su sami rai su
kuma same shi a yalwace. 11 Ni ne makiyayi mai kyau.
Makiyayi mai kyau yana bada ransa domin tumakinsa.
12 Wanda yake dan sako kuma, ba makiyayi ba, wanda
ba shine mai tumakin ba, in ya ga kyarkeci na zuwa
sai ya saki tumakin ya gudu. Sai kyarkecin ya dauke
su ya kuma warwatsa su. 13 Ya gudu domin shi mai
aikin kudi ne kuma bai damu da tumakin ba. 14 Nine
makiyayi mai kyau, na kuma san nawa, nawa kuma
sun san ni. 15 Uban ya san ni, ni ma na san Uban, na
kuma bada raina domin tumakin. 16 Ina da wadansu
tumaki wadanda ba na wannan garken ba. Wadannan,
kuma, dole in kawo su, su ma za su ji muryata saboda

za su zama garke daya da makiyayi daya. 17 Domin
wannan ne Uban yake kauna ta: Na bada raina domin
in same shi kuma. 18 Babu wanda zai dauke shi daga
wurina, amma ina bayar da shi da kaina. Ina da ikon
bada shi, ina da iko in dauke shi kuma. Na karbi
wannan umarnin daga wurin Ubana." 19 Tsattsaguwa
ta sake tashi tsakanin Yahudawa domin wadannan
kalmomin. 20 Dayawa a cikinsu suka ce, yana da aljani,
kuma mahaukaci ne. Don me ku ke sauraronsa?" 21
Wadansu suka ce, wadannan ba kalmomin wanda
yake da aljani ba ne. Ko mai aljani zai iya bude
idanun makaho?" 22 Sai lokacin idin Tsarkakewa a
Urushalima ya zo. 23 A lokacin damuna ne, Yesu kuwa
yana tafiya a shirayi cikin haikalin Sulaimanu. 24 Sai
Yahudawa suka zagaye shi suka ce masa, "Har yaushe
ne za ka bar mu cikin shakka? In kai ne Almasihun, ka
gaya mana dalla-dalla." 25 Yesu ya ce masu, "Na gaya
maku, amma baku gaskata ba. Ayyukan da nake yi a
cikin sunan Ubana, su ke yin shaida a kaina. 26 Duk da
haka baku gaskata ba domin ku ba tumakina ba ne. 27
Tumakina suna jin murya ta; Na san su, suna kuma
bi na. 28 Ina ba su rai na har abada; ba za su taba
mutuwa ba, babu wanda zai kwace su daga hannu na.
(aiōn g165, aiōnios g166) 29 Ubana, wanda ya bani su, ya fi
kowa girma, kuma ba mai iya kwace su daga hannun
Uban. 30 Ni da Uban daya ne." 31 Sai Yahudawa suka
dauki duwatsu kuma domin su jajjefe shi. 32 Yesu
ya amsa masu, "Na nuna maku kyawawan ayyuka
masu yawa daga wurin Uban. Saboda wane daga cikin
wadannan ayyukan kuke jefe ni?" 33 Sai Yahudawa
suka amsa masa, "ba don wani aiki mai kyau muke
son mu jefe ka ba, amma don sabo, domin kai, mutum
ne, amma kana mayar da kanka Allah." 34 Yesu ya
amsa masu, "Ba a rubuce yake a shari'arku ba, 'Na ce,
"ku alloli ne"'?" 35 In ya kira su alloli, su wadanda
maganar Allah ta zo gare su (kuma ba za a iya karya
nassi ba), 36 kuna gaya wa wanda Uban ya kebe ya
kuma aiko cikin duniya, 'Kana sabo', domin Na ce,
'Ni dan Allah ne'? 37 In ba na aikin Ubana, kada ku
gaskata ni. 38 Amma, idan ina yin su, ko ba ku gaskata
da ni ba, ku gaskata da ayyukan saboda ku sani, ku
kuma gane cewa Uban yana ciki na, ni kuma ina cikin
Uban." 39 Suka sake kokarin kama shi, amma ya yi
tafiyarsa, ya fita daga hannunsu. 40 Ya yi tafiyarsa
kuma har gaba da kogin Urdun zuwa inda Yahaya ke
yin baftisma ada, ya kuma zauna a wurin. 41 Mutane
masu yawa suka zo wurinsa, suka ce,"Hakika Yahaya
bai yi wasu alamu ba, amma dukan abubuwan da
Yahaya ya ce game da wannan mutum gaskiya ne." 42
Mutane dayawa suka bada gaskiya gare shi a wurin.

11 To wani mutum mai suna Li'azaru, yayi rashin
lafiya. Shi mutumin Baitanya ne, wato kauyen
su Maryamu da 'yar'uwarta Matta. 2 Wato wannan
Maryamu da ta shafe Ubangiji da mur ta kuma share
masa kafafunsa da gashin kanta, wadda dan'uwanta
Li'azaru ke rashin lafiya. 3 'Yan'uwannan mata suka
aika sako wurin yesu, cewa, "Ubangiji, duba, shi
wanda kake kauna yana rashin lafiya". 4 Da Yesu ya
ji, sai ya ce "Wannan ciwo ba zai kai ga mutuwa ba,
amma domin daukakar Allah ne, domin Dan Allah ya
sami daukaka tawurin ta". 5 Yesu yana kaunar Matta,
da 'yar'uwarta da Li'azaru. 6 Da yaji cewa Li'azaru
na rashin lafiya, sai ya tsaya kwana biyu a inda ya
ke. 7 Bayan haka, sai ya ce wa almajiransa, "Bari mu
je Yahudiya kuma." 8 Sai almajiransa suka ce masa,
"Mallam, harwayau Yahudaya na neman ka domin su
jefe ka da duwatsu, kuma kana son komawa can?"
9 Yesu ya amsa, "Ba sa'a goma sha biyu ce ta haske
a rana guda ba? Idan mutum ya yi tafiya da rana,
ba za ya yi tuntube ba, domin yana gani ta wurin
hasken wannan duniya. 10 Amma idan mutum ya yi
tafiya chikin dare, za ya yi tuntube domin haske ba
ya tare da shi. 11 Ya fadi wadannan al'amura, kuma
bayan wadannan abubuwa, sai ya ce masu, "Abokinmu
Li'azaru ya yi barci, amma zan je don In tashe shi
daga barci". 12 Sai almajirai suka ce masa, "Ubangiji,
idan barci yake yi, ai za ya farka." 13 Yesu kuwa
ya yi maganar mutuwar Li'azaru ne, amma su suna
tsammani yana magana akan barci ne na hutu. 14 Sai
Yesu ya yi masu bayani cewa, "Li'azaru ya mutu. 15
Ina farinchiki domin ku, da bani a wurin domin ku
gaskata. Bari mu je wurinsa." 16 Toma wanda ake kira
Dan tagwaye, ya ce wa sauran almajirai, "Bari mu tafi
domin mu mutu tare da Yesu." 17 Da Yesu ya iso, sai
ya tarar cewa Li'azaru ya rigaya ya yi kwana hudu a
kabari. 18 Baitanya kuma tana kusa da Urushalima,
'yar tafiya marar nisa ce a tsakanin su. 19 Yahudawa
dayawa sun zo wurin Maryamu da Matta domin su yi
masu ta'aziyar mutuwar dan'uwansu. 20 Da Matta ta
ji cewa Yesu na zuwa, sai ta tafi domin ta same shi,
amma Maryamu na zamne a cikin gida. 21 Matta ta
ce wa Yesu, "Ubangiji, da kana nan tare da mu, da
dan'uwana baya mutu ba". 22 Ko yanzu na san cewa

duk abinda ka roka a wurin Allah, za ya ba ka. 23 Yesu
ya ce mata, “Dan'uwanki za ya rayu kuma. 24 Sai Matta
ta ce masa, “Na san zaya rayu kuma a tashin mattatu
na ranar karshe.” 25 Yesu ya ce mata, “Ni ne tashin
matattu, ni ne kuma rai; wanda ya bada gaskiya gare
ni, ko ya mutu, za ya rayu; 26 Kuma duk wanda yake
raye, ya kuma bada gaskiya gare ni, ba zai mutu ba
dadai. Kin gaskata da wannan?” (aiōn g165) 27 Sai ta ce
masa, “I, Ubangiji, Na gaskata cewa kaine Almasihu,
Dan Allah, wanda ke zuwa duniya. 28 Sa'adda ta fadi
haka, sai ta koma ta kira yar'uwarta Maryamu gefe
guda. Ta ce, “mallam ya iso, kuma yana kiran ki.” 29
Da ta ji haka, sai ta tashi da sauri ta tafi wurin sa. 30
Yesu bai rigaya ya shiga kauyen ba, yana nan inda
Matta ta zo ta same shi. 31 Da Yahudawan nan dake
tare da Maryamu, wato wadannan da suka zo mata
ta'aziya, suka ga ta fita daga chikin gida da sauri, sai
suka bi ta, suna tsammanin cewa ta tafi ta yi kuka ne
a kabari. 32 Da Maryamu ta kai inda Yesu ya ke, sai ta
fadi gaban sawayensa, ta ce, “Ubangiji, inda kana tare
da mu, da dan'uwana bai mutu ba”. 33 Da Yesu ya gan
ta tana kuka, da wadannan Yahudawa da suka bi ta,
sai ya yi juyayi a ruhu ya damu kuma; 34 sai ya ce, “A
ina kuka kwantar da shi?” Sai suka ce masa, “Ubangiji,
zo ka gani.” 35 Yesu ya yi kuka. 36 Sai Yahudawa
suka ce, “Dubi yadda yake kaunar Li'azaru!” 37 Amma
wadansun su suka ce, “Shi wannan mutum da ya iya
ba makaho ganin gari, da bai iya hana wannan mutum
mutuwa ba? 38 Yesu yana cikin juyayi kuma a cikin
kansa, sai ya tafi kabarin. Kabarin a kogo ne an kuma
rufe bakinsa da dutse. 39 Sai Yesu ya ce, “A kawar da
dutsen.” Matta yar'uwar Li'azaru wanda ya mutu, ta ce
wa Yesu, “Ubangiji, Yanzu jikin ya ruba domin ya kai
kwana hudu da mutuwa”. 40 Yesu ya ce mata, “Ba na
ce maki idan kin gaskata za ki ga daukakar Allah ba?”
41 Sai suka kawar da dutsen. Yesu ya daga idanunsa
ya ce, “Uba, na gode maka domin kana ji na.” 42 Na
san kana ji na a kowane lokaci, amma domin wannan
taro da ke tsaye kewaye da ni nike wannan magana,
domin su bada gaskiya cewa kaine ka aiko ni.” 43
Bayan ya yi wannan magana, sai ya daga murya ya ce,
“Li'azaru, ka fito!” 44 Sai mataccen ya fito; kafafunsa
da hannayensa na daure da likkafani, fuskarsa kuma
na lullube da tsumma. Yesu ya ce masu, “Ku kwance
shi, ya tafi”. 45 To dayawa daga cikin yahudawan da
suka zo wurin Maryamu suka kuma ga abinda Yesu
ya yi, suka gaskata da shi; 46 amma wadansu suka
koma wurin farisawa suka fada masu abubuwan da
Yesu ya yi. 47 Sai manyan firistoci da farisawa suka
tara majalisa wuri guda, suka ce, “menene za mu yi?”
Mutumin nan yana alamu masu yawa. 48 Idan mun
kyale shi haka, duka za su gaskata da shi; Romawa za
su zo su kwace wurinmu da al'ummar mu. 49 Duk da
haka, wani daga cikin su wato, Kayafas wanda shine
babban firist a wannan shekara, ya ce da su, “baku
san komai ba”. 50 Ba ku lura cewa ya fi maku kyau
mutum daya ya mutu domin mutane, a maimakon
dukan al'umma ta hallaka.” 51 Ya fadi wannan ne ba
don kansa ba, amma sabo da shine babban firist, ya
yi anabci ne cewa ya kamata Yesu ya mutu domin
al'ummar; 52 kuma ba don alummar kawai ba, amma
domin a tattara 'ya'yan Allah da suke warwatse ko'ina
wuri daya. 53 Tun daga wannan rana suka fara neman
hanyar da za su kashe Yesu. 54 Tun daga nan Yesu ya
dena tafiya a sarari chikin Yahudawa, amma sai ya
koma wani yanki kusa da jeji a wani gari da ake kira
Ifraimu. A can kuma ya zamna da almajiransa. 55 Idin
ketarewa na Yahudawa ya yi kusa, da yawa sun tafi
Urushalima daga yankin kasar kamin ranar idi domin
su tsarkake kan su. 56 Suka shiga neman Yesu, suna
magana da junan su yayin da suke tsaitsaye a haikali,
cewa “me kuke tunani? Ba za ya zo idin bane?” 57
Babban firist da farisawa sun rigaya sun ba da umurni
cewa duk inda aka ga Yesu a zo a shaida domin su
kama shi.

12 Kwana shidda kafin idin ketarewa, Yesu ya zo
Baitanya inda Li'azaru yake, wato wannan da
Yesu ya tada daga matattu. 2 Sai suka shirya masa
abinci a wurin kuma Matta ce ke hidima, Li'azaru
kuwa ya kasance cikin wadanda ke kan tebiri tare da
Yesu. 3 Sai Maryamu ta dauki wani turare da aka yi
da man nard, ta shafe kafafun Yesu da shi, ta kuma
share kafafun nasa da gashin kanta. Sai gida ya cika
da kamshin turaren. 4 Yahuza Iskariyoti, daya daga
cikin almajiransa, wanda zai bashe shi, ya ce, “ 5
“Me yasa ba a sayar da wannan turare dinari dari
uku a ba gajiyayyu ba?” 6 Ya fadi haka ba don ya
damu da gajiyayyu ba, amma domin shi barawo ne:
shi ne ma'aji, kuma yana sata daga jakkar kudi. 7 Yesu
ya ce, “Ku kyale ta ta ajiye abinda ta tanada domin
jana'iza ta. 8 Gajiyayyu suna tare da ku a koyaushe,
ni kuwa ba zan kasance da ku koyaushe ba. 9 To
babban taron Yahudawa sun ji cewa Yesu yana wurin,
sai suka zo, ba don Yesu kawai ba amma domin su

ga Li'azaru, wanda Yesu ya tada daga matattu. 10
Sai manyan firistoci suka kulla makirci akan yadda
za su kashe Li'azaru shima; 11 domin saboda shi ne
yahudawa dayawa suka je suka bada gaskiya ga Yesu.
12 Kashegari, babban taro suka zo idin. Da suka ji
cewa Yesu na zuwa Urushalima, 13 Sai suka dauki
ganyen dabino suka fita gari suka tare shi da kira mai
karfi suna cewa, “Hosanna! Mai albarka ne wanda
yake zuwa cikin sunan Ubangiji, Sarkin Isra'ila. 14
Yesu ya sami wani Aholakin jaki, ya hau kansa; kamar
yadda aka rubuta, 15 “Kada ki ji tsoro ke 'yar Sihiyona;
duba, ga Sarkinki na zuwa, zaune a kan danJaki”.
16 Almajiransa basu fahimci wannan al'amari ba da
farko, amma bayan da aka daukaka Yesu, sai suka
tuna cewa an rubuta wadannan abubuwa game da shi,
kuma sun yi masa wadannan abubuwa. 17 Sai taron da
ke tare da Yesu a ranar da ya kira Li'azaru daga kabari
ya kuma tashe shi daga matattu, suka bada shaida. 18
Domin wannan ne kuma taron suka zo domin su sadu
da shi saboda sun ji cewa ya yi wannan alama. 19 Don
haka, sai farisawa suka shiga magana a tsakanin su
suna cewa “Duba, babu abinda zaku iya yi; kun ga,
duniya ta gama bin sa. 20 Akwai wadansu Helinawa
cikin wadanda suka je sujada a idin. 21 Wadannan
suka tafi wurin filibus, mutumin Betsaida da ke Galili,
suka ce masa, “Mallam, muna so mu ga Yesu. 22
Filibus ya tafi ya fadawa Andrawus; sai Andrawus
ya tafi tare da Filibus, suka kuwa gaya wa Yesu. 23
Yesu ya amsa masu ya ce, “sa'a ta zo da za'a daukaka
Dan mutum. 24 Hakika, hakika, Ina ce maku, in ba
kwayar alkama ta fadi kasa ba ta mutu, za ta kasance
ita kadai; amma idan ta mutu, za ta bada 'ya'ya masu
yawa. 25 Duk wanda yake son ransa, zai rasa shi;
amma wanda ba ya son ransa a duniyan nan za ya
kiyaye shi domin rayuwa ta har abada. **(aiōnios g166)** 26
Idan wani na bauta mani, to bari ya biyo ni; kuma duk
inda nike, a can bawana zai kasance kuma. Duk wanda
ke bauta mani, Uban zai girmama shi. 27 Yanzu raina
na cikin damuwa, to me zan ce? 'Uba, ka cece ni daga
wannan sa'a? Amma Saboda wannan dalili ne na zo
wannan sa'a. 28 Uba, ka daukaka sunanka”. Sai wata
murya daga sama ta ce, “Na daukaka shi, zan kuma
sake daukaka shi. 29 Daganan sai taron dake tsaye
kuma suka ji muryar, suka ce an yi tsawa. Wasu suka
ce, “Mala'ika ya yi magana da shi”. 30 Yesu ya amsa
ya ce, “wannnan murya ta zo ba saboda ni ba, amma
domin ku.” 31 Yanzu za'a shar'anta duniya. Yanzu
za'a kori mai mulkin duniyan nan. 32 Sa, annan ni,
idan an daga ni daga duniya, zan jawo dukan mutane
zuwa gare ni”. 33 Ya fadi wannan ne domin ya nuna
irin mutuwar da za ya yi. 34 Taro suka amsa masa
cewa, “Mun ji a cikin shari'a cewa Almasihu za ya
kasance har abada. Yaya za ka ce, 'za'a daga dan
mutum'? Wanene wannan dan mutum?” **(aiōn g165)** 35
Yesu ya ce masu, “Nan da lokaci kadan za ku kasance
da haske, ku yi tafiya tun haske na tare da ku, kada
duhu ya mamaye ku. Wanda ke tafiya cikin duhu, bai
san inda za shi ba. 36 Ku gaskata ga haske tun yana
tare da ku domin ku zama yayan haske”. Yesu ya fadi
wadannan abubuwa sannan ya tafi ya boye masu.
37 Kodashike Yesu ya yi alamu da dama a gabansu,
duk da haka ba su gaskata shi ba. 38 Saboda maganar
annabi Ishaya ta cika, wadda ya ce, “Ubangiji, wa ya
gaskata rahoton mu? Ga wa kuma hannun Ubangiji
ya bayyana? 39 Saboda wannan dalili basu gaskata
ba, gama Ishaya ya sake cewa, 40 ya makantar da su,
ya kuma taurare zuciyarsu, saboda kada su gani da
idanunsu, su kuma sami fahimta da zuciyarsu, su juyo
wurina in warkar da su. 41 Ishaya ya fadi wadannan
abubuwa ne domin ya hangi daukakar Yesu ya kuma
yi magana game da shi. 42 Amma duk da haka, dayawa
cikin shugabanni suka gaskata Yesu. Amma saboda
farisawa, basu shaida shi a sarari ba, domin kada a
kore su daga majami'a. 43 Suna son yabo daga mutane
fiye da yabon dake zuwa daga Allah. 44 Yesu ya yi
magana da babbar murya, ya ce, “Wanda ya gaskata
ni, ba ni yake gaskatawa kadai ba, amma kuma yana
gaskata wanda ya aiko ni, 45 kuma wanda ke gani
na, yana ganin shi wanda ya aiko ni. 46 Na zo ne
a matsayin haske a duniya, saboda duk wanda ya
gaskata da ni ba za ya yi tafiya cikin duhu ba. 47 Duk
wanda ya ji maganata baya gaskata ba, ba ni hukunta
shi; gama ban zo in yi wa duniya hukunci ba, amma
don in ceci duniya. 48 Wanda ya ki ni, ya kuma ki ya
karbi magana ta, akwai wanda za ya yi masa hukunci.
Kalmar da na fada, ita ce za ta yi masa hukunci a
rana ta karshe. 49 Maganar da ni ke yi, ba ra'ayina ba
ne. Amma Uba wanda ya aiko ni shi ke bani umarni
game da abin da zan ce da abin da zan fadi. 50 Na
san umarninsa rai ne madawwami, don haka na ce
- kamar yadda Uba ya fada, haka ni ma nake fadi.”
**(aiōnios g166)**

**13** Kamin bukin idin ketarewa, sa'adda Yesu ya san
lokaci ya yi da zai tashi daga wannan duniya
zuwa wurin Uba, da yake ya kaunaci nasa wadanda ke
duniya- ya kaunace su har karshe. 2 Iblis ya rigaya ya
sa a zuciyar Yahuza Iskariyoti dan Saminu, ya bashe
da Yesu. 3 Ya san cewa Uba ya bada kome a hannunsa,
kuma ya zo daga wurin Allah, kuma zai koma wurin
Allah. 4 Ya tashi daga cin abincin, ya tube tufafinsa,
ya dauki tawul ya lullube kansa da shi. 5 Sa'an nan ya
zuba ruwa a bangaji, ya fara wanke kafafun almajiran,
yana shafe su da tawul din da ya lullube jikinsa da
shi. 6 Ya zo wurin Bitrus Saminu, sai Bitrus ya ce
masa,"Ubangiji, za ka wanke mani kafa?" 7 Yesu ya
amsa ya ce, "Abin da nake yi ba za ka fahimce shi
yanzu ba, amma daga baya za ka fahimta." 8 Bitrus ya
ce masa, "Ba za ka taba wanke mani kafa ba." Yesu ya
amsa masa ya ce, "In ban wanke maka ba, ba ka da
rabo da ni". (aiōn g165) 9 Bitrus ya ce masa, "Ubangiji, ba
kafafuna kadai za ka wanke ba, amma da hannayena
da kaina." 10 Yesu ya ce masa, "Duk wanda ya yi
wanka ba ya da bukata, sai dai a wanke kafafunsa,
amma shi tsarkakakke ne baidaya; ku tsarkakakku ne,
amma ba dukanku ba." 11 (Don Yesu ya san wanda
zai bashe shi, shiyasa ya ce, "Ba dukanku ne ke da
tsarki ba.") 12 Bayan Yesu ya wanke masu kafafu, ya
dauki tufafinsa ya zauna kuma, ya ce masu, "Kun
san abin da na yi muku? 13 kuna kirana, 'Malam, da
Ubangiji,' kun fadi daidai, don haka Nake. 14 Idan ni
Ubangiji da kuma mallam, na wanke maku kafafu, ya
kamata kuma ku wanke wa junan ku kafafu. 15 Gama
na baku misali, saboda ku yi yadda na yi maku. 16
Lalle hakika ina gaya muku, bawa ba ya fi mai gidansa
girma ba; dan aike kuma ba ya fi wanda ya aiko shi
girma ba. 17 Idan kun san wadannan abubuwa, ku
masu albarka ne idan kun aikata su. 18 Ba ina magana
akan dukanku ba; Na san wadanda na zaba. Amma
domin Nassi ya cika: 'Shi Wanda ya ci gurasata, ya
tayar mani'. 19 Ina fada maku wannan yanzu tun kafin
haka ta faru domin sa'adda ta faru, ku gaskata Ni
ne. 20 Hakika, hakika, Ina gaya maku, wanda ya karbi
wanda na aiko, Ni ya karba, wanda kuma ya karbe ni,
ya karbi wanda ya aiko ni. 21 Bayan Yesu ya fadi haka,
ya damu a ruhu, ya yi shaida ya ce, "Lalle hakika, ina
gaya muku cewa daya daga cikinku zai bashe ni." 22
Almajiran suka kalli juna, suna juyayin ko akan wa
yake magana. 23 Daya daga cikin almajiransa, wanda
Yesu yake kauna, yana a teburi, jingine a kirjin Yesu.
24 Siman Bitrus ya ce wa almajirin, "ka fada mana ko
akan wa ya ke magana." 25 Sai ya sake jingina a kirjin
Yesu, ya ce masa, "Ubangiji, wanene?" 26 Sannan Yesu
ya amsa, "Shine wanda zan tsoma gutsuren gurasa
in ba shi." Sannan bayan ya tsoma gurasar, sai ya ba
Yahuza Dan Siman Iskariyoti. 27 To bayan gurasar, sai
shaidan ya shige shi, sai Yesu ya ce masa, "Abinda
kake yi, ka yi shi da sauri." 28 Babu wani a teburin
da ya san dalilin dayasa ya fada masa wannan. 29
Wadansu sun yi tsamanin cewa, tun da Yahuza ne ke
rike da jakkar kudi, Yesu ya ce masa, "Ka sayi abinda
muke bukata don idin", ko kuma ya bada wani abu
domin gajiyayyu. 30 Bayan Yahuza ya karbi gurasar,
sai ya fita nan da nan. Da daddare ne kuwa. 31 Bayan
Yahuza ya tafi, Yesu ya ce, "Yanzu an daukaka Dan
mutum, kuma an daukaka Allah a cikinsa. 32 Allah
zai daukaka shi a cikin kansa, kuma zai daukaka shi
nan da nan. 33 'Ya'ya kanana, ina tare da ku na wani
gajeren lokaci. Zaku neme ni, kuma kamar yadda
na fadawa Yahudawa, 'in da zan tafi ba za ku iya
zuwa ba.' Yanzu kuma na fada maku wannan. 34 Ina
baku sabuwar doka, ku kaunaci juna; kamar yadda na
kaunace ku, haka kuma ku kaunaci juna. 35 Ta haka
kowa zai san ku almajiraina ne, idan kuna kaunar
juna." 36 Siman Bitrus ya ce masa, "Ubangiji, ina za
ka?" Yesu ya amsa ya ce, "Inda za ni, ba zaka iya bi na
ba yanzu, amma zaka bini daga baya." 37 Bitrus ya ce
masa, "Ubangiji, don me ba zan iya binka a yanzu ba?
Zan bada raina domin ka." 38 Yesu ya amsa ya ce, "Za
ka bada ranka domina? Lalle hakika, ina gaya maka,
kafin zakara ya yi cara zaka yi musu na sau uku."

**14** "Kada zuciyarku ta bachi. Kun gaskata da Allah,
sai kuma ku gaskata da ni. 2 A gidan Ubana akwai
wurin zama dayawa. Da ba haka ba, da na fada maku,
domin zan tafi in shirya maku wuri. 3 In kuwa na je na
shirya maku wuri, zan dawo in karbe ku zuwa wurina
domin inda nake kuma ku kasance. 4 Kun san hanya
inda zan tafi." 5 Toma ya ce wa Yesu, "Ubangiji, bamu
san inda za ka tafi ba, yaya za mu san hanyar?" 6 Yesu
ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne rai; Ba
mai zuwa wurin Uba sai ta wurina. 7 Da kun san ni, da
kun san Ubana kuma. Amma daga yanzu kun san shi,
kuma kun gan shi." 8 Filibus ya ce wa Yesu, "Ubangiji,
ka nuna mana Uban, wannan za ya ishe mu." 9 Yesu
ya ce masa, "Ina tare da ku da dadewa, amma har
yanzu baka san ni ba, Filibus? Duk wanda ya gan ni,

ya ga Uban. Yaya za ka ce, 'Nuna mana Uban'? 10 Baka
gaskata cewa Ina cikin Uban, Uban kuma yana ciki
na ba? Maganganun da nake fada maku, ba da ikona
nake fadi ba, amma Uban ne da yake zaune a ciki na
yake yin ayyukansa. 11 Ku gaskata ni cewa ina cikin
Uban, Uban kuma na ciki na, ko kuwa ku bada gaskiya
domin ayyukan kansu. 12 “Lalle hakika, ina gaya
maku, duk wanda ya gaskata ni zai yi ayyukan da nake
yi, kuma zai yi ayyuka fiye da wadannan, domin zan
tafi wurin Uba. 13 Duk abinda kuka roka da sunana,
zan yi shi domin a daukaka Uban cikin Dan. 14 Idan
kuka roke ni komai cikin sunana, zan yi shi. 15 “Idan
kuna kaunata, za ku kiyaye dokokina. 16 Sa, annan
zan yi addu'a ga Uba, zai kuwa baku wani mai ta'aziya
domin ya kasance tare daku har abada. (aiōn g165) 17
Ruhun gaskiya. Wanda duniya ba zata iya karba ba,
domin bata gan shi ba, ko ta san shi. Amma ku kun
san shi, domin yana tare da ku, zai kuma kasance a
cikin ku. 18 Ba zan barku ku kadai ba; zan dawo wurin
ku. 19 Sauran dan gajeren lokaci, duniya kuma ba zata
ka ra gani na ba, amma ku kuna gani na. Saboda ina
raye, kuma zaku rayu. 20 A wannan rana zaku sani
ina cikin Ubana, ku kuma kuna ciki na, ni ma ina
cikin ku. 21 Shi wanda yake da dokokina yake kuma
bin su, shine ke kauna ta, kuma shi wanda ke kauna
ta Ubana zai kaunace shi, Ni ma kuma zan kaunace
shi in kuma bayyana kaina gare shi.” 22 Yahuza (ba
Iskariyoti ba) ya ce ma Yesu, “Ubangiji, meyasa za
ka bayyana kanka a gare mu, ba ga duniya ba?” 23
Yesu ya amsa ya ce masa,”Kowa yake kauna ta, zai
kiyaye maganata. Ubana kuwa zai kaunace shi, za mu
zo wurinsa mu zauna tare da shi. 24 Shi wanda baya
kauna ta, ba ya kiyaye maganganuna. Maganar da
kuke ji ba daga gareni take ba, amma daga Uba wanda
ya aiko ni take. 25 Na fada maku wadannan abubuwa,
sa'adda nake tare da ku. 26 Saidai, mai ta'aziyar- Ruhu
Mai Tsarki wanda Uba zai aiko cikin sunana, zai koya
maku kome, kuma zai tunashe ku dukan abinda na
fada maku. 27 Na bar ku da salama; ina ba ku salamata.
Ba kamar yadda duniya ke bayarwa Nake bayarwa ba.
Kada zuciyarku ta baci, kuma kada ku tsorata. 28 Kun
ji dai na fada maku, 'zan tafi, kuma Zan dawo gare
ku'. Idan kuna kaunata, za ku yi farinciki domin za
ni wurin Uban, gama Uban ya fi ni girma. 29 Yanzu
na fada maku kafin ya faru, domin idan ya faru, ku
gaskata. 30 Ba zan kara magana mai yawa da ku ba,
domin mai mulkin duniyan nan yana zuwa. Bashi da
iko a kai na, 31 amma domin duniya ta san cewa ina
kaunar Uban, Ina yin daidai abinda Uban ya Umarce
ni. Mu tashi mu tafi daga nan.

15 “Nine itacen inabi na hakika, Ubana kuwa shi
ne manomin. 2 Yakan cire duk wani rashe a
cikina da ba ya bada 'ya'ya, mai bada 'ya'ya kuwa
ya kan gyara shi domin ya kara bada 'ya'ya. 3 Kun
rigaya kun tsarkaka saboda maganar da na yi muku.
4 Ku zauna ciki na, Ni kuma cikin ku. Kamar yadda
reshe ba ya iya bada 'ya'ya shi kadai sai ya zauna
cikin itacen, haka kuma ba za ku iya ba, sai kun
zauna ciki na. 5 Ni ne itacen inabi, ku ne rassan.
Wanda ya zauna ciki na, ni kuma cikin sa, yana bada
'ya'ya dayawa, gama in ba tare da ni ba, ba za ku
iya yin kome ba. 6 Wanda kuma bai zauna a ciki na
ba, akan jefar da shi kamar reshe, ya bushe, kuma
sukan tattara rassan su jefa a wuta, su kone. 7 In kun
zauna a ciki na, maganata kuma ta zauna a cikin ku,
sai ku roki duk abinda kuke so, za a kuwa yi maku.
8 Ta haka ake daukaka Ubana: cewa ku bada 'ya'ya
dayawa, kuma cewa ku almajiraina ne. 9 Kamar yadda
Ubana ya kaunace ni, haka Ni ma na kaunace ku; Ku
zauna cikin kaunata. 10 Idan kun kiyaye dokokina,
za ku zauna cikin kaunata kamar yadda Na kiyaye
dokokin Ubana, na kuma zauna cikin kaunarsa. 11
Ina gaya maku wadannan al'amura domin farincikina
ya kasance a cikin ku, kuma domin farincikinku ya
zama cikakke. 12 “Wannan shine umarnina, cewa ku
kaunaci juna kamar yadda na kaunace ku. 13 Babu
wanda ke da kaunar da tafi haka, wato ya bada ransa
domin abokansa. 14 Ku abokaina ne idan kuna yin
abubuwan da na umarce ku. 15 Nan gaba ba zan kara
ce da ku bayi ba, don bawa bai san abinda Ubangijinsa
ke yi ba. Na kira ku abokaina, domin na sanar da ku
duk abinda na ji daga wurin Ubana. 16 Ba ku kuka
zabe ni ba, amma Ni ne na zabe ku, na aike ku don ku
je ku bada 'ya'ya, 'ya'yanku kuma su tabbata. Wannan
ya zama domin duk abinda kuka roki Uba a cikin
sunana, zai baku. 17 Na baku wannan umarni: domin
ku kaunaci juna. 18 In duniya ta ki ku, ku sani cewa ta
kini kafin ta ki ku. 19 Da ku na duniya ne, da duniya
ta kaunace ku kamar nata. Amma saboda ku ba na
duniya bane, na kuma zabe ku daga duniya, don haka
duniya take kin ku. 20 Ku tuna da maganar da na yi
muku, 'Bawa ba ya fi Ubangijinsa girma ba.' Idan sun
tsananta mani, ku ma za su tsananta maku; Idan sun

kiyaye maganata, za su kuma kiyaye maganarku. 21 Za
su yi maku duk wadannan abubuwa saboda sunana,
don basu san wanda ya aiko ni ba. 22 Da ban zo na yi
masu magana ba, da basu da zunubi, amma yanzu,
basu da wata hujja don zunubinsu. 23 Duk wanda ya ki
ni ya ki Ubana. 24 Da ban yi ayyukan da babu wanda
ya taba yinsu a cikin su ba, da basu da zunubi, amma
yanzu sun gani, sun kuma ki ni da Ubana duka. 25 An
yi wannan kuwa domin a cika maganar da ke rubuce
a cikin shari'arsu, ' Sun ki ni ba dalili.' 26 Sa'adda Mai
Ta'aziya- wanda zan aiko maku daga wurin Uban,
wato, Ruhun gaskiya, wanda ke fita daga wurin Uban-
ya zo, zai bada shaida a kai na. 27 Ku ma kuna bada
shaida saboda kuna tare da ni tun daga farko.

16 "Na fada maku wannan ne domin kada kuyi
tuntube. 2 Zasu fitar da ku daga majami'u.
Amma, sa'a tana zuwa, wadda idan wani ya kasheku,
zai yi zaton aikin Allah yake yi. 3 Za suyi haka ne
kuwa domin ba su san Uban ko ni ba. 4 Na fada
maku wadannan abubuwa ne domin in lokacin da
zasu faru yayi, ku tuna na fada maku." Ban fada maku
wadannan abubuwa ba tun da farko, domin ina tare
da ku. 5 Yanzu kuwa za ni wurin wanda ya aiko ni,
duk da haka a cikinku, ba wanda ya tambaye ni, 'Ina
za ka?' 6 Amma saboda na fada maku wadannan
abubuwa, bakin ciki ya cika zuciyarku. 7 Amma ina
gaya maku gaskiya: zai fi ye maku in na tafi. Domin
in ban tafi ba, Mai Ta'aziyya ba zai zo gare ku ba, in
kuwa na tafi, zan aiko shi gare ku. 8 Idan kuwa ya zo,
Mai Ta'aziyyar zai fadarkar da duniya a kan zunubi,
da adalci, da kuma hukunci. 9 Game da zunubi, domin
basu gaskata da ni ba, 10 Game da adalci, domin za ni
wurin Uba, kuma ba za ku sake ganina ba, 11 game
da hukunci kuma, domin an yanke wa mai mulki
duniyan nan hukunci. 12 "Akwai abubuwa da yawa da
zan gaya maku, amma ba za ku iya fahimta a yanzu
ba. 13 Saboda haka, sa'adda Ruhu na gaskiya ya zo,
zai bishe ku a cikin dukan gaskiyar, domin ba zai yi
magana don kansa ba, sai dai duk abin da ya ji, shi
zai fada, zai kuma sanar da ku al'amuran da zasu
faru. 14 Zai daukaka ni, domin zai dauko abubuwa
dake nawa ya sanar da ku. 15 Duk abinda Uba yake
da shi, nawa ne. Domin wannan ne nace zai dauko
abubuwa da yake nawa ya sanar da ku. 16 "Bayan dan
lokaci kadan, ba zaku kara ganina kuma ba. bayan
dan lokaci kadan kuma, zaku gan ni." 17 Sai wadansu
almajiransa sukace wa juna, "Me nene wannan da
yake fadi mana, 'Bayan dan lokaci kadan ba zaku gan
ni ba, bayan dan lokaci kadan kuma zaku gan ni?' da
kuma, ' zan tafi wurin Uba'?" 18 Saboda haka sukace,
"Me nene wannan da yake fada, 'Bayan dan lokaci
kadan'? Bamu san abinda yake fada mana ba." 19
Yesu kuwa ya ga suna so su tambaye shi, sai ya ce
masu, "Wato kuna tambayar juna ne abinda nake
nufi da cewa, "Bayan dan lokaci kadan ba zaku gan
ni ba, bayan dan lokaci kadan kuma zaku gan ni'?
20 Hakika, hakika, ina gaya maku, zaku yi kuka da
makoki, amma duniya za ta yi farin ciki, zaku cika da
bakin ciki, amma bakin cikinku zai koma farin ciki. 21
Mace takan ji zafi lokacin da take nakuda don lokacin
haihuwa ya zo. Amma da zarar ta haifi jinjirin nan,
ba ta kara tunawa da zafin, domin ta na fariciki an
haifi mutum a duniya. 22 To yanzu dai kuna bakin
ciki, amma zan sake ganinku, kuma ba wanda zai
iya kwace maku wannan farin ciki. 23 A rannan, ba
zaku tambaye ni komai ba. Hakika hakika, ina gaya
maku, komai kuka roki Uba a cikin sunana zai ba ku
shi. 24 Harwa yau, ba ku roki komai cikin sunana ba.
Ku roka, zaku karba, domin farin cikin ku ya zama
cikakke." 25 "Na fada maku wadannan abubuwa cikin
karin magana. Amma sa'a tana zuwa da ba zan kara
fada maku komai ba cikin karin magana, amaimakon
haka zan gaya maku komai a sarari game da Uba. 26 A
ranar nan, zaku yi roko a cikin sunana kuma bance
maku zan yi addu'a ga Uba a madadinku ba, 27 domin
Uba da kansa yana kaunarku, domin kun kaunace
ni, kun kuma gaskata daga wurin Uban na fito. 28
Daga wurin Uban na fito, kuma na shigo duniya. Har
wa yau, kuma zan bar duniya in koma wurin Uba."
29 Almajiransa sukace, duba, "Yanzu kake magana
a sarari, ba cikin karin magana ba! 30 Yanzu mun
sani ka san komai, ba sai wani ya tambaye ka ba. Ta
haka muka gaskata daga wurin Allah ka fito." 31 Yesu
ya amsa masu yace, "Ashe, yanzu kun gaskata? 32
Duba, sa'a na zuwa, I, sa'ar ta yi, da za a warwatsa
ku, kowa ya koma gidansa, kuma ku bar ni ni kadai.
Duk da haka kuwa ba ni kadai nake ba, domin Ubana
yana tare da ni. 33 Na fada maku wannan ne domin a
ciki na ku sami salama. A duniya kuna shan tsanani,
amma ku karfafa: na yi nasara da duniya,"

17 Da Yesu ya fadi wandannan abubuwa, sai ya
tada idanunsa sama ya ce, ya Uba, sa'a ta zo; ka
daukaka Danka, domin Dan shi ya daukaka ka, 2 kamar

yadda ka ba shi iko akan dukkan 'yan adam, ya ba da
rai madawwami ga duk wanda ka ba shi. (aiōnios g166) 3
Wannan ne rai madawwami: wato su san ka, Allah
makadaici na gaskiya, da shi kuma wanda ka aiko,
Yesu Almasihu. (aiōnios g166) 4 Na daukaka ka a duniya,
na gama aikin da ka ba ni in yi. 5 Yanzu, ya Uba, ka
daukaka ni tare da kai da daukaka wadda ni ke da ita
tare da kai tun kafin duniya ta kasanci. 6 Na bayyana
sunanka ga mutunen da ka ba ni acikin duniya. Na
ka suke, ka ba ni su, sun kuwa kiyaye maganarka. 7
Yanzu kuwa sun san duk iyakar abinda ka ba ni daga
gare ka yake, 8 don kuwa maganganun da ka fada
mani. Na fada masu, sun kuma karba, sun sani kuwa
hakika na fito daga gareka ne, kuma sun gaskata kai
ne ka aiko ni. 9 Ina yi masu addu'a. Ba domin duniya
ni ke yin addu'a ba, amma domin wadanda ka bani
gama na ka ne. 10 Gama dukan abinda ke nawa na
ka ne, naka kuwa nawa ne, an kuma daukaka ni a
cikinsu. 11 Ba na cikin duniya kuma, amma wadannan
mutane suna cikin duniya, ni kuwa ina zuwa wurin
ka. Ya Uba mai Tsarki, ka adanasu cikin sunanka
da ka ba ni domin su zama daya, kamar dai yadda
muke daya. 12 Lokacin da ina tare da su, na adanasu
acikin sunanka da ka ba ni. Na kiyaye su, kuma ko
daya kuwa daga cikinsu ba ya bace ba, sai dai dan
hallakar nan, domin Nassi ya cika. 13 Amma yanzu
ina zuwa wurinka, Ina fadar wadannan abubuwa tun
ina duniya, domin farin cikina ya zama cikakke a
zukatansu. 14 Na ba su maganarka, kuma duniya ta
tsane su domin su ba na duniya ba ne, kamar yadda
ni ba na duniya ba ne. 15 Ba ina roko ka dauke su daga
cikin duniya ba, amma domin ka tsare su daga mugun
nan. 16 Su ba na duniya ba ne, kamar yadda ni ba
na duniya ba ne. 17 Ka kebe su domin kanka cikin
gaskiya. maganarka gaskiya ce. 18 Kamar dai yadda
ka aiko ni cikin duniya, haka kuma na aike su cikin
duniya. 19 Na kebe kaina gareka sabili da su, domin
su ma kansu a kebe su gareka cikin gaskiya. 20 Ina
addu'a ba domin wadannan kadai ba, amma har da
wadanda zasu gaskata da ni ta wurin maganarsu, 21
Domin su zama daya dukansu, kamar yadda kai, ya
Uba, ka ke ciki na, ni kuma na ke cikin ka. Ina roko
suma su kasance a cikinmu, domin duniya ta gaskata
cewa ka aiko ni 22 Daukakar da ka bani, ita nake basu,
domin su zama daya, kamar yadda mu ke daya; 23
ni a cikinsu, kai kuma a ciki na. Domin su kammalu
cikin zama daya, domin duniya ta sani cewa ka aiko
ni, kuma ka kaunace su, kamar yadda ka kaunace ni.
24 Ya Uba, ina so wadanda ka ba ni, su ma su kasance
tare da ni inda nake, domin su dubi daukakata da
ka yi mani. Domin ka kaunace ni tun kafin halittar
duniya. 25 Ya Uba mai adalci, duniya kam, ba ta sanka
ba, amma ni na sanka; kuma wadannan sun sani kai
ne ka aiko ni. 26 Na sanar masu da sunanka, zan kuma
sanar da shi domin kaunar da ka yi mani ta kasance a
cikinsu, ni kuma in kasance a cikinsu,

18 Bayan Yesu ya fadi wadannan maganganu, ya
fita shi da almajiransa zuwa daya barayin kwarin
Kidiron, inda wani lambu ya ke, ya kuma shiga da
almajiransa. 2 Yahuza ma wanda zai bashe shi ya san
wurin, domin Yesu ya saba zuwa wurin da almajiransa.
3 Yahuza kuwa, bayan ya dauko kungiyar soja daga
manyan firistoci, da Farisawa, da 'yan majalisa, suka
zo wurin, rike da fitilu, da cociloli, da makamai. 4 Sai
Yesu, da ya san duk abinda ke faruwa da shi, yayiwo
gaba, yace masu, ''Wa kuke nema'' 5 Suka amsa masa
su ka ce, ''Yesu Banazare'' Yesu yace masu, Ni ne''
Yahuza kuma, wanda ya bashe shi, yana tsaye tare da
sojojin. 6 Sa'adda ya ce masu, ''Ni ne'', suka koma da
baya, suka fadi a kasa. 7 Ya sake tambayarsu kuma,
''Wa ku ke nema?'' su ka ce, ''Yesu Banazare.'' 8 Yesu
ya amsa, ''Ai, na gaya maku cewa, Ni ne. In kuwa
ni ku ke nema, ku bar wadannan su tafi abinsu;''
9 Wannan kuwa domin maganar daya fada ta cika,
''Daga cikin wadanda ka ba ni, ko daya bai bace mani
ba.'' 10 Saminu Bitrus kuwa, da ya ke yana da takobi,
ya zaro ya kai wa bawan babban firist sara, ya dauke
masa kunnensa na dama, sunan bawan Malkus ne. 11
Yesu ya ce wa Bitrus, ''Mai da takobin ka kubenta.
Ba zan sha kokon da Uba ya ba ni ba.'? 12 Sai sojojin
da hafsan, da 'yan majalisar Yahudawa, suka kama
Yesu, suka daure shi. 13 Da fari suka tafi da shi wurin
Hanana, don shi surukin Kayafa ne, wanda ya ke shi ne
babban firist a shekaran nan. 14 Kayafa kuma shi ne
ya ba Yahudawa shawara, cewa ya fiye masu mutum
daya ya mutu domin mutane. 15 Saminu bitrus ya bi
bayan Yesu, haka kuma wani almajirin yayi. Almajirin
nan kuwa sananne ne ga babban firist, sai ya shiga
har farfajiyar babban firist din tara da Yesu; 16 Amma
bitrus kuwa ya tsaya a bakin kofa daga waje. Sai daya
almajirin da ya ke sananne ga babban firist ya fita,
yayi magana da macen da ta ke tsaron kofar, sa'an
nan ya shigo da Bitrus. 17 Sai yarinyar mai tsaron
kofar ta ce wa Bitrus, ''kai ma ba kana cikin almajiran

mutumin nan ba?'' Yace ''bani ba.'' 18 To, barorin
da dogaran Haikali suna tsaye a wurin, sun kuwa
hura wutar gawayi, suna jin dumi, gama ana sanyi.
Bitrus ma yana tsaye tare da su yana jin dumin. 19
babban firist ya tambayi Yesu game da almajiransa da
koyarwarsa kuma. 20 Yesu ya amsa masa, Ai, na yi wa
duniya magana a bayyane. Na kuma sha koyarwa a
majami'u da Haikali in da Yahudawa duka sukan taru.
Ban fadi komai a boye ba. 21 Don me kake tambaya
ta? Ka tambayi wadanda suka saurare ni a kan abinda
na fada, ai, sun san abinda na fada. 22 Sa'adda Yesu ya
fadi wannan, wani daga cikin 'yan majalisar da ke
tsaye a wurin ya nushi Yesu, yace, ''Kana amsa wa
babban firist haka.'' 23 Yesu ya amsa masa yace, ''Idan
na fadi mugun abu to, ka bada shaida kan hakan. In
kuwa dai dai na fada, to, dan me za ka nushe ni?''
24 Sai Hanana ya aika daYesu a daure wurin Kayafa,
babban firist. 25 To Saminu Bitrus yana tsaye yana jin
dumin. Mutanen kuwa suka ce masa, ''Anya kai ma
ba cikin almajiransa ka ke ba?'' Sai yayi musu yace,
''A'a, ba na ciki.'' 26 Sai wani daga cikin bayin babban
firist, wato dan'uwan wanda Bitrus ya fillewa kunne,
yace, ''Ashe, ban gan ka tare da shi a lambun ba? 27
Bitrus ya sake yin musu, nan da nan kuwa zakara
yayi cara. 28 Daga wurin Kayafa kuma suka kai Yesu
fadar Gwamna. Da asuba ne kuwa, su kansu ba su
shiga fadar Gwamnan ba, wai don kada su kazantu
su kasa cin jibin Ketarewa. 29 Sai bilatus fa ya fita
zuwa wurinsu, yace, 'Wane zargi ku ke kawowa akan
mutumin nan?' 30 ''Sai suka amsa suka ce, ''idan da
mutumin nan bai yi mugun abu ba, me zai sa mu
yi kararsa a wurin ka'' 31 bilatus yace masu, ''Ku
tafi da shi da kan ku mana, ku hukunta shi bisa ga
shari'arku!'' Sai Yahudawa su kace masa, ''Ai, ba mu
da ikon zartar da hukuncin kisa akan kowa.'' 32 Sun
fadi Wannan ne don a cika maganar da Yesu yayi,
wadda ta kwatanta irin mutuwar da zai yi. 33 Sai
bilatus ya sake shiga cikin fadar Gwamnan, ya kira
Yesu ya ce masa, ''kai sarkin Yahudawa ne?'' 34 Yesu
ya amsa, '' wannan fadarka ce, ko kuwa wadansu ne
suka ce da ni haka a wurinka?'' 35 Bilatus ya amsa “Ni
ba Bayahude bane, ko kuwa?'' Ai, jama'arka ne da
manyan firistoci suka bashe ka gareni. ''Me ka yi?''
36 Yesu ya amsa, ''Mulkina ba na duniya nan ba ne.
Da mulkina na duniyan nan ne da barorina za su yi
yaki kada a bashe ni ga Yahudawa. To, mulkina ba
daga nan ya ke ba.'' 37 Sai Bilatus yace masa, ''Wato
ashe, sarki ne kai?'' Yesu ya amsa, ''Yadda ka fada, ni
sarki ne. Domin wannan dalili aka haife ni, domin
kuma wannan dalili na zo cikin duniya, don in bada
shaida game da gaskiya. Kowane mai kaunar gaskiya
kuma yakan saurari muryata.'' 38 Bilatus yace masa,
''Menene gaskiya?'' Bayan da ya fadi haka, ya sake
fitowa wurin Yahudawa, yace masu, ''Ni kam, ban
sami mutumin nan da wani laifi ba. 39 Amma dai kuna
da wata al'ada, in Idin Ketarewa ya yi, na kan sakar
maku mutum daya. To, kuna so in sakar maku sarkin
Yahudawa?'' 40 Sai suka sake daukar kururuwa suna
cewa, ''A; a, ba wannan mutum ba, sai dai Barabbas.''
Barabbas din nan kuwa dan fashi ne.

**19** Sai Bilatus yayi wa Yesu bulala. 2 Sojojin kuwa
suka saka rawanin kaya. Suka kuwa dora wa Yesu
a kai suka sa mashi kaya irin na saurata. 3 Suka zo
wurin sa sukace, “Ranka ya dade, sarkin Yahudawa!
sai suka nushe shi. 4 Sai Bilatus ya sake fita waje yace
masu, “Dubi, zan kawo maku mutumin domin ku sani
ban same shi da wani laifi ba”, 5 Yesu kuwa ya fito, da
rawanin kaya da kaya irin na sarauta. Sai Bilatus yace
“Ga mutumin nan”. 6 Da manyan firistocin tare da yan
majalisar suka ga Yesu, sai suka yi ta ihu suna cewa “A
gicciye shi, A gicciye shi” Sai Bilatus yace masu, “ku
dauke shi ku gicciye shi, ni kam ban same shi da wani
laifi ba”. 7 Sai Yahudawan sukace mashi, “Ai muna da
shari'a, kuma bisa ga shari'ar ya cancanci mutuwa
domin ya mai da kansa Dan Allah”. 8 Da Bilatus ya
ji wannan zance sai ya tsorata kwarai. 9 Sai ya sake
shiga fadar Gwamna, yace wa Yesu, “Daga ina ka fito?”
amma Yesu bai amsa mashi ba. 10 Sai Bilatus yace
masa “Ba zaka yi mani magana ba? Baka san ina da
iko in sake ka ba, kuma in gicciye ka? 11 Yesu ya amsa
masa, “Ai ba ka da iko a kaina sai dai in an baka daga
sama, Saboda haka, wanda ya mika ni a gare ka shine
mafi zunubi”. 12 Da jin haka, sai Bilatus yayi kokari a
sake shi, amma sai Yahudawa suka tada murya sukace,
“In ka saki mutumin nan, kai ba abokin Kaisar bane,
duk wanda ya maida kansa sarki, ya sabawa Kaisar”.
13 Da Bilatus ya ji irin maganganunsu sai ya fito da
Yesu waje ya kuma zauna akan kujeransa a inda ake
kira “Dakalin shari'a,” a Yahudanci kuma, “Gabbata.”
14 To a ran nan ana shirye shiryen idin ketarewa,
da misalin sa'a ta shidda kenan, wato tsakar rana,
Bilatus yace wa Yahudawan “Ga sarkin ku!” 15 Su kuwa
suka yi ihu, a tafi da shi, a tafi da shi, a gicciye shi,

Bilatus yace masu "In gicciye sarkin ku? Sai manyan
firistocin sukace "Ba mu da wani sarki sai Kaisar". 16
Sai Bilatus ya mika Yesu domin su gicciye shi. 17 Sai
suka tafi da Yesu, ya fito yana dauke da gicciyen zuwa
wurin da ake kira "Wurin kwalluwa" da Yahudanci
kuma "Golgota". 18 Suka gicciye Yesu a wurin, tare da
wasu mutum biyu, daya a kowane gefe, Yesu kuwa na
tsikiya. 19 Bilatus kuwa ya rubuta wata alama a kan
gicciyen, "YESU BANAZARE, SARKIN YAHUDAWA". 20
Yahudawa da yawa kuwa suka karanta wannan alama
domin wurin da aka gicciye Yesu yana kusa da Birnin.
Alamar kuwa an rubuta ta da Yahudanci, da Romanci,
da Helenanci. 21 Sai manyan firistocin yahudawa
sukace wa Bilatus, kada ka rubuta sarkin Yahudawa,
amma kace, 'wannan yace "Ni ne sarkin Yahudawa"'.
22 Bilatus kuwa ya amsa, "Abinda na rubuta na rubuta
kenan." 23 Bayan da sojojin suka gicciye Yesu, sai suka
yayyaga rigarsa kashi hudu, kowane soja da nasa,
kashin, sai kuma alkyabbar. Alkyabbar kuwa bata da
dinki an saka tane daga sama har kasa. 24 Sai sukace
wa junansu, "Kada mu yaga alkyabbar, amma kuzo mu
jefa kuri'a a kan ta mu gani ko wanene zai dauke ta,
anyi haka ne domin a cika nassi cewa "Sun raba rigata
a tsakaninsu, sun kuwa jefa kuri'a domin alkyabbata.
25 Sojojin suka yi wadannan abubuwa. Uwar Yesu,
da 'yar'uwarta, da Maryamu matar Kilofas, da kuma
Maryamu Magadaliya. Wadannan mataye suna tsaye
kusa da gicciyen Yesu. 26 Da Yesu ya ga mahaifiyarsa
da almajirin nan da yake kauna tsaye kusa da juna,
yace, "Mace, dubi, dan ki!" 27 Sai yace wa almajirin,
"Dubi, mahaifiyarka!" Daga wannan sa'a almajirin ya
dauke ta zuwa gidansa. 28 Bayan wannan Yesu, saboda
ya san yanzu komai ya kammala, domin a cika nassin,
sai yace "Ina jin kishi. 29 A gefensu kuma akwai gora
cike da ruwan inabi mai tsami, sai suka tsoma soso
a cikin ruwan inabin mai tsami suka daura a wata
sanda sai suka mika masa a baki. 30 Da Yesu ya tsotsi
ruwan tsamin, sai yace "An gama" Sai ya sunkuyar da
kansa ya kuwa saki ruhunsa. 31 Sai Yahudawan, domin
ranar shirye shirye ne, domin kada a bar jikunansu
akan gicciye har ranar asabacin (domin asabacin rana
ce mai muhimmanci), suka roki Bilatus ya kakkarye
kafafunsu kuma ya saukar da su. 32 Sai sojojin suka zo
suka karya kafafun mutum na farko da kuma mutum
na biyun wadanda aka gicciye tare da Yesu. 33 Da suka
iso kan Yesu sai suka tarar ya riga ya mutu, sai basu
kuwa karya kafafunsa ba. 34 Duk da haka daya daga
cikin sojojin ya soki kuibin shi da mashi, nan da nan
sai jini da ruwa suka fito. 35 Wanda ya ga wannan,
shi ya zama shaida, shaidarsa kuwa gaskiya ce. Ya
sani cewa abinda ya fada gaskiya ne saboda ku ma ku
gaskata. 36 Wadannan sun faru ne domin a cika nassi,
"Babu ko daya daga cikin kasusuwansa da za'a karya".
37 Kuma wani nassin yace, "Zasu dube shi wanda suka
soka." 38 Bayan wadannan abubuwa, Yusufu mutumin
Arimatiya, wanda yake almajirin Yesu ne (amma a
boye saboda tsoron Yahudawa) ya roki Bilatus izini
domin ya dauke jikin Yesu. Bilatus kuwa ya bashi
izini, sai Yusufu yazo ya dauki jikin. 39 Nikodimu ma
ya zo, wanda da farko ya zo wurin Yesu da daddare,
ya kawo hadin man kamshi na mur da al'ul wajen
nauyin awo dari. 40 Sai suka dauki jikin Yesu suka
sa shi a likkafanin lillin tare da kayan kamshin nan,
domin jana'iza bisa ga al'adar Yahudawa. 41 To a
wurin da aka gicciye shi kuwa akwai wani lambu, a
cikin lambun kuma akwai sabon kabari wanda ba'a
taba sa kowa ba. 42 Da yake ranar shirye shirye ce ta
Yahudawa, kabarin kuwa na kusa, sai suka sa Yesu a
ciki.

**20** To da sassafe ranar farko ta mako, da sauran
duhu, Maryamu Magadaliya ta zo kabarin, ta
tarar an kawar da dutsen daga kabarin. 2 Sai ta ruga
da gudu zuwa wurin Saminu Bitrus tare da almajirin
nan da Yesu ke kauna, tace masu, "Sun dauke Ubangiji
daga kabarin, bamu kuwa san inda aka sa shi ba."
3 Sai Bitrus tare da almajirin nan suka fita, kuma
suka tafi kabarin, 4 dukansu suka ruga da gudu tare,
amma daya almajirin ya riga Bitrus isowa kabarin,
5 Sai ya sunkuya ya leka ciki, ya ga likkafanin lillin
a wurin, amma fa bai shiga ciki ba. 6 Sai Saminu
Bitrus ya iso daga bayansa sai ya shiga kabarin, ya
tarar da likkafanin lillin a ajiye. 7 sai fallen kuma da
yake kansa. Ba'a ajiye tare da likkafanin ba amma aka
linkeshi aka ajiye shi daban. 8 Sai almajirin nan da
ya riga isa kabarin shi ma ya shiga ya gani, sai ya
ba da gaskiya. 9 Har ya zuwa wannan lokacin basu
san nassin daya ce zai tashi daga matattu ba. 10 Sai
almajiran suka sake komawa gida kuma. 11 Amma
Maryamu tana tsaye a bakin kabarin tana kuka. Yayin
da take kuka, sai ta sunkuya ta leka cikin kabarin.
12 Sai ta ga mala'iku guda biyu cikin fararen kaya
zaune, daya ta wurin kai daya kuma ta wurin kafafu
inda aka kwantar da Yesu. 13 Sukace mata, "Uwargida

don me kike kuka? Sai tace masu, “Domin sun dauke
Ubangijina, ban kuwa san inda suka ajiye shi ba. 14
Bayan ta fadi haka, ta juya sai ta ga Yesu tsaye a
wurin. Amma bata san cewa Yesu bane, 15 Yesu yace
mata, “Uwargida, me yasa kike kuka? Wa kuma kike
nema? Domin tana zaton shine mai kula da lambun,
sai tace masa, “Maigida in kaine ka dauke shi, gaya
mani inda ka sa shi, ni kuwa in dauke shi.” 16 Yesu
yace mata, “Maryamu”. Sai ta juya, tace masa da
Armaniyanci “Rabboni!” wato mallam. 17 Yesu yace
mata, kada ki taba ni, domin har yanzu ban hau wurin
Uba ba tukuna, amma kije wurin 'yan'uwana kice
masu, zan je wurin Ubana da Ubanku, Allahna da
kuma Allahnku”. 18 Maryamu Magadaliya ta je tace
wa almajiran, “Na ga Ubangiji” Ta kuma ce ya fada
mata wadannan abubuwa. 19 Da yamma a wannan
rana, a rana ta farko ta mako, almajiran suna kulle
a daki saboda tsoron Yahudawa, Yesu yazo ya tsaya
a tsakaninsu, yace “Salama Agareku”. 20 Bayan ya
fadi haka, sai ya nuna masu hannuwansa da kuibinsa.
Da almajiran suka ga Ubangiji, sai suka yi farin ciki.
21 Yesu ya sake ce masu, “salama agareku. “Kamar
yadda Uba ya aiko ni, haka Ni ma na aike ku”. 22
Da Yesu ya fadi haka, sai ya hura masu lumfashinsa,
yace masu, “Ku karbi Ruhu Mai Tsarki. 23 Duk wanda
kuka gafarta wa zunubai, an gafarta masa; kowa kuka
rike zunubansa, an rikesu.” 24 Toma, daya daga cikin
sha biyun, wanda ake kira Dan Tagwai, baya tare
dasu lokacin da Yesu ya bayyana. 25 Sauran almajiran
sukace masa “Mun ga Ubangiji”. Sai yace masu, “In
ban ga gurbin kusoshi a hannuwansa ba, in sa yatsana
a gurbin kusoshin ba, in kuma sa hannuna cikin
kuibinsa ba, ba zan bada gaskiya ba. 26 Bayan kwana
takwas har wa yau almajiran na cikin gida, Toma
ma na tare dasu, kofofin suna kulle, sai ga Yesu a
tsakaninsu yace, “Salama agareku”. 27 Sa'an nan yace
wa Toma, “Iso nan da yatsanka, dubi hannuwana.
Miko hannunka kuma kasa a kuibina, kada ka zama
marar bada gaskiya, sai dai, mai bada gaskiya”. 28
Toma ya amsa yace “Ya Ubangijina da Allahna!” 29
Yesu yace masa, “Wato saboda ka gan ni, ka bada
gaskiya? Albarka ta tabbata ga wadanda basu gani ba,
amma kuwa sun bada gaskiya. 30 Yesu yayi wadansu
alamu da yawa dabam dabam a gaban almajiransa,
wadanda ba'a rubuta a littafin nan ba. 31 Amma an
rubuta wadannan ne, domin ku bada gaskiya Yesu
shine Almasihu, Dan Allah, ta wurin gaskatawa kuma
ku sami rai cikin sunansa.

21 Bayan wadannan abubuwa, Yesu ya sake bayyana
kansa ga almajiran a bakin tekun Tibariya. Ga
yadda ya bayyana kansa: 2 Saminu Bitrus na tare da
Toma wanda ake kira Dan Tagwai, da Natana'ilu daga
Kana ta kasar Galili, da 'ya'yan nan na Zabadi, da kuma
wadansu almajiran Yesu biyu. 3 Saminu Bitrus yace
masu, “Zani su.” sukace masa “Mu ma za mu je tare
da kai.” Sai suka fita suka shiga jirgi, amma a daren
nan basu kama komai ba. 4 To, gari na wayewa, sai ga
Yesu tsaye a bakin gaci, amma almajiran basu gane
cewa Yesu bane. 5 Sai Yesu yace masu, “Samari, kuna
da wani abinda za a ci?” Suka amsa masa sukace “A'a”.
6 Yace masu, “Ku jefa taru dama da jirgin zaku samu
wasu.” Suka jefa tarunsu har suka kasa jawo shi don
yawan kifin. 7 Sai almajirin nan da Yesu yake kauna
yace wa Bitrus, “Ubangiji ne fa!” Da Saminu Bitrus
yaji, Ashe, Ubangiji ne, yayi damara da taguwarsa,
(don a tube yake), ya fada a tekun. 8 Sauran almajiran
kuwa suka zo a cikin karamin jirgi, (domin basu da
nisa da kasa, kamar kamu dari biyu zuwa sama), janye
da tarun cike da kifi. 9 Da isowarsu gaci, sai suka ga
garwashin wuta a wurin da kifi akai, da kuma gurasa.
10 Yesu ya ce masu “Ku kawo wandansu daga cikin
kifin da kuka kama yanzu”. 11 Sai Saminu Bitrus ya
hau, ya jawo tarun gaci, cike da manyan kifaye dari
da hamsin da uku. Amma duk da yawansu, tarun
bai tsage ba. 12 Yesu yace masu, “Ku zo ku karya
kumallo”. Daga cikin almajiran kuwa babu wanda yayi
karfin halin tambayarsa “Ko shi wanene?” Domin
sunsani Ubangiji ne. 13 Yesu zo ya dauki gurasar ya ba
su, haka kuma kifin. 14 Wannan shine karo na uku
da Yesu ya bayyana ga almajiransa bayan tashinsa
daga matattu. 15 Da suka karya kumallon, Yesu yace
wa Saminu Bitrus, “Bitrus dan Yahaya, kana kaunata
fiye da wadannan?” Bitrus yace masa “I ya Ubangiji,
ka sani ina kaunarka” Yesu yace masa “Ka ciyar da
'ya'yan tumakina”. 16 Ya sake fada masa karo na biyu,
“Saminu Dan Yahaya, kana kaunata?” Bitrus Yace
masa “I ya Ubangiji, ka sani ina kaunarka”. Yesu yace
masa, “Ka lura da Tumakina”. 17 Ya sake fada masa,
karo na uku, “Bitrus Dan Yahaya, kana kaunata? Sai
Bitrus bai ji dadi ba domin Yesu ya fada masa karo
na uku, “Kana kaunata” Yace masa, “Ubangiji ka san
komai duka, ka sani ina kaunarka.” Yesu yace masa

“Ka ciyar da tumaki na. 18 Hakika, hakika, Ina gaya
maka, lokacin da kake kuruciyarka, kakan yi wa kanka
damara, ka tafi inda ka ga dama. amma in ka tsufa,
zaka mike hannuwanka wani yayi maka damara, ya
kai ka inda baka nufa ba.” 19 To Yesu ya fadi haka
ne domin ya nuna irin mutuwar da Bitrus zai yi ga
daukakar Allah. Bayan ya fadi haka, sai yace wa Bitrus,
ka biyo ni. 20 Bitrus ya juya sai ya ga almajirin da
Yesu yake kauna yana biye dasu; wanda ya jingina a
kirgin Yesu lokacin cin jibin nan da yace “Ya Ubangiji,
wanene zai bashe ka?” 21 Da Bitrus ya gan shi, yace
wa Yesu “Ya Ubangiji, Me mutumin nan zai yi?” 22
Yesu yace masa, “Idan ina so ya zauna har in dawo
ina ruwanka? Ka biyo ni.” 23 Wannan zance ya yadu
cikin 'yan'uwa cewa, wannan almajirin ba zai mutu
ba. Alhali Yesu bai cewa Bitrus, wannan almajirin
ba zai mutu ba, Amma “Idan ina so ya zauna har in
dawo ina ruwanka?” 24 Wannan shine almajirin da
yake shaida wadannan abubuwa, wanda ya rubuta su,
kuma mun tabbata shaidarsa gaskiya ne. 25 Akwai
kuma sauran abubuwa da yawa wanda Yesu yayi. Idan
da an rubuta kowannensu daya bayan daya, ina gaya
maku, ko duniya bazata iya daukar litattafan da za a
rubuta ba.

# Ayyukan Manzanni

**1** Littafin da na rubuta da farko, Tiyofilos, ya fadi
abubuwan da Yesu ya fara yi ya kuma koyar, 2 har
zuwa ranar da aka karbe shi zuwa sama. Wannan kuwa
bayan da ya ba da umarni ga zababbun manzanninsa
ta wurin Ruhu Mai Tsarki. 3 Bayan ya sha wahala, ya
bayyana kan sa da rai a garesu, da alamu da dama
masu gamsarwa. Kwana arba'in ya baiyana kansa a
garesu yana yi masu magana game da mulkin Allah. 4
Yayin da yana zaune tare da su ya basu umarni cewa
kada su bar Urushalima, amma su jira alkawarin Uban,
wanda ya ce, ''Kun ji daga gare ni, 5 cewa Yahaya babu
shakka ya yi baftisma da ruwa, amma ku za a yi maku
baftisma da Ruhu Mai Tsarki nan da kwanaki kadan.''
6 Sa'adda suna tare suka tambaye shi, ''Ubangiji, a
wannan lokaci ne za ka maido da mulki ga Isra'ila?"
7 Ya ce masu, ''Ba naku bane ku san lokaci ko sa'a
wanda Uba ya shirya ta wurin ikonsa. 8 Amma za
ku karbi iko, idan Ruhu Mai Tsarki ya zo bisanku,
sa'annan za ku zama shaidu na cikin Urushalima
da kuma cikin dukan Yahudiya da Samariya, har ya
zuwa karshen duniya." 9 Lokacin da Ubangiji Yesu
ya fadi wadannan abubuwa, yayin da suna kallon
sama, sai aka dauke shi zuwa sama, kuma girgije ya
boye shi daga idanunsu. 10 Da suka dinga kallon sama
yayin da ya tafi, nan da nan, mazaje biyu suka tsaya a
gabansu cikin fararen tufafi. 11 Suka ce, ''Ku mazajen
Galili me yasa ku ke tsaye a nan kuna kallon sama?
Wannan Yesu wanda ya hau zuwa sama zai dawo
kamar yadda kuka gan shi yana tafiya zuwa sama.'' 12
Da suka dawo Urushalima daga dutsen Zaitun, wanda
ke kusa da Urushalima, tafiyar Asabaci daya ne. 13 Da
suka iso, sai suka haye zuwa cikin bene inda suke da
zama. Sune su Bitrus, Yahaya, Yakubu, Andarawus,
Filibus, Toma, Bartalamawus, Matiyu, Yakubu dan
Alfa, Siman mai tsattsauran ra'ayi, kuma da Yahuza
dan Yakubu. 14 Dukansu kuwa suka hada kai gaba
daya, yayin da suka ci gaba da naciya cikin addu'a.
Tare da su kuma akwai mata, Maryamu mahaifiyar
Yesu, da kuma 'yan'uwansa. 15 A cikin wadannan
kwanaki Bitrus ya tashi tsaye a tsakiyar 'yan'uwa,
kimanin mutane dari da ashirin, ya ce, 16 '' 'Yan'uwa,
akwai bukatar Nassi ya cika, wanda Ruhu Mai Tsarki
ya fada a baya ta bakin Dauda game da Yahuza, wanda
ya jagoranci wadanda suka kama Yesu 17 Domin
yana daya daga cikinmu kuma ya karbi rabonsa na
ladan wannan hidima," 18 (Wannan mutum fa ya
sai wa kansa fili da cinikin da ya yi na muguntarsa,
kuma a nan ya fado da ka, cikinsa ya fashe, hanjinsa
suka zubo waje. 19 Duka mazaunan Urushalima suka
ji wannan, saboda haka suka kira wannan fili da
harshensu "Akeldama'' wato, "Filin Jini.") 20 "Domin
an rubuta a littafin Zabura, 'Bari filinsa ya zama kufai,
kada a bar kowa ya zauna wurin,'kuma, 'Bari wani
ya dauki matsayinsa na shugabanci.' 21 Saboda haka
ya zama dole, daya daga cikin wadanda suke tare da
mu tun lokacin da Ubangiji Yesu yana shiga da fita,
a tsakaninmu, 22 farawa daga baftismar yahaya har
zuwa ranar da aka dauke shi daga wurinmu zuwa
sama, ya zama daya daga cikin mu wurin shaidar
tashinsa." 23 Suka gabatar da mutum biyu, Yusufu
wanda ake kira Barsabbas, wanda kuma aka yiwa suna
Justus, da kuma Matayas. 24 Su ka yi addu'a suka
ce, ''Ubangiji, kai ka san zuciyar dukan mutane, ka
bayyana mana wanda ka zaba cikin su biyun nan 25
Domin ya dauki gurbin da kuma manzancin daga inda
Yahuza ya kauce zuwa nashi waje'' 26 suka jefa kuri'a
a kansu; zabe ya fada kan Matayas kuma suka lissafta
shi tare da manzanni sha dayan.

**2** Da ranar Fentikos ta zo, dukansu suna tare wuri
daya. 2 Nan da nan sai ga wata kara daga sama
kamar ta babbar iska, kuma ta sauko ta cika duka
gidan inda suke zaune. 3 Sai ga wasu harsuna kamar
na wuta sun bayyana a garesu aka rarraba su, kuma
suka zauna bisa kowannensu. 4 Dukansu suka cika
da Ruhu Mai Tsarki suka fara magana da wadansu
harsuna, yadda Ruhu ya ba su iko su yi magana. 5 A
lokacin akwai Yahudawa dake zaune a Urushalima,
mutanen Allah, daga kowace kasa karkashin sama. 6
Da suka ji wannan kara jama'a duk suka taru suka rude
saboda kowannensu ya ji suna magana da harshensa.
7 Suka yi mamaki matuka; suka ce, ''Lallai, wadannan
duka ba Galiliyawa ba ne? 8 Yaya mu ke jinsu duka,
kowannensu na magana a cikin harshen da aka haife
mu? 9 Fisiyawa da Mediyawa da Elimawa, da Yahudawa
da Kafadokiya, cikin Fontus da Asiya, 10 cikin Firgia da
Bamfiliya, cikin Masar da yankunan Libiya ta wajen
Sur, da baki daga Roma, 11 Yahudawa da tubabbun
cikin Yahudanci, Kiretawa da Larabawa, duk munji
su suna fadi a harshenmu game da manyan ayyukan
Allah.'' 12 Dukansu suka yi mamaki suka rikice; suka
ce da junansu, ''Menene ma'anar wannan?'' 13 Amma
wasu suka yi ba'a suka ce, ''Sun bugu ne da sabon

ruwan inabi.'' 14 Amma Bitrus ya tashi tare da sha
dayan, ya daga murya ya ce da su, ''Mutanen Yahuda
da dukanku dake zaune a Urushalima, bari ku san
wannan; ku saurari maganata. 15 Domin wadannan
mutanen ba buguwa suka yi ba yadda kuke zato,
domin yanzu karfe tara ne na safe kawai. 16 Amma
wannan shine abinda aka fada ta wurin annabi Yowel.
17 Allah ya ce, 'Haka zai kasance a kwanakin karshe,
zan zubo Ruhuna a kan dukan mutane, 'ya'yanku
maza da mata za su yi anabci, kuma samarinku za su
ga wahayoyi, kuma tsofaffinku za su yi mafarkai. 18
Haka kuma a bisa bayi na maza da mata, a kwanakin
nan zan zubo da Ruhuna, kuma za su yi anabci. 19
Zan nuna al'ajibai a sararin sama da kuma alamu a
bisa duniya, jini da wuta, da girgije. 20 Rana zata juya
ta koma duhu kuma wata ya koma jini, kafin Babbar
ranan nan ta Ubangiji ta zo. 21 Zai kuma zama dukan
wanda ya kira ga sunan Ubangiji zai sami ceto. 22
Mutanen Isra'ila, ku saurari wadannan magana. Yesu
Banazare, mutumin da Allah ya tabbatar da shi gareku
ta wurin manyan ayyuka da ban mamaki da alamu
da Allah ya yi ta wurinsa a tsakiyarku, kamar yadda
ku da kanku kuka sani. 23 Saboda tabbataccen shiri
da riga sani na Allah, aka bayar dashi, ku kuma, ta
hannun mutane 'yan tawaye, kuka gicciye shi kuma
kuka kashe shi. 24 Wanda Allah ya tayar, bayan ya cire
zafin mutuwa daga gareshi, saboda ba zai yiwu ba ta
rike shi. 25 Gama, game da shi, 'Ina ganin Ubangiji a
gabana ko yaushe, domin yana gefen hannun damana
saboda kada in firgita. 26 Saboda haka zuciyata na
farin ciki harshena yana yin murna. Kuma, jikina zai
zauna gabagadi. 27 Gama ba za ka watsar da raina
a lahira ba, ba kuwa za ka bar Mai Tsarkinka ya ga
ruba ba. (Hadēs g86) 28 Ka bayyana mani hanyar rai; da
fuskarka zaka cika ni da farin ciki. 29 'Yan'uwa, zan yi
magana da ku gabagadi game da baba Dauda: ya mutu
kuma aka bizne shi, kuma kabarinsa na nan tare da
mu har yau. 30 Domin haka, don shi annabi ne kuma
ya san Allah ya yi masa alkawari da rantsuwa cewa
daga cikin zuriyarsa zai sanya wani bisa kursiyinsa.
31 Ya hango wannan al'amari kuma ya yi magana
game da tashin Almasihu, 'Ba ayi watsi da shi ba a
lahira, kuma jikinsa bai ga rubewa ba.' (Hadēs g86) 32
Wannan Yesun - Allah ya tashe shi, wanda dukanmu
shaidu ne. 33 Saboda haka yadda aka tashe shi zuwa
hannun dama na Allah kuma ya karbi alkawarin Ruhu
Mai Tsarki daga wurin Uba, shine ya zubo mana
wannan da kuke gani kuma kuke ji. 34 Dauda bai
hau zuwa sama ba, amma ya ce, ''Ubangiji ya ce wa
Ubangijina, "Zauna hannun dama na, 35 har sai na
maida makiyanka abin takawar sawunka."' 36 Saboda
haka, bari gidan Isra'ila su sani tabbas wannan Yesun
wanda kuka gicciye, Allah ya maishe shi Ubangiji da
kuma Almasihu. 37 Da suka ji haka sai suka soku a
zukatansu, suka cewa Bitrus da sauran manzanni,
'''Yan'uwa me za mu yi?'' 38 Sai Bitrus ya ce masu,
''Ku tuba ayi wa kowannenku baftisma, cikin sunan
Yesu Almasihu domin gafarar zunubanku, kuma za ku
karbi baiwar Ruhu Mai Tsarki. 39 Domin alkawarin
a gareku ne da 'ya'yanku da duk wadanda ke nesa,
dukan iyakar mutanen da Ubangiji Allahnmu zai
kira.'' 40 Da maganganu da yawa ya ba da shaida kuma
ya karfafa su; ya ce, ''Ku ceci kan ku daga wannan
muguwar tsara.'' 41 Sai suka karbi maganar sa kuma
aka yi ma su baftisma, a wannan rana kuma aka sami
karin rayuka wajen dubu uku. 42 Su ka cigaba cikin
koyarwar manzanni da zumunta, cikin kakkaryawar
gurasa da kuma cikin addu'o'i. 43 Tsoro ya sauko bisa
kowane rai, kuma aka yi abubuwan ban mamaki da
alamu da yawa ta wurin manzannin. 44 Duka wadanda
suka ba da gaskiya suna tare kuma komai nasu na
kowanensu ne, 45 kuma suka saida kadarorinsu da
mallakarsu kuma suka rarrabawa kowa, bisa ga irin
bukatar da kowannensu yake da ita. 46 A kowace
rana suka cigaba tare da nufi daya a cikin haikali,
suna kakkarya gurasa a gidaje, kuma suna raba abinci
tsakaninsu cikin farin ciki da tawali'u a zuciya; 47
Suna yabon Allah kuma suna da tagomashi a gaban
dukan mutane. Ubangiji kuma kullum yana kara masu
wadanda suke samun ceto.

3 Sa'adda Bitrus da Yahaya suna hanya zuwa haikali
a lokacin addu'ar karfe uku. 2 Wani mutum, gurgu
ne tun daga haihuwa, ana daukar sa kulluyomi zuwa
kofar haikali da ake kira Kyakkyawa, domin bara gun
mutanen da ke shiga haikalin. 3 Da ya ga Bitrus da
Yahaya suna shiga haikalin, sai ya roke su sadaka. 4
Bitrus da Yahaya kuwa suka zuba masa ido, Bitrus
ya ce, ''Ka dube mu.'' 5 Gurgun nan kuwa ya dube
su, yana tsammanin zai sami wani abu a wurin su. 6
Amma Bitrus ya ce, "Azurfa da Zinariya ba ni da su,
amma abin da nake da shi, zan baka. A cikin sunan
Yesu Almasihu Banazare, Yi tafiya'' 7 Bitrus ya kama
hannun damarsa, ya daga shi; nan da nan kafafunsa da

kashin idon sawayensa suka samu karfi. 8 Da gurgun
ya yunkura, ya mike tsaye sai ya fara takawa; ya shiga
haikali tare da Bitrus da Yahaya, yana takawa, yana
tsalle, yana kuma girmama Allah. 9 Dukan mutane
suka gan shi yana tafiya yana kuma yabon Allah. 10
Sun lura cewa, shine mutumin da ke zama yana bara
a Kyakyawar kofar haikali; sai suka cika da mamaki
domin abin da ya faru. 11 Yayin da yake rike da Bitrus
da Yahaya, dukan jama'a suka matso wurinsu, a gefen
dakalin Sulaimanu, suna ta mamaki kwarai. 12 Da
Bitrus ya ga haka ya amsa wa jama'ar, “Ya ku mutanen
Isra'ila, don me ku ke mamaki?” Don me ku ka zura
mana ido, kamar mu ne muka sa shi ya yi tafiya da
ikon kanmu ko adalcin mu? 13 Allah na Ibrahim, da
Ishaku, da Yakubu, Allah na iyayenmu ya girmama
bawansa Yesu. Shi kuka ki kun kuma bashe shi a
gaban Bilatus da ya so ya sake shi. 14 Kuka ki Mai
Tsarkin nan, Mai Adalcin, maimakon haka kuka ce a
sakkar maku mai kisan kai. 15 Kun kashe mai ba da rai,
wanda Allah ya tayar daga matattu, mu kuwa shaidu
ne ga wannan al'amari. 16 Yanzu, ta bangaskiya ga
sunansa - wannan mutum da kuke gani kuma kun
san shi - ta wurin wannan sunan ne ya sami karfi.
Bangaskiya cikin Yesu ta ba shi cikakkiyar lafiya, a
gabanku duka. 17 Ya ku 'yan'uwa, na san kun yi haka
ne cikin rashin sani, yadda shugabaninku suka yi.
18 Amma duk abubuwan da Allah ya fada ta bakin
dukan anabawansa, cewa Almasihunsa zai sha wahala,
yanzu ya cika. 19 Saboda haka, Ku tuba, ku juyo,
domin a shafe zunubanku, domin lokacin sabuntuwa
daga wurin Ubangiji ya zo; 20 domin a aiko maku da
Almasihu wanda aka kaddara wato, Yesu. 21 Shine
wanda dole sama ta karbe shi har zuwa lokacin komo
da dukan abubuwa, game da abubuwan da Allah ya
fada tun da ta bakin annabawansa tsarkaka. (aiōn g165)
22 Musa hakika ya ce, 'Ubangiji Allah zai tayar maku
da wani annabi kamar ni daga cikin, 'yan'uwanku. Za
ku saurari dukan abin da zai fada maku. 23 Zai kasance
kowanne mutum da bai saurari annabin nan ba za
a kau da shi gabadaya daga cikin mutanensa.' 24 I,
dukan annabawa tun daga Sama'ila da wadanda suka
zo bayansa, sun yi magana sun ambaci wadannan
kwanaki. 25 Kune 'ya'yan annabawa da na alkawari
wanda Allah ya yi da kakanninku, yadda ya ce wa
Ibrahim, 'Daga zuriyarka dukan al'uman duniya za su
sami albarka.' 26 Bayan da Allah ya ta da bawansa,
a gareku ne ya fara aiko shi, domin ya albarkace ku
tawurin juyadda kowannenku daga muguntarsa.”

4 Yayin da Bitrus da Yahaya suna kan magana da
mutanen, sai firistoci da shugaban masu tsaron
Haikali da kuma Sadukiyawa suka afko masu. 2 Sun
damu sosai domin Bitrus da Yahaya suna koyar da
mutane game da Yesu kuma suna shelar tashinsa
daga matattu. 3 Suka kama su suka jefa kurkuku
sai washegari, domin yamma ta riga ta yi. 4 Amma
mutane da yawa da suka ji sakon suka ba da gaskiya;
kimanin mazaje dubu biyar ne kuwa suka ba da
gaskiya. 5 Washegari, da shugabaninsu, da dattawansu,
da Marubuta suka taru a Urushalima. 6 Anas babban
firist, yana nan, da Kayafa, da Yahaya da Iskandari, da
dukan dangin babban firist 7 Da suka kawo Bitrus da
Yahaya a tsakiyarsu sai suka tambaye su, “Da wanne
iko, ko cikin wanne suna k ka yi haka?” 8 Sai Bitrus,
cike da Ruhu Mai Tsarki, ya ce, “Ku shugabanni da
dattawan jama'a, 9 idan mu yau ana tuhumarmu
saboda aikin kirki da aka yi ga wannan mara lafiya -
ta yaya wannan mutum ya sami lafiya? 10 Bari ku da
dukan mutanen Isra'ila, ku san wannan, cikin sunan
Yesu Almasihu Banazare, wanda kuka giciye, wanda
Allah ya tayar daga matattu ta dalilinsa ne wannan
mutumin yake tsaye a gaban ku lafiyayye. 11 Yesu
Almasihu ne dutsen da ku magina kuka ki, amma
an mai da shi kan gini. 12 Babu ceto daga kowanne
mutum, domin babu wani suna da aka bayar karkashin
sama, a cikin mutane wanda ta wurinsa za a iya
samu ceto.'' 13 Sa'adda, suka ga karfin halin Bitrus da
Yahaya, suka gane mutane ne talakawa marasa ilimi,
sai suka yi mamaki, suka kuma lura suka gane Bitrus
da Yahaya sun kasance tare da Yesu. 14 Da yake suna
ganin mutumin nan da aka warkar tare da su, sai suka
rasa abin yi. 15 Amma bayan sun fitar da manzannin
daga majalisa sai suka tattauna a tsakaninsu. 16 Suka
ce, “Yaya za mu yi da wadannan mutane? Babu shakka
aikin al'ajibi ya faru ta wurinsu, kuma sananne ne ga
dukan mazauna Urushalima, kuma ba mu da iko mu
musanci haka. 17 Amma saboda kada ya cigaba da
yaduwa cikin mutane, bari mu yi masu kashedi kada
su kara magana da kowa cikin wannan suna.'' 18 Suka
kira Bitrus da Yahaya suka dokace su kada su kara
magana ko kuma koyarwa ko kadan a cikin sunan
Yesu. 19 Amma Bitrus da Yahaya suka amsa suka ce,
''Ko ya yi daidai a gaban Allah mu yi maku biyayya

fiye da shi, ku hukunta. 20 Baza mu iya daina magana
game da abubuwan da muka ji kuma muka gani ba.''
21 Bayan sun sake yi wa Bitrus da yahaya kashedi, sai
suka sake su, su tafi. Domin ba su iya samu wata hujja
da za su hore su a kai ba, domin dukan mutane suna
yabon Allah saboda abin da ya faru. 22 Mutumin da
ya sami wannan al'ajibi na warkarwa yana sama da
shekara arba'in. 23 Bayan an sake su, Bitrus da Yahaya
suka zo cikin mutanensu suka ba da rahoton duk abin
da manyan firistoci da dattawa suka fada masu. 24
Da suka ji haka, suka daga muryarsu tare ga Allah
suka ce, ''Ubangiji, kai da ka yi sama da duniya da
teku da duk abin da ke cikinsu, 25 kai wanda ta wurin
Ruhu Mai Tsarki ta bakin ubanmu Dauda bawanka, ya
ce, 'Me ya sa al'ummai suka tunzura, kuma mutane
suke tunanin abubuwan banza? 26 Sarakunan duniya
sun hada kansu tare, kuma shugabanninsu sun taru
don su yi gaba da Ubangiji, da kuma Almasihunsa.' 27
Hakika, Hiridus da Buntus Bilatus, tare da al'ummai da
mutanen Isra'ila, sun taru a wannan birni domin su yi
jayayya da bawanka mai tsarki Yesu, shafaffe. 28 Sun
taru domin su aiwatar da dukan abin da hannunka da
nufinka ya shirya zai faru. 29 Yanzu, Ya Ubangiji ka
dubi kashedin su, ka ba bayin ka ikon furta maganar
ka gabagadi. 30 Sa'adda ka mika hannunka domin
warkarwa, alamu da al'ajibai su faru ta wurin sunan
bawanka mai tsarki Yesu." 31 Bayan sun gama addu'a,
wurin da suka taru ya girgiza, suka cika da Ruhu
Mai Tsarki, suka furta maganar Allah gabagadi. 32
Babban taron da suka ba da gaskiya kansu hade yake;
kuma ba wanda ya ce da abinda ya mallaka nasa ne;
maimakon haka, komai na su daya ne. 33 Da iko mai
karfi manzannin suka yi shelar shaidarsu game da
tashin Yesu Ubangiji daga matattu, babban alheri
kuma na bisansu. 34 Babu wani a cikinsu wanda ya
rasa komai, domin masu filaye da gidaje suka sayar
suka kawo kudin abin da suka sayar 35 sai suka kawo
kudin gaban manzanni. Aka rarraba wa kowanne
mutum bisa ga bukatarsa. 36 Yusufu, Balawi, mutumin
tsibirin Kubrus, wanda manzannisu ka yi wa lakani da
suna Barnaba. (wato, mai karfafa zuciya). 37 Yana da
fili sai ya sayar da shi ya kawo kudin gaban manzanni.

5 Sai wani mai suna Hananiya da matarsa Safiratu,
suka sayar da filinsu, 2 Hananiya kuwa ya
boye wasu daga cikin kudin filin, (kuma da sanin
matarsa), sa'annan suka kawo ragowar kudin a gaban
manzannin. 3 Amma Bitrus ya ce, ''Hananiya don me
shaidan ya cika zuciyarka, har ka yi wa Ruhu Mai
Tsarki karya? Har ka boye wasu daga kudin filin? 4
Sa'adda ba ka sayar da filin ba, ba mallakarka bane?
Bayan da ka sayar ma, ba naka bane? Don me kayi
irin wannan tunanin a zuciyarka? To ba mutane ka yi
wa karya ba, Allah ka yi wa." 5 Nan take da jin haka,
Hananiya ya fadi ya ja numfashinsa na karshe. Dukan
mutanen da suka ji labarin kuwa tsoro mai girma ya
afko masu 6 Matasa suka zo suka nannade gawarsa,
suka fitar da shi waje suka binne shi. 7 Bayan wajen
sa'a uku, sai matarsa ta iso, ba tare da sanin abin da ya
faru ba. 8 Sai Bitrus ya ce mata, ''ki gaya mini ko nawa
kuka sayar da filin?'' Sai ta amsa, ''ta ce kaza ne."
9 Sa'annan Bitrus ya ce mata, ''Don me kuka shirya
wannan makidar tare da mijinki don ku gwada Ruhun
Ubangiji? Kiji tafiyar wadanda suka bizne mijinki a
bakin kofa, kuma za su dauke ki yanzu.'' 10 Nan take
sai ta fadi a gabansa, ta ja numfashinta na karshe,
matasan kuwa suka zo suka same ta ta mutu; sai
suka dauki gawarta suka kai waje suka kuma bizne ta
kusa da mijinta. 11 Tsoro mai girma kuwa ya afko wa
iklisiyar gaba daya da dakan wadanda suka ji wadan
nan al'amura. 12 Ayyukan alamu da ban mamaki
masu yawa kuwa sun faru ga mutane, ta hannun
manzannin. Dukansu kuma suna nan tare a dakalin
Sulaimanu, 13 Sai dai babu mai karfin halin ya hada
kai tare dasu; amma suna da kwarjini sosai a gaban
jama'a. 14 Har wa yau aka rika samun karin masu ba
da gaskiya, dinbin jama'a, maza da mata, 15 har sukan
dauki marasa lafiya su kai su bakin titi, suna kwantar
da su a bisa gadaje da shinfidu, domin idan Bitrus
ya zo wucewa ko da inuwarsa ma ta taba wasunsu.
16 Mutane dayawa kuwa sukan zo daga garuruwan
da ke kewaye da Urushalima, suna kuma kawo masu
rashin lafiya, da wadanda aljannu ke damunsu, aka
kuma warkar da su duka. 17 Amma babban firist ya
taso tare da duk wadanda ke tare da shi (wato 'yan
darikar Sadukiyawa); suka cika da kishi matuka 18
suka kama manzannin suka kuma jefasu a kurkuku.
19 A cikin dare sai mala'ikan Ubangiji ya bude kofofin
kurkukun ya kuma fito da su waje, ya ce, 20 "Kuje
ku tsaya a gaban haikali ku kuma gaya wa mutane
maganar wannan rai." 21 Sa'adda suka ji haka, sai
suka tafi haikalin da wayewar gari suka yi koyarwa.
Amma babban firist da jama'arsa suka zo suka kuma
kira taro da kuma dukan yan majalisa, da dattawan
jama'ar Isra'ilawa suka fito suka kuma ba da umarni,

a fito masu da manzannin. 22 Amma ma'aikatan da
suka je kurkukun basu sami kowa, a kurkukunba, sai
suka dawo suka ba da rahoto, 23 Su ka ce kurkukun
a rufe gam da masu gadi suna nan a tsaye a bakin
kofar amma da muka shiga, bamu sami kowa a ciki
ba. 24 Yanzu sa'adda shugaban haikalin da manyan
firistoci suka ji wadannan kalamai, sai suka rikice
sosai game da su, suka ce yanzu me wannan zai haifar.
25 Sai wani ya zo ya ce masu, ''Wadannan mutanen
da kuka jefa a kurkuku suna can a cikin haikali
suna koyar da jama'a.'' 26 Sai shugaban haikalin ya
je da ma'aikatansa suka kawosu, ba tare da tashin
hankali ba, domin gudun kada jama'a su jejjefesu.
27 Da suka kawo su, sai suka gabatar da su gaban
majalisa, babban firist kuwa ya tuhume su, 28 cewa
''Ba mun yi maku kashedi da karfi kada ku yi koyarwa
cikin wannan sunan ba? Amma ga shi duk kun cika
Urushalima da koyarwarku, kuna kuma neman kusa
jinin mutumin nan ya sauko kanmu." 29 Amma Bitrus
da manzannin suka amsa suka ce, ''Dole mu yi wa
Allah biyayya ba mutane ba. 30 Allah na ubanenmu ya
ta da Yesu, wanda kuka kashe, ta wurin rateye shi a
bisa itace, 31 Allah kuwa ya daukaka shi a hannun
damarsa, domin ya zama sarki da kuma mai ceto,
ya ba Isra'ila tuba da gafarar zunubai. 32 Mu kuwa
shaidu ne ga wadannan al'amura, haka ma Ruhu Mai
Tarki, wanda Allah ya bayar ga dukan wadanda suka
yi biyayya a gareshi.'' 33 Da yan majalisa suka ji haka
sai suka fusata kwarai da gaske, har suka nemi su
kashe manzannin. 34 Amma wani Bafarise mai suna
Gamaliel, malami ne kuma na attaura wanda dukan
jama'a suna martabawa, sai ya mike ya ba da umarni
cewa a fid da manzannin waje na dan lokaci. 35 Sai ya
ce masu ''Ya ku mutanen Isra'ila, ku lura sosai da a
binda kuke niyyar yi wa mutanen nan, 36 A kwanakin
baya wani ya zo mai suna Tudas ya dauki kansa wani
abu, kimanin mutane dari hudu ne suka bishi, amma
da aka kashe shi jama'arsa baki daya sai suka watse,
ba wanda ya kara jin labarinsu. 37 Bayansa kuma, aka
yi wani mai suna Yahuza na Galili wanda a kwanakin
kidaya, ya zo ya rinjayi mutane da yawa, shima ya
lalace, duk wadanda suka bi shi kuwa suka watse. 38
Don haka ina gaya maku ku rabu da mutanen nan,
domin idan shirinsu ko kuma ayyukansu na mutane
ne za su lalace. 39 Amnma idan abin nan daga Allah
yake baza ku iya lalata su ba; kada ya zama kuna gaba
da Allah.'' Sai suka rinjayu. 40 Da suka kira manzannin
ciki suka yi masu duka, sai suka umarce su da cewa
kada su sake koyarwa a cikin sunan Yesu, sai suka
barsu suka tafi. 41 Suka fita daga cikin majalisar, suna
murna domin sun cancanta su sha wulakanci saboda
sunan. 42 Bayan haka kullayomin suna zuwa haikali,
suna bi gida gida, suna wa'azi, suna kuma koyarwa ba
fasawa cewa Yesu shine Almasihu.

**6** A wadannan kwanaki, yawan almajiran ya ci gaba
da ribanbanya, sai Yahudawan da suke zama a kasar
Helanawa suka fara gunaguni game da Yahudawan
Isra'ila, domin basu damu da gwamrayensu, wajen
raba abinci da ake yi kullum. 2 Manzannin nan sha
biyu suka kira taron almajiran suka ce masu, ''Bai
kamata mu bar maganar Allah mu shiga hidimar
rabon abinci ba. 3 Don haka ku zabi 'yan'uwa maza
daga cikinku, mutane bakwai wadanda a ke ganin su
da daraja, cike da Ruhu da kuma hikima, wadanda za
mu zaba suyi wannan hidima. 4 Mu kuwa mu ci gaba
da da addu'a da kuma hidimar kalmar.'' 5 Maganar su
kuwa ta farantawa dukan jama'a rai sosai. Sai suka
zabi Istifanus, shi kuwa mutum ne cike da bangaskiya
kuma da Ruhu Mai Tsarki da Filibus, da Birokoros, da
Nikanar, da Timan, da Barminas, da kuma Nikolas,
mutmin Antakiya wanda ya yi tuban Yahudanci. 6
Masu bin kuwa suka gabatar da wadannan mutanen a
gaban manzannin, su kuwa suka yi masu addu'a suka
kuma dora hannuwansu a kansu. 7 Sai maganar Allah
ta yawaita; yawan almajiran kuwa ya rubanbanya
matuka a Urushalima; firistoci da yawa na Yahudawa
suka bada gaskiya. 8 Sai Istifanus, cike da alheri da
iko, ya rika yin ayyukan ban mamaki da alamu a
cikin jama'a. 9 Amma sai ga wadansu mutane daga
wata majami'a da ake kira majami'ar Yantattu, wato
su Kuramiyawa da Iskandariyawa, da kuma wasu
daga kasar Kilikiya da Asiya. Wadannan mutanen
kuwa suna muhawara da Istifanus. 10 Amma suka
kasa yin tsayayya da Istifanus, saboda irin hikima
da Ruhun da Istifanus ya ke magana da shi. 11 Sai
a asirce suka zuga wasu mutane su je su ce, ''Ai
munji Istifanus yana maganganun sabo game da Musa
da kuma Allah.'' 12 Sai suka zuga mutanen, har da
dattawa da marubuta suka tunkari Istifanus, suka
kama shi, suka kawo shi gaban majalisa. 13 Suka kawo
masu shaidar karya suka ce, ''Wannan mutumin har
yanzu bai dena maganganun gaba akan wannan wuri
mai tsarki da kuma shari'a ba. 14 Domin kuwa mun

ji shi, yana cewa wannan Yesu Banazarat zai rushe
wannan wuri zai kuma canza al'adun da muka gada
daga wurin Musa.'' 15 Dukan wadanda suke zaune a
majalisar suka zuba masa ido, sai suka ga fuskarsa
kamar ta mala'ika.

7 Sai babban firist ya ce, ''Wadannan al'amura
gaskiya ne?'' 2 Sai Istifanus ya amsa ya ce, ''Ya
'yan'uwa da ubanni, ku saurare ni, Allah Madaukaki
ya bayyana ga ubanmu Ibrahim tun yana can kasar
Mesofotamiya, kafin ma ya zauna a kasar Haran; 3 ya
ce masa, 'Ka bar kasarka da danginka, ka tafi kasar da
zan nuna maka.' 4 Sa'annan ya bar kasar Kaldiyawa
ya zo ya zauna a Haran; daga can, bayan rasuwar
mahaifinsa, sai Allah ya kira shi zuwa wannan kasa
da kuke ciki. 5 Amma Allah bai ba shi kasar gado
ba tukuna, ko da misalin tafin sawunsa. Amma ya
alkawarta - ko da yake bai riga ya haifi da ba tukuna
- wanda zai ba shi kasar gado, shi da zuriyarsa, a
bayansa. 6 Allah ya yi magana da shi kamar haka,
cewa zuriyarsa za su yi bakonci a wata kasa wadda ba
tasu ba, mutanen wannan kasar kuwa za su gwada
masu bakar azaba su kuma bautar da su har shekaru
dari hudu. 7 'Kuma zan hukunta wannan al'umma
da ta bautar da su,' Allah ya ce, 'Bayan haka za su
fito daga wannan kasa su bauta mini a wannan wuri.'
8 Allah ya ba Ibrahim alkawarin kaciya, sai Ibrahim
ya haifi Ishaku ya yi masa kaciya a rana ta takwas;
Ishaku ya haifi Yakubu, Yakubu kuma ya haifi ubanni
Isra'ila su goma sha biyu. 9 Wadannan 'yan'uwa suka
yi kyashin danuwansu Yusifu suka sayar da shi bauta
zuwa Masar. Amma Allah na tare da shi. 10 Ya kuwa
cece shi daga dukan sharin da yan uwansa suka kulla
masa, Allah kuwa ya ba shi tagomashi da hikima a
gaban Fir'auna, sarkin Masar. Fir'auna kuwa ya mai
da shi mai mulki a dukan kasar Masar da kuma dukan
mallakarsa. 11 Sai aka yi babbar yunwa a dukan kasar
Masar da ta Kan'ana, iyayenmu suka sha wuya saboda
rashin abinci. 12 Amma lokacin da Yakubu ya ji akwai
hatsi a kasar Masar, sai ya aiki ubannimu a karo na
farko. 13 Da suka je a karo na biyu, sai Yusifu ya
bayyana kansa ga yanuwansa; a wannan lokaci ne
Fir'auna ya gane da yanuwan Yusufu. 14 Yusufu ya
aiki yanuwansa su kawo Yakubu ubansu da dukan
mallakarsu da iyalansu zuwa Masar, Dukansu mutane
saba'in da biyar ne. 15 Yakubu ya tafi ya zauna a
Masar; shi da zuriyarsa har mutuwar su. 16 Aka dauke
su zuwa Shekem aka binne su a kabarin da Ibrahim ya
saya da kudin azurfa daga hannun yayan Hamor a
Shekem. 17 Yayin da alkawarin Allah ya kusato wanda
Allah ya fada wa Ibrahim, mutanen suka karu suka
hayayyafa kwarai a Masar, 18 Sai a ka yi wani sarki a
Masar wanda bai san Yusifu ba, 19 Wannan sarki ya
yaudari kakkaninmu ya yi masu mugunta kwarai da
gaske, har ma ya kai ga suna barin jariransu cikin
hasari don su ceci rayukansu. 20 A wannan lokaci ne
aka haifi Musa, kuma kyakkyawan yaro ne sai aka yi
renon sa tsawon wata uku a gidan mahaifinsa a asirce.
21 Yayin da aka jefar da shi, sai diyar Fir'auna ta dauke
shi ta rene shi kamar danta. 22 Aka ilimantar da
Musa da dukan ilimi irin na Masar; kuma ya shahara
cikin fasahar magana da kuma ayyukansa. 23 Amma
lokacin da yakai shekara arba'in, sai ya yi niyyar ya
ziyarci 'yan'uwansa, Isra'ilawa. 24 Sai ya ga wani na
cin zalin Ba Isra'ile, Musa kuwa ya taimaki wanda
ake kwara ta wurin murkushe Bamasaren: 25 zaton
Musa 'yan'uwansa za su fahimci taimakon Allah ne ya
zo masu amma ina! Basu gane ba. 26 Washegari ya
ga wasu Isra'ilawa na fada da junansu; ya yi kokari
ya raba su; sai ya ce masu, 'Malamai, ku 'yan'uwan
juna ne; don me kuke fada da junanku?' 27 Amma
shi wanda ake kwarar makwabcinsa ya ture Musa a
gefe guda, ya ce, 'Wa ya nada ka shugaba ko alkali
akanmu? 28 Kana so ka kashe ni ne, kamar yadda ka
kashe Bamasaren nan jiya?' 29 Da jin haka sai Musa ya
gudu, zuwa kasar Midinawa, a matsayin dan gudun
hijira. Anan ya haifi ''ya'ya biyu maza. 30 Bayan da
shekaru arba'in suka wuce, sai mala'ika ya bayyana
gare shi a jeji, kusa da dutsen Sinai, a cikin harshen
wuta a cikin jeji. 31 Sa'adda Musa ya ga wutar, mamaki
ya kama shi; sai ya maso kusa don ya kara dubawa,
sai ya ji muryar Ubangiji na cewa, 32 'Nine Allah na
ubanninka, Ibrahim, da na Ishaku, da na Yakubu.'
Musa ya razana har ma bai sake daga kai ya duba ba.
33 Ubangiji ya ce masa, 'Tube takalminka, domin in
da kake tsaye wuri mai tsarki ne. 34 Ba shakka na ga
wahalar da mutane na ke sha a Masar, kuma na ji
nishinsu, don haka na zo in cece su, yanzu fa sai ka zo,
in aike ka zuwa Masar.' 35 Wannan fa shine Musan da
suka ki, harma da cewa, 'Wanene ya nada ka alkali ko
shugaba a kanmu?' Shine kuma wanda Allah ya aiko
masu a matsayin shugaba da kuma mai ceto. Allah
ya aiko shi ta hannun mala'ikan da ya gani a daji.
36 Bayan alamu da al'ajibai iri-iri a Masar da kuma

Baharmaliya, Musa ya fito da su daga Masar da kuma
cikin jeji, a lokacin da suka yi tafiya shekara arbain. 37
Wannan shine Musan da ya cewa Isra'ilawa, 'Ubangiji
zai tayar maku da wani annabi kamar ni daga cikin
Yan'uwan ku.' 38 Wannan shine mutumin da ke tare
da mutane a jeji. Karkashin jagorancin mala'ikan
da ya yi magana da shi a dutsen Sinai. Wannan ne
mutumin da ke tare da ubannen mu, wannan shi ne
mutumin da ya ba mu maganar Allah mai rai. 39
Wannan shine mutumin da ubannenmu suka ki su yi
masa biyayya; su ka fitar da shi daga cikinsu, suka
kudurta a zuciyarsu za su koma masar. 40 A lokacin
ne suka cewa Haruna, 'ya yi masu allolin da za su
jagorance su zuwa masar. Domin kuwa ga zancen
Musan nan da ya fito da mu daga Masar, ba mu san
abin da ya faru da shi ba.' 41 Sai suka kera dan maraki
suka kawo wa gunkin hadaya, suka yi murna da abin
da hannayensu suka kera. 42 Allah ya bashe su su
bauta wa tauraran sama, kamar yadda yake a rubuce
cikin littattafafan annabawa, 'Kun mika mani hadayu
na yankakkun dabbobi a jeji ne a shekaru arba'in din
nan ya ku Isra'ilawa?' 43 Kun yarda da haikalin Molek
da kuma tauraron allahn nan Rafem, da kuma siffofin
nan da kuka kera don ku yi masu sujada; don haka zan
kai ku bauta har gaba da Babila.' 44 Kakkaninmu suna
da alfarwa ta sujada domin shaida a cikin jeji, kamar
yadda Allah ya umarta yayin da ya yi magana da
Musa, cewa ya yi shi bisa ga salon da aka nuna mashi.
45 Wannan shine Alfarwar da kakkaninmu suka zo
da shi, a lokacin Joshuwa. Wannan ya faru ne yayin
da suka mallaki wannan kasa ta al'ummai da Allah
ya kora a gaban kakkaninmu. Haka abin yake har ya
zuwa zamanin Dauda, 46 wanda ya sami tagomashi
a wurin Allah; don ya gina masujada domin Allah
na Yakubu. 47 Amma Sulaimanu ne ya gina Gidan
Allah. 48 Sai dai Madaukaki ba yakan zauna a gidan
da hannaye suka gina ba, kamar yadda annabin ya
ce, 49 'Sama kursiyina ce, duniya kuwa wurin ajjiye
sawayena ne. To wane irin gida za ku gina mani? inji
Ubangiji: ko kuwa ina ne wurin da zan huta? 50 Ko ba
hannayena ne suka yi dukan wadannan ba?' 51 Ku
mutane masu taurin kai masu zuciya mara kaciya da
kunnuwa marasa ji, kullum kuna gaba da Ruhu Mai
Tsarki, kuna aikata abin da kakkaninku suka aikata. 52
Wane annabi ne kakkaninku ba su tsanantawa ba? Sun
kashe annabawan da suka rigayi zuwan Mai Adalcin
nan, kuma kun zama wadanda suka kasance masu
bashe shi da masu kashe shi, 53 kune mutanen da kuka
karbi shari'a wadda mala'iku suka bayar, amma ba ku
kiyaye ta ba". 54 Yayin da majalisar suka ji wannan,
sai ransu ya baci kwarai, har suna cizon hakoransu
don gaba da Istifanus. 55 Amma shi, cike da Ruhu Mai
Tsarki, sai ya daga idonsa sama, ya ga daukakar Allah;
ya kuma hango Yesu na tsaye a hannun daman Allah.
56 Istifanus ya ce, "Duba, ina ganin sama ta bude, ga
Dan Mutum na tsaye a hannun dama na Allah." 57
Amma yan majalisar suka daga murya da karfi, suka yi
ihu, suka kuma toshe kunnuwansu, gaba dayansu suka
afka masa; 58 suka fitar da shi bayan gari, suka jejjefe
shi da duwatsu, don shaida sai suka tube manyan
rigunansu suka ajiye a gaban wani matashi da ake ce
da shi Shawulu. 59 Lokacin da suke kan jifan Istifanus,
ya dinga kira yana cewa, ''Ya Ubangiji Yesu, ka karbi
ruhu na." 60 Ya durkusa ya daga murya da karfi, ya ce,
"Ya Ubangiji, kada ka rike wannan zunubi a kansu."
Yayin da ya fadi wannan, sai ya yi barci.

8 Bulus ya amince da mutuwarsa. A wannan rana
tsanani mai zafi ya fara tasowa akan Iklisiya da
take a Urushalima, sai masu bangaskiya duka suka
bazu ko ina a cikin garuruwan Yahudiya da Samariya,
sai manzannin kadai aka bari. 2 Amintattun mutane
suka bizne Istifanus suka yi babban makoki game
da shi. 3 Amma Shawulu ya yi wa Iklisiya mugunta
kwarai, ya dinga shiga gida gida yana jawo mutane
maza da mata, kuma yana kulle su cikin kurkuku. 4
Duk da haka masu bangaskiyar nan da suka warwatsu
suka tafi suka dinga yada wa'azin maganar. 5 Filibus
ya tafi can Samariya ya yi shelar Almasihu. 6 Da taron
mutane suka ji kuma suka ga alamun da Filibus yake
yi, sai suka mai da hankali dukansu domin su ji abinda
yake fadi. 7 Domin kazaman ruhohi sun fito daga
cikin mutane da yawa da suka saurare shi suna kuka
da kururuwa; nakasassun mutane dayawa da guragu
suka warke. 8 Kuma aka yi farin ciki mai girma a
birnin. 9 Amma akwai wani mutum a cikin birnin
da ake kira Siman, wanda tun farko shi masafi ne
da kuma dan dabo, yana yi wa mutanen Samariya
abubuwan ban mamaki, yayin da yake kiran kansa
wani mai muhimmanci. 10 Dukan Samariyawa, manya
da yara, suna sauraronsa, su kan ce, ''Wannan mutum
shine ikon Allahn nan wanda ake kira mai girma.''
11 Suna sauraron sa, domin ya dade yana yi masu
abubuwan mamaki da tsafe-tsafensa. 12 Amma da

suka yi bangaskiya da wa'azin bisharar da Filibus yake
yi game da mulkin Allah da sunan Yesu Almasihu,
sai aka yi masu Baftisma dukansu maza da mata. 13
Har shima Siman da kansa ya ba da gaskiya. Bayan
an yi masa Baftisma ya cigaba da bin Filibus, da ya
ga ana nuna alamu da manyan ayyuka, sai ya yi
mamaki. 14 Da manzannin da ke Urushalima suka ji
labarin Samariya ta karbi maganar Allah, sai suka aika
masu Bitrus da Yahaya. 15 Da suka iso, suka yi masu
addu'a, domin su karbi Ruhu Mai Tsarki. 16 Domin
har wannan lokaci, Ruhu Mai Tsarki bai sauko kan
kowannensu ba; an dai yi masu baftisma ne kadai
cikin sunan Ubangiji Yesu. 17 Sai Bitrus da Yahaya
suka dora masu hannuwansu, sai suka karbi Ruhu Mai
Tsarki. 18 Sa'adda Siman yaga ana bayar da Ruhu Mai
Tsarki ta wurin dorawar hannuwan manzanni, ya basu
kudi. 19 Ya ce, “Ku bani wannan iko, ni ma, don duk
wanda na dora wa hannu ya karbi Ruhu Mai Tsarki.''
20 Amma Bitrus yace masa, ''Azurfarka ta lalace tare
da kai, saboda kana tunanin za ka malaki baiwar
Ubangiji da kudi. 21 Baka da wani rabo a wannan
al'amari, domin zuciyarka ba daidai take da Allah ba.
22 Saboda haka ka tuba daga wannan muguntarka, ka
kuma yi addu'a ga Ubangiji, domin mai yiwuwa ya
gafarta maka game da manufar zuciyarka. 23 Domin
na gane kana cikin bacin rai da kuma cikin daurin
zunubi.'' 24 Siman ya amsa ya ce, ''Kayi addu'a ga
Ubangiji domina, kada wani daga cikin abubuwan
nan da ka fada ya faru da ni.'' 25 Sa'anda Bitrus da
Yahaya suka bada shaida kuma suka fadi maganar
Ubangiji, sun koma Urushalima; akan hanya, suka
yi wa'azin bishara a kauyukan samariyawa da yawa.
26 Yanzu kuwa Mala'ikan Ubangiji ya yi wa Filibus
magana cewa, ''Tashi ka tafi ta kudu da hanyar da
ta yi kasa daga Urushalima zuwa Gaza'' (wannan
hanyar yana cikin hamada.) 27 Ya kuwa tashi ya
tafi. Sai ga wani mutum daga Habasha, baba ne mai
babban matsayi a karkashin Kandakatu, sarauniyar
Habasha. Shine yake mulkin dukan dukiyarta. Ya zo
Urushalima domin ya yi ibada. 28 Yana komawa zaune
cikin karussarsa, kuma yana karanta Littafin annabi
Ishaya. 29 Ruhun ya ce wa Filibus, ''Ka je kusa da
karussar nan.'' 30 Sai Filibus ya gudu ya same shi,
kuma ya ji shi yana karanta littafin annabi Ishaya,
sai ya ce, ''Ka fahimci abin da kake karantawa?'' 31
Bahabashen ya ce. ''Yaya zan iya, idan ba wani ya
bishe ni ba?'' Ya roki Filibus ya shigo cikin karussar
ya zauna tare da shi. 32 Wannan kuwa shine nassin
da Bahabashen yake karantawa, ''An kai shi kamar
tunkiya zuwa mayanka; shiru kuma, kamar dan rago a
hannun masu sosayarsa, bai bude baki ba. 33 Cikin
kaskancinsa aka yi masa shari'a da rashin adalci:
Wa zai bada tarihin tsararsa? Domin an dauke ransa
daga duniya.'' 34 Sai baban ya tambayi Filibus, ya ce,
''Na roke ka, gaya mani, game da wa annabin yake
magana? Da kansa, ko kuwa wani mutum dabam?'' 35
Filibus ya fara magana; akan littafin Ishaya, ya kuwa
yi masa wa'azi akan Yesu. 36 Yayin da suke tafiya
akan hanya, sai suka iso bakin wani kogi; Baban ya ce,
“Duba, ga ruwa anan; me zai hana ayi mani baftisma?”
37 Filibus ya ce,” Idan ka gaskanta da zuciya daya,
ana iya yi maka baftisma.” Sai Bahabashen ya ce,
“Na gaskata Yesu Almasihu shine Dan Allah.” 38 Sai
Bahabashen ya umarta a tsai da karussar. Sai suka zo
wurin ruwa dukan su biyu, Filibus da baban, Filibus
kuwa yayi masa baftisma. 39 Yayin da suka fito daga
cikin ruwan, Ruhun Ubangiji ya dauke Filibus; baban
bai sake ganin shi ba, sai ya ci gaba da tafiyar sa yana
murna. 40 Amma Filibus ya bayyana a Azotus. Ya
ratsa wannan yankin yana wa'azin bishara a dukan
garuruwan, har sa'anda ya iso Kaisariya.

9 Amma Shawulu, ya cigaba da maganganun
tsoratarwa har ma da na kisa ga almajiran Ubangiji,
ya tafi wurin babban firist 2 kuma ya roke shi wasiku
zuwaga majami'un da ke Dimashku, domin idan ya
sami wani da ke na wannan hanya, maza ko mata, ya
kawo su Urushalima a daure. 3 Yayin da yana tafiya,
ya kasance da ya iso kusa da Dimashku, nan da nan sai
ga wani haske daga sama ya haskaka kewaye da shi; 4
Sai ya fadi a kasa kuma yaji wata murya na ce da shi,
''Shawulu, Shawulu, me yasa kake tsananta mani?'' 5
Shawulu ya amsa, ''Wanene kai, Ubangiji?'' Ubangiji
ya ce, ''Nine Yesu wanda kake tsanantawa; 6 amma
ka tashi, ka shiga cikin birnin, kuma za a gaya maka
abinda lallai ne kayi. 7 Mutanen da ke tafiya tare da
Shawulu suka tsaya shiru sun rasa abin fada, suna
sauraron muryar, amma ba su ga kowa ba. 8 Shawulu
ya tashi daga kasa, kuma daga ya bude idanunsa,
baya ganin komai; sai suka kama hannuwansa suka yi
masa jagora suka kawo shi cikin birnin Dimashku.
9 Har kwana uku ba ya kallo, kuma ba ya ci balle
sha. 10 Akwai wani almajiri a Dimashku mai suna
Hananiya; sai Ubangiji ya yi magana da shi cikin

wahayi, ya ce, ''Hananiya.'' Sai ya ce, ''Duba, gani nan
Ubangiji.'' 11 Ubangiji ya ce masa, ''Tashi, ka tafi titin
da ake kira Mikakke, kuma a gidan wani mai suna
Yahuza ka tambaya mutum daga Tarsus mai suna
Shawulu; gama yana addu'a; 12 kuma ya gani cikin
wahayi mutum mai suna Hananiya na shigowa kuma
ya daura masa hannu, domin idanunsa su bude.'' 13
Amma Hananiya ya amsa, ''Ubangiji, na ji labari daga
wurin mutane da yawa game da mutumin nan, da irin
muguntar da ya aikata ga tsarkakan mutanenka da
ke Urushalima. 14 An bashi izini daga babban firist
domin ya kama dukan wanda ke kira bisa sunanka.'' 15
Amma Ubangiji ya ce masa, ''Jeka, gama shi zababben
kayan aiki na ne, wanda zai yada sunana ga al'ummai
da sarakuna da 'ya'yan Isra'ila; 16 Domin zan nuna
masa irin wahalar da zai sha sabo da sunana.'' 17
Sai Hananiya ya tafi, ya shiga gidan. Ya dora masa
hannu a kai, ya ce, ''Dan'uwa Shawulu, Ubangiji Yesu,
wanda ya bayyana a gareka a hanya sa'adda kake
zuwa, ya aiko ni domin ka sami ganin gari ka kuma
cika da Ruhu Mai Tsarki.'' 18 Nan take wani abu
kamar bawo ya fado daga idanun Shawulu, kuma ya
sami ganin gari; ya tashi aka yi masa baftisma; 19
kuma ya ci abinci sai aka karfafa shi. Ya zauna tare
da almajirai a Dimashku kwanaki da yawa. 20 Nan
take ya fara shellar Yesu cikin haikali, yana cewa
shine dan Allah. 21 Dukan wadanda suka saurare shi
suka yi mamaki suka ce ''Ba wannan mutumin ne
yake hallaka mutanen Urushalima da ke kira bisa ga
wannan suna ba? Ya kuma zo nan domin ya ba da su a
daure ga manyan firistoci.'' 22 Amma Shawulu kuwa
ya sami iko sosai, kuma yana haddasa damuwa tare da
rinjaya tsakanin Yahudawan dake zama a Dimashku
ta wurin tabbatar da Yesu shine Almasihu. 23 Bayan
kwanaki da yawa, sai Yahudawan suka yi shiri domin
su kashe shi. 24 Amma shirin su ya zama sananne ga
Shawulu. Suna fakkon sa ta wurin tsaron kofar birnin
dare da rana domin su kashe shi. 25 Amma da tsakar
dare almajiransa suka daukeshi a kwando, suka zurara
shi ta katanga. 26 Sa'adda ya zo Urushalima, Shawulu
ya yi niyyar hada kai da almajirai, amma dukansu
suna tsoronsa, domin ba su yarda cewa shima ya
zama almajiri ba. 27 Amma Barnaba ya dauke shi ya
kawo shi wurin manzannin. Ya kuwa gaya musu yadda
Shawulu ya sadu da Ubangiji a hanya, har Ubangiji ya
yi magana da shi, kuma yadda Shawulu ya yi wa'azi
cikin sunan Yesu gabagadi a Dimashku. 28 Ya sadu da
su lokacin shigar su da fitar su a Urushalima. Ya yi
wa'azi gabagadi cikin sunan Ubangiji Yesu 29 kuma
yana muhawara da Yahudawan Helenanci; amma sun
ci gaba da kokarin kashe shi. 30 Da 'yan'uwa suka
gane haka, sai suka kawo shi Kaisariya, suka kuwa
tura shi zuwa Tarsus. 31 Sa'annan iklisiya dake dukan
kasar Yahudiya, Galili da kuma Samariya suka sami
salama da kuma ginuwa; suka kuwa ci gaba da tafiya
cikin tsoron Ubangiji, da kuma ta'aziyar Ruhu Mai
Tsarki, iklisiyar kuwa ta karu da yawan mutane. 32
Har ta kai, yayin da Bitrus ya zaga dukan yankin
kasar, ya dawo wurin masu bi dake zama a garin
Lidda. 33 A can kuwa ya sami wani mutum mai suna
Iniyasu, wanda yake shanyayye ne, yana kwance har
tsawon shekara takwas a kan gado. 34 Bitrus ya ce
masa, ''Iniyasu, Yesu Almasihu ya warkar da kai. Tashi
ka nade shimfidarka.'' Nan take sai ya mike. 35 Sai
duk mazauna kasar Lidda da kasar Sarona suka ga
mutumin, suka kuma juyo ga Ubangiji. 36 Yanzu kuwa
a Yafa akwai wata almajira, mai suna Tabita, ma'ana
''Dokas.'' Wannan matar kuwa tana chike da ayyukan
nagarta da halin tausayi da take yi ga mabukata. 37 Ya
kai ga cewa a kwanakin can ta yi rashin lafiya har ta
mutu; da suka wanke gawar ta suka kwantar da ita a
bene. 38 Da shike Lidda na kusa da Yafa, almajiran
kuma sun ji cewa Bitrus yana can, suka aika mutane
biyu wurinsa. Suna rokansa, ''Ka zo garemu ba tare da
jinkiri ba.'' 39 Bitrus ya tashi ya tafi da su, da isowar
sa, suka kai shi benen. Sai dukan gwamrayen suka
tsaya kusa da shi suna kuka, sai suka dauko riguna
da sutura da Dokas ta dinka lokacin da take tare da
su. 40 Bitrus ya fitar da su duka daga cikin dakin, ya
durkusa, ya yi addu'a; sai, ya juya wurin gawar, ya ce,
''Tabita, tashi.'' Ta bude idanunta, da ta ga Bitrus ta
zauna, 41 Bitrus kuwa ya mika hannunsa ya tashe ta;
sa'annan ya kira masu bi da gwamrayen, ya mika ta a
raye garesu. 42 Wannan al'amari ya zama sananne
cikin dukan Yafa, kuma mutane da yawa suka bada
gaskiya ga Ubangiji. 43 Ya kasance, cewa, Bitrus ya
zauna kwanaki da dama a Yafa tare da wani mutum
mai suna Saminu, majemi.

**10** An yi wani Mutum a birnin Kaisariya, mai suna
Karniliyas, shugaban sojoji ne na kungiyar da
ake kira Italiya. 2 Mutum ne mai ibada, wanda ya
mika kansa da iyalinsa ga bautar Allah; ya kan bada
taimakon kudi mai yawa ga Yahudawa, kuma yana

addu'a ko yaushe ga Allah. 3 Wajen sa'a ta tara ga yini,
an bayyana masa cikin wahayi mala'kan Ubangiji na
zuwa gare shi sai mala'ikan ya ce masa, ''Karniliyas!''
4 Karniliyas ya zuba wa mala'ikan ido a tsorace ya ce
''Menene, mai gida?'' mala'ikan ya ce masa, ''Addu'ar
ka da taimakon ka ga talakawa ya kai sama matsayin
sadaka abin tunawa a gaban Allah, 5 ''Yanzu ka aika
mutane zuwa birnin Yafa su kawo mutum mai suna
Saminu wanda ake kira Bitrus. 6 Yana zama tare da
Saminu majemi, wanda gidansa ke bakin teku. 7 Da
mala'ikan da ya yi magana da shi ya tafi, Karniliyas ya
kira biyu daga barorin gidansa, da kuma soja guda mai
bautar Allah daga cikin sojojin da suke masa hidima.
8 Karniliyas ya fada masu dukan abin ya faru sai ya
aike su Yafa. 9 Washe gari wajen sa'a ta shida (tsakar
rana) suna cikin tafiya da suka yi kusa da birni, Bitrus
ya hau kan bene don ya yi addu'a. 10 Sai ya ji yunwa
kuma yana bukatar wani abinda da zai ci, amma a
yayin da mutanen na dafa abinci, sai ya ga wahayi.
11 Sai ya ga sararin sama ya bude kuma wani tasa
na saukowa, wani abu kamar babban mayafi yana
saukowa zuwa duniya, ana zuro shi ta kusuryoyinsa
hudu. 12 A cikinsu kuwa akwai dukan halitun dabbobi
masu kafa hudu da kuma masu rarrafe a duniya da
tsunstayen sama. 13 Sai murya ta yi magana da shi;
“Tashi, Bitrus, yanka ka ci '' 14 Amma Bitrus ya ce ''Ba
haka ba, Ubangiji, gama ban taba cin abu mara tsarki
ko mai kazanta ba.” 15 Amma muryar ta sake zuwa
masa karo na biyu kuma; “Abinda Allah ya tsarkake,
kada ka kira shi kazantacce.” 16 Wannan ya faru sau
uku; nan da nan sai aka dauki tasar zuwa sama. 17
A yayin da Bitrus na cikin rudani game da ma'anar
wahayin da ya gani, sai ga mutanen da Karniliyas
ya aika suna tsaye a bakin kofar gidan, bayan sun
tambayi hanyar zuwa gidan, 18 Kuma suka yi sallama
suna tambaya ko Saminu wanda ake kira Bitrus ya
sauka a nan. 19 A yayin da Bitrus yana kan tunani akan
wahayin, Ruhu ya ce masa, “Duba, mutane uku na
neman ka.” 20 Tashi ka sauka ka tafi tare da su. Kada
ka yi jinkirin tafiya tare da su, domin Nine na aike
su.” 21 Bitrus kuwa ya sauko wurin mutanen ya ce,
“Ni ne wanda kuke nema. Me ya sa kuka zo?” 22 Suka
ce, “Shugaban soja mai suna Karniliyas, adalin mutum
kuma mai bautar Allah, yana da kyakkyawar shaida a
dukan al'umman Yahudawa, shi ne wanda mala'ika
mai tsarki na Allah ya aika domin ka zo gidansa, ya ji
sako daga wurinka.” 23 Sai Bitrus ya gayyace su su zo
ciki kuma su zauna tare da shi. Washegari sai ya tafi
tare da su, kuma wadansu 'yan'uwa daga Yafa suka
raka shi. 24 Kashegari suka shiga Kaisariya, Karniliyas
kuwa yana jiran su; har ma ya gayyaci 'yan'uwansa
da kuma abokansa na kusa. 25 Ya kasance sa'adda
Bitrus ya shiga, Karniliyas ya sadu da shi kuma ya
durkusa ya yi masa sujada. 26 Amma Bitrus ya tashe
shi yana cewa, “Tashi tsaye! Ni ma mutum ne.” 27
A lokacin da Bitrus yake magana da shi, ya shiga
ciki sai ya tarar da mutane da yawa sun taru a wuri
daya. 28 Ya ce masu, “Ku da kanku kun sani bai dace
Bayahuden mutum ya yi ma'amulla ko ya ziyarci wani
ko wata kabila ba. Amma Allah ya ce da ni kada in ce
da kowa mara tsarki ko kazantacce. 29 Wannan shine
yasa na zo ba tare da musu ba, a lokacin da kuka kira
ni. Don haka na tambaye ku me ya sa kuka aika in
zo.” 30 Karniliyas ya ce “Kwanaki hudu da sun wuce
a daidai wannan lokaci, ina addu'a da cikin sa'a na
tara (karfe uku) a gidana, sai na ga mutum tsaye a
gabana da tufafi mai haske. 31 Ya ce, “Karniliyas, Allah
ya ji addu'ar ka, kuma taimakon ka ga talakawa ya
tuna ma Allah da kai. 32 Saboda haka ka aika da wani
Yafa, ya kira maka mutum mai suna Saminu wanda
ake kira Bitrus. Yana zama a gidan Saminu majemi,
da ke bakin teku. 33 [Idan ya zo, zai yi magana da
kai.] 34 Sai Bitrus ya bude bakinsa ya ce, “Gaskiya,
na fahimci Allah baya nuna bambanci. 35 Maimakon
haka, cikin kowace al'umma duk mai ibada kuma mai
aikata adalci karbabbe ne a gare shi. 36 Ku kun san
sakon da ya aika wa mutanen Isra'ila, a lokacin da
ya sanar da labarin mai kyau na salama ta wurin
Yesu Kristi, wanda shine Ubangiji na duka. 37 Ku da
kanku kun san al'amuran da suka kasance, wanda
ya faru cikin Yahudiya, farawa daga Galili, bayan
sanarwar baftismar da Yahaya ya yi. 38 Al'amura game
da Yesu Banazare, yadda Allah ya kebe shi da Ruhu
Mai Tsarki da iko kuma. Ya kuma ci gaba da aikin
alheri da warkarwa ga dukan wadanda shaidan ya
daure, domin Allah yana tare da shi. 39 Mu shaidu ne
ga dukan abubuwan da ya yi a kasar Yahudawa da
cikn Urushalima, wannan Yesu wanda suka kashe, ta
wurin giciye shi a akan itace. 40 Wannan mutumin,
Allah ya ta da shi rana ta uku ya kuma maishe shi
sananne, 41 ba ga dukan mutane ba, amma ga shaidun
da Allah ya zaba tun da farko - mu kanmu, wadanda
muka ci muka sha tare da shi bayan tashin sa daga
matattu, 42 Ya umarce mu mu yi wa mutane wa'azi

mu kuma tabbatar cewa shine wanda Allah ya zaba ya
yi shariya bisa masu rai da matattu. 43 Gareshi ne
dukan annabawa suka yi shaida, domin dukan wanda
ya bada gaskiya gareshi ya sami gafarar zunubai ta
wurin sunansa.` 44 Sa'adda Bitrus yana kan magana
game da wadannan abubuwa, Ruhu Mai Tsarki ya
sauko a kan dukan wadanda suke sauraron wa'azin sa.
45 Mutanen da ke kungiyar masu bi da suka yarda da
kaciya, dukan wadanda suka zo tare da Bitrus suka yi
mamaki, domin baiwar Ruhu Mai Tsarki ya sauko a
kan al'ummai. 46 Domin sun ji al'umman nan suna
magana da wasu harsuna suna yabon Allah. Sai Bitrus
ya amsa, 47 "Ko akwai wanda zai hana wa wadannan
baftisma ta ruwa, da shike suma sun karbi Ruhu Mai
Tsarki kamar mu?" 48 Sai ya ba da umarni a yi masu
baftisma cikin sunan Yesu Kristi. Sai suka roke shi ya
kasance da su na wasu kwanaki.

**11** Yanzu Manzani da 'yan'uwa wadanda suke cikin
Yahudiya suka ji cewa al'ummai ma sun karbi
maganar Allah 2 Lokacin da Bitrus ya je Urushalima,
wadanda suke na kaciya suka zarge shi; 3 suka ce, "Ka
hada kai tare da mutane marasa kaciya kana ci tare da
su!" 4 Amma Bitrus ya fara bayyana masu dalla-dalla;
ya ce, 5 Ina addu'a a cikin birnin Yafa, sai na ga wahayi
game da taska yana saukowa, kamar babban mayafi
da aka saukar daga sama ta kusurwan nan hudu. Ya
sauko gabana. 6 Na zura masa ido kuma na yi tunani
a kansa, na ga dabbobi masu kafa hudu na duniya,
miyagun dabbobi, da masu rarrafe, da tsuntsayen
sama. 7 Sai na ji murya tana ce da ni, "Tashi, Bitrus,
yanka ka ci." 8 Na ce, "Ba haka ba, Ubangiji: gama
babu abu mara tsarki ko mai kazanta da ya taba shiga
bakina." 9 Amma murya ta amsa kuma daga sama
cewa, "Abin da Allah ya kira mai tsarki, kada ka kira
shi mara tsarki." 10 Wannan ya faru sau uku, sai dukan
komai ya koma sama. 11 Nan da nan sai ga mutane
uku tsaye a gaban gidan da muke; an aike su daga
Kaisariya zuwa gare ni. 12 Ruhun ya umurce ni in tafi
tare da su, ba tare da nuna banbanci game da su ba.
Yan'uwan nan shida sun tafi tare da ni, sai muka shiga
gidan mutumin. 13 Ya fada mana yadda ya ga mala'ika
tsaye a cikin gidansa yana cewa "Aiki mutane zuwa
Yafa, su kirawo Saminu wanda ake kira Bitrus. 14 Zai
gaya maku sakon da za ku sami ceto kai da dukan
gidanka." 15 Da na fara magana da su, Ruhu Mai
Tsarki ya sauko akansu kamar yadda ya sauko mana
tun da farko. 16 Sai na tuna da maganar Ubangiji,
yadda ya ce,"Hakika Yahaya ya yi baptisma da ruwa,
amma ku za a yi maku baptisma da Ruhu Mai Tsarki."
17 To, idan Allah ya yi masu baiwa kamar yadda ya yi
mana yayin da muka bada gaskiya ga Ubangiji Yesu
Almasihu, wane ni da zan yi jayayya da Allah? 18 Da
suka ji wadannan abubuwa, suka rasa ta cewa, amma
suka daukaka Allah suka ce "Ga al'ummai ma Allah ya
basu tuba zuwa rai." 19 Sai wadanda suka warwatsu
saboda tsananin da ya bi bayan mutuwan Istifanas,
suka yadu har zuwa Finikiya, Kuburus da Antakiya,
amma suka yi wa'azin Yesu ga Yahudawa kadai. 20
Amma wadan sunsu, mutane daga Kuburus da Kurane,
suka zo Antakiya suka yi magana da hellenawa, suna
yi masu wa'azin Ubangiji Yesu. 21 Kuma ikon Ubangiji
yana tare da su, har mutane da yawa suka gaskata
kuma suka juyo wurin Ubangiji. 22 Labari game da su
ya iso kunnen ikilisiya da ke Urushalima: sai suka aika
da Barnaba zuwa can Antakiya. 23 Da ya iso kuma
ya ga kyautar Allah, sai ya yi farinciki; ya karfafa su
dukka su kafu cikin Ubangiji da dukan zuciyar su.
24 Domin shi mutumin kirki ne, cike kuma da Ruhu
Mai Tsarki da bangaskiya, sai mutane da yawa suka
karu ga Ubangiji. 25 Sai Barnaba ya tafi Tarsus domin
ya nemi Shawulu. 26 Da ya same shi, ya kawo shi
Antakiya. Ya kasance, shekara guda suna taruwa tare
da ikilisiya suka koyar da mutane da yawa. A Antakiya
ne aka fara kiran almajiran Krista. 27 A cikin kwanakin
nan wadansu annabawa daga Urushalima suka zo
Antakiya. 28 Daya daga cikinsu, mai suna Agabas ya
mike tsaye yayi magana da ikon Ruhu cewa za a yi
tsanani fari ko'ina a duniya. Wannan ya faru ne a
zamanin Kalaudiya. 29 Sai, almajiran, suka dau niyya
kowa gwargwadon karfinsa, su aika wa 'yan'uwa da ke
Yahudiya da taimako. 30 Suka yi haka; sun aika wa
dattawa da kudi ta hanun Barnaba da Shawulu.

**12** A lokacin nan Sarki Hiridus ya sa wa wasu masu
bi hannu domin ya musguna masu. 2 Ya kashe
Yakubu dan'uwan Yahaya da takobi. 3 Bayan da ya ga
hakan ya gamshi Yahudawa, sai ya kama Bitrus ma.
4 Bayan ya kama shi, sai ya tsare shi a kurkuku ya
kuwa sa sojoji hudu su dinga tsaron sa; yana niyyar
kawo shi gaban mutanen a bayan Idin katarewa. 5 To,
Bitrus na tsare a kurkuku, amma 'yan'uwa na iklisiya
suna yin addu'a ga Allah sosai domin sa. 6 Ana kamar
gobe Hiridus zai fitar da shi, a wannan daren, Bitrus

yana barci a tsakanin sojoji biyu, daure da sarkoki
biyu; sojoji kuma na gadi a bakin kurkukun. 7 Ba zato,
sai ga mala'ikan Ubangiji ya bayyana a gareshi, haske
ya haskaka dakin. Ya taba Bitrus a gefe ya tashe shi
kuma ya ce, “Tashi da sauri.” Sai ga sarkokin suka
zube daga hannunsa. 8 Mala'ikan ya ce masa, “Yi
damara ka sa takalmanka.” Bitrus kuwa yayi haka.
Mala'ikan ce ma sa, “Yafa mayafinka, ka biyo ni.” 9
Bitrus kuwa ya bi mala'ikan suka fita waje. Bai gane
abin da mala'ikan ke yi zahiri ne ba. Yana zaton ko
yana ganin wahayi ne. 10 Bayan da suka wuce masu
tsaron fari da na biyu, sun kai kofar da aka yi da
karfe wadda ta mike zuwa cikin gari; ta bude masu da
kanta. Suka fita sun bi titin, kuma nan take kuma sai
mala'ikan ya bar shi. 11 Da Bitrus ya komo hayyacin
sa, ya ce, “Hakika yanzu na gane Ubangiji ya aiko
da mala'ikansa don ya kubutar da ni daga hannun
Hiridus da abin da Yahudawa suke zato.” 12 Da ya
gane haka, ya zo gidan Maryamu mahaifiyar Yahaya
wanda sunan mahaifinsa Markus; masu bi da yawa
sun taru a can suna addu'a. 13 Da ya kwankwasa kofar
gidan, sai baiwar gidan mai suna Roda ta zo don ta
bude kofar. 14 Da ta gane muryar Bitrus, don farin
ciki ta kasa bude kofar; maimakon haka, ta koma daki
a guje, don ta basu labari Bitrus na tsaye a bakin kofa.
15 Suka ce mata, “Kin haukace.” Amma ta nace da
cewa haka ne. Suka ce, “Mala'ikansa ne.” 16 Amma
Bitrus ya ci gaba da kwankwasawa, da suka bude
kofar, sai suka ga ai shine, suka sha mamaki kwarai.
17 Bitrus kuwa ya yi masu hannu yana, masu alama su
yi shuru. Sai ya gaya masu labarin yadda Ubangiji ya
kubutar da shi daga kurkukun. Ya ce, “Ku gaya wa
Yakubu da dukan 'yan'uwa abin da ya faru.” Sai ya
bar su, ya tafi wani wuri. 18 Sa'anda gari ya waye ba
karamar hargowa ce ta tashi a cikin sojojin ba, game
da abin da ya faru da Bitrus. 19 Bayan da Hiridus
ya neme shi kuma bai same shi ba, sai ya tambayi
masu tsaron kuma ya bada umarni a kashe su. Sai ya
gangara daga Yahudiya zuwa Kaisariya ya yi zamansa
a can. 20 Yanzu kuwa Hiridus ya yi fushi sosai da
mutanen Taya da Sidon. Suka tafi wurinsa tare. Suka
roki Bilastasa, mataimakin sarkin, ya taimake su. Sai
suka nemi sasantawa don suna samun abinci daga
kasarsa ne. 21 A ranan da aka kayyade, Hirudus ya
sha damara da kayan saurata kuma ya zauna akan
kursiyi; ya yi masu jawabi. 22 Mutanen suka yi ihu,
“Wannan muryar allahce, ba ta mutum ba!” 23 Nan
take mala'ika Ubangiji ya buge shi don bai ba Allah
daukaka ba, nan take tsutsotsi suka cinye shi har ya
mutu. 24 Maganar Allah ta yadu tana ta ribabbanya.
25 Bayan Barnaba da Shawulu sun gama aikin su a
Urushalima. Suna dawowa, suka zo tare da Yahaya
wanda sunan mahaifinsa Markus ne. [Barnaba da
Shawulu suka koma Urushalima.]

13 A cikin iklisiyar da take Antakiya, akwai
annabawa da malamai. Sune su Barnabas, Saminu
(wadda ake kira Baki) da Lukiya Bakurame da Manayin
(wanda aka yi renon su tare da sarki Hiridus mai
mulki) da Shawulu. 2 Sa'adda suke bauta wa Allah
tare da azumi, sai Ruhu Mai Tsarki ya ce, “Ku kebe
mani Barnaba da Shawulu domin aikin da na kiraye
su”. 3 Bayan taron sun yi addu'a da azumi, sai suka sa
masu hannu, su suka sallame su. 4 Sai Shawulu da
Barnabas suka yi biyayya da Ruhu Mai Tsarki suka tafi
Sulukiya; daga nan suka ketare zuwa tsibirin Kuburus.
5 Sa'adda suke garin Salami, suka koyar da maganar
Ubangiji a majami'un Yahudawa, suna kuma tare da
Yahaya Markus mai taimakonsu. 6 Bayan sun zaga
tsibirin duka har Bafusa, nan suka iske wani Bayahude
mai suna Bar-yeshua mai tsafi kuma annabin karya. 7
Wannan mai tsafin wanda ke tare da Makaddas, shi
Sarjus Bulus mutum mai basira ne. Wannan kuwa
ya kira Shawulu da Barnaba domin yana so ya ji
maganar Allah. 8 Amma Elimas “mai tsafi” (fasarar
sunansa kenan) ya yi adawa da su; yana so ya baudar
da Makaddashin daga bangaskiya. 9 Amma Shawulu
wanda ake ce da shi Bulus yana cike da Ruhu Mai
Tsarki ya kafa masa ido. 10 Sai ya ce, “Kai dan iblis,
kana cike da kowace irin yaudara da mugunta. Kai
abokin gabar kowanne irin adalci ne. Ba za ka daina
karkata mikakkakun hanyoyin Ubangiji ba? 11 Yanzu
ga hannun Ubangiji bisa kanka, zaka zama makaho.
Ba za ka ga rana ba nan da dan lokaci.” Nan take kuwa
sai wani hazo da duhu suka rufe shi ya fara yawo
yana neman mutane su yi masa jagora. 12 Bayan da
Makaddashin ya ga abin da ya faru ya ba da gaskiya
saboda ya yi mamakin koyarwa game da Ubangiji. 13
Bulus da abokansa suka shirya suka ketare a jirgin
ruwa daga Bafusa zuwa Firjiya a Bamfiliya. Amma
Yahaya ya bar su ya koma Urushalima. 14 Bulus da
abokansa suka tafi daga Firjiya zuwa Antakiya na
kasar Bisidiya. Nan suka shiga majami'a ran Asabaci
suka zauna. 15 Bayan karatun dokoki da annabawa,

shugabanin iklisiyar suka tura sako cewa, “'Yan'uwa,
idan kuna da wani sakon karfafawa ga jama'a ku fadi.”
16 Bulus kuwa ya tashi ya yi alama da hannunsa ya
ce, “Mutanen Isra'ila da ku wadanda kuke girmama
Allah, ku ji. 17 Allahn Isar'ila ya zabi kakkaninmu
ya kuma ribabbanya su sa'adda suke kasar Masar da
kuma madaukakin iko ya fito da su daga cikinta. 18 Ya
yi hakuri da su a jeji har na tsawon shekara arba'in.
19 Bayan ya hallaka kasashe bakwai a kasar Kan'ana,
ya ba kakkaninmu kasar nan gado. 20 Duk wadanan
abubuwan sun faru shekaru dari hudu da hamsin da
suka wuce. Bayan wadannan, Allah ya ba su alkalai
har sai da annabi Sama'ila ya zo. 21 Sai jama'a suka
roka a ba su sarki, Allah kuwa ya ba su Saul dan
Kish, mutumin kabilar Binyamin ya zama sarki har na
tsawon shekara arba'in. 22 Allah kuwa ya cire shi daga
kan kujerar sarauta, ya daga Dauda ya zama sarkinsu.
A kan Dauda ne Allah ya ce, 'Na sami Dauda dan Yessi,
mutumin da zuciyata ke so; zai yi duk abin da nake
so'. 23 Daga zuriyar mutumin nan Allah ya fito da
mai ceto, Yesu, kamar yadda aka alkawarta zai yi. 24
Wannan ya faru kafin Yesu ya zo, Yahaya ya yi shelar
baftimar tuba ga jamma'ar Isra'ila. 25 Sa'adda Yahaya
ya gama aikin sa, sai ya ce, 'Wanene ni a tsamanin
ku? Ba nine shi ba. Amma ku saurara, akwai wani mai
zuwa bayana wanda maballin takalminsa ban isa in
kwance ba.' 26 Yan'uwa 'ya'ya daga zuriyar Ibrahim,
da wadanda ke bautar Allah a cikinku, saboda mune
aka turo sakon ceto. 27 Saboda wadanda ke zaune
cikin Urushalima, da masu mulkinsu, ba su gane shi
ba, kuma sun cika fadin annabawa da a ke karantawa
kowace ranar Asabaci ta wurin kashe shi. 28 Duk da
cewa ba su sami dalilin mutuwa a kansa ba, suka
roki Bilatus ya kashe shi. 29 Bayan sun gama duk
abin da aka rubuta game da shi, sai suka sauke shi
daga giciye suka sa shi a cikin kabari. 30 Amma Allah
ya tashe shi daga matattu. 31 Mutanen da suka zo
tare da shi daga Galili da Urushalima kuwa suka yi
ta ganinsa har kwanaki da yawa. Wadanan mutane
kuma sune shaidunsa ga jama'a a yanzu. 32 Mun kawo
maku labari mai dadi game da alkawaran da aka yi
wa kakkaninmu. 33 Ubangiji ya bar mana alkawaran.
Don haka ya ta da Yesu daga matattu. Kamar yadda
ya ke a littafin zabura ta biyu: ''Kai da na ne yau
na zama mahaifinka.'' 34 Kuma dalilin tayar da shi
daga matattu shine saboda kada jikinsa ya rube, ya
yi magana kamar haka: ''Zan baku albarkun Dauda
masu tsarki tabatattu.'' 35 Wannan shine dalilin da
ya yi magana kuma a wata Zabura, 'Ba za ka bar Mai
Tsarkinka ya rube ba.' 36 Bayan Dawuda ya yi wa
Allah bauta a cikin zuciyarsa da kuma abin da Allah
yake so, ya mutu, aka binne shi tare da kakkaninsa, ya
kuma ruba, 37 amma wanda Allah ya tayar bai ga ruba
ba. 38 'Yan'uwa, ku sani cewa ta wurin mutumin nan
aka yi maku wa'azin gafarar zunubai. 39 Ta wurinsa
ne duk wanda ya ba da gaskiya zai kubuta daga dukan
abin da dokar Musa bata 'yantar da ku a kai ba. 40
Saboda haka ku yi hankali da abubuwan da annabawa
suka fada kada su faru a kanku: 41 'Ku masu reni,
za ku rude don mamaki, ku kuma shude; saboda ina
aiki a cikin kwananakinku, aikin da ba za ku yarda ba
ko da wani ya gaya maku.” 42 Da Bulus da Barnaba
suna fita kenan, sai jama'a suka rokesu, su sake yin
irin wannan magana ranar Assabaci mai zuwa. 43
Bayan da sujadar ta kare, Yahudawa da yawa da kuma
wadanda suka shiga addinin Yahudanci suka bi Bulus
da Barnaba, sai suka gargade su da su cigaba da aikin
alherin Allah. 44 Da Asabaci ta kewayo, kusan dukan
garin suka taru domin su ji maganar Ubangiji. 45
Sa'adda Yahudawa suka ga taron jama'a, sai suka cika
da kishi suna karyata abubuwan da Bulus ya fada suka
kuma aibata shi. 46 Amma Bulus da Barnaba sun yi
magana gabagadi suka ce, “Dole ne a fara fada maku
maganar Allah. Amma da yake kun ture ta, kun nuna
baku cancanci rai madawwami ba soboda haka zamu
juya ga al'ummai. (aiōnios g166) 47 Don haka Ubangiji ya
umarce mu, cewa, 'Na sa ku haske ga al'ummai, saboda
ku kawo ceto ga iyakar duniya.'” 48 Da al'ummai suka
ji haka, sai suka yi murna suka kuma yabi kalmar
Ubangiji. Dukan wadanda aka kaddarawa samin rai
madawwami suka tuba. (aiōnios g166) 49 Kalmar Ubangiji
kuwa ta bazu a kowanne bangaren yankin. 50 Amma
Yahudawan suka zuga wadansu mata masu sujada,
masu daraja da kuma shugabannin mazan garin.
Wannan ya tayar da tsanani ga Bulus da Barnaba har
suka fitar da su daga iyakar garinsu. 51 Amma Bulus
da Barnaba suka kade masu kurar kafarsu. Suka tafi
garin Ikoniya. 52 Amma almajiran suka cika da farin
ciki da kuma Ruhu Mai Tsarki.

14 A lokacin da Bulus da Barnaba sun shiga garin
Ikoniya suka shiga majami'an Yahudawa suka
yi wa'azi yadda har mutane da yawa daga cikin
Yahudawa da Hellinawa suka ba da gaskiya. 2 Amma
Yahudawa da basu yi biyayya ba, suka zuga al'umman

har suka yi fushi da 'yan'uwan. 3 Suka zauna a wurin
na tsawon lokaci, suna yni maganarsu gabagadi da
ikon Ubangiji, yana kuma shaidar sakon alherinsa.
Ya yi wannan ta wurin alamu da al'ajibai ta hannun
Bulus da Barnaba. 4 Saboda haka mutanen garin
sun rabu: wadansun su suka bi ra'ayin Yahudawa,
wasu kuwa sun bi manzannin. 5 Al'umman garin da
Yahudawa sun nemi jan hankali shugabanninsu, don
su wulakanta Bulus da Barnaba, su jajjefe su, 6 da
suka gane haka suka gudu zuwa biranen Likoniya,
Listira da Darbe, da garuruwa wadanda ke kewaye da
su, 7 a can suka yi wa'azin bishara. 8 A Listira akwai
wani wanda ke zaune bai taba tashi da kafafunsa
ba, don shi gurgu ne tun daga haihuwa. 9 Wannan
mutumin ya ji Bulus yana magana. Bulus ya kafa
masa ido, ya gane mutumin na da bangaskiya da za a
warkar da shi. Sai ya ce masa da murya mai karfi,
“Tashi ka tsaya akan kafafunka” 10 Sai mutumin ya yi
tsalle ya fara tafiya da kafafunsa, yana yawo. 11 Da
jama'an garin sun ga abin da Bulus ya yi, suka tada
muryarsu suna cewa da Likoniyanci, “Ai alloli sun
ziyarce mu daga sama, da kamanin mutane.” 12 Suna
kiran Barnaba da sunan “Zafsa,” Bulus kuwa suka kira
shi da sunan “Hamisa” domin shine yafi yin magana.
13 Sai firist din zafsa wanda dakin yin masa sujada na
kofar birni; ya kawo bijimai biyu da furannin da aka
saka su kamar gammo; shi da jama'arsa suna so su yi
masa hadaya. 14 Amma da manzannin, wato Barnaba
da Bulus, su ka ji labarin, suka yage rigunansu, suka
hanzarta zuwa gun taron mutanen. 15 Suna ta cewa,
“Kuji! Ku mutane don me kuke wannan abin? Mu
fa mutane ne kamarku. Mun kawo maku labari mai
dadi ne, da cewa, ku rabu da abubuwa marar amfani,
ku koma ga Allah mai rai, wanda ya hallici sama da
kasa da teku da dukan abubuwa da ke cikinsu. 16 A
da dai ya bar mutane su yi abinda suka ga dama. 17
Duk da haka, bai bar kansa ba tare da shaida ba, don
yana bada abubuwa masu kyau, yana ba ku ruwan
sama, lokatai masu albarka, ya cika ranku da abinci
da farin ciki.” 18 Duk da wadannan kalmomin da kyar,
Bulus da Barnaba suka iya tsayar da su daga yi masu
hadaya. 19 Amma wasu Yahudawa daga Antakiya da
wasunsu daga Ikoniya suka rinjayi tarun jama'ar. Suka
jajjefi Bulus suka ja shi zuwa wajen garin, suna ganin
kamar ya mutu. 20 Duk da haka da almajirai suka
kewaye shi a tsaitsaye, sai ya tashi ya koma cikin
garin. Washegari, ya tafi Darba tare Barnaba. 21 Bayan
sun yi wa'azin bishara a wannan birnin suka kuma
sami almajirai da yawa, suka dawo Listira, da Ikoniya
da Antikiya. 22 Suna karfafa zuciyar almajiran su rike
bangaskiyarsu, su ci gaba da ita, suna ce masu, “Ta
wurin jimrewa mai yawa zamu shiga mulkin Allah,
don haka dole ne mu sha wahala.” 23 Da suka zabar
masu dattawa a kowace iklisiya, sai suka yi addu'oi
da azumi, suka mika su ga Ubangiji, ga wanda suka
gaskanta a gareshi. 24 Sa'annan sun bi ta Bisidiya
suka kai Bamfiliya. 25 Da suka yi maganarsu a Biriya,
sun wuce zuwa har Italiya. 26 Ta jirgin ruwa zuwa
Antakiya, a nan ne aka mika su ga alherin Allah don
aikin da suka gama a yanzu. 27 Da isowarsu Antakiya
sun tara 'yan iklisiya a wuri daya, sun ba da labarin
dukan abin da Allah ya yi ta wurinsu. Da yadda Ya
bude kofa a wurin al'ummai ta bangaskiya. 28 Sun
zauna tare da almajiran na tsawon lokaci.

15 Wadansu mutane suka zo daga Yahudiya suka
koyar da 'yan'uwa, cewa, “Idan ba yi maku kaciya
bisa ga al'addar Musa ba, ba za ku sami ceto ba.” 2 Da
Bulus da Barnaba suka tunkare su da mahawara, sai
'yan'uwa suka yanke shawara Bulus da Barnaba da
wasu su je Urushalima wurin manzanni da dattawa a
kan wannan magana. 3 Da shike iklisiya ce ta aike su,
sai suka bi ta Finikiya da ta Samariya suka sanar da
tuban al'ummai. Ya kawo murna mai yawa a wurin
'yan'uwa. 4 Bayan sun zo Urushalima, sai iklisiya
da manzanni da dattawa, suka marabce su, sai suka
fada masu abin da Allah ya yi ta wurinsu. 5 Amma
wadansu mutane wadanda suka ba da gaskiya daga
cikin Farisawa, suka tashi suka ce, “Dole ne a yi masu
kaciya a kuma umarce su su kiyaye dokar Musa.” 6
Sai manzanin da dattawan suka taru don su duba
wannan lamari. 7 Bayan mahawara mai tsanani, sai
Bitrus ya tashi ya ce masu, “'Yan'uwa, kun san lokacin
baya da ya wuce, Allah ya yi zabi a cikinku, cewa ta
bakina ne al'ummai za su ji bishara, su kuma ba da
gaskiya. 8 Allah, wanda ya san zuciya, ya yi masu
shaida, ya kuma basu Ruhu Mai Tsarki kamar yadda
ya yi mana; 9 kuma bai bambanta mu da su ba,
ya tsabtace zuciyarsu ta wurin bangaskiya. 10 To,
saboda haka don me kuke gwada Allah, kuna sa wa
almajirai nauyi a wuya wanda ubanninmu duk da
mu ba mu iya dauka ba? 11 Amma mun gaskanta za
mu samu ceto ta wurin alherin Ubangiji Yesu, kamar
yadda suke.” 12 Dukan taron jama'ar suka yi shiru

sa'adda suke sauraron sakon shaidar da mamakin
abin da Allah ya yi ta wurin Bulus da Barnaba a cikin
al'ummai. 13 Bayan sun gama magana, Yakubu ya
amsa, ya ce, “'Yan'uwa, ku ji ni. 14 Saminu ya fada
yadda Allah ya fara nuna jinkai ga al'ummai domin ya
dauke jama'a daga cikinsu domin sunansa. 15 Maganar
annabawa ta yarda da wannan, kamar yadda yake a
rubuce, 16 'Bayan wadannan abubuwa zan dawo, zan
gina gidan Dauda wanda ya fadi kasa; in sake gina
bangonsa, in tsayar da shi, 17 saboda sauran jama'a su
nemi fuskar Ubangiji, har da al'ummai da ake kira da
sunana. 18 Wannan shine abin da Ubangiji ya fadi,
shi wanda ya yi wadannan abubuwa da aka sani tun
zamanin da. (aiōn g165) 19 Saboda haka, a gani na kada
mu matsa wa al'umman da suka juyo gun Allah; 20
amma zamu rubuta masu da cewa, su guje wa gumaka
da zina da faskanci da maye da cin mushe. 21 Tun
zamanin da akwai mutane a kowanne birni wadanda
suke wa'azi da karatun Musa a majami'u kowanne
Asabaci.” 22 Sai ya yi wa manzanin kyau su da dattawa
da dukan iklisiyar su zabi Yahuza da Barnaba da Sila
da dattawan iklisiya a tura su Antakiya tare da Bulus
da Barnaba. 23 Sai suka rubuta wasika, “Manzani da
dattawa da 'yan'uwa zuwa ga al'ummai 'yan'uwa a
Antakiya da Suriya da Kilikiya, gaisuwa mai yawa.
24 Mun ji cewa wasu mutane daga cikinmu wadanda
ba mu umarce su ba, sun fita daga cikinmu sun yi
maku koyarwar da ta daga maku hankali. 25 Ya yi
kyau da dukanmu, muka amince mu zabi wadansu
mutane mu tura su wurinku tare da Bulus da Barnaba,
26 mutane wadanda suka sadaukar da ransu domin
sunan Ubangiji Yesu Almasihu. 27 Mun aika Yahuza
da Sila su gaya maku wadannan abubuwa. 28 Saboda
haka ya yi kyau Ruhu Mai Tsarki da mu, kada mu sa
maku nauyi fiye da wadannan abubuwan: 29 ku bar yi
wa gumaka hadaya, ku bar cin mushe da shan kayan
maye da zina da faskanci, in kun kiyaye wadannan
abubuwa za ku zauna lafiya. Ku huta lafiya.” 30 Da aka
sallame su, sai suka je Antakiya. Bayan sun tara jama'a
sai suka ba su wasikar. 31 Bayan da suka karanta ta, sai
suka yi murna sosai saboda karfafawa. 32 Yahuza da
Sila, da shike su annabawa ne, suka karfafa 'yan'uwa
da kalmomi masu yawa. 33 Bayan sun yi kwananki
a wurin, sai aka sallame su zuwa wurin 'yan'uwa
wadanda suka aiko su. 34 Amma ya gamshe Sila ya
zauna a wurin. 35 Amma Bulus da Barnaba suka
tsaya a Antakiya da sauran 'yan'uwa, suna koyar da
maganar Ubangiji. 36 Bayan kwanaki kadan Bulus ya
ce ma Barnaba, “Mu koma yanzu mu ziyarci dukan
'yan'uwa da muka yi masu bisharar Ubangiji, mu
ga yadda suke. 37 Barnaba yana so su dauki Yahaya
wanda kuma ake kira Markus. 38 Amma Bulus ya yi
tunanin bai kamata a tafi da Markus ba, tun da ya bar
su a Bamfiliya bai ci gaba da su ba. 39 Nan jayayya ta
tashi tsakaninsu, har suka rabu da juna sai Barnaba
ya tafi tare da Markus suka ketare zuwa Kuburus. 40
Amma Bulus ya zabi Sila suka tafi, bayan 'yan'uwa
sun yi masu addu'ar alherin Allah ya kiyaye su. 41
Bulus ya tafi ya zazzaga Suriya da Kilikiya yana ta
karfafa iklisiyoyin.

16 Bulus ya kuma isa Darbe da Listira, in da akwai
wani almajiri mai suna Timoti a wurin, dan wata
Bayahudiya wadda ta ba da gaskiya; ubansa kuwa
Baheline ne. 2 Ana maganar kirki a kansa ta bakin
'yan'uwa da ke Listira da Ikoniyan. 3 Bulus ya yi wa
Timoti kaciya, domin yana so su yi tafiya tare, domin
kuma saboda Yahudawan da ke wurin, sun san cewa
ubansa Baheline ne. 4 Suna shiga cikin biranen, suna
yi wa iklisiyoyi gargadi da su yi biyayya da umurnan
da Manzanni da dattawa suka rubuta a Urushalima. 5
Bangaskiyar iklisiyoyi kuwa ta karu, ana kuma samun
karuwa na wadanda suke ba da gaskiya kowace rana.
6 Bulus da abokan aikin sa sun shiga cikin lardin
Firigiya da Galatiya, tun da Ruhu Mai Tsarki ya hana
su wa'azin kalmar a cikin yankin Asiya. 7 Sun zo kusa
da Misiya, da nufin shiga cikin Bitiniya, Ruhun Yesu ya
hana su. 8 Da suka ratse ta cikin Misiya, sai suka shiga
birnin Taruwasa. 9 Bulus ya ga wahayi cikin dare,
wani mutumin Makidoniya na kiransa, yana cewa. ''Ka
zo Makidoniya ka taimake mu''. 10 Bulus, da ganin
haka, ya kama hanya zuwa Makidoniya, da tunanin
Allah ne ya ke so su kai wa mutanen Makidoniya
bishara. 11 Da barin Taruwasa, Bulus da kungiyarsa
sun shiga jirgin ruwa zuwa Samutaraki, da gari ya
waye kuma sun tafi Niyafolis; 12 Daga nan kuma suka
tafi Filibi, birni na Makidoniya, mai muhimmanci
ne a yankin Roma, in da mun yi zango kwanaki da
dama. 13 Ranar Asabaci mun je kofar gari, gefen rafi,
da tunanin samun wurin addu'a. Mun zauna mun
kuma yi magana da matan da sun taru a wurin. 14
Wata mace mai suna Lidiya, 'yar kasuwa ce a birnin
Tiyatira, mai bautar Allah ce, ta saurare mu. Ubangiji
ya bude zuciyarta, ta mai da hankali ga maganar da

Bulus ke fadi. 15 Sa'anda da aka yi mata Baftisma tare
da mutanen gidanta, ta ce da mu, “Idan kun dauke
ni mai bautar Allah, ku zo gidana ku zauna.” Sai ta
rinjaye mu. 16 A daidai wannan lokaci, muna tafiya
wurin addu'a, wata yarinya mai ruhun duba ta hadu
da mu. Iyayen gijinta na arziki da ita sosai. 17 Tana
bin Bulus, tare da mu, tana fadi da murya mai karfi
cewa, ''Wadannan mutanen, bayin Allah mafi daukaka
ne, suna sanar maku hanyar ceto ne''. 18 Ta dauki
kwanaki tana haka. Amma Bulus ya yi fushi da ita
ainun, ya juya ya umarci ruhun, ya ce, ''Na umarce
ka, ka rabu da ita a cikin sunan Yesu Almasihu''.
Ruhun ya yi biyayya ya rabu da ita nan take. 19 Da
iyayengijinta suka ga cewa hanyar shigar kudinsu ta
toshe, sai suka kama Bulus da Sila, suka ja su cikin
kasuwa suka kai su gaban mahunkunta. 20 Da suka kai
su Kotu, suka ce, ''Wadannan mutane Yahudawa ne,
suna kawo tashin hankali a birninmu. 21 Suna koyar
da abubuwa da ba su karbuwa a gare mu, balle mu
aikata, a matsayinmu na Romawa.” 22 Sai jama'a gaba
daya sun tayar wa Bulus da Sila; alkalan kuma sun
yage rigunansu, sun ba da umarni a duki Bulus da Sila
da bulala. 23 Bayan dukan, an jefa su Bulus a kurkuku,
an ba mai tsaron kurkukun umurni ya kulle su da
kyau, kada su gudu. 24 Shi kuma ya yi hakanan, ya sa
masu sarkoki a kafafun su, kamar yadda aka umurce
shi. 25 Da tsakar dare, Bulus da Sila suna yin adu'a, su
na raira wakoki ga Allah, sauran 'yan sarkar su na jin
su. 26 Nan da nan sai ga wata girgizar kasa, wadda ta
sa ginshikan kurkukun sun kadu, nan da nan kofofin
kurkukun sun bude, 'yan sarka kuma, sarkokin su sun
karkatse. 27 Mai tsaron kurkukun ya tashi daga barci
ya ga kofofin kurkukun a bude, ya zaro takobi, zai
kashe kan sa, a tunanin sa, 'yan sarkar sun gudu. 28
Amma Bulus ya ta da murya da karfi, ya ce, ''kada
kayi wa kanka barna, domin dukan mu muna nan''. 29
Mai tsaron kurkukun ya aika a kawo fitila, ya shiga
ciki a gurguje da rawan jiki, ya fadi a gaban Bulus da
Sila, 30 ya fitar da su waje ya ce, ''Shugabanni, me ya
kamata in yi domin in tsira?'' 31 Sun ce masa, ''ka ba
da gaskiya ga Yesu Ubangiji, da kai da gidan ka, za ku
sami tsira''. 32 Bulus da Sila suka fada masa maganar
Ubangiji, tare da iyalinsa. 33 Shi mai tsaron kurkukun
ya dauke su cikin daren, ya wanke raunukansu, an
kuma yi masa Baftisma nan da nan tare da iyalinsa. 34
Ya kai Bulus da Sila gidansa, ya ba su abinci. Murna ta
cika gidan mai tsaron kurkukun, domin iyalin sa duka
sun ba da gaskiya ga Allah. 35 Da gari ya waye, alkalai
sun ba da sako a saki Bulus da Sila. 36 Mai tsaron
kurkukun kuwa ya sanar wa Bulus wannan magana ta
alkalan, saboda haka ya ce wa Bulus, ''Ku tafi cikin
salama''. 37 Amma Bulus ya ce masu, “Sun yi mana
duka a fili a gaban mutane mu da muke Romawa,
ba a kashe mu ba, sun kuma sa mu a kurkuku; suna
koran mu a asirce? Su zo da kansu su fitar da mu. 38
Masu tsaron kurkuku sun mayar da maganar Bulus ga
alkalan, wanda ya sa sun firgita, da jin cewa Bulus
da Sila Romawa ne. 39 Alkalai da kansu sun zo sun
roki Bulus da Sila; da suka fitar da su daga kurkukun,
sun ce wa Bulus da Sila su bar birnin. 40 Da hakanan
ne Bulus da Sila suka fita daga kurkuku, sun je gidan
Lidiya. Da Bulus da Sila sun ga 'yan'uwa, sun karfafa
su, sa'annan suka bar birnin.

17 Bayan sun wuce biranen Amfibolis da Aboloniya,
sun iso birnin Tasalunika, in da akwai wata
majami'ar Yahudawa a wurin. 2 Bulus, kamar yadda
ya saba, ya nufi wurinsu, yana tattaunawa da su
har Asabaci uku, daga cikin littattafai. 3 Bulus ya
bude littattafai yana bayyana masu cewa, dole ne
Almasihu ya sha wahala, ya kuma tashi daga matattu.
Ya ce, ''Wannan Yesu kuwa da nake sanar maku, shine
Almasihu''. 4 Wasu Yahudawa sun yarda, sun bi Bulus
da Sila, da wadansu Helenawa, da Shugabannin Mata
da jama'a da yawa. 5 Yahudawan da basu ba da gaskiya
ba suka cika da kishi, suka dauki wadansu 'yan ta'adda
daga cikin kasuwa, suka tada tarzoma cikin birnin,
mutane da yawa na bin su. Sun kai hari a gidan Yason,
da niyyar fitar da Bulus da Sila a gaban jama'a. 6
Amma da ba su ga Bulus da Sila ba, suka ja Yason
da wasu 'yan'uwa masu bi zuwa gaban mahukuntar
birnin, suna cewa, ''Wadannan ne fa masu ta da
zaune tsaye, gashi sun zo mana. 7 Wadannan mutane
da Yason ya marabta, sun saba wa dokokin Kaisar;
Suna cewa akwai wani sarki mai suna - Yesu.'' 8 Da
taron jama'a, da mahukuntan birnin suka ji haka,
sun damu. 9 Bayan da sun amshi kudi daga wurin
Yason da sauran 'yan'uwan, sai suka sake su. 10 A
wannan daren, 'yan'uwa masu bi suka fitar da Bulus
da Sila, suka aike su garin Biriya. Da isar su can, su ka
nufa majami'ar Yahudawa. 11 Mutanen Biriya daban
suke da na Tasalunika, sun yarda da sakon Bulus da
zuciya daya, suna kuma binciken littattafai kowace
rana domin su tabbatar da sakon Bulus, ko gaskiya ne.

12 Saboda haka mutane da yawa cikin su sun ba da
gaskiya, tare da wadansu sannanun mata Helenawa
da maza da yawa. 13 Amma da Yahudawan Tasalunika
suka ji cewa Bulus yana wa'azin kalmar Allah a Biriya,
sun haura can, sun tada hankulan jama'a. 14 Nan da
nan, masu bi na Biriya sun dauki Bulus sun aika shi
zuwa teku, an bar Sila da Timoti a Biriya tukuna. 15
Wadanda sun fitar da Bulus, sun kai shi har zuwa
birnin Atina. Bulus ya ba su sako, su fada wa Sila da
Timoti suyi hanzari su same shi. 16 Sa'anda Bulus
yana jiran zuwan Sila da Timoti a Atina, ya yi fushi a
ransa, da ya ga birnin cike da gumakai. 17 Ya tattauna
da Yahudawa a cikin majami'a tare da masu yin sujada
ga Allah, da kuma wadanda yake samu a kowace rana,
a kasuwa. 18 Amma wadan su Abikuriyawa da masana
sun yi karo da shi. Wadansun su na cewa, ''Menene
wannan sakaren ke cewa?'' Wadansu kuma sun ce,
''Da alama mai wa'azi ne na wasu alloli dabam,''
domin yana wa'azin Yesu da tashin sa daga matattu.
19 Suka dauki Bulus zuwa Tudun Arasa, suna cewa,
''Ko za ka sanar mana da wannan sabuwar koyaswar
taka? 20 Abubbuwan da kake fadi, baki ne a gare mu.
Muna so mu san ma'anar su.'' 21 (Atiniyawa da bakin
da ke cikinsu, suna ba da lokacin su ga fadin sabobbin
abubuwa da sauraron su). 22 Bulus ya tsaya a tsakiyar
Tudun Arasa ya ce, ''Ku mutanen Atiniya na lura
masu kwazon addini ne ku. 23 Na lura da abubuwan
sujadar ku yayin da nake zagawa, amma na ga wani
bagadi da rubutu a kansa mai cewa, ''Ga Allah wanda
ba a sani ba.” Abin da kuke bauta wa cikin rashin
sani, shi nake sanar maku. 24 Allahn da ya yi duniya
da kome da ke cikinta, tun da ya ke shine Ubangijin
sama da kasa, ba ya zama a haikalin da mutane suka
gina da hannu. 25 Ba ya neman taimakon kowa, babu
kuma wanda ya isa ya ba shi. Shine ke ba da rai, da
numfashi da kowanne abu. 26 Daga mutum daya ya
hallici dukan al'umman duniya, ya rarraba, ya kuma
sanya kowa a inda ya shirya masa. 27 Domin su nemi
Allah ko za su iya kaiwa zuwa gareshi su same shi, ga
shi kuwa ba ya nesa da kowannenmu. 28 A cikinsa
muke rayuwa, muna walwala, kamar yadda wani daga
cikin masananku yace, 'Mu 'ya'yansa ne'. 29 Idan mu
'ya'yan Allah ne, bai kamata mu danganta Allah da
zinariya ko azurfa, ko kuma duwatsu da itatuwa da
an sassaka ba. 30 Saboda haka ne, Allah ya kawar
da kwanakin jahilci, amma ya ba da umarni kowa a
ko'ina ya tuba. 31 Akwai ranar da ya shirya zai yi wa
duniya shari'a cikin adalci, ta wurin mutumin da ya
zaba. Allah ya nuna wannan mutumin, ta wurin ta
da shi daga matattu''. 32 Da mutanen Atina sun ji
batun tashi daga matattu, wadansu suka yi wa Bulus
ba'a; amma wadansu kuma sun ce, ''Za mu saurare ka
kuma, a kan wannan maganar.'' 33 Bayan haka, Bulus
ya bar su. 34 Amma wasu maza a cikinsu sun yarda
da bisharar, sun ba da gaskiya, hade da Diyonisiyus
dan Majalisar Tudun Arasa da wata mace mai suna
Damaris, da wadansu tare da su.

18 Bayan haka sai Bulus ya tafi Antakiya daga
nan, ya wuce Korinti. 2 A can ya sadu da wani
Bayahude mai sunan Akila, dan kasar Buntus ne;
bai dade da zuwa garin ba, daga Italiya ya zo da
matarsa mai suna Balkisu, saboda Kalaudiyas ya ba da
umarni dukan Yahudawa su bar Roma; sai Bulus ya je
wurinsu. 3 Bulus ya zauna a gidansu don sana'arsu
daya ce, wato, masu aikin Tanti ne. 4 Saboda haka
Bulus na zuwa majami'a, yana yin nazari tare da su
a kowace Asabaci. Yana kokari ya rinjayi Yahudawa
da Helinawa. 5 Amma a lokacin da Sila da Timoti
suka iso Makidoniya, Ruhu ya matsa Bulus ya shaida
wa Yahudawa cewa Yesu Almasihu ne. 6 Lokacin
da Yahudawa suka tayar masa suna zarginsa. Bulus
ya kakkabe rigansa a gabansu yana cewa, “Alhakin
jininku yana kanku; daga yanzu zan koma wurin
al'ummai.” 7 Da ya bar wurinsu, ya tafi gidan Taitus
Yustus mai wa Allah sujada. Gidansa na kusa da
majami'a. 8 Kiristus shine shugaban majami'a, sai
shi da dukan iyalin gidansa sun ba da gaskiya ga
Ubangiji. Korantiyawa da yawa suka ji jawabin Bulus
suka ba da gaskiya, aka yi masu Baftisma. 9 Da dare
Ubangiji ya ce wa Bulus a cikin wahayi, “Kada ka ji
tsoro, amma ka yi magana kada kuma ka yi shuru.
10 Gama ina tare da kai, ba wanda zai cutar da kai,
gama ina da mutane anan garin.” 11 Bulus ya zauna a
nan tsawon shekara daya da wata shida, yana koyar
masu da maganar Allah. 12 Amma da Galiyo ya samu
zaman gwamnan Akaya, sai Yahudawa suka tayar
wa Bulus har suka kai shi gaban dakalin shari'a. 13
Suna cewa, “Wannan mutumin yana kokarin rinjayar
mutane su yi sujadar da ta saba wa dokarmu.” 14
Duk da haka kafin Bulus ya yi magana, Galiyo ya ce
wa Yahudawa, “Ku Yahudawa in da karar ku ta wani
babban laifi ce wanda ya aikata, da sai in hukunta. 15
Amma tun da ya ke akan al'amurar, kalmomi ne, da ta

sunaye da dokokin ku, ku je ku sasanta al'amuran
ku." 16 Galiyo ya kore su daga dakalin shari'a. 17
Saboda haka sai suka kama Sastanisu, suka yi masa
duka sosai a gaban dakalin shari'a. Amma Galiyo bai
damu da yadda suka karasa ba. 18 Bulus kuwa, bayan
ya zauna tare da su na wasu kwanaki masu yawa, ya
bar 'yan'uwan zuwa Suriya ta jirgin ruwa, tare da
Balkisu da Akila. Kafin ya bar tashar jiragen ruwa da
ke a Sankuriya, ya tafi saboda ya aske kansa, domin
ya dauki alkawarin Banazare. 19 Da suka iso Afisa,
Bulus ya bar Balkisu da Akila anan. Shi kuwa ya shiga
majami'ar Yahudawa yana nazari tare da su. 20 Da
suka roki Bulus ya zauna da su na tsawon lokaci, bai
yarda ba. 21 Ya kama hanyarsa ya bar su ya ce, "In
Allah ya yardar mani zan dawo wurinku wata rana."
Sai ya shiga jirgin ruwa daga Afisa. 22 Daga saukar su
a Kaisariya, sai ya haura zuwa Urushalima ya gai da
iklisiya daga nan ya tafi Antakiya. 23 Bayan ya zauna
na dan lokaci a wurin, Bulus ya kama hanyarsa zuwa
yakin Galatiya da Firjiya anan ya karfafa almajirai.
24 A nan dai akwai wani Bayahude mai suna Afolos,
dan asalin Iskandariya ne da haihuwa, ya zo Afisa. Shi
masani ne a maganar Allah. 25 Afolos dai ya sami horo
daga maganar Ubangiji. Shi mai kokari ne a ruhu,
yana wa'azi da koyarwa daidai game da Yesu. Amma
ya san da Baftismar Yahaya ne kadai. 26 Afolos ya fara
wa'azinsa da gabagadi a cikin majami'a. Da Balkisu da
Akila suka ji shi sai suka yi abokantaka da shi, suka
kara bayyana masa game da labarin hanyar Allah
mafi daidai. 27 Da ya so ya wuce zuwa cikin Akaya
'yan'uwa suka karfafa shi, sun rubuta wa almajiran da
ke a Akaya, don su karbe shi da hannu biyu. Da ya
iso wurinsu, ya kuwa karfafa 'yan'uwa da sun ba da
gaskiya ta wurin alheri. 28 Afolos ya ba Yahudawa
mamaki da irin ikon da yake da shi da gwanintarsa,
yadda yake nunawa daga nassoshi cewa Yesu shine
Almasihu.

19 Sa'adda Afolos yake a Koranti, Bulus ya zagaya
kasar tudu ya zo birnin Afisa, a nan kuma ya
sami wadansu almajirai. 2 Bulus ya ce masu, "Ko kun
karbi Ruhu Mai Tsarki sa'anda kuka ba da gaskiya?"
Suka amsa, "A'a bamu taba jin labarin Ruhu Mai
Tsarki ba. 3 Bulus ya ce, "Wacce irin baftisma aka yi
maku?" Suka ce, "Baftismar Yahaya" 4 Bulus ya amsa
ya ce, "Yahaya ya yi wa mutane baftismar tuba, ya ce
su ba da gaskiya wanda zai zo bayansa, wato, Yesu
kenan." 5 Da mutanen suka ji haka, sai aka yi masu
baftisma cikin sunan Ubangiji Yesu. 6 Sa'adda Bulus
ya dibiya hannu a kansu, Ruhu Mai Tsarki kuma ya
sauka a kansu suka yi magana da harsuna da kuma
annabci. 7 Su wajen mutum goma sha biyu ne. 8
Bulus ya shiga majami'a ya yi ta koyarwa gabagadi
misalin tsawon wata uku. Yana bi da su cikin nazarin
maganar yana fahimtar da mutane su gaskanta game
da abubuwa da suka shafi mulkin Allah. 9 Amma
sa'adda wadansu Yahudawa suka taurare, suka ki
yin biyayya, sai suka fara bata hanyar Almasihu a
gaban taron. Saboda haka sai Bulus ya janye daga
wurinsu tare da wadanda suka ba da gaskiya. Ya fara
koyarwa a makarantar Tiranus. 10 Haka ya cigaba
shekaru biyu har duk mazaunan Asiya suka ji maganar
Ubangiji, Yahudawa da Helenawa. 11 Allah ya yi
manyan al'ajibai ta hannun Bulus, 12 har marasa
lafiya suka warke, mugayen ruhohi suka fito daga
cikin mutane, sa'adda suka karbi kyallaye da mayafai
daga jikin Bulus. 13 Amma akwai Yahudawa masu
tsubu da suka biyo ta wajen, suka dauka wa kansu
su yi amfani da sunan Yesu. Suka ce, "Mun dokace
ku cikin sunan Yesu wanda Bulus yake wa'azinsa,
ku fita." 14 Wadanda suka yi wannan su bakwai ne
'ya'yan wani babban firist Bayahude mai suna Siba. 15
Mugun ruhun ya amsa ya ce, "Na san Yesu, na san
Bulus, amma ku, su wanene?" 16 Sai mugun ruhun
da ke cikin mutumin ya fada a kan matsubatan ya fi
karfinsu ya kuma bubuge su. Suka runtuma da gudu
suka fice daga dakin tsirara da raunuka. 17 Wannan ya
zama sanannen abu ga dukan mutane, Yahudawa da
Helenawa mazaunan Afisa. Suka ji tsoro kwarai, sunan
Ubangiji Yesu ya sami daukaka. 18 Masu bi da yawa
kuma, suka zo suka furta mugayen ayyukan da suka
aikata. 19 Masu sihiri suka kawo littattafansu suka
kona a gaban mutane. Da aka yi jimilar tamaninsu, aka
samu sun kai dubu hamsin na azurfa. 20 Sai maganar
Ubangiji ta yadu da iko ta hanyoyi da yawa. 21 Da
Bulus ya kammala aikinsa na bishara a Afisa, Ruhu
ya bishe shi sai ya bi ta Makidoniya da Akiya a kan
hanyarsa zuwa Urushalima. Ya ce, "Bayan na je can,
dole in je Roma." 22 Bulus ya aiki almajiransa biyu
Timoti da Irastus zuwa Makidoniya, wadanda suka
taimake shi. Amma shi da kansa ya jira a Asiya na
dan lokaci. 23 A wannan lokacin sai aka yi babban
tashin hankali a Afisa game da wannan Hanyar. 24
Wani Makeri mai suna Damatrayus wanda ke kera
sifoffin gunkin azurfa na Dayana, wanda sana'a ce

mai kawo wa makera riba sosai. 25 Ya tattara makera
ya ce da su, “Kun sa ni da wanan sana'a ne muke
samun kudi mai yawa. 26 Kun gani kun kuma ji cewa,
ba a Afisa kadai ba, amma har da fadin kasar Asiya
wannan Bulus ya rinjayi mutane da yawa. Yana cewa
babu alloli da ake kerawa da hannu. 27 Ba sana'ar
mu kadai ke cikin hatsari ba, amma har da haikalin
allahnmu Dayana babba zai zama mara amfani. Ta
haka za ta rasa girmanta, ita da dukan kasar Asiya
da duniya ke wa sujada.” 28 Da suka ji haka sai suka
fusata kwarai, suka yi kira mai karfi suna cewa “Mai
girma ce Dayana ta Afisa.” 29 Gari gaba daya ya rude,
jama'a kuma sun hanzarta zuwa wurin taron. Kafin
wannan lokaci, sun riga sun kama abokan tafiyar
Bulus, wato Gayus da Aristakas wadanda suka zo daga
Makidoniya. 30 Bulus ya yi niyya ya shiga cikin taron
jama'ar, amma almajiran suka hana shi. 31 Haka nan
ma wadansu abokan Bulus da ke shugabanin yankin
al'umma Asiya sun aika masa da roko mai karfi kada
ya shiga dandalin. 32 Wadansu mutane na kirarin
wani abu, wadansu kuma na kirarin wani abu dabam,
domin jama'a sun rude. Da yawa daga cikinsu ma ba
su san dalilin taruwarsu ba. 33 Yahudawa suka kawo
Iskandari ya tsaya a gaban taruwan jama'a. Iskandari
ya mika hannunsa sama domin ya yi bayani ga jama'a.
34 Amma da suka gane shi Bayahude ne, sai dukansu
suka kwala ihu wajen sa'a biyu, “Mai girma ce Dayana
ta Afisa.” 35 Da magatakardar garin ya sha kan jama'a,
sai ya ce, “Ya ku mutanen Afisa, wanene bai san cewa
birnin Afisa cibiya ce na allahn nan Dayana mai girma
da na sifar da ta fado daga sama ba? 36 Tun da ba
a karyata wadannan abubuwa ba, ya kamata ku yi
shuru don kada ku yi wani abu a gaggauce. 37 Gama
kun kawo wadannan mutane a wannan dakin sharia
ba a kan su mafasa ne na haikali ba ko kuma masu
sabo ga allahnmu ba. 38 Saboda haka idan Damatrayas
da makeran da ke tare da su na da wata tuhuma
a kan wani, kotuna suna nan a bude masu shari'a
kuma suna nan. Ba ri su kai karar junansu. 39 Amma
idan akwai maganganu na dubawa, za a daidaita su a
taronmu na lokaci lokaci. 40 Domin hakika muna cikin
hatsarin zargi game da hargitsin yau. Babu dalilin
wanan yamutsi domin ba mu da bayani a kansa.” 41
Da ya fadi haka, sai ya sallami taron.

20 Bayan da rikici ya kare, Bulus ya aika a
kira al'majiran, ya karfafa su. Sa'annan ya yi
bankwana da su, ya tashi zai tafi Makidoniya. 2 Bayan
ya ratsa cikin lardunan yana yi wa masu bi gargadi
sosai, sai ya zo kasar Helenawa. 3 Sa'adda ya yi wata
uku a wurin, Yahudawa suka kulla masa makirci, yayin
da yake shirin hawa Jirgi zuwa Suriya, sai ya canza
ra'ayi ya koma ta Makidoniya. 4 Masu yi wa Bulus
rakiyar zuwa yankin Asiya sun hada da Sobatarus
dan Burus daga Biriya; Gayus mutumin Derbe; Timoti
da Aristakus da Sakundus, dukansu masu bi ne daga
Tasalonika; da Tikikus da Trofimus daga Asiya. 5
Amma wadansu har suka rigaye mu, suka jira mu a
Taruwasa. 6 Da muka shiga Jirgi daga Filibi bayan
kwanakin Gurasa mara yisti; bayan kwanaki biyar
muka iske su a Taruwasa; kwananmu bakwai a wurin.
7 A rana ta fari ga mako, da muka taru domin karya
gurasa. Bulus ya yi wa masubi jawabi, don ya yi niyyar
ya tafi da wayewar gari; jawabinsa ya kai har tsakar
dare. 8 A benen da suka taru akwai fitilu da yawa.
9 Wani matashi mai suna Aftikos yana zaune a kan
taga, barci mai nauyi ya dauke shi; da shike Bulus ya
tsawaita jawabinsa, saurayin da shike barci mai nauyi
ya dauke shi sai ya fado daga kan bene na uku aka
dauke shi matacce. 10 Sai Bulus ya sauka ya mike a
bisansa ya rungume shi, sa'annan ya ce, “Kada kowa
ya damu; domin yana darai bai mutu ba.” 11 Sa'annan
ya hawo kan bene domin cin gurasa tare da su, ya
yi magana da su har gari ya waye daga nan ya bar
su. 12 Suka kawo saurayin da rai, sun sami ta'aziya
ba kadan ba. 13 Amma mu, da muka riga Bulus zuwa
gun Jirgin, muka shiga zuwa Asos, mun shirya mu
dauki Bulus a jirgi amma shi ya kudurta ya yi tafiya a
kasa. 14 Da muka sadu a Asos, mun dauke shi a Jirgin
ruwa zuwa Mitilitus. 15 Bayan tashin mu daga can,
washegari muka zo tsibirin Kiyos. Washegari kuma
muka zo birnin Militus. 16 Amma Bulus ya kudurta
wucewa Afisa a Jirgi, don kada ya bata lokaci a Asiya,
don yana sauri in ya yiwu ranar Fentekos ta same
shi a Urushalima. 17 Daga Militus ya aika a kira masa
dattawan iklisiyar Afisa. 18 Da suka zo wurinsa sai
ya ce masu, “Ku da kanku kun san tun daga ranar
da na sa kafata a Asiya, irin zaman da muka yi da
kasancewar mu tare. 19 Na bauta wa Ubangiji da
tawaliu har da hawaye, da wahalun da na sha saboda
makircin Yahudawa. 20 Kun sani ban ji nauyin sanar
da ku kowanne abu mai amfani ba, na bi ku gida gida
ina koyar da ku abubuwa a sarari. 21 Kunsan yadda
na gargadi Yahudawa da Hellenawa game da tuba ga

Allah da bangaskiya ga Ubangiji Yesu. 22 Yanzu fa,
gashi, zan tafi Urushalima, Ruhu Mai Tsarki ya nuna
mani a fili dole in je, ban san abin da zai faru da ni a
can ba. 23 Sai dai Ruhu Mai Tsarki ya nuna mani a
kowanne gari cewa, sarkoki da wahalu suna jira na. 24
Amma ban dauka cewa raina yana da wani amfani
gare ni ba, domin in cika tsere da hidimar da na karba
daga wurin Ubangiji Yesu, ta shaidar bisharan alherin
Allah. 25 Yanzu fa, duba, na san dukanku, wadanda na
yi wa wa'azin mulkin Allah, ba za ku kara gani na ba.
26 Don haka na shaida maku a wannan rana, ba ni da
alhakin jinin kowanne mutum. 27 Don banji nauyin
sanar maku da dukan nufin Allah a gare ku ba. 28
Saboda haka ku kula da kanku, da masubi da Ruhu
Mai Tsarki ya sanya ku shugabanni. Ku kula ku yi
kiwon iklisiyar Allah, wadda ya saya da jininsa. 29 Na
sani cewa bayan tafiyata, kyarketai masu zafi za su
shiga tsakaninku, kuma baza su rangwanta wa masubi
ba. 30 Na sani har daga cikinku wadansu mazaje za su
zo su fadi gurbattatun zantattuka, domin su janye
almajirai zuwa gare su. 31 Saboda haka ku yi lura. Ku
tuna da cewa shekara uku ban fasa yi wa kowannenku
gargadi da hawaye dare da rana ba. 32 Yanzu ina
mika ku ga Allah, da maganar Alherinsa, wadda take
da ikon gina ku ta kuma ba ku gado tare da dukan
wadanda ke cikin kebabbu na Allah. 33 Ban yi kyashin
azurfa, ko zinariya, ko tufafin wani ba. 34 Ku da kanku
kun sani na yi aiki da hannuwana, na biya bukatu na
da na wadanda ke tare da ni. 35 Na zama maku abin
koyi a kowace hanya game da yadda za ku taimaka
wa nakasassu ta wurin aiki, da yadda za ku tuna da
maganar Ubangiji Yesu, maganar da shi da kansa
ya ce: ''Bayarwa tafi karba albarka.'' 36 Bayan da ya
yi magana haka, ya durkusa ya yi addu'a tare da su
duka. 37 Dukansu kuwa suka yi kuka mai tsannani,
suka rungume shi kuma suka sunbace shi. 38 Suka
yi bakin ciki musamman domin abin da ya ce masu,
ba za su kara ganinsa ba. Sai dukansu suka yi masa
rakiya zuwa wurin jirgin ruwa.

21 Da muka rabu da su, muka shiga jirgin ruwa
muka mike hanya zuwa birnin Kos, washegari sai
birnin Rodusa, daga nan sai kuma zuwa birnin Batara.
2 Da muka sami jirgi mai hayewa zuwa Fonisiya sai
muka shiga. 3 Da muka hango tsibirin Kubrus muka
bar shi a hagun mu muka nufi Suriya, muka sauka a
birnin Taya domin a nan ne jirgin ruwan zai sauke
kayansa. 4 Bayan mun sami almajirai sai muka zauna
can kwana bakwai. Al'majiran suka ce ma Bulus, ta
wurin Ruhu, kada ma ya je Urushalima. 5 Bayan
'yan kwanaki muka cigaba da tafiyarmu. Dukansu
da matansu da 'ya'yansu suka raka mu har bayan
birnin. Sa'annan muka durkusa a bakin gacci muka
yi addu'a muka yi sallama da juna. 6 Sai muka shiga
jirgin ruwa, su kuma suka koma gida. 7 Da muka
gama tafiyarmu a Taya muka iso Talamayas. A nan ne
muka gaisa da 'yan'uwa, muka zamna kwana daya
da su. 8 Washegari muka tashi muka tafi Kaisariya.
Muka shiga gidan Filibus mai shaida bishara, daya
daga cikin bakwai din, muka zauna da shi. 9 Wannan
mutum yana da 'ya'ya hudu mata, budurwai masu yin
annabci. 10 Sa'anda muka zauna can 'yan kwanaki,
wani annabi ya zo daga Yahudiya mai suna Agabus. 11
Ya zo wurinmu ya dauki damarar Bulus ya daure tasa
kafar da hannayensa ya ce, “Ruhu Mai Tsarki ya ce,
'Haka Yahudawa za su daure mai wannan damarar,
zasu kuma bashe shi ga al'ummai.'” 12 Da muka ji
wannan sakon, sai dukanmu da mazaunan wurin
muka roki Bulus kada ya tafi Urushalima. 13 Sai Bulus
ya amsa ya ce, “Me kuke yi, kuna kuka kuna karya
mani zuciya? Bama a shirye don dauri kadai nake
ba har ma da mutuwa a Urushalima, sabili da sunan
Ubangiji Yesu.” 14 Tun da Bulus bashi da niyyar a
rinjaye shi, muka daina kuka muka ce, “Bari nufin
Ubangiji ya tabbata.” 15 Bayan wadannan kwanaki,
muka dauki jakkunanmu muka haura Urushalima.
16 Wadansu almjirai daga Kaisariya suka bi mu. Sun
zo ne tare da wani ana ce da shi Manason, mutumin
Kuburus mai bi na farko, wanda za mu zauna da shi.
17 Da muka isa Urushalima, 'yan'uwa suka marabce
mu da farin ciki. 18 Washegari Bulus ya tafi tare da mu
zuwa wurin Bitrus, dukan dattawa kuma suna nan. 19
Bayan ya gaishe su, sai ya shaida masu daya bayan
daya abubuwan da Allah ya yi cikin al'ummai ta wurin
hidimarsa. 20 Da suka ji haka, suka yabi Ubangiji suka
ce masa, “Ka gani, dan'uwa, dubban Yahudawa sun
bada gaskiya suna kuma da niyyar kiyaye shari'a.
21 An kuma gaya masu a kanka cewa, kana koya wa
Yahudawan da suke zaune cikin al'ummai su yi watsi
da Musa. Kana koya masu kada su yi wa 'ya'yansu
kaciya, kada kuma su bi tsofaffin al'adu. 22 Me ya
kamata mu yi? Hakika za su ji ka zo. 23 Sabo da haka
ka yi abin da muka fada maka yanzu. Muna da maza
hudu da suka dauki wa'adi. 24 Tafi da wadannan ka

tsarkake kanka tare da su, ka dauki dukan dawainiyar
su dana askin kai. Ta haka kowanne mutum zai sani
abubuwan da ake fadi a kanka karya ne. Za su sani
cewa kai mai kiyaye shari'a ne. 25 Game da al'umman
da suka bada gaskiya mun yi masu wasika, mun bada
umarni su kaurace kansu daga sadakokin da aka mika
wa gumaku, da jini, da abin da aka makare da kuma
fasikanci. 26 Sai Bulus ya dauki mazannan, washegari
ya tsarkake kansa tare da su, suka shiga haikali, domin
ya sanar da cikar ranakun tsarkakewarsu, wato ranar
ba da sadaka domin kowanne dayansu. 27 Da kwanakin
nan bakwai suka yi gab da cika, wadansu Yahudawa
daga Asiya suka ga Bulus a haikali, sai suka zuga
taro, suka danke shi. 28 Suna ta kururuwa, “Mutanen
Isra'ila ku taimaka mana. Wannan shine mutumin da
ke koya wa dukan mutane ko'ina abubuwa gaba da
mutane, da shari'a da kuma wannan wurin. Banda
haka ya kawo Helenawa cikin haikalin nan ya kazantar
da wannan wuri tsatsarka.” 29 Domin dama sun ga
Tarofimas mutumin Afisa tare da Bulus cikin birni,
suka yi zaton ya kawo shi cikin haikali. 30 Sai duk
gari ya rude, mutane suka runtuma suka danke Bulus.
Suka ja shi waje daga cikin haikalin, nan da nan aka
rufe kofofin. 31 Suna kokarin kashe shi kenan, sai
labari ya kai wurin hafsan sojoji cewa Urushalima duk
ta yamutse da tarzoma. 32 Nan take ya dauki mayaka
da jarumawa, suka sheka da gudu wurin taron. Da
mutane suka ga hafsan sojoji da rundunansa sai suka
daina dukan Bulus. 33 Sai hafsan ya tafi ya danke Bulus
ya sa aka daure shi da sarkoki biyu. Ya tambaya ko
shi wanene da kuma laifinsa. 34 Wadansu cikin taron
suna ta kururuwa wadansu su ce wannan, wadansu su
ce, wancan. Tunda hafsan bai fahimci abin da suke
fadi ba, sabo da ihunsu, ya dokaci a shigar da Bulus
farfajiyar sojoji. 35 Da suka kai matakala, sojoji suka
dauki Bulus sabo da tsananin husatar taron jama'a. 36
Domin taron suka biyo baya suna ihu suna cewa, “A
kashe shi.” 37 An kusa shigar da shi farfajiyan kenan
sai Bulus ya ce wa babban hafsan, “Ko ka yarda inyi
magana da kai?” Hafsan ya ce, “Ka iya Helenanci? 38
Ashe ba kai ne Bamasaren nan da kwanakin baya ka
haddasa tawaye, ka dauki 'yan ta'adda dubu hudu ka
kai su jeji ba?” 39 Bulus ya ce, “Ni Ba'ibrane ne daga
birnin Tarsus a Kilikiya. Ni dan kasar babban birni ne.
Ka amince mani in yi magana da mutanen.” 40 Da
hafsan ya bashi izni, Bulus ya mike a kan matakala ya
daga hannayensa sama ya yi nuni su yi shuru. Da wuri
ya yi tsit, Bulus ya yi masu magana da Ibraniyanci. Ya
ce,

22 “Yanuwa da Ubanni, ku saurari kariya ta zuwa
gare ku yanzu.” 2 Da taron sun ji Bulus na
magana a harshen Ibraniyawa sai sun yi tsit. Ya ce, 3
Ni Bayahude ne daga garin Tarwasa na Kilikiya, amma
a karkashin Gamaliyal aka ilimantar da ni. An horar da
ni sosai bisa ga bin hanyar dokokin kakkaninmu. Ina
da himma ga bin Allah kamar yadda ku ma kuna da
ita. 4 Na tsananta wa wannan Hanyan har ga mutuwa;
na daure maza da mata sa'annan na jefa su cikin
gidan yari. 5 Hakannan ma babban firist da dukan
dattawa za su ba da shaida cewa na karbi izini daga
wurinsu domin 'yan'uwa da ke a Dimashku, saboda
in tafi can. Haki na shine in daure mabiyan Hanyan
nan, in kawo su Urushalima domin a hukunta su. 6
Sa'anda ina cikin tafiya, ina kuma kusa da Dimashku,
da tsakar rana sai farat daya ga babban haske daga
sama ya haskaka kewaye dani. 7 Na fadi kasa sa'anan
na ji murya na ce da ni, 'Shawulu, Shawulu, don
me kake tsananta mani?' 8 Na amsa, 'Wanene kai,
Ubangiji?' Ya ce mani, 'Nine Yesu Banazarat wanda
kake tsananta wa.' 9 Wadanda ke tare da ni sun
ga hasken, amma ba su gane muryar wanda ya yi
magana da ni ba. 10 Na ce, 'Me zan yi ya Ubangiji?”
Ubangiji ya ce mani, 'Tashi ka tafi cikin Dimashku,
a can za a fada maka abinda wajibi ne ka yi. 11 Ban
iya ganin wuri ba domin walkiyar hasken, sai na tafi
cikin Dimashku ta wurin jagorancin wadanda ke tare
da ni. 12 A can na sami wani mai suna Ananiya, mai
tsoron Allah bisa ga sharia, da kyakyawan suna kuma
a gaban Yahudawa da ke zama a can. 13 Ya zo gare ni
ya ce, 'Dan'uwa Shawulu, karbi ganin gari.' A daidai
wannan sa'a na gan shi. 14 Sa'annan ya ce, 'Allah na
kakkaninmu ya zabe ka ka san nufinsa, ka ga Mai
Adalcin nan, ka kuma ji muryar da ke fitowa daga
bakinsa. 15 Gama za ka zama mashaidinsa ga dukan
mutane game da abinda ka gani da wanda ka ji. 16
A yanzu me ka ke jira? 'Tashi a yi maka baftisma a
wanke zunubanka, kana kira bisa sunansa.' 17 Bayan
da na dawo Urushalima, sa'anda ina addu'a a cikin
haikali, sai na karbi wahayi. 18 Na gan shi ya ce
mani, 'Gaggauta ka bar Urushalima yanzu, domin
ba za su yarda da shaidarka game da ni ba.' 19 Na
ce, 'Ubangiji, su da kansu sun san yadda na sa su a
kurkuku na kuma doddoke wadanda suka gaskanta da

kai a kowacce masujada. 20 A sa'anda a ke zubar da
jinin mashaidinka Istifanus, ina nan tsaye ina goyon
baya, ina kuma lura da rigunan wadanda suka kashe
shi.' 21 Amma ya ce mani, 'Tafi, domin zan aike ka
can wurin Al'ummai.' 22 Mutanen sun bar shi yayi
magana har zuwa ga wannan lokacin. Amma sai suka
ta da murya suna cewa, 'A kawar da wannan dan taliki
daga duniya: don bai kamata ya rayu ba.' 23 Sa'anda
suke tadda muryarsu, suna jefar da tufafinsu da kuma
baza kura a iska, 24 babban hafsan ya umarta a kawo
Bulus a farfajiyan. Ya umarta da cewa a bincike shi da
bulala, domin ya san dalilin da suka ta da ihu gaba
da shi haka. 25 Bayan da suka daure shi da tsirkiya,
Bulus ya ce wa Jarumin da ke kusa da shi, "Ko daidai
ne bisa ga doka a yi wa Barome wanda ma sharia ba
ta kashe shi ba bulala?" 26 Da Jarumin ya ji haka, ya
tafi wurin babban hafsan, yana cewa, "Me kake so ka
yi? Gama wanan mutumin dan asalin Roma ne." 27
Babban hafsa ya zo ya ce masa, "Gaya mani, kai dan
asalin Roma ne?" Bulus ya ce, "Haka ne." 28 Babban
hafsan ya amsa masa, "Da kudi masu yawa na sayi
yancin zama dan kasa." Amma Bulus ya ce, "An haife
ni dan kasar Roma. 29 "Sai mutanen da sun zo su
tuhume shi sun bar shi nan da nan. Babban hafsa shi
ma ya tsorata da ya gane Bulus dan asalin Roma ne,
domin ya riga ya daure shi. 30 Washegari, babban
hafsan ya so ya san gaskiyar tuhuma da Yahudawa
suke yi a kan Bulus. Sai ya kwance shi daga sarka, ya
kuma umarci babban firist da dukan majalisa su sadu.
Sai ya kawo Bulus ya sa shi a tsakiyarsu.

**23** Bulus ya kura wa yan majalisa ido yace,
"'Yan'uwa, na yi rayuwa tare da Allah da
lamiri mai kyau har wannan ranan." 2 Babban firist
Hannaniya ya ba wandanda suke tsaye tare da shi
urmarni su buge bakinsa. 3 Bulus ya ce, "Allah zai
buge ka, kai munafiki. Kana zama domin ka shari'anta
ni da shari'a, kuma ka umarce a buge ni, gaba da
sharia?" 4 Wanda suka tsaya a gefe suka ce, "Kada ka
zage babban firis na Allah." Bulus yace, "Ban sani
ba, 'yan'uwa, cewa shi babban firis ne. 5 Domin a
rubuce yake, Ba za ku zargi shugaban mutanenku ba."
6 Da Bulus ya ga cewa, daya bangaren Sadukiyawa
ne dayan kuma Farisawa, ya yi magana da karfi a
majalisa, "'Yan'uwa, ni Bafarise ne, dan Farisawa.
Don tabbacin tashin matattu ne kuna shari'anta
ni." 7 Daya fadi haka, mahawara ta fara a tsakanin
Farisawa da Sadukiyawa, sai taron ya rabu kashi biyu.
8 Don Sadukiyawa suka ce babu tashin matattu, babu
mala'iku, babu kuma ruhohi, amma Farisawa suka ce
dukan abubuwan nan sun kasance. 9 Sai mahawara
ta tashi, wadansu marubutan Farisawa suka tashi
da mahawara cewa, "Ba mu same mutumin nan da
laifi ba sam. Ko mala'iku da ruhohi ne suka yi masa
magana?" 10 Da jayayya ta tashi, babban hafsa ya
ji tsoro kada su yayaga Bulus, sai ya umarce sojoji
suje su kwato shi da karfi daga 'yan majalisa, su tafi
da shi farfajiya. 11 Da dare Ubangiji ya tsaya kusa
da shi yace, "Kada ka ji tsoro, kamar yadda ka ba
da shaida game da ni a Urushalima, dole zaka sake
zama shaida a Roma." 12 Da gari ya waye, wadansu
Yahudawa sun yi yarjejeniya suka dauka wa kansu
la'ana: suka ce ba za su ci ba ba za su sha ba sai sun
kashe Bulus. 13 Mutane fiye da arba'in suka kulla
wannan makirci. 14 Suka je wurin manyan firistoci da
dattawa suka ce, "Mun sa wa kanmu la'ana, ba za mu
ci ba, ba za mu sha ba sai mun kashe Bulus. 15 Yanzu,
bari majalisa ta ba wa babban hafsa izini a kawo shi
a gaba, kamar zai yanke hukunci. Mu kam, a shirye
muke mu kashe shi kafin ya iso nan. 16 Amma dan
yar'uwan Bulus ya ji suna labe, sai ya tafi ya shiga
farfajiyar ya fada wa Bulus. 17 Bulus ya kira daya daga
cikin jarumai yace, "Dauki saurayin nan ka kai shi
wurin babban hafsa, don yana da abin da zai fada
masa." 18 Jarumin ya dauke saurayin ya kai shi wurin
babban hafsa yace, "Bulus dan sarka ne yace in kawo
saurayin nan a gaban ka. Yana da abin da zai fada
maka." 19 Babban hafsa ya kai shi wani lungu, sai
ya tambaye shi, "Menene kake so ka fada mani?" 20
Saurayin yace, "Yahudawa sun yarda su roke ka ka
kawo Bulus gobe a majalisa, kamar zasu kara bincike a
kan al'amarin. 21 Amma kada ka yarda da su, mutane
fiye da arba'in suna jiransa. Sun sa wa kansu la'anna,
ba za su ci ba ba za su sha ba sai dai sun kashe shi.
Yanzu a shirye suke; suna jira ka ba su izini." 22 Sai
babban hafsa yace wa saurayin ya tafi, da ya gama
masa magana, "Kar ka fada wa wani al'amuran." 23
Sai ya kira jarumai biyu yace, "Ku shirya sojoji dari
biyu, yan dawakai saba'in, masu daukar mashi dari
biyu su tafi kaisariya karfe uku na dare." 24 Ya umarta
a shirya dabbobin da Bulus zai hawo da zasu kai shi
lafiya wurin Filikus gwamna. 25 Sai ya rubuta wasika
a misalin haka: 26 Gaisuwa zuwa Kuludiyas Lisiyas
zuwa ga mai martaba gwamna Filikus. 27 Yahudawa

sun kama wannan mutumin suna shirin kashe shi, na
abko masu da sojoji na kwace shi, bayan da na ji shi
Barome ne. 28 Inna son sani dalilin zarginsa, sai na kai
shi majalisa. 29 Na gane cewa ana zarginsa ne a kan
tambayoyi game da shari'ansu, amma ba wani zargi
da ya cancanci dauri ko mutuwa. 30 Da aka sanar da
ni shirin makircin, sai na tura shi wurinka ba da bata
lokaci ba, na umarce masu zarginsa su kawo zarginsu
wurinka. Huta lafiya." 31 Sai sojoji suka yi biyayya
da umarni da aka basu: suka dauki Bulus suka kawo
shi dadare a wurin Antibatris. 32 Da gari ya yawe,
yan dawakai suka tafi tare da shi kuma sauran sojoji
suka koma farfajiya. 33 Bayan da yandawakan suka isa
Kaisiririya sun mika wasika ga gwamna, suka kuma
danka Bulus a hanunsa. 34 Da gwamna ya karanta
wasikar, sai ya tambaye su daga wani yanki ne Bulus
ya fito; da ya ji daga yankin kilikiya ne, 35 Yace zan
saurare ka sosai lokacin da masu zargin ka sun zo. Sai
ya umarta a tsare shi a fadar Hiridus.

**24** Bayan kwanaki biyar, sai Ananiyas babban firist,
Wasu dattawa da wani masanin shari'a mai suna
Tartilus, sun tafi can. Suka kai karar Bulus gaban
gwamna. 2 Lokacin da Bulus ya tsaya gaban gwamna,
Tartilus ya fara zarginsa yace wa gwamnan, "Saboda
kai mun sami zaman lafiya; sa'annan hangen gabanka
ya kawo gyara a kasarmu; 3 don haka duk abin da
ka yi mun karba da godiya, ya mai girma Filikus. 4
Domin kada in wahalsheka, ina roko a yi mani nasiha
don in yi magana kadan. 5 An iske mutumin nan yana
barna irir iri, yana kuma zuga jama'ar Yahudawa a
dukan duniya su yi tayarwa. 6 Har ma ya yi kokarin
kazantar da haikali; saboda haka muka kama shi.
[Mun so mu shari'anta masa bisa ga dokarmu.] 7
Amma Lisiyas jami'i ya zo ya kwace shi da karfi daga
hannunmu. 8 Idan ka binciki Bulus game da wadannan
al'amura, kai ma, zai tabbatar maka abin da muke
zarginsa a kai. 9 Dukan Yahudawa suna zargin Bulus
cewa wadannan abubuwa gaskiya ne. 10 lokacin da
gwamnan ya alamta wa Bulus ya yi magana sai yace,
"Yanzu na fahimci cewar da dadewa kana mulkin
kasarnan, don haka da farin ciki zan yi maka bayani.
11 Zaka iya tabbatarwa cewa bai kai kwana sha biyu ba
tun da nake zuwa Urushalima don yin sujada. 12 Da
suka same ni a haikali, ban yi jayayya ko kawo rudami
a tsakanin jama'a ba. 13 Don haka ba su da tabbas
akan abinda suke zargina a kansa yau. 14 Amma na
sanar da kai, bisa ga abin da suke kira darika, haka ni
ma nake bautawa Allah na kakanninmu. Na yi aminci
wajen kiyaye dukan abin da ke a rubuce a Attaurat da
litattafan annabawa. 15 Ina sa bege ga Allah, kamar
yadda za a yi tashin matattu, masu adalci da miyagu;
16 a kan haka kuma, nake kokarin zama mara abin
zargi a gaban Allah da mutane ina yin haka cikin
dukan al'amura. 17 Bayan wadansu shekaru na zo in
kawo wasu sadakoki da baikon yardar rai. 18 Cikin
kudurin yin haka, sai wasu Yahudawa daga kasar
Asiya suka iske ni a cikin ka'idodin tsarkakewa a
haikali, ba da taro ko ta da hargitsi ba. 19 Yakamata
wadannan mutanen su zo gabarka a yau, har idan
suna da wani zargi a kai na. 20 In kuwa ba haka ba
bari mutanennan su fada in sun taba iske ni da wani
aibu a duk lokacin da na gurfana a gaban majalisar
Yahudawa; 21 sai dai ko a kan abu daya da na fada
da babbar murya sa'adda na tsaya a gabansu, 'Wato
batun tashin matattu wanda ake tuhumata ake neman
yi mani hukunci yau.'" 22 Filikus yana da cikakken
sanin tafarkin Hanyar, shi yasa ya daga shari'ar. Yace
da su, "Duk sa'anda Lisiyas mai ba da umarni ya zo
daga Urushalima, zan yanke hukunci." 23 Sa'annan ya
umarci jarumin ya lura da Bulus, amma ya yi sassauci,
kada ya hana abokansa su ziyarce shi ko su taimake
shi. 24 Bayan wadansu kwanaki, Filikus da mai dakinsa
Druskila, ita Bayahudiya ce, ya kuma aika a kira Bulus
ya saurare shi game da bangaskiya cikin Kristi Yesu.
25 Amma sa'adda Bulus yake bayyana zancen adalci,
kamunkai, da hukunci mai zuwa, Filikus ya firgita
ya ce, "Yanzu ka tafi. Amma idan na sami zarafi an
jima, zan sake neman ka." 26 A wannan lokacin, yasa
zuciya Bulus zai bashi kudi, yayi ta nemansa akai-
akai domin yayi magana da shi. 27 Bayan shekaru
biyu, Borkiyas Festas ya zama gwamna bayan Filikus,
domin neman farin jini a wurin Yahudawa, ya ci gaba
da tsaron Bulus a gidan yari.

**25** Da Festas ya shiga lardin, kuma bayan kwana
uku, ya tashi daga Kaisariya ya tafi Urushalima.
2 Sai babban firist da manyan Yahudawa suka kawo
wa Festas sara a kan Bulus. 3 Suka roki tagomashi
wurin Festas ya kira Bulus zuwa Urushalima domin
su kashe shi a hanya. 4 Amma Festas ya amsa masu
cewa, Bulus dan sarka ne a Kaisariya, kuma ba da
dadewa ba shi da kansa zai koma can. 5 "Saboda haka
duk wadanda za su iya, su biyo mu. Idan akwai wani
laifi game da mutumin, sai ku zarge shi." 6 Bayan

kwana takwas ko goma, sai ya gangara zuwa Kaisariya.
Washegari ya zauna bisa kursiyin shari'a ya bada
umarni a kawo Bulus a gabansa. 7 Da Bulus ya iso,
Yahudawa daga Urushalima suka tsaya kusa, suka yi
ta kawo kararraki, amma basu iya tabbatar da su ba. 8
Bulus ya kare kansa ya ce, "Ban yi wa kowa laifi ba, ko
Yahudawa, ko haikali, ko kuma Kaisar." 9 Amma Festas
yana neman farin jini wajen Yahudawa, sabo da haka
ya tambayi Bulus ya ce, "Kana so ka je Urushalima in
shari'anta ka a can game da wadannan abubuwa?"
10 Bulus ya ce, "Ina tsaye a Ddakalin Shari'ar Kaisar
inda dole a shari'anta ni. Ban yi wa Yahudawa laifi
ba, kamar yadda ka sani sosai. 11 Idan lallai na yi
laifi kuma na yi abin da ya chanchanci mutuwa, ban
ki ba in mutu. Amma idan zarginsu karya ne, kada
kowa ya bashe ni gare su. Ina daukaka kara zuwa ga
Kaisar." 12 Bayan Festas ya tattauna da majalisa ya
amsa ya ce, "Kana kira ga Kaisar; za ka tafi wurin
Kaisar." 13 Bayan wadansu kwanaki, sarki Agaribas da
Barniki suka iso Kaisariya domin su ziyarci Festas. 14
Da ya kasance kwanaki da yawa, Festas ya fada wa
sarki labarin Bulus ya ce, "Akwai wani mutum dan
sarka da Filikus ya bari a kurkuku. 15 Sa'anda nake a
Urushalima, babban firist da dattawan Yahudawa suka
kawo kararsa gare ni, suka roka a kashe shi. 16 Game
da wannan na amsa na ce masu, ba al'adar Romawa ba
ce a ba da mutum tagomashi; sai wanda ake kararsa
an bashi zarafi ya kare kansa a gaban masu kararsa, ya
kuma bada hujjojinsa game da kararakin. 17 Saboda
haka, da duk suka taru ban bata lokaci ba, washegari
na zauna a kujerar shari'a, na ba da umarni a kawo
mutumin. 18 Da masu karar suka fadi kararsu, sai na
fahimci karar ba wani muhimmin abu a cikinta. 19 Sai
dai na ga cewa jayayya ce tsakanin su ta addini a kan
wani Yesu da ya mutu, wanda Bulus ya ce yana da
rai. 20 Na rasa yadda zan bincike wannan al'amarin,
sai na tambaye shi ko zai je Urushalima a shari'anta
shi kan wadannan abubuwa. 21 Amma da Bulus ya
nemi a lura da shi, Kaisar ya shari'anta shi, sai na
ba da umarni a ajiye shi har sai na aika shi wurin
Kaisar." 22 Agaribas yace wa Festas. "Zan so ni ma
in saurari mutumin nan." "Gobe za ka ji shi," in ji
Fostus. 23 Washegari Agaribas da Barniki suka zo
tare da kasaitaccen taro suka shiga dakin taro tare
da hafsoshi da shugabanin gari. Da Festas ya ba da
umarni, aka fito da Bulus wurinsu. 24 Festas ya ce,
"Sarki Agaribas da dukanku da kuke tare da mu a nan,
kun ga mutumin nan, dukan Yahudawa sun gana da ni
a Urushalima da nan kuma. Suna mani ihu cewa, bai
chanchanta a bar shi da rai ba. 25 Na gane bai yi wani
abin da ya chanchanci mutuwa ba; amma saboda ya
daukaka kara zuwa Kaisar, na yanke shawara in aika
shi. 26 Amma ba ni da wani dalili na musamman da
zan rubuta wasika ga Kaisar. Saboda wannan dalili na
kawo shi gabanku, masamman kai ya sarki Agaribas.
Domin in sami karin abin da zan rubuta game da shi.
27 Gama a ganina wauta ce in aika dan sarka ba tare
da na rubuta laifi a kansa ba."

**26** Sai Agaribas ya ce wa Bulus, "Za ka iya kare
kan ka." Sai Bulus ya daga hannunsa ya fara
kare kansa. 2 "Ina farinciki, ya sarki Agaribas, game
da saran da Yahudawa ke kawowa a kaina yau; 3
musamman ma don kai masani ne game da al'adun
Yahudawa da al'amuransu. Don haka, ina rokanka ka
yi hakuri ka saurare ni. 4 Hakika, dukan Yahudawa
sun san yadda na yi rayuwa ta daga kurciyata a kasa
ta, da kuma Urushalima. 5 Sun san ni tun farko, kuma
yakamata su yarda cewa na yi rayuwa kamar Bafarase,
darikan nan mai tsatsauran ra'ayi ta addininmu. 6
Yanzu ina tsaye a nan dominn a shari'anta ni, saboda
alkawalin da Allah ya yi wa ubanninmu. 7 Domin
wannan shine alkawalin da kabilunmu goma sha biyu
suka sa zuciya su karba, yayin da suke yin sujada da
himma ga Allah dare da rana. Saboda wanan bege,
Sarki Agaribas, Yahudawa ke tuhuma ta. 8 Me ya sa
wani zai yi tunani cewa abin mamaki ne Allah ya ta
da mattatu? 9 Da, na yi tunanin yin abubuwa gaba da
sunan Yesu Banazarat. 10 Na yi wadanan a Urshalima.
Na kulle masu bi da yawa a kurkuku, sanadiyar iko da
na samu daga wurin manyan firistoci, kuma da ake
kashe su ma, ina ba da goyon baya. 11 Na wahalshe
su sau dayawa a cikin dukan majamiu ina kuma yin
kokari in tilasta masu su yi sabo. Na yi gaba mai zafi
da su kuma na tsananta masu har zuwa birane na
wadansu kasashe. 12 A sa'anda nake yin wannan, na
tafi Dimashku da izinin manyan firistoci; 13 a cikin
tafiyata kuma, da tsakar rana, ya sarki, na ga haske
daga sama da ya fi rana sheki, ya haskaka kewaye da ni
da kuma wadanda ke tafiya tare da ni. 14 Da dukanmu
muka fadi kasa, na ji wata murya na magana da ni a
harshen Ibraniyawa tana cewa, 'Shawulu, Shawulu,
don me kake tsananta mani? Yana da wuya ka hauri
abin da ke mai tsini.' 15 Sai na ce, 'Wanene kai ya

Ubangiji?' Ubangiji ya amsa, 'Ni ne Yesu wanda kake
tsanantawa. 16 Yanzu ka tashi tsaye domin saboda
wannan dalili ne na bayyana gare ka in sanya ka,
ka zama bawa da mashaidi na game da abubuwan
da ka sani a kaina yanzu da wadanda zan bayyana
maka daga bisani; 17 Zan kubutar da kai daga wurin
mutane da kuma al'ummai da zan aike ka wurinsu, 18
domin ka bude idanunsu ka juyo su daga duhu zuwa
haske da daga ikon Shaidan zuwa ga Allah, domin
su karbi gafarar zunubai da gado da zan ba wadanda
na kebe wa kaina ta wurin bangaskiya gare ni.' 19
Saboda haka, sarki Agaribas, ban yi rashin biyayya da
wahayin da na gani daga sama ba; 20 amma, da farko
ga wadanda ke a Dimashku, sa'annan a Urushalima da
kasar Yahudiya gaba daya, da dukan Al'ummai, na yi
wa'azi domin su tuba su kuma juyo ga Allah, su yi
ayyukan da suka chanchanci tuba. 21 Domin wannan
dalili ne Yahudawa suka kama ni a cikin haikali kuma
suke kokari su kashe ni. 22 Allah ya taimake ni har
wa yau, domin in iya tsayawa gaban mutane kanana
da manya, in bada shaida game da iyakar abin da
annabawa da Musa suka fada zai faru; 23 wato lallai
Almasihu zai sha wahala, ya kuma zama na farko
da za'a rayar daga matattu ya kuma yi shelar haske
zuwa ga mutanen Yahudawa da Al'ummai." 24 Da
Bulus ya gama kare kansa, Festas ya yi magana da
babban murya, "Bulus, kana hauka; yawan iliminka
yasa ka hauka." 25 Amma Bulus ya ce, "Ba na hauka,
ya mai girma Festas; amma da karfin zuciya nake fadi
kalmomin gaskiya da na natsuwa. 26 Saboda sarkin ya
san wadannan abubuwa duka; shi ya sa nake magana
gabagadi, don na hakikance cewa, ba abin da ke a
boye gare shi; gama ba a yi wadannan abubuwa a boye
ba. 27 Ko ka gaskanta da annabawa, Sarki Agaribas?
Na sani ka gaskanta." 28 Agaribas ya ce wa Bulus,
"A cikin karamin lokaci kana so ka rinjaye ni ka mai
da ni Krista?" 29 Bulus ya ce, "Ina roko ga Allah,
domin ko a karamin lokaci ko a dogon lokaci, ba kai
kadai ba, amma har da wadanda ke sauraro na yau su
zama kamar ni, amma ban da wadannan sarkokin." 30
Sai sarki ya tashi tsaye tare da gwamna da Barniki
da dukan wadanda ke zaune tare da su; 31 da suka
bar dakin taron, suka ci gaba da magana da juna
suna cewa, "Wannan mutum bai yi wani abin da ya
chanchanci mutuwa ko kuma dauri ba." 32 Agaribas
ya ce wa Fastos, "Da mutumin nan bai daukaka kara
zuwa ga Kaisar ba da an sake shi."

27 Bayan da aka amince zamu tafi Italiya, sun mika
Bulus tare da wadansu daurarru a hanun wani
jarumi mai suna Yuliyas, daga batalian Agustas. 2
Muka shiga Jirgin ruwa daga Adramatiya, wanda ke
shirin tashi zuwa kusa da gefen tekun Asiya. Sai muka
je teku. Aristakus mutumin Tasalonika a Makidoniya
ya tafi tare damu. 3 Washegari muka sauka birnin
Sidon, inda Yuliyas ya nuna wa Bulus karamci ya
kuma yarda abokansa su bi shi don ya kula da su.
4 Daga wurin, muka bi teku muka tafi ta Tsibirin
Kubrus, domin matsananciyar iska da ke gaba damu.
5 Sa'adda muka ketare ruwa zuwa sassan Kilikiya da
Bamfiliya, muka zo Mira ta birnin Lisiya. 6 Anan,
jarumin ya sami jirgin ruwa daga Iskandariya wanda
za shi Italiya. Ya samu cikinsa. 7 Kwana da kwanaki
muna tafiya a hankali a karshe da kyar muka sauka
kusa da Sinidus, iska ta hana mu tafiya, sai muka
ratsa ta Karita, kusa da Salmina. 8 Da wahala muka
bi ta makurda har muka zo wani wuri da ake kira
Mafaka Mai Kyau wanda ke kusa da birnin Lasiya. 9
Yanzu mun dauki dogon lokaci, gashi lokacin azumin
Yahudawa ya wuce, tafiyar kuma ta zama da hatsari.
Bulus ya gargade su, 10 ya ce, "Jama'a, na gane
tafiyarmu zata zamar mana da barna da asara mai
yawa, ba ga kaya da jirgin kadai ba amma har da
rayukan mu." 11 Amma jarumin ya fi mai da hankali
ga maganar shugabansa da mai jirgin ruwan, fiye da
abubuwan da Bulus ya fadi. 12 Da shike tashar ba za ta
yi dadin zama da hunturu ba, mafi yawa sun ba da
shawara a bar wurin, in maiyiwuwa ne muga mun kai
birnin Finikiya, don mu yi hunturu a can. Finikiya
tashar jirgin ruwa ce a Karita, tana fuskantar arewa
maso gabas da kudu maso gabas. 13 Sa'adda iska daga
kudu ta huro a hankali, sun tsammaci bukatarsu ta
biya. Sai suka janye linzamin jirgin ruwan sukabi
ta Karita kusa da gaba. 14 Amma bayan wani dan
lokaci sai iska mai karfi da ake kira Yurokilidon, ta
fara bugun mu daga tsibirin. 15 Sa'adda Jirgin ruwan
ya kasa fuskantar iskar, sai muka bi inda iskar ta
nufa. 16 Sai muka bi ta inda muka sami kariya kusa
da wani dan tsibiri wanda ake kira Kauda; kuma da
wahala muka daure karamin jirgin a jikin babban. 17
Bayanda suka daga shi, sun yi amfani da igiyoyi don
su daure jirgin don gudun fadawa kan yashin Sirtis,
suka bar jirgin yana ta korarsu. 18 Mun yi ta fama
da hadari ba kadan ba, da gari ya waye ma'aikatan
jirgin suka fara zubar da kaya daga jirgin. 19 A rana ta

uku, ma'aikatan jirgi suka jefar da kaya daga cikin
jirgin da hannuwansu. 20 Kwanaki dayawa ba mu ga
hasken rana da taurari a bisan mu ba. Babban hadari
kadai ke dukanmu, duk mun fidda zuciya zamu tsira.
21 Sa'adda sun dade basu ci abinci ba, sai Bulus ya
tashi a gaban ma'aikatan jirgi yace, "Jama'a, da kun
saurare ni, da bamu tashi daga Karita ba, balle mu
fuskanci wannan barna da asarar. 22 Yanzu fa ina
karfafa ku kuyi karfin hali, domin ba wanda zai rasa
ransa a cikinku, sai dai jirgin kadai za a rasa. 23 Domin
daren da ya gabata mala'ikan Allah wanda ni nasa ne,
wanda kuma nake bautawa -mala'ikansa ya tsaya kusa
dani 24 ya ce, "Kada ka ji tsoro, Bulus, dole ka tsaya
gaban Kaisar, duba kuma, Allah cikin jinkansa ya baka
dukan wadannan da ke tafiya tare da kai. 25 Domin
haka, jama'a, kuyi karfin hali, domin na gaskanta da
Allah, kamar yadda aka fada mani haka zai faru. 26
Amma lallai dole ne a jefa mu kan wani tsibiri". 27
Sa'adda dare na goma sha hudu ya yi, ana ta tura mu
nan da can a cikin tekun Adriyat, wajen tsakar dare,
ma'aikatan jirgin sun tsammaci sun kusanci wata
kasa. 28 Da suka gwada sai suka iske kamu ashirin;
bayan dan lokaci kadan, sun sake aunawa sai suka iske
kamu sha biyar ne. 29 Tsoro ya kama su ko watakila a
jefar da mu kan duwatsu, sai suka jefa linzami hudu
daga karshen jirgin suka yi addu'a don gari ya waye da
sauri. 30 Ma'aikatan jirgin ruwan suna neman hanyar
da za su rabu da jirgin kuma sun jefa karamin jirgin
a cikin teku. Suka yi kamar zasu jefa wasu linzamai
daga gaban jirgin. 31 Amma Bulus ya ce ma jarumi
da sojojin, "Idan mutanen nan ba zasu tsaya cikin
jirgin ba, ba zaku tsira ba". 32 Sai sojojin suka yanke
igiyoyin jirgin suka kuma barshi ya fadi. 33 Da gari ya
fara wayewa, Bulus ya roke su duka su dan ci abinci,
ya ce, "Yau kwana goma sha hudu kenan ba ku ci
kome ba. 34 Saboda haka na roke ku ku ci abinci,
domin wannan saboda lafiyarku ne; kuma ko gashin
kanku daya baza ku rasa ba". 35 Da ya fadi haka sai ya
dauki gurasa ya yi godiya ga Allah a idanun kowa. Sai
ya gutsutsura gurasa ya fara ci. 36 Sai dukansu suka
karfafu suka kuma ci abinci. 37 Mu mutane 276 (dari
biyu da saba'in da shida) ne cikin jirgin. 38 Da suka ci
suka koshi, suka zubar da alkamar cikin teku domin
su rage nauyin jirgin. 39 Da gari ya waye, basu fahimci
kasar ba, amma suka hangi wani lungu a gacci, sai
suka yi shawara tsakaninsu ko su tuka jirgin zuwa
cikin lungun. 40 Sai suka yanke linzaman suka bar su
cikin tekun. Cikin lokaci guda suka kwance igiyoyin
da ke juya jirgin, suka saki filafilan goshin jirgi suka
nufi gabar tekun. 41 Da suka iso inda ruwa biyu suka
hadu, sai jirgin ya tsaya kasa. Gaban jirgin ya kafe
a nan, ba damar matsawa, sai kuma kurar jirgin ta
fara kakkaryewa saboda haukan rakuman ruwa. 42
Shirin sojojin ne su kashe 'yan kurkukun domin kada
su yi iyo su tsere. 43 Amma shi hafsan ya so ya ceci
Bulus, sai ya tsai da shirin su, ya ba da umarni, duk
masu iya iyo su yi tsalle su fada ruwa su kai gacci. 44
Sa'annan sauran mazajen su biyo baya, wadansu a kan
karyayyun katakai, wadansu akan abubuwan da ke a
jirgin. Ta haka ne dukanmu muka kai gacci lafiya.

28 Sa'adda muka sauka lafiya, sai muka ji cewa
sunan tsibirin Malita. 2 Mutanen garin sun nuna
mana alheri matuka don sun hura wuta don mu
ji dimi, saboda ruwan sama da sanyin da ake yi.
3 Amma sa'adda Bulus ya tara kiraruwa don hura
wuta, sai maciji saboda zafin wuta, ya fito ya nade
hannuwansa. 4 Da mazaunan garin suka ga maciji
ya nade hannuwansa, sai suka cema junansu, "Ba
shakka wannan mutumin mai kisan kai ne, koda
shike ya tsira daga Teku, sharia baza ta barshi da
rai ba". 5 Amma ya karkade macijin cikin wuta ba
tare da ya cutar da shi ba. 6 Sun saurara su gani ko
zai kumbura ko ya fadi matacce. Amma da suka jira
dan lokaci basu ga wata matsala ta same shi ba sai
suka canza tunaninsu sukace shi wani allah ne. 7 A
kusa da wannan wurin tsibirin akwai wasu gonakin
wani babban mutumin tsibirin, mai suna Babiliyas. Ya
karbe mu ya biya bukatun mu har kwana uku. 8 Ana
nan ashe mahaifin Babiliyas yana fama da zazzabi
da atuni. Bulus ya shiga, yayi masa addu'a, ya dibiya
masa hannu, ya sami warkarwa. 9 Sa'adda wannan ya
faru, sauran marasa lafiya da ke tsibirin sun zo sun
sami warkarwa. 10 Mutanen sun mutunta mu kwarai.
Yayin da muke shirin tafiya, sun bamu duk abinda
muke bukata. 11 Bayan watanni uku, mun shiga jirgin
Iskandariya wanda tun da hunturu yake a tsibirin mai
zane kamannin Tagwaye Maza. 12 Bayan saukar mu a
birnin Sirakus, mun yi kwana uku a wurin. 13 Daga
nan sai muka tafi, har muka zo birnin Rigiyum. Bayan
kwana daya iska mai karfi daga kudu ta taso, a cikin
kwana biyu muka iso Butiyoli. 14 A can muka iske
wasu 'yan'uwa suka roke mu mu zauna tare da su har
kwana bakwai. Ta wannan hanyar ce muka zo Roma.

15 Daga can da 'yan'uwa suka ji labarin mu, suka fito
don su tarbe mu tun daga Kasuwar Abiyas da kuma
Rumfuna Uku. Da Bulus ya gan su, ya yi wa Allah
godiya ya kuma sami karfafawa. 16 Sa'adda muka shiga
Roma, aka yardar wa Bulus ya zauna shi kadai tare da
sojan da ke tsaronsa. 17 Ana nan bayan kwana uku,
Bulus ya kira shugabannin Yahudawa. Bayan da suka
taru, sai ya ce masu, "Yan'uwa, ko da shike ban yi wa
kowa laifi ko keta al'adun Ubanninmu ba, duk da haka
an bashe ni daurarre tun daga Urushalima zuwa ga
hannunwan mutanen Roma. 18 Bayan tuhumata, sun
yi kudirin saki na, domin ban yi laifin da ya cancanci
mutuwa ba. 19 Amma da Yahudawa suka tsaya a kan
ra'ayin su, ya zama dole in daukaka kara zuwa ga
Kaisar, ba domin ina da wani dalilin da zan yi karar
al'ummata ba ne. 20 Saboda wannan ne na bukaci
ganinku in yi magana da ku. Saboda begen da Isra'ila
suke da shi ya sa nake daure da wannan sarkar". 21
Sai suka ce masa, "Bamu karbi wasiku daga Yahudiya
game da kai ba, babu kuma wani daga cikin 'yan'uwa
wanda ya kawo mana wani rahoto ko wata magana
game da kai. 22 Amma muna so mu ji daga gare ka
abin da kayi tunani ka kuma gani game da wannan
darikar, gama mun sani ana kushenta a ko'ina." 23
Sa'adda suka sa masa rana, mutane da dama suka
same shi a masaukinsa. Ya gabatarda zantattukan a
gare su, yana tabbatar da bayyanuwar mulkin Allah.
Har ya nemi ya rinjaye su a kan zancen Yesu, tun
daga attaurat ta Musa zuwa litattafan annabawa, ya
yi wannan tun daga safiya har yamma. 24 Wasu sun
kawar da shakkar abin da aka fada, amma wadansu
basu gaskanta ba. 25 Da shike ba su yarda da junansu
ba, sai suka tafi bayan da Bulus ya fadi kalma daya,
"Ruhu Mai Tsarki ya yi magana ta bakin annabi Ishaya
zuwa ga kakanninku. 26 Ya ce, 'Jeka wurin al'umman
nan ka ce, cikin ji zaku ji amma ba zaku fahimta ba;
zaku gani amma ba zaku gane ba. 27 Amma zuciyar
mutanen nan ta yi kanta, kunnuwansu sun ji da kyar,
sun rufe idanunsu; don kada su gani su gane, su
kuma ji da kunuwansu, kuma su fahimta da zuciyarsu,
domin su juyo ni kuma in warkar da su." 28 Saboda
haka, sai ku sani cewa wannan ceto na Allah an aikar
da shi zuwa ga Al'ummai, za su kuma saurara." 29
[Sa'adda ya fadi wannan zantattuka, Yahudawa suka
tashi, suna gardama da junansu.] 30 Bulus ya zauna
shekaru biyu a cikin gidan hayarsa, yana marabtar
duk wadanda suka zo wurinsa. 31 Yana wa'azin mulkin
Allah, yana koyarwa da al'amuran Ubangiji Yesu Kristi
gaba gadi. Ba wanda ya hana shi.

# Romawa

**1** Bulus, bawan Yesu Almasihu, kirayayye ya zama
manzo, kuma kebabbe domin bisharar Allah. 2
Wannan itace bisharar da ya alkawarta tuntuni ta
wurin annabawansa ta wurin tsarkakakkun littattafan
sa. 3 Game da Dansa ne, haifaffe daga zuriyar Dauda
ga zancen jiki. 4 Ta wurin tashinsa daga mattatu aka
aiyana shi ya zama Dan Allah ta wurin ikon Ruhu na
tsarkakewa. Yesu Almasihu Ubangijimu. 5 Ta wurinsa
muka karbi alheri da manzanci sabo da biyayyar imani
a cikin dukkan al'ummai, domin darajar sunansa.
6 cikin wadannan al'ummai kwa, ku ma an kiraku
ku zama na Yesu Almasihu. 7 Wannan wasika ga
dukkanku ne da kuke cikin Roma, kaunatattu na
Allah, kirayayyun mutane tsarkakakku. Bari alheri ya
kasance tare daku, da salama daga Allah Ubanmu, da
kuma Ubangiji Yesu Almasihu. 8 Abu na farko dai ina
yi wa Allah na godiya ta wurin Yesu Almasihu domin
ku duka, domin kuwa ana labarta bangaskiyarku ko
ina a cikin dukkan duniya. 9 Domin kuwa Allah shi ne
shaida ta, wanda nake bautawa a cikin ruhuna a cikin
bisharar Dansa, yadda a koyaushe na ke ambaton
ku. 10 A kullum ina roko cikin addu'o'ina domin ta
kowanne hali in yi nasarar zuwa gare ku da izinin
Allah. 11 Gama ina marmarin ganin ku, domin in
baku wata baiwa ta ruhaniya, domin in karfafa ku.
12 Wato ina dokin in sami cikakkiyar karfafawa a
cikin ku, ta wurin bangaskiyar junanmu, wato tawa
da taku. 13 Yanzu fa bana so ku rasa sani, yan'uwa,
sau da yawa nake yin niyyar zuwa wurinku, amma
har yanzu hakan din bata samu ba. Na so yin hakan
din ne don in sami 'ya'ya na ruhu a cikinku kamar
dai yadda ya ke a sauran Al'ummai. 14 Ina dauke da
nawayar Hellinawa da ta sauran jama'a, masu hikima
da marasa hikima. 15 Don a shirye na ke in sanar da
bishara a gare ku, ku da kuke cikin Roma. 16 Don kuwa
ni ba na jin kunyar yin bishara, don ita ce ikon Allah
don samun ceto ga duk wanda ya gaskata, da farko
dai Yahudawa kana kuma Hellinawa, 17 Domin a cikin
ta adalcin Allah ya bayyana daga bangaskiy zuwa
bangaskiya, kamar yadda yake a rubuce, "Mai adalci
zai rayu ne tawurin bangaskiya." 18 Domin fushin
Allah ya bayyana ne daga sama gaba da rashin ibada
da rashin adalci na yan'adam, wadanda suke danne
gaskiya ta wurin rashin adalcin su. 19 Dalili kuwa
abinda yakamata a sani game da Allah a bayyane ya
ke a gare su. Domin kuwa Allah ya bayyana masu
shi a zahiri. 20 Domin al'amuransa da ba'a iya gani a
bayyane suke tun halittar duniya. A na iya gane su
ta wurin halitatattun abubuwa. Wadannan al'amura
kuwa sune madawwamin ikonsa da Allahntakarsa.
Sakamakon haka, wadannan mutane ba su da hujja.
(aïdios g126) 21 Dalili kuwa, koda suna jin sun san Allah,
amma basu darajanta shi a matsayin Allah ba, ko kuma
su nuna masa godiya. Maimakon haka, suka zama
wawaye a cikin tunaninsu, zukatansu marasa tunani
sun duhunta. 22 Suna daukar kansu akan masu hikima
ne su, amma sai ga su sun zama wawaye. 23 Sun
musanya daukakar Allah madawwami da ta kamannin
abubuwan da basa dawwama, kamar mutum, da
tsuntsaye, da dabbobi masu kafafu hurhudu, da
masu jan ciki. 24 Saboda haka Allah ya bashe su
ga sha'awoyin kazantar zukatansu, su wulakantar
da jukunansu a junansu. 25 Sune suka musanya
gaskiyar Allah da karya, Kuma suke sujada da bauta
ga halittaccen abu, maimakon Mahaliccin, Wanda
yake abin yabo har abada. Amin. (aiōn g165) 26 Saboda
haka Allah ya bashe su, ga sha'awowin su na lalata da
wulakanci, har matansu suka canza ka'idar jima'i da
aka saba zuwa madigo mace da mace. 27 Mazajensu
ma suka sauya ka'idar jima'i tsakanin mace da miji
zuwa namiji da namiji suna yin aikin lalata. Maza su
na kwana da maza suna aikata aikin ban kyama, suna
kuwa girbe sakamakon aiknsu na ban kyama. 28 Tunda
shike ba su amince da Allah a cikkin al'amuransu ba,
Allah ya bashe su ga bataccen hankalinsu, su aikata
wadannan munanan abubuwa. 29 Suna cike da dukkan
rashin adalci, mugunta, kyashi, keta, kuma cike da
kishi, kisan kai, tarzoma, makirci, da kuma munanan
manufafofi. 30 Masu gulma da kage, makiyan Allah.
Masu tada zaune tsaye, masu taurin kai, da ruba,
masu kaga kowadanne miyagun abubuwa, kuma masu
kin yin biyayya ga iyayensu. 31 Masu duhun zuciya;
masu cin amana, marasa soyayya, da kuma rashin
tausayi. 32 Suna sane da tsarin Allah cewa masu
yin irin wadannan al'amura sun cancanci hukuncin
mutuwa. Ba kuwa yin wadannan abubuwan ka dai
suke yi ba, harma goyon bayan masu yinsu suke yi.

**2** Saboda da haka baka da hujja, kai mutum,
kai mai shara'antawa, domin kuwa abinda kake
shara'antawa akan wasu kana kada kanka da kanka.
Domin kuwa kai mai shar'antaawa kana aikata
wadannan abubuwa. 2 Amma mun san cewa shari'ar

Allah ta gaskiya ce sa'adda zata fado wa masu aikata
wadannan irin abubuwa. 3 Amma ka lura da wannan,
ya kai mutum, mai shara'anta masu aikata wadannan
ababuwa. Duk da shike kaima kana aikatawa. Kana jin
zaka kubucewa hukuncin Allah? 4 Ko kana raina falalar
alheransa da yake yi ta wajen jinkirin hukuncinsa,
da hakurinsa? Baka san cewa alheransa musanman
domin su kai ka ga tuba bane? 5 Amma saboda taurin
kanka da zuciyarka marar tuba, kana tanadarwa kanka
fushi, a ranar fushi, wato ranar bayyanuwar shari'ar
adalci ta Allah. 6 Zai baiwa kowanne mutum daidai
sakamakon ayyukansa: 7 Ga wadanda kuma suka nace
da yin ayyukan alheri ba fasawa, sun samarwa kansu,
yabo da daraja, da rai na har'abada. (aiōnios g166) 8
Amma ga masu son kai, wadanda suka ki yin biyayya
ga gaskiya, suka yiwa rashin adalci biyayya, fushi
da hasala mai zafi zai afko masu. 9 Allah kuma zai
sauko da bala'i da bakin ciki ga dukkan rayukan da
suka aikata mugunta, ga Yahudawa da fari, sannan
kuma Hellinawa. 10 Amma yabo daraja da salama
zasu kasance ga dukkan wadanda suka aikata ayukan
alheri, ga Yahudawa da fari sannan Hellanawa. 11
Domin kuwa Allah ba mai tara bane. 12 Ga wadanda
suka yi zunubi batare da shari'aba, zasu hallaka ba
tare da shari'a ba, ga wadanda suka yi zunubi cikin
shari'a kuma za'a hukunta su bisa ga shari'a. 13 Domin
kuwa ba masu jin shari'ar ne masu adalci agaban
Allah ba, amma masu aikatawa ne zasu samu barata.
14 Gama al'umai da basu san shari'a ba, bisa ga dabi'a
sun yi abinda ke na shari'a, sun kuma zame wa kansu
shari'a, koda shike basu da shari'ar. 15 Dalilin haka
kuwa sun nuna cewa ayukan da shari'a take bukata
na nan a rubuce a zuciyarsu. lamirinsu kuma na yi
masu shaida, tunanainsu kuma, ko dai yana kashe
su, ko kuma yana karesu. 16 hakanan kuma ga Allah.
Wannan zai faru ranar da Allah zai shara'anta asiran
boye na dukkan mutane, bisa ga bishara ta cikin Yesu
Almasihu. 17 Da shike kana kiran kanka Bayahude,
kana zaune akan shari'a, kana alfahari cikin Allah,
18 ka san nufinsa, ka kuma san abubuwan da suka
bambanta da hakan, ka kuma sami koyarwa cikin
shari'ar. 19 Da shike kana da gabagadi akan cewa kai
jagora ne ga makafi, haske ga wadanda suke cikin
duhu, 20 mai horo ga marasa hikima, mai koyar da
jirirai, kuma a cikin shari'ar kana da abin da ya shafi
sani da kuma gaskiya. 21 ku da kuke koyar da wadansu,
ba ku koyar da kanku? ku da kuke wa'azi kada ayi
sata, ba ku yin sata? 22 Ku da ke wa'azi kada ayi zina,
ba ku yin zina? ku da ke hana bautar gumaka, ba ku
yin sata a haikali? 23 ku masu murna da tinkaho cikin
shari'ar, ba kwa wulakanta Allah cikin kurakuranku
na rashin bin shari'a? 24 ''Domin kuwa an wulakanta
sunan Allah cikin Al'umai sabili da ku,'' kamar yadda
aka riga aka rubuta. 25 Lallai kuwa kaciya tana da
riba a gare ku, idan kuka kiyaye doka, amma idan
ku marasa bin doka ne kaciyarku ta zama rashin
kaciya. 26 domin kuwa idan mutum marar kaciya
zai kiyaye dukkan bukatun doka, baza'a iya daukan
rashin kaciyarsa a matsayin mai kaciya ba? 27 Sannan
idan mutum marar kaciya ta jini zai kiyaye dukkan
dokoki, ba zai iya shara'anta ku masu kaciya ta shari'a
ba? Haka kuma ya kasance ne domin kuna da shari'a
a rubuce da kuma kaciya amma ba kwa bin doka! 28
Domin shi kuwa ba Bayahude bane a waje; ba kuwa
mai kaciyar da aka tsaga fata ba. 29 Amma Bayahude
ne ta ciki, sanna kuma mai kaciyar zuciya da kuma
ruhu ba wasika ba, irin wanna mutumin yabonsa ba
daga wurin mutane yake zuwa ba, amma daga Allah.

3 To ina fifikon da bayahude yake dashi? Kuma ina
ribar kaciya? 2 Akwai muhimmancinsu ta kowacce
hanya. Tun farko dai, yahudawa ne aka dankawa
wahayi daga Allah. 3 Idan wasu yahudawa basu bada
gaskiya ba fa? Rashin bangaskiyarsu zai hana amincin
Allah aiki? 4 Bazai taba zama haka ba. Maimakon haka,
bari Allah ya zama mai gaskiya, ko da kowanne mutum
makaryaci ne. Kamar yadda aka rubuta, “Domin a
nuna kai mai adalci cikin maganganunka, kuma kayi
nasara a lokacin da aka kawo ka gaban shari'a.” 5
Amma idan rashin adalcinmu ya nuna adalcin Allah,
to me zamu ce? Allah ba marar adalci ba ne, wanda ke
aiwatar da fushinsa, ko kuwa? Ina magana bisa ga
tunanin mutuntaka. 6 Bazai taba zama haka ba. Domin
idan haka ne ta yaya Allah zai shar'anta duniya? 7
Amma idan gaskiyar Allah ta wurin karyata ta habaka
yabonsa, To me yasa ake shar'anta ni a matsayin
mai zunubi? 8 To me zai hana ace kamar yadda
ake fadin zancen karya a kanmu, wasu kuma sun
dauka cewa mun fadi hakan, “Bari muyi mugunta,
domin nagarta tazo?” Hukuncin su halal ne. 9 To me
kenan? Zamu ba kanmu hujja ne? ko kadan. Domin
mun riga munyi zargin yahudawa da hellinawa, da
cewar dukkansu, suna karkashin zunubi. 10 Kamar
yadda aka rubuta, babu wani mai adalci, babu ko

daya. 11 Babu wani mai fahimta. Babu wani mai
neman Allah. 12 Dukansu sun kauce hanya, dukansu
gaba daya sun zama marasa amfani. Babu mai aikin
nagarta, a'a, babu ko da guda daya. 13 Makogwaronsu
a bude yake kamar kabari. Harsunansu na dauke
da cuta. Dafin macizai na karkashin lebunansu. 14
Bakunansu cike suke da la'ana da daci. 15 Sawayensu
na saurin zuwa zubar da jini. 16 Tafarkinsu wahala ce
da lalacewa. 17 Wadannan mutane basu san hanyar
salama ba. 18 Babu tsoron Allah a idanunsu." 19
To mun san dai duk abin da shari'a tace, shari'a
na magana ne da wadanda ke karkashinta, domin
a rufe kowanne baki, domin dukan duniya ta bada
amsa a gaban Allah. 20 Domin a gabansa babu wanda
zai barata ta wurin ayukan shari'a. Domin ta wurin
shari'a ne sanin zunubi yazo. 21 Amma yanzu ba
tare da shari'a ba an bayyana sanin adalcin Allah,
wanda shari'a da annabawa suke shaidawa. 22 Wato,
adalcin Allah ta wurin bangaskiya cikin Yesu Almasihu
ga dukkan wadanda ke bada gaskiya. Domin babu
bambanci: 23 Domin duk sun yi zunubi sun kuma kasa
kaiwa ga darajar Allah, 24 Da alherinsa an baratar
da mu ta wurin fansar dake cikin Yesu Almasihu.
25 Amma Allah ya bayar da Yesu Almasihu wanda
yake hadayar fansa ta wurin bangaskiya cikin jininsa.
Ya mika Almasihu a matsayin tabbacin hukuncinsa,
sabo da kuma ketarewar zunubanmu na baya 26 cikin
hakurinsa. Duk wannan ya faru ne domin a bayyana
adalcinsa cikin wannan zamani, domin ya tabbatar da
kansa mai hukunci, kuma ya nuna shine mai baratar
da kowa saboda bangaskiya cikin Yesu. 27 To ina
fahariya? An fitar da ita. A kan wane dalilin? Don
ayyuka? A'a, amma ta dalilin bangaskiya. 28 Domin
wannan muka kammala cewar ana baratar da mutum
ta wurin bangaskiya ba tare da ayyukan shari'a ba.
29 Ko kuwa Allah Allahn yahudawa ne kadai? Shi ba
Allahn al'ummai bane? I, na al'ummai ne kuma. 30
Idan dai lallai Allah daya ne, zai baratar da mai kaciya
ta wurin bangaskiya, da marar kaciya kuma ta wurin
bangaskiya. 31 Mun kawar da shari'a kenan ta wurin
bangaskiya? ba zai taba kasancewa haka ba. Maimako
ma, muna inganta shari'a kenan.

4 Me kenan zamu ce game da Ibrahim, kakanmu
a jiki, me ya samu? 2 Domin idan Ibrahim ya
sami kubutarwa ta wurin ayuka, ai da ya sami dalilin
fahariya, amma ba a gaban Allah ba. 3 Kuma fa me
nassi ke fadi? "Ibrahim ya bada gaskiya ga Allah, sai
aka lisafta ta adalci gare shi." 4 Yanzu fa shi dake
yin ayyuka, ladansa ba a lisafta shi alheri ba ne,
amma abun da ke nasa. 5 Amma kuma shi da bai da
ayyuka kuma maimakon haka ya gaskanta ga wanda
ke kubutar da masu zunubai, bangaskiyarsa an lisafta
ta a misalin adalci. 6 Dauda ya yi furcin albarka bisa
mutumin da Allah ya lisafta mai adalci da rashin
ayyuka. 7 Sai ya ce, "Masu albarka ne wadanda aka
yafe laifofinsu, kuma wadanda zunubansu a rufe suke.
8 Mai albarka ne mutumin da ko kadan Ubangiji ba
zaya lisafta zunubin sa ba." 9 To albarkar da aka fadi
ko a bisansu wadanda aka yi wa kaciya ne kadai, ko
kuwa a bisan su ma marasa kaciya? Domin mun yi
furcin, "Bangaskiyar Ibrahim an lisafta ta adalci ce
agare shi." 10 Yaya aka lisafta ta? Bayan Ibrahim ya yi
kaciya, ko kuwa a rashin kaciya? Ba a cikin kaciya ba,
amma a rashin kaciya. 11 Ibrahim ya amshi alamar
kaciya. Wannan shi ne hatimin adalcin bangaskiyar
da ya ke da ita tun cikin rashin kaciyarsa. Albarkacin
wannan alama ce, ta sa shi ya zama uban dukkan
wadanda suka badagaskiya, ko da shike ba su da
kaciya. Wato ma'ana, adalci za a lisafta masu. 12
Wannan kuma yana da ma'anar cewa Ibrahim ya
zama uban kaciya ga wadanda suka fito ba domin
masu kaciya kadai ba, amma kuma domin wadanda
ke biyo matakin ubanmu Ibrahim. Kuma wannan
itace bangaskiyar da ya ke da ita a rashin kaciya.
13 Domin ba ta wurin shari'a aka bada alkawarin
nan da aka yi wa Ibrahim da zuriyarsa ba, wannan
alkawarin da ya ce zasu gaji duniya. Maimako, a ta
wurin adalcin bangaskiya ne. 14 Domin idan su da ke
na shari'a magada ne, bangaskiya bata da komai, kuma
alkawarin an wofintar da shi kenan. 15 Domin shari'a
ta kan jawo fushi, amma ta wurin rashin shari'a, babu
karya umarni. 16 Saboda wannan dalili haka ta faru
ta wurin bangaskiya, domin ya zama bisa ga alheri.
Kamar haka, alkawarin ya tabbata ga dukkan zuriya.
Kuma wannan zuriya ba zata kunshi wadanda suke da
sanin shari'a ba kadai, har ma da wadanda ke daga
bangaskiyar Ibrahim. Saboda shi ne uban dukkan
kowa, 17 kamar yadda aka rubuta, "Na maishe ka uba
ga kasashe masu yawa." Ibrahim na gaban aminin sa,
wato, Allah, mai bada rai ga mattatu kuma ya kan kira
abubuwan da basu da rai su kuma kasance. 18 Duk da
halin da ke a bayyane, Ibrahim ya gaskata ga Allah kai
tsaye game da abubuwan da ke nan gaba. Sai ya zama
uba ga kasashe masu yawa, kamar yadda aka ambata,

“... Haka zuriyarka zata kasance.” 19 Ba ya karaya a
bangaskiya ba. Ibrahim ya yarda da cewa jikinsa ya
rigaya ya tsufa (shekarun sa na misalin dari). Ya kuma
yarda da cewa mahaifar Saratu bata iya bada 'ya'ya
ba. 20 Amma domin alkawarin Allah, Ibrahim bai ji
nauyin rashin bangaskiya ba. Maimakon haka, ya sami
karfafawa a bangaskiyarsa sai ya daukaka Allah. 21
Ya na da cikakkiyar gamsuwa cewa idan Allah ya yi
alkawari, shi mai iya kammalawa ne. 22 Haka nan
ne kuma aka lisafta masa wannan a matsayin adalci.
23 To ba'a rubuta kawai damin amfaninsa kadai ba,
da aka lisafta dominsa. 24 A rubuce yake domin mu,
domin wadanda za'a lisafta su, mu da muka bada
gaskiya gare shi wanda ya tada Yesu Ubangijinmu
daga matattu. 25 Wannan shi ne wanda aka bashe shi
domin zunubanmu kuma an tada shi saboda fasar
mu.

5 Tun da shike mun sami barata, sabili da bangaskiya,
mun sami salama tare da Allah ta wurin Yesu
Almasihu. 2 . Ta wurin sa kuma mun sami iso zuwa ga
alheri inda muke tsayawa albarkacin bangaskiyarmu.
Muna murna da gabagadin da Allah ya ba mu game
da abin da zai faru, gabagadin da zamu dandana nan
gaba cikin daukakar Allah. 3 Ba kuwa haka kadai ba,
amma muna murna da shan wahalolinmu. Mun san
cewa shan wuya na haifar da 4 Jimiri, Jimiri kuma na
kawo amincewa, amincewa na kawo gabagadi game
da abin da zai zo nan gaba. 5 Wannan gabagadi wato
begen da muke da shi baya kunyatarwa, domin kuwa
an kwarara mana kaunar Allah a cikin zuciyarmu
ta wurin Ruhu Mai Tsarki, da aka ba mu. 6 Domin
kuwa ko yayin da muke raunana, Almasihu ya mutu
a lokacin da ke dai dai domin marasa ibada. 7 To ai
kuwa yana da wuya kwarai wani mutum ya yarda
ya mutu don mutumin kirki ma. Watakila, wani na
iyayin kasada ya yarda ya mutu don nagarin mutum.
8 Amma Allah ya tabbatar mana da kaunarsa a gare
mu, don kuwa tun muna masu zunubi, Almasihu ya
mutu domin mu. 9 Balle ma yanzu, da muka barata ta
wurin jininsa, za mu sami tsira daga fushin Allah. 10
Domin kuwa, in tun muna makiya, aka sulhunta mu
da Allah ta wurin mutuwar Dansa, balle ma, yanzu da
muka sami sulhu, zamu sami tsira ta wurin ransa.
11 Bama haka kadai ba, amma muna murna a cikin
Allah ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu, wanda
ta wurinsa ne muka sami wannan sulhu. 12 Saboda
haka, kamar yadda ta wurin mutum daya zunubi ya
shigo cikin duniya, ta haka mutuwa ta shigo ta dalilin
zunubi. 13 Domin kuwa tun kafin a bada shari'a,
zunubi na nan a duniya, amma ba' a lissafin zunubi
in da ba shari'a. 14 Duk da haka, mutuwa ta mallake
tun daga Adamu har Musa, har ma wadanda basu yi
zunubin keta umarni irin na Adamu ba, wanda yake
misalin mai zuwan nan a gaba. 15 Amma kyautar ba
kamar keta umarnin take ba. Domin in sabo da laifin
mutum dayan nan ne, da yawa suke mutuwa, haka ma
alherin sa da baiwarsa ta wurin mutum dayan nan,
Yesu Almasihu, sai baiwar ta wadata zuwa ga masu
yawa. 16 Domin kyautar ba kamar sakamakon wannan
da yayi zunubin bace. Ta haka din nan ne, hukuncin
nan mai tsanani ya zo sabo da zunubin mutum dayan.
Har yanzu dai, wannan baiwa ta yanci ta zo ne bayan
laifuffuka masu yawa. 17 Domin, idan sabo da laifin
mutum dayan nan ne, mutuwa ta mallake, saboda
dayan, haka ma wadanda suka karbi alheri mai yawa
da kuma baiwar adalci ta wurin ran, Yesu Almasihu. 18
Don haka, kamar yadda zunubin dayan ya sa hukunci
ya zo kan dukka, haka ma aikin adalci na dayan zai
kawo barata da rai ga mutane masu yawa. 19 Kuma
kamar yadda rashin biyayyar dayan ta sa mutane
masu yawan gaske su zama masu zunubi, haka ma ta
biyayyar dayan mutane da yawan gaske za su sami
adalci. 20 Amma shari'a ta zo, inda ta sa zunubi ya
habaka. Amma inda zunubi ya habaka, alheri ma ya
habaka ribin ribi. 21 Wannan ya faru ne, don kamar
yadda zunubi yai mallaka zuwa mutuwa, haka kuma
alheri ya mallaka zuwa adalci da rai na har abada ta
wurin Yesu Almasihu Ubangijin mu. (aiōnios g166)

6 Me kuwa zamu ce yanzu? Sai mu ci gaba da yin
zunubi domin Alheri ya yawaita? 2 Ba zai taba
faruwa ba. 'Yaya za'ace mu da muka mutu cikin zunubi
mu ci gaba da rayuwa cikin sa? 3 Ba ku san cewa duk
wadanda aka yi masu baftisma cikin Almasihu Yesu
an yi masu baftisma har ya zuwa mutuwarsa ne ba?
4 An kuwa binne mu tare da shi, ta wurin baftisma
cikin mutuwarsa. Haka kuma ya kasance ne domin
kamar yadda Almasihu ya tashi daga matattu cikin
daukakar Uba. Sakamakon haka muma zamu yi tafiya
cikin sabuwar rayuwa. 5 Domin kuwa idan muna tare
dashi cikin kamannin mutuwarsa zamu kuwa zauna
tare dashi har ga kamannin tashinsa. 6 Mun kuma
san cewa, an giciye wannan tsohon mutunmin nan

namu tare dashi, domin a hallaka jikin zunubi. wanna
kuwa ya kasance ne domin kada mu ci gaba da bautar
zunubi. 7 Duk kuma wanda ya mutu an ambace shi
a matayin adali akan zunubi. 8 Amma idan muka
mutu tare da Almasihu, mun bada gaskiya zamu yi
rayuwa tare dashi. 9 Muna da sanen cewa an tada
Almasihu daga matattu, don haka kuwa ba matacce
yake ba. Mutuwa kuma bata da iko a kansa. 10 Game
da mutuwar da yayi ga zunubi yayi sau daya kuma
domin dukka. Rayuwar da yake yi kuma yana yi wa
Allah ne. 11 Don haka ku ma sai ku dauki kanku a
matsayin matattu ga zunubi amma rayayyu ga Allah
cikin Almasihu Yesu. 12 Sabili da haka kada ku bar
zunubi yayi mulki a cikin jikinku, har ku yi biyayya
ga sha'awarsa. 13 Kada ku mika gabobin jikinku ga
zunubi a matsayin kayan aikin rashin adalci. Amma
ku mika kanku ga Allah rayayyu daga mutuwa. Ku
kuma mika gabobin jikinku ga Allah a matsayin kayan
aiki na adalci. 14 kada ku ba zunubi dama yayi mulki
a kanku, domin ba karkashin doka kuke ba, amma
karkashin alheri kuke. 15 To sai me? Sai mu yi zunubi
wai don ba a karkashin doka muke ba amma alheri. ba
zai taba faruwa ba. 16 Ba ku san cewa duk ga wanda
kuka mika kanku a matsayin bayi, a gareshi ku bayi
ne ba? Wannan fa gaskiya ne, ko dai ku bayi ne ga
zunubi wanda kaiwa ga mutuwa ko kuma bayi ga
biyayya wanda ke kaiwa ga adalci. 17 Amma godiya ta
tabbata ga Allah! domin da ku bayin zunubi ne, amma
kun yi biyayya daga zuciyarku irin salon koyarwar
da aka baku. 18 An 'yantar daku daga bautar zunubi,
an kuma maishe ku bayin adalci. 19 Ina magana da
ku kamar mutum, domin kasawarku ta nama da jini.
Kamar yadda kuka mika gabobin jikinku ga kazamta
da miyagun ayyuka, haka ma yanzu ku mika gabobin
jikinku a matsayin bayi na adalci. 20 Domin a lokacin
da kuke bayin zunubi, ku yantattu ne ga adalci. 21 A
wannan lokacin wanne amfani kuka samu na ayyukan
da yanzu kuke jin kunyarsu? Domin kuwa sakamakon
wadannan ayyuka shine mutuwa. 22 Amma yanzu
da da aka yantar daku daga zunubi aka mai da ku
bayin Allah, amfaninsa ku kuwa shine tsarkakewarku.
Sakamakon kuwa shine rai na har abada. **(aiōnios g166)**
23 Don kuwa sakamakon zunubi mutuwa ne. Amma
kyautar Allah itace rai madauwami cikin Almasihu
Yesu Ubangijinmu. **(aiōnios g166)**

7 'Yan'uwa, ko baku sani ba (domin ina magana
da wadanda suka san shari'a), cewar shari'a na
mulkin mutum muddin ransa? 2 Domin ta wurin
shari'a matar aure a daure take muddin mijinta nada
rai, amma idan mijinta ya mutu, ta kubuta daga
shari'ar aure. 3 To don haka idan, mijinta na da rai,
sai ta tafi ta zauna da wani mutumin, za'a kirata
mazinaciya. Amma idan mijin ya mutu, ''yantarciya ce
daga shari'a, domin kada ta kasance mazinaciya idan
ta auri wani mutum. 4 Domin wannan, 'yan'uwana, ku
ma an sa kun mutu ga shari'a ta wurin jikin Almasihu,
saboda a hada ku aure da wani, wato, ga wanda aka
tashe shi daga matattu, domin mu haifawa Allah
'ya'ya. 5 Domin sa'adda muke cikin jiki, ana motsa
dabi'armu ta zunubi dake cikin jikunan mu ta wurin
shari'a domin mu haifi 'ya'ya zuwa mutuwa. 6 Amma
yanzu an kubutar damu daga shari'a, mun mutu
daga abin da ya daure mu, domin mu yi bauta cikin
sabuntuwar Ruhu, ba cikin tsohon rubutun shari'a ba.
7 To me zamu ce kenan? ita shari'ar kanta zunubi ce?
ba zai taba faruwa ba. Duk da haka. Idan ba ta wurin
shari'a ba, ba zan taba sanin zunubi ba, in ba ta wurin
shari'a ba. Ba zan taba kyashin abin wani ba, har sai
da shari'a tace, “Kada kayi kyashi.” 8 Amma zunubi,
sai ya dauki zarafi ta wurin dokar, ya jawo dukkan
sha'awa dake cikina. Domin in da babu shari'a, zunubi
matacce ne. 9 Ada na rayu sau daya ba tare da shari'a
ba, amma da dokar ta zo, sai zunubi ya farfado, ni
kuma na mutu. 10 Dokar wadda ta kamata ta kawo
rai, sai na same ta matacciya. 11 Domin zunubin, ya
dauki zarafi ta wurin dokar, ya rude ni, kuma ta wurin
dokar ya kashe ni. 12 Domin haka, shari'ar na da
tsarki, dokar na da tsarki, adalci da kuma kyau. 13 To
abu mai kyau ya zamar mani mutuwa kenan? ba zai
taba zama haka ba. Amma zunubi, domin ya nuna shi
zunubi ne ta wurin abin da ke mai kyau, sai ya kawo
mutuwa a cikina. Wannan ya kasance haka ne domin
ta wurin dokar, zunubi ya zama cikakken zunubi. 14
Domin mun san shari'a mai Ruhaniya ce, amma ni ina
cikin jiki. An sai da ni karkashin bautar zunubi. 15
Domin ni ma ban fahimci abin da nake aikatawa ba.
Domin abin da nake so in aikata, ba shi nake aikatawa
ba, kuma abin da bana so, shi nake aikatawa. 16 Amma
idan na aikata abin da bana so, na amince da shari'a
kenan, cewar shari'a nada kyau. 17 Amma yanzu ba
ni ke aikata abin ba, amma zunubi da ke zaune a
cikina. 18 Domin na san a cikina, wato cikin jikina,

babu wani abu mai kyau. Domin marmarin aikata abu
mai kyau na tare da ni, amma ba ni iya aikatawa. 19
Domin abu mai kyau da na ke so in aikata bana iyawa,
amma muguntar da ba na so ita na ke aikatawa. 20 To
idan na yi abin da ba ni so in aikata, wato kenan ba
ni bane ke aikatawa, amma zunubin da ke zaune a
cikina. 21 Don haka, sai na iske, akwai ka'ida a cikina
dake son aikata abu mai kyau, amma kuma ainihin
mugunta na tare dani. 22 Domin a cikina ina murna
da shari'ar Allah. 23 Amma ina ganin wasu ka'idoji
daban a gabobin jikina, su na yaki da wannan sabuwar
ka'idar da ke cikin tunanina, suna kuma sanya ni
bauta ta wurin ka'idar zunubi wadda ke cikin gabobin
jikina. 24 Ni wahalallen mutum ne! wa zai kubutar
dani daga wannan jiki na mutuwa? 25 Amma godiya
ga Allah ta wurin Yesu Almasihu Ubangijinmu! Domin
haka ni kaina a wannan hannu bisa ga tunani na ina
bautawa shari'ar Allah. Duk da haka, ta wani gefen
ina bautawa ka'idar zunubi da ke tare da jikina.

8 Saboda haka babu kayarwa yanzu ga wadanda ke
cikin Almasihu Yesu. 2 Domin ka'idar ruhun rai
a cikin Almasihu Yesu ta maishe mu 'yanttatu daga
ka'idar zunubi da mutuwa. 3 Saboda abin da shari'a
bata iya aikatawa ba domin kasawa ta wurin jiki, Allah
ya yi. Ya aiko da dansa a kamanin jiki mai zunubi
domin ya zama hadaya domin zunubi, sai ya yi Allah
wadai da zunubi a cikin jiki. 4 Ya yi haka domin
bukatar shari'a ta sami cika a cikinmu, mu da muke
tafe ba ta gwargwadon jiki ba, amma ta gwargwadon
ruhaniya. 5 Wadanda ke rayuwa gwargwadon jiki
sukan lura da al'amuran jiki, amma su da ke rayuwa a
gwargwadon Ruhu sukan mai da hankali ga al'amuran
Ruhu. 6 To kwallafa rai ga jiki mutuwa ce, amma
kwallafa rai ga Ruhu rai ne da salama. 7 Haka yake
domin kwallafa rai ga jiki gaba yake da Allah, gama
baya biyyaya ga shari'ar Allah, balle ma ya iya. 8
Wadanda ke a jiki ba su iya faranta wa Allah zuciya. 9
Duk da haka, ba ku cikin jiki amma a cikin Ruhu, idan
gaskiya ne, Ruhun Allah na rayuwa cikinku. Amma
idan wani ba shi da Ruhun Almasihu, shi ba na sa
bane. 10 In Almasihu na cikinka, jikin ka fa matacce
ne ga zunubi, amma ruhu na rayuwa bisa ga adalci.
11 Idan Ruhun wanda ya tada Yesu daga matattu na
raye a cikinku, to shi wanda ya tada Almasihu da ga
matattu za ya bada rai ga jikinku masu matuwa ta
wurin Ruhunsa, da ke rayuwa a cikin ku. 12 To, 'yan'
uwa, muna da hakki amma ba bisa jiki ba, da za mu
yi rayuwa bisa ga dabi'ar jiki. 13 Gama idan kun yi
rayuwa gwargwadon jiki, za ku mutu kenan, amma
idan ta wurin Ruhu ku ka kashe ayyukan jiki, za ku
rayu. 14 Gama duk wadanda Ruhun Allah ke bishe
su, su 'ya 'yan Allah ne. 15 Gama ba ku karbi ruhun
bauta da ke sa tsoro ba. Maimakon haka, kun karbi
ruhun diyanci, ta wurinsa muke tadda murya muna
kira, “Abba, Uba!” 16 kansa na bada shaida tare da
namu ruhun cewa mu 'ya'yan Allah ne. 17 Idan mu
'ya'ya ne, ai mu magada ne kenan, magadan Allah.
Kuma mu magada ne tare da Almasihu, hakika idan
mun sha wahala tare da shi za a kuma daukaka mu
tare da shi. 18 Gama na yi la'akari cewa wahalonin
zamanin nan ba su isa a kwatanta su da daukakar
da za'a bayyana mana ba. 19 Saboda yadda halitta
ke marmarin bayyanuwar 'ya'yan Allah. 20 Gama
an kaskantar da halitta ga banza, ba da nufin ta ba,
amma na shi wanda ya kaskantar da ita. Ta na cikin
tabbacin alkawarin. 21 Cewa halitta kanta za ta kubuta
daga bautar rubewa, kuma za a kawo ta zuwa ga
'yantarwa na yabon daukakar 'ya'yan Allah. 22 Gama
mun sani dukan halitta na nishi da zafin nakuda tare
har ya zuwa yanzu. 23 Ba haka kadai ba, amma ko mu
kanmu, da ke nunar farko na Ruhu—mu kanmu muna
nishi acikin mu, muna jiran diyancinmu, wato ceton
jikinmu kenan. 24 Gama ta wanan hakikancewa aka
cece mu. Amma dai abin da muke da tabbacin zai faru
ba mu gan shi ba tukuna, domin wanene wa ke begen
tabbatacce abin da yake gani? 25 Amma idan muna da
tabbacin abin da ba mu gani ba tukuna, to sai mu jjira
shi da hakuri. 26 Hakanan, Ruhu kuma ke taimako
a kasawarmu. Gama ba mu da san yadda zamu yi
addu'a ba, amma Ruhu kansa na roko a madadinmu da
nishe-nishen da ba'a iya ambatawa. 27 Shi da ke bidar
zuciya yana sane da tunanin Ruhu, domin yana roko a
madadin masu badagaskiya ta wurin nufin Allah. 28
Mun san cewa ga wadanda ke kaunar Allah, yakan
aikata dukan al'amura domin su zuwa ga alheri, ga
duk wadanda aka kira bisa ga nufinsa. Dukan abubuwa
sukan zama alheri. 29 Saboda wadanda ya sani tuntuni
su ne ya kardara su zama da kamanin dansa, domin ya
zama dan fari a cikin 'yan'uwa masu yawa. 30 Su da ya
kaddara, ya kiraye su. Wadanda ya kira, su ya kubutar.
Su da ya kubutar, sune kuma ya daukaka. 31 Me zamu
ce game da wadannan al'amura? Idan Allah na tare da
mu, wake gaba da mu? 32 Shi da baya hana dansa ba,

amma ya bada shi a madadinmu dukka, me zai hana
shi bamu dukkan abubuwa a yalwace tare da shi? 33
Wa zaya kawo wata tuhuma ga zababbu na Allah?
Allah ne ke “yantarwa. 34 Wanene ke hukumtawa?
Almasihu ne da ya mutu sabili da mu har ma fiye da
haka, shi wanda kuma aka tasar. Yana mulki tare da
Allah a wuri mai daukaka, shi ne kuma ya ke roko
sabili da mu. 35 Wa za ya raba mu da kaunar Allah?
Kunci, ko bacin rai, ko tsanani, ko yunwa, ko tsiraci,
ko hadari, ko takobi? 36 Kamar yadda aka rubuta,
“Saboda kai ake kisanmu dukkan yini. An mai da mu
kamar tumaki yanka.” 37 A dukan al'amuran nan mun
fi karfi a ce da mu masu nasara ta wurin shi da ke
kaunar mu. 38 Gama na tabata cewa ko mutuwa, ko
rai, ko mala'iku, ko mulkoki, ko al'amuran yanzu, ko
al'amura masu zuwa, ko iko, 39 ko tsawo, ko zurfi, kai
ko wace irin halitta, ba su isa su raba mu da kaunar
Allah, da ke a cikin Almasihu Yesu Ubangijin mu ba.

**9** Gaskiya ne nake gaskiya nake fada cikin Almasihu.
Ba karya nake yi ba. Lamirina, na shaida a cikin
Ruhu Mai Tsarki. 2 cewa ina da matukar bakin-ciki
da takaici marar karewa a zuciyata. 3 Dama ace, a
la'anta ni, in rabu da Almasihu saboda 'yan'uwana,
wato dangina da suke zuriyata bisa ga jiki. 4 Sune
Isra'ilawa, sun sami karbuwa, da daukaka, da baiwar
shari'a, da yi wa Allah sujada, da alkawarai. 5 Dukkan
ubanni nasu ne daga cikinsu Almasihu ya fito bisa ga
jiki- wanda shi ke Allah bisa kowa. Yabo ya tabbata a
gare shi har abada. Amin. (aiōn g165) 6 Amma ba wai
alkawarin Allah ya kasa ba ne, ba dukkan Isra'ilawa ne
suke Isra'ilawa na gaskiya ba. 7 Haka nan, ba dukkan
zuriyar Ibrahim ne 'ya'yansa ba. Amma ''ta wurin
Ishiyaku ne za'a kira zuriyarka.'' 8 Yana nuna mana
cewa ba 'ya'yan jiki su ne 'ya'yan Allah ba. Amma
'ya'yan alkawari ne ake kirga su, kuma aka kebe su. 9
Wanna ce kalmar alkawari, ''badi warhaka zan dawo,
Saratu kuwa zata sami da.'' 10 Amma ba wannan
kadai ba, bayan Rifkatu ta dauki ciki daga gun mijinta,
ubammu Ishiyaku. 11 Yaran nan kafin ma a haife su,
balle ma a ce sun yi wani abu mai kyau ko laifi, saboda
zaben da Allah yayi, bai danganta da abin da suka
yi ba, ko don aiki ba, amma don shine mai kira— 12
kamar yadda Ya ce, mata, “babban zaya yiwa karamin
bauta,'' haka nassi yace, 13 ''Kamar yadda aka rubuta:
“Yakubu na ke kauna, amma Isuwa na ki shi.” 14 To
me zamu ce kenan? Allah ya yi rashin adalci kenan?
Ko kadan. 15 Gama ya ce wa Musa, ''Ina nuna jinkai ga
wanda zan yi wa jinkai, zan ji tausayi ga wanda zan
tausaya masa.'' 16 Saboda haka, ba don wanda ke da
aniya ba ne, ko kuwa wanda yake kokari ba, amma
saboda Allah mai nuna jinkai. 17 Gama nassi ya ce da
Fir'auna, '' Saboda wannan dalilin ne, na tada kai, don
in nuna ikona mai karfi a kanka, don sunana ya yadu
ga dukkan duniya.'' 18 Ta haka Allah ya nuna jinkansa
ga wanda ya so, ya taurarar da zuciyar wanda ya ga
dama. 19 Za kuce mani, to don me, ''Yake kama mu
da llaifi? Wa ya taba yin jayayya da nufinsa?'' 20 In
ma mun duba, kai mutum wanene kai da zaka ja da
Allah? Ko abin da aka gina zai ce wa magininsa, ''Don
me yasa ka ginani haka?'' 21 Ko maginin ba shi da
iko akan yimbu daya da zai gina tukunya mai daraja,
wata kuma tukunyar don kowanne irin aiki? 22 In ace
Allah, dake niyyar nuna fushinsa da ikonsa, ya sanu,
sai ya jure da matukar hakuri mai yawa da tukwanen
fushi da ya shirya don hallakarwar fa? 23 To ko ma ya
yi haka don ya nuna yalwar daukakarsa da take dauke
da alheri, wanda ya shirya don daukakarsa tun farko?
24 Zai yiwu ma ya yi haka ne domin mu, mu da ya kira,
ba ma daga cikin Yahudawa kadai ba, amma har ma
daga cikin al'ummai? 25 Kamar yadda ya ce a cikin
littafin Yusha'u: ''zan kira wadanda ba mutanena
ba mutanena, da kuma kaunatattunta wadanda ba
kaunatattu ba. 26 Zai zama kuma a inda aka ce da
su, “ku ba mutanena bane, za a kisa su 'ya'yan Allah
mai rai.”' 27 Ishaya ya yi kira game da Isra'ila, ''in a
ce yawan 'ya'yan Isra'ila zasu zama kamar yashi a
bakin teku, ragowarsu ne kawai za su sami ceto. 28
Ubangiji zai tabbatar da cikar kalmarsa a duniya, ba
kuwa da dadewa ba. 29 Yadda Ishaya ya rubuta ada,
''In da ba Ubangiji mai runduna bai bar mana zuriya
ba, da zamu zama kamar Saduma, da kuma an maida
mu kamar Gomarata. 30 To me za mu ce kenan? Ko
al'ummai, da ba sa neman adalci, sun samu adalci ta
wurin bangaskiya. 31 Amma Isra'ila, wadanda suka
nemi adalcinsu ta wurin shari'a, ba su kai ga gaci ba.
32 To don me? don ba su neme shi da bangaskiya ba,
amma ta ayyuka. Sun yi tuntube a kan dutse da zai sa
laifi. 33 Kamar yadda aka rubuta, “Ga, shi na ajiye
dutse a kan Sihiyona dutsen tuntube mai sa laifi. Ga
wanda ya bada gaskiya gare shi ba zai ji kunya ba.”

**10** 'Yan'uwana, muradin zuciyata da dukkan addu'oi
na ga Allah dominsu shine don su sami ceton.

2 Domin na shaida game da su cewa suna da kwazo
game da Allah, amma ba a kan sani ba. 3 Don, ba su
da sani akan adalcin Allah, suna kokarin tabbatar da
adalcin kansu. Ba su bada kan su ga adalcin Allah
ba. 4 Gama Almasihu shi ne cikar doka zuwa ga
adalci ga dukkan wadanda suka gaskata. 5 Musa kam
ya rubuta game da adalci da zai samu ta shari'a:
''mutumin da ya aikata adalcin shari'a, zai rayu ta
wurin wannan adalcin.'' 6 Amma adalcin da ya zo
ta wurin bangaskiya yace, ''Kada ku ce a zuciyarku,
wa zai hau zuwa sama?''(don ya sauko da Almasihu
kasa). 7 Kada ku ce, ''Wa zai gangara zuwa kasa?''
(Wato wa zai fito da Almasihu daga cikin matattu).
(Abyssos g12) 8 Amma me yake cewa? “kalmar tana
kusa da kai a cikin bakinka da kuma cikin zuciyarka.”
Wato kalmar bangaskiya, wadda muke shaidawa. 9
Don idan da bakinka, ka shaida Yesu Ubangiji ne,
kuma ka gaskata a zuciyarka cewa Allah ya tashe shi
daga matattu, za ka sami ceto. 10 Don da zuciya ne
mutum yake gaskatawa zuwa ga adalci, da kuma baki
ne yake shaida zuwa ga ceto. 11 Don nassi na cewa,
''Duk wanda ya gaskata da shi ba zai ji kunya ba,'' 12
Gama ba bambanci tsakanin Bayahude da Ba'al'ume.
Gama dukkansu Ubangijinsu daya ne, Shi mayalwaci
ne ga dukkan wanda ya kira shi. 13 Duk wanda ya kira
sunan Ubangiji zai sami ceto. 14 To ta yaya zasu kira
ga wanda basu gaskata ba? Kuma ta yaya zasu gaskata
ga wanda ba su taba jin labarinsa ba? 15 Kuma ta yaya
zasu ji in ba ayi masu wa'azi ba? Kuma ta yaya zasu
yi wa'azin in ba an aike su ba? - Kamar yadda yake
a rubuce, “Ina misalin kyau na kafafun wadanda ke
shaida labarin farin ciki na abubuwa masu kyau!” 16
Amma ba dukkansu ne suka ji bishara ba. Gama Ishaya
ya ce, ''Ubangiji, wa ya gaskata da sakon? 17 Saboda
haka bangaskiya na zuwa ta wurin ji, jin kuwa daga
maganar Almasihu. 18 Amma na ce, “ko basu ji ba
ne? I, tabbas'' muryarsu ta kai dukkan duniya, kuma
kalmominsu sun kai har karshen duniya.'' 19 yau, na
ce, ''Ko Isra'ila basu sani ba ne?'' Da farko Musa ya ce,
“Zan sa kuyi fushi da kishi da abin da ba al'umma ba.
Abin da nake nufi nan shine al'ummar da basu da
fahinta, zan more su, in tayar maku da hankali.'' 20
Amma Ishaya da karfin hali ya ce, ''Ga wadanda basu
neme ni ba suka same ni. Na bayyana ga wadanda
basu nemi ni ba. 21 ''Amma ga Isra'ila kam ya ce, ''
na mika hannu na ga masu rashin biyayya dukkan
tsawon rana, domin su mutane ne masu taurin kai.''

11 Sai na ce, Allah ya ki mutanensa ne? Ba zai
taba yiwuwa ba. Domin ni ma ba-Isra'ile ne, na
zuriyar Ibrahim, a kabilar Bilyaminu. 2 Allah bai ki
mutanen sa da ya ke da rigyasaninsu ba. Ko kun san
abin da nassi ya ce game da Iliya, yadda ya kai karar
Isra'ila a gaban Allah? 3 Ya ce, ''Ubangiji, sun kashe
annabawanka, sun rushe alfarwanka kuma, Ni kadai
ne na rage, ga shi suna neman su kashe ni.'' 4 Amma
wacce amsa ce Allah ya ba shi? Ya ce, ''Ina da mutane
dubu bakwai da na kebe don kaina, da ba su taba
rusuna wa Ba'al ba.'' 5 Ban da haka ma, ban da haka
ma a wannan lokacin akwai sauran zabe na alheri. 6
Amma tun da ta wurin alheri ne, ba ga ayyuka ba.
In ba haka ba, alheri ba zai zama alheri ba kenan. 7
Sai kuma me? Abin da Isra'ila ke nema, ba su samu
ba, amma zababbun sun same shi, saura kuma sun
taurare. 8 Kamar yadda yake a rubuce, ''Allah ya ba
su ruhun rashin fahimta, ga idanu amma ba za su
gani ba, ga kunnuwa amma ba za su ji ba, har zuwa
wannan rana.'' 9 Dauda kuma ya ce, ''bari teburinsu
ya zama taru, da tarko, ya zama dutsen tuntube da
abin ramako a gare su. 10 Bari idanunsu ya duhunta
domin kada su gani; bayansu kuma a duke kullum.''
11 Na ce, ''sun yi tuntube domin su fadi ne?'' Kada
abu kamar haka ya faru. A maimakon haka, juyawa
baya da suka yi ya sa, ceto ya zo ga Al'ummai, domin
ya sa su kishi. 12 Idan yanzu juyawa baya da sun yi
ya zama arziki ga duniya, rashin su kuma arziki ga
Al'ummai, yaya kwatancin girmansa zai kasance in
sun zo ga kammala? 13 Yanzu ina magana da ku ku da
ke Al'ummai. Tunda yake ni ne manzo ga Al'ummai,
ina kuma fahariya cikin hidimata. 14 Yana yiwuwa in
sa ''yan'uwa na kishi, domin mu ceci wadansu su. 15
Idan kinsu ya kawo sulhuntawa ga duniya, Karbarsu
kuma zata zama yaya? Zata zama rai ne daga mutuwa.
16 'ya'yan farko sunan haka ma kakkabensu yake, Idan
saiwar itace na nan, haka ma rassan za su zama. 17
Amma idan an karye wasu daga cikin rassan, idan ku
rassan zaitun na ainihi ne, da aka samu daga cinkinsu,
kuma idan kuna da gado tare da su, acikin saiwar
itacen zaitun din. 18 Kada ku yi fahariya a kan rassan.
Amma idan kuka yi fahariya to ba ku bane masu
karfafa saiwar amma saiwar ce ke karfafa ku. 19 Kana
iya cewa, ''An karye rassan domin a same ni a ciki.''
20 Wannan gaskiya ne! Saboda rashin bangaskiyarsu
ne ya sa aka karye su daga rassan, amma ku tsaya da
karfi acikin bangaskiyarku. Kada ku dauki kanku fiye

da yadda ya kamata, amma ku ji tsoro. 21 Domin idan
Allah bai bar ainihin rassan ba, to ba zai bar ku ba. 22
Ku duba yadda irin ayyuka masu tsananni na Allah. Ta
daya hannun kuma, tsanannin kan zoa kan Yahudawa
wadanda suka fadi. Har 'ila yau jinkai Allah ya zo
maku, idan kun cigaba cikin alherinsa baza a sare ku
ba. Amma in kun ki za a sare ku. 23 Hakanan, idan ba
su ci gaba cikin rashin bangaskiyarsu ba, za a maida
su cikin itacen. Domin Allah zai iya sake maida su. 24
Idan an yanke ka daga itacen zaitun da ke na jeji, har
ya yiwu an hada ka cikin itacen zaitun na ainihi, yaya
kuma wadannan Yahudawa wadanda sune ainihin
rassan, da za'a maido cikin zaitun da ke na ainihi?
25 Yan'uwa, ba na so ku kasance cikin duhu a game
da wannan asirin, domin kada ku zama da hikima
cikin tunaninku. Wannan asirin shine cewa wannan
taurarewa ta faru a Isra'ila, har sai da Al'ummai
suka shigo ciki. 26 Ta haka dukan Isra'ila za su tsira,
kamar yadda yake a rubuce: ''Daga cikin Sihiyona
mai Kubutarwa zai fito; Zai kawar da kazanta daga
cikin Yakubu. 27 Wannan zai zama alkawarina da su,
sa'adda na kawar da zunubansu.'' 28 A wani bangaren
kuma game da bishara, su makiya ne amamadinku, ta
wani fannin kuma bisa ga zabin Allah su kaunattatu
ne saboda ubanni. 29 Domin baye-baye da kiran Allah
basa canzawa. 30 Domin ku ma da ba ku yin biyayya
ga Allah, amma yanzu kun sami jinkai saboda rashin
biyayyarsu. 31 Ta wannan hanyar dai, wadannan
Yahudawan sun zama marasa biyayya. Sakamakon
haka shine ta wurin jinkan da aka nuna maku, suma
su samu jikai yanzu. 32 Domin Allah ya rufe kowa ga
rashin biyayya, domin ya nuna jinkai ga kowa. (eleēsē
g1653) 33 Ina misalin zurfin wadata da kuma hikima da
sani na Allah! Hukunce-hukuncensa sun fi gaban a
bincika, hanyoyinsa kuma sun fi gaban ganewa! 34
Don wanene ya san tunanin Ubangiji? Wanene kuma
ya zama mai bashi shawara? 35 Ko kuma, wanene ya
fara ba Allah wani abu, domin a biya shi?'' 36 Daga
wurinsa ne, ta wurinsa ne kuma, a gare shi ne kuma
dukan abu suka fito. A gare shi daukaka ta tabbata
har abada. Amin. (aiōn g165)

**12** Ina rokon ku 'yan'uwa, saboda yawan jinkan nan
na Allah, da ku mika jikunanku hadaya mai rai,
mai tsarki kuma abar karba ga Allah. wannan itace
hidimarku ta zahiri. 2 Kada ku kamantu da wannan
duniya, amma ku sami canzawa ta wurin sabunta
tunaninku, kuyi haka don ku san abin da ke nagari,
karbabbe, kuma cikakken nufin Allah. (aiōn g165) 3 Don
ina cewa, saboda alherin da aka bani, ka da waninku
ya daukaka kansa fiye da inda Allah ya ajiye shi; a
maimakon haka ku kasance da hikima, gwargwadon
yadda Allah yaba kowa bangaskiya. 4 Domin muna
da gababuwa da yawa a jiki daya, amma ba dukansu
ne ke yin aiki iri daya ba. 5 haka yake a garemu,
kamar yadda muke da yawa haka cikin jikin Almasihu,
dukkanmu gabobin juna ne. 6 Muna da baye-baye
dabam-dabam bisa ga alherin da aka bayar a gare mu.
Idan baiwar wani anabci ne, yayi shi bisa ga iyakar
bangaskiyarsa. 7 In wani yana da baiwar hidima, sai
yayi hidimarsa. Idan baiwar wani koyarwa ce, yayi
koyarwa. 8 Idan baiwar wani karfafawa ce, yayi ta
karfafawa; Idan baiwar wani bayarwa ce, yayi ta da
hannu sake; Idan baiwar wani shugabanci ne, yayi shi
da kula; Idan baiwar wani nuna jinkai ne, yayi shi da
sakakkiyar zuciya. 9 Ku nuna kauna ba tare da riya ba.
Ku Ki duk abin da ke mugu ku aikata abin da ke nagari.
10 Akan kaunar 'yan'uwa kuma, ku kaunaci juna yadda
ya kamata; akan ban girma kuma, ku ba juna girma. 11
Akan himma kuma, kada ku yi sanyi; akan ruhu kuma,
ku sa kwazo; Game da Ubangiji kuma, ku yi masa
hidima. 12 Akan gabagadi kuma, ku yi shi da farin ciki;
akan tashin hankali kuma, ku cika da hakuri; akan
adu'a kuma, ku nace. 13 Ku zama masu biyan bukatar
tsarkaka, ku zama masu karbar baki a gidajenku. 14
Ku albarkaci masu tsananta maku, kada ku la'anta
kowa. 15 Ku yi farinciki tare da masu farinciki; Ku yi
hawaye tare da masu hawaye. 16 Tunanin ku ya zama
daya. Kada tunaninku ya zama na fahariya, amma
ku yi abokantaka da matalauta. Kada wani a cikin ku
ya kasance da tunanin yafi kowa. 17 Kada ku rama
mugunta da mugunta. Ku yi ayukan nagarta a gaban
kowa. 18 Ku yi duk abin da za ku iya yi domin ku yi
zaman salama tare da kowa. 19 'Yan'uwa, kada ku yi
ramako, ku bar Allah ya rama maku. A rubuce yake, ''
'Ramako nawa ne; zan saka wa kowa,' in ji Ubangiji.''
20 ''Amma idan makiyin ka na jin yunwa, ba shi abinci
ya ci. Idan yana jin kishin ruwa, ba shi ruwan sha.
Idan kun yi haka, garwashin wuta ne za ku saka akan
duk makiyi.'' 21 Kada mugunta ta rinjaye ku, amma
ku rinjayi mugunta ta wurin yin aikin nagarta.

**13** Bari kowa yayi biyayya da hukuma, saboda
babu wata hukuma sai dai in tazo daga Allah;

mahukunta da suke nan kuwa daga Allah ne. 2 Saboda
da haka duk wanda ya ja hukuma ya ja da dokar
Allah; kuma dukan wadanda suka ki hukuma za su
sha hukunci. 3 Don kuwa mahukunta ba abin tsoro
ne ga masu nagarta ba, amma ga masu aikata laifi.
Kuna so ku zama marasa tsoron hukuma? Kuyi abu
nagari, zaku sami yabo daga yin hakan. 4 Saboda shi
bawan Allah ne a gare ku don nagarta. Amma in kun
yi abu mara kyau, kuyi tsoro, saboda ba ya dauke
da takobi ba tare da dalili ba. Don shi bawan Allah
ne mai saka wa mugu da fushi. 5 Saboda haka dole
kuyi biyayya, ba don fushi ba, amma saboda lamiri. 6
Saboda wannan ne kuke biyan haraji. Don masu mulki
bayin Allah ne, wadanda suke yin haka kullum. 7 Ku
bawa kowa hakkinsa; haraji ga mai haraji; kudin fito
ga mai fito; tsoro ga wanda ya cancanci tsoro; girma
ga wanda cancanci girmamawa. 8 Kada ku rike bashin
kowa, sai dai ku kaunaci juna. Domin duk wanda
ya kaunaci dan'uwansa ya cika doka. 9 To, "Kada
kuyi zina, kada kuyi kisa, kada kuyi sata, kada kuyi
kyashi, idan har akwai wata doka kuma, an takaita
ta a wannan jimlar: "Ka kaunaci dan'uwanka kamar
kanka." 10 Kauna bata cutar da makwabci. Domin
haka, kauna tace cikar shari'a. 11 Saboda wannan, kun
san lokaci yayi, ku farka daga barci. Domin cetonmu
yana kusa fiye da yadda muke tsammani. 12 Dare yayi
nisa, gari ya kusan wayewa. Don haka, sai mu rabu
da ayyukan duhu, mu yafa makaman haske. 13 Sai
muyi tafiya yadda ya kamata, kamar da rana, ba a
cikin shashanci ko buguwa ba. Kada kuma muyi tafiya
cikin fasikanci da muguwar sha'awa, ba kuma cikin
husuma ko kishi ba. 14 Amma ku yafa Ubangiji Yesu
Almasihu, kada kuwa ku tanadi halin mutumtaka, don
biye wa muguwar sha'awarsa.

**14** Ku karbi duk wanda yake da rarraunar
bangaskiya, ba tare da sukar ra'ayinsa ba. 2
Wani yana da bangaskiyar yaci komai, wani wanda
yake da rauni yakanci ganye ne kawai. 3 Kada wanda
yake cin komai ya raina wanda baya cin kowanne
abu. Kada kuma wanda baya cin kowanne abu ya
shara'anta sauran da suke cin komai. Saboda Allah
ya karbe shi. 4 Kai wanene, kai wanene da kake
ganin laifin bawan wani? Tsayawarsa ko faduwarsa ai
hakin maigidansa ne, amma Ubangiji yana da ikon
tsai da shi. 5 Wani yakan daukaka wata rana fiye
da sauran. Wani kuma yana daukan ranakun daidai.
Kowa ya zauna a cikin hakakkewa akan ra'ayinsa. 6
Shi wanda ya kula da wata rana, ya kula da ita don
Ubangiji. Kuma wanda yaci, yaci ne domin Ubangiji,
domin yana yi wa Allah godiya. Shi wanda bai ci ba,
yaki ci ne domin Ubangiji. Shima yana yi wa Allah
godiya. 7 Domin babu wanda yake rayuwa don kansa
a cikinmu, kuma babu mai mutuwa don kansa. 8
Domin in muna raye, muna raye don Ubangiji. Kuma
in mun mutu, mun mutu ne don Ubangiji. Ashe, ko
muna raye, ko a mace mu na Ubangiji ne. 9 Domin
wannan dalilin Almasihu ya mutu ya kuma tashi,
saboda ya zama Ubangiji ga matattu da rayayyu. 10
Amma ku don me kuke shara'anta yan'uwanku? kai
kuma don me kake raina dan'uwanka? Dukan mu
zamu tsaya gaban kursiyin shari'ar Allah. 11 Domin
a rubuce yake, "Na rantse, "inji Ubangiji", kowacce
gwiwa zata rusuna mani, kowanne harshe kuwa zai
yabi Allah." 12 Domin kowannenmu zai fadi abin da
shi yayi da bakinsa a gaban Allah. 13 Saboda da haka
kada muyi wa juna shari'a, amma maimakon haka
ku dauki wannan kudduri, don kada kowa ya zama
sanadin tuntunbe ko faduwa ga dan'uwansa. 14 Na
sani na kuma tabbata tsakani na da Ubangiji Yesu,
ba abin da yake mara tsarki ga asalinsa. Sai dai ga
wanda ya dauke shi marar tsarki ne yake zama marar
tsarki. 15 Idan har abincinka na cutar da dan'uwanka,
ba ka tafiya cikin kauna. Kada ka lalata wanda Yesu ya
mutu domin sa da abincinka. 16 Saboda haka, kada
abubuwan da aka dauka kyawawa su zama abin zargi
ga wadansu. 17 Saboda mulkin Allah ba maganar ci
da sha ba ne, amma game da adalci ne, salama, da
farin ciki a cikin Ruhu Mai Tsarki. 18 Domin wanda
yake bautar Almasihu a wannan hanya, karbabbe
ne ga Allah, kuma jama'a sun yarda da shi. 19 Don
haka, mu nemi abubuwa na salama da abubuwan
da zasu gina juna. 20 Kada ku lalata aikin Allah don
abinci. Komai yana da tsarki, amma kaiton mutumin
da yake cin abin da zai sa shi ya fadi. 21 Bashi da kyau
a ci nama ko a sha ruwan inabi, ko duk abin da zai
jawo faduwar dan'uwanka. 22 Wannan bangaskiyar
da kuke da ita, ku adana ta tsakaninku da Allah. Mai
albarka ne wanda zuciyarsa bata da laifi akan abin da
hankalinsa ya ga daidai ne. 23 Duk wanda yayi shakka
amma kuma yaci, ya sani yayi laifi kenan, domin ba
tare da bangaskiya bane. Duk abin da ba na bangaskya
bane zunubi ne.

**15** Yanzu mu da muke da karfi ya kamata mu dau
nauyi raunana, kuma bai dace mu nuna son kai
ba. 2 Bari kowannenmu ya faranta wa makwabcinsa
rai, domin wannan yana da kyau, don a gina shi. 3
Domin Almasihu bai faranta wa kansa rai ba. Kamar
yadda aka rubuta, "zagin da wadansu suka yi masa ya
sauka a kaina." 4 Don abin da aka rubuta a baya an
rubuta ne domin a gargade mu, domin ta hakuri da
karfafawar litattafai mu sami karfi. 5 Yanzu Allah mai
hakuri da karfafawa ya baku zuciya daya ta zaman
tare da juna bisa ga halin Yesu Almasihu. 6 Domin
ya yi haka ne da zuciya daya domin ku yi yabo da
bakinku daya. 7 Domin ku karbi juna, kamar yadda
Yesu ma ya karbe ku domin a daukaka Allah. 8 Saboda
na ce an mai da Almasihu bawan kaciya a madadin
gaskiyar Allah. Ya yi wannan ne don a tabbatar da
alkawarai da aka ba kakanin kakaninmu. 9 Domin
Al'umai su daukaka Allah saboda jinkansa, kamar
yadda ya ke a arubuce, "Domin ta haka zan yabe ka
cikin Al'umai in yi wakar yabon sunanka." 10 Kuma an
ce. "Ku yi faranciki, ku Al'ummai tare da mutanensa."
11 Kuma." Ku yabi Ubangiji, ku dukan Al'ummai; bari
dukan mutane su yabe shi." 12 Kuma, Ishaya ya ce "Za
a sami tsatson Yessi, wanda zai tashi ya yi mulki a
kan Al'umai, Al'umai za su sami karfin hali a cikinsa."
13 Yanzu Allah mai karfafawa ya cika ku da dukkan
farin ciki salama, saboda da bangaskiyarku, domin ku
sami cikkakiyar karafafawa, ta wurin ikon Ruhu Mai
Tsarki. 14 Ni kaina na amince da ku, yan'uwa. Kuma
na amince cewa ku da kanku kuna cike da alheri, cike
da dukkan sani. Na amince cewa za ku sami zarafi ku
gargadi juna. 15 Amma ina rubuta maku da gabagadi
kan wadansu abubuwa, domin in tunasheku, saboda
baiwar da aka bani daga wurin Allah. 16 Cewa baiwar
ta sa na zama bawan Almasihu Yesu da aka aika ga
Al'ummai, limami na bisharar Allah. Zan yi wannan
saboda baikon Al'ummai ya zama karbabbe, kuma
kebbabe ga Allah ta wurin Ruhu Mai Tsarki. 17 Don
haka ina jin dadi cikin Yesu Almasihu da abubuwa
na Allah. 18 Domin ba ni da abin da zan ce, sai abin
da Yesu ya aikata ta wurina, domin Al'ummai su yi
biyayya ta magana da aiki. 19 Ta wurin alamu, da
al'jibai, da ikon Ruhu Mai Tsarki. Daga Urushalima, da
kewaye har zuwa Ilirikum, an kai bisharar Almasihu
ko'ina dukka. 20 A cikin hanyar nan, burina in sanar
da bishara, amma a inda ba a san Yesu ta wurin
sunansa ba, don kada in sa gini akan harshashi wani.
21 Kamar yadda yake a rubuce."Wadanda ba a taba
fada wa labarinsa ba, su gane. Wadanda ba su taba jin
labarinsa ba su fahimta." 22 Saboda an hana ni zuwa
wurin ku a lokatai da dama. 23 Amma yanzu bani da
sauran wani wuri a lardin nan, kuma cikin shekaru
masu yawa ina da marmarin in zo wurin ku. 24 Duk
lokacin da zan tafi Asbaniya ina begen ganin ku yayin
wucewa, don ku raka ni bayan na ji dadin zama da ku
na dan lokaci. 25 Amma yanzu ina tafiya Urushalima
don in yi wa tsarkaka hidima. 26 Domin abin farinciki
ne ga mutanen Makidoniya da Akaya su yi bayarwa
domin gajiyayyu masu bada gaskiya wadanda suke a
Urushalima. 27 Suna jin dadi domin hakika kamar
bashi ne a kansu. Domin Al'ummai sun yi tarayya da
su cikin ayyukan ruhaniya, ya zama hakki a kansu su
ma su taimake su da abubuwa. 28 Domin lokacin da
na gama basu kudin, zan zo gareku a hanyata ta zuwa
Asbaniya. 29 Na san cewa lokacin da na zo gareku, zan
zo da cikakkun albarku na Almasihu. 30 Yanzu ina
rokonku, yan'uwa, ta wurin Ubangiji Yesu Almasihu,
da kaunar Ruhu Mai Tsarki, ku yi ta fama tare da
ni a cikin yin addu'o, inku ga Allah saboda ni. 31
Kuyi haka saboda in tsira daga wadanda suke masu
biyayya ga Yahudiya, domin kuma hidimata saboda
Urushalima ta zama karbabbiya. 32 Ku yi addu'a cewa
in zo wurinku da farinciki ta wurin nufin Allah, cewa
tare da ni da ku, mu sami hutu. 33 Allah na salama ya
kasance tare da ku duka. Amin.

**16** Ina gabatar muku da fibi 'yar'uwarmu, wanda
take hidima a Ikilisiya dake cikin Kankiriya.
2 Domin ku karbe ta cikin Ubangij. A hanyar da
ta dace ga masu bada gaskiya, ku tsaya tare da
ita cikin kowacce bukata. Domin ita da kanta ta
zama da taimako ga masu yawa, har da ni ma. 3
Ku gai da Bilkisu da Akila abokan aiki cikin Yesu
Almasihu. 4 Wadanda sabo da ni suka sadaukar da
ransu. Ina godiya garesu, ba ni kadai ba, amma kuma
da dukan Ikilisiyoyin Al 'mmai. 5 Gaida Ikilisiya da ke
gidansu. Ku gai da Abainitas kaunataccena. Wanda
shi ya fara bada gaskiya ga Almasihu a Asiya. 6 Ku
gai da Maryamu, wadda ta yi maku aiki tukuru. 7
Ku gai da Andaranikas da Yuniyas, yan'uwana da
abokan kurkukuna. Su sanannu ne cikin manzani,
wadanda suke cikin Almasihu kafin ni. 8 Ku gai da
Amfiliyas kaunatace na cikin Ubangiji. 9 Ku gai da
Urbanas abokin aikinmu cikin Almasihu, da Istakis
kaunataccena. 10 Ku gai da Abalis amintacce cikin

Almasihu. Ku gai da wadanda su ke gidan Aristobulus.
11 Ku gai da Hirudiya, dan'uwa na, da wadanda ke
gidan Narkissa, wadanda ke cikin Ubangiji. 12 Ku
gai da Tarafina daTarafusa, masu aikin Ubangiji. 13
Ku gai da Barsisa kaunatacciya, wadda ta yi aikin
Ubangiji da yawa. Ku gai da Rufas zababbe cikin
Ubangiji da mamarsa da ni. 14 Ku gai da Asinkiritas
da Filiguna da Hamis da Baturobas da Hamisu da
kuma yan'uwa da ke tare da su. 15 Ku gai da Filolugus
daYuliya da Niriyas da yan'uwansa, da Ulumfas da
kuma dukan tsarkaka da ke tare su. 16 Ku gaggai da
juna da tsatsarkar sumba. Dukan Ikilisiyoyin Almasihu
na gaishe ku. 17 Yanzu ina rokon ku, yan'wa, ku yi
tunani fa game da masu kawo rabuwa da tuntube.
Sabanin koyarwar da ku ka koya. Ku yi nesa da su.
18 Domin irin mutanen nan ba sa bauta wa Ubangiji
Yesu, sai dai tumbinsu. Ta dadin bakinsu suke rudin
zuciyar marasa laifi. 19 Domin rayuwar biyayyarku
takai ga kunnen kowa, na yi farin ciki da ku, amma
ina so ku zama da hikima game da abin ya ke mai
kyau, ku zama marasa laifi ga abin da ke na mugunta.
20 Allah na salama zai sa ku tattake Shaidan da sauri
kalkashin sawayen ku. Alherin Ubangijin mu Yesu
Almasihu ya kasance tare da ku. 21 Timoti abokin
aikina, yana gaishe ku, haka Lukiyas da Yason da
Susibataras da kuma yan'uwana. 22 Ni Tartiyas wanda
ya rubuta wasikan nan, na gaisheku cikin Ubangiji.
23 Gayus mai masaukina da kuma dukan Ikilisiya,
suna gaishe ku. Arastas ma'ajin birni na gaishe ku, da
Kwartus dan'uwanmu. 24 Alherin Ubangijinmu Yesu
Almasihu ya kasance tare da ku dukka. Amin. 25 Yanzu
ga wanda ke da Ikon karfafa ku bisa ga bisharata da
wa'azin Yesu Almasihu, wanda ta gare shi ne aka
bayyana asiran nan da suke boye tun da dadewa,
(aiōnios g166) 26 amma yanzu sanannu ne ta wurin
litattafan Annabawa bisa umarnin Allah madauwami,
domin biyayyar bangaskiya cikin Al'ummai dukka.
(aiōnios g166) 27 Ga Allah mai hikima kadai, ta wurin
Yesu Almasihu daukaka ta tabbata har abada. Amin.
(aiōn g165)

# 1 Korintiyawa

**1** Bulus, kirayayye daga Almsihu Yesu don zama
manzo ta wurin nufin Allah, da dan'uwanmu
Sastanisu, 2 zuwa ga Ikilisiyar Allah da ke korinti,
zuwa ga wadanda aka kebe su cikin Almasihu
Yesu, wadanda aka kira domin su zama al'umma
maitsarki. Muna kuma rubuta wa dukan masu kira
bisa sunan Ubangijinmu Yesu Almasihu a ko'ina, wato
Ubangijinsu da Ubangijinmu kuma. 3 Bari alheri da
salama su zo gare ku daga Allah Ubanmu da Ubangiji
Yesu Almasihu. 4 Kodayaushe ina gode wa Allahna
domin ku, saboda alherin Allah da Almasihu Yesu ya yi
maku. 5 Ya ba ku arziki ta kowace hanya, cikin dukkan
magana da dukkan ilimi. 6 Kamar yadda shaida game
da Almasihu ta tabbata gaskiya a tsakaninku. 7 Saboda
haka baku rasa wata baiwa ta ruhaniya ba yayinda
kuke marmarin jiran bayyanuwar Ubangijinmu Yesu
Almasihu. 8 Zai kuma karfafa ku zuwa karshe, saboda
ku zama marasa aibi a ranar Ubangijinmu Yesu
Almasihu. 9 Allah mai aminci ne shi wanda ya kira ku
zuwa zumunta ta Dansa, Yesu Almasihu Ubangijimu.
10 Ina rokon ku, yan'uwa, cikin sunan Ubangijinmu
Yesu Almasihu, ku yarda da juna, kada tsattsaguwa ta
kasance tsakanin ku. Ina rokon ku ku zama da zuciya
daya da kuma nufi daya. 11 Gama mutanen gidan
Kulowi sun kawo kara cewa akwai tsattsaguwa a cikin
ku. 12 Ina nufin: kowannen ku na cewa, “Ina bayan
Bulus,” ko “Ina bayan Afollos,” ko “Ina bayan Kefas,”
ko “Ina bayan Almasihu.” 13 Almasihu a rarrabe yake?
An gicciye Bulus domin ku? Ko an yi maku baftisma a
cikin sunan Bulus? 14 Na godewa Allah domin ban yi
wa wanin ku baftisma ba, sai dai Kirisfus da Gayus.
15 Na yi wannan saboda kada wani ya ce an yi maku
baftisma a cikin sunana. 16 (Na kuma yi wa iyalin
gidan Sitifanas baftisma. Banda haka, ban sani ko na
yi wa wani baftisma ba.) 17 Gama Almasihu bai aiko
ni domin yin baftisma ba, amma domin yin wa'azin
bishara. Bai aiko ni domin in yi wa'azi da kalmomin
hikimar mutum ba, saboda kada giciyen Almasihu
ya rasa ikonsa. 18 Gama wa'azin gicciye wauta ne ga
wadanda su ke mutuwa. Amma cikin wadanda Allah
ke ceto, ikon Allah ne. 19 Gama a rubuce yake, “Zan
watsar da hikimar masu hikima. Zan dode fahimtar
masu basira.” 20 Ina mai hikima? Ina masani? Ina mai
muhawara na duniyan nan? Allah bai juya hikimar
duniya zuwa wauta ba? (aiōn g165) 21 Tunda duniya
cikin hikimarta bata san Allah ba, ya gamshi Allah ta
wurin wautar wa'azi ya ceci masu bada gaskiya. 22
Gama Yahudawa suna bidar al'ajibai, Helinawa kuma
suna neman hikima. 23 Amma muna wa'azin Almasihu
gicciyayye, dutsen tuntube ga yahudawa da kuma
wauta ga Helinawa. 24 Amma ga wadanda Allah ya
kira, Yahudawa da Helinawa, muna wa'azin Almasihu
a matsayin iko da kuma hikimar Allah. 25 Gama
wautar Allah tafi mutane hikima, kuma rashin karfin
Allah yafi mutane karfi. 26 Dubi kiranku, yan'uwa. Ba
dukkan ku ke da hikima a ma'aunin mutane ba. Ba
dukkan ku ke da iko ba. Ba dukkan ku ke da haifuwa
ta sarauta ba. 27 Amma Allah ya zabi abubuwan da
suke wofi na duniya domin ya kunyatar da masu
hikima. Allah ya zabi abin da ke marar karfi a duniya
domin ya kunyatar da abinda ke mai karfi. 28 Allah
ya zabi abinda ke marar daraja da kuma renanne a
duniya. Ya ma zabi abubuwan da ake dauka ba komai
ba, domin ya wofinta abubuwan da ake dauka masu
daraja. 29 Ya yi wannan ne domin kada wani ya sami
dalilin fahariya a gabansa. 30 Domin abinda Allah
ya yi, yanzu kuna cikin Almasihu Yesu, wanda ya
zamar mana hikima daga Allah. Ya zama adalcinmu,
da tsarkinmu da fansarmu. 31 A sakamakon haka,
kamar yadda nassi ya ce, “Bari mai yin fahariya, ya yi
fahariya cikin Ubangiji.”

**2** Lokacin da na zo wurin ku, yan'uwa, ban zo da
gwanintar magana ko hikima ba yayinda na yi
shelar boyayyun bayanai game da Allah [ a yayinda
na bada shaida game da Allah]. 2 Domin na kudura a
zuciyata kada in san komai lokacin da nake tare da
ku, sai dai Yesu Almasihu, gicciyayye. 3 Ina tare da ku
cikin kasawa, da tsoro, da fargaba mai yawa. 4 Kuma
sakona da shelata basu tare da kalmomin hikima
masu daukar hankali. Maimakon haka, sun zo da
bayyanuwar Ruhu da iko, 5 saboda kada bangaskiyarku
ta zama cikin hikimar mutane, amma cikin ikon Allah.
6 Yanzu muna maganar hikima ga wadanda suka
ginu, amma ba hikima ta duniyan nan ba, ko ta masu
mulkin wannan zamani, wadanda suke shudewa. (aiōn
g165) 7 Maimakon haka, muna maganar hikimar Allah
ta boyayyar gaskiya, boyayyar hikima da Allah ya
kaddara kafin zamanin daukakarmu. (aiōn g165) 8 Babu
wani mai mulki na zamanin nan da ya san wannan
hikimar, domin inda sun gane ta a wancan lokacin,
da basu gicciye Ubangijin daukaka ba. (aiōn g165) 9

Amma kamar yadda yake a rubuce, “Abubuwan da
babu idon da ya gani, babu kunnen da ya ji, babu
zuciyar da ta yi tsammanin sa, abubuwan da Allah ya
shirya wa wadanda suke kaunarsa. 10 Wadannan ne
abubuwan da Allah ya bayyana mana ta wurin Ruhu.
Gama Ruhu yana bincika komai, har ma abubuwa
masu zurfi na Allah. 11 Gama wanene ya san tunanin
mutum, sai dai ko ruhun mutumin da ke cikinsa?
Haka ma, babu wanda ya san abubuwa masu zurfi na
Allah sai dai Ruhun Allah. 12 Ba mu karbi ruhu na
duniya ba, amma Ruhun da ya zo daga wurin Allah,
domin mu san abubuwan da aka bamu a sake daga
wurin Allah. 13 Muna maganar wadannan abubuwa da
kalmomin da hikimar da mutum baza ta iya koyarwa
ba, amma wadanda Ruhu ke koyar da mu. Ruhu yana
fassara kalmomi na ruhaniya da hikima ta ruhaniya.
14 Mutum marar ruhaniya ba ya karbar abubuwan da
suke daga Ruhun Allah, gama wauta suke a gareshi.
Ba zai iya sanin su ba domin Ruhu ne yake bayyana
su. 15 Shi wanda yake mai ruhaniya yana shari'anta
dukan abubuwa, amma shi baya karkashin shari'ar
sauran mutane. 16 “Wa zai iya sanin zuciyar Ubangiji,
da zai iya ba shi umarni?” Amma mu muna da lamiri
irin na Almasihu.

**3** Amma ni, yan'uwa, ba zan iya magana da ku kamar
mutane masu ruhaniya ba, amma kamar mutane
masu jiki, kamar jarirai cikin Almasihu. 2 Na shayar
da ku da Madara ba da nama ba, don baku isa cin
nama ba, kuma ko yanzu ma baku isa ba. 3 Gama har
yanzu ku masu jiki ne. Muddin akwai kishi da jayayya
a tsakaninku, ashe, ku ba masu jiki ba ne, kuma kuna
tafiya bisa magwajin mutane? 4 Domin in wani ya
ce, “Ina bayan Bulus,” wani kuma ya ce, “Ina bayan
Afollos,” ashe, ba zaman mutuntaka kuke yi ba? 5
To wanene Afollos? Wanene kuma Bulus? Bayi ne
wadanda kuka bada gaskiya ta wurin su, kowannen su
kuwa Allah ya bashi ayyuka. 6 Ni nayi shuka, Afolos
yayi banruwa, amma Allah ne ya sa girma. 7 Don
haka, da mai shukar da mai banruwan, ba komi bane.
Amma Allah ne mai sa girman. 8 Da mai shukar, da
mai banruwan, duk daya suke, kuma kowannen su
zai sami nasa lada, gwargwadon aikinsa. 9 Gama mu
abokan aiki ne na Allah. Ku gonar Allah ne, ginin
Allah kuma. 10 Bisa ga alherin Allah da aka bani a
matsayin gwanin magini, na kafa harsashi, wani kuma
yana dora gini a kai. Sai dai kowane mutum, ya lura
da yadda yake dora ginin. 11 Gama ba wanda ke iya
kafa wani harsashin daban da wanda aka rigaya aka
kafa, wato, Yesu Almasihu. 12 Yanzu fa in wani ya dora
gini a kan harashin da zinariya, ko azurfa, ko duwatsu
masu daraja, ko itace, ko ciyawa, ko tattaka, 13 aikinsa
zai bayyanu, domin ranar nan zata tona shi. Gama za
a bayyana shi cikin wuta. Wutar kuwa zata gwada
ingancin aikin da kowa ya yi. 14 Duk wanda aikinsa ya
tsaya, zai karbi lada; 15 amma duk wanda aikinsa ya
kone, zai sha Asara, amma shi kansa zai tsira, sai dai
kamar ta tsakiyar wuta. 16 Ashe, baku san ku haikalin
Allah ne ba, Ruhun Allah kuma yana zaune a cikin ku?
17 Idan wani ya lalata haikalin Allah, Allah zai lalata
shi. Gama haikalin Allah mai tsarki ne, kuma haka ku
ke. 18 Kada kowa ya rudi kansa. Idan wani a cikin ku
na ganin shi mai hikima ne a wannan zamani, bari ya
zama” wawa” domin ya zama mai hikima. (aiōn g165)
19 Gama hikimar duniyar nan wauta ce a gun Allah.
Gama a rubuce yake, “Yakan kama masu hikima a cin
makircin su.” 20 Har wa yau, “Ubangiji ya san tunanin
masu hikima banza ne.” 21 haka ba sauran fariya akan
mutane! Domin kuwa kome naku ne, 22 Ko Bulus, ko
Afollos, ko kefas, ko duniya, ko rai, ko mutuwa, ko
abubuwa na yanzu, ko abubuwa masu zuwa. Duka
naku ne, 23 Ku kuwa na Almasihu ne, Almasihu kuma
na Allah ne.

**4** Ga yadda za ku dauke mu, kamar bayin Almasihu
da kuma masu rikon asiran Allah. 2 Hade da
wannan, ana bukatar wakilai su zama amintattu. 3
Amma a gare ni, karamin abu ne ku yi mani shari'a,
ko a wata kotu irin ta mutane. Gama bani yi wa
kaina shari'a. 4 Ban sani ko akwai wani zargi a kaina
ba, amma wannan bai nuna cewa bani da laifi ba.
Ubangiji ne mai yi mani shari'a. 5 Sabili da haka,
kada ku yanke shari'a kafin lokaci, kafin Ubangiji
ya dawo. Zai bayyana dukkan boyayyun ayyuka na
duhu, ya kuma tona nufe-nufen zuciya. San nan kowa
zai samu yabonsa daga wurin Allah. 6 Yan'uwa, ina
dora wadannan ka'idoji a kaina da Afollos domin
ku, yadda ta wurin mu za ku koyi ma'anar maganar
nan cewa, “kada ku zarce abin da aka rubuta.” Ya
zama haka domin kada waninku ya kumbura yana
nuna fifiko ga wani akan wani. 7 Gama wa yaga
bambanci tsakanin ku da wasu? Me kuke da shi da
ba kyauta kuka karba ba? Idan kyauta kuka karba,
don me kuke fahariya kamar ba haka ba ne? 8 Kun

rigaya kun sami dukkan abubuwan da kuke bukata!
Kun rigaya kun zama mawadata! Kun rigaya kun fara
mulki- kuma ba tare da mu ba! Hakika, marmarina
shine ku yi mulki, domin mu yi mulki tare da ku.
9 A tunanina, mu manzanni, Allah ya sa mu a jerin
karshe kamar mutanen da aka zartar wa hukuncin
mutuwa. Mun zama abin kallo ga duniya, ga mala'iku,
ga mutane kuma. 10 Mun zama marasa wayo sabili da
Almasihu, amma ku masu hikima ne a cikin Almasihu.
Mu raunana ne, amma ku masu karfi ne. Ana ganin
mu marasa daraja, ku kuwa masu daraja. 11 Har zuwa
wannan sa'a, muna masu yunwa da kishi, marasa
tufafi masu kyau, mun sha kazamin duka, kuma mun
zama marasa gidaje. 12 Mun yi fama sosai, muna
aiki da hanuwanmu. Sa'adda an aibata mu, muna sa
albarka. Sa'adda an tsananta mana, muna jurewa. 13
Sa'adda an zage mu, muna magana da nasiha. Mun
zama, kuma har yanzu an dauke mu a matsayin kayan
shara na duniya da abubuwa mafi kazamta duka. 14
Ban rubuta wadannan abubuwa domin in kunyata ku
ba, amma domin in yi maku gyara kamar kaunatattun
yayana. 15 Ko da kuna da masu riko dubu goma a
cikin Almasihu, ba ku da ubanni da yawa. Gama ni na
zama ubanku cikin Almasihu Yesu ta wurin bishara.
16 Don haka, ina kira gare ku da ku zama masu koyi da
ni. 17 Shiyasa na aiko Timoti wurin ku, kaunatacce
da amintaccen dana cikin Ubangiji. Zai tunashe ku
hanyoyina cikin Almasihu, kamar yadda nake koyar
da su ko'ina da kowace Ikilisiya. 18 Amma yanzu,
wadansun ku sun zama masu fahariya, suna yin kamar
ba zan zo wurinku ba. 19 Amma zan zo gare ku ba da
dadewa ba, idan Ubangiji ya nufa. Sannan zan san
fiye da maganar masu fahariya, amma kuma zan ga
ikonsu. 20 Gama Mulkin Allah ba magana kadai ya
kunsa ba, amma ya kunshi iko. 21 Me kuke so? In zo
wurin ku da sanda ne ko kuwa da kauna da ruhun
nasiha?

**5** Mun ji cewa akwai lalata mai kazanta a cikin ku,
irin lalatar ba ba a yarda da ita ba ko a cikin
al'ummai. Labarin da na samu shine, wani daga cikin
ku yana kwana da matar mahaifinsa. 2 Kuma kuna
fahariya sosai! Ba bakinciki ya kamata ku yi ba? Shi
wanda ya yi haka, dole a fitar da shi daga cikin ku. 3
Gama Kodashike ba ni tare da ku cikin jiki, amma ina
tare daku a ruhu, na rigaya na hukunta wanda yayi
wannan, tamkar ina wurin. 4 Lokacin da ku ka taru a
cikin sunan Ubangijinmu Yesu, ruhuna yana nan tare
da ku cikin ikon Ubangiji Yesu, na rigaya na hukunta
wannan mutum. 5 Na yi haka ne domin in mika
wannan mutum ga Shaidan domin a hallaka jikin,
don ruhunsa ya tsira a ranar Ubangiji. 6 Fahariyarku
bata yi kyau ba. Ko baku sani ba yisti dan kadan ya
kan bata dukan dunkule? 7 Ku tsarkake kan ku daga
tsohon yisti domin ku zama sabon dunkule, wato
gurasar da ba ta da yisti. Gama an yi hadayar Almsihu,
dan ragonmu na idi. 8 Don haka, bari mu yi idinmu
ba da tsohon yisti ba, wato yisti irin na rashin tabi'a
da mugunta. Maimakon haka, bari muyi bukin idi da
gurasa marar yisti ta aminci da gaskiya. 9 Na rubuta
maku a cikin wasikata cewa kada ku yi hudda da
fasikan mutane. 10 Ba ina nufin fasikan mutane na
wannan duniya ba, ko masu zari, ko 'yan'damfara, ko
masu bautar gumaka, tunda kafin ku rabu da su sai
kun bar wannan duniya. 11 Amma yanzu ina rubuta
maku cewa kada ku yi hudda da duk wanda ake kira
dan'uwa amma yana zama cikin fasikanci, ko zari, ko
bautar gumaka, ko in shi mai ashar ne, ko mashayi,
ko dan'damfara. Kada ko abinci ku ci da irin wannan
mutum. 12 Domin ta yaya zan iya shar'anta wadanda
ba 'yan Ikklisiya ba? Maimakon haka, ba ku ne zaku
shar'anta wadanda ke cikin ikilisiya ba? 13 Amma
Allah ke shar'anta wadanda ke waje. “Ku fitar da
mugun mutumin daga cikin ku.”

**6** Idan wani a cikin ku yana jayayya da wani, to sai
ya tafi kotu gaban alkali marar bada gaskiya, a
maimakon gaban masu bi? 2 Ko ba ku sani ba, masubi
ne za su yiwa duniya shari'a? Kuma idan ku za ku
yi wa duniya shari'a, sai ku kasa sasanta al'amura
marasa mahimmanci? 3 Baku sani ba mu za mu yiwa
mala'iku shari'a? Balle shari'ar al'amuran wannan
rai? 4 Idan kuna shar'anta al'amuran yau da kullum,
don me ku ke kai irin wadannan matsaloli gaban
wadanda ba 'yan ikilisiya ba? 5 Na fadi wannan domin
ku kunyata. Babu wani mai hikima a cikin ku ko daya
da zai iya sasanta gardama a tsakanin 'yan'uwa? 6
Amma kamar yadda yake, mai bi ya na kai karar mai
bi a kotu, kuma a gaban mai shari'a wanda ba mai
bi ba! 7 Kasancewar rashin jituwa a tsakanin Kirista
na nuna cewa kun rigaya kun gaza. Don me ba za ka
shanye laifi ba? Don me ba za ka yarda a kware ka ba?
8 Amma kun yi wa wadansu laifi kun kuma cutar su, su
kuwa 'yan'uwanku ne! 9 Ba ku sani ba marasa adalci
ba za su gaji Mulkin Allah ba? Kada ku gaskata karya.

Da fasikai, da masu bautar gumaka, da mazinata, da
karuwai maza, da masu ludu, 10 da barayi, da masu
zari, da mashaya, da masu zage-zage, da 'yan damfara
- ba waninsu da zai gaji Mulkin Allah. 11 Kuma da
haka wadansu a cikinku suke, amma an tsarkake ku,
an mika ku ga Allah, an maida tsayuwar ku dai-dai a
gaban Allah a cikin sunan Ubangji Yesu Almasihu,
kuma ta wurin Ruhun Allahnmu. 12 Dukkan abu halal
ne a gare ni", amma ba kowanne abu ne mai amfani
ba. "Dukan abu halal ne a gare ni," amma ba zan
yarda wani abu ya mallake ni ba. 13 "Abinci don ciki
ne, kuma ciki don abinci ne", amma Allah za ya kawar
da su duka. Ba a yi jiki saboda fasikanci ba. Maimakon
haka, jiki don Ubangiji ne, kuma Ubangiji zai yi wa
jiki tanaji. 14 Allah ya tada Ubangiji, kuma za ya tashe
mu ta wurin ikonsa. 15 Ba ku sani ba jikunanku gabobi
ne na Almasihu? Na dauki gabobin Almasihu in hada
su da karuwa? Allah ya sawwake! 16 Ko baku sani
ba dukan wanda yake hade da karuwa, ya zama jiki
daya da ita kenan? 17 Kamar yadda Littafi ya fadi, "Su
biyun za su zama nama daya." Amma wanda yake
hade da Ubangiji ya zama ruhu daya da shi kenan.
18 Ku gujewa fasikanci! Kowane zunubi mutum yake
aikatawa a waje da jikinsa yake, amma mutum mai
fasikanci yana zunubi gaba da jikinsa. 19 Ba ku sani ba
jikinku haikali ne na Ruhu Mai-tsarki, wanda yake
zaune a cikinku, wanda ku ka samu daga wurin Allah?
Ba ku sani ba cewa ku ba na kanku ba ne? 20 An saye
ku da tsada. Don haka, ku daukaka Allah da jikin ku.

7 Game da abubuwan da kuka rubuto: "Yayi kyau
ga mutum kada ya taba mace." 2 Amma Saboda
jarabobi na ayyukan fasikanci masu yawa, ya kamata
kowane mutum ya kasance da matarsa, kowace mace
kuma ta kasance da mijinta. 3 Kowanne maigidanci
ya ba matarsa hakin ta, kuma kowace mace ta ba
maigidan ta hakinsa na saduwa da juna. 4 Matan ba
ta da iko akan jikin ta amma maigidan ne. Haka ma,
maigidan bashi da iko akan jikinsa amma matar ce. 5
Kada ku hana wa junanku saduwa, sai dai da yardar
junanku domin wani dan lokaci. Kuyi haka domin ku
bada kanku ga addu'a. Daganan sai ku sake saduwa,
domin kada Shaidan ya jarabce ku saboda rashin
kamun kanku. 6 Amma ina fada maku wadannan
abubuwa ne a matsayin nuni, ba a matsayin umurni
ba. 7 Na so da kowa da kowa kamar ni yake. Amma
kowa na da baiwarsa daga wurin Allah. Wani na da
irin wannan baiwar, wani kuma waccan. 8 Ga marasa
aure da gwamraye, Ina cewa, yana da kyau a garesu su
zauna ba aure, kamar yadda nike. 9 Amma idan baza
su iya kame kansu ba, ya kamata su yi aure. Gama yafi
masu kyau su yi aure da su kuna da sha'awa. 10 Ga
masu aure kwa, ina bada wannan umarni- ba ni ba,
amma Ubangiji: "Kada mace ta rabu da mijinta." 11
Amma idan har ta rabu da mijinta, sai ta zauna ba
aure ko kuma ta shirya da shi. Haka kuma "Kada miji
ya saki matarsa." 12 Amma ga sauran ina cewa-Ni, ba
Ubangiji ba-idan wani dan'uwa yana da mata wadda
ba mai bi ba, kuma idan ta yarda ta zauna da shi, to
kada ya sake ta. 13 Idan kuwa mace tana da miji marar
bi, idan ya yarda ya zauna tare da ita, to kada ta kashe
aure da shi. 14 Gama miji marar bada gaskiya ya zama
kebabbe saboda matarsa, sannan mata marar bada
gaskiya ta zama kebbiya saboda mijinta mai bi. In ba
haka ba 'ya'yanku za su zama marasa tsarki, amma
a zahiri su kebabbu ne. 15 Amma idan abokin aure
marar bi ya fita, a bar shi ya tafi. A irin wannan hali,
dan'uwa ko 'yar'uwa ba a daure suke ga alkawarinsu
ba. Allah ya kira mu da mu zauna cikin salama. 16
Yaya kika sani, ke mace, ko za ki ceci mijinki? ko
yaya ka sani, kai miji, ko za ka ceci matarka? 17 Bari
dai kowa ya yi rayuwar da Ubangiji ya aiyana masa,
kamar yadda Allah ya kirawo shi. Wannan ce ka'idata
a dukkan ikilisiyu. 18 Mutum na da kaciya sa'adda aka
kira shi ga bada gaskiya? Kada yayi kokarin bayyana
kamar marar kaciya. Mutum ba shi da kaciya sa'adda
aka kira ga bangaskiya? To kada ya bidi kaciya. 19
Gama kaciya ko rashin kaciya ba shine mahimmin abu
ba. Mahimmin abu shine biyayya da dokokin Allah. 20
Kowa ya tsaya cikin kiran da yake lokacin da Allah ya
kira shi ga bada gaskiya. 21 Kai bawa ne lokacin da
Allah ya kirawo ka? Kada ka damu da haka. Amma
idan kana da zarafin samun 'yanci, ka yi haka. 22
Domin wanda Ubangiji ya kira shi lokacin da yake
bawa, shi 'yantacce ne na Ubangiji. Hakanan kuma,
wanda shike 'yantacce lokacin da aka kira shi ga bada
gaskiya, Bawan Almasihu ne. 23 An saye ku da tsada,
donhaka kada ku zama bayin mutane. 24 Yan'uwa, a
kowace irin rayuwa kowannenmu ke ciki lokacin da
aka kira mu ga bada gaskiya, bari mu tsaya a haka. 25
Game da wadanda basu taba aure ba, ba ni da wani
umarni daga wurin Ubangiji. Amma ina bada ra'ayina
kamar mutum wanda, ta wurin jinkan Allah, yake
yardajje. 26 Don haka, Ina ganin saboda yamutsin

dake tafe ba da jimawa ba, ya yi kyau mutum ya zauna
yadda yake. 27 Kana daure da mace? Kada ka nemi
'yanci daga gare ta. Baka daure da mace? Kada ka
nemi auren mace. 28 Amma idan ka yi aure, ba ka yi
zunubi ba. Kuma idan mace marar aure ta yi aure,
bata yi zunubi ba. Saidai su wadanda suka yi aure
za sha wahalhalu iri-iri a yayinda suke raye, kuma
ina so in raba ku da su. 29 Amma wannan nike fadi
ya'nuwa: lokaci ya kure. Daga yanzu, bari wadanda
suke da mata suyi rayuwa kamar basu da su. 30 Masu
kuka su zama kamar marasa kuka, masu farinciki
kamar marasa farinciki, masu sayen abubuwa kamar
marasa komai. 31 Wadanda suke harka da duniya
kamar ba su harka da ita, domin ka'idar duniyan
nan tana kawowa ga karshe. 32 Ina so ku kubuta
daga damuwa mai yawa. Mutum marar aure yana
tunani akan al'amuran Ubangiji, yadda zai gamshe
shi. 33 Amma mai aure yana tunani akan al'amuran
duniya, yadda za ya gamshi matarsa, 34 hankalinsa
ya rabu. Mace marar aure ko budurwa tana tunanin
al'amuran Ubangiji, yadda za ta kebe kanta a jiki da
ruhu. Amma mace mai aure tana tunanin al'amuran
duniya, yadda za ta gamshi mijinta. 35 Ina fadar
wannan domin amfaninku ne, ba domin in takura ku
ba. Na fadi wannan domin abinda ke daidai, yadda
zaku bi Ubangiji ba tare da hankalinku ya rabu ba. 36
Amma idan wani yana tunani da cewa baya yin abinda
ya dace ga budurwarsa- idan ta wuce shekarun aure,
kuma hakan ya zama dole- sai yayi abinda yake so. Ba
zunubi yake yi ba. Sai suyi aure. 37 Amma idan ya
tsaya da karfi a zuciyarsa, idan baya shan wani matsi
kuma yana iya kame kansa, har ya kudurta a zuciyarsa
yayi haka, wato ya kiyaye budurwarsa da yake tashi,
to hakan ya yi daidai. 38 Don haka, shi wanda ya auri
budurwarsa yayi daidai, sannan shi wanda ya zabi
yaki yin aure yafi yin daidai. 39 Mace tana a daure ga
mijinta a duk tsawon rayuwarsa. Amma idan mijin ya
mutu, tana da 'yanci ta auri duk wanda take so ta
aura, amma a cikin Ubangiji. 40 Amma a ganina, za
ta fi farinciki idan za ta zauna yadda take. Kuma ina
tunanin ni ma ina da Ruhun Allah.

8 Game da abinci da ake yiwa gumakai hadaya: Mun
sani cewa, "Dukanmu muna da ilimi." Ilimi ya kan
kawo takama, amma kauna tana ginawa. 2 Idan wani
yana tunanin ya san wani abu, wannan mutumin bai
rigaya ya san abinda ya kamata ya sani ba. 3 Amma
idan wani yana kaunar Allah, to ya san da wannan
mutum. 4 Game da abincin da aka yiwa gumakai
hadaya: Mun san cewa, "Gunki a duniyan nan ba wani
abu bane," kuma cewa" Babu wani Allah sai guda
daya." 5 To wata kila ma a ce wadanda ake kira alloli
sun kasance, ko a cikin sama ko duniya, kamar yadda
akwai wadanda ake ce dasu "alloli dabam dabam a
duniya ko a sama," kamar yadda akwai "alloli da
iyayengiji" da yawa. 6 "Amma a wurin mu, Allah
daya ne, Uban dukan duniya, daga wurinsa aka halita
dukan abu, domin sa muke rayuwa, Ubangiji Yesu
Almasihu daya, wanda ta wurin sa kome ya kasance,
mu kuma daga wurinsa muke." 7 Amma ba kowa
ke da wannan ilimi ba. Shi ya sa tun da, wadan su
na bauta wa gunki, kuma suna cin wannan abincin
kamar abin da aka mika wa gunki. Lamirin su ya
kazantu sabo da yana da rauni. 8 Amma ba abinci ke
bamu tagomashi a wurin Allah ba. Ko mun ci, bamu
kara karbuwan mu ba, ko ba mu ci ba, ba mu rage
karbuwan mu ba. 9 Amma, ka yi hatara kada 'yancin
ka ya zama sanadiyar tuntuben wani mai rarraunar
bangaskiya. 10 Anar misali, idan wani mai rarraunar
lamiri ya hango ka mai ilimi, kana cin abincin da aka
mika wa gunki, ai ba ka bashi kwarin gwiwa kenan
yaci abincin da aka mika wa gunki ba? 11 Sabili da
ganewar ka akan yanayin gumaka, dan'uwa rarrauna
wanda Yesu ya mutu domin sa ya hallaka. 12 Saboda
haka, idan ka saba wa 'yan'uwa masu raunin a lamiri,
ka yi zunubi a gaban Almasihu. 13 Idan abinci zai sa
dan'uwa na yayi tuntube, zan huta cin nama, domin
kada in jawo wa 'yan'uwana faduwa. (aiōn g165)

9 Ni ba yantacce bane? Ni ba Manzo ba ne? Ban ga
Ubangijinmu Yesu ba? ba ku ne aikin hannuna
cikin Ubangiji ba? 2 Idan ni ba Manzo ba ne ga
wadansu, hakika ni Manzo ne a gare ku. Ai kune
shedar manzanci na cikin Ubangiji. 3 Ga kariya ta zuwa
masu zargi na, 4 Ba mu da 'yanci mu ci mu sha? 5 Ba
mu da 'yanci mu dauki mace mai bada gaskiya kamar
sauran manzanni da Kefas da 'yan'uwan Ubangiji? 6
ko ni da Barnabas ne kawai muka cancanci aiki? 7
Wake aikin soja daga aljihunsa? Wake shuka gonar
inabi baya ci daga 'ya'yan ta ba? Ko kuwa wake kiwon
tumaki ba ya shan madarasu? 8 Ina wannan zance
da ikon mutum ne? Doka bata fadi haka ba? 9 Gama
a rubuce yake a attaura ta Musa cewa, Takarkari
mai tattake hatsi kada a sa masa takunkumi. Amma

shanu ne Ubangiji ke zance a kai? 10 Ba don mu yake
magana ba? An rubuta domin mu ne. Domin wanda
yake noma, yayi cikin bege. mai tattake hatsi kuma
yayi da begen samu. 11 Idan mun yi shuka ta ruhaniya
a rayuwarku, mai wuya ne mu girbi kayan ku na jiki?
12 Idan wadansu sun mori wannan 'yanci a gurin
ku, ba mu fi su cancanta ba? duk da haka bamu yi
amfani da wannan 'yancin ba, maimakon haka, mun
yi jimriya da duk abin da zaya hana bisharar Yesu
Almasihu. 13 Baku sani ba masu bauta a haikali suna
samun abincinsu ne daga haikalin? Baku sani ba masu
bauta a bagadi, suna da rabo daga abin da ake kawowa
kan bagadin? 14 Haka kuma Ubangiji ya umarta masu
aikin bishara zasu ci abincinsu ta hanyar bishara. 15
Amma ban yi amfani da wannan 'yanci ba, ba kuma
ina rubuta maku domin ayi mani wani abu bane,
na gwanmace in mutu maimakon wani ya hana ni
wannan fahariya. 16 Ko nayi shelar bishara, ba ni da
dalilin fahariya domin ya zama dole in yi. Kaito na
idan ban yi shelar bishara ba 17 Idan na yi hidimar
nan da yardar zuciyata, ina da sakamako, idan kuma
ba da yaddar zuciyata ba, harwa yau akwai nauwaya
akai na. 18 To menene sakamako na? shi ne in yi
shelar bishara kyauta, da haka ba zan yi amfani the
'yanci na cikin bishara ba 19 Ko da shike ni 'yantacce
ne ga duka, amma na mai da kaina bawan kowa
domin in ribato masu yawa, 20 Ga yahudawa, na zama
bayahude, domin in ribato yahudawa, ga wadanda ke
karkashin shari'a, na maishe kaina kamarsu, domin in
ribato wadanda ke karkashinta. Na aikata wannan
ko da shike bana karkashin shari'a 21 Ga wadanda
basu karkashin shari'a, na maishe kaina kamar su.
Ko da shike ban rabu da shari'ar Allah ba. Amma ina
karkashin dokar Almasihu. Na yi haka ne domin in
ribato wadanda ba sa karkashin shari'a. 22 Ga marasa
karfi, na maishe kaina kamar marar karfi, domin in
ribato raunana. Na mai da kaina dukan abu ga dukan
mutane domin in sami zarafin da zan ribato wadansu
zuwa ceto. 23 Ina dukan abu sabili da bishara, domin
kuma in sami albarkar da ke cikinta 24 Baku sani ba
mutane da dama suna shiga tsere amma daya neke
karbar sakamakon, saboda haka ku yi tsere domin ku
karbi sakamako. 25 Dan wasa yana motsa jiki da kame
kansa. Yana yi saboda ya karbi wannan sakamako
mai lalacewa, amma muna tsere domin mu karbi
sakamako marar lalacewa. 26 Saboda haka ba na tsere
ko fada haka nan kamar mai bugun iska. 27 Amma ina
matse jiki na in maishe shi bawa, kada bayan na yi wa
wadansu wa'azi ni kuma a karshe a fitar da ni.

10 Ina son ku sani, 'yan'uwa, cewa ubaninmu duka
suna karkashin gajimarai kuma sun bi ta cikin
teku. 2 Dukansu an yi masu baftisma cikin gajimarai da
kuma teku, 3 kuma dukansu sun ci abincin ruhaniya
iri daya. 4 Dukansu sun sha abin sha na ruhaniya
iri daya. Gama sun sha daga wani dutsen ruhaniya
da ya bisu, kuma wannan dutsen Almasihu ne. 5
Amma Ubangiji bai ji dadin yawancinsu ba, saboda
haka gawawakin su suka bazu a jeji. 6 Wadan nan
al'amura, an rubuta mana su domin muyi koyi da su,
kada mu yi sha'awar miyagun ayyuka kamar yadda
suka yi. 7 Kada ku zama masu bautar gumaka kamar
yadda wadansun su suka yi. Wannan kamar yadda aka
rubuta ne, "Mutanen sukan zauna su ci su sha kuma
su tashi suyi wasa." 8 Kada mu shiga zina da faskanci
kamar yadda yawancin su suka yi, a rana guda mutane
dubu ashirin da uku suka mutu. 9 Kada mu gwada
Almasihu kamar yadda yawancinsu suka yi, macizai
suka yi ta kashe su. 10 kada kuma ku zama masu
gunaguni kamar yadda suka yi, suka yi ta mutuwa a
hannun malaikan mutuwa. 11 Wadannan abubuwa
sun faru dasu ne a matsayin misalai a garemu. An
rubuta su domin gargadinmu - mu wadanda karshen
zamanai yazo kanmu. (aiōn g165) 12 Saboda haka, bari
duk wanda yake tunanin shi tsayyaye ne, to yayi
hattara kada ya fadi. 13 Babu gwajin da ya same ku
wanda ba a saba da shi ba cikin dukan mutane. A
maimako, Allah mai aminci ne. Da ba zaya bari ku
jarabtu ba fiye da iyawarku. Tare da gwajin zai tanadar
da hanyar fita, domin ku iya jurewa. 14 Saboda haka
ya kaunatattu na, ku guji bautar gumaka. 15 Ina
magana da ku kamar masu zurfin tunani, domin ku
auna abin da ni ke fadi. 16 Kokon albarka da muke sa
wa albarka, ba tarayya bane cikin jinin Almasihu?
Gurasa da muke karyawa ba tarayya bane cikin jikin
Almasihu? 17 Domin akwai gurasa guda, mu da muke
dayawa jiki daya ne. Dukanmu munci daga gurasa
daya ne. 18 Dubi mutanen Isra'ila: ba wadanda ke cin
hadayu ke da rabo a bagadi ba? 19 Me nake cewa?
gunki wani abu ne? Ko kuma abincin da aka mika wa
gunki hadaya wani abu ne? 20 Amma ina magana
game da abubuwan da al'ummai suke hadaya, suna wa
aljannu ne hadaya ba Allah ba. Ba na son kuyi tarayya
da al'janu! 21 Ba zaku sha daga kokon Ubangiji ku

kuma sha na Al'janu ba, ba za kuyi zumunta a teburin
Ubangiji ku yi a na Al'janu ba. 22 Ko muna so mu sa
Ubangiji kishi ne? Mun fi shi karfi ne? 23 “Komai dai
dai ne,” amma ba komai ke da amfani ba, “Komai dai
dai ne,” amma ba komai ke gina mutane ba. 24 Kada
wani ya nemi abinda zaya amfane shi. A maimako,
kowa ya nemi abinda zaya amfani makwabcinsa. 25
Kana iya cin duk abin da ake sayarwa a kasuwa, ba
tare da tamboyoyin lamiri ba. 26 Gama “duniya da
duk abin da ke cikin ta na Ubangiji ne.” 27 Idan marar
bangaskiya ya gayyace ka cin abinci, kana kuma da
niyyar zuwa, ka je ka ci duk abinda aka kawo maka,
ba tare da tamboyoyin lamiri ba. 28 Amma idan wani
ya ce maka, “Wannan abinci an yi wa gumaka hadaya
da shi ne” To kada ka ci. Wannan za ka yi ne saboda
wanda ya shaida maka, da kuma lamiri ( gama duniya
da dukan abinda ke cikin ta na Ubangiji ne). 29 Ba
ina nufin lamirin ka ba, amma lamirin wanda ya fada
maka. Don me za a hukunta 'yanci na domin lamirin
wani? 30 Idan na ci abincin tare da bada godiya, don
mi za a zage ni don abin da na bada godiya a kansa?
31 Saboda haka, ko kana ci ko kana shi, ka yi komai
domin daukakar Allah. 32 Kada ka zama sanadiyyar
tuntube, ga Yahudawa, ko Helenawa, ko ikilisiyar
Allah. 33 Na yi kokari in farantawa dukan mutane rai
cikin dukan abubuwa. Ba riba nake nema wa kaina ba,
amma domin kowa. Na yi wannan ne domin su sami
ceto.

**11** Ku yi koyi da ni, kamar yadda nake koyi da
Almasihu. 2 Yanzu ina yaba maku ne, don kuna
tunawa da ni cikin abu duka. Ina kuma yaba maku
wajen bin al'adun da na ba ku daidai yadda na ba
ku. 3 Amma fa ina son ku fahimta da cewa, shugaban
kowane mutum Almasihu ne, shugaban kowace mace
mutumin ne, shugaban Almasihu Allah ne. 4 Kuma
duk mutumin da ya yi addu'a ko annabci kansa a rufe,
ya wulakanta shugabansa. 5 Amma duk macen da
ta yi addu'a ko annabci kanta a bude, ta wulakanta
shugabanta. Gama yayi dai dai da idan tayi aski. 6
Gama idan mace ba zata rufe kanta ba, to ta yanke
gashinta ya zama gajere. Idan abin kunya ne mace ta
yanke gashinta ko ta aske kanta, bari ta rufe kanta.
7 Bai kamata na miji ya rufe kansa ba, tun da yake
shi siffa ne da daukakar Allah. Amma mace daukakar
namiji ce. 8 Don kuwa namiji ba daga jikin mace
yake ba. A maimako, matar daga jikin namiji take. 9
Ba a kuma halicci namiji don mace ba. A maimako,
an halicci mace don namiji. 10 Shi ya sa mace za ta
kasance da alamar iko a kanta, saboda mala'iku. 11
Duk da haka, a cikin Ubangiji, mace ba a rabe take
da namiji ba, haka kuma namiji ba a rabe yake da
mace ba. 12 Kamar yadda mace take daga namiji,
haka ma namiji kuma haihuwar mace ne. Amma
dukkan abubuwa daga Allah suke. 13 Ku hukunta da
kanku: Daidai ne mace ta yi addu'a ga Allah kanta
a bude? 14 Ashe, ko dabi'a bata nuna maku cewa
abin kunya ne namiji, ya kasance da dogon gashi
ba? 15 Ba dabi'a ta koya maku cewa idan mace tana
da dogon gashi, daukakar ta ne ba? Gama domin
rufewa aka yi mata baiwar gashin. 16 To idan wani
yana da niyyaryin gardama game da wannan, mu dai
bamu da wata al'adar, ikilisiyoyin Allah kuma haka. 17
Amma game da umarnin dake biye, ban yaba maku
ba, taruwarku ba ta kirki ba ce, ta rashin gaskiya ce.
18 Farko dai sa'adda kuke, taron ikklisiya, na ji har
akwai rarrabuwa tsakaninku, har na fara amincewa da
maganar. 19 Dole ne a sami tsattsaguwa a tsakaninku,
don a iya gane wadanda suke amintattu a cikinku.
20 Domin, in kun taru a wuri daya, ba jibin Ubangiji
kuke ci ba! 21 Ya yin da kuke ci, kowa na cin abincinsa
ne kamin sauran Wani yana jin yunwa, wani kuma
ya zarin ci, har ya bugu. 22 Baku da gidajen da zaku
ci ku sha, kuna raina ikkilisiyar Allah, kuna kuma
wulakanta wa wadanda basu da komai? To, me zan ce
maku? Yaba maku zan yi? Ba zan yaba maku ba akan
wannan. 23 Amma abin da na karba a gun Ubangiji
shi nake baku cewa Ubangiji Yesu, a daren da aka
bashe shi ya dauki gurasa. 24 Bayan ya yi godiya, sai
ya kakkarya ya ce, “wanna shi ne jikina wanda yake
saboda ku, ku yi domin tunawa da ni.” 25 Ta wannan
hanya kuma, sai ya dauki kokon, ya ce, “kokon nan na
sabon alkawari ne, da aka tabbatar da shi da cikin
jinina. Ku yi haka kuna sha don tunawa da ni.” 26
Duk sa'adda kuke cin gurasar nan, kuna kuma sha
cikin kokon nan, kuna bayyana mutuwar Ubangiji
ke nan, har sai ya dawo. 27 Saboda haka duk wanda
ya ci gurasar nan, ko ya sha a cikin kokon nan, na
Ubangiji da rashin cancanta, ya yi laifin wulakanta
jikin Ubangiji da jininsa. 28 Sai kowa ya fara auna
kansa, kafin ya ci gurasar, ya kuma sha a cikin kokon
nan. 29 In kowa ya ci, ya sha ba tare da rarrabewa da
jikin Ubangiji ba, lalle ya jawowa kansa hukunci, ta
wurin ci da sha da ya yi. 30 Shi ya sa da yawa a cikin
ku suke raunana, kuma suna fama da rashin lafiya, har

ma wasun ku da dama suka yi barci. 31 Amma, in mun
auna kanmu, ba a za a hukunta mu ba. 32 In kuwa
Ubangiji ne ya ke hukunta mu, To, muna horuwa
ke nan, don kada a kayar damu tare da duniya. 33
Saboda haka, ya ku 'yan'uwana, idan kuka tattaru
don cin abinci, sai ku jira juna. 34 Idan kuwa wani
yana jin yunwa, ya ci a gida, kada ya zama taronku ya
jawo maku hukunci. Batun sauran abubuwan da kuka
rubuta kuwa, zan ba da umarni a kai sa'ad da na zo.

12 Game da baye bayen Ruhu Mai Tsarki 'yan'uwa,
bana so ku zama da jahilci. 2 Kun san cewa
lokacin da ku ke al'ummai, an rude ku da alloli marasa
magana ta hanyoyi dabam dabam marasa kan gado. 3
Saboda haka ina so ku sani babu wanda ya ke magana
da Ruhun Allah da zai ce, "Yesu la'ananne ne." Babu
kuma wanda zaya ce, "Yesu Ubangili ne," sai dai ta
Ruhu Mai Tsarki. 4 Akwai bay bye iri iri, amma Ruhu
daya ne. 5 Akwai hidimomi iri iri, amma Ubangiji daya
ne. 6 Akwai aikace aikace iri iri, amma Allah daya ke
bayyanawa kowane mutum yadda zai aiwatar da su. 7
To ga kowanne an bayar da ikon nuna ayyukan Ruhu
a fili domin amfanin kowa. 8 Ga wani ta wurin Ruhu
an bayar da baiwar hikima, kuma ga wani kalmar
sani ta wurin Ruhu daya. 9 Ga wani an ba shi baiwar
bangaskiya ta wurin Ruhun nan, ga wani kuwa an
ba shi baiwar warkarwa ta wurin wannan Ruhun. 10
Ga wani yin ayyukan iko, ga wani kuwa annabci. Ga
wani kuwa an ba shi baiwar bambance ruhohi, ga
wani harsuna daban daban, kuma ga wani fassarar
harsuna. 11 Dukan wadannan Ruhu daya ne ya ke
iza su, ya kuma rarraba baye bayen ga kowannen su
yadda ya nufa. 12 Kamar yadda jiki daya ne amma
da gabobi da yawa kuma duk gabobin na jiki daya
ne, haka nan Almasihu yake. 13 Gama ta Ruhu daya
aka yi wa kowa baftisma cikin jiki daya, ko Yahudawa
ko al'ummai, ko bayi ko 'ya'ya, dukan mu kuwa an
shayar da mu Ruhu daya. 14 Gama jiki ba daya ba ne
sungun, amma gabobi ne da yawa. 15 Idan kafa ta ce,
"tun da dai ni ba hannu ba ne to ni ba fannin jikin
bane," wannan baya rage masa matsayin sa a jikin
ba. 16 Kuma da kunne zaya ce, '''Da yake ni ba ido
ba ne, ai, ni ba gabar jiki ba ne,'' fadar haka ba za ta
raba shi da zama gabar jikin ba. 17 Idan dukan jikin ya
kasance ido ne da me za a ji? Da dukan jikin kunne
ne, da me za a sunsuna? 18 Amma Allah ya shirya
gabobin jiki bisa ga tsarin sa. 19 Amma da duk jiki
gaba daya ce, da ina jikin zai kasance? 20 Ga shi akwai
gabobi da yawa, kuma jiki daya ne. 21 Ba da ma ido
ya fadawa hannu, ''Bana bukatar ka,'' ko kuma kai
ya fadawa kafafu, ''Ba na bukatar ku.'' 22 Amma, sai
ma gabobin da ake gani kamar raunannu su ne masu
humimmanci, gabobin jiki kuwa da ake gani kamar
sun kasa sauran daraja, mu kan fi ba su martaba.
23 Ta haka gabobinmu marasa kyan gani, akan kara
kyautata ganinsu. Gabobin mu masu kyan kuma ba sai
an yi masu ado ba. 24 Amma Allah ne da kansa ya hada
jiki, yana bada mafificiyar martaba ga kaskantacciyar
gaba. 25 Yayi haka ne domin kada a sami tsattsaguwa
a cikn jikin, amma domin gabobin su kula da juna
da matsananciyar lura. 26 Kuma idan gaba daya na
wahala, dukan gabobin suna wahala tare. ko kuma
idan an girmama gaba daya, dukan gabobin na farin
ciki tare. 27 Yanzu ku jikin Almasihu ne, saboda haka
kuma kowannen ku gabarsa ne. 28 A cikin ikilisiya,
Allah ya sa wasu su zama, na farko manzanni, na biyu
annabawa, na uku masu koyarwa, sa'an nan sai masu
yin ayyukan iko, sai masu aikin warkarwa, da masu
bayar da taimako, da masu aikin tafiyar da al'amura,
da masu harsuna daban daban. 29 To kowa manzo
ne? ko kuwa duka annabawa ne? ko kuma duka masu
koyarwa ne? Kowa ne ke yin manyan ayyukan iko?
30 Ko kuwa dukan su ne suke da baiwar warkarwa?
Dukan su ne ke magana da harsuna? ko kuma dukan
su ne ke fassara harsuna? 31 Amma bari ku himmantu
ga neman baiwa mafi girma. Kuma zan nuna maku
wata hanya mafificiya.

13 Koda ya zamanto ina magana da harsunan
mutane, har ma da na mala'iku, amma kuma ba ni
da kauna, na zama kamar kararrawa mai yawan kara,
ko kuge mai amo. 2 Ko da ya zamanto ina da baiwar
annabci kuma na fahimci dukkan boyayyar gaskiya,
da dukkan ilimi, ko ina da matukar bangaskiya, har
ma zan iya kawar da duwatsu. muddin ba ni da kauna,
ni ba komai ba ne. 3 Ko da ya zamanto na bayar
da dukan mallakata domin a ciyar da matalauta,
in kuma mika jikina domin a kona. Amma in ba ni
da kauna, ban sami ribar komai ba. (Na bayar da
jikina ne domin inyi fahariya.) 4 Kauna na da hakuri
da kirki. kauna bata kishi ko fahariya. kauna ba ta
girman kai 5 ko fitsara. Bata bautar kanta. Bata saurin
fushi, kuma bata ajiyar lissafin laifuffuka. 6 Bata farin
ciki da rashin adalci. A maimako, tana farin ciki da
gaskiya. 7 Kauna tana jurewa cikin dukan abubuwa,

tana gaskata dukan abubuwa, tana da yarda game
da dukan abubuwa, tana daurewa dukan abubuwa. 8
Kauna ba ta karewa. Idan akwai anabce anabce, zasu
wuce. Idan akwai harsuna, zasu bace. Idan akwai ilimi,
zaya wuce. 9 Domin muna da sani bisa - bisa kuma
muna anabci bisa - bisa. 10 Sa'adda cikakke ya zo, sai
marar kammalar ya wuce. 11 Da nake yaro, nakan
yi magana irinta kuruciya, nakan yi tunani irin na
kuruciya, nakan ba da hujjojina irin na kuruciya. Da
na isa mutum na bar halayen kuruciya. 12 Gama yanzu
muna gani sama - sama kamar ta madubi, amma a
ranar fuska da fuska, yanzu na sani bisa - bisa, amma
a lokacin zan sami cikakken sani kamar yadda aka yi
mani cikakken sani. 13 To, a yanzu abubuwan nan uku
sun tabbata: bangaskiya, da gabagadi mai zuwa, da
kuma kauna, amma duk mafi girma a cikinsu ita ce
kauna.

14 Ku dafkaci kauna kuma ku himmatu domin baye
bayen ruhaniya, musamman domin kuyi anabci.
2 Domin wanda yake magana da harshe bada mutane
yake magana ba amma da Allah. domin babu mai
fahimtarsa saboda yana zancen boyayyun abubuwa
ciki Ruhu. 3 Amma wanda yake anabci da mutane
yake magana domin ya gina su, ya karfafa su, kuma
ya ta'azantar dasu. 4 Wanda yake magana da wani
harshe, kansa yake ginawa, amma mai yin annabci
kuwa, ikilisiya yake ginawa. 5 To, fatana ace dukan
ku kuna magana da harsuna. Amma fiye da hakama,
fatana ace kuyi anabci. Wanda yake anabci yafi wanda
yake magana da harsuna ( sai dai idan wani ya fassara
domin ikilisiya ta ginu). 6 Amma yanzu, 'yan'uwa,
in na zo wurin ku ina magana da harsuna, ta yaya
zaku karu dani? ba zaya yiwu ba, sai idan nayi maku
magana da wahayi, ko sani, ko anabci, ko koyarwa. 7
Idan kayan kida marasa rai suna fitar da sauti - kamar
su sarewa da algaita - kuma basu fitar da amo daban
daban, ta yaya wani zaya san irin amon da sarewar da
algaitar suke kadawa? 8 Domin idan aka busa kaho da
sauti marar ma'ana, ta yaya wani zaya san lokacin da
ya dace ya shirya zuwa yaki? 9 Haka yake game da ku.
Idan kuka furta zance marar ma'ana, ta yaya wani
zaya fahimci abinda kukace? zaku yita magana, kuma
babu wanda zaya fahimce ku. 10 Babu shakka akwai
harsuna daban daban a duniya, kuma babu wanda
baya da ma'ana. 11 Amma idan ban san ma'anar wani
harshe ba, zan zama bare ga mai maganar, kuma
mai maganar zaya zama bare a gareni. 12 haka yake
gare ku. Tun da kuna da dokin bayyanuwar Ruhu,
ku himmatu da habaka cikin gina ikilisiya. 13 To
wanda yake magana da harshe yayi addu'a domin ya
iya fassarawa. 14 Domin idan nayi addu'a da harshe,
ruhuna yayi addu'a, amma fahimtata bata karu ba. 15
To, me zan yi? Zan yi addu'a da ruhuna, in kuma yi
addu'a da fahimtata. Zan yi raira waka da ruhuna,
kuma in raira waka da fahimtata. 16 In ba haka ba,
idan ka yi yabon Allah da ruhu kawai, ta yaya wanda
yake waje zai ce, “Amin” a kan godiyar da kake yi in
bai san abin da kake fada ba? 17 Babu shakka kayi
godiya sosai, amma wanin baya ginu ba. 18 Nagodewa
Allah ina magana da harsuna fiye da ku duka. 19
Duk da haka dai a taron ikilisiya na gwammace in
yi magana da kalmomi biyar cikin fahimta saboda
inganta wadansu fiye da dubu goma da harshe. 20
'Yan'uwa, kada ku zama yara cikin tunani, sai dai
a wajen aikin mugunta, ku yi halin jarirai, amma a
tunaninku ku girma. 21 A rubuce yake a shari'a cewa,
“zan yi magana da mutanen nan ta wurin mutane
masu bakin harsuna, da kuma lebunan baki. Duk da
haka kuwa ba za su saurare ni ba”, in ji Ubangiji. 22
Amma harsuna alamu ne, ba ga masu bada gaskiya
ba, sai dai ga marasa ba da gaskiya. Annabci kuwa
alama ce ga masu ba da gaskiya, amma ba don marasa
bangaskiya ba. 23 Saboda haka, in dukan ikilisiya
ta taru, kowa kuwa yana magana da wasu harsuna,
wadansu na waje da kuma marasa ba da gaskiya suka
shigo, ashe, ba sai su ce kun haukace ba ba? 24 In
kuwa kowa yana yin annabci, wani kuma marar ba da
gaskiya ko wani daga waje ya shigo, maganar kuwa
zata ratsa shi. Za a ma hukanta shi a kan maganar, 25
asiran zuciyarsa kuma za su tonu. Sakamokon haka,
sai ya fadi ya yi wa Allah sujada, zaya furta cewa lallai
Allah yana tare da ku. 26 Sai me kuma 'yan'uwa?
idan kuka tattaru, wani yana da zabura, koyarwa,
wahayi, harshe, ko fassara. Kuyi komai domin gina
ikilisiya. 27 Idan wani yayi magana da harshe, bari
a sami mutum biyu ko uku a yawansu, kuma kowa
yayi daya bayan daya. Sai wani ya fassara abinda
aka fada. 28 Amma idan babu wanda zaya fassara,
bari dukansu suyi shiru a ikilisiya. Bari kowa yayi wa
kansa maganar a gida shi kadai da kuma Allah. 29 Bari
annabawa biyu ko uku suyi magana, bari sauran su
saurara tare da bambance abinda ake fada. 30 Idan
kuma anba wani fahimta wanda yana zaune a cikin

sujadar, bari wanda yake ta magana kafin yanzu yayi
shiru. 31 Dukanku kuna iya yin annabci daya bayan
daya, domin kowannen ku yayi koyi, a kuma samu
karfafawa. 32 Gama ruhohin annabawa suna karkashin
annabawa, 33 domin Allah ba Allahn rudu ba ne, na
salama ne. Haka yake kuwa a duk ikllisiyoyin masu
bangaskiya. 34 Mataye suyi shiru a ikilisiyoyi. Domin
ba a basu dama ba suyi magana. A maimako, su zama
masu sadaukar da kansu, kamar yadda doka ta ce. 35
Idan akwai abinda suke so su koya, bari su tambayi
mazajen su a gida. Domin abin kunya ne mace tayi
magana a ikilisiya. 36 Daga wurinku maganar Allah ta
zo ne? ko kuwa a gare ku kadai ta iso? 37 In wani yana
zaton shi ma annabi ne, ko kuwa mai ruhaniya, to, sai
ya fahimta, abin nan da nake rubuta maku umarni ne
daga wurin Ubangiji. 38 In kuwa wani ya ki kula da
wannan, shi ma kada a kula da shi. 39 Saboda haka,
'yan'uwa, ku yi marmarin yin annabci sosai, sa'an
nan kada ku hana kow yin magana da harsuna. 40 Sai
dai a yi komai ta hanyar da ta dace bisa ga tsari.

**15** Yanzu ina tunashshe ku 'yan'uwa, game da
bisharar nan da nake shelarwa, wadda kuka
karba kuke kuma dogara da ita. 2 Da wannan bishara
aka yi maku ceto, idan kuka rike wa'azi da na yi maku
da karfi, sai in dama kun gaskanta a banza. 3 Domin
na baku muhimmin sako kamar na farko da na karba:
cewa Almasihu ya mutu domin zunubanmu, bisa ga
nassosi, 4 cewa kuma an bizne shi, ya kuwa tashi daga
matattu a rana ta uku bisa ga nassosi. 5 Cewa kuma ya
bayyana ga Kefas, sa'an nan ga sha biyun. 6 Daga nan
ya bayyana ga 'yan'uwa sama da dari biyar a lokaci
guda. Wadanda mafi yawan su na da rai har yau,
amma wasun su sun yi barci. 7 Daga nan ya bayyana ga
Yakubu, da kuma ga manzannin duka. 8 A karshe, sai
ya bayyana a gare ni, kamar dan da aka haifa bakwaini.
9 Gama ni ne mafi kankanta a cikin manzanni. Ban
cancanci a kira ni manzo ba, domin na tsanantawa
ikklisiyar Allah. 10 Amma saboda alherin Ubangiji ina
matsayin da nake a yau, kuma alherin sa da ke ciki na
ba a banza yake ba. A maimako, nayi aiki tukuru fiye
da su duka. Amma duk da haka ba ni bane, amma
alherin Allah da ke tare da ni. 11 Saboda haka ko nine
ko Su, haka mukayi wa'azin, haka kuma kuka gaskata.
12 To idan anyi shela a matsayin cewa Yesu ya tashi
daga matattu, tayaya wadansunku su ke cewa babu
tashin matattu? 13 Amma idan babu tashin matattu,
Almasihu ma ai ba a tashe shi ba kenan. 14 idan kuwa
ba a tashi Almasihu ba, wa'azin mu ya zama banza
kenan, haka kuma bangaskiyar ku ta zama banza. 15
Mun kuma zama shaidun karya game Allah kenan,
muna shaida akan Allah cewa ya tashi Almasihu daga
matattu alhali ko bai tashe shi ba. 16 Domin idan
babu tashin matattu, kai, ko Almasihu ma ba a tashe
shi ba kenan. 17 Idan har ba a tashi Almasihu ba,
bangaskiyar ku a banza take, har yanzu kuma, kuna
cikin zunuban ku. 18 To wadanda suka mutu cikin
Almasihu kuma sun hallaka kenan, 19 idan a wannan
rayuwa ce kadai muke da bege cikin Almasihu, to
cikin dukkan mutane munfi kowa zama abin tausayi.
20 Amma yanzu, Almasihu ya tashi daga matattu,
wanda ya sa shi ya zama nunar fari cikin tashi daga
matattu. 21 Domin yadda mutuwa ta shigo duniya
ta hanyar mutum guda, hakkan nan ma tashi daga
matattu. 22 Gama kamar yadda a cikin Adamu duka
suka mutu, haka kuma a cikin Almasihu za a rayar da
duka. 23 Amma kowanne da tsarinsa: Almasihu, nunan
fari, sannan su wadanda ke na Almasihu za a rayar da
su lokacin zuwansa. 24 Sa'an nan karshen zai gabato,
lokacin da Almasihu zai mika mulkin ga Allah Uba.
sa'an nan ne zaya kawar da dukkan mulki, martaba da
iko. 25 Gama mulkinsa zai habaka har sai ya sa dukkan
makiyansa a karkashin sawayen sa. 26 Mutuwa kuwa,
ita ce makiyi na karshe da za'a hallaka. 27 Domin
“yasa dukkan komai a karkashin ikonsa,” Amma da
aka ce” yasa dukkan komai a karkashin ikonsa,” a
sarari yake cewa wannan baya hada da wanda yasa
dukan komai a karkashin ikonsa ba. 28 Idan dukan abu
na karkashin mulkinsa, to Dan da kansa zaya kasance
a karkashin ikon shi wanda yasa komai a karkashin
ikonsa. Wannan zaya kasance ne saboda Allah Uba ya
zama dukkan komai cikin dukkan komai. 29 ko kuma
me zai faru da wadanda ake yi wa baftisma domin
matattu? Idan kuwa babu tashin matattu sam sam, ina
amfanin yi masu baftisma domin su? 30 Kuma me yasa
muke cikin hadari kowace sa'a? 31 Ina mutuwa kullum.
Wannan nake furtawa ta wurin fahariya, 'yan'uwa,
wadda nake da ita cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu.
32 Menene ribata, a idanun mutane, idan nayi kokowa
da bisashe a Afisa, idan babu tashin matattu? “bari
mu ci mu sha, domin gobe zamu mutu.” 33 Kada fa a
yaudare ku, domin “tarayya da mugaye takan bata
halayen kirki.” 34 “Ku natsu! kuyi zaman adalci! kada
ku cigaba da zunubi. Domin wasunku basu da sanin

Allah. Ina fadar wannan domin in baku kunya. 35
Amma wani zaya ce, "Yaya za'a yi tashin matattu?
Wane irin jiki kuma zasu tashi da shi? 36 Ku jahilai ne
sosai! Abinda ka shuka ba zaya fara girma ba sai ya
mutu. 37 Abinda ka shuka ba jikin da zaya kasance
bane, amma kwayar irin ne kawai. Wanda zaya zama
alkama ko wani abu daban. 38 Amma Allah zaya bashi
jiki yadda ya zaba, ga kowane kwayar iri da nashi
jikin. 39 Ba duka jiki ne yake iri daya ba. A maimako,
akwai jiki irin na mutane, akwai kuma wani irin na
dabbobi, kuma wani jikin irin na tsuntsaye, kuma
da irin na kifi. 40 Akwai kuma jikina na samaniya
da jikina na duniya. Amma daukakar jikin samaniya
wata daban ce kuma daukakar jikin duniya daban
ce. 41 Akwai daukaka irin ta rana, da kuma wata
daukakar irin ta wata, da kuma wata daukakar irin ta
taurari. Domin wani tauraron ya bambanta da wani
wajen daukaka. 42 Haka yake a tashin matattu. Abinda
aka shuka mai lalacewa ne, wanda aka tayar marar
lalacewa ne. 43 An shuka shi cikin rashin daraja; an
tayar da shi cikin daukaka. An shuka shi cikin rauni;
an tayar da shi cikin iko. 44 An shuka shi jiki na zahiri;
an tayar da shi jiki na ruhaniya. Idan akwai jiki na
zahiri, to akwai jiki na ruhaniya. 45 Haka kuma aka
rubuta, "Adamu na farko ya zama rayayyen taliki."
Adamu na karshe ya zama Ruhu mai bayar da rai. 46
Amma na ruhaniyar ba shine ya fara zuwa ba amma
na zahirin, daga nan na ruhaniyar. 47 Mutumin farkon
ai daga turbaya ya fito, wato na duniya. Amma shi
na biyun daga sama yake. 48 kamar yadda mutumin
ya fito daga turbaya haka ma wadanda aka halitta
da turbaya. kamar yadda mutumin yake daga sama
haka ma wadanda ke na sama. 49 Kamar yadda muke
dauke da jiki mai kamannin turbaya, haka ma zamu
kasance da kamannin mutumin sama. 50 To wannan
na fada, 'yan'uwa, cewa nama da jini ba za su gaji
mulkin Allah ba. Haka kuma mai lalacewa ba za
ya gaji marar lalacewa ba. 51 Duba! ina gaya maku
asirtacciyar gaskiya: Ba dukanmu zamu mutu ba,
amma dukanmu za a canza mu. 52 Za a canza mu
nan da nan, cikin keftawar ido, a kaho na karshe.
Domin za a busa kaho, kuma za a tada matattu marasa
lalacewa, kuma za a canza mu. 53 Domin wannan
jiki mai lalacewa dole ya sanya jiki marar lalacewa,
kuma wannan jiki mai mutuwa dole ya sanya marar
mutuwa. 54 Amma idan wannan jiki mai lalacewa ya
sanya marar lalacewa, kuma wannan jiki mai mutuwa
ya sanya marar mutuwa, sai abinda aka rubuta ya cika,
"An hadiye mutuwa cikin nasara." 55 "Mutuwa, ina
nasararki? Mutuwa, ina dafinki?" (Hadēs g86) 56 Gama
dafin mutuwa zunubi ne, kuma ikon zunubi shari'a ce.
57 Amma godiya ga Allah, wanda ya bamu nasara ta
wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu! 58 Saboda haka,
ya ku 'yan'uwana kaunatattu, ku dage kuma kada ku
jijjigu. Ko yaushe ku habaka da aikin Ubangiji, domin
kun san cewa aikinku cikin Ubangiji ba a banza yake
ba.

16 Yanzu game da zancen tattara gudunmuwa
ga masu bi, kamar yadda na umurci ikilisiyun
Galatiya, haka za ku yi. 2 A ranar farko ga mako,
kowannen ku ya ajiye wani abu, yana tarawa bisa ga
iyawarku. Ku yi haka don in na zo ba sai an tattara
ba. 3 Sa'adda na zo, zan aiki duk wadanda kuka yarda
da su da wasiku don su kai sakonku Urushalima. 4
Sannan idan ya dace nima in tafi, sai su tafi tare da
ni. 5 Zan zo wurinku sa'adda na ratsa Makidoniya.
Domin zan ratsa ta makidoniya. 6 Meyuwa in jima a
wurinku, har ma in yi damuna, domin ku taimaka
mani game da tafiyata, duk inda za ni. 7 Gama ba
na so in yi maku gani na gajeren lokaci. Don ina so
in dau lokaci tare da ku, idan Ubangiji ya yarda. 8
Amma zan tsaya Afisus har ranar Fentikos. 9 Gama
an bude mani kofa mai fadi, kuma akwai magabta da
yawa. 10 Sa'adda Timoti ya zo, ku tabbata ya sami
sakewa acikinku, tun da aikin Ubangiji yake yi kamar
yadda nake yi. 11 Kada fa kowa ya rena shi. Ku tabbata
kun sallame shi lafiya, domin ya komo gare ni, don
ina duban hanyarsa tare da yan'uwa. 12 Game da
zancen dan'uwanmu Afollos kuwa, na karfafa shi ya
ziyarce ku tare da 'yan'uwa. Sai dai baya sha'awar
zuwa yanzu. Amma zai zo sa'adda lokaci ya yi. 13
Ku zauna a fadake, ku tsaya daram cikin bangaskiya,
kuna nuna halin maza, ku yi karfin hali. 14 Bari dukan
abinda kuke yi ayi shi cikin kauna. 15 Kun dai sani
iyalin gidan Sitefanas su suka fara tuba a Akaya, kuma
sun bada kansu ga yi wa masu bi hidima. Yanzu ina
rokonku, 'yan'uwa, 16 kuyi biyayya da irin wadannan
mutane da duk wanda ke taimakawa a cikin aikin,
yana kuma fama tare da mu. 17 Na yi farinciki da
zuwan Sitefanas, da Fartunatas, da Akaikas. Sun debe
mini kewarku. 18 Gama sun wartsakar da ruhuna da
naku kuma. Don haka, Sai ku kula da irin wadannan
mutane. 19 Ikilisiyoyin kasar Asiya suna gaishe ku.

Akila da Bilkisu, tare da ikilisiyar da take taruwa a
gidansu, suna gaishe ku cikin Ubangiji. 20 Dukan
'yan'uwa masu bi na gaishe ku. Ku gaida juna da
sumba maitsarki. 21 Ni Bulus, nake rubuta wannnan
da hannuna. 22 Duk wanda ba ya kaunar Ubangiji bari
ya zama la'ananne. Ubangijinmu, Ka zo! 23 Alherin
Ubangiji Yesu ya kasance tare da ku. 24 Bari kaunata
ta kasance tare da ku duka a cikin Almasihu Yesu. [
Amin ].

# 2 Korintiyawa

**1** Bulus, manzon Almasihu Yesu ta wurin nufin Allah,
da kuma Timoti dan'uwan mu, zuwa ga Ikilisiyar
Allah da ke a Korantus, da kuma dukan 'yan'uwa da
ke yankin kasar Akaya. 2 Bari alheri ya kasance tare
da ku da kuma salama ta Allah Ubanmu da kuma
Ubangiji Yesu Almasihu. 3 Bari yabo ya tabbata ga
Allah da kuma Uba na Ubangijinmu Yesu Almasihu.
Shine Uba na dukan jiyejiyenkai, da kuma Allah na
dukan ta'aziya. 4 Allah yana ta'azantar da mu a
cikin dukan wahalarmu, domin mu iya ta'azantar da
wadanda ke cikin kowace wahala. Muna ta'azantar
da wasu da irin ta'aziyar da Allah ke ta'azantar da
mu. 5 Gama kamar yadda wahalhalun Almasihu suka
karu domin mu, haka kuma ta'aziyarmu ta yawaita
cikin Almasihu. 6 Amma fa idan muna shan wuya,
domin ta'aziyarku ne da cetonku. Haka kuma in mun
ta'azantu, domin ta'aziyarku ne. Ta'aziyarku tana
aiki ne sosai yayinda kuka jure da irin shan wuyar
da mu ma muke sha. 7 Kuma gabagadinmu game da
ku tabbatacce ne. Mun kuwa sani kamar yadda kuke
tarayya cikin shan wahalhalun, haka kuma za ku yi
tarayya cikin ta'aziyyar. 8 Gama ba mu so ku rasa sani,
'yan'uwa, game da tsananin da ya same mu a Asiya.
An murkushe mu gaba daya har fiye da karfin mu,
har ma mun fidda zuciya za mu rayu. 9 Hakika, mun ji
hukuncin mutuwa akan mu. Amma wannan ya faru
ne domin kada mu dogara ga kanmu, sai dai ga Allah,
wanda ke tada matattu. 10 Ya kubutar da mu daga
wannan mummunan hatsari na mutuwa, kuma zai
sake kubutar da mu. Mun kafa begenmu gare shi cewa
zai sake kubutar da mu. 11 Zai aikata wannan yayinda
kuka taimake mu da addu'ar ku. Sa'an nan da dama za
su bada godiya a madadin mu don tagomashin alheri
da aka yi mana ta wurin addu'o'in mutane masu
yawa. 12 Muna kuwa alfahari da haka: wato shaidar
lamirinmu. Gama da kyakkyawan nufi da aminci da
ke zuwa daga Allah muka tafiyar da rayuwarmu a
Duniya. Mun yi wannan ne musamman tare da ku-
ba kuwa cikin hikimar Duniya ba, amma ta wurin
alherin Allah. 13 Bamu rubuta maku abinda ba za ku
iya karantawa ko fahimta ba. Ina fata za ku fahimce
mu baki daya, 14 kamar yadda kuka fahimce mu kadan
yanzu. Daganan a ranar Ubangijinmu Yesu za mu
zama dalilinku na alfahari, kamar yadda za ku zama
namu. 15 Saboda gabagadin da nake da shi game da
haka, naso in zo gare ku da farko, domin ku amfana
da ziyara sau biyu. 16 Ina da shirin ziyaratar ku a kan
hanyata ta zuwa Makidoniya. Daga nan kuma ina da yi
niyyar in sake ziyartar ku, a tafiya ta daga Makidoniya,
domin ku aike ni a hanyata ta zuwa Yahudiya. 17
Yayinda nake irin wannan tunani, ina shakka ne?
Ina shirya abubuwa ne bisa ga magwajin mutum, ta
yadda har zan ce “I, i” da “A, a, a, a” a lokaci guda?
18 Amma kamar yadda Allah yake amintacce, ba ma
fadin ''I'' da ''A'a'' a lokaci guda. 19 Gama Dan Allah,
Yesu Almasihu, wanda Silbanus da Sila, da Ni muka
shaida maku, ba “I” da “A, a” ba ne. Maimakon haka,
Shi “I” ne a kodayaushe. 20 Gama dukan alkawaran
Allah 'I' ne a cikin sa. Haka kuma ta wurin sa muna
cewa ''Amin'' zuwa ga daukakar Allah. 21 Yanzu dai
Allah ne ya tabbatar da mu da ku a cikin Almasihu, ya
kuma kebe mu. 22 Ya sa hatiminsa a kan mu ya kuma
ba mu Ruhu a zuciyar mu a matsayin tabbacin abinda
zai bamu daga baya. 23 Maimakon haka, na yi kira
ga Allah ya zama shaida domina, cewa dalilin dayasa
banzo Korintis ba domin in kare ku ne. 24 Ba muna
kokarin mu sarrafa yadda bangaskiyar ku za ta zama
ba ne. Maimakon haka, muna aiki tare da ku ne domin
farincikinku, yayinda kuke tsaye cikin bangaskiyarku.

**2** Don haka na yanke shawara daga bangarena, ba
zan sake zuwa wurin ku cikin yanayi mai tsanani
ba. 2 Idan na bata maku rai, wa zai karfafa ni, in
ba shi wanda na bata wa rai ba? 3 Na rubuto maku
kamar yadda na yi domin idan na zo gareku kada
in sami bacin rai a wurin wadanda ya kamata su
faranta mani rai. Ina da gabagadi game da dukan
ku, cewa farincikin da nake da shi, shine kuke da
shi duka. 4 Domin kuwa na rubuto maku cikin kunci
da bacin rai da kuma hawaye mai yawa. Ba zan so
in sake bata maku rai ba. Maimakon haka, na so ku
san zurfin kaunar da nake da ita domin ku. 5 Idan
wani ya kawo sanadin bacin rai, ba ni kadai ya kawo
wa wannan abin ba, amma ta wani fannin- domin
kada a tsananta- har a gare ku duka. 6 Hukuncin nan
da galibinku kuka yi wa mutumin nan ya isa. 7 Don
haka, yanzu a maimakon hukunci, ku gafarta masa,
ku kuma ta'azantar da shi. Ku yi haka domin kada
bakinciki mai yawa ya danne shi. 8 Don haka ina
karfafa ku da ku nuna irin kaunar da kuke yi masa a
fili. 9 Wannan shine dalilin da ya sa na rubuto maku,
domin in gwada ku, ko kuna biyayya cikin komai. 10

Duk mutumin da kuka gafarta wa, ni ma na gafarta
masa. Abin da na gafarta-idan na gafarta wani abu-an
gafarta ne domin ku a gaban Almasihu. 11 Wannan ya
zama haka ne domin kada shaidan ya yaudare mu.
Don ba mu jahilci irin makircinsa ba. 12 Na samu
budaddiyar kofa daga wurin Ubangiji yayin da nazo
birnin Tarwasa, in yi wa'azin bisharar Almasihu a
can. 13 Duk da haka, raina bai kwanta ba, domin ban
ga dan'uwana Titus a can ba. Sai na bar su a can,
na dawo Makidoniya. 14 Amma godiya ta tabbata ga
Allah, wanda cikin Almasihu yake kai mu ga nasara
a koyaushe. Ta wurin mu ya baza kamshi mai dadi
na saninsa ko'ina. 15 Gama mu, kamshi ne mai dadi
na Almasihu ga Allah, a tsakanin wadanda ake ceton
su, da kuma tsakanin wadanda suke hallaka. 16 Ga
mutanen da suke hallaka, kamshi ne daga mutuwa
zuwa mutuwa. Ga wadanda suke samun ceto kuma
kamshi ne daga rai zuwa rai. Wanene ya cancanci
wadannan abubuwan? 17 Gama mu ba kamar sauran
mutane muke ba, masu sayar da maganar Allah domin
samun riba. Maimakon haka, da tsarkakkiyar manufa,
muke magana cikin Almasihu, kamar yadda Allah ya
aiko mu, a gaban Allah.

3 Muna fara sake yabon kanmu ne? Ba mu bukatar
wasikun shaida daga gare ku ko zuwa gare ku,
kamar wadansu mutane, ko ba haka ba? 2 Ku da
kanku kune wasikar shaidarmu, wadda aka rubuta a
zukatanmu, wadda Kuma dukan mutane suka sani
suke kuma karantawa. 3 Kuma kun nuna ku wasika ne
daga Almasihu, wadda muka isar. Ba da tawada aka
rubuta ta ba amma da Ruhun Allah mai rai. Ba bisa
allunan duwatsu aka rubuta ta ba, amma bisa allunan
zukatan mutane. 4 Gama wannan ne gabagadin da
muke da shi cikin Allah ta wurin Almasihu. 5 Ba mu da
wata gwanintar kanmu da za mu yi takamar wani abu
ya zo daga gare mu. Maimakon haka, gwanintar mu
daga Allah take. 6 Allah ne ya maishe mu kwararrun
bayi na sabon alkawari. Wannan alkawari ne ba na
rubutu ba amma na Ruhu. Gama rubutu kisa yake yi,
amma Ruhu rai yake bayarwa. 7 To hidimar da ta
haifar da mutuwa- wadda aka rubuta bisa duwatsu- ta
zo cikin irin wannan daukaka da har Israila ba su iya
kallon fuskar Musa kai tsaye ba. Wannan kuwa saboda
daukakar da ke fuskarsa ne, daukaka mai shudewa.
8 Ina misalin girman daukakar hidimar da Ruhu ke
yi? 9 Gama idan hidimar kayarwa tana da daukaka,
ina misalin yalwatar daukaka da hidimar adalchi za
ta yi! 10 Babu shakka, abin da aka maishe shi mai
daukaka a da, ba ya da sauran daukaka a wannan
fanni, saboda irin daukakar da ta zarce shi. 11 To
idan har mai shudewar nan ya na da daukaka, ina
misalin daukakar da abu na dindindin zai samu! 12
Dashike muna da wannan tabbaci, muna da gabagadi
sosai. 13 Ba kamar Musa muke ba wanda ya sa mayafi
ya rufe fuskarsa, ta yadda mutanen Isra'ila basu iya
kallon karshen daukaka mai shudewa ba kai tsaye.
14 Amma tunaninsu ya zama a rufe. Har yau kuwa
mayafin na nan sa'adda ake karanta tsohon alkawari.
Ba a bude shi ba, saboda a cikin Almasihu ne kadai
ake kawar da shi. 15 Amma har yau, duk lokacin da
ake karanta littafin Musa, akwai mayafi shimfide a
zukatansu. 16 Amma sa'adda mutum ya juyo wurin
Ubangiji, an kawar da mayafin. 17 To Ubangiji shine
Ruhun. Inda Ruhun Ubangiji yake, akwai 'yanci. 18
Dukan mu yanzu, da fuskoki marasa mayafi, muna
ganin daukakar Ubangiji. Muna samun sakewa zuwa
cikin irin wannan daukaka, daga wannan mataki na
daukaka zuwa wani matakin, kamar dai daga wurin
Ubangiji, wanda shine Ruhun.

4 Don haka, domin muna da wannan hidima, da
kuma yadda muka karbi jinkai, ba mu karaya ba. 2
Maimakon haka, sai muka rabu da dukan hanyoyin da
ke na kunya, kuma na boye. Ba mu rayuwar makirci,
kuma bamu yiwa maganar Allah rikon sakaci. Ta
wurin gabatar da gaskiya, muna mika kanmu ga
lamirin kowa a gaban Allah. 3 Amma, idan bisharar mu
a rufe take, tana rufe ne ga wadanda ke hallaka. 4 A
al'amarinsu, allahn wannan duniya ya makantar da
zukatansu marasa bada gaskiya. A sakamakon haka,
ba su iya ganin hasken bisharar daukakar Almasihu
ba, wanda shine surar Allah. (aiōn g165) 5 Gama ba mu
yin shelar kanmu, amma Almasihu Yesu a matsayin
Ubangiji, mu kuma bayinku saboda Yesu. 6 Gama
Allah shine wanda ya ce, “Haske zai haskaka daga
cikin duhu.” Ya haskaka cikin zukatanmu don ya bada
hasken sanin daukakar Allah a gaban Yesu Almasihu.
7 Amma muna da wannan dukiya a randunan yunbu,
yadda zai zama a bayyane cewa mafi girman iko na
Allah ne ba namu ba. 8 Muna shan tsanani ta kowace
hanya, ba a ci mu dungum ba. Mun rikice amma ba
mu karaya ba, an tsananta mana amma ba a watsar
da mu ba. 9 Ana tsananta mana amma ba a yashe
mu ba. Aka doddoke mu amma ba mu lalace ba. 10

Mu dai a kullayaumin muna dauke da mutuwar Yesu
a jikkunanmu, saboda a bayyana rayuwar Yesu a
jikkunanmu kuma. 11 Mu da muke a raye kuwa a
kulluyaumin ana mika mu ga mutuwa saboda Yesu,
domin rayuwar Yesu ta zama a bayyane a jikunanmu
na mutuntaka. 12 Saboda haka, mutuwa tana aiki a
cikinmu, amma rai na aiki a cikinku. 13 Amma dai
muna da wannan Ruhu na bangaskiya kammar yadda
aka rubuta: “Na gaskata, saboda haka na furta.” Mu
ma mun gaskata, haka kuwa muke fada. 14 Mun sani
cewa wanda ya tada Ubangiji Yesu daga matattu za ya
sake tada mu tare da Yesu. Mun san cewa zai gabatar
da mu tare da ku a gabansa. 15 Dukan abubuwa sabili
da ku suke domin, yayin da aka baza alheri ga mutane
dayawa, bada godiya ta karu ga daukakar Allah. 16
Don haka ba mu karaya ba. Kodashike daga waje muna
lalacewa, daga ciki ana sabunta mu kulluyaumin.
17 Domin wannan 'yar wahala ta dan lokaci tana
shirya mu zuwa ga nauyin madauwamiyar daukaka
wadda ta wuce gaban aunawa. (aiōnios g166) 18 Domin
ba muna kallon abubuwan da ake gani bane, amma
abubuwan da ba a gani. Abubuwan da muke iya gani
ba masu dawwama ba ne, amma abubuwan da ba a
gani madawwama ne. (aiōnios g166)

5 Mun san cewa idan wannan gidan da muke zaune a
ciki ya rushe, muna da wani ginin daga wurin Allah.
Gida ne wanda ba hannuwan mutane suka gina ba,
amma madawwamin gida ne a cikin sama. (aiōnios g166)
2 Domin a cikin wannan jiki muna gurnani, muna jira a
suturta mu da wurin zaman mu na samaniya. 3 Muna
jiran wannan ne domin ta wurin suturtar da mu ba za
a same mu tsirara ba. 4 Gama babu shakka yayinda
muke cikin wannan alfarwa, muna gurnani, muna
nawaita. Ba mu so muyi zaman hutanci. Maimakon
haka, muna so a suturtar da mu, domin rai ya hadiye
abu mai mutuwa. 5 Wanda kuwa yake shirya mu
domin ainihin wannan abu Allah ne, wanda ya ba
mu Ruhu a matsayin alkawarin abinda ke zuwa. 6
Domin wannan mu zama da gabagadi koyaushe. Mu
lura da cewa yayinda muka shagala cikin jiki, muna
nesa da Ubangiji. 7 Gama bisa ga bangaskiya muke
tafiya, ba bisa ga ganin ido ba. 8 Don haka muna da
gabagadi. Mun gwammace mu rabu da jiki domin
mu zauna tare da Ubangiji. 9 Sai muka maishe shi
burinmu, ko muna cikin jiki ko nesa, mu gamshe shi.
10 Domin tilas dukanmu mu hallara a gaban kursiyin
shari'a na Almasihu, saboda kowa ya karbi sakamakon
abubuwan da yayi cikin jiki, ko masu kyau ne ko
marasa kyau. 11 Don haka, domin mun san tsoron
Ubangiji, muna rinjayar mutane. Allah na ganin yadda
muke a fili. Ina fatan hakan a fili take ga lamirinku.
12 Ba muna kokarin mu rinjaye ku domin ku kalle
mu a matsayin amintattun mutane ba. Maimakon
haka, muna ba ku dalilin yin takama da mu, domin ku
sami amsar da za ku bada ga wadanda ke fahariya da
kasancewarsu amma ba game da abinda ke zuciya
ba. 13 Gama idan mun fita daga hankulanmu, saboda
Allah ne. Kuma idan muna cikin hankalinmu, domin
ku ne. 14 Domin kaunar Almasihu ta tilas ta mu,
domin mun tabbatar da wannan: cewa mutum daya
ya mutu domin kowa, kuma domin wannan duka
sun mutu. 15 Kuma Almasihu ya mutu domin kowa,
domin wadanda ke raye kada su sake rayuwa domin
kansu. A maimakon haka, su yi rayuwa domin shi
wanda ya mutu kuma aka tashe shi. 16 Domin wannan
dalili, daga yanzu ba za mu kara shar'anta kowa
bisa ga ma'aunin 'yan'adam ba, ko da yake a baya
mun taba duban Almasihu a haka. Amma yanzu mun
daina shar'anta kowa ta haka. 17 Saboda haka, duk
wanda ke cikin Almasihu, sabon halitta ne. Tsofaffin
al'amura sun shude. Duba, sun zama sababbi. 18 Dukan
wadannan abubuwa daga Allah ne. Ya sulhunta mu da
kansa ta wurin Almasihu, ya kuma ba mu hidimar
sulhu. 19 Wato, cikin Almasihu, Allah na sulhunta
duniya zuwa gare shi, ba tare da lissafin zunubansu a
kansu ba. Yana damka mana sakon sulhu. 20 Don haka
an zabe mu a matsayin wakilan Almasihu, kamar dai
Allah na kira ga mutane ta wurin mu. Muna rokon ku,
saboda Almasihu: ''ku sulhuntu ga Allah!'' 21 Shi ya
maida Almasihu ya zama hadaya domin zunubinmu.
Shine wanda bai taba zunubi ba. Ya yi haka ne don
mu zama adalchin Allah a cikin sa.

6 haka, tundashike muna aiki tare, na roke ku kar
ku yi watsi da alherin Allah. 2 Domin ya ce, “A
lokacin alheri na saurare ku, kuma a ranar ceto na
agaje ku.” Yanzu ne fa, lokacin alheri. Duba, yanzu
ne ranar ceto. 3 Ba mu sa sanadin faduwa a gaban
kowannen ku, domin ba mu so hidimarmu ta zama
marar amfani. 4 Maimakon haka, mun tabbatar da kan
mu ta wurin dukan ayyukanmu, cewa mu bayin Allah
ne. Mu bayinsa ne ta wurin yawan jimiri, azaba, kunci,
wahala, 5 duka, kurkuku, tarzoma, cikin aiki tukuru,

cikin rashin barci yawancin dare, cikin yunwa, 6
cikin tsarki, ilimi, hakuri, kirki, cikin Ruhu Mai tsarki,
da sahihiyar kauna. 7 Mu bayinsa ne cikin kalmar
gaskiya, cikin ikon Allah. Muna kuma da makamai na
adalci, a hanun dama da hagu. 8 Muna aiki cikin daraja
da rashin daraja, kushe da yabo. Ana zargin mu a kan
mu mayaudara ne, duk da haka mu masu gaskiya ne.
9 Muna aiki kamar ba a san mu ba, gashi kuwa mu
sanannu ne. Muna aiki kamar masu mutuwa-duba!
-har yanzu muna raye. Muna aiki kamar wadanda
aka hukunta, amma ba hukuncin kisa ba. 10 Muna
aiki kamar muna bakinciki, amma a koyaushe muna
farinciki. Muna aiki kamar matalauta, amma muna
azurta mutane dayawa. Muna aiki kamar ba mu da
komai, amma mun mallaki komai. 11 Mun fada maku
dukan gaskiyar, Korantiyawa, kuma zuciyar mu a bude
ta ke. 12 Ba mu kange zukatan ku ba, ku ne kuka kange
zukatanku a gare mu. 13 Yanzu a sabanin haka-Ina
magana da ku kamar yara-ku bude mana zukatanku.
14 Kada ku yi cudanya da marasa bangaskiya. Wace
tarayya ke tsakanin adalci da take shari'a? Ko kuma
wace zumunta ce ke tsakanin haske da duhu? 15 Wace
yarjejeniya ke tsakanin Almasihu da Ibilis? ko kuma
me ya hada masu bangaskiya da marasa bangaskiya?
16 ko wace yarjejeniya ce a tsakanin haikalin Allah da
gumaka? Domin kuwa mu haikali ne na Allah mai
rai, kamar yadda Allah ya ce: "Zan zauna a cikin su,
in kuma yi tafiya a tsakanin su. Zan zama Allahnsu,
su kuma za su zama mutanena." 17 Sabili da haka,
"Ku fito daga cikin su, kuma ku zama kebabbu," in ji
Ubangiji. "Kada ku taba kazamin abu, zan kuma karbe
ku. 18 Zan zama Uba a gare ku, ku kuma za ku zama
'ya'ya maza da mata a gare ni," in ji Ubangiji Mai iko
duka.

**7** Kaunatattu, da shike muna da wadannan alkawura,
bari mu tsaftace kanmu, daga dukan abubuwan
da ke kazantar da jikinmu da ruhunmu. Bari mu bidi
tsarki cikin tsoron Allah. 2 Ku ba mu dama! Bamu
bata wa kowa rai ba. Ba mu cutar da kowa ko mu
zambaci kowa ba. 3 Ba domin in kayar da ku na fadi
haka ba. Domin kuwa na riga na fada muku, cewa
kuna zuciyar mu, domin mu mutu tare mu kuma rayu
tare. 4 Ina da muhimmin gabagadi a cikin ku, Ina
fahariya da ku. Ina cike da ta'aziya. Farincikina ya
cika makil duk da wahalhalunmu. 5 Yayin da muka zo
Makidoniya, jikinmu bai samu hutu ba. A maimakon
haka, mun shiga matsaloli ta ko wace hanya ta wurin
tashin hankali a waje tsoro kuma a ciki. 6 Amma
Allah, mai ta'azantar da raunana, ya ta'azantar da mu
ta wurin zuwan Titus. 7 Ba ta wurin isowar sa kadai
Allah ya yi mana ta'aziyya ba. Amma kuma ta wurin
ta'aziyyar da Titus ya samu daga wurin ku. Ya gaya
mana irin matsananciyar kaunarku, bakincikinku, da
zurfin kulawarku a kaina. Na kuwa yi farinciki sosai. 8
Kodashike wasikata, ta bata maku rai, ban yi da na
sanin haka ba. Amma sa'adda na ga wasika ta ta bata
maku rai, na yi da na sani. Sai dai bacin ranku, na dan
lokaci ne. 9 Yanzu kuwa, ina farinciki, ba domin bacin
ranku ba, amma domin bacin ranku ya kawo ku ga
tuba, kun fuskanci bakinciki na ibada, donhaka ba
ku yi rashi ba sabili da mu. 10 Domin bakinciki daga
Allah ya kan kai ga tuba da ke kammala ceto ba tare
da-da na sani ba. Bakinciki na duniya kuwa ya kan
kai ga mutuwa. 11 Ku dubi irin kyakkyawar niyya da
bakincikin nan daga Allah ya haifar a cikin ku. Ina
misalin girman niyyar nan taku ta nuna cewa baku
da laifi. Ina misalin girman fushinku, tsoronku, da
sa zuciyarku, himmar ku, da marmarin ku na ganin
cewa an yi adalci! A cikin komai, kun nuna kanku
marasa laifi a cikin wannan al'amari. 12 Kodayake
na rubuto maku, ban rubuto saboda mai laifin ba, ko
kuma saboda wanda aka yi wa laifin. Na rubuto ne
domin himmarku gare mu ta sanu gare ku a gaban
Allah. 13 Dalilin haka ne muka samu karfafawa. Baya
ga ta'aziyyar mu, mun kuma yi murna sosai saboda
farin cikin Titus, domin ruhunsa ya wartsake ta wurin
ku duka. 14 Domin kuwa idan na yi fahariya da ku
a gaban sa, ban ji kunya ba. A sabanin haka, kamar
yadda kowane abu da muka fada maku gaskiya ne,
fahariyarmu a kan ku ga Titus ta zama gaskiya. 15
Kaunarsa a gare ku tana da girma, kamar yadda ya
rika tunawa da biyayyarku duka, yadda kuka karbe
shi da tsoro da rawar jiki. 16 Ina farinciki matuka
domin ina da cikakken gabagadi a cikin ku.

**8** Muna so ku sani, 'yan'uwa, game da alherin Allah
da aka bayar ga Ikkilisiyoyin Makidoniya. 2 A
lokacin babban gwajin wahala, yalwar farincikinsu
da tsananin talaucinsu ya haifar da yalwar bayarwa
hannu sake. 3 Domin ina shaida, sun yi bayarwa iya
kokarinsu, fiye da abinda ma suke iyawa. Cikin yaddar
ransu 4 da roko mai yawa suka nace da a ba su zarafi
su yi tarayya a wannan hidima ga masu bi. 5 Haka ya

auku ba kamar yadda muka yi zato ba. A Maimakon
haka, sai da suka fara bada kansu ga Ubangiji. Kuma
suka bada kansu gare mu bisa ga nufin Allah. 6 Sai
muka karfafa Titus, wanda ya rigaya ya fara wannan
aiki, domin ya kammala wannan aiki na bayarwa ta
fannin ku. 7 Amma kun habaka cikin komai-cikin
bangaskiya, cikin magana, cikin sani, cikin aiki tukuru,
cikin kaunarku dominmu. Don haka, ku tabbata kun
habaka a wannan aiki na bayarwa. 8 Na fadi haka ne
ba kamar ina umurtar ku ba. A maimakon haka, na
fadi haka ne in gwada sahihancin kaunarku ta wurin
kwatanta ta da himmar sauran mutane. 9 Domin kun
san alherin Ubangijinmu Yesu Almasihu. Kodashike
shi mai arziki ne, amma ya zama matalauci, domin ta
wurin talaucinsa ku yi arziki. 10 A wannan al'amari
zan ba ku shawarar da za ta taimake ku. Shekarar da
ta wuce, ba fara wani abu kawai kuka yi ba, amma
kun yi marmarin ku yi shi. 11 Yanzu ku kammala
shi. Kamar yadda kuke da niyya da marmarin yin
haka a lokacin, bari ku yi kokari ku kawo shi ga
kammalawa iyakar iyawar ku. 12 Idan kuna niyya
ku yi wannan aiki, abu mai kyau ne karbabbe kuma.
Tabbas ya zama dai-dai da abinda mutum ke da shi,
ba abinda ba ya da shi ba. 13 Domin wannan aiki
ba domin a nawaita maku sannan wadansu su samu
sauki ba ne. A maimakon haka, ya kamata a sami
daidaituwa. 14 Yalwar ku a wannan lokaci za ta zama
abin biyan bukatarsu. Haka nan kuma domin yalwar
su ta iya biyan bukatarku, domin a sami daidaituwa.
15 Yana nan kamar yadda aka rubuta: “Wanda ke da
shi dayawa bai samu raguwar komai ba, kuma wanda
yake da kadan bai rasa komai ba.” 16 Amma godiya ga
Allah, da yasa a zuciyar Titus marmarin kulawa da ku
kamar wadda nake da ita domin ku. 17 Gama ba rokon
mu kadai ya karba ba, amma ya yi da gaske akan haka.
Ya zo gare ku ne da yardar kan sa. 18 Mun aiko tare
da shi dan'uwa da ake yaba masa a tsakanin dukan
Ikkilisiyoyi domin ayyukansa a cikin shelar bishara. 19
Ba domin wannan kadai ba, amma Ikkilisiyoyi ne suka
zabe shi ya tafi tare da mu a cikin yin wannan hidima
ta alheri. Wannan domin girmama Ubangiji ne kansa
da kuma domin aniyarmu ta taimakawa. 20 Muna
gudun kada kowa ya sa mana laifi game da wannan
alheri da muke dauke da shi. 21 Niyyar mu ce mu yi
kyakkyawan abu, ba a gaban Ubangiji kadai ba, amma
a gaban mutane ma. 22 Mun kuma aiki wani dan'uwan
tare da su. Mun sha gwada shi, kuma mun same shi
da himma wajen ayyuka da dama. Yanzu kuma ya
kara himma, saboda amincewa mai girma da yake da
ita gare ku. 23 Game da Titus, shi abokin tafiyata ne,
kuma abokin aikina domin ku. Game da yan'uwanmu,
an aiko su ne daga Ikkilisiyoyi. Su kuwa daraja ne ga
Almasihu. 24 Don haka, ku nuna masu kaunarku, ku
kuma nuna wa Ikilisiyoyi dalilin fahariyarmu game da
ku.

9 Game da hidima domin tsarkaka, ya dace in rubuta
maku. 2 Na san marmarinku, wanda na yi fahariya
da shi a gaban mutanen Makidoniya. Na gaya masu
Akaya sun riga sun shirya tun bara. Kwazon ku ya
sa yawancin su sun shiga aiki. 3 To na aiko maku da
'yan'uwa saboda kada fahariyarmu akanku ta zama a
banza, domin kuma ku zauna a shirye, kamar yadda
na ce za ku yi. 4 Idan kuwa ba haka ba, idan wani
cikin makidoniyawa ya biyoni kuma ya tarar da baku
shirya ba, za mu ji kunya-ba ni cewa komai game da
ku-domin ina da gabagadi a kan ku. 5 Sai na ga ya
dace in turo 'yan'uwa su zo wurin ku kafin lokaci yayi
suyi shirye shirye game da gudummuwar da kuka yi
alkawari. Wannan ya zama haka ne domin a shirya
shi a matsayin bayarwar albarka, ba wani abin kwace
ba. 6 Batun shine: wanda ya shuka kadan zai girbi
kadan, wanda kuma ya shuka da manufar albarka zai
girbi albarka 7 Bari kowa ya bayar bisa ga yadda ya
yi niyya a zuciyarsa. Kada ya bayar da bacin rai ko
kamar dole. Gama Allah yana kaunar mai bayarwa da
dadin rai. 8 Allah na da ikon ya sa kowace albarka
ta ribanbanya domin ku, domin, a koyaushe, a cikin
dukan abubuwa, ku sami duk abinda kuke bukata.
Hakan zai kasance domin ku ribabbanya kowanne
kyakkyawan aiki. 9 Kamar yadda aka rubuta, ''Ya
rarraba arzikinsa, ya bada shi ga matalauta. Adalcinsa
ya dawwama har abada.'' (aiōn g165) 10 Shi wanda ke
bayar da iri ga mai shuka da gurasa domin abinci,
zai bayar ya kuma ribabbanya maku iri domin shuka.
Zai sa girbin adalcinku ya karu. 11 Za ku wadata ta
kowace hanya domin ku zama masu bayarwa, wannan
kuwa zai sa a yi wa Allah godiya ta wurin mu. 12
Aiwatar da wannan hidima ba biyan bukatun tsarkaka
kawai take yi ba. Tana kuma ribanbanya zuwa ayyuka
masu yawa na bada godiya ga Allah. 13 Domin an
gwada ku an tabbatar da ku akan wannan hidima,
za ku kuma daukaka Allah ta wurin biyayyar ku ga
shaidar bisharar Almasihu. Za ku kuma daukaka Allah

ta wurin yalwar bayarwarku gare su da kowa duka. 14
Suna marmarin ganin ku, suna kuma yi maku addu'a.
Suna yin haka saboda alherin Allah mai girma da ke
bisan ku. 15 Godiya ga Allah domin kyautarsa wadda
ta fi gaban bayyanawa.

10 Ni, Bulus, da kaina nake rokon ku, ta wurin
tawali'u da nasihar Almasihu. Ina da saukin kai
yayinda nake gaban ku, amma ina da gabagadi a gare
ku yayinda ba na tare da ku. 2 Ina rokon ku, yayinda
nake gabanku, ba ni so in zama mai tsaurin hali. Amma
ina ganin zan bukaci zama mai gabagadi sa'adda nake
tsayayya da su wadanda ke zaton muna zama bisa
ga jiki. 3 Kodashike dai muna tafiya bisa jiki, ba ma
yin yaki bisa jiki. 4 Domin makaman da muke yaki da
su ba na jiki ba ne. Maimakon haka, makamai ne na
Allah da ke da ikon rushe ikokin shaidan. Suna kawar
da dukan gardandamin da ke kawo kaucewa. 5 Muna
kuma rushe duk wani abinda ke gaba da sanin Allah.
Muna kuma kama kowanne tunani zuwa biyayya ga
Almasihu. 6 Muna kuma shirye mu hukunta kowanne
irin aiki na rashin biyayya, da zarar biyayyarku ta
tabbata. 7 Dubi abin da aka sa a bayyane a gaban ku.
In har wani ya tabbata shi na Almasihu ne, bari fa ya
tunatar da kansa cewa kamar yadda shi na Almasihu
ne, hakanan muma muke. 8 Ko da zan yi fahariya da
ikon da muke dashi, wanda Ubangiji ya ba mu domin
mu inganta ku, ba domin mu rushe ku ba, ba zan
ji kunya ba. 9 Ba na so ya zama kamar ina firgita
ku ne da wasikuna. 10 Domin wadansu mutane na
cewa, "Wasikunsa na da iko da firgitarwa, amma in ka
gan shi kumama ne. Kalmominsa ba abin saurare ba
ne." 11 Bari wadannan mutane su sani cewa abinda
muke fadi a kalmomin wasikunmu lokacin da ba mu
nan, haka za mu yi in muna nan. 12 Mu dai ba mu
hada kanmu da kowa, ko kuma mu kwatanta kanmu
da wadanda ke yabon kansu. Amma yayin da suke
gwada kansu da junansu, suke kuma kwatanta kansu
da junansu, ba su da ganewa. 13 Saidai, ba za mu
yi fahariya fiye da yadda ya kamata ba. Maimakon
haka, za mu yi haka ne gwalgwadon iyakar abinda
Allah ya sa muyi, iyakar da takai gareku. 14 Gama
bamu yi zarbabi ba sa'adda muka kai gareku. Mune na
farko da muka kai gare ku da bisharar Almasihu. 15
Ba mu yi fahariya fiye da kima game da aikin wasu
ba. Maimakon haka, muna fatan bangaskiyar ku ta
karu domin bangaren aikin mu ya kara fadada kwarai,
kuma a daidai iyakarsa. 16 Muna fatan haka, domin
mu kai bishara zuwa yankunan da ke gaba da naku.
Ba za mu yi fahariya akan aikin da aka yi a yankin
wani ba. 17 "Amma bari duk wanda zai yi fahariya,
ya yi ta cikin Ubangiji." 18 Domin ba wanda ya ke
shaidar kansa shine yardajje ba. Maimakon haka, sai
dai wanda Ubangiji ke shaidarsa.

11 Ina fatan za ku jure da ni cikin wauta kadan.
Ko da yake lallai kuna jurewa da ni! 2 Domin
ina kishi sabili da ku. Kishi na kuwa irin na Allah ne
domin ku. Tun da na alkawartar da ku a cikin aure
ga miji daya. Na kuma yi alkawarin in gabatar da ku
kamar budurwa mai tsarki ga Almasihu. 3 Gama ina
fargaba a kan ku, ko watakila, kamar yadda macijin
ya yaudari Hauwa'u ta wurin kissarsa, Ya zamana
tunaninku ya kauce daga sahihiyar sadaukarwa ga
Almasihu. 4 Anar misali idan wani ya zo ya kawo
shelar wani Yesu daban da wanda muka yi maku
wa'azinsa. Ko kuma kun karbi wani ruhu daban da
wanda muka karba. Ko kuma kun karbi wata bishara
daban da wadda muka karba. Amincewar da kuka
yi wa wadannan abubuwa ta isa! 5 Don kuwa ina
tsammanin ba a baya nake ba ga sauran wadanda ake
kira manyan manzanni. 6 To ko ma ba a ilimantar da
ni ba akan yin jawabi, ban rasa horarwar ilimi ba. Ta
kowace hanya kuma cikin abubuwa duka mun sanar
da ku wannan. 7 Na yi zunubi ne da na kaskantar
da kai na domin a daukaka ku? Domin na yi maku
wa'azin bisharar Allah kyauta. 8 Na yi wa sauran
Ikilisiyoyi kwace ta wurin karbar gudummuwa daga
wurin su domin inyi maku hidima. 9 Lokacin da ina
tare da ku kuma na sami kai na cikin bukata, ban dora
wa kowa nauyi ba. Domin 'yan'uwa da suka zo daga
Makidoniya sun biya bukatuna. A cikin komai na kebe
kaina daga zama nawaya a gare ku, kuma zan cigaba
da yin haka. 10 Kamar yadda gaskiyar Almasihu ke ciki
na, ba zan yi shiru da wannan fahariya tawa ba a cikin
dukan kasar Akaya. 11 Don me? Saboda ba na kaunar
ku? Allah ya sani. 12 Amma abinda na ke yi, zan cigaba
da yi. Zan yi haka ne domin in yanke zarafin wadanda
ke son samun zarafi kamar mu akan abubuwan da
suke fahariya da shi. 13 Don irin wadannan mutane
manzannin karya ne masu aikin yaudara. Suna badda
kama kamar manzannin Almasihu. 14 Wannan ba
abin mamaki ba ne, domin shaidan ma yakan badda
kama ya fito kamar mala'ikan haske. 15 Ba wani

babban abin mamaki ba ne idan bayin sa sun badda
kamanninsu don a dauka bayin adalci ne su. Karshen
su zai zama sakamakon abin da suka aikata. 16 Ina
kara fadi: Kada wani ya yi zaton ni wawa ne. Idan kun
yi zaton hakan, to ku dauke ni kamar wawan don inyi
fahariya kadan. 17 Abinda nake fadi game da wannan
gabagadi mai fahariya ba bisa ga amincewar Ubangiji
ba ne, amma ina magana a matsayin wawa. 18 Tun da
mutane dayawa suna fahariya bisa ga jiki, ni ma zan
yi fahariya. 19 Gama kuna murnar tarayya da wawaye.
Ku masu hikima ne! 20 Kuma kuna hakuri da wanda
zai bautar da ku, idan ya tauye ku, yana amfani da
ku don ribar kansa, idan ya dauki kansa fiye da ku,
ko ya mammare ku a fuska. 21 Ina mai cewa mun
kunyata da muka rasa gabagadin yi maku haka. Duk
da haka idan wani zai yi fahariya-Ina magana kamar
wawa-Ni ma zan yi fahariya. 22 Su yahudawa ne? Ni
ma haka. Su Isra'ilawa ne? Nima haka. Su zuriyar
Ibrahim ne? Nima haka. 23 Su bayin Almasihu ne?
(Ina magana kamar ba ni cikin hankalina) na fi su ma.
Na ma yi aiki tukuru fiye da su duka, shiga kurkuku
fiye da kowa, a shan duka babu misali, a fuskantar
haduran mutuwa da yawa. 24 Daga hannun yahudawa
sau biyar na sha bulala ''Arba'in ba daya''. 25 Sau uku
na sha dibga da sanduna. Sau daya aka jejjefe ni da
duwatsu. Sau uku na yi hadari a jirgin ruwa. Na yi
tsawon dare da yini guda a tsakiyar teku. 26 Ina shan
tafiye tafiye, cikin hadarin koguna, cikin hadarin 'yan
fashi, cikin hadari daga mutane na, cikin hadari daga
al'ummai, cikin hadarin birni, cikin hadarin jeji, cikin
hadarin teku, cikin hadarin 'yan'uwan karya. 27 Na
sami kaina ina aiki tukuru cikin mawuyacin hali, cikin
yin dare dayawa ba barci, cikin yunwa da kishin ruwa,
cikin yawan azumi, cikin sanyi da tsiraici. 28 Baya ga
wadannan duka, akwai nauyi a kaina kullayaumin
saboda damuwata akan Ikkilisiyoyi duka. 29 Waye
kumama, wanda ban zama kumama akan shi ba?
Wanene aka sa yayi tuntube, kuma ban kuna ba? 30
Idan zan yi fahariya, zan yi fahariya akan abinda ke
nuna kasawata. 31 Allah kuma Uba na Ubangijinmu
Yesu, wanda ya isa yabo har abada, ya san ba karya
nake yi ba! (aiōn g165) 32 A Damasku, gwamnan da ke
mulki karkashin sarki Aritas yasa aka yi tsaron birnin
Damasku domin a kama ni. 33 Amma ta taga cikin
kwando aka ziraro ni bayan ganuwar birni, na kuwa
kucce daga hannunsa.

12 Dole ne in yi fahariya, ko dashike bata da ribar
komai. Amma zan ci gaba da wahayoyi da ruyoyi
daga Ubangiji. 2 Na san wani mutum cikin Almasihu,
wanda shekaru goma sha hudu da suka wuce-ko a
cikin jiki ne ko ba a jiki ba, ban sani ba, Allah ya
sani-an dauke shi zuwa sama ta uku. 3 Kuma na san
wannan mutumin-ko cikin jiki ko kuma ba cikin jiki
ba, ban sani ba, Allah ya sani- 4 an dauke shi zuwa
Firdausi ya kuma ji madaukakan al'amura wadanda ba
mai iya fadi. 5 A madadin irin wannan mutumin zan
yi fahariya. Amma a madadin kaina ba zan yi fahariya
ba, sai dai game da kumamancina. 6 Idan ina so inyi
takama, ba zai zama wauta ba, domin gaskiya zan rika
fada. Amma zan guje wa fahariya, domin kada wani
ya dauke ni fiye da abinda ya gani ko ya ji daga gare
ni. 7 Zan kuma gujewa fahariya saboda irin wadannan
gagaruman ruyoyi. Domin kada in cika da girman
kai, an ba ni kaya cikin jikina, manzon shaidan ya
wahalshe ni, domin kada in yi girman kai dayawa. 8
Na roki Ubangiji har sau uku domin ya kawar mini
da wannan. 9 Amma ya ce mani, “Alherina isasshe
yake a gare ka, domin ta wurin kumamanci karfi
yake cika.” Don haka zan gwammace takama a akan
kasawata, domin ikon Almasihu ya zauna a ciki na.
10 Sabili da haka a gamshe nake ta dalilin Almasihu,
cikin kumamanci, ko raini, ko matsaloli, ko jarabobi,
ko kuma nawaya. Don ko dayaushe na raunana, ina
da karfi kuma. 11 Na zama wawa! Amma ku ne kuka
tilasta mani haka, ya kamata ku yabe ni, domin ban
kasa ga wadan da ake kira manyan manzanni ba, ko da
shike ni ba komai ba ne. 12 Cikakkun alamun mazanni
sun faru a tsakanin ku, da cikakken hakuri, alamu
da abubuwan ban mamaki da manyan ayyuka. 13 Ta
yaya kuka zama da rashin muhimmanci akan sauran
Ikkilisiyoyin, sai dai don ban zama matsala a gare
ku ba? Ku gafarce ni a kan wannan laifin. 14 Duba!
A shirye nake domin in zo gare ku karo na uku. Ba
zan so in zamar maku nawaya ba, domin ba kayanku
nake so ba. Amma ku nake so. Domin ba 'ya'ya ne
ya kamata su yi wa iyaye tanadi ba. Amma iyaye ne
ya kamata su yi wa 'ya'ya tanadi. 15 Zan yi murnar
biyan bukatunku, ko ya kai ga in bada rai na. Idan
ni na kaunace ku, sosai, sai ni za a kaunata kadan?
16 Amma kamar yadda yake, ban nawaita maku ba.
Amma, da shike ni mai dabara ne, Ni ne na kama ku
da yaudara. 17 Ko na cutar da ku ta wurin wadanda na
turo maku? 18 Rokar Titus na yi domin ya zo gare ku,

sa'an nan na turo shi da wani dan'uwa. Ko da na turo
Titus, ya cutar da ku ne, ba cikin hanya daya muka yi
tafiya ba? Ba a sawu daya muka yi tafiya ba? 19 Kuna
tsammanin a dukan wannan lokaci muna kare kan
mu a gaban ku ne? A gaban Allah, a cikin Almasihu
muke fadin komai domin ku sami karfi. 20 Ina tsoro
domin idan na zo ba zan same ku yadda nake zato ba.
Ina tsoro kuma ba za ku same ni kamar yadda ku ke
zato ba. Ina tsoron cewa za a sami gardandami, kishi,
barkewar fushi, buri na son kai, gulma, girman kai da
yamutsi. 21 Ina tsoron cewa bayan na dawo, Allahna
zai iya kaskantar da ni a gaban ku. Ina tsoron cewa
zan yi bakinciki domin mutane dayawa da suka yi
zunubi kafin yanzu, wadanda kuma ba su tuba daga
rashin tsarki da zina da fasikanci da ayyukan sha'awa
da suka aikata ba.

13 Wannan ne karo na uku da nake zuwa gare ku,
''Ana tabbatar da kowanne zargi ta bakin shaidu
biyu ko uku.'' 2 Na riga na yi magana a baya da
wadanda suka yi zunubi da kuma sauran a lokacin da
ina tare da ku karo na biyu, kuma ina sake fadi: Idan
na sake zuwa, ba zan raga masu ba. 3 Ina fadi maku
wannan ne domin kuna neman shaida ko Almasihu
na magana ta bakina. Shi ba kasashshe bane zuwa
gare ku. Maimakon haka, Shi mai iko ne a cikin ku. 4
Domin an gicciye shi cikin kasawa, amma yana da rai
ta ikon Allah. Don mu ma kasassu ne a cikin shi, amma
za mu rayu tare da shi cikin ikon Allah dake cikinku.
5 Ku auna kanku ku gani ko kuna cikin bangaskiya. Ku
yi wa kanku gwaji. Ba ku lura da cewa Yesu Almasihu
yana cikin ku ba? Yana cikin ku, sai dai in ba a amince
da ku ba. 6 Gama ina da gabagadin cewa za ku iske an
amince da mu. 7 Ina addu'a ga Allah cewa ba za a same
ku da laifi ba. Ba wai ina rokon mu bayyana kamar
mun ci gwadawar ba. Maimakon haka, ina addu'a ku
yi abinda ke dai dai, ko dayake mun yi kamar mun
fadi gwadawar. 8 Domin bamu iya yin wani abu na
tsayayya da gaskiya ba, sai dai mu yi domin gaskiya. 9
Muna farin ciki idan mun kasa ku kuma kun yi karfi.
Muna addu'a kuma domin ku kammalu. 10 Na rubuta
wadannan abubuwa yayinda ba ni tare da ku, saboda
yayin da zan kasance da ku ba zan zamar maku mai
fada ba. Ba na so inyi amfani da ikon da Ubangiji ya
bani in tsattsaga ku, sai dai in gina ku. 11 A karshe,
'yan'uwa, ku yi farinciki, ku yi aiki don sabuntuwa,
ku karfafa, ku yarda da juna, ku zauna cikin salama.
Kuma Allahn kauna da salama zai kasance tare da ku.
12 Ku gai da juna da tsattsarkar sumba. 13 Masu bi
duka suna gaishe ku. 14 Bari alherin Ubangiji Yesu
Almasihu, da kaunar Allah, da zumuntar Ruhu Mai
Tsarki su kasance tare da ku duka.

# Galatiyawa

1 Wannan Bulus manzo ne. Manzancina kuwa, bai zo
daga mutane ba ko mutum, amma ta wurin Yesu
Almasihu da Allah Uba wanda da ya tashe shi daga
matattu. 2 Ni da dukan 'yan'uwa da nake tare da su a
nan, ina rubuto maku ku iklisiyoyi da ke a Galatiya. 3
Alheri zuwa gare ku da salama daga Allah Ubanmu da
kuma Ubangjinmu Yesu Almasihu, 4 wanda ya ba da
kansa domin zunubanmu saboda ya kubutar da mu
daga wannan mugun zamani, bisa ga nufin Allah da
Ubanmu. (aiōn g165) 5 Daukaka ta tabbata a gare shi
har abada abadin. (aiōn g165) 6 Na yi mamaki kwarai
yadda kuka juya da sauri zuwa wata bishara daban.
Na yi mamakin cewa kuna juyawa daga shi wanda ya
kira ku ta wurin alherin Almasihu. 7 Ba wata bishara,
amma akwai wadansu mutane da suke kawo maku
rudani kuma suna so su gurbata bisharar Almasihu. 8
Amma, ko da mu ne ko mala'ika daga sama ya yi maku
shelar wata bishara ta daban da wadda muka yi shelar
ta, la'ananne ne. 9 Kamar yadda muka fadi maku a
da, yanzu kuma ina sake fada, “Idan wani ya yi maku
shelar wata bishara ta daban da wadda kuka karba,
la'ananne ne.” 10 To yanzu ina neman shaidar mutane
ne ko Allah? Ina neman in gamshi mutane ne? Idan
har yanzu ina kokarin in gamshi mutane ne, ni ba
bawan Almasihu ba ne. 11 Ina son ku sani fa 'yan'uwa,
cewa bisharar da nake shelar ta ba daga mutane take
ba. 12 Ban karbe ta daga mutum ba, ba ma wanda ya
koyar mani A maimakon haka, ta wurin wahayin Yesu
Almasihu ne zuwa gare ni. 13 Kun riga kun ji game da
rayuwa ta a da cikin Yahudanci, yadda da nake da
kwazon tsananta wa iklisiyar Allah fiye da misali kuma
ina lalatar da ita. 14 Ina gaba-gaba cikin Yahudanci
fiye da yawancin tsararrakina. A kwazo kuwa fiye da
kima game da al'adun ubannina. 15 Amma ya gamshi
Allah ya zabe ni daga cikin mahaifiyata. Ya kira ni
ta wurin alherinsa. 16 Ya bayyana dansa a gareni,
saboda in yi shelar sa cikin al'ummai. Nan da nan,
ban nemi shawarar nama da jini ba 17 kuma ban tafi
Urushalima ba wurin wadanda suka zama manzanni
kafin ni. Maimakon haka sai na tafi Arebiya, daga
nan sai na dawo Dimashku. 18 Bayan shekara uku
na je Urushalima don in san Kefas, na zauna da shi
na kwana goma sha biyar. 19 Amma ban ga ko daya
daga cikin manzannin ba sai Yakubu kadai, dan'uwan
Ubangiji. 20 Duba, a gaban Allah, ba karya nake yi ba
cikin abin da na rubuta maku. 21 Daga nan sai na je
lardin Suriya da Kilikiya. 22 Har a lokacin babu wanda
ya san ni a fuska a iklisiyoyin Yahudiya da suke cikin
Almasihu, 23 amma sai labari kawai suke ji, “Wanda a
da yake tsananta mana yanzu yana shelar bangaskiyar
da a da yake rusarwa.” 24 Suna ta daukaka Allah
saboda ni.

2 Daga nan, bayan shekara goma sha hudu na koma
Urushalima tare da Barnaba. Na kuma dauki Titus
tare da ni. 2 Na koma ne domin Allah ya nuna mani in
koma. Sai na gabatar masu shelar bisharan da nake
yi a cikin al'ummai. (Amma a kebe na yi magana da
wadanda aka dauka muhimman shugabanni). Na yi
haka ne domin in tabbatar da cewa ba gudun banza
nake yi ba, ko kuma na yi gudun banza. 3 Amma
ko Titus wanda yake tare da ni, Baheline, ba wanda
ya tilasta masa ya yi kaciya. 4 Wannan maganar ta
taso ne daga 'yan'uwan karya da suka zo cikinmu a
boye su ga 'yancin mu a cikin Yesu Almsihu. Sun yi
marmarin su maishe mu bayi ga doka. 5 Ba mu mika
kanmu biyayya gare su ba ko da na sa'a daya, domin
gaskiyar bishara ta kasance babu canzawa domin ku.
6 Amma su wadanda a ke ganin su da muhimmanci ba
su taimaka mani da komai ba. Ko su wanene su bai
dame ni ba. Allah ba ya karbar wanda mutane suka fi
so. 7 Maimakon haka, suka ga an danka mani shelar
bishara ga wadanda ba su da kaciya. Kamar yadda aka
ba Bitrus shelar bishara ga masu kaciya. 8 Gama Allah
wanda yake yin aiki a cikin Bitrus domin manzanci
zuwa ga masu kaciya, haka kuma yake aiki ciki na
zuwa ga al'ummai. 9 Da Yakubu, Kefas, da Yahaya,
wadanda a ke gani masu gina ikilisiya, suka fahimci
alherin da aka ba ni, suka bamu hannun dama na
zumunci ni da Barnaba, Sun yi haka ne kawai domin
mu mu tafi zuwa wurin al'ummai, su kuma su je wurin
masu kaciya. 10 Suna kuma so mu tuna da matalauta.
Ni ma ina da aniyar yin haka. 11 Da Kefas ya kai
Antakiya, na yi tsayayya da shi a gabansa domin shine
ke da kuskure. 12 Da ma Kefas yana cin abinci tare
da al'ummai kafin zuwan wasu mutane daga wurin
Yakubu. Amma da wadannan mutane suka iso, sai ya
dena kuma ya ware kansa daga al'umman. Yana jin
tsoron wadannan mutanen da ke bukatar kaciya. 13
Hakannan ma sauran Yahudawa da suke tare da shi
sun bi munafurcin sa. A sakamakon haka Barnaba ma
ya bi munafurcin su. 14 Da na ga basu bin gaskiyar da

take cikin bisharar, na gaya wa Kefas a gaban su duka,
"Idan kai Bayahude ne kana rayuwar ka ta al'ummai a
maimakon rayuwar Yahudawa, to ta yaya za ka tilasta
wa al'ummai su yi zaman Yahudawa? " 15 Mu da
muke Yahudawa daga haihuwa, ba ''Al'ummai masu
zunubi ba.'' 16 Ku sani fa, babu wanda za a baratar ta
ayyukan shari'a. A maimakon haka an baratar da su
ta wurin bangaskiya cikin Yesu Almasihu. Mun zo
ga cikin Almasihu Yesu domin mu samu baratarwa
ta bangaskiya cikin Almasihu, kuma ba ta ayyukan
shari'a ba. Domin ta ayyukan shari'a babu wanda
zai samu baratarwa. 17 Amma idan mun nemi Allah
ya baratar da mu cikin Almasihu, mun samu kanmu
masu zunubi kenan, Almasihu ya zama bawan zunubi
ne? Ko kadan! 18 Idan na sake gina dogara ta a kan
shari'a, dogarar da na juya wa baya, na nuna kai na
mai karya shari'a kenan. 19 Ta wurin shari'a na mutu
ga shari'a, domin in yi rayuwa irin ta Allah. 20 An
giciye ni tare da Almasihu, ba nine ke rayuwa ba
kuma, amma Almasihu ke rayuwa a cikina. Rayuwar
da nake yi a yanzu a cikin jiki, ina yin ta ne, ta wurin
bangaskiya ga dan Allah, wanda ya kaunace ni ya ba
da kansa domina. 21 Ban yi watsi da alherin Allah ba,
domin idan adalci ya wanzu ta wurin shari'a, ashe
Almasihu ya mutu a banza kenan.

3 Ku Galatiyawa marasa wayo! Wanne mugun ido
ya cuce ku? Ashe, ba Yesu Almasihu gicciyayye aka
nuna a gaban idon ku ba? 2 Ina so in gane wannan
daga wurin ku ne kawai. Kun karbi Ruhun ta wurin
ayyukan doka ne ko ta wurin ba da gaskiya ga abin
da kuka ji? 3 Rashin wayonku ya yi yawa haka ne?
Kun fara da Ruhu, sai kuma yanzu ku karasa a cikin
jiki? 4 Kun fuskanci abubuwa da yawa a banza ne -
har idan a banza ne? 5 To, shi wanda ya ba ku Ruhun,
da ayyuka masu iko a tsakanin ku, ya yi ne ta wurin
ayyukan shari'a ko ta wurin ji tare da bangaskiya? 6
Ibrahim ''ya ba da gaskiya ga Allah, kuma an lisafta
mashi wannan a matsayin adalci.'' 7 Ta wannan hanya
ku fahimta su wadanda suka ba da gaskiya, 'ya'yan
Ibrahim ne. 8 Nassi ya riga ya hangi gaba cewa, ta
wurin bangaskiya Allah zai baratar da Al'ummai. An
yi wa Ibrahim shelar bishara tuntuni: ''A cikinka ne
dukan al'ummai za su yi albarka.'' 9 Saboda haka,
wadanda suka ba da gaskiya, masu albarka ne tare da
Ibrahim wanda ke da bangaskiya. 10 La'ana na kan
wadanda sun dangana ga ayyukan shari'a. Gama a
rubuce yake, ''La'ananne ne kowanne mutum da bai
tsaya ga duk abin da ke a rubuce cikin littafin shari'a
ba, ya kuma aikata shi duka."' 11 Yanzu a sarari yake,
Allah ba ya baratar da kowa ta wurin shari'a, domin
''Mai adalci zai rayu ta bangaskiya.'' 12 Doka ba daga
bangaskiya take ba, 'Amma a maimakon haka, "Shi
wanda ke yin wadannan abubuwa cikin shari'a, zai yi
rayuwa ta wurin shari'a.'' 13 Almasihu ya fanshe mu
daga la'anar shari'a da ya zama la'ananne saboda mu.
Kamar yadda yake a rubuce, ''La'ananne ne duk wanda
aka sargafe a bisa itace.'' 14 Dalilin shine, albarkan da
ke bisan Ibrahim ta zo ga al'ummai cikin Almasihu
Yesu, domin mu samu karban alkawarin Ruhu ta
wurin bangaskiya. 15 'Yan'uwa, ina magana bisa ga
ka'idojin mutane. Idan mutane sun yi yarjejeniya,
babu mai kawar da shi ko a kara shi. 16 Yanzu fa,
an fada alkawaran nan ne ga Ibrahim da zuriyarsa.
Bai ce, ''ga zuriya ba'' da manufar masu yawa; amma
a maimakon haka ga daya kadai, ''ga zuriyar ka,''
wanda shine Almasihu. 17 Yanzu na fadi wannan.
Shari'a, wadda ta zo shekaru 430 daga baya, ba ta
kawar da alkawarin da Allah ya tabbatar da shi ba
tun a baya. 18 Domin idan da gadon ya zo ta dalilin
shari'a ne, da ba za ya zo kuma ta dalilin alkawari ba.
Amma Allah ya ba da shi ga Ibrahim kyauta ta wurin
alkawari. 19 Me ya sa kenan aka ba da shari'a? An
kara ta ne saboda laifuffuka, har sai zuriyar Ibrahim
din nan ta zo ga wadanda aka yi masu alkawarinta.
An kaddamar da ikon shari'ar ta wurin mala'iku, ta
hannun matsakaici. 20 Yanzu dai matsakanci yana
nufin mutum fiye da daya, duk da haka Allah daya ne.
21 Shari'a tana tsayayya da alkawaran Allah kenan? Ko
kadan! Domin idan da an ba da shari'a da ke iya bayar
da rai, babu shakka da adalci ya zo ta wurin wannan
shari'a. 22 A maimakon haka, nassi ya kulle abubuwa
duka a karkashin zunubi. Allah ya yi wannan domin
alkawarin sa na ceton mu ta wurin bangaskiya cikin
Yesu Almasihu ya samu a ba da shi ga wadanda suka
gaskanta. 23 Amma kafin bangaskiya cikin Almasihu
ta zo, an kulle mu kuma aka tsare mu da shari'a har
zuwa ga wahayin bangaskiya. 24 Daga nan shari'a
ta zama mana jagora har sai da Almasihu ya zo,
domin mu samu baratarwa ta wurin bangaskiya. 25
Yanzu da bangaskiya ta zo, ba mu kuma a karkashin
jagora. 26 Domin dukanku 'ya'yan Allah ne ta wurin
bangaskiya cikin Almasihu Yesu. 27 Dukanku da aka yi
wa baftisma cikin Almasihu, kun suturce kanku da

Almasihu. 28 Babu Bayahude ko Baheline, bawa ko
'yantacce, babu na miji ko mace, domin dukanku daya
ne cikin Almasihu Yesu. 29 Idan ku na Almasihu ne, ku
zuriyar Ibrahim ne kenan, magada bisa ga alkawarin.

**4** Ina cewa muddin magaji yaro ne, babu bambancin
sa da bawa, ko da yake shine mai mallakan dukan
kadarorin. 2 A maimakon haka, yana karkashin masu
jagora da amintattu har sai lokacin da mahaifinsa
ya ajiye. 3 Hakannan mu ma, lokaci da muke yara,
an rike mu cikin kangi na tushin ka'idojin wannan
duniya. 4 Amma da lokacin ya yi daidai, Allah ya
aiko da dansa, haihuwar mace, haihuwar karkashin
shari'a. 5 Ya yi haka ne domin ya fanshi wadanda ke a
karkashin shari'a, domin mu karbi diyanci a matsayin
'ya'ya. 6 Domin ku 'ya'ya ne, Allah ya aiko da Ruhun
Dansa cikin zuciyarmu, Ruhun wanda ke kirar, “Abba,
Uba.” 7 Saboda wannan dalilin kai ba kuma bawa
ba ne amma da. Idan kai da ne, hakannan kuma kai
ma magaji ne ta wurin Allah. 8 Duk da haka a da,
da ba ku san Allah ba, bayi ne ku ga alloli wadanda
ainihi ba alloli ba ne ko kadan. 9 Amma yanzu da
kuka san Allah, ko kuma, yanzu da Allah ya san ku,
me ya sa kuke sake komawa zuwa ga tushen ka'idodin
nan mara karfi da amfani? Kuna so ku sake komawa
zaman bayi kuma daga farko? 10 Kuna kiyaye ranaku
na musamman, sabobin watanni, lokatai, da shekaru.
11 Ina ji maku tsoro. Ina tsoro cewa kamar na yi aiki
cikinku a wofi. 12 Ina rokon ku 'yan'uwa, ku zama
kamar yadda nake, domin ni ma na zama kamar ku.
Ba ku yi mani laifin komai ba. 13 Amma kun sani cewa
saboda rashin lafiya ne na yi maku shelar bishara da
farko. 14 Ko da yake halin da nake ciki cikin jiki a
zahiri ya sa ku cikin gwaji, ba ku raina ni ba ko kuma
kuka watsar da ni. A maimakon haka, kun karbe ni
kamar mala'ikan Allah, kamar ni Almasihu Yesu ne da
kansa. 15 Saboda haka, yanzu ina murnar taku? Domin
ina shaidar ku, idan mai yiwuwa ne, da kun kwakulo
idanunku, kun ba ni. 16 To kenan, na zama makiyin
ku ne saboda na gaya maku gaskiya? 17 Suna neman
ku da himma ba domin wani alheri ba ne. Suna so
su raba ni da ku domin ku bi su. 18 Yana da kyau ko
yaushe a yi himma domin dalilai masu kyau, ba kuma
kawai sa'adda ina tare da ku ba. 19 'Ya'yana kanana,
sabili da ku ina cikin zafin nakuda kuma sai Almasihu
ya samu kafuwa cikinku. 20 Da ma a ce ina tare da ku
yanzu in canza muryata, domin ina damuwa a kanku
kwarai. 21 Ku gaya mani, ku da kuke marmarin ku zo
karkashin shari'a, ba ku ji abin da shari'ar ta ce ba?
22 A rubuce yake cewa, Ibrahim yana da 'ya'ya maza
biyu, daya dan baiwa ne, dayan kuma dan 'yantaciyar
mace ne. 23 Abin lura anan, dan baiwar an haife
shi ta hanyar mutuntaka ne, amma dan 'yantaciyar
macen, an haife shi ta wurin alkawari ne. 24 Ana iya
bayyana abubuwan nan a hanyar kwatanci kamar
haka, wadannan mata na kama da alkawarai ne guda
biyu. Dayan alkawarin daga dutsen Sinayi ne. Ta haifi
'ya'ya da ke bayi ne su. Ita ce Hajaratu. 25 Yanzu fa,
Hajaratu ita ce dutsen Sinayi da ke Arebiya. Misali
ce na Urushalima na yanzu, domin tana cikin bauta
tare da 'ya'yanta. 26 Amma Urushalima da ke bisa
'yantacciya ce, ita ce mahaifiyarmu. 27 Kamar yadda
yake a rubuce, “Ki yi murna, ke bakarariya, ke da ba ki
taba haihuwa ba. Ki yi shewa na farinciki, ke da ba ki
dandana haihuwan da ba. Domin 'ya'yan bakarariya
da yawa suke, fiye da ta mace mai miji.” 28 Yanzu
fa, 'yan'uwa, kamar yadda Ishaku yake, haka muke,
wato 'ya'yan alkawari. 29 A lokacin can, shi wanda
aka haife shi ta hanyar mutuntaka ya tsananta wa
wanda aka haife shi ta hanyar Ruhu. Haka yake har
yanzu. 30 Amma menene nassi ya ce? “Ka kori baiwar
nan tare da danta. Domin dan baiwar nan ba za ya ci
gado tare da dan macen nan da ke 'yantacciya ba.” 31
Saboda haka 'yan'uwa, mu ba 'ya'yan baiwa ba ne,
a maimakon haka, mu 'ya'yan macen nan ne da ke
'yantacciya.

**5** Saboda 'yanci ne Almasihu ya yantar da mu. Sai ku
dage kada ku sake komawa cikin kangin bauta. 2
Duba, ni Bulus, ina gaya maku cewa idan an yi maku
kaciya, Almasihu ba zai zama da amfani a gare ku
ba a kowace hanya. 3 Haka kuma, na shaida ga ko
wanda mutum wadda aka yi masa kaciya ya zama
dole ya yi biyayya da dukan shari'a. 4 Kun rabu da
Almasihu, dukanku wadanda aka “baratar” ta wurin
shari'a. Kun fadi daga alheri. 5 Domin ta wurin Ruhu,
cikin bangaskiya, muna jira gabagadi na adalci. 6
A cikin Almasihu kaciya ko rashin kaciya ba shi da
ma'ana. Bangaskiya kadai mai aiki ta wurin kauna
ita ce mafi muhimmanci. 7 Da kuna tsere da kyau,
wanene ya tsayar da ku daga yin biyayya da gaskiya?
8 Rinjayarwa da ke sa yin wannan, ba daga wanda ya
kira ku ba ne 9 Ai karamin yisti shi yake sa dukan kulli
ya kumbura. 10 Ina da wannan gabagadin game da ku

cikin Ubangiji cewa ba za ku yi tunani a wata hanya
daban ba. Shi wanda ya rikita ku zai sha hukunci
ko wanene shi. 11 'Yan'uwa, idan har yanzu wa'azin
kaciya nake yi, don me har yanzu ake tsananta mani?
Inda haka ne dutsen sanadin tuntube game da gicciye
da ya ragargaje. 12 Ina fata wadanda suke badda ku
su maida kansu babani. 13 'Yan'uwa, domin Allah
ya kira ku zuwa ga yanci, kada dai ku mori yancin
nan ya zama zarafi domin jiki. A maimakon haka
ta wurin kauna ku yi wa juna hidima. 14 Saboda
dukan shari'a ta cika ne a cikin doka guda daya; "Ka
kaunaci makwabcinka kamar kanka." 15 Amma idan
kuna cizo da hadiye juna, ku lura kada ku hallakar
da junanku. 16 Na ce, ku yi tafiya cikin Ruhu, ba za
ku cika sha'awoyin jiki ba. 17 Domin jiki yana gaba
mai karfi da Ruhu, Ruhu kuma yana gaba da jiki.
Domin wadannan akasin juna suke. Sakamakon shine
ba za ku iya yin abin da kuke so ba. 18 Amma idan
Ruhu ne ke bishe ku, ba ku karkashin shari'a. 19
Yanzu ayyukan jiki a bayyane suke. Sune al'amuran
lalata, rashin tsarki, sha'awoyi, 20 bautar gumaka,
sihiri, yawan fada, jayayya, kishi, zafin fushi, gasa,
tsattsaguwa, hamayya, 21 hassada, buguwa, buguwa
da tarzoma, da dai sauran irin wadannan abubuwa.
Na gargade ku, kamar yadda a da na gargade ku, cewa
wadanda suke aikata wadannan abubuwa ba za su gaji
mulkin Allah ba. 22 Amma 'ya'yan Ruhu kauna ne,
farinciki, salama, hakuri, kirki, nagarta, bangaskiya,
23 tawali'u, da kamun kai. Babu wata shari'a da ke
gaba da wadannan abubuwa. 24 Wadanda suke na
Almasihu Yesu sun giciye halin jiki tare da marmarin
sa da miyagun sha'awoyi. 25 Idan muna zaune cikin
Ruhu, mu yi tafiya da Ruhu. 26 Kada mu zama masu
girman kai, ko muna cakunar juna, ko muna kishin
juna.

6 'Yan'uwa, idan an kama mutum yana yin wani laifi,
ku da kuke da ruhaniya sai ku dawo da mutumin a
hanya cikin ruhun tawali'u, ka lura da kanka don kada
kai ma ka fada a cikin gwaji. 2 Ku dauki damuwar juna,
ta yin haka za ku cika shari'ar Almasihu. 3 Domin
idan kowa ya zacci shi wani abu ne alhali shi ba komai
ba ne rudin kansa yake yi. 4 Sai kowa ya auna aikin
sa. Sa'annan zai sami abin da zai yi takama, ba sai ya
kwatanta kansa da wani ba. 5 Domin kowa zai dauki
nauyin kayansa. 6 Wanda aka koya masa maganar,
wajibi ne ya ci amfanin abubuwansa masu kyau duka
tare da malaminsa. 7 Kada fa a yaudare ku ba a yi wa
Allah ba'a. Dukan abin da mutum ya dasa, shine abin
da zai girba. 8 Domin shi wanda ya shuka wa kansa
dabi'ar zunubi zai girbi hallaka, amma shi wanda
ya shuka cikin Ruhu, zai girbi rai madawwami daga
Ruhu. (aiōnios g166) 9 Kada mu gaji da aikata nagarta,
domin a lokacin da ya dace za mu yi girbi idan ba mu
gaji ba. 10 Saboda haka, lokacin da muke da zarafi, sai
mu yi nagarta ga kowa. Mu yi nagarta mussamman ga
wadanda suke na iyalin bangaskiya. 11 Dubi yawan
wasikun da na rubuta maku da hannuna. 12 Wadanda
suke so su nuna hali mai kyau cikin jiki suke tilasta
ku yin kaciya. Suna yin haka ne kadai saboda kada a
tsananta masu saboda gicciyen Almasihu. 13 Domin
ko su wadanda suke masu kaciya ba su kiyaye shari'a.
Maimakon haka suna so ne a yi maku kaciya don
su yi fahariya game jikinku. 14 Bari kada ya zama
ina fahariya sai dai ta gicciyen Ubangijinmu Yesu
Almasihu. Ta wurinsa ne aka gicciye duniya a gare
ni, ni kuma ga duniya. 15 Domin kaciya ko rashin
kaciya ba komai ba ne. Maimakon haka, sabon halita
ne ke da muhimmanci. 16 Ga dukan wadanda za su
zauna cikin wannan ka'ida, bari salama da jinkai su
kasance tare da su da kuma bisa Isra'ila na Allah. 17
Daga yanzu zuwa nan gaba kada wani ya dame ni,
domin ina dauke da tabbai na Yesu a jikina. 18 Alherin
Ubangijinmu Yesu Almasihu ya kasance da ruhun ku,
'yan'uwa. Amin.

# Afisawa

1 Bulus, manzon Yesu Almasihu ta wurin nufin Allah,
zuwa ga kebabbu na Allah da ke a Afisa wanda suke
aminci cikin Yesu. 2 Bari alheri ya kasance da ku, da
salama daga wurin Allah Ubanmu da Ubangijinmu
Yesu Almasihu. 3 Yabo ya tabbata ga Allah Uban
Ubangijinmu Yesu Almasihu. Shine ya albarkace mu
da kowanne albarku na ruhaniya da ke cikin sammai
cikin Almasihu. 4 Kafin halitar duniya, Allah ya zabe
mu da muka ba da gaskiya cikin Yesu. Ya zabe mu
domin mu yi zaman tsarki da rayuwar da babu aibu a
gabansa. 5 Cikin kauna Allah ya kaddara ya dauke
mu mu zama yayansa ta wurin Yesu almasihu. Ya
yi wannan domin ya gamshe shi ya yi abin da ya ke
so. 6 Sakamakon shine Allah ya karbi yabo domin
daukakan alherinsa. Wannan shine abinda ya ba mu
hannu sake ta wurin kaunataccensa. 7 Gama cikin
kaunataccensa aka fanshe mu ta wurin jininsa, da
gafarar zunubai ta wurin wadataccen alherinsa. 8
Ya ba da wannan alherin a yalwace cikin dukan
hikima da fahimta. 9 Allah ya bayyana mana gaskiyar
al'amarin da aka boye na shirinsa, ta wurin abin
da yake so ya nuna cikin Almasihu. 10 Idan lokaci
ya yi na kammala shirinsa, Allah zai kawo dukan
abubuwan da ke sama da kasa cikin Yesu. 11 An zabe
mu cikin Almasihu mu zama abin gado na Allah. Ya
yi mana wannan shirin tun da cikin shirin sa, shi
mai yin dukan abu ta dalilin nufinsa. 12 Allah ya
yi haka saboda mu rayu domin yabon daukakarsa.
Mune na farko da muka sami bege cikin Almasihu. 13
A cikin Almasihu ne kuma kuka samu jin maganar
gaskiya, bisharan cetonku ta wurin Yesu. A cikinsa
ne kuka bada gaskiya aka hatimce ku da Ruhu Mai
Tsarki wanda aka alkawarta. 14 Ruhun shine tabbacin
gadonmu kafin mu kai ga samunsa. Wannan don
yabon daukakarsa ne. 15 Sabo da haka, tun lokacin da
na ji labarin bangaskiyarku cikin Ubangiji Yesu da
kaunar ku zuwa dukan wadanda aka kebe dominsa. 16
Ban fasa tunawa da ku ba ina addu'a saboda ku cikin
addu'o'ina. 17 Ina addu'a da cewa Allah Ubangijinmu
Yesu Almasihu, Uban daraja, ya ba ku ruhun basira
da wahayin saninsa. 18 Ina addu'a idanun zuciyarku
su bude domin ku san tabacin kiranku. Ina addu'a
dominku san arzikin mulkin gadonsa cikin wadanda
aka kebe dominsa. 19 Ina addu'a ku san ikon nan nasa
mai girma mara iyaka da ke cikin mu da muka ba da
gaskiya. Wannan girman yana ta wurin aikin karfin
ikonsa ne. 20 Wannan shine ikon da ya yi aiki cikin
Almasihu lokacin da Allah ya tashe shi daga matattu
ya sa shi a hannun damansa cikin sammai. 21 Ya sanya
shi bisa birbishin dukan sarauta, iko, mulki, karfi, da
kowanne irin suna. Ya sanya Almasihu ba a wannan
zamanin kadai ba, amma da zamani mai zuwa. (aiōn
g165) 22 Allah ya saka dukan abubuwa a karkashin
kafafun Almasihu. Ya sa shi shugaban dukan abubuwa
a cikin ikilisiya. 23 Ikilisiya jikinsa ne, cikarsa wanda
ya cika dukan abubuwa cikin kowacce hanya.

2 Amma da ku matattu ne cikin zunubanku da
laifofinku. 2 A cikinsu kuka yi rayuwa bisa ga
al'amuran duniyan nan. Kuka biye wa mai sarautar
ikokin sararin sama, wannan ruhun ne da ke aiki cikin
kangararrun 'ya'ya. (aiōn g165) 3 Da can dukanmu muna
cikin wadannan marasa bada gaskiya. Muka biye wa
mugun burin jikinmu. Muna aikata halin mutuntaka
da na tunaninmu. Bisa ga dabi'a 'ya'ya ne wadanda
sun cancanci fushin Allah, kamar wadansu. 4 Amma
Allah mai yalwar jinkai ne, sabili da matukar kauna
da ya kaunace mu. 5 Sa'anda muke matattu cikin
zunubai, ya kawo mu cikin sabon rai tare da Almasihu.
Ta wurin alheri aka cece mu. 6 Allah ya tashe mu tare
ya kuma sa muka zauna tare a matsayi guda cikin
Almasihu Yesu. 7 Ya yi wannan domin a zamanai
masu zuwa ya nuna mana matukar yalwar arzikin
alherinsa ta wurin Yesu. Yana nuna mana wannan ta
wurin alherinsa. (aiōn g165) 8 Domin ta wurin alheri aka
cece ku ta wurin bangaskiya, wannan ba daga gare ku
ba ne, kyauta ce ta Allah. 9 Ba daga ayyuka ba, Saboda
wannan dalili kada kowa ya yi fahariya. 10 Gama mu
aikin hannuwansa ne, halitattu cikin Almasihu Yesu
domin mu yi kyawawan ayyuka, wadanda tun da Allah
ya tanada, mu yi rayuwa a cikinsu. 11 Saboda haka ku
tuna da ku al'ummai ne a dabi'ar jiki. Ana kiranku
"marasa kaciya", abin da ake kira kaciya cikin jiki
wadda hannayen mutane ke yi. 12 Gama a lokacin
nan a rabe kuke da Almasihu. Ku bare ne ga mutanen
Isra'ila. Ku baki ne ga wa'adodi na al'kawarai. Ba ku
da tabbaci a kan gobe. Ba ku da Allah a cikin duniya.
13 Amma yanzu a cikin Almasihu Yesu ku da da kuke
nesa da Allah, an kawo ku kusa da shi ta wurin jinin
Almasihu. 14 Gama shine salamar mu. Domin ya mai
da biyun daya. Cikin jikinsa ne ya rushe katangar gaba
da ta raba mu da juna. 15 Wato ya kawar da shari'a

mai umarnai da sharudda, domin ya halitta sabon
mutum daya a cikinsa. Yin haka ya kawo salama. 16
Ya yi haka domin ya sulhunta mutum biyu cikin jiki
daya ga Allah ta wurin gicciye. Ta wurin gicciye ya
kashe gabar da ke tsakaninsu. 17 Yesu ya zo ya yi
maku shelar salama ku da kuke nesa da ku na kusa. 18
Domin ta wurin Yesu dukanmu biyu cikin Ruhu daya
muna da hanya zuwa wurin Uba. 19 Sabo da haka
yanzu ku al'ummai, ko daya, ba bare ba ne. Maimakon
haka ku abokai ne tare da kebabbun Allah, abokan
aiki. 20 Wadanda an gina su bisa tushen manzanni da
annabawa. Almasihu Yesu da kansa shine mafificin
dutsen ginin. 21 A cikinsa dukan ginin ya hade tare,
suna kuma girma kamar haikali cikin Ubangiji. 22 A
cikinsa ne kuma ake gina ku gaba daya kun zama
mazaunin Allah a cikin Ruhu.

3 Saboda haka, ni Bulus, dan sarka sabili da Almasihu
dominku al'ummai. 2 Ina zaton kun ji a kan aiki
mai girma na alherin Allah da ya ba ni dominku. 3
Ina rubuto maku bisa ga wahayin da aka sanashe ni.
Wannan ita ce boyayyar gaskiya da na rubuta a takaice
a cikin wata wasikar. 4 Sa'adda kuka karanta a kan
wannan, za ku iya fahimtar basira ta cikin boyayyar
gaskiya a kan Almasihu. 5 Wanda a zamanun da ba a
bayyana wa mutane ba. Amma yanzu an bayyana shi
ga manzanni da annabawa kebabbu a cikin Ruhu. 6
Wannan boyayyar bishara ita ce al'ummai ma abokan
gado ne tare da mu, gabobi ne cikin jiki daya. Abokan
tarayya ne kuma cikin alkawaran Almasihu Yesu ta
wurin bishara. 7 Domin wannan na zama bawa ta
wurin baiwar alherin Allah da ya bani ta wurin karfin
ikonsa. 8 Allah ne ya ba ni wannan baiwa. Ko da
shike nine mafi kankanta cikin kebabbun Allah, in yi
shelar bishara ga al'ummai akan wadatar Almasihu
marar matuka. 9 In kuma fahimtar da dukan mutane
a kan shirin Allah, wannan boyayyar gaskiya wadda
tun zamanai da suka wuce Allah ya boye, shi da ke
mahallicin dukan abubuwa. (aiōn g165) 10 Saboda haka,
ta wurin ikilisiya, masu iko da masu mulkin sararin
sama za su san hikimar Allah ta fuskoki daban daban.
11 Wannan ya kasance bisa ga dawwamammen nufi
da ya zartar cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu. (aiōn
g165) 12 Gama a cikin Almasihu muna da gabagadi, da
dama, da amincewa sabili da gaskiyar mu a cikinsa. 13
Saboda haka ina rokon ku kada ku karaya da wahalar
da na sha domin ku wadda ta zama daukakar ku. 14
Saboda haka nake durkusawa da gwiwa ta a gaban
Uba, 15 wanda ta wurinsa ake kiran kowanne iyali na
sama da na kasa. 16 Ina addu'a ya amince maku bisa
ga yalwar wadatar daukakarsa, ku karfafa matuka
da iko ta wurin Ruhunsa, da yake cikinku. 17 Ina
addu'a Almasihu ya zauna a cikin zuciyar ku ta wurin
bangaskiya. Ina kuma addu'a ku kafu ku kuma ginu
da zurfi kwarai cikin kaunarsa. 18 Ku kasance cikin
kaunarsa domin ku gane, tare da dukan masu bi,
menene zurfi, da fadi, da tsawon kaunar Almasihu. 19
Ina addu'a domin ku san mafificiyar kaunar Almasihu
da ta wuce sani. Ku yi wannan domin a cika ku da
dukan cikar Allah. 20 Yanzu ga wanda yake da ikon
aikata dukan abu fiye da abin da muke roko ko tunani,
bisa ga ikonsa da ke aiki a cikinmu, 21 daukaka ta
tabbata a gare shi a cikin ikilisiya ta wurin Almasihu
Yesu har ya zuwa zamanun zamanai har abada abadin.
Amin. (aiōn g165)

4 Saboda haka a matsayi na na dan sarka saboda
Ubangiji; ina rokon ku ku yi zaman rayuwa da ta
cancanci kiran da Allah ya kiraye ku. 2 Ku zamna da
matukar tawali'u da sahihanci da hakuri. Ku karbi
juna cikin kauna. 3 Ku yi kokarin zaman dayantaka
cikin Ruhu kuna hade cikin salama. 4 Akwai jiki daya
da kuma Ruhu daya, kamar yadda aka kira ku a kan
begen nan daya. 5 Ubangiji daya, bangaskiya daya, da
kuma baftisma daya. 6 Allah daya ne da Uban duka.
Shine bisa duka, ta wurin duka, da kuma cikin duka. 7
Ko wannenmu an ba shi baiwa bisa ga awon baiwar
Almasihu. 8 Kamar yadda nassi ya ce, “Da ya haye
zuwa cikin sama, ya bi da bayi cikin bauta. Ya kuma yi
wa mutane baye baye. 9 Menene ma'anar, “Ya hau?”
Ana cewa kenan ya sauka har cikin zurfin kasa. 10
Shi da ya sauka shine kuma wanda ya hau birbishin
sammai. Ya yi wannan domin ya cika dukan abubuwa.
11 Almasihu ya ba da baye baye kamar haka: manzanni,
annabawa, masu shelar bishara, makiyaya, da masu
koyarwa. 12 Ya yi haka domin ya shiryar da masu bi
saboda hidima, domin gina jikin Almasihu. 13 Ya yi
haka har sai mun kai dayantakar bangaskiya da sanin
Dan Allah. Ya yi haka har sai mun kai ga manyanta,
kamar wadanda suka kai cikakken matsayin nan na
falalar Almasihu. 14 Wannan ya zamanto haka domin
kada mu kara zama kamar yara. Kada a yi ta juya
mu. Wannan haka yake domin kada mu biye wa iskar
kowacce koyarwa ta makirci da wayon mutane masu

hikimar yin karya. 15 Maimakon haka za mu fadi
gaskiya cikin kauna domin mu yi girma cikin dukan
tafarkun da ke na sa, shi da yake shugaba, Almasihu.
16 Almsihu ya hada dukan jikin masu ba da gaskiya.
Jikin yana hade ta wurin kowanne gaba, domin jikin
ya yi girma ya gina kansa cikin kauna. 17 Saboda
haka ina yi maku gargadi cikin Ubangiji cewa, kada
ku sake yin rayuwa irin ta al'ummai da suke yi cikin
azancin wofi marar amfani. 18 Sun duhunta cikin
tunaninsu. Bare suke da rai irin na Allah, ta wurin
jahilcin da ke cikinsu da ta wurin taurare zukatansu.
19 Basa jin kunya. Sun mika kansu ga mutumtaka ta
yin kazamtattun ayyuka da kowacce zari. 20 Amma
ba haka kuka koyi al'amuran Almasihu ba. 21 Ina
zaton kun rigaya kun ji a kansa. Ina zaton an koyar
da ku cikinsa, kamar yadda gaskiyar Yesu ta ke. 22
Dole ku yarda halin ku na da, wato tsohon mutum.
Tsohon mutumin ne ya ke lalacewa ta wurin mugun
buri. 23 Ku yarda tsohon mutum domin a sabonta
ku cikin ruhun lamirinku. 24 Ku yi haka domin ku
yafa sabon mutum, mai kamanin Allah. An hallitta
shi cikin adalci da tsarki da gaskiya. 25 Saboda haka
ku watsar da karya. "Fadi gaskiya ga makwabcin ka",
domin mu gabobin juna ne. 26 "Ku yi fushi, amma
kada ku yi zunubi." Kada ku bari rana ta fadi kuna kan
fushi. 27 Kada ku ba shaidan wata kofa. 28 Duk mai
yin sata, kada ya kara yin sata kuma. Maimakon haka,
ya yi aiki. Ya yi aiki da hannuwan sa domin ya sami
abin da zai taimaka wa gajiyayyu. 29 Kada rubabbun
maganganu su fito daga cikin bakinku. Maimakon
haka, sai ingantattu da za su ba da alheri ga masu
ji. 30 Kada ku bata wa Ruhu Mai Tsarki na Allah rai
domin ta wurin sa ne aka hatimce ku domin ranar
fansa. 31 Sai ku watsar da dukan dacin rai, da hasala,
da fushi, da tankiya, da reni tare da dukan mugunta.
32 Ku yi wa juna kirki, ku zama da taushin zuciya. Ku
yafe wa juna, kamar yadda Allah cikin Almasihu ya
gafarta maku.

**5** Saboda haka ku zama masu koyi da Allah, kamar
kaunatattun 'ya'yansa. 2 Ku yi zama cikin kauna
kamar yadda Almasihu ya kaunace mu, ya kuma mika
kansa sadaka da hadaya ga Allah dominmu, hadaya
mai kanshi abin karba ga Allah. 3 Fasikanci ko kowacce
irin kazamta, ko kazamar lalata kada a ambace su a
tsakaninku, don haka ya dace ga masu bi. 4 Kada a
ambaci batsa, maganar wauta ko alfasha wadanda ba
su dace ba. Maimakon haka, mu zama masu godiya. 5
Domin wannan kun sani cewa ba fasiki, ko mara tsarki,
ko mai hadama wato mai bautar gumaka zai sami gado
cikin mulkin Almasihu da Allah. 6 Kada kowa ya rude
ku da maganganun wofi. Saboda wadannan abubuwa
ne fushin Allah ke zuwa kan kangararrun 'ya'ya. 7
Kada ku yi tarayya tare da su. 8 Domin da ku duhu
ne, amma yanzu ku haske ne cikin Ubangiji. Sai ku yi
tafiya kamar 'ya'yan haske. 9 Saboda amfanin haske
shine dukan alheri, adalci da gaskiya. 10 Kuna bidar
abin da Ubangiji ke murna da shi. 11 Kada ku sa hannu
ga ayyuka marasa amfani da ayyukan duhu amma
gara a tone su. 12 Don abubuwan da suke yi a boye
abin kunya ne a bayyana su. 13 Dukan abu, idan haske
ya bayyana su, za a gan su. 14 Domin duk abin da aka
bayyana ya zama haske. Saboda haka aka ce, "Ka farka,
kai mai barci, ka tashi daga cikin matattu; Almasihu
kuwa zai haskaka bisanka". 15 Saboda haka, ku maida
hankali yadda kuke rayuwar ku, ba kamar mutane
marasa hikima ba amma kamar masu hikima. 16 Ku
yi lura yadda kuke amfani da lokaci don kwanakin
miyagu ne. 17 Kada ku zama wawaye. Maimakon
haka, ku fahimci ko menene nufin Ubangiji. 18 Kuma
Kada ku bugu da ruwan inabi, don yana iya lalata
rayuwa. Maimakon haka, ku cika da Ruhu Mai Tsarki.
19 Kuna magana da junanku cikin zabura da wakoki da
wakokin ruhaniya, kuna rairawa da yabo da zuciyarku
ga Ubangiji. 20 Kullum kuna ba da gaskiya domin
dukan abubuwa cikin sunan Ubangiji Yesu ga Allah
Uba. 21 Kuna sarayadda kanku ga juna cikin girmama
Almasihu. 22 Mata, ku yi biyayya ga mazan ku kamar
ga Ubangiji. 23 Domin miji shine shugaban matarsa
kamar yadda Almasihu yake shugaban ikilisiya. Shine
kuma mai ceton jiki. 24 Amma kamar yadda ikilisiya
take biyayya ga Almasihu, haka kuma dole mata suyi
ga mazajen su cikin kowanne abu. 25 Mazaje, ku
kaunaci matanku kamar yadda Almasihu ya kaunaci
ikilisiya har ya ba da kansa dominta, 26 Ya yi wannan
domin ya tsarkake ta. Ya wanke mu da ruwan wanki
ta wurin kalma. 27 Ya yi wannan domin ya mika ma
kansa ikilisiya mai daraja, ba tare da tabo ko cikas
ko wani abu kamar wadannan, amma ta zama da
tsarki da kuma mara aibi. 28 Hakannan kuma, mazaje
su kaunaci matansu kamar jikunnansu. Wanda yake
kaunar matarsa yana kaunar kansa. 29 Ba wanda
ya taba kin jikinsa. Amma, yakan ciyadda shi yana
kaunarsa, kamar yadda Almasihu ya kaunaci ikilisiya.

30 Domin mu gabobin jikinsa ne. 31 “Domin wannan
mutum zai rabu da ubansa da uwarsa ya manne wa
matarsa, su biyu su zama nama daya”. 32 Wannan
asirin gaskiyar, da girma yake, amma ina magana ne
game da Almasihu da ikilisiyarsa. 33 Duk da haka,
kowannenku dole ya kaunaci matarsa kamar kansa,
matar kuma dole ta girmama mijinta.

6 'Ya'ya, ku yi biyayya ga iyayenku chikin Ubangiji,
domin wannan daidai ne. 2 “Ka girmama mahaifinka
da mahaifiyarka” (Doka ta fari kenan da alkawari), 3
“ta haka za ku yi albarka, domin kwanakinku su yi
tsawo a duniya”. 4 Hakanan, ku ubanni kada ku cakuni
'ya'yan ku har su yi fushi, amma ku goye su cikin
horon Ubangiji da gargadinsa. 5 Bayi, ku yi biyayya ga
iyayengijinku na duniya tare da girmamawa da tsoro
da zuciya mai gaskiya. Ku yi masu biyayya kamar ga
Almasihu. 6 Ku yi masu biyayya ba don lallai suna
kallonku ba domin ku faranta masu rai. Maimakon
haka, ku yi biyayya kamar bayi ga Almasihu. Ku yi
nufin Allah daga zuciya. 7 Ku yi hidima da dukan
zuciya, kamar kuna bautar Ubangiji ba mutane ba. 8
Sai ku sani cewa duk abinda mutum ya yi zai karbi
sakamako daga wurin Ubangiji, ko shi bawa ne ko
'yantacce. 9 Ku kuma iyayengiji, ku yi irin wannan ga
barorin ku. Kada ku razana su. Kun sani shi wanda
ke Ubangijinsu da ku daya ne yana sama. Kun sani
tare da shi baya nuna tara. 10 A karshe, ku karfafa
cikin Ubangiji da cikin karfin ikonsa. 11 Ku dauki
dukan makamai na Allah, domin ku iya dagewa gaba
da dabarun shaidan. 12 Gama yakinmu ba da nama da
jini bane. Amma, da ikoki da mulkoki da mahukuntan
wannan zamani mai duhu da rundunai masu duhu na
mugunta cikin sammai. (aiōn g165) 13 Don haka ku dauki
dukan makamai na Allah, domin ku iya tsayawa da
karfi cikin muguwar rana. Bayan kun yi komai za ku
tsaya da karfi. 14 Saboda haka ku tsaya da karfi. Ku yi
wannan bayan kun yi damara cikin gaskiya kuna yafa
sulke na adalci. 15 Ku yi wannan bayan kun daure
kafafunku da shirin kai bisharar salama. 16 Cikin
dukan abu ku dauki garkuwar bangaskiya, wadda za
ku kashe dukan kibau masu wuta na mugun. 17 Ku
dauki kwalkwalin ceto da takobin Ruhu, wanda shine
maganar Allah. 18 Tare da kowacce irin addu'a da roko
kuna addu'a kullum cikin Ruhu. Da wannan lamiri,
kuna tsare wannan da iyakacin kula da dukan juriya
da roko saboda dukan masu bi. 19 Ku yi mani addu'a,
domin in karbi sako duk sa'adda na bude bakina.
Ku yi addu'a in sami gabagadin bayyana boyayyar
gaskiyar bishara. 20 Saboda bishara nake jakada cikin
sarkoki, yadda a cikinta zan yi magana gabagadi
yadda takamata. 21 Amma domin ku san rayuwa
ta, da yadda nake, Tikikus, dan'uwa kaunatacce da
amintaccen bawa cikin Ubangiji, zai sanar da ku
dukan abu. 22 Saboda wannan dalili na aiko shi gare
ku, domin ku san al'amuran mu, kuma domin ku sami
ta'aziya a zukatan ku. 23 Bari salama ta kasance tare
da 'yan'uwa, kauna da bangaskiya daga wurin Allah
Uba da Ubangiji Yesu Almasihu. 24 Alheri ya kasance
tare da wadannan da suke kaunar Ubangijinmu Yesu
Almasihu tare da kauna mara mutuwa.

# Filibbiyawa

1 Bulus da Timoti bayin Almasihu Yesu, zuwa ga
dukan wadan da aka kebe cikin Almasihu Yesu da
ke a Filibi, tare da masu kula da ikilisiya da dikinoni. 2
Bari alheri ya kasance tare da ku da salama daga Allah
Ubanmu da Ubagijinmu Yesu Almasihu. 3 Ina godiya
ga Allahna duk lokacin da na tuna da ku. 4 Ko yaushe
cikin addu'a ta dominku duka, da farin ciki na ke
addu'a. 5 Ina godiya domin tarayyar ku a cikin bishara
tun daga rana ta fari har ya zuwa yanzu. 6 Na tabbata
game da wannan abu, shi wanda ya fara aiki mai kyau
a cikinku zai ci gaba da shi har ya kai ga kammala
zuwa ranar Yesu Almasihu. 7 Daidai ne in ji haka
game da dukanku domin kuna zuciya ta. Dukanku
abokan tarayya ta ne cikin alherin Allah wajen dauri
na da kuma kariyar bishara, da tabbatar da bishara.
8 Domin Allah mashaidi na ne, a kan yadda ina da
marmarin ku duka cikin zurfin kaunar Almasihu Yesu.
9 Ina yin wannan addu'a: kaunar ku ta habaka gaba
gaba a cikin sani da dukan fahimta. 10 Ina addu'a a
kan haka domin ku gwada ku zabi mafifitan abubuwa.
Ina addu'a domin ku zama sahihai marasa abin zargi a
ranar Almasihu. 11 Wannan kuma domin a cika ku da
'ya'yan adalci da ake samu ta wurin Yesu Almasihu,
zuwa ga daukaka da yabon Allah. 12 Yanzu ina so ku
sani, 'yan'uwa, cewa al'amuran da suka faru da ni sun
zama dalilan cin gaban bishara kwarai da gaske. 13
Sakamakon haka, sarkokina cikin Almasihu sun zama
sanannu ga dukan sojojin fada da kuma sauran jama'a,
14 har galibin 'yan'uwa cikin Ubangiji suka karfafa
kwarai sabili da sarkokina, suka fito a fili suka yi
shelar maganar Allah gabagadi. 15 Lalle wadansu suna
shelar Almasihu cikin kishi da husuma, wadansu kuwa
domin kyakyawar manufa. 16 Masu shelar Almasihu
domin kauna sun sani cewa an ajiye ni nan domin in
kare bishara. 17 Amma wadansu kuwa suna shelar
Almasihu saboda sonkai da rashin gaskiya. A zaton su
suna wahalar da ni cikin sarkokina. 18 Sai kuma me?
Ta kowace hanya, ko da gangan ko da gaske, shelar
Almasihu ake yi, ina kuma murna da wannan! I, zan yi
murna. 19 Domin na sani wannan zai kai ga sanadiyar
kubuta ta. Wannan zai faru sabili da addu'ar ku, da
kuma taimakon Ruhun Yesu Almasihu. 20 Bisa ga abin
da hakikance nake tsammani da tabbaci cewa ba zan
kunyata ba. Maimakon haka, da dukan karfin hali
kamar kullum, da yanzu kuma, ina da burin kawo
daukaka ga Almasihu a cikin jikina. Ina da begen
Almasihu ya sami daukaka a cikin jikina ko cikin
rayuwa ko cikin mutuwa. 21 Domin ni a gare ni rai
Almasihu ne, mutuwa kuwa riba ce. 22 Amma idan
ya zamanto rayuwata cikin jiki za ta kawo amfanin
hidima to, ban san wanda zan zaba ba. 23 Amma
dukansu biyu suna jan hankali na. Ina da burin in
bar nan in kasance tare da Almasihu, wannan ya
fiye mani kwarai! 24 Duk da haka rayuwata cikin jiki
wajibi ne sabili da ku. 25 Tunda shike ina da tabbas
a kan wannan, na kuma sani zan rayu, in cigaba da
kasancewa da ku duka domin cigaban ku, da farincikin
ku, cikin bangaskiya. 26 Sakamakon haka, takamar ku
cikin Almasihu Yesu za ta bunkasa sabili da dawowa ta
a gare ku. 27 Ku tafiyar da al'amuran ku kamar yadda
ya cancanci bisharar Almasihu, ku yi haka domin
ko na zo in duba ku, ko bana nan inji yadda kuke
tsaye daram cikin ruhu guda. Ina fatan in ji cewa da
nufi daya kuke fama tare saboda bangaskiyar nan ta
bishara. 28 Kada ku tsorata da kome da magabtanku
za su yi. Alama ce a gare su ta hallakar su. Amma ku
kuwa alama ce ta ceton ku, wannan kuwa daga Allah
ne. 29 Gama an yi maku alheri, sabo da Almasihu,
ba gaskantawa da Almasihu kawai ba, amma har ma
shan wuya dominsa. 30 Kuna da shan wuya irin tawa
wanda kuka gani, wanda kun ji nake sha har yanzu.

2 Idan akwai wani abin karfafawa cikin Almasihu.
Idan da wata ta'aziyya daga kaunarsa. Idan akwai
zumunta a Ruhu. Idan da tatausan jinkai da tausayi.
2 Ku cika farin cikina don ku zama da tunani irin
haka, kuna da kauna daya, kuna tarayya cikin Ruhu
daya, ku kasance da manufa iri daya. 3 Kada ku yi
komai cikin sonkai ko girman kai. A maimakon haka
cikin zuciya mai tawali'u kowa na duban wadansu
fiye da kansa. 4 Kada kowa ya dubi bukatun sa, amma
yana lura da bukatun wadansu. 5 Ku yi tunani cikin
hanya wadda ke cikin Almasihu Yesu. 6 Wanda ya
yi zama cikin siffar Allah, bai mai da daidaitarsa da
Allah wani abin da zai rike ba. 7 Maimakon haka, ya
wofintar da kansa. Ya dauki siffar bawa. Ya bayyana
cikin kamannin mutane. An same shi a bayyane
kamar mutum. 8 Ya kaskantar da kansa, ya yi biyayya
har ga mutuwa, mutuwa ta gicciye. 9 Saboda haka
Allah ya ba shi mafificiyar daukaka. Ya ba shi suna
wanda yafi kowanne suna. 10 Domin a cikin sunan
Yesu kowace gwiwa za ta durkusa, gwiwoyin wadanda

ke cikin sama da kuma duniya da kuma karkashin
duniya. 11 Kuma kowanne harshe zai furta cewa
Yesu Almasihu Ubangiji ne, zuwa daukakar Allah
Uba. 12 Domin wannan kaunatattuna, kamar yadda
kullum kuke biyayya ba sai ina nan kadai ba. Balle
yanzu da bananan, ku yi aikin cetonku da tsoro da
far gaba. 13 Gama Allah ne yake aiki a cikinku ku
yi nufi duka da aikata abin da zai gamshe shi. 14
Ku yi kowanne abu ba tare da gunaguni da gardama
ba. 15 Domin ku zama marasa abin zargi kuma masu
gaskiya, 'ya'yan Allah marasa aibi. Ku yi haka domin
ku haskaka kamar haske a cikin wannan duniya, a
tsakiyar karkatacciyar da gurbatacciyar tsara. 16 Ku
rike kalmar rai da karfi domin in sami dalilin daukaka
Almasihu a ranarsa. Sa'annan zan san cewa ban yi
tseren banza ba, ban kuma yi wahalar banza ba. 17 Ko
da ana tsiyaye ni kamar sadaka a kan hadaya da kuma
hidimar bangaskiyarku, na yi farin ciki, kuma na yi
farin ciki tare da ku duka. 18 Kamar haka kuma sai ku
yi farin ciki, ku yi farin ciki tare da ni. 19 Amma na yi
niyya in aiko da Timoti wurin ku ba da dadewa ba,
domin ni ma in sami karfafuwa idan na san al'amuran
ku. 20 Gama bani da wani wanda halinmu yayi daidai
da nasa, wanda yake juyayin ku da gaskiya. 21 Domin
duka ribar kansu suke nema bata Yesu Almasihu
ba. 22 Amma kun san darajar sa, kamar yadda da ke
hidimar mahaifisa, haka ya bauta mani cikin bishara.
23 Shi nake sa zuciyar in aiko maku ba da dadewa ba
idan naga yadda al'amura nake gudana. 24 Amma ina
da gabagadi cikin Ubangiji cewa ni da kaina zan zo
ba da dadewa ba. 25 Amma ina tunanin yakamata
in sake aiko maku da Abafaroditus, shi dan'uwana
ne, abokin aiki, da abokin yaki, manzon ku da kuma
bawa domin bukatu na. 26 Da shike yana marmarin
ku duka, ya damu kwarai da shike kun ji yayi rashin
lafiya. 27 Da gaske yayi rashin lafiya har ya kusan
mutuwa. Amma Allah ya ji tausayin sa, ba shi kadai
ba, amma har da ni, domin kada in yi bakin ciki kan
bakin ciki. 28 Domin haka na yi niyyar aiko shi, saboda
idan kun sake ganinsa za ku yi farin ciki ni kuma
in kubuta daga juyayi. 29 Ku karbi Abafaroditus da
dukan murna cikin Ubangiji. Ku ga darajar mutane
irin sa. 30 Domin saboda aikin Almasihu ne ya kusan
mutuwa. Ya sadakar da ransa domin ya bauta mani
domin ya cika hidimar da ya kamata ku yi mani.

3 A karshe, 'yan'uwana, ku yi farin ciki cikin Ubangiji.
In sake rubuta maku wadannan abubuwa ba wani
abu mai nauyi ba ne a gare ni. Wadannan abubuwa
zasu tsare ku. 2 Ku yi hankali da karnuka. Ku yi
hankali da miyagun ma'aikata. Ku yi hankali da masu
yanke-yanke. 3 Gama mune kaciyar. Don mune muke
sujada ta wurin Ruhun Allah. Mune masu fahariya
chikin Almasihu Yesu, kuma ba mu da gabagadi cikin
jiki. 4 Ko da shike, ni kaina ina gabagadi ga jiki. Idan
wani zai iya tunanin gabagadi ga jiki, ni na fi shi. 5
An yi mani kaciya a rana ta takwas, daga mutanen
Israila, na kabilar Biliyaminu, Bayahuden Yahudawa;
ga zancen shari'a Bafarisiye nake. 6 Wajen himma na
tsanantawa ikilisiya. Ga zancen adalci cikin sharia,
na zama mara abin zargi. 7 Amma duk wadannan
abubuwan da suka zama riba a gare ni, na dauke
su asara ne saboda Almasihu. 8 I, lallai ina lisafta
dukan wadannan abubuwa asara saboda mafificin
sanin Almasihu Yesu Ubangijina. Saboda shine na yi
asarar dukan abubuwa. Na maishe su marasa amfani
domin in ribato Almasihu, 9 a iske ni cikinsa. Ba ni da
wani adalcin kaina ta wurin shari'a. Maimakon haka,
ina da adalci ta wurin bangaskiya cikin Almasihu,
adalcin dake daga wurin Allah ta wurin Bangaskiya.
10 Yanzu ina so in san shi da ikon tashinsa, da tarayya
cikin shan wuyarsa. In kuma zama kamarsa wajen
mutuwarsa, 11 domin ta ko kaka in kai ga tashi daga
cikin matattu. 12 Ba wai na rigaya na sami wadannan
abubuwa bane, ko kuma na riga na zama cikakke.
Amma ina nace bi domin in cafki wannan da Almasihu
Yesu ya cafko ni dominsa. 13 'Yan'uwa, ban dauka
cewa na riga na cafka ba tukuna. Amma akwai abu
daya da nake yi: ina mantawa da abin da ke baya,
ina kutsawa zuwa ga abin da ke gaba. 14 Ina nacewa
zuwa ga manufar nan in kai ga samun ladar nasara
na madaukakin kiran Allah cikin Almasihu Yesu. 15
Dukan mu wadanda muke kammalallu, sai mu yi
tunani ta wannan hanyar, idan kuwa kun yi tunanin
wani abu daban, to Allah zai bayyana maku wannan
kuma. 16 Sai dai, in da muka rigaya muka kai, bari mu
rike shi haka. 17 Ku zama masu koyi da ni, 'yan'uwa.
Ku duba da kyau wadannan da suke tafiya yadda
muka zama abin koyi a gare ku. 18 Mutane da dama
suna tafiya -sune wadanda na ba ku labarin su, yanzu
kuma ina fada maku har da hawaye - kamar makiyan
gicciyen Almasihu ne. 19 Karshen su hallaka ne.
Domin allahn su ciki ne, fahariyar su kuma tana cikin

kunyar su. Tunanin su na kan al'amuran duniya. 20
Amma mu 'yangarincin mu a sama yake, daga inda
muke sauraron mai ceto, Ubangiji Yesu Almasihu. 21
Za ya sake jikinmu na kaskanci ya siffanta shi kamar
jikin darajarsa, siffantacce ta karfin ikonsa inda ya
sarayar da dukan abubuwa a gare shi.

4 Saboda haka, kaunatattu 'yan'uwana da nake
marmari, farin ciki na da rawani na, a wannan
hanya ku tsaya daram cikin Ubangiji, kaunatattun
abokai. 2 Ina rokon Afodiya, ina rokon Sintiki, ku zama
da ra'ayi daya cikin Ubangiji. 3 Babu shakka, ina sake
rokon ku, abokan tarayyar takunkumina na gaske:
ku taimaka wa matayen nan. Domin mun yi wahala
tare a cikin yada bishara tare da Kilimas da sauran
abokan aiki na, wanda sunayensu na rubuce cikin
littafin rai. 4 Yi farin ciki cikin Ubangiji kullayomi.
Ina sake cewa, yi farin ciki. 5 Bari dukan mutane su
ga jimirin ku. Ubangiji ya yi kusa. 6 Kada ku damu
da kowanne abu, maimakon haka, cikin komai tare
da addu'a, da rokeroke, da godiya, bari rokeroken
ku su sanu ga Allah. 7 Salamar Allah, da ta zarce
dukan ganewa za ta tsare zuciyarku da tunaninku
cikin Almasihu Yesu. 8 A karshe, 'yan'uwa, duk abin
da ke mai gaskiya, duk abin da ya isa ban girma, duk
abin da ke mai adalci, duk abin da ke mai tsabta, duk
abin da ke karbabbe, duk abin da ke kawo kauna, duk
abin da ke da kyakkyawan ambato, idan akwai yabo,
yi tunani a kan wadannan abubuwan. 9 Wadannan
abubuwan da kuka koya kuka karba kuka ji kuka gani
a rayuwa ta, ku aikata wadannan abubuwan. Allah mai
salama zai kasance tare da ku. 10 Na yi farin ciki sosai
cikin Ubangiji domin yanzu a karshe kun sabunta
kulawar ku game da ni. Kun kula da ni da gaske
kwanakin baya, amma ba ku samu zarafin taimako
ba. 11 Ba don bukata ta bane nake fada wannan.
Domin na koyi dangana a kowanne irin yanayi. 12
Na san yadda zan zauna cikin bukata, na kuma san
yadda zan samu a yalwace. A kowace hanya cikin
kowanne abu na koyi asirin yadda zan ci da yawa da
yadda zan zauna da yunwa, yadda zan zama a yalwace
kuma in zama cikin bukata. 13 Zan iya yin komai ta
wurinsa shi da yake karfafa ni. 14 Duk da haka, kun yi
zumunta da ni cikin kunci na. 15 Kun kuma sani, ku
Filibiyawa, cewa da farkon bishara, lokacin da na bar
Makidoniya, babu ikilisiya da ta tallafe ni cikin batun
bayarwa da karba sai ku kadai. 16 Ko lokacin da nake
Tassalonika, kun aika da gudumawar biyan bukatu na
fiye da sau daya. 17 Ba domin ina neman kyauta ba
ne. A maimakon haka, ina neman amfani da zai kawo
karuwa cikin ajiyar ku. 18 Na karbi dukan abubuwan,
ina da shi a yalwace. An kosar da ni. Na karba ta
hanun Abafroditus abubuwa daga wurinku. Shesheki
na dadin kamshi mai dandanno, karbabbiyar hadaya
mai gamsarwa ga Allah. 19 Allah na zai cika dukan
bukatunku bisa ga yalwarsa da ke cikin daukaka cikin
Almasihu Yesu. 20 Yanzu bari daukaka ta tabbata ga
Allah da Ubanmu har abada abadin. Amin. (aiōn g165) 21
Gai da kowanne mai bi cikin Almasihu Yesu. Dukan
'yan'uwa da ke tare da ni suna gaisuwa. 22 Dukan
masu bi a nan suna gaisuwa, musamman wadanda
suke gidan Kaisar. 23 Bari alherin Ubangijin Yesu
Almasihu ya zauna tare da ruhunku. Amin

# Kolossiyawa

1 Bulus manzon Almasihu Yesu ta wurin nufin Allah
da Timoti dan'uwanmu, 2 zuwa ga masu bada
gaskiya da amintattun 'yan'uwa cikin Almasihu da
suke a Kolosi. Bari alheri da salama su kasance tare da
ku daga wurin Allah Ubanmu. 3 Muna godiya ga Uban
Ubangijinmu Yesu Kristi, kuma kullum muna addu'a
dominku. 4 Mun ji bangaskiyar ku cikin Almasihu
Yesu da kaunar da kuke da ita wa dukan kebabbu ga
Allah. 5 Kuna da kaunar nan domin bege na hakika ga
abin da aka tanadar maku a sama. Kun riga kun ji
game da begen nan na hakika maganar gaskiya da
bishara, 6 wanda ta zo maku. Wannan bishara tana
ba da yaya tana kuma hayayyafa da kuma girma a
cikin dukan duniya. Tana yin haka a cikinku kuma tun
ranar da kuka ji ta kun kuma yi koyi game da alherin
Allah cikin gaskiya. 7 Wannan itace bishara kamar
yadda kuka koye ta a wurin Abafaras, kaunataccen
abokin bautar mu, wanda ke amintacce mai hidimar
Almasihu a madadin mu. 8 Abafaras ya bayyana mana
kaunarku a Ruhu. 9 Saboda da wannan kauna, tun
daga ranar da muka ji haka, ba mu fasa yi maku addu'a
ba. Muna ta roko domin ku cika da sanin nufinsa
cikin dukan hikima da fahimta ta ruhaniya. 10 Muna
ta addu'a domin ku yi tafiya da ta cancanci Ubangiji
a kowace hanya da za ta faranta masa rai. Muna ta
addu'a cewa za ku ba da 'ya'ya cikin kowanne aikin
nagari kuma za ku yi girma cikin sanin Allah. 11 Muna
addu'a ku karfafa a cikin kowanne iyawa bisa ga ikon
daukakarsa zuwa ga matukar jimrewa da hakuri. 12
Muna addu'a za ku yi godiyar farinciki ga Uban, wanda
ya sa kuka samu rabo cikin gado na masu bangaskiya
cikin haske. 13 Ya kwato mu daga mulkin duhu ya
kuma maishe mu ga mulkin kaunataccen Dansa. 14 Ta
wurin Dan ne muka sami fansa, gafarar zunubai. 15
Dan shine surar Allah mara ganuwa. Shine farkon
dukan hallitta. 16 Domin ta wurinsa ne aka halicci
dukan abubuwa, wadanda ke sama da wadanda ke
duniya, masu ganuwa da marasa ganuwa. Ko kursiyai
ko mulkoki ko sarautai ko ikoki, dukan abubuwa shi ya
hallice su kuma dominsa. 17 Ya kasance kafin dukan
abubuwa, a cikinsa ne kuma komai yake hade. 18 Kuma
shine kan jikin, ikilisiya. Shine farko da kuma dan fari
daga cikin matattu, don haka yana da wuri na fari a
cikin dukan abubuwa. 19 Domin Allah ya yi farinciki
cewa dukan cikarsa ta kasance a cikinsa, 20 kuma ya
sulhunta kowanne abu zuwa gare shi ta wurin Dan.
Allah ya kawo salama ta wurin jinin giciyensa. Allah
ya sulhunta duka zuwa gare shi, ko abubuwan da ke
duniya ko abubuwan da ke sama. 21 Domin a da ku
baki ne ga Allah, kuma makiyansa ne cikin zuciya da
cikin mugun ayyuka. 22 Amma yanzu, ya sulhunta
ku ta wurin mutuwarsa ta jiki. Ya yi haka domin ya
mika ku tsarkakaku, marasa aibu da marasa abin zargi
a gabansa, 23 idan kuka ci gaba cikin bangaskiya,
kafaffu da tsayayyu, marasa kaucewa daga begen ku
na hakika na bishara da kuka ji. Wannan itace bishara
da aka yi wa kowanne halitaccen taliki a karkashin
sama. Wannan itace bishara wadda ni, Bulus, na zama
bawa. 24 Yanzu ina murna da wahala ta domin ku. A
jikina cika abin da ya rage cikin wahalar Almasihu
domin jikinsa wadda itace ikilisiya. 25 Saboda wannan
ikilisiya na zama bawa, bisa ga haki da Allah ya ba ni
domin ku, domin cika sakon Allah. 26 Wannan shine
asirin gaskiya da yake a boye shekara da shekaru da
zamanai. Amma a yanzu an bayyana shi ga wadanda
suka gaskanta da shi. (aiōn g165) 27 A gare su ne Allah
ya so ya bayyana yalwar daukakar asirin gaskiyarsa a
tsakanin al'ummai. Ya nuna Almasihu ne ke cikin ku,
tabbacin daukaka mai zuwa. 28 Wannan shine wanda
muke shella. Muna gargadar da kowanne mutum,
muna kuma koyar da kowanne mutum tare da dukan
hikima, don mu mika kowanne mutum cikakke cikin
Almasihu. 29 Domin wannan nake aiki da himma bisa
ga karfinsa da yake aiki a cikina da iko.

2 Ina so ku san yadda na sha faman gaske dominku,
domin wadanda ke a Lawudikiya, da kuma wadansu
da yawa da a jiki basu taba ganin fuska ta ba. 2 Na
yi aiki saboda zuciyar su ta sami karfafawa ta wurin
hada su cikin kauna zuwa dukan arziki na tabbaci da
fahimtar asirin gaskiya na Allah, wato Almasihu. 3 A
cikinsa dukan taskar hikima da sani ke boye. 4 Na fadi
haka domin kada wani ya yaudare ku da jawabi mai
jan hankali. 5 Ko da yake ba na tare da ku a jiki, duk
da haka ina tare da ku a cikin Ruhu. Ina murnar ganin
ku a yanayi mai kyau da kuma karfin bangaskiyar ku
cikin Almasihu. 6 Kamar yadda kuka karbi Almasihu
Ubangiji, ku yi tafiya cikinsa. 7 Ku kafu da karfi a
cikinsa, ku ginu a kansa, ku kafu cikin bangaskiya
kamar yadda aka koya maku, ku yawaita cikin yin
godiya. 8 Ku lura kada wani ya rinjaye ku ta hanyar
ilimi da yaudarar wofi bisa ga al'adun mutane, bisa

ga bin abubuwan duniya, ba na Almasihu ba. 9 A
cikinsa ne dukan Allahntaka ta bayyana ta jiki. 10 Ku
kuwa kun cika a cikinsa. Shine gaban kowanne iko
da sarauta. 11 A cikinsa ne aka yi maku kaciya, ba
kaciya irin da yan adam suke yi ba, ta cire fatar jiki,
amma ta kaciyar Almasihu. 12 An binne ku tare da
shi ta wurin baftisma. Kuma a cikinsa ne aka ta da
ku ta bangaskiya a cikin ikon Allah, wanda ya tashe
shi daga mutattu. 13 A lokacin da kuke matattu cikin
laifofinku, a cikin rashin kaciyar ku ta jiki, ya rayar da
ku tare da shi kuma ya yafe maku dukan laifofinku. 14
Ya share rubutattun basussukanku da ka'idodin da
suke gaba da mu. Ya cire su duka ya kafa su a kan
giciye. 15 Ya cire ikoki da sarautu. A fili ya falasa su
ya shugabance su zuwa ga bukin nasara ta wurin
giciyensa. 16 Saboda haka, kada kowa ya shari'anta
ku ta wurin ci ko sha, ko kuma sabon wata, ko game
da ranakun Assabaci. 17 Wadannan sune inuwar
abubuwan da ke zuwa nan gaba, amma ainihin shi ne
Almasihu. 18 Kada kowa wanda ke son kaskanci da
sujadar mala'iku ya sharantaku ku rasa sakamakonku.
Irin wannan mutum yana shiga cikin abubuwan da ya
gani ya zama mai girman kai a tunaninsa na jiki. 19 Ba
ya hade da kai. Daga kan ne dukan jiki da gabobi da
jijiyoyi ke amfani suna kuma hade tare; yana girma da
girman da Allah yake bayarwa. 20 In kun mutu tare da
Almasihu ga ala'muran duniya, don me kuke rayuwa
kamar kuna karkashin duniya: 21 "Kada ku rike, ko ku
dandana ko ku taba?" 22 Dukan wadannan abubuwa
karshen su lalacewa ne in ana amfani da su, bisa ga
kaidodi da koyarwar mutane. 23 Wadannan dokoki
suna da hikima ta jiki irin ta addini da aka kago na
kaskanci da kuma wahalar da jiki. Amma ba su da
amfanin komai a kan abin da jiki ke so.

**3** Idan dai Allah ya tashe ku tare da Almasihu, ku
nemi abubuwan da ke sama, inda Almasihu ke
zaune a hannun dama na Allah. 2 Yi tunanin a kan
abubuwan da ke sama, ba a kan abubuwan da ke kasa
ba. 3 Gama ku kun mutu, ranku kuma yana boye
tare da Almasihu cikin Allah. 4 Sa'anda Almasihu
ya bayyana, wanda shine ranku, sa'anan ku kuma
zaku bayyana tare da shi cikin daukakarsa. 5 Ku
kashe sha'awacce-sha'awaccen da suke a duniya -
zina da fasikanci, rashin tsarki, muguwar sha'awa,
mummunar buri, da kuma kwadayi, wadda shine
bautar gumaka. 6 Saboda wandannan abubuwa ne
fushin Allah ke zuwa a kan marasa biyayya. 7 A cikin
wadannan abubuwa ne kuka yi rayuwa a da da kuke
zauna a cikinsu. 8 Amma yanzu dole ku kawar da
wadannan - zafin rai, fushi, mugayen manufofi, zage-
zage, da kazamar magana daga bakinku. 9 Kada ku yi
wa juna karya, domin kun tube tsohon mutumin da
ayyukansa, 10 kun kuma yafa sabon mutum, wanda
ake sabontawa cikin sani bisa ga surar wannan da
ya hallice shi. 11 A nan ne inda babu Baheline da
Bayahude, mai kaciya da marar kaciya, bare, baubawa,
ko Basikitiye, bawa ko yantacce, amma Almasihu
shine duka, yana kuma cikin duka. 12 A matsayin ku
na zababbun Allah, masu tsarki da kaunatattu sai
ku yafa jinkai, ayyukan kirki, saukin kai, kamewa da
hakuri. 13 Yi hakuri da juna. Ku yi wa juna alheri.
Idan wani na da damuwa da wani, ku gafarta kamar
yadda Ubangiji ya gafarta maku. 14 Fiye da wadanan
abubuwa duka, ku kasance da kauna, wanda itace
cikakkiyar kammalla. 15 Bari salamar Almasihu ta
mallaki zukatanku. Sabili da wannan salama ce aka
kiraye ku cikin jiki daya. Ku yi godiya. 16 Ku bar
maganar Almasihu ta zauna a cikinku a yalwace. Da
dukan hikima, ku koyar, ku kuma gargadi juna da
zabura, wakoki, da wakokin yabo na ruhaniya. Kuna
rairawa tare da godiya cikin zukatanku ga Allah. 17
Kuma duk abin da zaku yi cikin magana ko aiki ku
yi duka cikin sunan Ubangiji Yesu. Kuna yin godiya
ga Allah Uba ta wurinsa. 18 Mata, ku yi biyayya
ga mazajenku, yadda yakamata a cikin Ubangiji. 19
Mazaje, ku kaunaci matayenku, kada ku muzguna
masu. 20 Yaya, ku yi wa iyayen ku biyayya cikin dukan
komai, domin wannan yana faranta wa Ubangiji rai.
21 Ku Ubanni, kada ku cakuni 'ya'yanku domin kada su
karaya. 22 Bayi, ku yi wa iyayengijinku na jiki biyayya
cikin kowane abu, ba tare da bautan ganin ido ba don
faranta wa mutane rai, amma da sahihiyar zuciya. Ji
tsoron Ubangiji. 23 Duk abin da kuke yi, ku yi aiki
daga zuci domin Ubangiji ba domin mutane ba. 24 Kun
san cewa, zaku karbi sakamako na gado daga wurin
Ubangiji. Domin Ubangiji Almasihu kuke bauta wa. 25
Domin kowa ya yi rashin adalci zai karbi sakamakon
rashin adalcin da ya yi, kuma babu son kai.

**4** Ku iyayengiji, ku ba bayinku abin ke daidai ya
kuma dace garesu. Kun sani cewa ku ma, kuna da
Ubangiji a sama. 2 Ku cigaba da himmantuwa ga yin
addu'a. Ku zauna a fadake cikin addu'a da godiya.
3 Ku yi addu'a tare domin mu kuma, domin Allah

ya bude kofa domin kalmar, a fadi asirin gaskiyar
Almasihu. Don wannan ne nake cikin sarka. 4 Ku yi
addu'a domin in iya fadinsa daidai, yadda yakamata
in fada. 5 Ku yi tafiya da hikima game da wadanda
suke a waje, ku yi amfani da lokaci. 6 Bari maganarku
ko yaushe ta zama ta alheri. Bari ta zama da dadin ji
domin ku san yadda za ku amsa wa kowanne mutum.
7 Game da abubuwan da nake ciki, Tikikus zai sanar
maku da su. Shi kaunataccen dan'uwa, amintaccen
bawa, shi abokin barantaka na ne a cikin Ubangiji. 8
Na aike shi wurinku don wannan, domin ku iya sanin
halin da muke ciki, don kuma ya karfafa zukatanku.
9 Na aike shi tare da Onisimus, amintacce da kuma
kaunataccen dan'uwa, wanda daya ne daga cikin
ku. Za su gaya maku duk abin da ya faru anan. 10
Aristarkus, abokin sarka na, yana gaishe ku da Markus,
dan'uwan Barnaba (wanda a kansa ne kuka sami
umarni; in yazo, ku karbe shi), 11 da kuma Yesu
wanda ake kira Yustus. Wadannan ne kadai daga cikin
masu kaciya abokan aiki na domin mulkin Allah. Sun
zama ta'aziya a gare ni. 12 Abafaras na gaishe ku. Shi
daya daga cikinku ne kuma bawan Almasihu Yesu ne.
Kullum yana maku addu'a da himma, don ku tsaya
cikakku da hakikancewa a cikin nufin Allah. 13 Gama
ina shaidarsa a kan ya yi aiki da himma domin ku,
domin wadanda ke Lawudikiya, da na Hirafolis. 14
Luka kaunataccen likita da Dimas suna gaishe ku.
15 Ku gai da 'yan'uwa dake a Lawudikiya, da Nimfa
da ikilisiyar da ke cikin gidanta. 16 Lokacin da aka
karanta wannan wasika a tsakanin ku, sai a karanta ta
kuma a cikin ikilisiyar Lawudikiya, ku kuma tabbata
kun karanta wasika daga Lawudikiya. 17 Ku gaya wa
Arkibas, “Mai da hankali ga hidimar da ka karba cikin
Ubangiji, don ka cika shi.” 18 Wannan gaisuwa da
hannu na ne - Bulus. Ku tuna da sarka na. Alheri ya
tabbata a gare ku.

# 1 Tessalonikawa

**1** Bulus, Sila, da Timoti zuwa ga Ikilisiyar
Tassalonikawa cikin Allah Uba da Ubangiji Yesu
Almasihu. Alheri da Salama su kasance a gare ku. 2
Kullum muna bada godiya ga Allah domin ku dukka,
kamar yadda muke ambaton ku a addu'o'in mu. 3
Muna tunawa da ku ba fasawa a gaban Allahn mu da
Ubanmu kuma ayyukanku na bangaskiya, da kauna.
Da hakurin bege na abinda ke gaba cikin Ubangijinmu
Yesu Almasihu. 4 'Yan'uwa kaunatattu na Allah, Mun
san kiran ku, 5 yadda bishararmu ta zo gare ku ba ta
magana kadai ba, amma da iko, ta wurin Ruhu Mai
Tsarki, haka kuma tawurin tabbatarwa. Ta haka kuma,
kun san irin mutanen da muke acikin ku kuma domin
ku. 6 Kun zama masu koyi da mu da kuma Ubangiji,
kamar yadda kuka karbi kalmar cikin tsanani mai
yawa da murna tawurin Ruhu Mai Tsaki. 7 Sakamakon
haka, kuka zama abin misali ga dukkan wadanda ke
Makidoniya da na Akaya wadanda suka bada gaskiya.
8 Gama daga gare kune maganar Allah ta bazu ko ina,
ba kuwa Makidoniya da Akaya kadai ba. A maimako,
har ma zuwa ko ina bangaskiyarku cikin Allah ta
kai. Don haka, bama bukatar muce maku komai. 9
Domin su da kansu suna bada labarin irin zuwan mu
gare ku. Suna fadin yadda kuka juyo ga Allah daga
bautar gumaka don ku bautawa Allah mai rai. 10 Suna
bayyana cewa kuna jiran bayyanar Dansa daga sama,
wanda ya tasar daga matattu. Wannan shine Yesu,
wanda ya 'yantad da mu daga fushi mai zuwa.

**2** Domin ku da kanku kun sani, 'yan'uwa, cewa zuwan
mu gareku, ba a banza yake ba. 2 Kun kuma san
yadda aka wulakantar damu, aka kuma kunyatar
damu a Filibi, kamar yadda kuka sani. Muna nan
kuwa da karfin zuciya cikin Allahnmu domin yi maku
bisharar Allah cikin fama da yawa. 3 Domin kuwa
gargadinmu zuwa a gare ku ba gurbatacciya bace,
ko cikin rashin tsarki, ba kuma ta yaudara bace. 4
A maimako, kamar yadda Allah ya amince damu, ya
kuma damka mana amanar bishararsa, haka kuma
muke yin magana. Muna maganar ba domin mu
gamshi mutane ba, amma domin mu gamshi Allah.
Domin shi ne yake gwada zuciyarmu. 5 Domin bamu
taba yi maku dadin baki ba, ko sau daya, kamar yadda
kuka sani, ko kwadayi a asirce, kamar yadda Allah
shine shaidar mu. 6 Bamu kuma nemi daukaka daga
mutane ko daga gare ku ko kuma wadansu ba. Da
mun so da mun mori ikonmu a matsayin manzannin
Almasihu. 7 A maimakon haka, mun kaskantar da
kanmu a tsakanin ku kamar yadda uwa take ta'azantar
da 'ya'yan ta. 8 Don haka muna da kauna domin ku, ba
bisharar Allahnmu kadai muke jin dadin yi maku ba,
amma harda bada rayukan mu domin ku. Domin kun
zama kaunatattu ne a garemu, 9 Kufa tuna, 'yan'uwa,
game da aikinmu da famarmu. Dare da rana muna
aiki sosai domin kada mu nawaita wa kowane dayan
ku. A lokacin da muke yi maku bisharar Allah. 10 Ku
shaidu ne, haka ma Allah, yadda muka yi rayuwar
tsarki da kuma adalci da rashin abin zargi a wajenku
wadanda kuka bada gaskiya. 11 Don haka kun kuma
sani yadda muka rika yi da kowannenku, kamar uba
da 'ya'yansa, yadda muka yi ma ku garadi da kuma
karfafa ku, mun kuma shaida. 12 Domin ku yi tafiya a
hanyar da ta dace ga Allah, wanda ya kira ku zuwa
ga mulkinsa da kuma daukakarsa. 13 Domin wannan
dalili ne yasa muke yi wa Allah godiya a koyaushe.
Domin a lokacin da kuka karbi maganar Allah daga
wurinmu wadda kuka ji, kun karbeta da gaske ba
kamar maganar mutum ba. A maimako, kuka karbeta
da gaskiyarta, kamar yadda take, maganar Allah.
Wannan kalma kuma ita ce ke aiki a cikin ku wadanda
kuka yi bangaskiya. 14 Domin ku 'yan'uwa, kun zama
masu koyi da ikilisiyoyin Allah da ke Yahudiya cikin
Almasihu Yesu. Domim kuma kun sha wahala irin
tamu daga wurin mutanen kasarku kamar yadda
suma suka sha a hannun Yahadawa. 15 Yahudawane
suka kashe Ubangiji Yesu da sauran Annabawa, kuma
Yahudawane suka koro mu, Basu gamshi Allah ba. A
maimako, suna hamayya da dukkan mutane. 16 Sun
kuma haramta mana yin magana da Al'ummai domin
su sami ceto. Sakamakon haka kuwa kullum suna cika
zunubansu. Fushi kuma ya afko kansu daga karshe.
17 Mu kuma, 'yan'uwa, mun rabu daku na karamin
lokaci, a zahiri, ba a zuciya ba, mun kuma yi iyakar
kokarinmu da marmarin ganin fuskarku. 18 Domin
mun yi maramarin zuwa gareku. Ni, Bulus, ba sau
daya ba, amma Shaidan ya hanamu. 19 To menene
begenmu a gaba, ko murnarmu ko rawanin alfahari,
a gaban Ubangijinmu Yesu a ranar zuwansa? Ko ba
ku bane, da kuma sauran jama'a? 20 Don kuwa kune
daukakarmu da kuma farin cikinmu.

**3** Saboda haka, da bamu iya jimrewa ba, sai mukayi
tunanin cewa ya dace mu dakata a Atina tukunna.
2 Sai muka aikaTimoti, dan'uwanmu dakuma bawan
Allah a bisharar Almasihu, domin karfafaku ya kuma
ta'azantar daku a fannin bangaskiya. 3 Mun yi haka
ne saboda kada waninku ya raunana domin wadannan
wahaloli. Domin ku da kanku kun sani cewa don
haka aka kiraye mu. 4 Hakika, a lokacin da muke
tare daku, mun gaya maku cewa muna daf da shan
wahala, haka ya kuma kasance, kamar yadda kuka
sani. 5 Domin haka, da ban iya jimrewa ba, sai na aiko
domin in san yadda bangaskiyar ku take. Watakila ko
magafci a wata hanya ya rinjaye ku, sai ya kasance
wahalarmu ta zama a banza. 6 Amma Timoti da ya
dawo daga gareku sai ya kawo mamu labari mai dadi
akan bangaskiyarku da kuma kaunarku. Yako gaya
mana cewa kuna kyakkyawan tunani a kanmu, kuma
kuna marmarin ganinmu yadda muke marmarin
ganinku. 7 Sabili da haka, 'yan'uwana, mun sami
ta'aziyya tawurinku domin bangaskiyarku, a cikin
dukkan bakin cikinmu da shan wuyamu. 8 Yanzu a
raye muke, idan kun tsaya da karfi a cikin Ubangiji. 9
Gama wace irin godiya zamu ba Allah sabili da ku,
domin dukan farin cikin da muke dashi a gaban Allah
domin ku? 10 Dare da rana muke yi maku addu'a
sosai domin muga fuskokinku kuma mu cika abin
da kuka rasa cikin bangaskiyarku. 11 Bari Allah da
kuma Ubanmu da kansa, da Ubangijinmu Yesu, ya
bida sawayen mu zuwa gareku. 12 Bari Ubangiji yasa
ku karu ku kuma ribambamya a kaunar 'yan'uwanku
da dukan mutane, kamar yadda muke maku. 13 Bari
yayi haka domin ya karfafa zukatanku marassa abin
zargi a cikin tsarki a gaban Allah da Ubanmu a lokacin
zuwan Ubangijinmu Yesu da dukan tsarkakansa.

**4** A karshe, 'yan'uwa, muna karfafa ku kuma muna
yi maku gargadi cikin Ubangiji Yesu. Yadda kuka
karbi umarni a garemu game da yadda dole za kuyi
tafiya kuma ku gamshi Allah, kuma a cikin wannan
hanya ku tafi, ku kuma wuce haka. 2 Domin kun san
umarnin da muka baku cikin Ubangiji Yesu. 3 Gama
wannan ne nufin Allah: kebewar ku - cewa ku kauce
wa zina da fasikanci, 4 Cewa kowannenku ya san
yadda zai rike mata tasa cikin tsarki da girmamawa.
5 Kada kayi mata cikin zautuwar sha'awa ( kamar
al'ummai wadanda basu san Allah ba). 6 Kada wani
ya kuskura yaci amanar dan'uwansa akan wannan
al'amari. Gama Ubangiji mai ramuwa ne akan dukkan
wadannan al'amura, Kamar yadda a baya muka yi
maku kashedi kuma muka shaida. 7 Gama Allah
bai kira mu ga rashin tsarki ba, amma ga rayuwar
tsarki. 8 Domin haka, duk wanda yaki wannan ba
mutane yaki ba, amma Allah, wanda ya bada Ruhunsa
Mai Tsarki a gareku. 9 Game da kaunar 'yan'uwa,
baku bukatar wani ya sake rubuta maku, gama ku da
kanku Allah ya koyar da ku kaunar 'yan'uwa. 10 Ba
shakka, kunayin haka ga dukkan 'yan'uwa wadanda
ke cikin dukkan Makidoniya. Amma muna gargadin
ku 'yan'uwa, kuyi haka bugu da kari. 11 Kuma muna
gargadin ku 'yan'uwa kuyi kokari ku zauna a natse,
ku kula da al'amuranku, kuyi aiki da hannuwanku,
Yadda muka umarceku a baya. 12 Kuyi haka domin
tafiyar ku ta zama dai dai a gaban wadanda basu bada
gaskiya ba, kuma ya zama baku cikin bukatar komai.
13 Bamu so ku zama da rashin fahimta ba, 'yan'uwa,
game da wadanda sukayi barci, domin kada kuyi bacin
rai kamar sauran wadanda basu da tabbacin abinda
ke gaba. 14 Domin idan mun bada gaskiya Yesu ya
mutu kuma ya tashi, haka kuma tare da Yesu Allah
zai maido da duk wadanda suka yi barci a cikinsa.
15 Gama muna fada maku wannan daga maganar
Ubangiji, cewa mu da muke a raye, da aka bari har
zuwan Ubangiji, babu shakka ba za mu riga wadanda
suka yi barci ba. 16 Gama Ubangiji da kan sa zai sauko
daga sama. Zai zo da muryar babban mala'ika, da
karar kahon Allah, sai matattu cikin Almasihu su
fara tashi. 17 Sai mu da muke a raye, wadanda aka
bari, tare dasu za'a fyauce mu zuwa cikin gizagizai,
mu hadu da Ubangiji cikin sararin sama. Haka zamu
cigaba da kasancewa da Ubangiji. 18 Domin haka ku
ta'azantar da juna da wadannan maganganu.

**5** Yanzu fa game da zancen lokatai da zamanai
'yan'uwa, ba ku da bukatar a rubuta maku wani
abu. 2 Domin ku da kanku kun sani kwarai cewa
ranar zuwan Ubangiji kamar barawo take da dare. 3
Da suna zancen “zaman lafiya da kwanciyar rai,” sai
hallaka ta zo masu ba zato ba tsammani. Zai zama
kamar nakudar haihuwa ce da ke kama mace mai
ciki. Ba su kwa da wata hanyar kubuta. 4 Amma ku,
'yan'uwa, ai ba cikin duhu kuke ba har da wannan
rana zata mamaye ku kamar barawo. 5 Domin dukkan
ku 'ya'yan haske ne 'ya'yan rana kuwa. Mu ba 'ya'yan
dare ba ne ko na duhu, 6 Don haka, kada muyi barci

kamar yadda sauran ke yi. Maimakon haka, bari mu
kasance muna zaman tsaro kuma muna a fadake. 7
Don masu yin barci da dare suke yin barci, haka kuma
masu sha su bugu ma da dare suke yi. 8 Tunda shike
mu 'ya'yan rana ne, bari mu zauna a natse. Bari musa
sulke na bangaskiya da kauna, mu kuma sa kwalkwali
don ceton mu dake gaba. 9 Domin Allah bai kaddara
mu ga fushinsa ba, sai dai ga samun ceto ta wurin
Ubangijin mu Yesu Almasihu. 10 Shi ne wanda ya mutu
domin mu, don ko da muna raye ko muna mace, mu
iya rayuwa tare da shi, 11 Domin haka ku ta'azantar
da juna ku kuma inganta juna, kamar yadda kuke
yi. 12 Muna rokon ku, 'yan'uwa, ku bada daraja ga
wadanda suke aiki a tsakaninku wadanda kuma suke
shugabanci a kan ku cikin Ubangiji, wadanda kuma
suke horonku. 13 Muna kuma rokon ku, da ku kula
dasu ku kuma kaunacesu sabili da irin ayyukansu.
Ku kuma yi zaman lafiya da junan ku. 14 Muna yi
maku gargadi 'yan'uwa; ku jawa marassa ji kunne, ku
karfafa marassa karfin zuciya, ku taimaki gajiyayyu,
kuyi zaman hakuri da kowa. 15 Ku lura kada wani ya
rama mugunta da mugunta, Maimakon haka ma, Ku
cigaba da abinda ke mai kyau ga juna da kowa duka.
16 Kuyi farin ciki koyaushe. 17 Kuyi addu'a ba fasawa.
18 A cikin kome kuyi godiya. Domin wannan ne nufin
Allah a cikin Yesu Almasihu game daku. 19 Kada ku
hana Ruhun Allah aiki a cikin ku. 20 Kada ku raina
anabce anabce. 21 Ku gwada komai. Ku rike abinda
ke mai kyau. 22 Ku kaucewa duk wani abinda yayi
kama da mugunta. 23 Bari Allah na salama ya mai
da ku cikakun tsarkaka. Bari dukkan ruhun ku, da
zuciyar ku, da jikin ku su zama adanannu marassa
zargi domin zuwan Ubangijin mu Yesu Almasihu. 24
Wanda ya kira ku mai aminci ne, wanda kuma zai
aikata. 25 Yan'uwa, kuyi addu'a domin mu. 26 Ku
gaida dukkan yan'uwa da tsattsarkar sumba. 27 Ina
rokon ku saboda Ubangiji ku karanta wasikar nan ga
dukkan 'yan'uwa. 28 Bari alherin Ubangijin mu Yesu
Almasihu shi kasance tareda ku.

# 2 Tessalonikawa

**1** Bulus da Silbanus da Timoti, zuwa ga ikilisiyar
Tasolonika cikin Allah Ubanmu da Ubangiji Yesu
Almasihu. **2** Bari alheri ya kasance tare da ku da
salama daga Allah Ubanmu da Ubangijinmu Yesu
Almasihu. **3** Lallai ne mu godewa Allah kulluyaumin
domin ku, yan'uwa. Domin hakan dai dai ne, saboda
bangaskiyarku ta karu sosai, kuma kaunar junanku
tana karuwa. **4** Mu da kanmu muna fahariya da
ku a ikilisiyoyin Allah. Muna maganar hakurinku
da bangaskiyarku a cikin dukkan tsananin da kuke
fuskanta. Muna maganar kuncin da kuke jimrewa.
**5** Wannan itace alamar shari'ar Allah ta adalci.
Sakamakon haka shine za a dauke ku cancantattu na
mulkin Allah wanda kuke wahala dominsa. **6** Adalci
ne ga Allah ya mayar da kunci ga wadanda suke
kuntata maku, **7** ya kuma baku hutu ku dake shan
wuya tare da mu. Zai yi haka ne a bayyanar Ubangiji
Yesu daga sama da Mala'ikun ikonsa. **8** A cikin wuta
mai huruwa zai dau fansa bisa wadanda basu san
Allah ba da wadanda basu karbi bisharar Ubangijinmu
Yesu almasihu ba. **9** Za su sha azaba ta hallaka har
abada daga fuskar Ubangiji da kuma daukakar ikonsa.
(aiōnios g166) **10** Zai yi wannan lokacin da yazo a wannan
rana don jama'arsa su daukaka shi, kuma ya zama
abin mamaki ga dukkan wadanda suka bada gaskiya.
Domin kun gaskata shaidarmu a gare ku. **11** Saboda
wannan muke addu'a kullum domin ku. Muna addu'a
domin Allahnmu ya sa ku cancanci kiran ku. Muna
addu'a ya biya ku muradin ku na yin nagarta da
dukkan wani aikin bangaskiya da kuma iko. **12** Muna
addu'a haka domin sunan Ubangijinmu Yesu ya sami
daukaka daga gare ku. Addu'armu itace ya daukaka
ku, saboda alherin Allahnmu da Ubangijinmu Yesu
Almasihu.

**2** Yanzu game da zuwan Ubangijinmu Yesu Almasihu
da taruwarmu domin kasancewa tare da shi; muna
rokonku yan'uwa, **2** kada kuyi saurin damuwa ko
ku gigice saboda wani ruhu ko kuma sako ko kuma
wasika da ta yi kamar daga wurin mu, da ke cewa
ranar zuwan Ubangiji ta rigaya ta zo. **3** Kada wani ya
yaudare ku ta kowace hanya. Domin wannan rana
baza ta zo ba sai fandarewar nan ta zo kuma an
bayyana mutumin tawayen nan wato dan hallaka. **4**
Wannan shi ne wanda ya ke gaba, yana kuma daukaka
kansa fiye da duk abin da ake kira Allah ko kuma
ake bautawa. Sakamakon haka yana zama a kursiyin
Allah har ma yana cewa shine Allah. **5** Baku tuna ba
lokacin da nake tare daku na gaya maku wadannan
abubuwa? **6** Yanzu kun san abinda ke tsaida shi,
domin a bayyana shi a lokacin da ya dace. **7** Ko yanzu
asirin take shari'a ya na aiki, sai dai a kwai wanda
ke tsaida shi yanzu har sai an dauke shi. **8** Sa'anan
za'a bayyana dan tawayen, wanda Ubangiji Yesu zai
hallaka shi da numfashin bakinsa. Ubangiji zai mayar
da shi ba kome ba ta wurin bayyanuwar zuwansa.
**9** Mai tawayen nan kuwa, zai zo ne bisa ga aikin
shaidan da dukan iko, alamu, da al'ajiban karya, **10**
da kuma dukan yaudara ta rashin adalci. Wadannan
abubuwa za su zama ga wadanda suke hallaka, saboda
ba su karbi kaunar gaskiya ba domin su sami ceto. **11**
Saboda wannan dalilin Allah ya aiko masu da sabani,
saboda su yarda da karya. **12** Sakamakon shine dukkan
su za'a yi masu shari'a, wato wadanda ba su yarda
da gaskiya ba suna kuma jin dadin rashin adalci.
**13** Amma muna masu godiya kulluyaumin ga Allah
domin ku, yan'uwa wadanda Ubangiji yake kauna.
Ubangiji ya zabe ku a matsayin yayan fari don ceto
cikin tsarkakewar Ruhu da gaskatawa da gaskiya. **14**
Wannan shine abinda ya kira ku gare shi ta wurin
bishararmu domin ku sami daukakar Ubangijinmu
Yesu Almasihu. **15** Saboda haka yan'uwa, ku tsaya
da gaske. Ku rike al'adun da aka koya maku, ko ta
kalma ko kuma ta wasikarmu. **16** Yanzu bari Ubangiji
Yesu Almasihu da kansa, da Allah Ubanmu wanda
ya kaunace mu ya ba mu madawwamiyar ta'aziya da
gabagadi mai kyau domin gaba ta wurin alheri, (aiōnios
g166) **17** ya ta'azantar da ku ya kuma gina zuciyarku
cikin kowane aiki mai kyau da kalma.

**3** Yanzu yan'uwa, ku yi mana addu'a saboda maganar
Ubangiji tayi sauri ta sami daukaka, kamar yadda
take tare da ku. **2** Ku yi addu'a domin mu kubuta daga
mutane masu mugunta da keta, gama ba kowa ke da
bangaskiya ba. **3** Amma Ubangiji mai aminci ne, shi
wanda zai kafa ku ya tsare ku daga mugun. **4** Muna da
gabagadi cikin Ubangiji a kan ku, cewa kuna yi, kuma
za ku ci gaba da yin abubuwan da muka umurta. **5**
Ubangiji ya bi da zuciyarku zuwa kaunar Allah da
kuma jimrewar almasihu. **6** Yanzu muna umurtar ku,
yan'uwa, a cikin sunan Ubangiji Yesu Almasihu, ku
guji duk dan'uwa wanda yake zaman banza ba kuma

akan al'adun da kuka karba daga wurin mu ba. **7**
Saboda ku da kan ku kun sani yana da kyau kuyi koyi
da mu. Ba mu yi zama a cikin ku kamar wadanda ba
su da tarbiya ba. **8** Ba mu kuma ci abincin kowa ba
tare da mun biya ba. Maimakon haka, mun yi aiki
dare da rana cikin wahala da kunci domin kada mu
dora wa kowa nauyi. **9** Mun yi haka ba don ba mu da
iko ba. Maimakon haka, mun yi wannan ne saboda mu
zama abin koyi a wurin ku, domin ku yi koyi da mu.
**10** Lokacin da muke tare da ku, mun umurce ku, “Duk
wanda ba ya son yin aiki, kada yaci abinci.” **11** Saboda
mun ji cewa wasun ku sun ki yin aiki. Ba su aiki sai dai
shiga shirgin wasu. **12** Irin wadannan, muke umurta
da kuma karfafa wa cikin Ubangiji Yesu Almasihu,
da su yi aiki da natsuwa, suna cin abincin kan su.
**13** Amma ku yan'uwa, kada ku rabu da yin abinda
ke daidai. **14** In wani yaki biyayya da kalmominmu
cikin wannan wasika, ku kula da shi kuma kada kuyi
ma'amalar komai dashi, saboda ya ji kunya. **15** Kada
ku dauke shi a matsayin makiyi, amma ku gargade
shi a matsayin dan'uwa. **16** Bari Ubangijin salama da
kansa ya ba ku salama kulluyaumin ta kowace hanya.
Ubangiji ya kasance tare da ku duka. **17** Wannan ita ce
gaisuwa ta, ni Bulus, da hannuna, wanda shine alama
a kowace wasika ta. Haka nake rubutu. **18** Bari alherin
Ubangijinmu Yesu Almasihu ya kasance tare da ku
duka.

# 1 Timoti

**1** Bulus, manzon Almasihu Yesu bisa ga umarnin
Allah Mai cetonmu, da Almasihu Yesu begenmu,
2 zuwa ga Timoti, dana na gaske cikin bangaskiya:
Alheri, jinkai da salama daga wurin Allah da Almasihu
Yesu Ubangijinmu. 3 Kamar yadda na nanata maka
ka yi, da zan tafi Makidoniya cewa, ka dakata a Afisa
domin ka umarci wadansu mutane kada su koyar
da wata koyarwa dabam. 4 Kada su bata lokacinsu
wajen sauraron tatsunniyoyi da kididdiga marar
iyaka. Wannan yana haddasa gardandami, maimakon
taimakawa shirin Allah, da ke ta wurin bangaskiya.
5 Manufar shari'a kuwa kauna ce daga tsabtacciyar
zuciya, da tsatstsakan lamiri, da kuma sahihiyar
bangaskiya. 6 Wadansu sun kauce daga tafarkin sun
juya zuwa ga maganganun banza. 7 Suna so su zama
malaman sha'ria, amma basu fahimci abin da suke
fada ba ko abin da suka tsaya akai. 8 Amma mun
sani shari'a tana da kyau idan an yi amfani da ita
bisa ga ka'ida. 9 Gama mun san wannan, shari'a ba
domin mai adalci take ba, amma domin marasa bin
doka, mutane masu tawaye, da marasa bin Allah, da
masu zunubi, da marasa Allah, da masu sabo. An bada
shari'a domin masu kisan iyaye maza da iyaye mata,
da masu kisan kai, 10 Domin fasikai da 'yan ludu,
domin masu satar mutane su kai su bauta, domin
makaryata, da masu shaidar zur, da kuma dukan abin
da ke gaba da amintaccen umarni. 11 Wannan umarni
bisa ga daukakkiyar bisharar Allah ne mai albarka,
wadda aka bani amana. 12 Ina gode wa Almasihu
Yesu Ubangijimu. wanda ya karfafa ni, gama ya karbe
ni amintacce, ya sani cikin hidimarsa. 13 Dama can
ni mai sabo ne, mai tsanantawa kuma dan ta'adda.
Amma duk da haka aka yi mani jinkai domin na yi su
cikin jahilci da rashin bangaskiya. 14 Amma alherin
Ubangijinmu ya kwararo mani tare da bangaskiya, da
kauna da ke cikin Almasihu Yesu. 15 Wannan bishara
amintacciya ce, ta isa kowa ya karba, cewa Almasihu
Yesu ya zo cikin duniya domin ceton masu zunubi,
a cikinsu kuwa ni ne mafi lalacewa. 16 Saboda haka
ne na sami jinkai, domin ta wurina ni na farko, a
nuna hakurin Yesu Almasihu. Ya yi wannan domin in
zama misali ga wadanda za su bada gaskiya zuwa rai
madawwami. (aiōnios g166) 17 Yanzu, ga Sarkin zamanai,
marar mutuwa, boyayye, Allah makadaici girma, da
daukaka su tabbata a gare shi har abada abadin. Amin.
(aiōn g165) 18 Ina danka wannan umarni gareka, dana,
Timoti. Ina haka ne bisa ga anabcin da aka yi a baya
game da kai, domin ka shiga yaki mai kyau. 19 Ka yi
wannan domin ka zama da bangaskiya da kyakkyawan
lamiri. Wadansu mutane sun ki sauraron wannan suka
yi barin bangaskiyarsu. 20 Kamar su Himinayus da
Iskandari, wadanda na bada su ga shaidan domin su
horu su koyi kin yi sabo.

**2** Don haka da farko dai, Ina roko a yi roke-roke
da addu'o'i, da yin roko domin jama, a dukka, da
ba da godiya, a yi haka domin dukkan mutane, 2
domin sarakuna da dukkan masu mulki, domin mu yi
zaman salama da rayuwa a natse cikin Allahntaka da
daraja. 3 Wannan yana da kyau da karbuwa a gaban
Allah mai cetonmu. 4 Yana so dukkan mutane su
sami ceto, su kai ga sanin gaskiya. 5 Domin Allah
daya ne, Matsakanci kuma daya ne, tsakanin Allah da
mutum, wannan mutum Almasihu Yesu ne. 6 Ya bada
kansa fansa domin kowa, domin shaida a daidaitaccen
lokaci. 7 Sabo da wannan dalilin, aka sa ni kaina, na
zama mai shelar bishara da manzo. Gaskiya nake fada.
Ba karya nake yi ba. Ni mai koyarwa ne na al'ummai
cikin gaskiya da kuma imani. 8 Saboda haka, ina so
maza da ke a kowanne wuri suyi addu'a, kuma suna
daga hannuwa masu tsarki a sama ba tare da fushi da
gardama ba. 9 Kazalika, ina so mata su sa kayan da ya
cancanta, da adon da ya dace da kamun kai. Kada su
zama masu kitson gashi da zinariya da azurfa da tufafi
masu tsada. 10 Ina so su sa tufafin da ya cancanci
matan da ke rayuwar Allahntaka ta wurin kyawawan
ayyuka. 11 Mace ta koya cikin natsuwa da saukin
kai a cikin komai. 12 Ban ba da izini mace ta koyar
ko ta nuna iko a kan namiji ba, amma ta zauna da
natsuwa. 13 Adamu ne aka fara halitta, kafin Hauwa'u.
14 Ba Adamu ne aka yaudara ba, amma macen ce
aka yaudara cikin laifi. 15 Duk da haka, zata sami
ceto ta wurin haifuwar 'ya'ya, idan suka ci gaba cikin
bangaskiya, da kauna da tsarki da sahihiyar zuciya.

**3** Wannan magana tabattaciya ce: Idan wani na
da marmari ya zama shugaban Ikilisiya, ya na
marmarin aiki mai kyau. 2 Don haka, wajibi ne
shugaban Ikilisiya ya zama mara abin zargi. Ya zama
mai mace daya. Wajibi ne ya zama mai kamewa, mai
hankali, mai natsuwa mai karbar baki. Wajibi ne ya
iya koyarwa. 3 Kada ya zama mashayin giya, da mai
tankiya. A maimakon haka ya zama da natsuwa, mai

salama. Ba mai son kudi ba. 4 Wajibi ne ya iya lura
da gidansa da kyau, 'ya'yansa su zama masu yi masa
biyayya da dukkan bangirma. 5 Gama idan mutum
bai iya sarrafa gidansa ba, ta yaya zai iya lura da
Ikkilisiyar Allah? 6 Bai kamata ya zama sabon tuba ba,
domin kada ya kumbura da girman kai, kada ya fadi
cikin irin hukunci da aka yi wa Ibilis. 7 Wajibi ne kuma
ya kasance mai kyakyawar shaida a cikin wadanda ba
masubi ba, domin kada ya fadi cikin kunya da kuma
tarkon Ibilis. 8 Hakanan kuma Dikinoni su kasance da
halin mutunci, ba masu magana biyu ba. Bai kamata
su zama mashayan giya ko masu hadama ba. 9 Su
zama masu rikon bayyananniyar gaskiyar bangaskiya
da lamiri mai tsabta. 10 Daidai ne kuma a fara tabbatar
da su, daga nan su fara hidima domin basu da abin
zargi. 11 Hakanan ma mata su zama masu mutunci. Bai
kamata su zama magulmanta ba, amma masu kamewa
da aminci cikin komai. 12 Tilas Dikinoni su zama
masu mata daya daya. Su iya kulawa da 'ya'yansu
da gidajensu. 13 Gama wadanda suka yi hidima da
kyau sun sami tsayawa mai kyau da gabagadi cikin
bangaskiyar da ke cikin Almasihu Yesu. 14 Ina rubuta
maka wadannan abubuwa, da sa zuciya zan zo wurin
ka ba da jimawa ba. 15 Amma idan na yi jinkiri, ina
rubuta maka ne domin ka san yadda za ka gudanar da
al'amuranka a cikin gidan Allah, wato Ikklisiyar Allah
rayyayiya, ginshiki da kuma mai tallafar gaskiya. 16
Babu musu an bayyana cewa ibadarmu ta gaskiya da
girma take: "Ya bayyana kansa cikin jiki, Ruhu ya
baratar da shi, mala'iku suka gan shi, aka yi shelarsa a
cikin al'ummai, aka gaskanta shi a duniya, sa'an nan
aka dauke shi sama cikin daukaka.

4 To Ruhu ya fada a fili cewa, a zamanin karshe
wadansu mutane za su kauce daga bangaskiya, su
mai da hankalin su ga ruhohi masu rudi, da koyarwar
aljannu, 2 cikin karya da munafunci. Lamirinsu zai
yi kanta. 3 Za su haramta aure da karbar abincin
da Allah ya halitta, domin su raba da godiya a
cikin wadanda suka bada gaskiya suka kuma san
gaskiyar. 4 Gama duk abin da Allah ya halitta yana
da kyau. Domin duk abin da muka karba da godiya,
bai kamata mu ki shi ba. 5 Gama an tsarkake shi ta
wurin maganar Allah da addu'a. 6 Idan ka tuna wa
'yan'uwa wadannan abubuwa za ka zama bawan kirki
na Almasihu. Domin ana gina ka ne ta wurin maganar
bangaskiya da kuma kyakkyawar koyarwa wadda ka
bi. 7 Amma ka guji labaran almara wadanda tsofaffin
mata ke so. Maimakon haka sai ka hori kanka cikin
bin Allah. 8 Domin horon jiki ya na da amfani kadan.
Amma horon kai cikin bin Allah yana da amfani ga
dukkan abubuwa. Gama a cikinsa akwai alkawari
domin wannan rayuwar da kuma rayuwa mai zuwa. 9
Maganan nan amintacciyace ta isa a karbe ta dungum.
10 Dalilin da ya sa kenan mu ke aiki tukuru. Domin
muna sa bege ga Allah mai rai, mai ceton dukkan
mutane, musamman masu ba da gaskiya. 11 Ka yi
shela ka kuma koyar da wadannan abubuwa. 12 Kada
ka yarda kowa ya rena kuruciyarka. Maimakon haka,
ka zama abin koyi ga dukkan masubi: a furci, hali,
kauna, aminci da kuma tsarki. 13 Har sai na zo, ka
himmatu da yin karatu, da wa'azi, da kuma koyarwa.
14 Kada ka yi sakaci da baiwar da ka ke da ita wadda
aka baka ta wurin anabci sa'ad da dattawa suka dibiya
maka hannayensu. 15 Ka kula da wadannan abubuwa.
Ka himmatu a cikinsu. Domin ci gabanka ya zama
sananne a idanun kowa. 16 Ka kula da kanka da kuma
koyawarka. Ci gaba a cikinsu. Domin ta yin haka ne za
ka ceci kanka da masu sauraronka.

5 Kada ka tsauta wa dattijo. Sai dai ka gargade shi
kamar mahaifi. Ka gargadi samari kamar 'yan'uwa.
2 Gargadi dattawa mata kamar iyaye mata, 'yan mata
kamar 'yan'uwa mata cikin dukkan tsarki. 3 Ka
girmama gwamraye, gwamraye na gaske. 4 Amma
gwamruwar da take da 'ya'ya ko jikoki, bari su fara
nuna bangirma cikin danginsu. Bari su sakawa iya-
yensu, domin Allah yana jin dadin haka. 5 Amma
gwamruwa ta gaske da ke ita kadai, ta kafa begenta
ga Allah. Kullum tana tsananta yin roke-roke da
addu'o'i dare da rana. 6 Amma, mace mai son zaman
annashuwa ta riga ta mutu, ko da shike tana raye. 7
Kuma ka yi wa'azin wadannan al'amura donsu zama
marasa abin zargi. 8 Amma idan mutum bai iya biyan
bukatun 'yan'uwansa ba, musamman iyalin gidansa,
ya musunci bangaskiya, kuma gara marar bi da shi. 9
Bari a lisafta mace gwamruwa idan ba ta kasa shekara
sittin ba, matar miji daya. 10 A san ta da kyawawan
ayyuka, ko ta kula da 'ya'yanta, ko tana mai karbar
baki, ko mai wanke kafafun masubi, ko mai taimakon
wadanda ake tsanantawa, mai naciya ga kowanne
kyakkyawan aiki. 11 Amma game da gwamraye masu
kuruciya, kada a sa su cikin lissafi. Domin idan suka
fada cikin sha'awoyin jiki da ke gaba da Almasihu,

sukan so su yi aure. 12 Ta wannan hanya ce sun tara
wa kansu tsarguwa saboda sun tada alkawarinsu na
fari. 13 Sun saba da halin ragwanci, suna yawo gida
gida. Ba zama raggwaye kawai su ka yi ba. Amma sun
zama magulmata, masu shishshigi, masu karambani.
Suna fadin abin da bai dace ba. 14 Saboda haka ina so
gwamraye masu kuruciya su yi aure, su haifi 'ya'ya, su
kula da gida, domin kada a ba magabci zarafin zargin
mu ga aikata mugunta. 15 Domin wadansu sun rigaya
sun kauce zuwa ga bin shaidan. 16 Idan wata mace mai
bada gaskiya tana da gwamraye, bari ta taimakesu,
don kada a nawaita wa Ikilisiya, domin Ikilisiya ta iya
taimakon gwamraye na gaske. 17 Dattawa wadanda
suke mulki da kyau sun cancanci girmamawa ninki
biyu, musamman wadanda suke aiki da kalma da kuma
koyarwa. 18 Gama nassi ya ce, "Kada a sa takunkumi a
bakin takarkari lokacin da yake sussukar hatsi," kuma
"Ma'aikaci ya cancanci a biya shi hakinsa." 19 Kada ka
karbi zargi game da dattijo sai shaidu sun kai biyu
ko uku. 20 Ka tsauta wa masu zunubi gaban kowa
domin sauran su ji tsoro. 21 Na umarce ka a gaban
Allah, da Almasihu Yesu, da zababbun mala'iku ka
kiyaye ka'idodin nan ban da hassada kuma kada ka
yi komai da nuna bambanci. 22 Kada ka yi garajen
dibiya wa kowa hannuwa. Kada ka yi tarayya cikin
zunuban wani. Ka tsare kanka da tsabta. 23 Kada ka ci
gaba da shan ruwa. Amma, maimakon haka ka sha
ruwan inabi kadan saboda cikinka da yawan rashin
lafiyarka. 24 Zunuban wadansu mutane a bayyane
suke, sun yi gaba da su cikin hukunci. Amma wadansu
zunubansu na bin baya. 25 Haka kuma, wadansu
kyawawan ayyukansu a bayyane suke, amma wadan
sun ma ba su boyuwa.

6 Bari duk wadanda ke bayi a karkashin karkiya su
ga iyayengijinsu sun cancanci dukan daraja. Su yi
haka domin kada a sabawa sunan Allah da koyarwarsa.
2 Bayin da suke da iyayengiji da ke masu ba da gaskiya
kada su rena su saboda su 'yan'uwa ne. A maimakon
haka, su yi masu hidima da kwazo. Gama iyayengijin
da suke cin ribar aikinsu masu bi ne, kaunattatu kuma.
Ka koyar ka kuma bayyana wadannan abubuwa. 3
Idan ya kasance wani na koyar da wani abu dabam
bai kuma yarda da amintaciyar koyarwa ba, wato
maganar Ubangijinmu Yesu Almasihu. Alal misali ba
su aminice da koyarwa da ke kai ga Allahntaka ba. 4
Wannan mutum mai girman kai ne, kuma bai san
komai ba. A maimakon haka, yana da matukar jayayya
da gardama game da kalmomi. Wadannan kalmomi
na kawo kishi, da husuma, da zage-zage, da miyagun
zace-zace, da 5 yawan rashin jituwa tsakanin mutane
masu rubabbun hankula. Sun bijire wa gaskiya. Suna
tunani cewa ibada hanya ce ta yin arziki." Ka zame
daga wadannan abubuwa. 6 Yanzu bin Allah tare da
dangana babbar riba ce. 7 Gama ba mu kawo komai a
duniya ba, ba zamu iya fita cikinta da komai ba. 8
A maimakon haka, mu dangana da abinci da kuma
sutura. 9 To wadanda ke son zama mawadata su
kan fada cikin jaraba, cikin tarko. Suna fadawa cikin
abubuwan wauta da sha'awoyi masu illa da kowanne
abu da ke sa mutane su dulmaya cikin lallacewa da
hallaka. 10 Gama son kudi shine tushen kowacce
irin mugunta. Wadansu mutane garin neman kudi
sun kauce daga bangaskiya, sun kuma jawowa kansu
bakin ciki mai yawa. 11 Amma kai, mutumin Allah, ka
guji wadannan abubuwa, ka bi adalci, ibada, aminci,
kauna, jimiri, da tawali'u. 12 Ka yi fama, fama mai
kyau na bangaskiya. Ka kama rai madawami da aka
kira ka gare shi. A kan wannan ne ka ba da shaida
a gaban shaidu masu yawa game da abin da ke da
kyau. (aiōnios g166) 13 Ina ba ka wannan umarni a gaban
Allah wanda ke rayar da dukan abubuwa, da gaban
Almasihu Yesu, wanda ya fadi abin da ke gaskiya
ga Bilatus Babunti. 14 Ka bi doka daidai, babu abin
zargi har bayanuwar Ubangijinmu Yesu Almasihu. 15
Allah zai nuna bayyanuwarsa a daidai lokaci- Allah,
mai albarka, Makadaicin iko, Sarkin da ke sarauta,
Ubangiji mai mulki. 16 Shine kadai marar mutuwa,
mai zama cikin hasken da ba ya kusantuwa. Ba wanda
ke ganinsa, ko ya iya hango shi. Girma ya tabbata a
gare shi da kuma madawwamin iko. Amin. (aiōnios g166)
17 Ka gaya wa masu dukiya a cikin wannan duniya
kada su daga kai, kada su sa bege ga arziki mara
dawwama. Maimamakon haka, su sa begensu ga Allah
wanda ke ba mu wadatar gaske domin jin dadin mu.
(aiōn g165) 18 Gaya masu su yi nagarta su arzurta a
ayyuka nagari, su zama masu bayarwa hannu sake. 19
Ta haka za su ajiye wa kansu harsashi mai kyau kan
abin da ke zuwa domin su amshi rayuwa ta kwarai. 20
Timoti, ka kare abin da aka ba ka. Ka nisanci maganar
wauta da gardamomin da ke sabawa juna wanda
ake kira ilimi a karyace. 21 Wadansu mutane suna
shelar wadannan abubuwa, don haka sun kauce wa
bangaskiyar. Bari alheri ya kasance tare da kai.

# 2 Timoti

1 Bulus, manzon Almasihu Yesu ta wurin nufin Allah,
bisa ga alkawarin rai da ke cikin Almasihu Yesu, 2
zuwa ga Timoti, kaunataccen da: Alheri, jinkai, da
salama daga Allah Uba da Almasihu Yesu Ubangijinmu.
3 Na gode wa Allah, wanda na ke bautawa tun daga
kakannina, da lamiri mai tsabta, sa'adda na ke tuna
wa da kai cikin addu'o'ina koyaushe (dare da rana).
4 Sa'adda na tuna da hawayenka, na yi marmarin
ganinka, saboda in cika da farin ciki. 5 An tunashshe
ni game da sahihiyar bangaskiyarka, wadda ta samo
asali daga kakarka Loyis da mahaifiyarka Afiniki.
Na kuma tabbata ta na zaune a cikinka. 6 Wannan
shine dalilin da ni ke tunashshe ka cewa ka sake rura
baiwar Allah da ke cikinka wadda ka samu sa'adda na
dibiya maka hannuwana. 7 Domin Allah bai ba mu
ruhun tsoro ba, amma na iko da kauna da kamun
kai. 8 Saboda haka kada ka ji kunyar shaida ga me da
Ubangijinmu, ko ni, Bulus, daurarrensa. Maimakon
haka, ka zama a shirye ka sha wahala domin bishara
bisa ga ikon Allah. 9 Allah ne ya cecemu kuma ya
kira mu da kira mai tsarki. Ya yi wannan, ba ta wurin
ayyukanmu ba, amma ta wurin shirinsa da alherinsa.
Ya ba mu wadannan abubuwan a cikin Almasihu
Yesu kafin farkon zamanai. (aiōnios g166) 10 Amma
yanzu an bayyana ceton Allah ta wurin bayyanuwar
mai cetonmu Almasihu Yesu. Almasihu ne ya kawo
karshen mutuwa ya kuma kawo rai marar karshe
da ya bayyana ta wurin bishara. 11 Domin wannan,
an zabe ni mai wa'azi, manzo da mallami zuwa ga
al'ummai. 12 Domin wannan dalili na ke shan wahalar
wadannan abubuwa. Amma ban ji kunya ba, domin na
san shi, wanda na gaskanta. Na sakankance zai iya
adana abinda na mika masa har zuwa ranan nan. 13
Ka adana misalin amintattun sakwanni da ka ji daga
gare ni, ta wurin bangaskiya da kauna da ke cikin
Almasihu Yesu. 14 Abu mai kyau da Allah ya danka
maka, ka tsare shi ta wurin Ruhu Mai Tsarki, da ke
zaune a cikinmu. 15 Ka dai sani, dukkan wadanda su
ke zama a Asiya sun juya mani baya. A cikin kungiyar
akwai Fijalas da Harmajanas. 16 Bari Ubangiji ya yi wa
iyalin Onisifaras jinkai, domin ya na yawan yi mani
hidima, kuma ba ya jin kunyar sarkata. 17 Maimakon
haka, sa'adda ya ke a Roma, ya neme ni da kokarin
gaske, ya kuma same ni. 18 Bari Ubangiji ya sa, ya sami
jinkai daga gare shi a wannan rana. Dukkan hanyoyin
da ya taimake ni a kasar Afisa, kun sani sarai.

2 Domin wannan kai, dana, ka karfafa cikin alherin
da ke cikin Almasihu Yesu. 2 Abubuwan da ka ji
daga gare ni a bainar jama'a masu yawa, ka danka su
ga mutane masu aminci da za su iya koya wa wadansu
kuma. 3 Ka daure shan tsanani tare da ni, kamar
amintaccen sojan Almasihu Yesu. 4 Ba bu sojan da
zai yi bauta yayin da ya nannade kansa da al'amuran
wannan rayuwar, domin ya gamshi shugabansa. 5
Hakanan, idan wani yana gasa a matsayin dan wasa,
ba zai sami rawani ba tukuna har sai in ya karasa
tseren bisa ga ka'idodin gasar. 6 Wajibi ne manomi
mai kwazon aiki ya fara karbar amfanin gonarsa. 7 Ka
yi tunani game da abin da na ke gaya maka, gama
Ubangiji zai ba ka ganewa a cikin komai. 8 Ka tuna da
Yesu Almasihu, daga zuriyar Dauda, wanda a ka tayar
daga matattu. Bisa ga wa'azin bisharata, 9 wanda na
ke shan wahala har ya kai ga dauri kamar mai laifi.
Amma maganar Allah ba a daure ta ba. 10 Saboda
haka na jure wa dukkan abubuwa domin wadanda
aka zaba, saboda su ma su sami ceton da ke cikin
Almasihu Yesu, da daukaka madawwamiya. (aiōnios
g166) 11 Wannan magana tabbatacciya ce: "Idan mun
mutu tare da shi, za mu kuma rayu tare da shi. 12 Idan
mun jure, zamu kuma yi mulki tare da shi. Idan mun
yi musun sa, shi ma zai yi musun mu. 13 Idan mun
zama marasa aminci, shi mai aminci ne koyaushe,
domin shi ba zai yiwu ya musunta kansa ba." 14 Ka yi
ta tuna masu da wadannan abubuwan. Ka yi masu
kashedi a gaban Allah kada su yi ta dauki ba dadi
game da kalmomi. Saboda wannan bai da wani amfani.
Domin wannan zai halakar da ma su sauraro. 15 Ka yi
iyakacin kokarika domin ka mika kanka ma'aikacin
Allah wanda aka tabbatar, wanda babu dalilin kunya a
gareshi. Wanda ya ke koyar da kalmar gaskiya daidai.
16 Ka guje wa masu maganar sabo, wanda ya kan kara
kaiwa ga rashin bin Allah. 17 Maganarsu za ta yadu
kamar ciwon daji. Daga cikinsu akwai Himinayus da
Filitus. 18 Wadannan mutanen sun kauce wa gaskiya.
Sun fadi cewa an rigaya an yi tashin matattu. Suka
birkitar da bangaskiyar wadansu. 19 Duk da haka,
ginshikin Allah ya tabbata. Ya na da wannan hatimi:
"Ubangiji ya san wadanda ke nasa," Kuma "Duk mai
kira bisa ga sunan Ubangiji dole ya rabu da rashin
adalci." 20 A gida mai wadata, ba kayayyaki na zinariya

da azurfa ba ne kawai. Haka kuma akwai kayayyaki
na itace da yunbu. Wadansu domin aikin mai daraja,
wadansu kuma ga aiki mara daraja. 21 Idan wani ya
tsarkake kansa daga rashin daraja, shi kayan aiki ne
mai daraja. An kebe shi, abin aiki domin mai gidan,
kuma a shirye domin kowanne aiki mai kyau. 22
Ka guje wa sha'awoyi na kuruciya, ka nemi adalci,
bangaskiya, kauna da salama da wadanda suke kira
ga sunan Ubangiji daga zuciya mai tsabta. 23 Amma
ka ki tambayoyi na wauta da jahilci. Ka sani sukan
haifar da gardandami. 24 Tilas bawan Ubangiji ya
guje wa jayayya. A maimakon haka dole ya zama mai
tawali'u ga kowa, mai iya koyarwa, kuma mai hakuri.
25 Dole ne ya koyarwa mutane da su ke jayayya da shi
a cikin tawali'u. Watakila Allah ya ba su ikon tuba
domin sanin gaskiyar. 26 Suna iya sake dawowa cikin
hankalinsu kuma su bar tarkon Ibilis, bayan da ya
cafke su domin nufinsa.

**3** Amma ka san da wannan: a cikin kwanakin karshe
za a yi lokuta masu matsananciyar wahala. 2 Gama
mutane za su zama masu son kansu, masu son kudi,
masu Kumburi, da girman kai, masu sabo, marasa
biyayya ga iyaye, marasa godiya, da kuma marasa
tsarki. 3 Za su kasance marasa dabi'a, wadanda basu
son jituwa da kowa, masu tsegumi, marasa kamun
kai, 'yan tawaye, marasa kaunar nagarta. 4 Za su
zama masu zagon kasa, taurin kai, masu takama, da
masu kaunar anishuwa fiye da kaunar Allah. 5 Za su
kasance da siffar ibada amma za su musunci ikonta.
Ka juya daga wadannan mutanen. 6 A cikinsu akwai
wadanda suke shiga gidaje suna yaudarar mataye
marasa hikima. Wadannan ne mataye wadanda suke
cike da zunubi, kuma sun kauce hanya sabili da
sha'awoyi dabam daban. 7 Wadannan matayen suna ta
koyo, amma ba za su taba kai wa ga sanin gaskiya ba.
8 Kamar yadda Yannisu da Yambrisu suka yi jayayya
da Musa. Haka nan wadannan malaman karya kuma
suke yin tsayayya da gaskiya. Mutane ne lalatattu a
zuciya, marasa sahihiyar bangaskiya. 9 Amma ba za
su yi nisa ba. Domin wautarsu za ta bayyana a fili ga
kowa, kamar wadannan mutane. 10 Amma kai, ka bi
koyarwata, da dabi'ata, nufe nufena, da bangaskiyata,
da jimriyata, da kaunata, da hakurina, 11 da yawan
kuncina, da wahalolina, da duk abubuwan da suka
faru da ni a Antakiya, da Ikoniya da kuma Listra. Na
jure a cikin kuncina. Amma a cikinsu dukka, Ubangiji
ya cece ni. 12 Duk wadanda su ke so su yi rayuwa
ta ibada a cikin Almasihu Yesu za su sha tsanani.
13 Miyagun mutane da masu hila za su yi ta kara
lalacewa. Za su badda wasu. Su da kansu ma sun
bijire. 14 Amma kai, ka ci gaba da abubuwan da ka
koya kuma ka gaskata da zuciya daya. Ka san daga
wurin wanda ka koya. 15 Ka san da cewa, tun kana
dan karamin yaro ka san wadannan littattafai masu
tsarki. Wadannan suna iya mai da kai mai hikima
domin ceto ta wurin bangaskiya a cikin Almasihu
Yesu. 16 Dukkan Nassi hurarre ne daga Allah. Yana
da amfani domin koyarwa, domin tsautawa, domin
gyara, kuma domin horarwa cikin adalci. 17 Wannan
domin mutumin Allah ya zama cikakke ne, shiryayye
domin dukkan ayyukan nagarta.

**4** Ina bada wannan umarni a gaban Allah da Yesu
Almasihu, wanda zai yi wa rayayyu da matattu
shari'a, kuma saboda bayyanuwarsa da mulkinsa: 2
Ka yi wa'azin Kalma. Ka himmantu a kai ko da zarafi
ko ba zarafi. Ka tsautar, ka kwabar, ka gargadar, da
dukan hakuri da koyarwa. 3 Gama lokaci na zuwa
wanda mutane ba za su jure wa koyarwar kirki ba.
Maimakon haka, zasu tattara wa kansu malamai bisa
ga sha'awowin zuciyarsu. Za su rika fada masu abin
da kunnuwansu ke so. 4 Za su juya kunnuwansu
daga koyarwar gaskiya, za su koma wa tatsunniyoyi
na banza. 5 Amma kai, sai ka natsu a cikin dukan
abubuwa. Ka jure wa wahala; ka yi aikin mai bishara,
ka cika hidimarka. 6 Gama ana-tsiyaye ni. Lokacin
yin kaurata yayi. 7 Na yi tsere na gaskiya; na kuma
kammala tseren; na rike bangaskiya. 8 An adana mani
rawani na adalci, wanda Ubangiji, alkali mai adalci,
zai ba ni a ranan nan. Ba ni kadai ba, amma kuma
ga dukkan wadanda suke kaunar zuwansa. 9 Ka yi
iyakacin kokarinka ka zo wurina da sauri. 10 Domin
Dimas ya yashe ni. Ya kaunaci wannan duniyar, ya tafi
Tassalonika, Kariskis ya tafi Galatiya, Titus kuma ya
tafi Dalmatiya. (aiōn g165) 11 Luka ne kadai yake tare da
ni. Ka nemo Markus ka zo tare da shi domin yana da
amfani a gareni a cikin aikin. 12 Na aiki Tikikus zuwa
Afisus. 13 Ka kawo mani mayafin da na bari a Taruwasa
wurin Karbus, idan za ka zo ka taho da shi, duk da
littatafan nan, musanman takardun nan. 14 Iskandari
makerin dalma ya kulla mani makirci ba kadan ba.
Ubangiji zai biya shi gwargwadon ayyukansa. 15 Kai
ma ka yi hankali da shi, domin yana tsayyaya da

maganganunmu sosai. 16 Da farkon kariyar kaina,
babu wanda ya goyi bayana. Maimakon haka kowa
ya guje ni. Bana so dai a lissafta wannan a kansu. 17
Amma Ubangiji ya kasance tare da ni, ya kuma karfafa
ni, yadda ta wurina, shelar ta sami cika da kyau,
domin dukan al'ummai su ji. An kwato ni daga bakin
zaki. 18 Allah zai kubutar ni daga dukan ayyukan
mugunta, ya kuma cece ni domin mulkinsa na sama.
Daukaka ta tabatta a gareshi har abada abadin. Amin.
(aiōn g165) 19 Ka gayar da Briskilla, da Akila, da gidan
Onisifurus. 20 Arastus ya nan zaune a Korinti, amma
na bar Turufimus ya na zazzabi a Militus. 21 Ka yi
iyakar kokarinka, ka zo kamin hunturu. Yubulus yana
gayar da kai, haka ma Budis da Linus da Kalafidiya da
dukan 'yan'uwa. 22 Bari Ubangiji ya kasance tare da
ruhunka. Bari Alheri ya kasance da kai.

# Titus

1 Bulus, bawan Allah, kuma manzon Yesu Almasihu,
ta wurin bangaskiyar zababbun mutanen Allah da
sanin gaskiya da ta yadda da allahntaka. 2 Wadannan
na cikin begen rai marar matuka wanda Allah, wanda
babu karya a cikinsa, ya alkawarta kafin dukkan
lokatan zamanai. (aiōnios g166) 3 A daidai lokaci, ya
bayyana maganarsa ta wurin sakonsa da ya damka
mani in shelar. Zan yi wannan ta wurin umarnin
Allah mai ceton mu. 4 Zuwa ga Titus, da' na gaske a
cikin bangaskiyarmu. Alheri, jinkai da salama daga
wurin Allah Uba da Almasihu Yesu mai ceton mu.
5 Sabili da wannan ne na bar ka a Karita domin ka
daidaita abubuwan da basu cika ba, ka kuma nada
dattibai a dukan birane kamar yadda na umarceka.
6 Dole ne dattijo ya zama marar abin zargi, mijin
mace daya, da amintattun 'ya'ya wadanda babu wani
zargi na mugunta ko rashin kamun kai a kansu. 7
Wajibi ne shugaban Ikklisiya, a matsayin sa na mai
kulla da haikalin Allah, ya zama marar aibi. Kada ya
zama mai surutu ko rashin hakuri. Kada ya zama mai
saurin fushi, ko mashayi, ko mai hayaniya, ko mai
handama. 8 Maimakon haka, ya zama mai karbar
baki, abokin abinda ke mai kyau. Dole ne ya zama mai
hankali, adali, cike da allahntaka, da kuma kamun kai.
9 Ya zama mai rike amintaccen sakon da aka koyar
da karfi, yadda zai iya karfafa wasu da koyarwa mai
kyau ya kuma yi wa wadanda suke hamayya da shi
gyara. 10 Domin akwai kangararrun mutane dayawa,
musamman masu kaciya. Maganganunsu na banza ne.
Suna yaudara kuma suna badda mutane. 11 Wajibi ne
mu hana su. Suna koyar da abinda bai kamata su koyar
ba saboda makunyaciyar riba suna kuma rusar da
iyalai dungum. 12 Daya daga cikinsu, kuma mai hikima
ne daga cikinsu, yace, “Kirawa manyan makaryata
ne, lalatattu kuma miyagun dabbobi, masu kyiuya
da zarin cin abinci.” 13 Wannan magana gaskiya
ne, ka yi masu gyara da tsanani yadda zasu kafu
a cikin bangaskiya. 14 Kada ka mai da hankalin ka
ga tatsunniyoyi na Yahudawa ko dokokin mutane
wadanda sun sauya gaskiya. 15 Ga wadanda suke da
tsarki, komai mai tsarki ne. Amma wadanda suke
marasa tsarki da rashin bangaskiya, komai marar
tsarki ne. Domin zuciyarsu da lamirinsu sun gurbata.
16 Suna cewa sun san Allah, amma sun musanta shi ta
wurin ayyukansu. Sun zama abin kyama da marasa
biyayya. Ba za a iya tabbaatar dasu ba akan wani aiki
maikyau.

2 Amma kai, ka fadi abinda yayi daidai da amintaccen
umarni. 2 Dole tsofaffin mazaje su zama masu
kamun kai, masu daraja kansu, masu-hankali, masu
aminci cikin bangaskiya, cikin kauna da jurewa. 3
Haka ma tsofaffin mataye su kame kansu da girma,
ba magulmata ba. Kada su zama bayi wajen yawan
shan ruwan inabi. Su koyar da abubuwa masu kyau
4 domin su koyar da kananan mataye da hikima su
kaunaci mazajensu da 'ya'yansu. 5 Su horar dasu
su zama masu hikima da tsabtar zuci, masu tsaron
gidajensu, kuma masu biyayya da mazajensu. Suyi
wadannan abubuwa saboda kada maganar Allah ta
sami zargi. 6 Ta haka kuma, ka karfafa samari, su
zama masu hankali. 7 A kowanne fanni, ka mayar da
kan ka abin koyi a cikin kyawawan ayyuka; idan kayi
koyarwa, ka nuna mutunci da martaba. 8 Ka bada
sako lafiyayye marar abin zargi, yadda masu hamayya
da maganar Allah zasu ji kunya, domin rashin samun
mugun abin fadi akan mu. 9 Bayi suyi biyayya ga
iyayengijin su a cikin komai. Su faranta masu rai, ba
suyi gardama dasu ba. 10 Kada suyi sata. Maimakon
haka, sai su nuna dukan bangaskiya mai kyau, domin
suyi wa koyarwarmu game da Allah mai cetonmu
kwalliya a cikin dukan komai. 11 Domin alherin Allah
ya bayyana ga dukan mutane. 12 Yana koya mana
mu musanci miyagun ayyuka, da sha'awoyin duniya.
Yana horar damu muyi zama cikin hankali, da adalci
a cikin hanyar allahntaka a wannan zamani (aiōn g165)
13 yayin da muke cigaba da jiran karba albarkataccen
begenmu, wato bayyanuwar daukakar Ubangiji Allah
da kuma mai cetonmu Yesu Almasihu. 14 Yesu ya
bada kansa domin mu, domin ya cece mu daga rashin
kiyaye doka ya mai damu masu tsarki, domin sa,
mutane na musamman wadanda suke da marmarin
aikata kyawawan ayyuka. 15 Ka yi magana da karfi ka
karfafawa wadannan abubuwa. Ka yi gyara da dukan
iko. Kada ka bar wani ya raina ka.

3 Ka tuna masu su zama masu sadaukar da kai ga
masu mulki da masu iko, suyi masu biyayya, su
zama a shirye domin kowane kyakkyawan aiki. 2 Ka
tuna masu kada su zagi kowa, su gujiwa gardama, su
bar mutane su bi hanyarsu, su kuma nuna tawali'u
ga dukan mutane. 3 Domin a da, mu da kan mu
marasa tunani ne kuma masu rashin biyayya. Mun

kauce hanya muka zama bayi ga sha'awoyin duniya
da annashuwa. Mun yi zama a cikin mugunta da kishi.
Mu lalatattu ne kuma muna kiyyaya da junanmu. 4
Amma da jinkan Allah mai ceton mu da kaunarsa
ga 'yan Adam ta bayyana, 5 ba saboda wani aikin
adalci da muka yi ba, amma sabili da jinkan sa ne ya
cece mu. Ya cece mu ta wurin wankewar sabuwar
haihuwa da sabuntuwar Ruhu Mai Tsarki. 6 Allah
ya zubo mana Ruhu Mai Tsarki a wadace ta wurin
Yesu Almasihu mai cetonmu. 7 Ya yi wannan saboda,
bayan mun samu 'yantarwa ta wurin alherinsa, za
mu zama magada a cikin begen rai na har abada.
(aiōnios g166) 8 Wannan amintaccen sako ne. Ina son
kayi magana gabagadi game da wadannan abubuwa,
yadda dukan wadanda suka bada gaskiya ga Allah za
suyi kudirin yin kyawawan ayyuka da Allah ya mika
masu. Waddannan abubuwa masu kyau ne da kuma
riba ga dukan mutane. 9 Amma ka guji gardandami
na wofi, da lissafin asali, da husuma da jayayya game
da dokoki. Wadannan abubuwa basu da amfani kuma
marasa riba. 10 Ka ki duk wani dake kawo tsattsaguwa
a tsakaninku, bayan ka tsauta masa sau daya ko biyu,
11 ka kuma sani cewa wannan mutumin ya kauce
daga hanyar gaskiya, yana zunubi kuma ya kayar da
kansa. 12 Sa'adda na aiki Artimas da Tikikus zuwa
wurin ka, kayi hanzari ka same ni a Nikobolis, a can
na yi shirin kasancewa a lokacin hunturu. 13 Kayi
hanzari ka aiko Zinas wanda shi gwani ne a harkar
shari'a, da Afolos ta yadda ba zasu rasa komai ba. 14
Ya kamata Jama'armu su koyi yadda zasu yi ayyuka
masu kyau da zasu biya bukatu na gaggawa yadda ba
za suyi zaman banza ba. 15 Dukan wadanda suke tare
da ni suna gaishe ka. Ka gai da masu kaunar mu a
cikin bangaskiya. Alheri ya kasance tare da dukan ku.

# Filemon

1 Bulus, daurarren Yesu Almasihu, da kuma
dan'uwa Timotawus zuwa ga Filimon, kaunataccen
abokinmu da kuma abokin aikin mu, 2 da Afiya
yar'uwanmu da Arkifus abokin aikin mu a filin daga,
da kuma Ikilisiyar da take taruwa a gidan ka: 3
Alheri da salama su kasance gare ka daga wurin Allah
Ubanmu, da Ubangiji Yesu Almasihu. 4 Kowane lokaci
ina gode wa Allah. Ina ambaton ku cikin addu'oi na. 5
Na ji labarin kauna da bangaskiya da ka ke da ita a
cikin Ubangiji Yesu da dukkan yan'uwa masu bi. 6 Ina
addu'a zumuntar bangaskiyarka ta inganta ga kawo
sanin kowane kyakkyawan abu dake cikin mu a cikin
Almasihu. 7 Na yi farinciki kwarai, na kuma ta'azantu
saboda kaunarka, saboda zukatan masu bi sun kwanta
ta wurin ka, dan'uwa. 8 Saboda haka, ko da ya ke ina
da gabagadi a cikin Almasihu domin in ba ka umarni
ka yi abinda ya kamata ka yi, 9 duk da haka sabo da
kauna, na fi so in roke ka- Ni, Bulus, dattijo, a yanzu
kuma ga ni dan kurkuku domin Almasihu Yesu. 10 Ina
rokon ka saboda da na Onisimus, wanda na zama uba
a gare shi sa'adda nake cikin sarkokina. 11 Domin a da
kam, ba shi da amfani a wurin ka, amma yanzu yana
da amfani a gare ka da kuma a gare ni. 12 Na kuma
aike shi wurinka, shi wanda ya ke a cikin zuciyata
kwarai. 13 Na so da na rike shi a wuri na, domin ya
rika yi mini hidima a madadin ka, a lokacin da ni ke
cikin sarkoki saboda bishara. 14 Amma ba na so in
yi wani abu ba tare da sanin ka ba. Ba ni so nagarin
aikinka ya zama na dole amma daga kyakkyawar nufi.
15 Watakila dalilin da yasa ya rabu da kai na dan lokaci
ke nan, domin ka karbe shi kuma har abada. **(aiōnios
g166)** 16 Daga yanzu ba za ya zama bawa ba kuma,
amma fiye da bawa, wato kaunataccen dan'uwa. Shi
kaunatacce ne musamman a gare ni, har fiye da haka
ma a gare ka, a cikin jiki da kuma cikin Ubangiji.
17 Idan ka maishe ni abokin hidima, ka karbe shi
kamar yadda za ka karbe ni. 18 Idan kuwa ya yi maka
abinda ba daidai ba ko kuwa kana bin sa wani abu, ka
dauka yana wurina. 19 Ni, Bulus, na rubuta wannan
da hannuna: zan biya ka. Ba kuwa cewa sai na gaya
maka cewa ina bin ka bashin kanka ba. 20 I, dan'uwa,
ka yi mani alheri cikin Ubangiji; ka ba zuciyata hutu a
cikin Almasihu. 21 Saboda Ina da tabbaci game da
biyayyarka, na rubuta maka. Na san za ka yi fiye da
abinda na roka. 22 Harwayau, ka shirya mani masauki.
Domin ina fata ta wurin adu'oinku, nan ba da dadewa
ba za a maida ni wurin ku. 23 Efafaras, abokina cikin
Almasihu Yesu a kurkuku yana gaishe ka, 24 haka
ma Markus da Aristarkus, da Dimas, da Luka abokan
aikina. 25 Bari Alherin Ubangiji Yesu Almasihu ya
kasance da Ruhunka. Amin.

# Ibraniyawa

**1** A zamanin da, Allah ya yi wa kakanin kakanninmu
magana ta hanyoyi ma su yawa iri iri, ta bakin
annabawa. 2 Amma a zamanin nan na karshe, ya yi
mana magana ta wurin Dansa, wanda ya sa magajin
kome, wanda ta wurinsa ya halicci duniya. (aiōn g165)
3 Shi ne hasken daukakar Allah, ainihin kamanin
zatinsa. Ya na rike da dukkan abubuwa ta ikon
kalmarsa. Bayan da ya tsarkake zunubanmu, sai ya
zauna a hannun dama na madaukaki a can sama. 4
Ta haka ya ke da fifiko a kan mala'iku, kamar yadda
sunansa da ya gada yake da fifiko nesa a kan nasu. 5
Domin kuwa wanene a cikin mala'iku Allah ya taba
cewa, "Kai Da na ne, yau na zama Uba a gare ka?"
kuma, "Zan kasance Uba a gareshi, shi kuma, zai
kasance Da a gare ni?" 6 Kuma, da Allah ya kawo
magaji a duniya, sai ya ce, "Dukan mala'ikun Allah
su yi masa sujada." 7 A game da mala'iku kuma
sai ya ce, "yakan mai da mala'ikunsa ruhohi, masu
hidimarsa kuma harsunan wuta. 8 A game da Dan,
ya ce "kursiyinka, ya Allah, na har abada abadin ne.
Sandar sarautarka sanda ce ta tsantsar gaskiya. (aiōn
g165) 9 Ka kaunaci aikin adalci, ka ki aikin sabo. Saboda
haka Allah, wato Allahnka, ya shafe ka da man farin
ciki fiye da tsararrakinka." 10 "Tun farko, Ubangiji, kai
ne ka hallici duniya. Sammai kuma aikin hannayenka
ne. 11 Za su hallaka, amma kai madawwami ne. Duk za
su tsufa kamar tufafi. 12 Za ka nade su kamar mayafi,
za su kuma sauya, amma kai kana nan ba sakewa,
Har abada shekarunka ba za su kare ba." 13 Amma
wanene a cikin mala'ikun Allah ya taba cewa, "Zauna
a hannun dama na, sai na sa makiyanka a karkashin
kafafunka?" 14 Ashe, ba dukkan mala'iku bane ruhohi,
wadanda Allah yakan aika, don su yi wa wadanda za
su gaji ceto hidima?

**2** Saboda haka, lalle ne mu kara mai da hankali
musamman da abubuwan da mu ka ji, don kada mu
yi sakaci, su sullube mana. 2 Idan kuwa maganar nan
da aka fada ta bakin mala'iku ta zama tabbatacciya,
har kowanne keta umarni da rashin biyayya, suka
gamu da sakamakonsu wanda ya kamace su, 3 ta kaka
za mu tsira, in mun ki kula da ceto mai girma haka?
Domin Ubangiji da kansa, shi ne ya fara sanar da shi,
wadanda suka saurare shi kuma suka tabbatar mana
da shi. 4 San'nan kuma Allah da kansa ya shaida ta
wasu alamu, da abubuwan al'ajabai, da mu'ajizai iri
iri, da kuma baiwar Ruhu Mai Tsarki dabam dabam da
ya rarraba kamar yadda ya nufa. 5 Ai ba ga mala'iku
ba ne Allah ya sa mulkin duniyar nan da za a yi,
wanda muke zance. 6 Amma wani ya shaida a wani
wuri cewa, 'Mutum ma menene, har da za ka tuna
da shi? Ko dan mutum ma, har da za ka kula da
shi?' 7 Ka sa mutum ya gaza mala'iku; Ka nada shi da
daukaka da girma. Bisa dukkan hallitta. 8 Ka dora shi
a kan dukkan halittarka, ka kuma mallakar da kome
a karkashin sawayensa. Domin Allah ya mallakar
da dukkan abubuwa a karkashinsa. Bai bar kome a
kebe ba. Amma kuwa har a yanzu ba mu ga yana
sarrafa dukkan abubuwa ba tukuna. 9 Amma mun ga
wani wanda dan lokaci aka sa shi ya gaza mala'iku,
shine Yesu, an nada shi da daukaka da girma, saboda
shan wuyarsa ta mutuwa, wanan kuwa duk ta wurin
alherin Allah ne Yesu ya mutu saboda kowa. 10 Saboda
haka, ya dace ga Allah, shi da dukkan abubuwa suka
kasance domin sa, ta gare shi, domin ya kawo 'ya'ya
masu yawa ga samun daukaka. Domin a kammala
cetonsu ta wurin shan wuyarsa. 11 Domin da shi
mai tsarkakewar da kuma wadanda aka tsarkaken,
duk tushensu daya ne. Saboda wanan dalili ne shi
ya sa ba ya jin kunyar kiran su 'ya'uwansa. 12 Da
yace, "zan sanar da sunanka ga ya'uwana, a tsakiyar
taronsu zan yabe ka da waka." 13 Har wa yau, yace,
"Zan dogara a gare shi." Da kuma "Ga ni nan, ni
da 'ya'yan da Allah ya ba ni." 14 Wato tun da yake
'ya'yan Allah duk suna da nama da jini, Yesu ma ya
dauki kamannin haka, ta wurin mutuwa ya hallakar
da mai ikon mutuwa, wato Iblis. 15 Ya kuma 'yanta
duk wadanda tun haihuwarsu suke zaman bauta sabo
da tsoron mutuwa. 16 Don hakika ba mala'iku yake
taimako ba, a'a, zuriyar Ibrahim ne yake taimako. 17
Saboda haka, lalle ne ya zama kamar yan'uwansa ta
kowacce hanya, domin ya zama babban Firist, mai
jinkai, mai aminci kuma na al'amarin Allah, ya kuma
mika hadayar sulhu ta gafarta zunuban jama'a. 18
Tun da yake Yesu ma da kansa ya sha wahala, sa'adda
aka gwada shi, don haka, zai taimaki wadanda ake yi
wa gwaji.

**3** Don haka yanuwana tsarkaka, a bokan kira a
samaniya. Yi la'akari da Yesu. wato Manzo da
babban firist na shaidar bangaskiyarmu. 2 Shi
amintacce ne na Allah, wanda ya bashi hidima, kamar
yadda Musa ya kasance amintacce a gidan Allah. 3

Gama Yesu ya cancanci daukaka mafi girma fiye da
ta Musa. Domin wanda ya gina gida, ya fi gidan nan
daukaka. 4 Gama kowane gida, akwai wanda ya gina
shi, amma mai ginin komai shine Allah. 5 Musa hakika
amintaccen bawa ne a gidan Allah, yana ba da shaidar
abubuwan da za su faru a nan gaba. 6 Amma Almasihu
shi Da ne mai mulki a gidan Allah. Mu ne gidansa idan
mun rike begenmu da dukkan zuciyarmu. 7 Saboda
haka, kamar yadda Ruhu Mai Tsarki ya fadi: ''Yau, Idan
kun ji muryarsa, 8 kada ku taurare zuciyarku kamar
yadda 'ya'yan isra'ila suka yi cikin tawaye a lokacin
gwaji a jeji. 9 A lokacin nan ne kakanninku suka
yi mani tawaye, ta wurin gwada ni, bayan shekara
arba'in suna ganin ayyukana. 10 Saboda haka na yi
bakin ciki da wannan tsarar, sai na ce,' Kullum suna
yawan bijirewa a zukatansu. Basu san tafarkuna ba.'
11 Don haka na yi rantsuwa a cikin fushina, ba za su
shiga cikin hutuna ba." 12 Ku yi hankali 'yan'uwa
kada a tarar da mummunar zuciya marar bangaskiya
a tsakaninku, zuciya wadda ke juyawa daga Allah mai
rai. 13 Maimakon haka, ku karfafa juna a kowacce
rana, muddun muna cikin wannan rana kada wani
cikinku ya taurare zuciyarsa saboda yaudarar zunubi.
14 Gama mun zama abokan aiki da Almasihu, idan
mun rike begenmu cikinsa da karfi, daga farko zuwa
karshe. 15 Game da wannan, an fadi "Yau idan kun
saurari muryarsa, kada ku taurare zuciyarku, kamar a
kwanakin tawaye nan." 16 Su wanene suka ji muryar
Allah suka yi tawaye? Ba wadanda Musa ya yi masu
jagora daga Masar ba ne? 17 Kuma da su wa Allah ya yi
fushi shekara arba'in? Ba da wadanda suka yi zunubi
ba ne, wadanda gawawwakinsu suka warwatsu a jeji?
18 Da su wa Allah ya rantse ba za su shiga hutunsa
ba? In ba wadanda suka yi masa rashin biyayya ba?
19 Mun kuma gani cewa basu iya shiga hutunsa ba
saboda rashin bangaskiyarsu.

4 Saboda haka, sai muyi lura kwarai don kada wani
ya kasa kai ga shiga hutun da aka alkawarta maku
na Allah. 2 Don mun ji albishir game da hutun Allah
kamar yadda aka fada masu. Amma wancan sakon
bai anfana ga wadanda suka ji ba tare da sun bada
gaskiya ga sakon ba. 3 Ai mu, wadanda muka gaskata-
mune zamu shiga wannan hutun, kamar yadda ya ce,
"Yadda na yi rantsuwa cikin fushina, baza su shiga
hutu na ba." Ya fadi hakan, ko da yake ya gama aikin
hallittarsa tun daga farkon duniya. 4 Domin yayi fadi
a wani wuri game da rana ta bakwai, "Allah ya huta a
rana ta bakwai daga dukkan ayyukansa." 5 Ya sake
cewa, "Baza su taba shiga hutu na ba." 6 Saboda haka,
tun da hutun Allah na kebe domin masu su shiga,
kuma tun da Isra'ilawa da yawa wadanda suka ji sakon
nan mai kyau game da hutunsa ba su shiga ba saboda
rashin biyayya, 7 Allah ya sake shirya wata rana da ake
kira, "Yau." Ya sa wannan rana sa'adda yayi magana
ta wurin Dauda, wanda ya ce tun da dadewa da aka
fara fada, "Yau idan kun ji muryarsa, kada ku taurare
zukatanku." 8 Don idan Joshua ya ba su hutu, da Allah
ba zai sake magana a kan wata rana ba. 9 Saboda haka,
akwai hutun asabar kebabbe ga mutanen Allah. 10
Don shi wanda ya shiga hutun Allah shi kansa ma ya
huta daga ayyukansa, kamar yadda Allah yayi da nasa.
11 Saboda haka muyi marmarin shiga wancan hutun,
don kada kowa ya fadi ga irin rashin biyayyar da suka
yi. 12 Maganar Allah kuwa rayayyiyace, kuma mai ci,
fiye da takobi mai kaifi-biyu. Takan ratsa har tsakanin
rai da ruhu, kuma tana kaiwa bargo. Takan iya bincika
tunanin zuciya da manufarta. 13 Babu halittaccen abu
da ke boye a idon Allah. Sai dai, kome a sarari yake,
kuma a bayyane yake a idonsa wanda lallai ne zamu
bada lissafin kanmu a gare shi. 14 Da yake muna da
babban firist wanda ya ratsa sammai, Yesu Dan Allah,
sai mu riki bangaskiyarmu da karfi. 15 Domin babban
firist namu ba marar tausayi ga kasawarmu bane,
amma wanda aka jarraba ne ta ko wanne hali irin
yadda aka yi mana, sai dai ba'a same shi da zunubi ba.
16 Sai mu zo wurin kursiyin alheri gabagadi, domin a
yi mana jinkai mu kuwa sami alherin da zai taimake
mu a lokacin bukata.

5 Kowanne babban firist, da yake an zabe shi ne
daga cikin mutane, a kansa shi ya wakilci mutane
ga al'amarin Allah, don ya mika sadakoki da kuma
hadayu domin kawar da zunubai. 2 Yana kuma iya
tafiyar da jahilai da sangartattu a cikin salihanci,
tun da shi ke rarrauna ne shi ta ko'ina. 3 Saboda
haka, wajibi ne ya mika hadayu, ba saboda kawar da
zunuban jama'a kadai ba, har ma da na kansa. 4 Ba
wanda zai kai kansa wannan matsayi mai girma, sai
dai Allah ya yi kiransa ga haka, kamar yadda aka kirayi
Haruna. 5 Haka kuma, Almasihu, ba shi ya daukaka
kansa ya zama Babban firist ba, sai dai wannan ne ya
sa shi, wanda ya ce da shi, "Kai Dana ne; Yau na zama
Uba a gare ka.'' 6 Kamar dai yadda a wani wuri kuma

ya ce, “Kai firist ne na har abada, bisa ga kwatancin
Malkisadak.” (aiōn g165) 7 Almasihu, a lokacin zamansa
a duniya, ya yi addu'o'i da roke-roke, tare da kuka
mai tsanani, har da hawaye, ga wannan da yake da
ikon cetonsa daga mutuwa, aka kuwa saurare shi
saboda tsannin mika kansa. 8 Ko da yake shi Da ne,
ya koyi biyayya ta wurin wuyar da ya sha. 9 Har
ya kai ga kammala, sai ya zama tushe madawwami,
ceto ga dukkan wadanda suke masa biyayya. (aiōnios
g166) 10 Gama Allah yana kiransa Babban firist, bisa ga
kwatancin Malkisadak. 11 Muna da abu da yawa da za
mu fada a game da Yesu, amma zai yi wuyar bayani,
da yake basirarku ta dushe. 12 Ko da yake yanzu kam,
ya kamata ku zama masu koyarwa, duk da haka, ashe,
ba ku wuce wani ya sake koya muku jigajigan farko
na Maganar Allah ba? har ya zamana sai an ba ku
madara ba abinci mai tauri ba? 13 To, duk wanda yake
madara ce abincinsa, bai kware da maganar adalci ba,
kamar jariri yake. 14 Amma abinci mai tauri, ai, na
manya ne, wato wadanda hankalinsu ya horu yau da
kullum, don su rarrabe nagarta da mugunta.

6 Saboda haka, sai mu ci gaba a kan ka'idodin farko
na al'amarin Almasihu, har ya zuwa kammala,
ba wai mu sake koyar da jigajigan nan na tuba da
ibada marar tasiri ba, da na gaskatawa da Allah, 2
da kuma na koyarwa a kan wanke-wanke, da dora
hannu, da tashin matattu, da dawwamammen hukuci.
(aiōnios g166) 3 Za mu kuwa ci gaba in Allah ya yarda.
4 Domin wadanda aka haskaka zukatansu sarai, har
suka dandana baiwar nan Basamaniya, suka kuma
sami rabo na Ruhu Mai Tsarki, 5 har su ka dandana
dadin Maganar Allah, da ikon zamani mai zuwa, (aiōn
g165) 6 sa'an nan kuma suka ridda—ba mai yiwuwa ba
ne a sake jawo su ga tuba, tun da yake sake gicciye
Dan Allah suke yi su da kansu, suka kuma wulakanta
shi a sarari. 7 Kasa ma da take shanye ruwan da ake yi
a kai a kai, take kuma fid da tsire-tsire masu amfani
ga wadanda ake nomanta dominsu, Allah yakan sa
mata albarka. 8 Amma idan tsire-tsirenta kaya ne da
kashin yawo, ba ta da amfani ke nan, tana kuma gab
da la'antarwa, karshenta dai konewa ne. 9 Ko da yake
mun fadi haka, a game da ku kam, ya kaunatattu mun
tabbata kuna abubuwa mafiya kyau na zancen ceto.
10 Gama Allah ba marar adalci ba ne, har da zai ki
kula da aikinku, da kuma kaunar sunansa da kuke yi,
wajen yi wa tsarkaka hidima, har yanzu ma kuna yi.
11 Muna dai bukata kwarai kowannanku ya nuna irin
wannan himma ga yin cikkaken bege, tabbatacce, har
ya zuwa karshe. 12 Don kada ku yi ragwanci, sai dai ku
yi koyi da wadanda suka karbi cikar alkawaran nan, ta
wurin bangaskiyarsu da hakurinsu. 13 Sa'adda Allah
ya yi wa Ibrahim alkawari, da yake ba wani wanda
ya fi shi girma da zai rantse da shi, sai ya rantse
da kansa, 14 Ya ce, “Hakika zan yi maka albarka, in
kuma ribambamya zuriyarka.” 15 Ta haka, Ibrahim
bayan da ya jure da hakuri, ya karbi cikar alkawarin.
16 Hakika mutane sukan rantse da abin da ya fi su.
Rantsuwa kuma ita ce abar da take tabbatarwa da
kowacce magana. 17 Don haka, sa'adda Allah yake
son kara tabbatar wa magadan alkawarin nan dahir,
cewa nufinsa ba mai sakewa ba ne sam, sai ya hada
da rantsuwa, 18 Domin albarkacin abubuwa guda
biyun nan marasa sakewa, masu nuna, cewa ba shi
yiwuwa Allah ya yi karya, mu da muka gudu muka
sami mafaka, mu karfafa kwarai mu riski abin da
muka kafa bege a kai. 19 Muna da bege, kamar yadda
yake ga rai, kafaffe, tabbatacce, shi ne kuma yake
shiga har can ciki bayan labulen. 20 Inda saboda mu
ne Yasu ya riga mu shiga, da yake ya zama Babban
Firist na har abada, kwatancin Malkisadak. (aiōn g165)

7 Wannan ne Malkisadak, sarkin Salem, firist na Allah
Madaukaki, wanda ya gamu da Ibrahim na dawowa
daga yaki da wasu sarakuna ya kuma albarkace shi.
2 Ibrahim ya ba shi ushirin dukkan ganimar da ya
samu. Sunansa,” Malkisadak,” ma'anar itace, “Sarkin
adalci,” haka ma, “sarkin salem,” ma'anar iitace,”
Sarkin salama,” 3 Bashi da uwa bashi da uba, ba shi
da lissafin asalin zuriya, ba shi da farkon rayuwa
ba shi da karshen rai. Shi firist ne na har abada,
kamar Dan Allah. 4 Yanzu fa dubi irin girman wannan
mutum. Kakan kakanninmu Ibrahim ya bada ushira ta
abubuwan da ya samo na ganimar yaki gare shi. 5
Kuma hakika, zuriyar Lawi da suka karbi aikin nan na
firistanci suna da umarni daga shari'ar Allah cewa
su karbi zakka a gun jama'a, wato, daga yan'uwan
su Isra'ilawa, koda shike suma zuriyar Ibrahim ne.
6 Amma Malkisadak, shi da ba zuriyar Lawi ba ne,
ya karbi zakka daga Ibrahim, ya kuma albarkace shi,
shi wanda ya ke da alkawarai. 7 Ba jayayya, karami
shi ke karban albarka daga babba wanda ya girme
shi. 8 A wannan tsarin mutanen da ke karban zakka
wata rana sai ka ga sun mutu, amma a wani kauli

mutumin da ya karbi zakka a wurin Ibrahim, ance,
wanzaje ne har yau. 9 Kuma bisa ka'ida Lawi, wanda
ke karban zakka, shi ma ya bada zakka ga Ibrahim, 10
Saboda kuwa Lawi na cikin tsatson Ibrahim lokacin da
Malkisadak ya gamu da Ibrahim. 11 Yanzu in da mai
yiwuwa ne a sami kammala cikin aikin firistanci na
Lawiyawa (domin ta wurin ta ne aka bada shari'a), to
ina amfanin wani firist ya zo bisa ga ka'ida irin ta
Malkisadak, ba'a kuma ambaci ka'idar Haruna ba?
12 Don kuwa lokacin da aka canza firistanci, shari'a
kuma dole ne a sauya ta. 13 Domin mutumin da aka
fadi wadannan abubuwa a kansa na wata kabila ne,
wadda ba wani mutumin da ya taba yin aiki a kan
bagadi. 14 Wannan a bayyane yake Ubangijinmu ya
zo ne daga zuriyar Yahuza, kabilar da Musa bai taba
anbatonsu game da zancen firistanci ba. 15 Abinda
muke fadi a bayyane yake cewa, idan wani firist
ya taso da kamanin Malkisadak. 16 Wannan sabon
firist, ba firist ne da ya taso bisa ga ka'idar zuriya ta
yan'adam ba, amma ya zama firist ne ta rayuwa mai
iko marar shudewa. 17 Domin a rubuce yake cikin
littafi ga me da shi; “Kai firist ne na har'abada bisa ga
tsari irin na Malkisadak.” (aiōn g165) 18 Domin doka ta
fari an ajiye ta a gefe guda saboda rarrauna ce kuma
marar amfani. 19 Don kuwa shari'a ba ta iya kamalta
kome. Amma fa a kwai bege mai kyau a nan gaba
wanda ta gare shi ne zamu sami iso a gun Allah. 20
Kuma wannan kyakkyawan bege baya faruwa ba tare
da rantsuwa ba, don kuwa su wadancan firistocin
ba su dauki wata rantsuwa ba. 21 Amma Allah yayi
rantsuwa game da Yesu cewa, “Ubangiji ya rantse ba
kuwa zai fasa tunaninsa ba; 'Kai firist ne har'abada.'”
(aiōn g165) 22 Ta wurin haka Yesu ya bada tabbatacce
da kuma ingataccen alkwari. 23 Hakika, mutuwa ta
hana firistoci su yi aiki har'abada. Wannan shi ya sa
akwai firistoci da yawa daya bayan daya. 24 Amma
da shi ke Yesu na rayuwa ne har'abada, aikinsa na
firist ba a musanya shi sam sam. (aiōn g165) 25 Domin
haka kuma yana da cikakken ikon ceton wadanda ke
gusowa ga Allah ta wurinsa, domin kullum a raye ya
ke yana kuma roko dominsu 26 . Domin irin wannan
babban firist shi ne ya dace da mu. Ba shi da zunubi,
marar abin zargi, tsarkakakke, kebabbe daga masu
zunubi, ya na sama da sammai dukka. 27 Ba shi da
bukata, kamar manyan firistoci, da ke mika hadayu
kullum, da farko don zunubin kansu, sa'annan don
zunubin jama'a dukka. Amma Yesu yayi wannan sau
daya tak ba kari don kowa da kowa, yayin da ya mika
kansa. 28 Domin shari'a na nada mutane da ke da
gazawa a matsayin firistoci, amma maganar rantsuwa,
wadda ta zo a bayan shari'a, ta nada Dan, wanda ya ke
cikakke har'abada. (aiōn g165)

8 Yanzu abin da muke kokarin cewa shine: Muna da
babban firist wanda ke zaune a hannun dama na
kursiyi mai martaba dake sammai. 2 Shi kuwa bawa ne
a wannan wuri mai tsarki, haikali na gaskiya wanda
Allah ya shirya ba wani bil'adama ba. 3 Kowanne
babban firist kuwa yana mika bayebaye da hadayu.
Don haka ya kamata a sami abin hadaya. 4 Da a ce
Almasihu yana duniya ba zai zama firist ba ko kadan.
5 Domin a kwai masu mika hadaya bisa ga shari'a.
Suna hidimar misalin abubuwan da suke inuwar sama.
Kamar yadda Allah ya yi wa Musa gargadi yayin
da ya ke shirin gina Alfarwa: ''Duba'' Allah ya ce,
''kayi komai bisa ga salon da aka koya maka a bisa
dutse.” 6 Amma yanzu hidimar da Almasihu ya karba
ta dara tasu dukka, domin kuwa shine matsakancin
muhimmin alkawari, wanda aka kammala a kan
muhimman alkawura. 7 Domin kuwa idan alkawarin
fari ba shi da laifi babu anfanin neman alkawari na
biyu. 8 Da Allah ya sami laifi akan mutane, sai ya ce
''Zan sake sabon alkawari da gidan Isra'ila da kuma
gidan Yahuza. 9 kuma ba zai zama kamar yadda nayi
da kakanninku ba, kamar yadda na rike su a hannu
har Na fidda su daga kasar Masar. Basu kuma ci gaba
da Alkawarina ba, ni kuwa na yi watsi da su,'' inji
Ubangiji. 10 Gama wanna shine alkawarin da zan
yi da gidan Isra'ila bayan wadannan kwanaki, Inji
Ubangiji. Zan sa shari'a ta a bakinsu in kuma rubuta
ta a zuciyarsu, Zan kuma zama Allah a garesu, su
kuma su zama jama'ata. 11 Ba za su kuma koyar da
makwabta ko yan'uwansu cewa, ''ku san Ubangiji''
gama dukkanin su za su san ni, daga karami har zuwa
babba. 12 Zan kuma nuna tausayi ga ayyukan su na
rashin adalci, ba kuma zan kara tunawa da zunubansu
ba. 13 A kan fadin ''sabo'' ya mayar da alkawarin fari
tsoho. Wannan kuma da aka ambata tsoho na shirin
bacewa.

9 To ko da alkawarin farko ma ya na da wurin sujada
da kuma ka'idojin sujada a nan duniya. 2 Domin a
cikin alfarwar akwai daki da aka shirya, daki na waje
wanda ake kira wuri mai tsarki. A wannan wuri akwai
kebabbun fitilu, akwai teburi da kuma gurasa. 3 Kuma

bayan labule na biyun akwai wani daki, wanda ake kira
wuri mafi tsarki. 4 Yana da bagadin zinariya domin
turare. Yana kuma da akwatin alkawarin, wanda aka
lailaye shi gaba daya da zinariya. A cikinsa a kwai
kaskon zinariya dake dauke da manna, da sandar
Haruna wadda tayi toho, da kuma allunan duwatsu
na alkawarin. 5 A sama da akwatin alkawarin akwai
siffofin kerubobi masu daukaka da suke wa marfin
jinkai inuwa, wadanda yanzu ba zamu iya yin bayani
akansu ba daki daki. 6 Bayan an shirya wadannan
abubuwa, firistocin alfarwar sukan shiga daki na
wajen alfarwar akai akai suna aikin hidimominsu. 7
Amma babban firist din ne kadai yake shiga daki na
biyun, sau daya tak a shekara, kuma tilas sai tare da
jinin hadaya domin kansa, da kuma domin laifuffukan
mutane da a kayi ba dagangan ba. 8 Ruhu Mai Tsarki
yana nuna cewar ba'a riga an bayyana hanyar zuwa
wuri mafi Tsarki ba muddin alfarwar nan ta farko
na a tsaye. 9 Wannan ya zama bayani ne game da
lokacin yanzu. Da kyaututtuka da hadayu dukka da
ake mikawa basu iya sun kammala lamirin mai yin
sujadar ba. 10 Abinci ne da abin sha kawai wadanda
aka hada da bukukuwan wanke wanke dabam dabam.
Wadannan duka tsare tsare ne da aka shirya a dinga yi
a zahiri har sai an shirya sabuwar ka'ida. 11 Almasihu
yazo a matsayin babban firist na abubuwa masu
kyau da suka zo, ta wurin alfarwa babba, kammalalla
kuma mafi tsarki wadda ba hannuwan mutane suka
gina ba, wadda ba ta wannan duniyar aka halicce
ta ba. Amma almasihu ya zo a matsayin babban
firist na abubuwa masu kyau da ke zuwa. 12 Ba ta
jinin awaki da 'yan, maruka bane, amma Almasihu
da jininsa ya shiga wuri mafi tsarki sau daya tak
domin kowa dukka ya karbo mana fansa ta har abada.
(aiōnios g166) 13 To idan jinin awaki da na bajimai
da yayyafa tokar karsana bisa wadanda suka bata
tsarkinsu yana tsarkake su ya wanke jikkunansu. 14
To balle kuma jinin Almasihu, wanda ta wurin Ruhu
madawwami ya mika kansa hadaya marar aibi ga
Allah, wanda yake wanke lamirinmu daga matattun
ayyuka domin muyi bautar Allah mai rai? (aiōnios g166)
15 Domin wannan dalili, Almasihu shine magamin
sabon alkawari. Wannan kuwa ya kasance ne domin
anyi mutuwar da ta 'yantar da wadanda ke karkashin
tsohon alkawari daga sakamakon zunubansu, saboda
wadanda Allah ya kira su karbi alkawarin gadonsu
madawwami. (aiōnios g166) 16 Gama duk inda wani
ya rubuta wasiyya ya bari, dole ne a tabbatar da
mutuwar wanda yayi wasiyyar nan. 17 Gama sai inda
akayi mutuwa ake amfani da wasiyya, amma ba ta da
amfani idan wanda ya rubuta ta yana nan da rai. 18
Ko alkawari na farko bai tabbata ba sai tare da jini.
19 Gama bayan Musa ya bada dukkan dokoki da ke
cikin shari'ar ga dukkan mutanen, sai ya dauki jinin
'yan marukan da awakin, tare da ruwa, da jan yadi,
da reshen itacen doddoya mai soso, ya yayyafa bisa
mutanen da kuma littafin dokokin. 20 Daga nan yace,
“Wannan ne jinin alkawarin da Allah ya bayar da
dokoki gareku.” 21 Ta haka kuma, ya yayyafa jinin bisa
alfarwar da dukkan kayayyakin da ke cikinta wanda
ake hidimar firistanci da su. 22 Kuma bisa ga shari'a,
kusan komai da jini ake tsarkake shi. Idan babu zubar
da jini to babu gafarar zunubi. 23 Saboda haka ya zama
tilas wadannan kayayyaki na kwaikwayon abubuwan
dake cikin sama a tsarkake su da hadayar dabbobi.
Duk da haka abubuwa na sama dole a tsarkake su
da hadaya mafi kyau. 24 Domin Almasihu bai shiga
cikin wuri mafi tsarki da aka yi da hannuwa ba,
wanda kwaikwayo ne kawai na abin da ke na gaske.
Maimakon hakan, ya shiga cikin samaniya da kanta,
sa'an nan yaje gaban Allah domin mu. 25 Bai je wurin
don ya mika kansa sau da yawa, kamar yadda firist din
alfarwa yake yi ba, wanda yake shiga wuri mafi tsarki
kowacce shekara da jinin wata dabba. 26 Idan haka
ne, to dole ke nan ya sha wahala akai akai tun farkon
duniya. Amma yanzu sau daya ne tak aka bayyana shi
a karshen zamanai domin ya kauda zunubi ta wurin
mika hadayar kansa. (aiōn g165) 27 Kamar yadda aka
kaddara wa kowa ya mutu sau daya tak, kuma bayan
haka sai shari'a. 28 Haka kuma Almasihu, wanda
aka mika shi sau daya tak domin ya dauke zunuban
mutane da yawa, zai kuma bayyana karo na biyu, ba
domin yin aikin kawar da zunubi ba, amma domin
ceton wadanda suke jiran zuwansa da hakuri.

10 Domin shari'a hoto ce na kyawawan abubuwan
da ke zuwa, ba ainihin siffar wadannan abubuwa
ba. Wadanda ke gusowa kusa da Allah ba za su taba
ingantuwa ta wurin hadayu da firistoci ke mikawa
shekara da shekaru ba. 2 In ba haka ba, ba sai a dena
mika hadayun ba? Bisa ga wannan al'amari, inda
sun tsarkaka sau daya tak da masu sujada ba su san
menene zunubi ba. 3 Amma wadannan hadayun sun
zama matuni ne na zunubi shekara biye da shekara.
4 Domin ba shi yiwuwa jinin bijimai da awakai su

kawar da zunubai. 5 Yayin da Almasihu ya zo duniya,
ya ce, “Ba hadayu da sadakoki kake marmari ba.
Maimakon haka, ka shirya mini jiki domin hadaya. 6
Baka murna domin sadakoki da hadayu na konawa
domin zunubi. 7 Sai na ce, 'Duba, gani na zo in yi
nufinka, kamar yadda aka rubuta akaina.''' 8 Da fari
Yace ''ba hadayu, ko sadakoki, ko kuma hadaya ta
konawa domin zunubi kake bukata ba. Ba ka kuwa jin
dadinsu.'' Wadannan sune hadayun da ake bayarwa
bisa ga shari'a. 9 Sa'annan sai ya ce ''gani na zo domin
in aikata nufinka.” Ya kawar da hidimar farko domin
ya kafa hidima ta biyu. 10 A hidima ta biyu, an kebe
mu ga Allah ta wurin nufinsa ta wurin hadayar jikin
Yesu Almasihu bugu daya ba kari. 11 Haka, kowanne
firist ya ke tsayawa kulliyomi domin ya yi hidima
ga Allah. A kullum yana mika hadayu, iri daya, koda
shike ba za su taba kawar da zunubai ba. 12 A ta
wata hanya kuma, Almasihu ya mika hadaya sau daya
tak domin zunubai har abada, ya zauna a hannun
dama na Allah. 13 Yana jiran har a maida makiyansa
matashin sawayensa. 14 Domin ta wurin hadaya guda
dayan nan ya kammala har abada ga wadanda suka
sadaukar da kansu ga Allah. 15 Kuma Ruhu mai Tsarki
ya shaida mana. Abu na farko yace, 16 “Wannan shi
ne alkawarin da zan yi da su a bayan kwanakin nan,'
inji Ubangiji Zan sa dokokina a cikin zukatansu, kuma
zan rubuta su a lamirinsu. 17 Ba zan sake tunawa
da zunubansu da kurakuransu ba.'' 18 Yanzu fa duk
in da aka sami gafara domin wadannan abubuwa,
babu wata hadaya domin zunubi. 19 Saboda haka,
yan'uwa, ba mu da shakkar shigowa wurin nan mafi
tsarki ta wurin jinin Yesu. 20 Wannan ita ce sabuwar
rayayyar hanya da ya bude mana ta wurin labulen,
wato ta wurin jikinsa. 21 Saboda muna da babban firist
a gidan Allah. 22 Bari mu matso kusa da sahihiyar
zuciya, da kuma cikakken gabagadi cikin bangaskiya,
da zuciyarmu wadda aka tsarkake daga mummunan
tunani, da kuma jikunanmu wankakku da ruwa mai
tsabta. 23 Bari mu rike da karfi shaidar bangaskiyar
begenmu, ba tare da raurawa ba, domin Allahn, da
ya yi alkawari, mai aminci ne. 24 Bari mu kuma yi
lura yadda za mu iza juna ga kauna da ayyuka masu
dacewa. 25 Kada mu fasa zumunci da juna, kamar
yadda wadansu sukan yi. A maimakon haka, bari mu
karfafa juna a kulluyomin, kamar yada kuke ganin
kusantowar ranan nan. 26 Saboda idan mun ci gaba
da zunubin ganganci bayan mun rigaya mun sami
wannan sanin gaskiyar, hadayar irin wannan zunubi
bata samuwa. 27 Maimakon haka, sai fargabar babban
tsoron hukunci, da kuma wuta mai zafi, da zata cinye
makiyan Allah. 28 Dukkan wanda ya ki bin dokar
Musa zai mutu ba tausayi ta wurin shaidu biyu ko
uku. 29 Wanne irin hukunci kuke tsammani ya dace
ga wadanda suka raina Dan Allah, duk wadanda suka
maida jinin alkawarin nan kamar ba tsarkakakke
ba, wanda ta wurin jinin nan ne aka kebe shi ga
Allah- wadanda suka wulakantar da Ruhun alheri? 30
Domin mun san wanda yace, “Ramako nawa ne; Zan
yi sakayya.'' Sa'annan kuma, “Ubangiji zai hukumta
jama'arsa.” 31 Abin tsoro ne a fada cikin hannuwan
Allah mai rai! 32 Amma ku tuna da kwanakin baya,
bayan da ku ka sami haske, yadda kuka jure babban
fama cikin wahala. 33 Aka kunyatar da ku a gaban
jama'a, ta wurin ba'a da cin mutunci, kuna kuma
dandana irin azabar da wadansu suka shiga ciki. 34
Domin kuna da tausayi ga wadanda suke kurkuku, da
farin ciki, kun amince da kwace na dukiyarku da aka
yi, kun mallaki madauwamiyar mallaka mafi kyau.
Dominn kun ji tausayina sa'adda na ke a kurkuku. 35
Don haka kada ku yarda gabagadinku, wanda ke da
babban sakamako. 36 Domin kuna bukatar hakuri don
ku sami abin da Allah ya alkawarta, bayan kun aikata
nufinsa. 37 “Domin a dan karamin lokaci, mai zuwan
nan zai zo ba zai yi jinkiri ba. 38 Adalina kuwa zai
rayu ta wurin bangaskiya. In kuwa ya ja da baya, ba
zan yi farin ciki dashi ba.” 39 Amma mu bama cikin
wadanda suka ja da baya zuwa hallaka. Maimakon
haka, muna cikin wadanda suke da bangaskiya domin
kula da rayukanmu.

11 Bangaskiya ita ce tabbatawar al'muran da muke
begensu. Ita ce tabbatawar al'amuran da idanu
basu gani. 2 Domin ta wurin ta ne kakanninmu suka
sami yardar Allah. 3 Ta wurin ta ne aka hallicci duniya
da umarnin Allah, har ma abubuwan da ake gani ba'a
yi su daga abubuwan da suka kasance ba. (aiōn g165)
4 Ta dalilin bangaskiya ne Habila ya mikawa Allah
hadaya da ta fi dacewa fiye da ta Kayinu. Don haka ne
kuma aka yaba masa akan cewa shi adali ne. Ya sami
yardar Allah sabili da sadakarsa da ya bayar. Don haka
kuma, harwayau Habila yana magana, ko da shike ya
rigaya ya mutu. 5 Ta dalilin bangaskiya aka dauki
Anuhu zuwa sama domin kar ya ga mutuwa. “Ba a
same shi ba kuwa, domin Allah ya dauke shi.” Kamin

a dauke shi an shaida da cewa ya faranta wa Allah
zuciya. 6 Zai yi wuya matuka a faranta wa Allah zuciya
in ba tare da bangaskiya ba. Domin ya kamata dukkan
wanda zai zo ga Allah, tilas ne ya bada gaskiya da
kasancewar sa, kuma shi mai sakamako ne ga dukkan
masu nemansa. 7 Ta dalilin bangaskiya Nuhu, ya karbi
sako daga Allah akan al'amuran da ba'a gani ba, ta
wurin girmamawa da rawar jiki. ya gina jirgin ruwa
domin ya ceci iyalan sa. Dalilin haka kwa, Allah ya
hallakar da duniya, Nuhu kwa ya gaji adalci wadda
ke bisa ga bangaskiya. 8 Ta dalilin bangaskiya ne
Ibrahim, sa'an da aka kira shi, ya yi biyayya sai ya
tafi wurin da zai karba a matsayin gado. Ya kwa fita
bai ma san inda za shi ba. 9 Ta dalilin bangaskiya
kuma ya zauna bare a kasar alkawari. Ya yi zama
cikin Alfarwa tare da Ishaku da Yakubu, magadan
alkawari guda tare da shi. 10 Domin yana hangar
birnin da ke da tushi, Birnin da mai zaiyanar sa da
ginin sa shine Allah. 11 Ta dalilin bangaskiya, Ibrahim
ya sami haihuwa ko da shike shi da matarsa Saratu
sun yi nisa a cikin shekaru, kuma Saratu bakarariya
ce, ta kuma wuce lokacin haihuwa. Tun da shike sun
amince da wanda ya yi musu alkawari mai aminci
ne. 12 Sabo da haka, ta wurin mutumin nan daya,
wanda ya ke kamar matacce ne, aka haifi zuriya mai
dimbin yawa, su ka yawaita kamar taurari a sama
kamar yashi a bakin teku, wanda ba shi kidayuwa.
13 Dukkan su kuwa suka mutu a cikin bangaskiya
ba tare da sun karbi alkawarin ba. Maimakon haka,
sun hango, kuma sun marabcesu daga nesa, sai suka
amince su baki ne kuma matafiya ne a duniya. 14
Gama wadanda suka yi furci haka sun nuna a fili
cewa suna bidar kasa ta kansu. 15 Da kamar suna
tunanin kasar da suka fita daga ciki, da sun sa mi
damar komawa. 16 Amma kamar yadda yake, sun
bukaci kasa mafi dacewa, wato, wadda take a sama.
Saboda haka ne Allah bai ji kunyar a kira shi Allahnsu
ba, da shike ya shirya birni dominsu. 17 Ta dalilin
bangaskiya ne Ibrahim, sa'adda aka yi masa gwaji,
akan ya mika Ishaku dansa hadaya. 18 Shi ne kuwa
makadaicin dansa, wanda aka yi alkawari da cewa,
“Ta wurinsa ne za a kira zuriyarka.” 19 Ibrahim ya yi
tunani da cewa Allah na da ikon tada Ishaku ko daga
cikin matattu ma, haka kuwa yake a misalce, daga
matattun ne ya sake karbarsa. 20 Ta dalilin bangaskiya
ne kuma Ishaku ya albarkaci Yakubu da Isuwa game
da abubuwan da ke zuwa a gaba. 21 Dalilin bangaskiya
ne Yakubu, sa'adda yake bakin mutuwa, ya albarkaci
'ya'yan Yusufu dukkansu biyu. Yakubu ya yi ibada,
yana tokare a kan sandarsa. 22 Ta dalilin bangaskiya
Yusufu, sa'adda karshensa ya kusa, ya yi magana game
da fitar 'ya'yan Isra'ila daga Masar har ya umarce su
game da kasussuwansa. 23 Ta dalilin bangaskiya Musa,
sa'adda aka haife shi, iyayensa suka 'boye shi kimanin
watanni uku domin kyakkyawan yaro ne shi, kuma
basu ji tsoron dokar sarki ba. 24 Ta dalilin bangaskiya
ne kuma Musa, sa'adda ya girma, yaki a kira shi 'dan
diyar Fir'auna. 25 A maimakon haka, ya amince ya
sha azaba tare da jama'ar Allah, a kan shagali da
annashuwar zunubi na karamin lokaci. 26 Ya fahimci
cewa wulakanci domin bin Almasihu babbar wadata
ce fiye da dukiyar Masar. Gama ya kafa idanunsa a
kan sakamakon da ke gaba. 27 Ta dalilin bangaskiya
Musa ya bar Masar. Bai ji tsoron fushin sarki ba, ya
jure kamar yana ganin wannan da ba a iya ganinsa 28
Ta dalilin bangaskiya ya yi idin ketarewa da kuma
yayyafa jini, domin kada mai hallaka 'ya'yan fari ya
taba 'ya'yan fari na Isra'ila.` 29 Ta dalilin bangaskiya
suka haye baharmaliya kamar bushashiyar kasa.
Sa'adda Masarawa su ka yi kokarin hayewa, bahar din
ta hadiye su. 30 Ta dalilin bangaskiya ganuwar Yeriko
ta fadi, bayan sun kewaya ta har kwana bakwai. 31 Ta
dalilin bangaskiya Rahab karuwan nan bata hallaka
tare da marasa biyayya ba, don ta saukar da masu
leken asirin kasa a gidanta, ta kuma sallame su lafiya.
32 Me kuma za mu ce? Gama lokaci zai kasa mini
idan zan yi magana game da Gidiyon, Barak, Samson,
Yefta, Dauda, Sama'ila, da annabawa. 33 Ta dalilin
bangaskiya suka ci nasara kan kasashe, suka yi aikin
adalci, sa'annan suka karbi alkawura. Suka rufe bakin
zakuna, 34 suka kashe karfin wuta, suka tsira daga
bakin takobi, suka sami warkaswa daga cutattuka,
suka zama jarumawan yaki, sa'annan suka ci nasara
akan rundunar sojojin al'ummai. 35 Mata kuwa suka
karbi matattunsu da aka tayar daga mutuwa. Aka
azabtar da wadansu, ba su nemi yancin kansu ba,
domin suna begen tashi daga mattatu. 36 Wadansu
kuwa suka sha ba'a da duka da bulala, har ma da sarka
da kurkuku. 37 A ka jejjefe su. Aka tsaga su kashi biyu
da zarto. A ka karkashe su da takobi. Su na yawo sanye
da buzun tumakai da na awaki, suka yi hijira, suka
takura, suka wulakantu. 38 Duniya ma ba ta dauke
su a matsayin komai ba. Suka yi ta yawo a jazza, da
duwatsu, da kogwanni, da kuma ramummuka. 39 Ko

da yake mutanen nan amintattun Allah ne domin
bangaskiyarsu, basu karbi cikar alkawarin ba tukunna.
40 Domin Allah ya shirya mana wani abu mafi kyau ba
kuwa za su kammala ba sai tare da mu.

12 Da shike muna kewaye da wannan irin
kasaitaccen taro na shaidu, sai mu watsar da
dukkan abubuwan dake nawaita mana da kuma
zunubin da zai saurin makale ma na. Bari a cikin
hakuri mu yi tseren da ke gabanmu. 2 Bari mu kafa
idonmu ga Yesu, wanda shine mafarin bangaskiyarmu
da cikarta. Wanda sabili da murnar da a ka sa a
gabansa ya jimre giciye, ya kuma yi watsi da kunyarsa,
wanda kuma ya zauna a hannun dama na kursiyin
Allah. 3 Ku dube shi wanda ya jimre irin wannan
adawa daga masu zunubi, domin kada ku gaji ko ku
karai. 4 Ba ku yi tsayayya ko jayayya da zunubi har ta
kai ga zub da jininku ba tukunna. Kun kuma manta
da gargadin da a ka yi maku a matsayin 'ya'ya: 5
"Dana, kada ka dauki horon Ubangiji da wasa, kadda
kuma ka yi suwu lokacin da ka sami horonsa," 6
Domin kuwa Ubangiji yana horon dukkan wadanda
yake kauna, yana kuma hukunta duk wadanda ya
karba. 7 Ku daure wahala a matsayin horo. Allah
yana yi da ku kamar 'ya'yansa, domin kuwa wanne da
ne wanda ubansa bazai yi masa horo ba? 8 Amma
idan baku da horo kamar yadda sauran mutane ke da
shi, kun zama shegu kenan ba 'ya'ya ba. 9 Hakannan
kuma kamar yadda muke da iyaye a duniya wadanda
suke yi mana horo, kuma muna basu daraja. To ba
sai mu yiwa Ubanmu na Ruhaniya biyayya don mu
rayu ba? 10 Ta wani fanni kuwa iyayenmu suna yi
mana horo na kwanaki kadan bisa ga yadda suka
ga ya dace, Amma Allah kuwa yana yi mana horo
domin anfanin kanmu, domin kuma mu sami rabo
daga cikin tsarkinsa. 11 Ba horon da ke da dadi a
lokacin yinsa, amma sai zafi. Sai dai kuma bayan haka
yakan haifar da 'ya'ya na ruhaniya da kuma adalci
ga dukkan wadanda aka yi rainonsu a ciki. 12 Don
haka sai ku karfafa hannayenku da ke reto, da kuma
guwawunku da ke kaduwa. 13 Ku bi hanyoyi mikakku
domin abin da ya gurgunce kada ya karye amma ya
warke. 14 Ku bidi salama da kowa, da kuma rayuwar
tsarki wanda in ba tare da shi, babu wanda zai ga
Allah. 15 Ku mai da hankali domin kada waninku ya
rasa, alherin Allah, kuma kada wani tushe mai daci ya
tsiro a cikinku har ya haifar da fitina, domin kada
da dama daga cikinku su gurbata ta wurinsa. 16 Ku
yi hankali kuma kada a sami mazinanci ko marar
ibada a cikinku, kamar Isuwa, wanda sabili da abinci
ya sayar da 'yancinsa na dan fari. 17 Kun kuwa san
cewa sa'adda ya yi marmarin ya gaji albarka a gaba,
an kishi, domin kuwa bai sami damar tuba ba, ko da
shike ya nema har da hawaye. 18 Domin kuwa baku zo
ga dusen da ake tabawa da hannu ba, dutse ne mai
ci da wuta, da tukuki da bakin hayaki da hadari. 19
Ba Ku zo ga karar kaho mai ban razana da murya
mai firgitarwa ba, da masu sauraro suka yi roko kar
su sake jinta. 20 Don basu iya jimre abin da aka yi
doka a kan saba: "koma dabba ce ta taba dutsen,
sai a jejjefe ta." 21 Abin tsoro ne kuwa kwarai, har
Musa yace, "A tsoroce nake kwarai har na firgita."
22 Maimakon haka kun zone ga Dutsen Sihiyona da
kuma birni na Allah mai Rai, kuma na Urushalima
ta Samniya, da kuma dubun dubban mala'iku cikin
murna da farin ciki. 23 Kun zo taro na dukkan 'ya'yan
fari, rubuttatu a sama, kuma kun zo ga Allah wanda
shine alkalin dukka, hakannan kuma zuwa ga ruhu na
adalai wanda a ka rigaya aka tsarkake. 24 Kun zo ga
Yesu, wanda shine matsakancin sabon alkawari, kuma
ga jinin yayyafawa da ke magana fiye da na jinin
Habila. 25 Ku yi lura kada ku ki wannan da ke yi mu
ku magana. Gama in har basu kubuta yayin da su ka
yi jayayya da wanda ya yi mu su gargadi a duniya ba,
balle ma mu ba za mu kubuta ba in mun ki wanda ke
mana gargadi daga sama. 26 A wani karo, muryar sa
ta girgiza duniya. Amma yanzu yayi alkawari da cewa,
"Har'ila yau ba duniyar kadai zan girgiza ba, amma
har da sammai." 27 Wannan kalma, "Harl'ila yau,"
ta bayyana cirewar abubuwan nan da za su girgizu,
wato abubuwan da a ka halitta, domin abubuwan da
ba zasu girgizu ba su kasance. 28 Don haka, samun
mulkin da ba za ya girgizu ba, sai mu zama masu
godiya, kuma a cikin wannan yanayi mu yi wa Allah
sujada cikin daraja da tsaninin gimamawa. 29 Domin
kuwa Allahnmu wuta ne mai konewa.

13 Bari kaunar 'yan'uwa ta cigaba. 2 Kada ku manta
da karrama baki, domin ta wurin yin haka,
wasu suka marabci mala'iku ba tare da saninsu ba.
3 Ku tuna da wadanda ke cikin kurkuku, kamar dai
kuna tare da su cikin wannan hali. Kuma ku tuna
da masu shan azaba kamar tare kuke cikin wannan
hali 4 Bari kowa ya girmama aure, bari kuma a

tsarkake gadon aure, gama Allah zai shar'anta fasikai
da mazinata. 5 Bari halinku ya kubuta daga kaunar
kudi. Ku dangana da abubuwan da kuke dasu, domin
Allah da kansa yace, “Bazan barku ba, ba kuma zan
yashe ku ba.” 6 Bari mu zama da dangana domin mu
sami gabagadin cewa, “Ubangiji ne mai taimakona, ba
zan ji tsoro ba. To me mutum zai iya yi mani?” 7 Ku fa
lura da wadanda ke shugabanninku, wadanda suka
horar da ku cikin maganar Allah, kuma ku lura da
sakamakon rayuwarsu, ku yi koyi da bangaskiyarsu. 8
Yesu Almasihu daya ne a jiya, da yau, da har abada.
(aiōn g165) 9 Kada ku kauce zuwa ga bakin koyarwa
daban daban, domin yana da kyau zuciya ta ginu ta
wurin alheri, amma ba da dokoki game da abinci ba,
wadanda basu taimaki wadanda suka kiyayesu ba.
10 Muna da bagadin da wadanda ke hidima a cikin
alfarwa basu da ikon su ci daga bisansa. 11 Babban
firist na shiga wuri mai tsarki da jinin dabbobin da
aka yanka, hadayar zunubai, amma namansu a kan
kai bayan sansani a kone shi. 12 Domin haka Yesu
shima ya sha wahala a bayan kofar birnin, domin ya
tsarkake mutane ta wurin jininsa. 13 Domin haka bari
mu tafi gare shi a bayan sansani dauke da kunyarsa.
14 Domin bamu da wani birni dawwamamme a nan.
Maimako haka muna bidar birni dake zuwa. 15 Ta
wurin sa kuma, bari kullum mu mika hadayu na yabo
ga Allah, yabon kuwa shine kalmomin bakinmu da ke
daukaka sunansa. 16 Kada kuma mu manta da yin
nagarta da kuma taimakon juna, domin Allah na farin
ciki sosai da irin wadannan hadayun. 17 Ku yi biyayya
da sadaukarwa ga shugabanninku, domin suna aikin
tsaro a kanku saboda rayukanku, kamar wadanda zasu
bada lissafi. Kuyi biyayya gare su saboda su yi aikin
lura daku cikin farin ciki, ba da bakin ciki ba, don
in su yi da bakin ciki ba zai amfane ku ba. 18 Kuyi
mana addu'a, domin mun tabbata muna da lamiri
mai tsabta, kuma muna burin muyi rayuwar dake
daidai cikin dukkan al'amura. 19 Kuma ina karfafa ku
dukka kuyi haka, domin in sami dawowa gareku da
sauri. 20 To bari Allahn salama, wanda ya tada babban
makiyayin tumakin nan daga matattu, Ubangijinmu
Yesu, ta wurin jinin madawwamin alkawari, (aiōnios
g166) 21 ya kammala ku da dukan abu mai kyau domin
ku aikata nufinsa. Bari yayi aiki a cikinmu wanda
zai gamshe shi sosai. Ta wurin Yesu Almasihu, bari
daukaka ta tabbata gare shi har abada. Amin. (aiōn g165)
22 'Yan'uwa, yanzu dai ina karfafa ku, da ku jurewa
takaitacciyar maganar karfafawar da na rubuto maku.
23 Ina so ku sani an saki dan'uwan mu Timoti, tare da
shi zan zo in gan ku idan ya iso da sauri. 24 Ku gaida
shugabanninku dukka da kuma dukkan masu bada
gaskiya. 'Yan'uwa daga can Italiya suna gaishe ku. 25
Bari alheri ya kasance tare daku dukka.

# Yaƙub

1 Yakubu, bawan Allah, da kuma Ubangiji Yesu
Almasihu, zuwa ga kabilun nan goma sha biyu
da suke warwatse: ina gaishe ku. 2 Ku dauke su
duka da farin ciki, 'yan'uwana, duk sa'adda kuke
fuskantar jarabobi. 3 Ku sani cewa gwajin banskiyar
ku ta kan haifi jimiri. 4 Bari jimiri ya cika aikin sa,
domin ku kai ga cikakken girma kuma ku kammalu,
domin kada ku rasa komai. 5 Amma idan waninku
yana bukatar hikima, sai ya roki Allah, wanda yake
bayarwa a yalwace, ba tare da gori ba ga duk wanda
ya roke shi, zai kuwa ba shi. 6 Amma fa sai ya roka da
banskiya ba tare da shakka ba, don mai shakka kamar
rakumin ruwan teku yake, wanda iska take korarwa
tana tunkudawa. 7 Tilas ne wannan mutum kada
ya yi tunanin zai karbi wani abu a wurin Ubangiji.
8 Irin wannan mutumin mai zuciya biyu ne, mara
tsai da hankali a dukan hanyoyin sa. 9 Bari dan'uwa
matalauci ya yi takama da matsayin sa babba, 10 amma
mutum mai arziki kuma a kaskantaccen matsayin
sa, gama zai shude kamar furen ciyawa na jeji. 11
Domin rana na bullowa da zafi mai konarwa kuma
ya busar da ciyawa. Furen ya fadi, kuma kyaun sa
ya lalace. Haka ma, mai arziki zai bushe yana cikin
tsakiyar tafiyarsa. 12 Albarka ta tabbata ga mutum
mai jurewa da gwaji. Domin in ya jure gwajin, zai sami
rawanin rai, wanda aka yi alkawarin sa ga wadanda
ke kaunar Allah. 13 Kada wani ya ce idan aka gwada
shi, ''Wannan gwaji daga wurin Allah ne,'' domin
ba a gwada Allah da mugunta, shi kan sa kuwa ba
ya gwada kowa. 14 Amma kowanne mutum yakan
sami gwaji daga muguwar sha'awar sa, wadda take
janye shi kuma ta rinjaye shi. 15 Bayan da muguwar
sha'awar ta dauki ciki, sai ta haifi zunubi. Kuma bayan
da zunubi ya yi girma, yakan haifi mutuwa. 16 Kada
fa ku yaudaru, 'yan'uwana kaunatattu. 17 Kowace
kyakkyawar baiwa, da kowace cikakkiyar baiwa daga
sama take. Ta sauko ne daga wurin Uban haskoki.
Wanda babu sauyawa ko wata alamar sakewa kamar
yadda inuwa ke yi. 18 Allah ya zabi ya haife mu
ta wurin maganar gaskiya, domin mu zama kamar
nunar fari na dukan halittar sa. 19 Kun san wannan,
'yan'uwana kaunatattu: bari kowanne mutum ya yi
hanzarin kasa kunne, da jinkirin yin magana, da kuma
jinkirin yin fushi. 20 Domin fushin mutum ba ya aikata
adalcin Allah. 21 Saboda haka, sai ku yar da kowanne
irin aikin kazanta da yalwar mugunta. A cikin tawali'u
ku karbi dassashiyar maganar, wadda ke iya ceton
rayukan ku. 22 Ku zama masu aikata maganar, kada
ku zama masu jin ta kawai, kuna yaudarar kanku. 23
Domin duk wanda ya ke mai jin maganar ne kawai,
ba mai aikatawa ba, kamar mutum yake mai duba
fuskarsa a madubi. 24 Yakan dubi kansa sai ya tafi,
nan da nan kuwa sai ya manta da kamannin sa. 25
Amma duk mai duba shari'ar da bin ka'idar nan ta
'yanci, ya kuma nace biyayya da ita, ba zai zama
kamar wanda zai ji ya manta ba, wannan mutum zai
zama da albarka a cikin abin da yake yi. 26 Idan wani
yana zaton shi mai addini ne, amma bai kame bakinsa
ba, yana yaudarar zuciyarsa ne, addinin mutumin nan
na banza ne. 27 Addini sahihi kuma marar aibi a gaban
Allahnmu da Ubanmu, shine a kula da gwauraye da
marayu a cikin kuntatar su, kuma mutum ya kebe
kansa ya zama marar aibi daga duniya.

2 Ya ku 'yan'uwana, muddin kuna rike da bangaskiyar
ku ga Ubangijinmu Yesu Almasihu, Ubangijin
daukaka, kada ku nuna bambanci ga wadansu mutane.
2 Idan wani mutum ya halarci taron ku da zobban
zinariya da tufafi masu kyau, wani matalauci kuma ya
shigo da tufafi marasa tsabta. 3 Sa'adda kuka kula da
mai tufafi masu kyau nan, har kuka ce masa, "Idan ka
yarda ka zauna a nan wuri mai kyau,'' mataulacin
nan kuwa kuka ce masa, "Kai ka tsaya daga can," ko
kuwa, "Zauna a nan kasa a gaba na," 4 Ashe ba kuna
zartar da hukunci a tsakanin ku ba ke nan? Ba kun
zama alkalai na mungayen tunani kenan ba? 5 Ku
saurara, ya 'yan'uwana kaunatattu, ashe, Allah bai
zabi matalautan duniyar nan su zama mawadata cikin
bangaskiya ba, su kuma zama magada a cikin mulkin
nan da ya yi wa masu kaunar sa alkawari ba? 6 Amma,
kun wulakanta matalauta! Ashe, ba masu arzikin ne
suke matsa maku ba? Ba su ne kuwa suke jan ku zuwa
gaban shari'a ba? 7 Ba kuma sune ke sabon sunan nan
mai girma da ake kiran ku da shi ba? 8 Duk da haka,
idan kuka cika muhimmiyar shari'ar da nassi ya ce,
"Ka kaunaci makwabcin ka kamar kanka," to, madalla.
9 Amma in kun nuna bambanci, kun yi zunubi kenan,
shari'a ta same ku da laifin keta umarni. 10 Duk wanda
yake kiyaye dukan shari'a, amma ya yi tuntube a
hanya daya kadai, ya sabi shari'a gaba daya ke nan. 11
Domin wanda ya ce, "Kada ka yi zina," shi ne kuma ya
ce, "Kada ka yi kisan kai." Idan ba ka yi zina ba amma

ka yi kisan kai, ai, ka zama mai taka shari'a kenan. 12
Saboda haka, ku yi magana ku kuma yi aiki kamar
wadanda za a hukunta ta wurin 'yantacciyar shari'a.
13 Gama hukunci yana zuwa ba tare da jinkai ba ga
wadanda ba su nuna jinkai. Jinkai ya yi nasara a kan
hukunci. 14 Ina amfanin haka, 'yan'uwana, idan wani
ya ce yana da bangaskiya, kuma ba shi da ayyuka?
Wannan bangaskiyar ba za ta cece shi ba, ko za ta
iya? 15 Misali, idan wani dan'uwa ko 'yar'uwa ba
su da tufa mai kyau ko suna rashin abincin yini. 16
Misali, idan waninku kuma ya ce masu, “Ku tafi cikin
salama, ku kasance da dumi ku koshi.” Idan baku
ba su abubuwan da jiki ke bukata ba, ina amfanin
wannnan? 17 Haka ma, bangaskiya ita kadai, ba tare
da aikin da ya nuna ta ba, matacciya ce. 18 To, wani
zai ce, “Ai, kai kana da bangaskiya, ni kuwa ina da
ayyuka.” Nuna mani bangaskiyar ka ba tare da ayyuka
ba, ni kuma in nuna maka bangaskiya ta ta wurin
ayyuka na. 19 Ka gaskanta cewa Allah daya ne; ka yi
daidai. Amma ko aljannu ma sun gaskata, kuma suna
rawar jiki. 20 Kana so ka sani, kai marar azanci, cewa
bangaskiya ba tare da ayyuka ba banza ce? 21 Ba an
baratar da Ibrahim mahaifinmu ta wurin ayyuka ba,
sa'adda ya mika Ishaku dansa a bisa bagadi? 22 Ka
gani, ashe, bangaskiyar sa ta yi aiki da ayyukan sa,
kuma da cewa ta wurin ayyuka bangaskiyar sa ta ginu
sosai. 23 Nassi kuma ya cika da ya ce, “Ibrahim ya
gaskata Allah, aka kuma lisafta masa ita a matsayin
adalci.” Aka kuma kira shi abokin Allah. 24 Kun ga,
ta wurin ayyuka ne mutum yake samu baratarwa ba
ta wurin bangaskiya kadai ba. 25 Ta wannan hanyar
kuma, ba Rahab karuwar nan ta samu baratarwa ta
wurin ayyuka, da ta marabci masu leken asirin nan ta
fitar da su ta wata hanya dabam ba? 26 Kamar yadda
jiki idan ba tare da ruhu ba matacce ne, haka kuma,
bangaskiya ba tare da ayyuka ba matacciya ce.

3 Ba mutane dayawa za su zama masu koyarwa ba,
'yan'uwana. Mun san cewa za mu karbi hukunci
mafi tsanani. 2 Domin mukan yi tuntube ta hanyoyi
dayawa. Duk wanda bai yi tuntube ta hanyar kalmomi
ba, shi mutum ne ginanne sosai, wanda ke iya kame
dukan jikinsa. 3 Idan muka sa linzami a bakunan
dawakai, domin su yi mana biyayya, za mu iya sarrafa
jikunan su gaba daya. 4 Ku lura kuma da jiragen ruwa,
ko da yake suna da girma sosai kuma iska mai karfi
tana kora su, da karamin karfe ne matukin yake juya
su inda ya so. 5 Haka kuma harshe dan karamin gaba
ne a jiki, sai fahariyan manyan abubuwa. Ku lura
yadda dan karamin wuta yake cinna wa babban jeji
wuta. 6 Harshe ma wuta ne, a cikin dukan gabobin
mu, duniyar zunubai da aka sa cikin fannonin jikunan
mu. Yana gurbata dukan jiki, ya kuma sa al'amurar
rayuwa su kama da wuta. Shi kuwa gidan wuta ne
yake zuga shi. (Geenna g1067) 7 Domin kowace irin dabbar
jeji, tsunsu, da masu jan ciki, da hallittar teku, ana
sarrafa su kuma dan Adam har ya sarrafa su ma. 8
Amma game da harshe, babu wani a cikin 'yan Adam
da ya iya sarrafa shi. Mugunta ne mara hanuwa, cike
da dafi mai kisa. 9 Da wannan harshe muke yabon
Ubangiji da kuma Uba, da shi kuma muke la'antar
mutane wandanda aka hallitta cikin kamanin Allah.
10 Bakin da ake sa albarka, da shi kuma ake la'antarwa.
'Yan'uwana, ai, wannan bai kamata ba. 11 Mabulbulan
ruwa ba zai iya bubbugowa da ruwan dadi da na zartsi
tare ba, ko zai iya? 12 ''Yan'uwana, itacen baure ba zai
iya yin zaitun ba, zai iya? Ko kuwa gonar inabi ya yi
baure? Haka kuma, ruwan zartsi ba zai iya bayar da
ruwan dadi ba. 13 Ina mai hikima da fahimta a cikin
ku? Bari wannan mutumin, ta kyakkyawan zaman sa
ya nuna aikin da halin tawali'u da hikima ke sawa.
14 Amma in kuna da matsanancin kishi da kazamin
buri a cikin zuciyar ku, kada ku yi fahariya da karya
game da gaskiya. 15 Wannan hikima ba irin wadda
take saukowa daga sama ba ce, a maimakon haka, ta
duniya ce, mara ruhaniya, ta aljanu. 16 Domin duk
inda kishi da kazamin buri suke, a nan ake samun
hargitsi da kowanne irin aikin mugunta. 17 Amma
hikiman nan ta sama, da farko dai tsattsarka ce, mai
lumana ce, kamila ce, mai saukin kai, mai tsananin
jinkai, mai yawan alheri, mara gajiya, sahihiya kuma.
18 Kuma 'ya'yan adalci wanda ake shukawa a cikin
salama a tsakanin wadanda ke kulla zumunci.

4 Me ke kawo gaba da rashin jituwa a tsakanin ku?
Ba yana tasowa ne daga muguwar sha'awa da ke
yaki a cikin ku ba? 2 Kuna sha'awa, kuma ba ku da
shi. Kuna kisa da kyashi, kuma ba za ku iya samu
ba. Kuna danbe da fada. Har wa yau baku samu ba
domin baku tambaya ba. 3 Kun roka kuma ba a baku
ba saboda kuna roko ta hanya mara kyau, kuna so ku
yi amfani da shi domin miyagun sha'awoyin ku. 4
Ku mazinata! Baku sani ba, abokantaka da duniya,
tawaye ne ga Allah? Don haka duk wanda ya shiga

abokantaka da duniya ya zama magabcin Allah. 5 Ko
kuna zaton nassi ya fadi haka a banza ne, “Ruhun
nan da ke a cikinmu yana da kishi matuka?” 6 Amma
Allah ya bayar da karin alheri, shi ya sa nassi ya ce,
“Allah yana gaba da mai girman kai, Amma yana ba
da alheri ga mai tawaliu.” 7 Saboda haka ku mika
kan ku ga Allah. Ku yi tsayayya da shaidan, zai kuma
guje maku. 8 Ku matso kusa da Allah, shi kuma za
ya matsa kusa da ku. Wanke hannayen ku, ku masu
zunubi, ku tsabtace zukatan ku, ku masu zuciya biyu.
9 Ku yi bakin ciki, makoki, da kuka! Ku mayar da
dariyar ku ta koma bakin ciki, farin cikinku kuma
zuwa ga bakin ciki. 10 Ku kaskantar da kanku a gaban
Ubangiji, shi kuma za ya daukaka ku. 11 Kada ku rika
zargin juna, 'yan'uwa. Wanda ya ke zargin dan'uwa ko
shari'anta dan'uwansa, yana zargin shari'a kuma yana
hukunta shari'a. Idan ka hukunta shari'a, ya nuna ba
ka biyayya da shari'ar, amma mai hukunci. 12 Mai
ba da shari'a da yin hukunci daya ne. Shine mai iya
ceto kuma ya hallakar. Kai wanene, da ke hukunta
makwafcin ka? 13 Saurara, ku da kuke cewa, “Yau ko
gobe za mu tafi wancan birnin mu yi shekara guda
a wurin, muna kasuwanci, mu kuma yi riba.” 14 Wa
ya san abin da zai faru gobe, kuma yaya rayuwan ka
zai kasance? Kai kamar hazo ne mai bayyana bayan
dan lokaci kadan ya bace. 15 Maimakon haka, sai ka
ce, “Idan Ubangiji ya nufa, za mu rayu kuma mu yi
wannan ko wancan.” 16 Amma yanzu kana fahariya
da shirye shiryen ka na takama. Irin wannan fahariya,
mugunta ce. 17 Saboda haka ga wanda ya san abin da
ya kamata ya aikata amma bai yi ba, ya zama zunubi a
gare shi.

5 Ku zo yanzu, ku da kuke masu arziki, ku yi ta kuka
da kururuwa domin bakin ciki iri-iri da ke zuwa
gare ku. 2 Arzikin ku ya rube, tufafinku kuma duk
cin asu ne. 3 Zinariya da azurfarku sun yi tsatsa.
Tsatsar su kuwa zai zama shaida a kanku. Zai cinye
naman ku kamar wuta. Kun yi ajiyar dukiyarku domin
ranakun karshe. 4 Duba, hakin ma'aikata yana kuka -
hakin da kuka hana wa wadanda suka girbe maku
gonaki. Kuma kukan masu girbin ya tafi ya kai ga
kunnuwan Ubangiji mai Runduna. 5 Kun yi zama cikin
annashuwa a duniya kuma kun tsunduma kanku.
Kun sa zukatan ku sun yi kiba domin ranar yanka.
6 Kun hukunta kuma kun kashe adalin mutum. Bai
kuwa yi tsayayya da ku ba. 7 Saboda haka ku yi
hakuri, 'yan'uwa, har sai zuwan Ubangiji. Duba, yadda
manomi ya kan jira kaka mai amfani daga gona. Da
hakuri yake jiran ta har sai ta karbi ruwa na fari da na
karshe. 8 Ku, ma, ku yi hakuri. Ku karfafa zukatan
ku, domin zuwan Ubangiji ya yi kusa. 9 Kada ku yi
gunaguni, 'Yan'uwana, game da juna, don kada a
hukunta ku. Duba, mai shari'a na tsaye a bakin kofa.
10 Dauki misali, 'yan'uwa, daga shan wuya da hakurin
annabawa, wadanda suka yi magana a cikin sunan
Ubangiji. 11 Duba, mukan kira wadanda suka jimre
masu albarka. Kun dai ji irin jimiri da Ayuba ya yi,
kun kuma san nufin Ubangiji, yadda yake mai yawan
tausayi da jinkai. 12 Fiye da komai duka, 'yan'uwana,
kada ku yi rantsuwa, ko da sama, ko da kasa, ko da
kowace irin rantsuwa ma. A maimakon haka bari “I”
ya zama “I”, in kuwa kun ce “A'a”, ya zama “A'a”,
don kada ku fada a cikin hukunci. 13 Akwai wanda ke
fama a tsakanin ku? Sai ya yi addu'a, akwai wanda
yake murna? Sai ya raira wakar yabo. 14 Akwai mara
lafiya a tsakanin ku? Sai ya kira dattawan ikilisiya,
sai su yi masa addu'a. Suna shafa masa mai a cikin
sunan Ubangiji. 15 Addu'ar bangaskiya zai warkar da
mara lafiyan, Ubangiji zai tashe shi. Idan ma ya yi
zunubi, Allah zai gafarta masa. 16 Soboda haka, ku
furta zunuban ku ga juna, kuna yi wa juna addu'a,
don a warkar da ku. Addu'ar mai adalci tana da karfin
aiki kwarai da gaske. 17 Iliya dan Adam ne kamar mu.
Amma da ya nace da addu'a kada a yi ruwa, ba kuma
yi ruwa a kasar ba har shekara uku da wata shida. 18
Sai Iliya ya sake yin addu'a. Sammai suka ba da ruwa,
kasa kuma ta ba da amfanin ta. 19 Ya ku 'yan'uwana,
idan wanin ku ya baude wa gaskiya, wani kuma ya
dawo da shi, 20 wannan mutum ya sani cewa, duk
wanda ya dawo da mai zunubi a hanya daga baudewar
sa, zai cece shi daga mutuwa, kuma zai rufe dunbin
zunubai.

# 1 Bitrus

**1** Bitrus, manzon Yesu Almasihu, zuwa ga zababbu
wadanda suke baki, a warwatse cikin Buntus,
Galatiya, kappadokiya, Asiya, da Bitiniya. 2 Bisa ga
rigasanin Allah Uba, Ta wurin tsarkakewar Ruhu,
zuwa biyayya da yayyafar jinin Yesu Almasihu. Alheri
da salama su yawaita a gareku. 3 Albarka ga Allah
Uban Ubangijinmu Yesu Almasihu. Ta wurin jinkansa
mai girma, ya maya haihuwarmu zuwa bege mai rai
ta wurin tashin Yesu Almasihu daga matattu. 4 Zuwa
gado marar lalacewa, marar baci, ba kuma zai kode ba.
Wanda aka kebe a sama dominku. 5 Ku da ikon Allah
ya kiyaye ta wurin bangaskiya domin ceto wanda za'a
bayyana a karshen zamanai. 6 Cikin wannan kuna
murna da yawa, duk da ya ke ya zama wajibi gare
ku yanzu ku yi bakin ciki, a cikin jarabobi iri iri. 7
Wannan kuwa da nufin a iske aunawar bangaskiyarku
ne, bangaskiyar da tafi zinariya daraja, wadda takan
lalace ko da an gwada ta da wuta. Wannan ya faru
domin bangaskiyan nan taku ta jawo maku yabo da
girma da daukaka a bayyanuwar Yesu Almasihu. 8
Wanda kuke kauna, ko da yake baku ganshi ba. Ko
da yake baku ganinsa yanzu, duk da haka kun bada
gaskiya gare shi murnar da ku ke yi kwarai da farin
ciki wanda tafi gaban a fadi cike da daukaka. 9 Kuna
karbar sakamakon bangaskiyarku, ceton rayukanku.
10 Annabawan da su ka yi annabcin ceton da ya
zama naku su ka yi bidassa suka bincike kuma da
himma. 11 Sun nemi su san ko wanene da kuma
kowanne lokaci ne Ruhun Almasihu da ke cikinsu
yake bayyana ma su. Wannan ya faru ne sa'adda
yake gaya ma su tun da wuri game da shan wahalar
Almasihu da kuma daukakar da zata biyo baya. 12 An
kuwa bayyana wa annabawan cewa ba kansu suke
hidimtawa ba, amma ku suke yi wa hidima. Wannan
shine abin da suke yi game da abin da aka rigaya aka
gaya maku, ta wurin wadanda da Ruhu mai Tsarki
ya bishe su. Wanda aka aiko daga sama. Wadannan
sune abubuwan da mala'iku ma suka yi marmarin a
bayyana masu. 13 Domin wannan fa ku natsu. Ku yi
dammara a hankalinku. Ku kafa begenku sarai akan
alherin da za'a kawo maku a lokacin bayyanuwar
Yesu Almasihu. 14 Kamar 'ya'ya masu biyyaya, kada
ku biyewa sha'awoyinku na da a zamanin jahilcinku.
15 Amma yadda shi wanda ya kira ku mai tsarki ne,
kuma ku zama da tsarki cikin dukkan al'amuranku.
16 Domin a rubuce yake, "Ku zama da tsarki, gama
ni mai tsarki ne." 17 Idan ku na kira bisa gare shi
"Uba" shi wanda yake hukuntawa ba da tara ba, amma
gwar-gwadon aikin kowane mutum, sai kuyi zaman
bakuncinku da tsoro da bangirma. 18 Kun san cewa ba
da azurfa ko zinariya mai lalacewa aka fanshe ku ba,
daga halinn wauta da kuka gada daga wurin iyayenku.
19 Maimakon haka an fanshe ku da jinin Almasihu
mai daraja, marar aibu kamar na dan rago. 20 An zabi
Almasihu tun kafin kafawar duniya, amma a karshen
zamanu ya bayyanu a gare ku. 21 Ku da kuka bada
gaskiya ga Allah ta wurinsa, wanda ya tashe shi daga
matattu ya kuma bashi daukaka domin bangaskiyarku
da begenku su kasance cikin Allah. 22 Da shike kun
tsarkake rayukanku cikin biyayyar ku ga gaskiya
zuwa ga sahihiyar kauna ta 'yan'uwa, sai ku kaunaci
junanku da zuciya mai gaskiya. 23 da shike an sake
hai'huwarku ba daga iri mai lalacewa ba amma daga
iri marar rubewa, ta wurin maganar Allah wadda take
rayuwa ta kuma dawwama. (aiōn g165) 24 Gama "dukkan
jiki kamar ciyawa yake, dukkan darajarsa kuwa kamar
furen ciyawa take. Ciyawa takan yi yaushi, furenta ya
kan yankwane ya fadi, 25 amma maganar Ubangiji
tabbatacciya ce har abada. "Wannan ita ce maganar
bishara wadda akayi maku wa'azinta." (aiōn g165)

**2** Saboda haka sai ku tube dukkan keta, rikici, da
riya, kishi, da dukkan mugun zance. 2 Kammar
jarirai, sababbin haihuwa, ku yi marmarin madara
mai ruhaniya wadda take sahihiya, domin ta wurinta
kuyi girma zuwa ceto, 3 idan kun dandana Ubangiji
mai-alheri ne. 4 Kuzo gareshi rayayyen dutse wanda
mutane suka ki, amma zababbe ne mai-daraja wurin
Allah. 5 Ku kuma kamar rayayyun duwatsu ana gina
ku gida mai ruhaniya, domin ku zama tsarka-kan
fristoci, domin ku mika hadayu masu ruhaniya abin
karba ga Allah ta wurin Yesu Almasihu. 6 Gama
nassi ya ce, "Ga shi na sanya dutse na kan kusurwa,
zababe, mai daraja a cikin Sihiyona. Duk wanda ya
bada gaskiya gareshi ba zaya kunyata ba." 7 Daraja
a gareku take ku da kun bada gaskiya. Amma, ga
wadanda suka ki bada gaskiya, "Dutsen da magina
suka ki shine aka mai she shi kan kusurwa". 8 kuma,
"Dutsen sa tuntube da fa na sa tuntube. "Sun yi
tuntube, da shike sun ki biyayya da maganar, an kuwa
kaddara su ga wannan. 9 Amma ku zababben jinsi
ne, kungiyar fristoci ba-sarauci, al'umma mai-tsarki,

jama'ar mallakar Allah, domin ku sanar da mafifitan
al'amuran wanda ya kiraye ku daga chikin duhu zuwa
cikin haskensa mai'ban al'ajibi. 10 Ku da ba jama'a ba
ne a da, amma yanzu jama'ar Allah ne. Da baku sami
jinkai ba, amma yanzu kun sami jinkai. 11 Kaunatattu,
ina rokon ku misalin baki da masu-tafiya kuma, ku
guje wa sha'awoyin jiki wadanda ke yaki da rai. 12
Ku kasance da kyakkyawan hali a cikin al'ummai,
domin, sa'adda suke kushen ku kamar masu aikata
mugunta, sai su lura da nagargarun ayyukanku su
kuma daukaka Allah a ranar zuwansa. 13 Kuyi biyayya
ga kowacce hukuma ta mutane sabili da Ubangiji,
ko ga sarki domin shi ne shugaba. 14 Ko kuwa ga
masu mulki aikakkunsa ne domin su hori masu aikata
mugunta da yabawa masu aikata nagarta. 15 Gama
wannan nufin Allah ne, ta wurin aikin kirki ku, kwabi
jahilcin mutane marassa hikima. 16 Kamar 'yan'tattu
kada ku mori 'yan'cinku kamar mayafin mugunta,
amma ku zama kamar bayin Allah. 17 Ku girmama
dukkan mutane. Ku kaunaci 'yan'uwa, kuji tsoron
Allah. Ku girmama sarki. 18 Ku barori, kuyi biyayya ga
iyayen gidanku da dukkan bangirma, ba ga nagargaru
da masu saukin kai ba, amma har ga miskilai. 19 Gama
abin yaba wa ne idan sabili da lamiri zuwa ga Allah in
wani ya jimre da shan zalunci. 20 Gama wacce riba ke
nan idan kun yi zunubi ana horonku kuna jimrewa
da hukuncin? amma idan kunyi aikin kirki kuka sha
wuya a kansa kuka yi hakuri, wannan abin karba ne
wurin Allah. 21 Gama akan haka aka kiraye ku, gama
Almasihu ma yasha azaba saboda ku, ya bar maku
gurbi kubi sawunsa. 22 Bai taba yin zunubi ba, ba'a
taba jin yaudara a bakinsa ba. 23 Da'a ka zage shi
bai mai da zagi ba. Da ya sha azaba, bai yi kashedi
ba, amma ya mika kansa ga wanda yake yin shari'ar
adalci. 24 Shi da kansa ya dauki zunubanmu a cikin
jiki nasa ya kai su bisa itace, domin kada a iske mu
cikin zunubi, amma muyi rayuwa ga adalci. Ta wurin
raunukansa ne kuka warke. 25 Dukkanku da kun bata
kuna yawo kamar batattun tumaki, amma yanzu kun
dawo wurin makiyayi da mai tsaron rayukanku.

3 Haka ku kuma da kuke matan aure, kuyi biyayya
da na ku mazajen, domin in har wadansunsu basa
biyayya da maganar Allah, halin matansu ya shawo
kansu ba tare da magana ba, 2 Domin sun ga tsattsakan
halinku da ladabinku. 3 Haka ma adonku kar ya zama
na kwalliyar waje kitson kai, kayan zinariya ko tufafi
masu kawa. 4 Amma bari adon ya zama na mutum
na cikin zuciya, kuma adon ya zama kyan nan marar
dushewa, na kamun kai da natsatsen ruhu, wanda
yake da daraja a gaban Allah. 5 Haka tsarkakan mata
su ka yi ado kamar haka. Suka dogara ga Allah suka yi
biyayya ga mazajensu. 6 Ta haka Saratu ta yi biyayya
ga Ibrahim ta kira shi "ubangiji". Yanzu ku 'ya'yantane
in dai kun yi aiki nagari, idan kuma ba ku ji tsoron
wahala ba. 7 Kamar yadda na fada wa matan aure haka
ma mazaje, ku zauna da mata da sanin su raunana
ne abokan tarayya ne na karbar baiwar rayuwa. Ku
dinga yin haka domin a rika jin addu'oinku. 8 Daga
karshe, dukanku ku hada hankulanku, ku zama masu
juyayi, masu kauna kamar 'yan'uwa, masu taushin
zuciya, masu tawali'u. 9 Kada ku rama mugunta da
mugunta ko zagi da zagi. A maimakon haka ku cigaba
da sa albarka, gama sabili da haka ne musamman aka
kiraye ku, domin ku gaji albarka. 10 "Wanda duk yake
so ya more a rayuwarsa ya kuma ga kwanaki masu
alheri, to fa, ya kame harshen sa daga mugunta da
lebensa daga maganganun yaudara. 11 Ya rabu da
mugunta ya aikata abin da ke nagari. Bari ya nemi
zaman salama ya kuma dimanceta. 12 Idanun Ubangiji
suna duban adalai, kunnuwansa kuma suna sauraron
roke rokensu. Amma fuskar Ubangiji tana gaba da
masu aikata mugunta." 13 Wanene ya isa ya cuce ku
idan kun himmatu ga yin abin da ke nagari? 14 Amma
idan kuna shan wuya saboda adalci, ku masu albarka
ne. Kada ku ji tsoron abin da su ke tsoro. Kada ku
damu. 15 Maimakon haka, ku kebe Ubangiji a cikin
zukatanku cewa shi mai tsarki ne. Kullum ku zauna
da shiri domin ku amsa wa mai tambayar ku dalilin sa
begenku ga Allah. Amma fa kuyi haka tare da tawali'u
da bangirma. 16 Ku zama da tsatsakan lamiri domin
mutanen da ke zargin rayuwarku mai kyau cikin
Almasihu, su ji kunya domin suna maganar gaba da
ku kamar ku mugaye ne. 17 Ya fi kyau, a sha wuya
akan aiki nagari, idan nufin Allah ne, da a sha wuya
sabili da mugun aiki. 18 Almasihu ya sha wahala sau
daya tak sabili da zunubai. Shi da ya ke mai adalci ya
sha wahala domin mu marasa adalci, domin ya kawo
mu ga Allah. Aka kashe shi cikin jiki, amma aka rayar
da shi cikin Ruhu. 19 A Ruhu ne, ya je ya yi wa'azi
ga ruhohin da ke a yanzu cikin kurkuku. 20 Sun yi
rashin biyayya ne sa'adda hakurin Allah yake jiransu
a lokacin Nuhu a zamanin sassaka jirgin ruwa, sai
Allah ya tsirar da mutane kalilan wato rayuka takwas

daga cikin ruwa. 21 Wannan kwatancin baftismar da
take cetonmu yanzu ne, ba kamar ta wanke Dauda
daga jiki ba, sai dai ta rokon Allah da lamiri mai kyau
ta wurin tashin Yesu Almasihu daga matattu. 22 Ya
hau sama. Yana dama ga Allah. Mala'iku, da mulkoki
da masu iko dole su yi masa biyayya.

4 Saboda haka, tunda yake Almasihu ya sha wuya
a jiki, muma mu sha damara da wannan ra'ayi.
Duk wanda ya sha wuya a jiki ya daina aikata zunubi.
2 Wannan mutum kuma baya kara zaman biye wa
muguwar sha'awar mutumtaka, amma sai dai nufin
Allah dukkan sauran kwanakinsa a duniya. 3 Gama
lokaci ya wuce da zamu yi abin da al'ummai suke
son yi, wato fajirci, mugayen sha'awace-sha'awace,
da buguwa da shashanci da shaye-shaye da bautar
gumaku da abubuwan kyama. 4 Suna tunanin bakon
abu ku ke yi da ba kwa hada kai tare da su yanzu
a yin wadannan abubuwa, sai suna zarginku. 5 Za
su bada lissafi ga wanda yake a shirye ya shari'anta
masu rai da matattu. 6 Shi yasa aka yi wa matattu
wa'azin bishara, cewa ko da shike anyi masu shari'a
cikin jikunan mutane, su rayu bisa ga Allah a ruhu.
7 Karshen dukkan abubuwa yana gabatowa. Saboda
haka, ku zama natsatsu, ku natsu cikin tunaninku
domin yin addu'oi. 8 Gaba da kome, ku himmatu wajen
kaunar juna, domin kauna bata neman tona zunuban
wadansu. 9 Ku yi wa juna bakunta da abubuwa nagari
ba tare da gunaguni ba. 10 Yadda kowanne dayanku ya
sami baiwa, kuyi amfani da su domin ku kyautata wa
juna, kamar masu rikon amanar bayebaye na Allah,
wanda ya ba mu hannu sake. 11 Idan wani yana yin
wa'azi, ya zamana fadar Allah ya ke fadi, idan wani
yana hidima, ya yi da karfin da Allah ya ba shi, domin
cikin dukkan abubuwa a daukaka Allah ta wurin Yesu
Almasihu. Daukaka da iko nasa ne har abada abadin.
Amin. (aiōn g165) 12 Ya kaunatattu, kada ku zaci cewa
matsananciyar wahalar da ta zo ta gwada ku bakon
abu ne, ko kuma wani bakon abu ne yake faruwa a
gareku. 13 Amma muddin kuna tarayya da Almasihu
cikin wahalarsa, ku yi murna, domin kuyi farin ciki
da murna sa'adda za a bayyana daukakarsa. 14 Idan
ana zargin ku sabili da sunan Almasihu, ku masu
albarka ne, domin Ruhun daukaka da Ruhun Allah
ya tabbata a kanku. 15 Amma kada kowannen ku ya
sha wahala sabo da horon shi mai kisan kai ne, ko
barawo, ko mamugunci, ko mai shisshigi. 16 Amma in
wani yana shan wahala sabili da shi na Almasihu ne,
kada ya ji kunya, amma ya daukaka Allah a wannan
sunan. 17 Domin lokaci ya yi da shari'a za ta fara daga
gidan iyalin Allah. Idan kuwa za a fara da mu, menene
karshen wadanda suka ki biyayya da bisharar Allah?
18 Idan mutum, "mai adalci ya tsira da kyar, to, me
zai faru da marar bin Allah da mai zunubi kuma?"
19 Sabo da haka bari wadanda suke shan wuya bisa
ga nufin Allah, su mika rayukansu ga amintaccen
Mahalicci suna kuma yin ayyuka nagari.

5 Ina yiwa dattawan da ke cikinku gargadi, ni da
nike dan'uwanku dattijo, mashaidin shan wuyar
Almasihu, ni kuma mai samun rabo ne daga cikin
daukakar daza a bayyana. 2 Saboda haka na gargade
ku dattawa, kuyi kiwon garken Allah dake tare da
ku. Ku kula da su, ba a kan dole ba, amma domin
kuna son yin haka, bisa ga yin Allah. Ku kula da su, ba
don cin ribar banza ba amma sabo da yardar rai. 3
Kada ku zama kamar masu iko akan mutanen dake
hannunku, amma ku zama abin koyi ga garken. 4
Sa'adda za a bayyana Sarkin Makiyaya zaku karbi
rawanin da darajarsa bata dushewa. 5 Hakannan, ku
kuma samari kuyi biyayya ga dattawa. Dukanku kuyi
damara da tawali'u, kuna bauta wa juna, domin Allah
ya na tsayayya da mai girman kai, amma yana yiwa
masu tawali'u alheri. 6 Saboda haka ku kaskantar
da kanku karkashin hannuwan Allah mai iko duka
domin ya daukaka ku a madaidecin lokaci. 7 Ku jibga
masa duk taraddadin zuciyarku, domin yana kula da
ku. 8 Ku natsu, ku zauna a fadake. Magabcinku, ibilis,
kamar zaki mai ruri yana zazzagawa, yana neman
wanda zai cinye. 9 Ku yi tsayayyiyar gaba da shi.
Ku yi karfi cikin bangaskiyarku. Ku sani fa abokan
tarayyarku da suke cikin duniya suna jimrewa da
shan wuyan nan irin taku. 10 Bayan shan wuyarku na
dan lokaci kadan, Allah mai alheri mara iyaka, wanda
ya kiraye ku zuwa ga madawwamiyar daukakarsa
cikin Almasihu, zai kammalaku, ya kafa ku, ya kuma
karfafa ku. (aiōnios g166) 11 Mulki ya tabbata a gare shi
har abada abadin. Amin. (aiōn g165) 12 Na amince da
Sila amintaccen dan'uwa ne, kuma na rubuto maku a
takaice ta hannunsa. Ina yi maku gargadi ina kuma
shaida maku cewa abin da na rubuto alherin Allah
ne na hakika. Ku kafu a cikinsa. 13 Ita matar da ta
ke a Babila zababbiya tare da ku, ta na gaisheku, da
Markus, dana, yana gaisheku. 14 Ku gai da juna da

sumbar kauna. Salama ta tabbata a gare ku dukanku
da ke cikin Almasihu.

# 2 Bitrus

**1** Siman Bitrus, bawa da manzon Almasihu Yesu,
zuwa ga wadanda suka karbi bangaskiya mai daraja
kamar yadda muka karba, bangaskiya cikin adalcin
Allahnmu da Yesu Almasihu. 2 Bari alheri ya kasance
tare da ku; bari salama ta karu ta wurin sanin Allah
da na Yesu Ubangijinmu. 3 Dukkan abubuwan ikon
Allah na rayuwa da Allahntaka an bamu su ta wurin
sanin Allah, wanda ya kira mu ta wurin daukakarsa da
nagarta. 4 Ta wurin wanan, ya bamu babban alkawari
mai daraja. Yayi wanan ne saboda ku zama masu rabo
cikin Allahntaka, yayin da ku ka kubuta daga lalacewa
da ke cikin duniya saboda mugayen sha'awace sha,
awace. 5 Saboda wanan dalilin kuyi iyakacin kokarinku
ku kara nagarta ta wurin bangaskiyarku, kuma ta
wurin adalci, sani. 6 Ta wurin sani ku kara da kamun
kai, kuma ta wurin kamun kanku, ku kara da jimrewa,
ta wurin jimrewarku, ku kara da bin Allah. 7 Ta
wurin bin Allah, ku kara da kauna irin ta 'yan'uwa,
ta wurin kauna irin ta 'yan'uwa, ku kara kauna. 8
Idan wadannan abubuwan suna cikinku, kuma suka yi
girma a cikinku, baza a sami bakarare ko rashin 'ya'ya
cikin sanin Ubangijinmu Yesu Almasihu ba. 9 Amma
duk wanda ya rasa wadannan abubuwan yana kallon
abin da ke kusa ne kawai; ya makance. Ya manta da
cewa an wake shi daga tsofaffin zunubansa. 10 Saboda
haka, 'yan'uwa, kuyi iyakacin kokari ku tabbatar da
kiranku da zabenku. Idan kun yi wadannan abubuwan,
baza ku yi tuntube ba. 11 Ta haka zaku sami shiga cikin
mulki na har'abada na Ubangijinmu da Maicetonmu
Yesu Almasihu. (aiōnios g166) 12 Saboda haka a shirye
nake kulayomi in tunashe ku game da wadannan
abubuwan, ko da yake kun san su, kuma kun yi karfi
cikin gaskiya yanzu. 13 Ina tunani daidai ne in zuga
ku da tuni game da wadannan abubuwan, tun ina
cikin wannan jiki. 14 Domin na sani jim kadan zan
bar wannan jiki, kamar yadda Yesu Almasihu ya nuna
mani. 15 Zan yi iyakancin kokarina kulayomi domin ku
rika tunawa da abubuwan, bayan kaurata. 16 Domin
bamu bi labaru da aka kago na nuna wayo cikinsu
ba, da muka fada maku game da iko da bayyanuwar
Ubangijinmu Yesu Almasihu, amma mu shaidu ne
na ikonsa. 17 Gama ya karbi daukaka da daraja daga
wurin Allah Uba lokacin da murya ta zo daga ikon mai
daukaka cewa, "Wannan shine dana, kaunataccena,
wanda nake jin dadinsa kwarai." 18 Mun ji muryar
nan da ta zo daga sama, lokacin da mu ke tare da shi a
dutse mai tsarki. 19 Muna da wannan kalmar annabci
wanda akwai tabbaci sosai, kun yi daidai idan kun
mayar da hankali a kansu. Yana nan kamar fitillar da
take walkiya a wuri mai duhu kafin asubahi ya zo,
kuma taurarion asubahi ya tashi cikin zukatanku. 20
Ku san da wannan tun da farko, cewa babu annabci da
ke bisa ga fasarar mutum. 21 Domin babu annabcin da
ya taba zuwa ta wurin nufin mutum. Maimakon haka,
Ruhu Mai Tsarki ne ke iza su, su fadi maganar Allah.

**2** Annabawan karya sun zo ga mutane, hakannan
kuma malaman karya suma sun zo. A asirce za su
zo maku da karkatacciyar koyarwa mai hallakarwa, su
kuma yi musun sanin Ubangiji da ya fanshe su. Su
na jawowa kansu hallaka da sauri. 2 Da yawa za su
bi gurbinsu, kuma ta wurinsu za a sabawa sahihiyar
gaskiya. 3 Ta wurin hadama za su ribace ku ta wurin
maganganunsu na yaudara. Hallakarsu ba za ta yi
jinkiri ba; hukuncinsu na nan tafe. 4 Allah bai kebe
mala'ikkun da suka yi zunubi ba. Maimakon haka
ya tura su a cikin bakin duhun jahannama daure da
sarkoki, har ya zuwa ranar shari'a. (Tartaroō g5020) 5
Hakan nan kuma bai kebe duniya ta zamanin da ba.
Maimakon haka, ya kebe Nuhu, wanda yake wa'azin
adalci, tare da mutane bakwai, lokacin da ya kawo
ambaliyar ruwan Tsufana a fuskar duniyar marasa bin
Allah. 6 Sa'annan Allah ya kone biranen Sadoma da
Gomrata da wuta ya maishe su toka, wannan ya zama
misalin abin da zai faru da marasa ibada. 7 Amma
ga adalinnan Lutu, wanda ya zaku a ransa ta wurin
miyagun halayen mutanen, Ubangiji kuwa ya cece shi.
8 Ga wannan mutum mai adalci, wanda yayi zama a
cikinsu kowace rana ransa na baci, domin abin da yake
gani yake kuma ji. 9 Saboda haka Allah ya san yadda
zai ceci masu adalci daga gwaji, da yadda kuma zai
kama masu rashin adalci da hukunci a ranar shari'a.
10 Wannan kuwa musamman gaskiya ce ga wadanda
suka ci gaba da ayyuka na jiki suka kuma raina masu
mulki. Suna da taurin kai da kuma yin ganin dama. Ba
sa tsoron sabo ga wadanda aka daukaka. 11 Ko da shike
mala'iku suna da karfi da iko fiye da su, amma basu
kawo karar batanci a kansu a gaban Ubangiji ba. 12
Amma wadannan dabbobi marassa tunani an yi su ne
musamman domin a kama a yanka. Suna sabawa abin
da ba su sani ba. Zasu halaka. 13 Za su sami sakamakon
mugun aikinsu. Suna tunanin yin nishadi da rana

abin annashuwa ne. Su kan su tababbu ne. Suna jin
dadin ayyukansu na yaudara yayin da suke liyafa
tare da ku. 14 Suna da idanun sha'awace sha'awacen
mata mazinata; ba sa koshi da aikata zunubi. Suna
rinjayar wandanda ba su da tsayayyan hankali zuwa
ga munanan ayyuka, kuma sun kafa zukatansu ga
hadama, su 'ya'yan la'ana ne! 15 Sun bar bin hanyar
gaskiya. Sun bijire kuma sun bi hanyar Bal'amu dan
Be'or wanda yake kaunar ribar rashin adalci. 16 Amma
ya karbi tsautawa domin zunubinsa. Jaki ma da baya
magana ya tsauta wa haukan annabin da muryar dan
adam. 17 Wadannan mutane suna kamar mabulbullai
da babu ruwa. suna nan kamar gizagizai da iska ke
korawa. Duhu mai tsanani yana jiransu. 18 Su masu
babatu ne da girman kai. suna yadaurar mutane ta
wurin sha'awowin jiki. Suna yaudarar mutane da suke
kokarin su tsere daga wadanda suke rayuwa cikin
kuskure. 19 Suna masu alkawarin yanci, amma su da
kan su bayi ne ga zunubi. Domin mutum bawa ne ga
duk abinda ya rinjaye shi. 20 Duk wanda ya kubuta
daga shashanci na duniya ta wurin sanin Ubangiji
da mai Ceto Yesu Almasihu, sa'annan ya koma cikin
shashaci, yanayinsu na karshe ya zama da muni fiye
da na farkon. 21 Da ma zai fi masu kada su san hanyar
adalci da su san ta amma sa'annan su juya daga ka'ida
mai tsarki wanda aka damka masu. 22 Wannan karin
magana ya zama gaskiya a kan su: “Kare ya dawo yana
lashe amansa. Aladen da akayi masa wanka ya koma
cikin tabo.”

**3** Yanzu, ina rubata maku, kaunatattu, wannan
wasika ta biyu domin in tunashe ku, in kuma zuga
tunaninku na gaskiya, 2 don ku tuna da kalmomin da
annabawa tsarkaka suka fada a da, kuma da umurnin
Ubangijinmu da mai ceto da aka bayar ta wurin
manzaninku. 3 Ku san wannan da farko, cewa masu
ba'a za su zo a kwanakin karshe. Za su yi ba'a kuma
su ci gaba bisa ga sha'awowinsu. 4 Za su ce, “Ina
alkawarin dawowarsa? Tun lokacin da kakaninmu
suka mutu, dukkan abubuwa sun kasance yadda suke,
tun farkon halitta.” 5 Da gangan suka manta cewa
sama da kasa sun kasance daga ruwa, kuma ta wurin
ruwa, da dadewa ta wurin umarnin Allah, 6 kuma
cewa ta wurin wadannan abubuwa duniyar wancan
zamani ta halaka, da ambaliyar ruwan tsufana. 7
Amma sama da kasa na yanzu, an tanada su domin
wuta ta wurin wannan umarnin. An tanada su domin
ranar shari'a da halakar marassa ibada. 8 Kada ku
manta da wanan, kaunatattu, cewa rana daya a gun
Allah kamar shekaru dubu ne, kuma shekaru dubu
kamar rana daya suke. 9 Ubangiji baya jinkiri game da
alkawaransa kamar yadda wadansu ke ganin jinkiri.
Maimakon haka, yana hakuri da ku. Ba ya so ko
dayanku ya hallaka, amma kowanenku ya kai ga tuba.
10 Duk da haka, ranar Ubangiji za ta zo kamar barawo.
Sammai za su shude da kara mai karfi. Wuta zata kone
komai da komai, kuma duniya da dukkan ayyukan da
ke cikinta zasu bayyanu. 11 Da shike dukkan wadanan
abubuwa za a hallaka su haka, wadanne irin mutane
yakamata ku zama? Ya kamata kuyi rayuwar tsarki da
ta ibada. 12 Ku zauna cikin bege da kuma hanzarta
zuwan ranar Allah. A ranan nan, za a hallaka sammai
da wuta, kuma dukkan komai da komai zai narke cikin
zafi mai tsanani. 13 Amma bisa ga alkawarinsa, muna
jiran sabuwar sama da sabuwar duniya, inda adalci zai
kasance. 14 Saboda haka, kaunatattu, tun da kuna da
begen wadannan abubuwa, ku yi iyakacin kokarinku
a same ku marassa tabo da marasa aibu a gabansa,
cikin salama. 15 Kuma, ku dauki hakurin Ubangiji
domin ceto ne, kamar yadda kaunataccen danuwanmu
Bulus ya rubuta maku bisa ga hikima da aka ba
shi. 16 Bulus yayi magana akan wadanan abubuwa
cikin dukkan wasikunsa, a ciki akwai abubuwa da
suke da wuyar ganewa. Jahilai da mutane marassa
natsuwa sukan juya ma'anarsu, kamar yadda suke yi
wa sauran nassoshi, don hallakar kansu. 17 Saboda
haka, kaunatattu, tun da kun san wadannan abubuwa,
ku kula da kanku kada a badda ku ta wurin rudun
mutanen da ba su bin doka, har ku rasa amincinku. 18
Amma ku yi girma a cikin alheri da sanin Ubangijinmu
da mai ceto Yesu Almasihu. Bari daukaka ta tabbata a
gare shi yanzu da har abada. Amin. (aiōn g165)

# 1 Yohanna

1 Abin nan da yake tun daga farko, wanda muka ji,
wanda muka gani da idanunmu, wanda muka gani
hannuwanmu suka kama, a wajen maganar rai. 2 Ran
kuwa aka baiyyana shi, muka gani, muka bada shaida,
muka gaya maku labarin rai na har abada, wanda da
yake a wurin Uba, aka kuma sanar da mu. (aiōnios g166)
3 Wannan da muka gani muka ji muka baku labari,
domin kuyi zumunci da mu, zumuncinmu kuwa tare
da Uba yake da Dansa Yesu Almasihu. 4 Haka nan,
muna rubuta maku wadannan abubuwa domin farin
cikinmu ya cika. 5 Wannan shi ne sakon da muka ji
daga wurinsa mu kuwa muka sanar da ku: Allah haske
ne a wurinsa kuwa babu duhu ko kadan. 6 Idan mun ce
muna zumunci da shi kuma muna tafiya cikin duhu,
muna yin karya kuma bama aikata gaskiya. 7 Amma
idan muna tafiya cikin haske kamar yadda yake cikin
haske, muna zumunci da juna, jinin Yesu Dansa ya
wankemu daga dukka zunubi. 8 Idan mun ce bamu da
zunubi, muna rudin kanmu kenan, ba kuma gaskiya a
cikinmu. 9 Amma idan mun fadi zunubanmu, shi mai
aminci ne, mai adalci da zai gafarta mana zunubanmu,
ya kuma wankemu daga dukkan rashin adalci. 10 Idan
mun ce bamu yi zunubi ba, mun mai da shi makaryaci
kenan, maganarsa kuma bata cikinmu.

2 'Ya'yana, na rubuta ma ku wadannan abubuwa
domin kada kuyi zunubi. Amma idan wani yayi
zunubi muna da matsakanci a wurin Uba, Yesu
Almasihu, mai adalci. 2 Shine fansar zunubanmu,
ba ma namu kadai ba amma na duniya dukka. 3
Ta haka muka san cewa mun san shi, idan mun
kiyaye dokokinsa. 4 Duk wanda yace, "Na san Allah"
amma bai kiyaye dokokinsa ba, makaryaci ne gaskiya
kuwa ba ta cikinsa. 5 Amma duk wanda ya kiyaye
maganarsa, hakika kaunar Allah ta kammala a cikin
wannan mutum. Ta wurin haka muka sani muna
cikinsa. 6 Duk wanda yace yana cikin Allah dole ne shi
da kansa yayi tafiya kamar yadda Yesu Almasihu yayi.
7 Kaunatattu, ba sabuwar doka nike rubuta maku ba,
amma tsohuwar doka ce wadda kuka ji tun farko.
Tsohuwar dokar kuwa itace maganar da kuka ji tun
farko. 8 Amma yanzu ina rubuta maku sabuwar doka
wadda gaskiya ce a cikin Almasihu da cikinku, saboda
duhu yana wucewa, haske na gaskiya yana haskakawa.
9 Duk wanda yace yana cikin haske amma yana kin
dan'uwansa, yana cikin duhu har yanzu. 10 kuma
wanda yake kaunar dan'uwansa yana cikin haske
babu dalilin tuntube a wurinsa. 11 Amma duk wanda
yake kin dan'uwansa yana cikin duhu, yana kuma
tafiya cikin duhu, bai san ma inda ya nufa ba, domin
duhu ya makantar da shi. 12 Na rubuta maku, ya
ku kaunatun 'ya'yana, saboda an gafarta zunubanku
domin sunansa. 13 Na rubuta maku, ubanni, saboda
kun san shi wanda yake tun daga farko. Na rubuta
maku matasa saboda kun yi nasara da mugun. Na
rubuta maku, yara kanana, saboda kun san Uban. 14 Na
rubuta maku, Ubanni, saboda kun san shi wanda yake
tun daga farko. Na rubuta maku, matasa, saboda kuna
da karfi, kuma maganar Allah tana zaune cikinku.
Kuma kun yi nasara da mugun. 15 Kada kuyi kaunar
duniya ko abubuwan da suke cikin duniya. Idan wani
yayi kaunar duniya, kaunar Uban bata cikinsa. 16
Domin dukkan abubuwan da suke a cikin duniya,
kwadayi na jiki, abin da idanu suke sha'wa, da rayuwar
girman kai ta wofi, ba na Uban bane amma na duniya
ne. 17 Duniya tana wucewa tare da sha'awarta. Amma
dukkan wanda ya aikata nufin Allah zaya kasance
har abada. (aiōn g165) 18 Yara kanana, sa'a ta karshe
ce. Kamar dai yadda kuka ji magafcin Almasihu yana
zuwa, ko yanzu ma magaftan Almasihu da yawa sun
rigaya sun zo, ta haka muka san sa'a ta karshe ce. 19
Sun fita daga cikinmu, dama su bana cikinmu bane.
Gama idan da su namu ne da sun ci gaba tare damu.
Amma da yake sun fita, ya nuna su ba na cikinmu
bane. 20 Amma ku kun karbi shafewa daga wurin
Mai Tsarki, kuma dukkanku kun san gaskiya. 21 Bana
rubuta maku bane domin baku san gaskiya ba, amma
saboda kun santa, kuma ba wata karya da ta fito daga
gaskiya. 22 Wanene makaryaci shine wanda yayi musu
cewa Yesu ba Almasihu bane? Wannan mutumin shi
ne magafcin Almasihu, tun da yayi musun Uba yayi
musun Dan. 23 Ba wanda yayi musun Dan kuma yake
da Uban. Dukkan wanda ya amince da Dan yana da
Uban ma. 24 A game daku kuma, sai ku bari abinda
kuka ji daga farko ya zauna a cikinku. Idan abin da
kuka ji daga farko ya zauna a cikinku, kuma zaku
kasance a cikin Dan da kuma Uban. 25 Alkawarin da ya
bamu kenan, rai na har abada. (aiōnios g166) 26 Na rubuta
maku wadannan abubuwa ne game da wadanda zasu
baudar daku. 27 Game daku, shafewar daku ka samu
daga wurinsa tana nan a cikinku, baku bukatar wani
ya koyar daku. Amma kamar yadda shafewar da kuka

karba a wurinsa ta koya maku dukkan abu, kuma
gaskiya ne ba karya bane, tana nan a cikinku kamar
yadda a ka koya maku, ku kasance a cikinsa. 28 Yanzu
fa, 'ya'ya na kaunatattu, ku kasance a cikinsa domin
sa'adda zai baiyyana mu zama da gabagadi ba tare da
kunya ba a gabansa sa'adda zai zo. 29 Idan kun sani
shi mai adalci ne, kun sani dukkan wanda ke aikata
adalci haifaffe ne daga wurinsa.

3 Dubi irin kaunar da Allah ya bamu, har da za a kira
mu 'ya'yan Allah, haka muke kuwa. Saboda wannan
dalili ne duniya bata san muba, saboda bata san shi
ba. 2 Kaunatattu, yanzu mu 'ya'yan Allahne, kuma
ba a bayyana mana yadda zamu zama ba tukuna,
mun sani sa'adda Almasihu zai bayyana, zamu zama
kamarsa, domin zamu ganshi kamar yadda yake. 3
Dukkan wanda yake da wannan bege game da gidan
gobe ya kan tsarkake kansa, kamar yadda shima yake
da tsarki. 4 Dukkan wanda yaci gaba da yin zunubi
yana ketare shari'a kenan. Gama zunubi ketare shari'a
ne. 5 Kun sani Almasihu ya bayyana domin ya dauke
zunubai ne. Kuma a cikinsa babu zunubi. 6 Ba wanda
zai kasance a cikinsa da zai cigaba da yin zunubi.
Ba wanda zai ci gaba da aikata zunubi da zai ce ya
sanshi, ko kuma ya ganshi. 7 'Ya'yana kaunatattu,
kada ku bari kowa ya baudar da ku, wanda yake aikata
adalci shi adali ne, kamar yadda Almasihu yake adali.
8 Wanda yake aikata zunubi na ibilis ne, gama ibilis
yayi zunubi tun daga farko. Dalilin haka ne Dan Allah
ya bayyana, domin ya rushe ayyukan ibilis. 9 Duk
wanda aka haife shi daga Allah ba ya yin zunubi,
saboda irin Allah na cikinsa. Ba zaya iya ci gaba da
yin zunubi ba domin an haife shi daga wurin Allah. 10
Ta haka ne ake bambanta 'ya'yan Allah da 'ya'yan
ibilis. Dukkan wanda baya aikata adalci ba na Allah
bane; haka kuma wanda ba ya kaunar dan'uwansa. 11
Domin wannan shine sakon da kuka ji tun daga farko:
cewa mu kaunaci junanmu, 12 ba kamar Kayinu ba
wanda yake na shaidan kuma ya kashe dan'uwansa.
Me yasa ya kashe shi? Saboda ayyukansa miyagu ne,
na dan'uwansa kuma masu adalci ne. 13 Kada kuyi
mamaki 'yan'uwana, idan duniya ta ki ku. 14 Mun
sani mun ratsa mutuwa zuwa cikin rai, saboda muna
kaunar 'yan'uwa. Dukkan wanda ba ya yin kauna, shi
matacce ne. 15 Dukkan wanda yake kin dan'uwansa,
mai kisan kai ne. Kun kuma sani babu rai na har
abada a cikin mai kisankai. (aiōnios g166) 16 Ta wurin
haka muka san kauna, da ya ke Almasihu ya bayar da
ransa saboda mu. Mu ma ya kamata mu bada ranmu
saboda 'yan'uwamu. 17 Amma duk wanda yake da
kayan duniya, ya ga dan'uwansa cikin bukata, kuma
bai ji tausayinsa ba, ta yaya kaunar Allah ke cikinsa?
18 'Ya'yana kaunatattu, kada muyi kauna ta fatar
baki kawai, amma muyi aikin kauna da gaskiya. 19
Ta wurin haka mun sani mu masu gaskiya ne kuma
mun tabbatar da zuciyarmu a gabansa. 20 Gama idan
zuciyarmu bata kayar damu ba, Allah ya fi zuciyarmu
girma, kuma yana sane da kome. 21 Kaunatattu, idan
zuciyarmu bata kashe mu ba, muna da gabagadi a
gaban Allah. 22 Kuma duk abin da muka nema zamu
samu a wurinsa, saboda muna kiyaye dokokinsa,
muna yin abubuwan da suka gamshe shi. 23 Kuma
ummurninsa kenan: mu bada gaskiya ga sunan Dansa
Yesu Almasihu, mu yi kaunar juna kuma kamar yanda
ya bamu wannan doka. 24 Duk wanda yake kiyaye
umarnin Allah, yana cikinsa, Allah kuma yana cikin
mutumin. Ta haka muka gane cewa yana cikinmu, Ta
wurin Ruhu, wanda ya bamu.

4 Kaunatattu, kada ku amince da kowanne ruhu.
Amma ku gwada ruhohi ku gani ko na Allah ne,
gama annabawan karya masu yawa sun fito zuwa
cikin duniya. 2 Ta haka zaku gane Ruhun Allah,
dukkan ruhun da ya amince Yesu Almasihu ya zo
cikin jiki na Allah ne, 3 kuma dukkan ruhun da bai
amince da Yesu ba, ba na Allah bane. Wannan ruhun
magafcin Almasihu ne, wanda kuka ji cewa yana
zuwa, ya kuwa rigaya yazo cikin duniya. 4 'Ya'yana
kaunatattu, daga Allah ke, kuma kun rigaya kun yi
nasara da su da yake wanda ke cikinku ya fi wanda ke
cikin duniya girma. 5 Su na duniya ne, saboda haka
abin da suke fadi na duniya ne, duniya kuma tana
sauraronsu. 6 Mu na Allah ne, duk wanda ya san Allah
yana saurarenmu. Wanda ba na Allah bane, ba ya
sauraronmu. Ta haka muka gane ruhun gaskiya da
ruhun karya. 7 Kaunatattu, mu yi kaunar juna, gama
kauna ta Allah ce, wanda yake kauna an haife shi daga
wurin Allah, kuma ya san Allah. 8 Mutumin da baya
kauna ba na Allah ba ne, kuma bai san Allah ba, gama
Allah kauna ne. 9 A cikn haka aka bayyana kaunar
Allah a garemu, Allah ya aiko tilon Dansa cikin duniya
domin mu rayu ta wurinsa. 10 A cikin wannan akwai
kauna, ba mune muka kaunaci Allah ba, amma shi ya
kaunace mu ya aiko da Dansa ya zama mai gafarta

zunubanmu. 11 Kaunatattu, da yake Allah ya kaunace
mu haka, ya kamata mu kaunaci junanmu. 12 Ba
wanda ya taba ganin Allah. Idan muna kaunar juna,
Allah yana zaune cikinmu, kuma kaunarsa tana zaune
a cikinmu. 13 Ta haka mun sani muna zaune a cikinsa
shi kuma a cikinmu, saboda ya bamu Ruhunsa. 14
Mun gani mun shaida, cewa Allah ya aiko Dan, domin
ya zama mai ceton duniya. 15 Duk wanda ya amince
Yesu Dan Allah ne, Allah na zaune cikinsa, shi kuma a
cikin Allah. 16 Mun sani kuma mun gaskata da kaunar
da Allah yake da ita dominmu, Allah kauna ne wanda
yake zama cikin kauna yana zaune cikin Allah, Allah
kuma a cikinsa. 17 Dalilin wannan kauna ta kammala
a cikinmu, domin mu kasance da gabagadi a ranar
shari'a, domin kamar yanda ya ke haka muma muke
a cikin duniyan nan. 18 Babu tsoro a cikin kauna.
Amma cikkakiyar kauna takan kawar da tsoro, domin
kuwa tsoro na tafi tare da hukunci. Amma wanda
yake da tsoro ba shi da cikkakiyar kauna. 19 Muna
kauna domin Allah ne ya fara kaunarmu. 20 Idan wani
ya ce,"Ina kaunar Allah", amma yana kin dan'uwansa,
makaryaci ne. Domin wanda baya kaunar dan'uwansa
da yake gani, ba zai iya kaunar Allah da bai taba
gani ba. 21 Wannan ne umarnin da muke da shi daga
wurinsa: Duk wanda yake kaunar Allah dole ne ya
kaunaci dan'uwansa.

**5** Duk Wanda ya gaskata Yesu shine Almasihu haifaffe
na Allah ne. Kuma duk wanda ya kaunaci uba ya
kaunaci dan da uban ya haifa. 2 Haka muka sani muna
kaunar 'ya'yan Allah: yayin da muka kaunaci Allah,
kuma muka aikata umarninsa. 3 Wannan itace kaunar
Allah, cewa mu kiyaye umarninsa. Domin umarninsa
ba masu nawaitawa bane. 4 Duk wanda yake haifaffe
na Allah yakan yi nasara da duniya. Wannan itace
nasarar da ta rinjayi duniya, wato bangaskiyarmu. 5
Wanene wannan mai nasara da duniya? Sai dai wanda
ya gaskata Yesu Dan Allah ne. 6 Wannan shine wanda
yazo ta wurin ruwa da jini: Yesu Almasihu. Ya zo
ba ta wurin ruwa kadai ba, amma ta wurin ruwa da
jini. 7 Domin akwai uku wadanda suke bada shaida: 8
Ruhu, da ruwa, da kuma jini. Wadannan ukun kuwa
manufarsu daya ce. 9 Idan mun karbi shaidar mutane,
shaidar Allah ta fi girma. Wannan ita ce shaidar Allah,
wato ya bada shaida akan Dansa. 10 Wanda ya gaskata
da Dan Allah shaidar tana nan tare da shi. Duk wanda
bai bada gaskiya ga Allah ba, ya mai da shi makaryaci
kenan, domin bai gaskata da shaidar da Allah ya bayar
game da Dansa ba. 11 Wannan ita ce shaida: Allah ya
bamu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin
Dansa. (aiōnios g166) 12 Duk wanda yake da Dan, yana
da rai. Duk wanda ba shida Dan Allah kuwa bashi da
rai. 13 Na rubuto maku wannan ne don ku tabbata
kuna da rai madawwami—a gare ku wadanda suka
gaskata da sunan Dan Allah. (aiōnios g166) 14 Wannan
shine gabagadin da muke da shi a gabansa, wato, in
mun roki kome bisa ga nufinsa, zai ji mu. 15 Haka
kuma, in mun san yana jinmu—Duk abin da mu ka
rokeshi—mun sani muna da duk abin da muka roka
daga gare shi. 16 Idan wani ya ga dan'uwansa ya
yi zunubin da bai kai ga mutuwa ba, sai yayi masa
addu'a, Allah kuwa zai ba shi rai. Ina nufin wadanda
suka yi zunubin da bai kai ga mutuwa ba. Akwai
zunubin da yake kai wa ga mutuwa: Ban ce a yi addu'a
domin wannan ba. 17 Dukkan rashin adalci, zunubi
ne, amma akwai zunubin da bai kai ga mutuwa ba. 18
Mun sani kowanne haiffafe daga wurin Allah ba ya yin
zunubi. Amma wanda ke haifaffe daga wurin Allah,
ya kan kare shi, mugun nan kuwa ba zai iya yi masa
illa ba. 19 Mun sani mu na Allah ne, mun kuma sani
dukkan duniya tana hannun mugun nan. 20 Amma
mun sani Dan Allah yazo, kuma ya bamu fahimta,
domin mu san wanda yake shi ne mai gaskiya. Haka
kuma muna cikin wannan wanda shine gaiskiya, kuma
cikin Dansa Yesu Almasihu. Shine Allah na gaskiya, da
kuma rai na har abada. (aiōnios g166) 21 'Ya'ya, ku tsare
kanku daga bautar gumaka.

# 2 Yohanna

1 Daga dattijon zuwa ga uwar gida zababbiya da
yayanta, wadanda nake kauna da gaskiya, ba ni
kadai ba, amma da dukan wadanda sun san gaskiya -
2 domin gaskiya da take cikinmu za ta kuma kasance
tare da mu har abada. (aiōn g165) 3 Alheri da jinkai da
salama za su kasance tare da mu, daga Allah Uba da
kuma daga Yesu Almasihu Dan Uba, a cikin gaskiya da
kauna. 4 Na yi murna sosai sa'anda na sami wadansu
yayanki suna tafiya cikin gaskiya, kamar yadda muka
karbi wannan umarni daga Uba. 5 Yanzu ina rokon ki,
uwar gida, ba kamar ina rubuta maki sabon umarni
ba, amma wannan da muka samu tun da can, cewa
mu kaunaci junanmu. 6 Wannan kuma itace kauna,
cewa mu yi tafiya bisa ga umarnin sa. Wannan shine
umarnin, daidai kamar yadda kuka ji da fari, da cewa
ku yi tafiya a cikinsa. 7 Gama masu yaudara sun fito a
duniya, wadanda ba su yarda cewa Yesu ya zo cikin
jiki ba. Wannan ne mayaudari da kuma magabcin
Almasihu. 8 Ku dubi kanku, domin kada ku rasa
abubuwan da mu duka muka yi aiki a kansu, amma
domin ku karba dukan sakamon ku. 9 Duk wanda ya ci
gaba da tafiya ba cikin koyarwa Almasihu ba, ba shi da
Allah. Wanda ya zauna cikin koyarwar kwa yana tare
da Uban da kuma Dan. 10 Duk wanda ya zo wurinku,
ba tare da wannan koyarwar ba, kar ku karbe shi cikin
gidanku, kada ma ku gaishe shi. 11 Domin duk wanda
ya gaishe shi ya yi tarayya da shi kenan cikin miyagun
ayyukan sa. 12 Ina da abubuwa dayawa da nake so
in rubuta maki amma al'kalami tawada da takarda
baza su iya daukar su duka ba. Amma duk da haka ina
begen zuwa gare ki domin mu yi magana fuska da
fuska, domin farin cikn mu ya zama cikakke. 13 Yayan
yar'uwarki zababbiya suna gaishe ki.

# 3 Yohanna

1 Daga dattijon zuwa ga Gayus, wanda nake kauna
da gaske. 2 Ya kaunatace na, ina addu'a domin ka
samu albarka cikin kowanne al'amari, da kuma koshin
lafiya, kamar yadda ruhun ka yake lafiya. 3 Na yi farin
ciki kwarai sa'adda wadansu 'yan'uwa suka zo suka ba
da shaida a kan bangaskiyar ka, kamar yadda ka ke
bin gaskiya. 4 Ba abin da ya fi faranta mani rai kamar
in ji yayana suna tafiya cikin gaskiya. 5 Ya kaunatace
na, kana aiki da aminci zuwa ga 'yan'uwa da baki, 6
wadanda suka shaida kaunar ka a gaban ikilisiya. Zai
yi kyau ka yi masu taimako da kyakkyawar salama, ta
hanyar da ta dace da masu ibada, 7 domin sabili da
sunan nan ne suka fito, ba su kuma karbar kome a
hannun al'ummai. 8 Don haka ya kamata mu karbi
irin wadannan mutane, domin mu zama abokan aiki
tare da su a kan gaskiya. 9 Na rubuta wasika zuwa
ga ikilisiya, amma Diyotariffis, wanda ya fi kowa son
girma a cikinsu, bai karbe mu ba. 10 Saboda haka, idan
na zo, zan tuna masa da irin ayukkan sa, da kuma
yadda yake babbata sunayen mu a wurin jama'a da
miyagun kalmomi. Wannan ma bai ishe shi ba, har
ma yana kin karbar 'yan'uwa. Ya kuma hana wadanda
suke son su yin hakan, harma ya kan kore su daga
ikilisiya. 11 Ya kaunatace na, kada ka yi koyi da mugun
abu, sai dai abu mai kyau. Dukan wanda yake yin
abu mai kyau na Allah ne; mai aikata mugunta kuma
bai san Allah ba. 12 Dimitiriyas yana da kyakkyawar
shaida a gun kowa har a wurin gaskiyar da kanta.
Mu ma mun shaida shi, ka kuma san shaidar mu
gaskiya ce. 13 Ina da abubuwa dayawa da zan rubuta
maka, amma ban so in rubuta maka su da alkalami da
tawada ba. 14 Ina sa zuciya mu sadu ba da dadewa ba,
sa'annan mu yi magana ido da ido. Bari salama ta
kasance tare da kai. Abokanmu suna gaishe ka, kuma
ka isadda sakon gaisuwar mu ga sauran abokai da
sunayen su.

# Yahuda

1 Yahuza, bawan Yesu Almasihu kuma dan'uwan
Yakubu, zuwa ga kirayayyu, kaunatattu a cikin
Allah Uba, kebabbu domin Yesu Kristi: 2 bari jinkai da
salama da kauna su ribabanya a gare ku. 3 Kaunatattu,
ina iyakar kokari in rubuta maku game da ceton
mu duka, ya zama dole in gargade ku sosai game da
bangaskiya wadda aka mika wa masu bi sau daya
tak ba kari. 4 Don wasu mutane sun sadado sun
shigo da sanda a asirce wadanda an rubuta game da
hukuncin su tun da dadewa-mutane marasa imani,
wanda suka canza alherin Allah zuwa lalata, kuma
sun karyata makadaicin Shugaba da Ubangijinmu,
Yesu Almasihu. 5 Ina so in tunashe ku-ko da shike
kun rigaya kun san abin, da cewa Allah ya ceci wasu
mutane daga kasar masar, amma daga baya ya hallaka
wadanda basu ba da gaskiya ba. 6 Kuma mala'iku
wadanda ba su rike matsayin ikon su ba, amma suka
bar wurin zaman su na ainihi-Allah ya tsare su a
sarka na har'abada a cikin bakin duhu domin babban
ranar shari'a. (aïdios g126) 7 Suna nan kamar Saduma
da Gwamrata da kuma biranen da ke kewaye da su,
wadanda suka ba da kansu ga fasikanci suna bin
sha'awoyi wanda ba na dabi'a ba. Aka mai da su
abin misalin wadanda suka sha wuta mara matuka.
(aiōnios g166) 8 Haka kuma, wadannan masu mafarkan
suna lalatar da jikinsu. Suna raina masu mulki, kuma
suna fadar miyagun abubuwa a kan masu daukaka.
9 Amma ko Mika'ilu babban mala'ika, a lokacin da
yake jayyaya da muhawara da shaidan a kan gawar
Musa, bai kuskura ya fadi wata kalmar hukunci a
kansa ba. Maimakon haka ya ce, “Bari Ubangiji ya
tsauta maka!'' 10 Amma waddannan mutane suna
kawo batanci game da dukan abin da ba su gane ba.
Wadannan mutane masu halin dabbobi ne, suna kwa
jawo wa kansu hallaka kenan. 11 Kaiton su! Domin
sun bi hanyar Kayinu, kuma sun tsunduma cikin
kuskuren Bal'amu domin samun riba. Suka hallaka
cikin husuma irin ta Kora. 12 Wadannan hatsari ne
a boye cikin bukukuwan ku na kauna. Suna shagali
ba kunya ba tsoro, suna ciyar da kansu kadai. Su
holokon hadari ne marar ruwa, wanda iska ke korar
sa. Su itatuwa ne shirim ba yaya, mattatu ribi biyu,
tumbukakku tun daga saiwa. 13 Su rakuman teku ne
masu hauka, suna fahariya cikin kumfar kunyar su.
Su kamar taurari ne masu tartsatsi. Wadanda aka
tanada wa duhu baki kirin na har abada. (aiōn g165)
14 Ahnuhu, mutum na bakwai daga Adamu, ya yi
anabci game da su cewa, “Duba, Ubangiji zai zo da
tsarkakan sa dubun dubbai. 15 Domin ya zartar da
hukunci a kan dukan kowa, ya kuma cakune dukan
marasa da'a a cikin dukan ayyukan su na rashin da'a
wanda suka aikata a hanyar da bata cancanta ba, da
kuma kalmomi masu kaifi da masu zunubi suka fada
game da shi.” 16 Wadannan masu cecekuce ne, masu
gunaguni, wadanda ke bin sha'awar su ta mugunta,
masu tinkaho da fahariya, masu bambadanci domin
ribar kansu. 17 Amma ku, kaunatattu, ku tuna da
kalmomin da manzannin Yesu Almasihunmu suka
gaya maku tun da. 18 Sun ce maku, “A cikin kwanaki
na karshe, za a samu masu ba'a, wadanda ke bin
sha'awoyin su na rashin ibada,” 19 Wadannan mutane
masu haddasa tsatsaguwa ne, kuma su yan duniya ne,
ba su kuma da Ruhu. 20 Amma ku, kaunatattu, ku
gina kanku a cikin mafificiyar bangaskiyar ku mai
daraja, kuma kuna addu'a a cikin Ruhu Mai Tsarki. 21
Ku rike kanku a cikin kaunar Allah, kuna kuma jiran
jinkan Ubangijinmu Yesu Almasihu wanda ke kawo rai
na har abada. (aiōnios g166) 22 Ku nuna jinkai ga masu
shakku. Ceci wadansu ta wurin fizge su daga wuta. 23
Ga wadansu kuma ku nuna jinkai da rawar jiki, kuyi
kyamar koda tufafin jikinsu ma. 24 Yanzu, zuwa ga
wanda yake da iko ya hana ku tuntube, ya kuma sa ku
tsaya a gaban madaukakiyar kasancewarsa, marasa
abin zargi da kuma murna mai yawa, 25 zuwa ga Allah
makadaici mai ceton mu ta wurin Yesu Almasihu
Ubangijinmu, daukaka, da girma, da mulki, da iko su
kasance, kamin dukan lokuta, yanzu, da har abada.
Amin. (aiōn g165)

# Ru’uya ta Yohanna

**1** Wannan shine wahayin Yesu Almasihu da Allah
ya bashi ya nuna wa bayinsa abinda zai faru ba
da dadewa ba. Ya bayyana wannan ta wurin aiko da
mala'ikansa ga bawansa Yahaya. 2 Yahaya yayi shaida
akan abinda ya gani game da maganar Allah da kuma
shaidar da aka bayar game da Yesu Almasihu. 3 Mai
albarka ne wanda ke karanta littafin nan da murya
mai karfi, da kuma wadanda ke saurararon kalmomin
wannan annabci kuma suke biyayya da abinda aka
rubuta a ciki, domin kuwa lokaci ya kusato. 4 Ni
Yahaya, zuwa ga ikilisiyoyi bakwai na kasar Asiya:
alheri zuwa gare ku da salama daga wanda ke yanzu,
wanda ya kuma kasance a da, shi ne kuma mai zuwa
nan gaba, kuma daga ruhohin nan bakwai da ke gaban
kursiyinsa, 5 kuma daga Yesu Almasihu, wanda ke
amintaccen mashaidi, dan fari na tashi daga cikin
matattu, kuma mai mulkin sarakunan duniya. Ga
wanda ya ke kaunar mu ya kuma kwance mu daga
daurin zunubanmu ta wurin jininsa, 6 ya maishe
mu masu mulki, firistoci na Allahnsa da Ubansa -
daukaka da iko su tabbata gare shi har abada abadin,
Amin. (aiōn g165) 7 Duba yana zuwa tare da gizagizai,
kowane ido zai gan shi, har ma da wadanda suka
soke shi. Haka kuma dukkan kabilun duniya za su yi
makoki saboda da shi. I, Amin. 8 “Nine na farko da na
karshe”, in ji Ubangiji Allah, “Wanda yake shine a
yanzu, shine wanda ya kasance a da, kuma shi ne mai
zuwa nan gaba, Mai iko duka.” 9 Ni, Yahaya- dan'uwan
ku da wanda ke tarayya daku cikin shan wahala, da
mulki da tsawon jimrewa wadanda ke cikin Yesu -
ina tsibirin da ake kira Batmusa saboda maganar
Allah da kuma shaida game da Yesu. 10 Ina cikin
Ruhu a ranar Ubangiji. Sai naji wata murya mai karfi
a baya na kamar ta kaho. 11 Ta ce, “Rubuta abinda
ka gani a cikin littafi, ka kuma aika wa ikilisiyoyin
nan bakwai - ga Afisus, ga Simirna, ga Birgamas,
ga Tayatira, ga Sardisu, ga Filadalfiya, da kuma ga
Laudikiya.” 12 Na juya don in ga wanda muryarsa
ke magana da ni, da na juya sai na ga fitilu bakwai
akan madorin su 13 A tsakiyar fitilun akwai wani mai
kama da dan mutum, yana sanye da doguwar tufa
har tafin sawunsa, da damara ta zinariya kewaye a
kirjinsa. 14 Kansa da gashinsa fari fat kamar auduga -
kamar dusar kankara, kuma idanun sa kamar harshen
wuta. 15 Kafaffunsa kamar gogaggiyar tagulla, kamar
tagullar da aka tace da wutar makera, muryar sa
kuma kamar kugin ambaliyar ruwan teku ne. 16
A hannunsa na dama yana rike da taurari bakwai,
daga bakinsa kuma kakkaifan takobi mai kaifi biyu ke
fitowa. Fuskarsa tana haskakawa kamar sa'adda rana
ke haskakawa kwarai. 17 Lokacin da na gan shi, na
fadi kamar mataccen mutum a kafaffunsa. Ya dora
hannunsa na dama a kaina ya ce, “Kada ka ji tsoro.
Nine na farko da na karshe, 18 da kuma wanda ke
raye. Na mutu, amma duba ina raye har abada! Kuma
ina da mabudin mutuwa da na hades. (aiōn g165, Hadēs
g86) 19 Domin haka ka rubuta abinda ka gani, abin
da ke yanzu, da abin da zai faru bayan wanan. 20
Akan boyayyar ma'ana game da taurari bakwai da
ka gani a hannun dama na, da madorin fitilu bakwai
na zinariya: Taurarin nan bakwai mala'iku ne na
ikilisiyoyi bakwai, kuma madorin fitilun nan bakwai
ikilisiyoyi ne bakwai.

**2** ''Zuwa ga mala'ikan dake ikilisiyar Afisus, ka
rubuta: 'Wadannan sune kalmomin wanda ke rike
da taurari bakwai a cikin hannun damarsa. wanda yake
tafiya a tsakanin zankayen fitilun zinari bakwai, 2 ''Na
san abubuwan da ka yi, da famar ka, da hakurinka da
jimirinka. Na sani ba ka jimrewa miyagun mutane, na
sani ka gwada wadanda suka ce da kansu, su manzanni
ne, amma ba haka ba, ka tarar da su makaryata. 3
Na san kana da tsawon jimrewa, kuma ka sha wahala
sosai sabili da sunana, kuma baka gaji ba. 4 Amma ga
rashin jin dadi na da kai, ka bar kaunar ka ta fari. 5
Domin haka ka tuna daga inda ka fadi. Ka tuba ka yi
abubuwan da ka yi da fari. Sai fa ka tuba, zan zo maka
in kuma cire fitilar ka daga mazauninta. 6 Amma kana
da wannan: Ka tsani abubuwan da Nikolatawa suka yi,
wanda nima na tsana. 7 wanda yake da kunnen ji ya
saurari abinda Ruhu yake fada wa ikilisiyoyi. Ga wanda
yayi nasara zan bashi dama ya ci daga itacen rai,
wanda ke cikin firdausin Allah.'' 8 Zuwa ga mala'ikan
da ke Ikilisiliyar Samirna rubuta: 'Wadannan su ne
kalmomin wanda yake shine farko shine karshe,
wanda ya mutu ya sake rayuwa kuma. 9 ''Na san
wahalun ka da talaucin ka amma kana da arziki. Nasan
masu bata suna wadanda suke cewa su Yahudawa ne,
amma ba haka suke ba. Su majami'ar Shaidan ne. 10
Kada ka ji tsoron wahalar da zaka fuskanta nan gaba.
Duba! Shaidan yana gab da jefa wadansun ku cikin
kurkuku, domin a gwada ku, kuma zaku sha wahala

ta kwana goma. Kuyi aminci har ga mutuwa zan
baku rawanin rai. 11 wanda yake da kunne ya saurari
abinda Ruhu yake fada wa ikilisiyoyi. Shi wanda yayi
nasara ba zai cutu a mutuwa ta biyu ba."" 12 ''Zuwa ga
mala'ikan dake ikilisiyar Burgamas rubuta: 'Wadannan
ne kalmomin wanda ya ke da takobi mai kaifi biyu; 13
''Na san inda kake zama can inda kursiyin shaidan
yake. Duk da haka ka rike sunana da karfi, na sani
baka yi musun bangaskiyar ka da ni ba, ko a lokacin
Antifas mashaidina, amintaccena, wanda aka kashe a
tsakaninku, can inda shaidan yake zama. 14 Amma
ga rashin jin dadi na kadan da kai: Kana da wadansu
da suke rike da koyarwar Bil'amu kamkam, wanda
ya koya wa Balak ya sa abin tuntubi gaban 'ya'yan
Isra'ila, domin su ci abincin da aka mika wa gumaka
kuma suyi fasikanci. 15 Hakannan kuma wasunku sun
rike koyarwar Nikolatawa kamkam. 16 Sabili da haka
ka tuba! Idan ka ki zan zo gare ka da sauri, kuma in yi
yaki gaba da su da takobi dake cikin bakina. 17 Bari
wanda yake da kunne ya sauriri abin da Ruhu yake
fadawa ikilisiyoyi. Ga wanda yayi nasara zan bada wata
boyayyar manna, kuma zan bashi farin dutse da sabon
suna a rubuce a kan dutsen, suna wanda ba wanda
ya sani, sai shi wanda ya karbe shi."" 18 Zuwa ga
mala'ikan ikilisiyar Tiyatira rubuta: 'Wadannan sune
kalamomin Dan Allah, wanda yake da idanu kamar
harshen wuta; sawayen kamar gogaggiyar tagulla: 19
''Na san abin da ka yi, kaunar ka, da bangaskiya da
hidima da tsawon jimrewar ka. Na san abinda ka yi
bada dadewa ba ya fi abinda ka yi da fari. 20 Amma
ga rashin jin dadi na da kai: Kana hakurce wa matar
nan Yezebel, wadda take kiran kanta annabiya. Ta
wurin koyarwarta, ta rudi bayina suyi fasikanci kuma
su ci abincin da aka mika wa gumaka sadaka. 21 Na
bata lokaci domin ta tuba amma bata so ta tuba da
fasikancin ta. 22 Duba! zan jefa ta a kan gadon jinya,
wadanda kuma suka yi zina da ita za su shiga babbar
wahala, sai dai in sun tuba daga ayukan ta. 23 Zan
buga 'ya'yanta da mutuwa, kuma dukan ikilisiyoyi
zasu san cewa nine wanda nake bincike tunani da
zukata. Zan ba kowanen ku bisa ga ayyukansa. 24
Amma ga sauran ku dake cikin Tayatira, ga kowanen
ku wanda bai rike wannan koyarwar ba, kuma bai
san abinda wadansu suke kira zurfafan abubuwan
Shaidan ba—ga ku na ce ban sa muku wata nawaya
ba.' 25 Duk da haka dole ku tsaya da karfi har in zo. 26
Wanda yayi nasara da wanda ya yi abin da na yi har
karshe, a gareshi zan bada iko akan al'ummai 27 Zai
yi mulkin su da sandar karfe, zai farfasa su kamar
randunan yumbu." 28 Kamar yadda na karba daga
wurin Ubana, ni kuma zan bashi tauraron asubahi. 29
Bari wanda yake da kunne ya saurari abinda Ruhu
yake fadawa ikilisiyioyi.""

3 "Zuwa ga mala'ikan ikilisiyar Sardisu rubuta: '
Wadannan ne kalmomin wanda yake rike da ruhohi
bakwai na Allah da taurari bakwai. "Na san abin da ka
aikata. Ka yi suna cewa kana raye amma kai mattacce
ne. 2 Ka farka ka karfafa abin da ya rage amma ya
kusan mutuwa, domin ban sami ayyukanka cikakku
a gaban Allahna ba. 3 Domin haka sai ka tuna, da
abubuwan da ka karba kuma kaji. Ka yi biyayya da su,
ka kuma tuba. Amma idan baka farka ba, zan zo maka
kamar barawo, kuma ba zaka farga da sa'ar da zan
zo gaba da kai ba. 4 Amma akwai sunayen mutane
kadan a Sardisu wadanda basu kazantar da tufafinsu
ba. Za su yi tafiya tare da ni sanye da fararen tufafi
domin sun cancanta. 5 Wanda ya yi nasara za a sanya
mashi fararen tufafi, kuma ba zan taba share sunansa
ba daga Littafin Rai, kuma zan fadi sunansa a gaban
Ubana, da kuma gaban mala'ikunsa. 6 Bari wanda
yake da kunne ya saurari abin da Ruhu ke fadawa
ikilisiyoyi."'" 7 Zuwa ga mala'ikan ikilisiyar cikin
Filadelfiya rubuta: kalmomin wanda yake maitsarki
ne kuma mai gaskiya - yana rike da mabudin Dauda,
yana budewa babu mai rufewa, kuma inda ya rufe ba
mai budewa. 8 Na san abin da ka aikata. Duba, na sa
budaddiyar kofa a gabanka wanda ba mai iya rufewa.
Na san kana da karamin karfi, duk da haka ka yi
biyayya da maganata kuma baka yi musun sunana ba.
9 Duba! Wadanda ke na majami'ar Shaidan, wadanda
suke cewa su Yahudawa ne; amma maimakon haka
karya suke yi. Zan sa su zo su rusuna a kafafunka,
kuma za su san cewa ina kaunarka. 10 Tun da ka jure
cikin hakuri ka kiyaye dokoki na, ni ma zan kiyaye ka
daga sa'a ta gwaji da zata sauko kan dukan duniya,
domin a gwada mazauna duniya. 11 Ina zuwa da sauri.
Ka rike abin da kake da shi kamkam domin kada wani
ya dauke maka rawani. 12 Zan sa wanda ya yi nasara
ya zama ginshiki a haikalin Allahna, kuma ba zai taba
fita daga cikin sa ba. Zan rubuta sunan Allahna a
kansa, sunan birnin Allahna (sabuwar Urushalima,
mai saukowa daga sama daga wurin Allahna), da kuma
sabon sunana. 13 Bari wanda yake da kunne ya ji abin

da Ruhu ke gayawa ikilisiyoyi.” 14 “Zuwa ga mala'ikan
ikilisiyar da ke Lawudikiya rubuta: 'Wadannan sune
kalmomin Amin, madogara da mai shaidar gaskiya,
mai mulki bisa hallittar Allah. 15 Na san abin da ka
aikata, ba ka sanyi ko zafi. Naso ko da kana sanyi ko
zafi! 16 Amma saboda kai tsaka-tsaka ne - ba zafi ba
sanyi - na kusa tofar da kai daga bakina. 17 Domin ka
ce, “Ni mai arziki ne, na mallaki kadarori da yawa, ba
na bukatar komai.” Amma ba ka sani ba kana cike
da takaici ne, abin tausayi, matalauci, makaho kuma
tsirara kake. 18 Saurari shawara ta: Ka sayi zinariya
a wuri na wadda aka goge da wuta domin ka zama
mai arziki, domin ka suturta kanka da fararen tufafi
masu kyalli domin kada ka nuna kunyar tsiraicin ka,
da mai domin ka shafa wa idanunka ka sami gani.
19 Ina horar da duk wanda nake kauna, ina kuma
koya masu yadda za su yi rayuwa. Saboda haka, ka
himmatu ka tuba. 20 Duba, ina tsaye a bakin kofa ina
kwankwasawa. Idan wani ya ji muryata ya bude kofar,
zan shigo cikin gidansa, in ci tare da shi, shi kuma
tare da ni. 21 Wanda ya ci nasara, zan bashi dama ya
zauna tare da ni bisa kursiyina, kamar yadda nima na
ci nasara kuma na zauna da Ubana a kan kursiyinsa.
22 Bari wanda yake da kunne ya saurari abin da Ruhu
yake fadawa wa ikilisiyoyi.”

**4** Bayan wadannan abubuwa na duba, sai ga
budaddiyar kofa a sama. Muryar fari da na ji kamar
kakaki, na cewa hauro in nuna maka abubuwan da
dole za su faru bayan wadannan al'amura.” 2 Nan da
nan ina cikin Ruhu, sai na ga wani kursiyin da aka
ajiye shi a sama, da wani zaune bisansa. 3 Shi da ke
zaune a kan tana da kamanin yasfa da yakutu. Akwai
Bakangizo kewaye da kursiyin kamanin bakangizon
kuwa zumurudu. 4 A kewaye da kursiyin kuwa akwai
kursiyoyi ashirin da hudu, masu zama bisa kursiyoyin
nan kuwa dattawa ne ashirin da hudu, sanye da
fararen tufafi, da kambunan zinariya bisa kawunansu.
5 Daga kursiyin walkiya na ta fitowa, cida, da karar
aradu. Fitilu bakwai na ci a gaban kursiyin, fitilun
sune ruhohin Allah guda bakwai. 6 Gaban kursiyin
akwai tekun gilashi, mai haske kamar karau. A tsakiyar
kursiyin da kewayen kursiyin akwai rayayyun hallitu
guda hudu cike da idanu gaba da baya. 7 Rayayyen
hallitta na farko na da kamanin zaki, rayayyen hallitta
na biyun kamanin dan maraki ne, rayayyen hailitta na
uku fuskar sa kamar dan adam, kuma rayayyen hallitta
ta hudu na da kamanin gaggafa mai tashi. 8 Dukan
rayayyun hallittan nan hudu na da fukafukai shida
shida, cike da idanu a bisa da karkashin fukafukan.
Dare da rana ba sa daina cewa, Mai Tsarki, Mai Tsarki,
Mai Tsarki ne Ubangiji Allah, mai iko duka, shine da
shine yanzu shine mai zuwa.” 9 A dukan lokacin da
rayayyun hallittun nan suke ba da girma, daukaka,
da godiya ga shi da ke zaune bisa kursiyin, wanda
ke raye har abada abadin, (aiōn g165) 10 sai dattawan
nan ashirin da hudu suka fadi da fuskokinsu a kasa
gaban shi da ke zaune bisa kursiyin. Suka yi sujada
ga shi da ke rayuwa har abada abadin, suna jefar da
kambinsu a gaban kursiyin, suna cewa, (aiōn g165) 11
“Ka cancanta, ya Ubangijinmu da Allahnmu, ka karbi
yabo da daukaka da iko. Domin kai ka hallicci dukan
komai, da kuma nufinka ne, suka kasance aka kuma
hallicce su.

**5** Sa'annan na ga a cikin hannun daman wanda ke
zaune a kan kursiyin, na ga littafi wanda ke da
rubutu ciki da waje, an kuma hatimce shi da hatimai
bakwai. 2 Na kuma ga wani kakkarfan mala'ika na
shela da murya mai karfi, “Wa ya isa ya bude littafin
ya kuma bambare hatimin?” 3 Ba wani a sama ko a
kasa ko karkashin kasa da ya iya ya bude littafin ko
ya karanta abin da ke cikinsa. 4 Na yi kuka mai zafi
saboda ba wani da ya cancanta da zai bude littafin ko
ya karanta abin da ke cikinsa. 5 Amma daya daga cikin
dattawan nan ya ce mani, “Kada ka yi kuka. Duba!
Zaki na kabilar Yahuza, Tushen Dauda, ya yi nasara.
Ya cancanci bude littafin da kuma hatimansa bakwai.”
6 Na ga Dan Rago yana tsaye tsakanin kursiyin da
rayayyun halittun nan guda hudu a cikin dattawa.
Yana kama da wanda aka kashe. Yana da kafonni
bakwai da idanuwa bakwai; wadannan sune ruhohin
Allah bakwai da aka aiko zuwa dukan duniya. 7 Ya
tafi ya karbi littafin daga hannun daman wanda ke
zaune bisa kursiyin. 8 Lokacin da Dan Ragon ya dauki
littafin, rayayyun halittun nan hudu da dattawan
nan ashirin da hudu suka fadi har kasa a gaban
Dan ragon. Kowannen su na dauke da molo da tasar
zinariya cike da kayan kamshi, wadanda kuwa sune
addu'o'in masu ba da gaskiya. 9 Suka raira sabuwar
waka: “Ka cancanta ka dauki littafinka kuma bude
hatimansa. Domin an yanka ka, da jininka ka saya wa
Allah mutane daga kowacce kabila, harshe, jama'a da
al'umma. 10 Ka maishe su mulki da firistoci su bauta

wa Allanmu, kuma za su yi mulki a duniya." 11 Da
na duba sai na ji karar mala'iku masu yawa kewaye
da kursiyin da rayayyun halitu da kuma dattawa.
Jimillarsu ya kai dubbai goma, sau dubbai goma, da
dubun dubbai. 12 Suka tada murya da karfi suka ce,
"Macancanci ne Dan Ragon da aka yanka ya karbi iko,
wadata, hikima, karfi, girma, daukaka da yabo." 13 Na
ji kowanne halittaccen abu da ke cikin sama da kasa
da karkashin kasa da cikin teku - dukan abubuwan
da ke cikinsu - na cewa, "Ga shi wanda ke zaune a
kan kursiyin da kuma Dan Ragon, yabo, girma, daraja,
da kuma ikon yin mulki, har abada abadin. (aiōn g165)
14 Sai rayayyun halittun nan hudu suka ce, "Amin!"
dattawan nan kuma suka fadi da fuskokinsu suka yi
sujada.

# 6

Na duba lokacin da Dan Ragon ya bude daya daga
cikin hatiman bakwai, sai na ji daya daga cikin
rayayyun halittattun hudu ya fada da murya kamar
tsawa, ''Zo!" 2 Sai Na duba sai ga wani farin doki,
mahayinsa na rike da baka, kuma an bashi rawani.
Ya fito a matsayin mai nasara domin ya yi nasara. 3
Sa'anda Dan Ragon ya bude hatimi na biyu, sai na
ji rayayyen halitta na biyu ya ce, ''Zo!'' 4 Sai wani
doki ya fito waje - jawur. Ga mahayin aka bashi dama
ya dauke salama daga duniya, domin mutanen ta su
karkashe juna. Wannan mahayin an bashi babbar
takobi. 5 Sa'anda Dan Ragon ya bude hatimi na uku,
sai na ji rayayyen halita na uku ya ce, ''Zo!'' Na ga
bakin doki, mai hawanta na rike da ma'auni a cikin
hannunsa. 6 Sai na ji kamar wata murya daga cikin
rayayyun halittattun nan hudu ta ce, "Mudun alkama
guda a kan albashin yini, kuma mudun sha'ir uku.
Amma kar ka bata mai da kuma ruwan inabi." 7 Da
Dan Ragon ya bude hatimi na hudu, na ji muryar
rayayyen halitta na hudu ya ce, ''Zo!'' 8 Sai na ga wani
doki ruwan toka. Mai hawansa an bashi suna mutuwa,
hades kuma tana biye da shi. An basu iko bisa kashi
hudu na duniya su kashe da takobi, yunwa, cututtuka,
da kuma namomin jeji na duniya. (Hadēs g86) 9 Da Dan
Ragon ya bude hatimi na biyar, a karkashin bagadi sai
na ga rayukan wadanda aka kashe saboda maganar
Allah, da kuma shaidar da suka rike. 10 Suka yi kuka
da babban murya, ''Sai yaushe ya mai iko duka, Mai
Tsarki da gaskiya, zaka shari'anta mazaunan duniya,
ka kuma dauki fansar jininmu? 11 Sai kowanne dayan
su aka bashi farar tufa aka kuma fada masu su kara
jira na lokaci kadan har sai adadin abokan bautar su
da kuma 'yan'uwansu maza da mata wadanda aka
kashe ya cika, kamar yadda aka kashe su. 12 Da Dan
Ragon ya bude hatimi na shidan, ina kallo sai ga
babbar girgizar kasa. Rana ta zama baki kirin kamar
bakar tufa, wata kuma ya zama kamar jini. 13 Taurarin
sama suka fado kasa, kamar yadda itacen baure ke
karkade 'ya'yansa da basu nuna ba, yayin da babbar
iska ta kada. 14 Sama kuma ta bace kamar takardar da
aka nannade. Kowanne dutse da tsibiri aka kau da shi
daga wurinsa. 15 Sai sarakan duniya da muhimman
mutane da sarakunan yaki, attajirai, da masu iko, tare
da kowanne mutum, bawa da 'yantacce suka boye
cikin duwatsu da tsaunuka. 16 Suka ce wa tsaunuka da
duwatsu, "Ku fado bisan mu! Ku boye mu daga fuskar
wanda yake zaune bisa kursiyin da kuma fushin Dan
Ragon. 17 Domin babban ranar fushin sa ta zo. Wa zai
iya tsayawa?''

# 7

Bayan wannan sai na ga mala'iku hudu suna tsaye
bisa kusurwoyi hudu na duniya, suka rike iskoki
hudu na duniya kamkam domin kada iska ta hura
a kan duniya, a kan teku, ko wani itace. 2 Sai na ga
wani mala'ika na zuwa daga gabas, wanda yake da
hatimin Allah mai rai. Ya yi kira da babbar murya da
mala'ikun nan hudu da aka basu dama su azabtar da
duniya da teku: 3 "Kada ku azabtar da duniya, da teku,
da itatuwa har sai mun sa hatimi bisa goshin bayin
Allahnmu." 4 Sai naji yawan wadanda aka hatimce:
144, 000, wadanda aka hatimce daga kowacce kabilar
mutanen Isra'ila: 5 dubu goma sha biyu aka hatimce
daga kabilar Yahuza, dubu goma sha biyu daga kabilar
Ra'ubainu, dubu goma sha biyu daga kabilar Gad, 6
dubu goma sha biyu daga kabilar Ashiru, dubu goma
sha biyu daga kabilar Naftali, dubu goma sha biyu
daga kabilar Manassa. 7 Dubu goma sha biyu daga
kabilar Saminu, dubu goma sha biyu daga kabilar
Lawi, dubu goma sha biyu daga kabilar Issaka, 8 dubu
goma sha biyu daga kabilar zabaluna, dubu goma sha
biyu daga kabilar Yusufu, sai kuma dubu goma sha
biyu daga kabilar Bilyaminu aka hatimce. 9 Bayan
wadannan abubuwa na duba, sai ga wani babban taro
wanda ba mai iya kirgawa daga kowacce al'umma,
kabila, mutane da harsuna tsaye a gaban kursiyin da
gaban Dan Ragon. Suna sanye da fararen tufafi da
ganyen dabino a hannuwansu, 10 kuma suna kira da
murya mai karfi: "Ceto ya tabbata ga Allahnmu wanda

ke zaune bisa kursiyi, da kuma Dan Ragon!" 11 Dukan
mala'iku suna tsaitsaye kewaye da kursiyin kuma
kewaye da dattawan nan da kuma rayayyun halittun
nan hudu, suka kwanta rib da ciki da fuskokinsu a
gaban kursiyin. Suka yi sujada ga Allah, 12 suna cewa,
"Amin! yabo, daukaka, hikima, godiya, girma, iko, da
karfi su zama na Allahnmu har abada abadin! Amin!"
(aiōn g165) 13 Sai daya daga cikin dattawan ya tambaye
ni, "Su wanene wadannan, da suke sanye da fararen
tufafi, kuma daga ina suka fito?" 14 Sai nace masa, "Ya
shugaba, "Ka sani," sai ya ce mani, "Wadannan sune
suka fito daga babban tsanani. Sun wanke tufafin su
sun maida su farare cikin jinin Dan Ragon. 15 Domin
wannan dalili, suke gaban kursiyin Allah, kuma suna
masa sujada dare da rana cikin haikalinsa. Shi wanda
ke zaune bisa kursiyin zai zama runfa a bisan su. 16
Ba za su kara jin yunwa ba, ko kishin ruwa ba. Rana
ba zata buge su ba, ko kowanne zafi mai kuna. 17
Domin Dan Ragon dake tsakiyar kursiyin zai zama
makiyayin su, kuma zai bishe su zuwa mabulbulan
ruwan rai, kuma Allah zai share dukan hawaye daga
idanuwansu."

**8** Lokacin da Dan Ragon nan ya bude hatimi na
bakwai, sai aka yi shiru a sama na kimanin rabin
sa'a. 2 Sa'anan na ga mala'iku bakwai wadanda ke
tsaye a gaban Allah, aka kuma basu kahonni bakwai 3
Wani mala'ika ya zo, rike da tasar turaren konawa na
zinariya, a tsaye gaban bagadi. Turaren konawa mai
yawa aka bashi saboda ya mika su tare da adu'o'in
dukan masu bada gaskiya akan bagadin kona turare na
zinariya a gaban kursiyin. 4 Hayakin turaren konawa,
da adu'o'in masu bada gaskiya, suka tashi sama a
gaban Allah daga hanun mala'ikar. 5 Mala'ikan ya
dauki tasar turaren konawa ya cika ta da wuta daga
bagadin. Sa'annan ya wurgo ta kasa zuwa duniya, sai
ga tsawar aradu, da cida, da walkiya mai haske, da
kuma girgizar kasa. 6 Mala'ikun nan bakwai wadanda
suke da kahonni bakwai suka yi shirin busa su. 7
Mala'ika na fari ya hura kahonsa, sai ga kankara da
wuta a garwaye da jini. Aka jeho shi kasa zuwa duniya
sai kashi daya cikin uku na duniya ya kone, daya cikin
uku na itatuwa suka kone, da duk danyar ciyawa suka
kone kaf. 8 Mala'ika na biyu ya busa kahonsa, sai
wani abu mai kama da babban dutse mai cin wuta aka
jefo shi cikin teku. Kashi daya cikin uku na tekun ya
zama jini, 9 daya cikin uku na rayayyun halittu da ke
cikin ruwa suka mutu, sai daya bisa uku na jiragen
ruwa aka hallaka. 10 Mala'ika na uku ya busa kahonsa,
sai gagarumin tauraro ya fado daga sama, yana ci
kamar cocila, bisa kashi daya cikin uku na koguna da
mabulbulan ruwa. 11 Sunan tauraron Daci. Kashi daya
cikin uku na ruwaye suka yi daci, sai jama'a da yawa
suka mutu domin ruwayen sun yi daci. 12 Mala'ika
na hudu ya busa kahonsa, sai daya cikin kashi uku
na rana ya harbu, da daya cikin kashi uku na wata
da kuma daya cikin kashi uku na taurari. Sai daya
cikin kashi uku nasu duka suka duhunce; daya cikin
kashi uku na yini da daya cikin uku na dare suka rasa
hasken su. 13 Da na duba sai na ji gaggafa da take
shawagi a tsakiyar sararin sama tana kira da babban
murya, "Kaito, kaito, kaito, ga mazaunan duniya sabili
da sauran karar kahonni na mala'ikun nan uku da za
su busa."

**9** Sa'annan mala'ika na biyar ya busa kahonsa. Na
ga tauraro daga sama da ya fado zuwa duniya. An
ba tauraron nan mabudin hanyar rami marar iyaka.
(Abyssos g12) 2 Ya bude hanyar rami marar iyaka, sai
hayaki ya fito daga kofar kamar hayaki daga babban
ramin wuta. Rana da iska suka juya duhu, sabili da
hayakin da ke fitowa daga kofar ramin. (Abyssos g12)
3 Daga cikin hayakin kuwa sai ga fari sun fito zuwa
duniya, aka ba su iko kamar na kunamai cikin duniya.
4 Aka gaya masu kada su yi wa ciyayi da kowanne
koren ganye ko itace illa, sai dai mutanen da basu
da hatimin Allah a goshinsu. 5 Ba a basu izini su
kashe wadannan mutane ba, sai dai su azabtar da
su na watani biyar. Zafinsu kuwa zai zama kamar na
cizon kunama idan ta harbi mutum. 6 A kwanakin
nan mutane za su nemi mutuwa, amma ba za su same
ta ba. Za su yi marmarin mutuwa, amma mutuwa za
ta guje su. 7 Farin kuwa suna kama da dawakai da
aka shirya domin yaki. A bisa kansu akwai wani abu
kamar rawanan zinariya, fuskokinsu kuma kamar na
'yan adam. 8 Gashinsu kuma kamar na mata yake,
hakoransu kamar hakoran zaki. 9 Sulkunansu kuma
kamar na karfe, karar fikafikansu kuma kamar karar
kekunan dawakin yaki masu yawa da dawakai da aka
shirya domin zuwa yaki. 10 Suna da wutsiya da kari
kamar kunamai; A wutsiyar su kuma suna da ikon da
zai azabtar da mutane na tsawon wata biyar. 11 Suna
da wani kamar sarki a kansu, mala'ikan rami marar
iyaka. Sunansa da Ibraniyanci Abadon, da Helenanci

kuma Afoliyon. (Abyssos g12) 12 Bala'i na fari ya wuce.
Duba! Bayan wannan akwai masifu guda biyu masu
zuwa. 13 Mala'ika na shida ya busa kahonsa, sai na ji
murya daga kahonin bagadin zinariya da ke gaban
Allah. 14 Muryar ta ce wa mala'ika na shida da ke
rike da kahon, "Kwance mala'ikun nan hudu da ke
daure a babban kogin Yufiretis," 15 Mala'iku hudun
da aka shirya domin wannan sa'a, da wannan rana,
da wannan wata, da kuma wannan shekara, aka sake
su su kashe daya bisa uku na 'yan adam. 16 Yawan
sojoji da ke kan dawakai shine 200, 000, 000. Na ji
adadin su. 17 Haka na ga dawakan a cikin wahayina
da mahayansu: Sulkunansu jawur kamar wuta, bakin
shudi, da kuma ruwan doruwa. Kawunan dawakan
suna kama da na zakuna, daga bakunansu kuma wuta,
da hayaki da farar wuta suka fito. 18 Aka kashe daya
bisa uku na mutane ta annoban nan uku: wuta, hayaki
da farar wuta da suka fito daka bakunansu. 19 Domin
iko na dawakan na bakunansu da wutsiyoyinsu -
domin wutsiyoyinsu suna kama da macizai, kuma
suna da kawuna wadanda dasu suke ji wa mutane
rauni. 20 Sauran 'yan adam, da ba a kashe su ta
wannan annoba ba, basu tuba daga ayyukan da suka
yi ba. Basu kuma daina bautar aljanu da gumakan
zinariya, da azurfa, da tagulla, da dutse, da itace ba -
abubuwan da ba su gani, ji, ko tafiya. 21 Basu kuma
tuba ba daga kisan kai, sihiri, fasikanci, ko kuma
ayyukansu na sata ba.

10 Sa'anan na ga wani babban mala'ika yana zuwa
daga sama. Yana lullube cikin girgije, a bisa kansa
akwai bakangizo. Fuskarsa kamar rana, kafafunsa
kamar ginshikan wuta. 2 Yana rike da karamin littafi
a hannunsa, da aka bude, sai ya sa kafarsa ta dama a
bisa teku, kafarsa ta hagu kuma a kan kasa. 3 Sai yayi
ihu da babbar murya kamar zaki mai ruri. Lokacin da
ya yi ihu, tsawan nan bakwai suka yi magana da karar
su. 4 Da tsawan nan bakwai suka yi magana, ina dab
da rubutu, amma na ji wata murya daga sama cewa,
"Ka rike asirin abin da tsawan nan bakwai suka fada.
Kada ka rubuta shi." 5 Sai mala'ikan da na gani tsaye
bisa teku da kasa, ya daga hannun damarsa sama. 6
Sai ya rantse da wannan da ke raye har abada abadin
- wanda ya halicci sama da duk abinda ke cikinsa,
da duniya da duk abin da ke a kanta, da teku da
dukan abin da ke cikinsa, sai mala'ikan ya ce, "Babu
sauran jinkiri. (aiōn g165) 7 Amma a ranar da mala'ika
na bakwai yana dab da busa kahonsa, a lokacin ne
asirin Allah zai cika, daidai da yadda ya sanar wa
bayinsa annabawa." 8 Muryar da na ji daga sama ta
sake magana da ni: "Tafi, ka dauki budadden littafin
da ke hannun mala'ikan da ke tsaye bisa teku da kan
kasa." 9 Sai na tafi wurin mala'ikan na ce da shi ka
bani karamin littafin. Yace dani, "Dauki littafin ka
ci. Zai sa cikinka ya yi daci, amma a bakinka zai yi
zaki kamar zuma." 10 Na dauki karamin littafin daga
hannun mala'ikan na ci. Ya yi zaki sosai a bakina
kamar zuma, amma da na ci, sai cikina ya zama da
daci. 11 Wani yace mani, "Dole ka sake yin annabci
kuma game da mutane masu yawa, da al'ummai, da
harsuna da sarakuna."

11 Aka bani sanda in yi amfani da ita kamar sandar
awo. Aka ce mani, "Tashi ka auna haikalin Allah
da bagadi, da wadanda ke sujada a cikinsa. 2 Amma
kada ka auna harabar haikalin, domin an ba da shi
ga Al'ummai. Za su tattake birnin mai tsarki har
wata arba'in da biyu. 3 Zan ba shaidu na biyu iko
su yi anabci na kwanaki dubu daya da dari biyu da
sittin, sanye da tsummoki. 4 Wadannan shaidu sune
itatuwan zaitun biyu da kuma fitilu biyu da suke tsaye
a gaban Ubangijin duniya. 5 Idan wani ya yi niyyar
cutar da su, wuta na fitowa daga bakinsu ta lashe
makiyansu. Duk mai son cutar da su, dole a kashe shi
ta wannan hanya. 6 Wadannan shaidu suna da iko su
kulle sama domin kada a yi ruwa a lokacin da suke
anabci. Suna da iko su juya ruwaye su zama jini, su
kuma bugi duniya da kowacce irin annoba duk lokacin
da suka ga dama. 7 Sa'adda suka gama shaidarsu,
dabban da ke fitowa daga rami marar iyaka zai yi
yaki da su. Zai ci nasara da su ya kashe su. (Abyssos
g12) 8 Gawawwakinsu zasu kwanta kan hanyar babban
birnin nan (wanda ma'anar sa ake kira Saduma da
Masar) inda aka gicciye Ubangijinsu. 9 Wajen kwana
uku da rabi wadansu daga dukan mutane, da kabila,
da harshe, da al'umma za su yi kallon gawawwakinsu.
Za su ki yarda a sa su cikin kabari. 10 Mazaunan
duniya zasu yi murna da biki a kansu. Har za su aika
wa juna kyautai saboda annabawan nan biyu da suka
azabtar da mazaunan duniya. 11 Amma bayan kwana
uku da rabi, numfanshin rai daga wurin Allah zai
shiga cikinsu sa'annan za su tsaya a kan kafafunsu.
Matsanancin tsoro zata fado kan wadanda za su gansu.
12 Sa'annan zasu ji murya mai kara daga sama tana ce
masu, "Ku hauro nan!" Sa'annan za su tafi sama cikin

gajimarai, makiyansu suna kallo. 13 A waccan sa'a za
a yi babbar girgizar kasa, sai kashi daya cikin goma
na garin ya fadi. Mutane dubu bakwai za su mutu a
girgizar kasar, wadanda suka tsira kuwa za su tsorata
su ba da daukaka ga Allah na sama. 14 Annoba ta biyu
ta wuce. Duba! Annoba ta uku tana zuwa nan da nan.
15 Sa'annan mala'ika na bakwai ya busa kahonsa, sai
muryoyi masu kara suka yi magana cikin sama cewa,
“Mulkin duniya ya zama mulkin Ubangijinmu da na
Almasihunsa. Zai yi mulki har abada abadin.” (aiōn g165)
16 Sa'annan dattawan nan ashirin da hudu da ke zaune
a kursiyoyinsu a gaban Allah, suka fadi fuskokinsu na
kasa. Suka yi wa Allah sujada. 17 Suka ce, “Mun yi
maka godiya, Ubangiji Allah, Madaukaki, wanda yake
yanzu da wanda yake a da, saboda ka dauki ikonka
mai girma ka fara mulki. 18 Al'ummai suka fusata,
amma hasalar ka ta zo. Lokaci ya zo da za a yi wa
mattatu sharia, da zaka ba da sakamako ga bayinka
annabawa, da masu ba da gaskiya, da wadanda suka ji
tsoron sunanka, karami da babba. Lokaci kuma ya
yi da za ka hallaka wadanda ke hallakar da duniya.”
19 Sa'annan aka bude haikalin Allah da ke sama, sai
aka ga akwatin alkawarinsa a cikin haikalinsa. Sai ga
hasken walkiya, da rugugi, da aradu, da girgizar kasa,
da manyan duwatsun kankara.

12 Aka ga wata babbar alama a sama: wata mace
ta yi lullubi da rana, kuma wata na karkashin
kafafunta; rawanin taurari goma sha biyu na bisa
kanta. 2 Tana da ciki, tana kuma kuka don zafin
nakuda - a cikin azabar haihuwa. 3 Sai aka ga wata
alama cikin sama: Duba! Akwai wani katon jan maciji
mai kawuna bakwai da kahonni goma, sai kuma ga
kambi guda bakwai bisa kawunansa. 4 Wutsiyarsa
ta share daya bisa uku na taurari a sama ta zubo su
kasa. Diragon nan ya tsaya a gaban matar da ta kusan
haihuwa, domin lokacin da ta haihu ya lankwame
yaronta. 5 Sai ta haifi da, namiji, wanda zai yi mulkin
dukan al'ummai da sandar karfe. Aka fizge yaron ta
zuwa ga Allah da kursiyinsa, 6 matar kuwa ta gudu
zuwa jeji inda Allah ya shirya mata domin a iya lura da
ita kwanaki 1, 260. 7 A lokacin sai yaki ya tashi a sama.
Mika'ilu da mala'ikunsa suka yi yaki da diragon, sai
diragon da nasa mala'iku suka yake su su ma. 8 Amma
diragon ba shi da isashen karfin da zai ci nasara. Don
haka, shi da mala'ikunsa ba su kara samun wuri a
sama ba. 9 Sai aka jefa katon diragon nan tare da
mala'ikunsa kasa, wato tsohon macijin nan da ake kira
Iblis ko Shaidan wanda ke yaudarar dukan duniya. 10
Sai na ji wata murya mai kara a sama: “Yanzu ceto ya
zo, karfi, da mulkin Allahnmu, da iko na Almasihunsa.
Gama an jefar da mai sarar 'yan'uwanmu a kasa - shi
da yake sarar su a gaban Allah dare da rana. 11 Suka
ci nasara da shi ta wurin jinin Dan Ragon da kuma
shaidar maganarsu, gama ba su kaunaci ransu ba, har
ga mutuwa. 12 Don haka, yi farinciki, ya ku sammai
da duk mazauna da ke cikinsu. Amma kaito ga duniya
da teku saboda iblis ya sauko gare ku. Yana cike da
mummunan fushi, domin ya san lokacin sa ya rage
kadan. 13 Da diragon ya ga an jefar da shi kasa, sai ya
fafari matar nan da ta haifi da namiji. 14 Amma aka ba
matar nan fukafukai biyu na babbar gaggafa domin
ta gudu zuwa inda aka shirya mata a jeji. A wannan
wuri ne za a lura da ita na dan lokaci, da lokatai, da
rabin lokaci - a lokacin da babu macijin. 15 Macijin
ya kwararo ruwa daga bakin sa kamar kogi, don ya
kawo ambaliyar da zai kwashe ta. 16 Amma kasa ta
taimaki matar. Kasa ta bude bakinta ta hadiye kogin
da diragon ya kwararo daga bakinsa. 17 Sai diragon
ya fusata da matar, sai ya tafi ya yi yaki da sauran
zuriyarta, wadanda suka yi biyayya da umarnan Allah
suna kuma rike da shaida game da Yesu.

13 Sai diragon ya tsaya a kan yashi, a gaban teku.
Sai na ga wani dabba yana fitowa daga teku.
Yana da kahonni goma da kawuna bakwai. A kan
kahonninsa akwai kambi goma, a kan kowanne kansa
akwai suna na sabo. 2 Wannan dabban da na gani yana
kama da damisa, kafafunsa kuma kamar na beyar,
bakinsa kuma kamar na zaki. Wannan diragon ya
ba shi karfinsa, da kursiyinsa da ikonsa mai girma
na sarauta. 3 Daya daga cikin kawunan dabban ya
yi kamar an kashe shi, amma rauninsa mai tsanani
ya warke. Sai dukan duniya ta yi mamaki a yayin da
suke bin dabban. 4 Su ma suka yi wa diragon sujada,
domin ya ba dabban ikonsa. Suka yi wa dabban sujada
suna ta cewa, “Wanene kamar dabban? Wa kuma zai
iya yin fada da shi?” 5 Aka ba dabban baki da zai iya
fadin kalmomin fahariya da sabo. Ya sami izini na
zartar da iko har wata arba'in da biyu. 6 Sai dabban ya
bude bakinsa yana maganganun sabo ga Allah: yana
sabon sunansa, da mazauninsa, da kuma wadanda
ke zaune a sama. 7 Aka yarje wa dabbar ya yi yaki
da masu bi ya kuma yi nasara da su. An kuma ba

shi iko bisa kowacce kabila, da jama'a, da harshe, da
al'umma. 8 Dukan wadanda ke zaune a duniya za su
yi masa sujada, dukan wadanda tun hallitar duniya
ba a rubuta sunayensu a littafin rai na Dan Rago
ba, wanda aka yanka. 9 Idan wani yana da kunne,
bari ya ji. Duk wanda za a dauke shi zuwa bauta, ga
bauta zai tafi. 10 Duk wanda za a a kashe da takobi, da
takobi za a a kashe shi. Wannan kira ne na dauriya,
hakuri da bangaskiya ga wadanda suke da tsarki. 11
Sai na ga wani dabban na fitowa daga cikin kasa.
Yana da kahonni biyu kamar na dan rago, ya kuma
yi magana kamar maciji. 12 Ya zartar da dukan ikon
dabban na farko a gabansa, ya kuma sa duniya da duk
mazaunanta su yi wa dabban nan na farko sujada,
wanda aka warkar masa da rauni mai kamar na ajali.
13 Ya yi manyan al'ajibai. Har ya sa wuta ta sauko kasa
daga sama a gaban mutane. 14 Ta wurin alamu da aka
yarje masa ya yi, ya yaudari mazaunan duniya. Ya ce
masu su yi wata siffa don girmama dabban da yake
da raunin takobi, amma duk da haka ya rayu. 15 Aka
yarje masa ya ba da numfashi ga siffar dabban domin
siffar ta yi magana, ta kuma sa a kashe duk wadanda
suka ki yin sujada ga dabban. 16 Ya kuma tilasta kowa,
kanana da manya, mawadata da matalauta, masu
yanci da bayi, su karbi alama a hannun dama ko kuma
a goshi. 17 Ba shi yiwuwa wani ya saya ko ya sayar sai
dai yana da alamar dabban, wato lambar nan da ke
wakiltar sunansa. 18 Wannan na bukatar hikima. Idan
wani yana da hikima, sai ya kididdige lambar dabban
nan. Gama lambar ta mutum ce. Lambarta itace 666.

14 Sai na duba na ga Dan Ragon yana tsaye a kan
Dutsen Sihiyona. Tare da shi akwai mutum dubu
dari da arba'in da hudu wadanda aka rubuta sunansa
da sunan Ubansa a goshinsu. 2 Na ji wata murya daga
sama mai kara kamar kogin ruwa mai gudu da kuma
aradu mai kara. Muryar da na ji ta yi kama da masu
molo suna kada molonsu. 3 Suka raira sabuwar waka a
gaban kursiyin da kuma gaban rayayyun halittun nan
hudu, da kuma dattawan. Ba mai iya koyon wakar nan
sai dai mutum 144, 000 nan wadanda aka fanso daga
duniya. 4 Wadannan sune wadanda basu kazantar
da kansu da mata ba, gama sun kebe kansu da tsarki
daga halin jima'i. Wadannan ne ke bin Dan Ragon duk
inda ya tafi. Aka fanso su daga cikin mutane domin
su zama nunan fari domin Allah da Dan Ragon. 5
Ba a iske karya a bakinsu ba; ba su da aibi. 6 Na ga
wani mala'ika na firiya a tsakiyar sararin sama, wanda
yake da madawwamin sako na labari mai dadi domin
a sanar da ita ga mazaunan duniya - ga kowacce
al'umma, da kabila, da harshe, da kuma jama'a. (aiōnios
g166) 7 Yayi kira da babbar murya, "Ku ji tsoron Allah,
ku daukaka shi. Gama sa'arsa ta hukunci ta yi. Yi masa
sujada, shi wanda ya yi sama da kasa, da teku, da
kuma mabulbular ruwa." 8 Sai wani malai'ka, malaika
na biyu, ya biyo yana cewa, "Ta fadi, Babila mai girma
ta fadi, wadda ta rinjayi dukan al'ummai su sha ruwan
inabin fasikancinta." 9 Wani mala'ika - na uku - ya
biyo su da murya mai karfi yana cewa, "Duk wanda ya
yi sujada ga dabban da kuma siffarsa, ya karbi alama a
goshinsa ko a hannunsa, 10 shi ma zai sha daga ruwan
inabin fushin Allah, ruwan inabi da aka zuba tsantsa
cikin kokon fushinsa. Wanda ya sha shi za a azabtar
da shi da wuta, da farar wuta, a gaban tsarkakan
mala'ikun Allah da kuma Dan Ragon. 11 Hayaki daga
azabarsu yana tashi sama har abada abadin, kuma
ba su da hutu dare ko rana - wadannan masu sujada
ga dabban da siffarsa da kuma dukan wadanda suka
karbi alamar sunansa. (aiōn g165) 12 Wannan shine kira
domin hakurin jimrewa na wadanda ke da tsarki,
wadanda suke biyayya ga dokokin Allah da bangaskiya
cikin Yesu." 13 Na ji murya daga sama cewa, "Rubuta
wannan: Masu albarka ne matattu da suka mutu
cikin Ubangiji." Ruhu yace, 'I' domin sun huta daga
wahalarsu, gama ayyukansu na biye da su." 14 Na duba
sai ga farin gajimare. Zaune a kan gajimaren akwai
wani kamar Dan Mutum. Yana da kambin zinariya
a kansa da lauje mai kaifi a hannunsa. 15 Sai wani
malaika ya fito daga haikalin, ya yi kira da murya
mai karfi ga wanda ke zaune kan gajimare: "Dauki
laujenka ka fara girbi, domin lokacin girbin duniya ya
yi." 16 Sai wanda ke zaune a kan gajimaren ya wurga
laujensa bisa kan duniya, aka kuma girbe duniya. 17
Wani mala'ika ya fito daga haikali a sama, shi ma yana
da kakkaifan lauje. 18 Sai wani mala'ika ya fito daga
bagadin kona turare, wanda yake da iko kan wutar.
Ya yi kira da murya mai karfi ga wanda yake rike
da kakkaifan lauje, "Ka dauki kakkaifan laujenka ka
tattara nonnan innabi daga itacen inabin na duniya,
gama inabin ya nuna." 19 Mala'ikan ya jefa laujensa
duniya ya tattara girbin inabin duniya. Ya zuba shi
a cikin babbar taskar wurin matsar ruwan inabi na
fushin Allah. 20 Aka tattake wurin matsar inabin a
bayan birni, jini ya yi ta gudu daga wurin matsar

inabin, ya kai kamar tsawon linzami a bakin doki, har
mil dari biyu.

15 Sai na ga wata alama cikin sama, babba mai
ban mamaki: Akwai mala'iku bakwai rike da
annobai bakwai, wadanda sune annobai na karshe
domin da su ne fushin Allah zai cika. 2 Na ga wani
abin da da ya bayyana mai kama da tekun gilashi mai
haske garwaye da wuta. Tsaye a gefen tekun sune
wadanda suka ci nasara a kan dabban da siffarsa,
da kuma lambar da ke wakiltar sunansa. Suna rike
da molayen da Allah ya ba su. 3 Suna rera wakar
Musa, bawan Allah, da wakar Dan Rago: ''Ayyukan
ka manya ne da ban mamaki, Ubangiji Allah, Mai
iko duka. Adalci da gaskiya hanyoyinka ne, Sarkin
al'ummai. 4 Wanene ba zai ji tsoron ka ba, Ubangiji,
ya kuma daukaka sunanka? Domin kai kadai ne mai
tsarki. Dukan al'ummai za su zo su yi sujada a gabanka
domin an bayyana ayyukan ka na adalci." 5 Bayan
wadannan abubuwa na duba, kuma aka bude haikalin
alfarwar shaida a cikin sama. 6 Daga wuri mafi tsarki
mala'iku bakwai masu rike da annobai bakwai suka
zo. Suna sanye da tufafi masu tsabta, da lallausar
linin mai haske, suna kuma da damarar zinariya a
kirjinsu. 7 Daya daga cikin rayyayun halitu hudu ya
ba mala'iku bakwai tasoshin zinariya bakwai cike da
fushin Allah wanda yake raye har abada abadin. (aiōn
g165) 8 Haikalin ya cika da hayaki daga daukakar Allah
da kuma ikonsa. Ba wanda ya iya shigarsa har sai da
annoban nan bakwai na mala'ikun nan bakwai suka
cika.

16 Na ji babban murya na kira daga cikin haikali
tana ce wa malai'iku bakwai, ''Ku je ku zuba
tasoshi bakwai na fushin Allah a kan duniya." 2
Mala'ika na fari ya je ya zuba tasarsa a kan duniya;
munanan gyambuna masu zafi suka fito wa mutane
wadanda suke da alamar dabbar, wadanda suka bauta
wa siffarsa. 3 Mala'ika na biyu ya zuba tasarsa cikin
teku. Ya zama jini, kamar jinin wanda ya mutu, kuma
kowane abu mai rai da ke cikin tekun ya mutu.' 4
Malaika na uku ya zuba tasarsa a cikin rafuffuka da
mabulbulan ruwa, sai suka zama jini. 5 Na ji mala'ikan
ruwaye ya ce, ''Kai mai adalci ne - wanda ya ke yanzu
wanda yake kuma a da, Mai Tsarkin nan, domin ka
shari'anta wadannan abubuwa. 6 Domin sun zubar da
jinin masu ba da gaskiya da annabawa, ka basu jini
su sha; shine abinda da ya dace da su. 7 Na ji bagadi
ya amsa, ''I, Ubangiji Allah Mai iko duka, shari'un ka
gaskiya ne da adalci.'' 8 Mala'ika na hudu ya zuba
tasarsa a kan rana, kuma aka ba shi izini ya kone
jama'a da wuta. 9 Suka kone da zafi mai tsanani, kuma
suka sabi sunan Allah, wanda ke da iko akan annobai.
Ba su tuba ba ko su daukaka shi. 10 Sai malaika na
biyar ya zuba tasarsa a kan kursiyin dabban, sai duhu
ya rufe mulkinsa. Suka cicciji harsunansu saboda
zafi. 11 Suka yi sabon Allah na sama domin zafi da
gyambunansu, suka kuma ki su tuba daga abin da
suka yi. 12 Mala'ika na shida ya zuba tasarsa cikin
babban rafi, Yufiretis. Ruwansa ya bushe domin a
shirya hanya da sarakuna za su zo daga gabas. 13 Na
ga kazamun ruhohi uku suna kama da kwadin da ke
fitowa daga bakin diragon, da makaryacin annabi. 14
Gama su ruhohin aljanu ne masu aikata alamun ban
mamaki. Sun fita za su wurin sarakunan dukan duniya
domin su tattaro su wuri daya saboda yaki a babbar
ranar Allah Mai iko duka. 15 (''Duba! Ina zuwa kamar
barawo! Mai albarka ne wanda ke zaune a fadake,
wanda ke sanye da tufafinsa domin ba zai fita tsirara
a ga tsiraicin sa ba.") 16 Aka kawo su tare a wurin da
ake kira Armagiddon da Ibraniyanci. 17 Mala'ika na
bakwai ya zuba tasarsa cikin iska. Sa'annan babbar
murya ta fito daga cikin haikali da kuma kursiyin,
cewa, ''An gama!'' 18 Aka yi walkiya, da kararraki masu
tsanani, da aradu da babbar girgizar kasa - girgizar da
ta fi kowacce da aka taba yi tun da 'yan adam suke a
duniya, girgizar da girma ta ke. 19 Babban birnin ya
rabu kashi uku, kuma biranen al'ummai suka fadi. Sai
Allah ya tuna da Babila mai girma, sai ya ba wancan
birnin koko cike da ruwan innabi wanda aka yi daga
fushinsa mai tsanani. 20 Kowanne tsibiri ya bace, sai
ba a kara ganin duwatsun ba. 21 Manyan duwatsun
kankara, masu nauyin talanti, suka fado daga sama
kan mutane. Suka zagi Allah domin annobar kankarar
saboda annobar ta yi tsanani.

17 Daya daga cikin mala'ikun nan bakwai wanda
ke rike da tasoshi bakwai ya zo ya ce mani,
"Zo, zan nuna maka hukuncin babbar karuwarnan
da ke zaune a kan ruwaye masu yawa. 2 Da ita ce
sarakunan duniya suka yi fasikanci. Da ruwan inabinta
na fasikanci marar dacewa ta sa mazaunan duniya
suka bugu." 3 Sai mala'ikan ya dauke ni cikin Ruhu ya
tafi da ni jeji, sai na ga mace zaune bisa jan dabba
cike da sunayen sabo. Dabbar tana da kawuna bakwai
da kahonni goma. 4 Matar kuwa tana sanye da tufafi

na shunayya da kuma jar garura, ta kuma ci ado
da kayan zinariya da duwatsu masu tamani da lu'u-
lu'ai. Tana rike da kokon zinariya a hannunta cike da
abubuwan kyama da na kazantar fasikancinta marar
dacewa. 5 Bisa goshinta an rubuta wani suna mai
boyayyar ma'ana: “Babila mai girma, uwar karuwai
da na kazamtattun abubuwan duniya.” 6 Sai na ga
matar a buge da jinin masu ba da gaskiya da kuma
jinin wadanda aka kashe su domin Yesu. Da na gan ta,
na yi mamaki kwarai da gaske. 7 Amma mala'ikan ya
ce mani, “Don me kake mamaki? Zan bayyana maka
ma'anar matar da kuma na dabbar da ke dauke da
ita, dabban nan da ke da kawuna bakwai da kahonni
goma. 8 Dabban da ka gani da, yanzu ba ta, amma ta
na kusan hawowa daga rami marar iyaka. Sa'annan za
ta je hallaka. Wadanda ke zaune a duniya, wadanda ba
a rubuta sunayensu cikin littafin rai ba tun kafuwar
duniya - za su yi mamaki idan suka ga dabbar da da ta
kasance, ba ta nan yanzu, amma ta kusa zuwa. (Abyssos
g12) 9 Wannan al'amari na bukatar hikima. Kawunnan
bakwai, tuddai ne bakwai da macen ke zaune a kai. 10
Su kuma sarakuna ne bakwai. Sarakuna biyar sun fadi,
daya na nan, amma dayan bai zo ba tukuna; sa'anda
ya zo zai kasance na dan lokaci kadan. 11 Dabban da
ya kasance a da, amma yanzu ba shi, shi ma sarki ne
na takwas; amma shi daya ne cikin sarakunan nan
bakwai, kuma zai tafi hallaka. 12 Kahonnin nan goma
da ka gani sarakuna goma ne wadanda ba a nada su
ba tukuna, amma za su karbi iko kamar na sarakai na
sa'a daya tare da dabban. 13 Ra'ayinsu daya ne, za su
ba da sarautarsu da ikon su ga dabban. 14 Za su yi yaki
da Dan Rago. Dan Ragon zai ci nasara a kansu domin
shi Ubangijin iyayengiji ne da Sarkin sarakuna - kuma
tare da shi sune kirayayyun, zababbun, amintattun.”
15 Mala'ikan ya ce mani, “Ruwayen da ka gani, inda
karuwar ke zaune, jama'a ce, da taro masu dumbin
yawa, da al'ummai da harsuna. 16 Kahonnin nan goma
da ka gani - su da dabban za su ki karuwar. Za su
washe ta su tsiranceta, za su lankwame namanta, za
su kone ta gaba daya da wuta. 17 Gama Allah ya sa
a zukantansu su yi nufinsa ta wurin amincewarsa,
su sadaukar da ikonsu na yin mulki ga dabban har
sai maganar Allah ta cika. 18 Matar da ka gani ita
ce babban birnin nan da ke mulki bisa sarakunan
duniya.”

18 Bayan wadannan abubuwa sai na ga wani mala'ika
yana saukowa daga sama. Yana da babban iko
sosai, duniya kuwa ta haskaka da daukakarsa. 2 Ya
yi kira da kakkarfar murya cewa, “Ta fadi, Babila
mai girma ta fadi! Ta zama mazaunin aljannu, da
matattarar kowanne kazamin ruhu da kuma mazaunin
kowanne kazami da kyamataccen tsuntsu. 3 Gama
dukan al'ummai sun sha ruwan innabin fasikancinta.
Sarakunan duniya sun aikata fasikanci da ita. Attajiran
duniya sun arzuta da ikon rayuwar annashuwarta.”
4 Sai na ji wata murya daga sama ta ce, “Ku fito
daga cikinta, mutanena, domin kada kuyi zunubi irin
na ta, domin kuma kada bala'inta ya auko maku.
5 Zunubanta sun taru sun yi tsayi har sama. Allah
kuma ya tuna da miyagun ayyukanta. 6 Ku saka mata
gwargwadon yadda ta saka wa wadansu, ku biya ta
ninki biyu na abin da ta yi; a cikin kokon da ta dama,
ku dama mata ninki biyu. 7 Kamar yadda ta daukaka
kanta ta yi ta annashuwa, ku wahalsheta da azaba da
bakin ciki haka. Domin ta ce a zuciyarta, 'Ina zaune
kamar sarauniya; ni ba gwauruwa ba ce, kuma ba
zan taba yin makoki ba,' 8 Saboda haka a rana daya
bala'inta zai auko mata; mutuwa, makoki da kuma
yunwa. Wuta za ta kona ta kurmus, domin Ubangiji
Allah mai iko ne, kuma shine mai hukuntata.” 9
Sarakunan duniya da suka yi fasikanci, har suka baude
tare da ita, za su yi kuka da kururuwa domin ta
sa'adda suka ga hayakin kunarta. 10 Za su tsaya can
nesa suna tsoron azabarta, suna cewa, “Kaito, kaiton
babban birni, Babila, birni mai iko! Domin cikin sa'a
guda hukuncinta ya zo.” 11 Manyan 'yan kasuwan
duniya za su yi kuka da bakin ciki dominta, da shike
ba wanda ke sayan kayanta kuma - 12 kayan zinariya,
azurfa, da duwatsun alfarma, da lu'u-lu'u, da lilin mai
laushi, da hajja mai ruwan jar garura, da siliki, da
jar alharini da itacen kamshi iri iri, da kayan da aka
sassaka da itace mai tsada, da na tagulla, da na bakin
karfe, da na dutse mai sheki, 13 da kirfa, da kayan
yaji, da turaren wuta, da mur da lubban, da ruwan
innabi, da mai, da garin alkama, da alkama, da shanu,
da tumaki, da dawakai, da kekunan doki, da bayi, da
rayukan 'yan adam. 14 Amfanin da kika kwallafa rai da
duk karfinki sun fice daga gareki. Duk annashuwarki
da darajarki sun bace, ba za a kara samunsu ba kuma.
15 Manyan 'yan kasuwa na wadannan kaya da suka
azurta ta wurinta, za su tsaya can nesa da ita, sabili
da tsoron azabarta, kuka da kururuwar bakin ciki.

16 Za su ce, “Kaito, kaito ga babban birni da take
sanye da lilin mai laushi da tufafi masu jar garura
da kuma jan alharini, da ta ci ado da kayan zinariya,
da duwatsu masu daraja da lu'u-lu'u! 17 A cikin sa'a
guda duk dukiyan nan ta lallace. Kowanne matukin
jirgin ruwa, da fasinjoji, da masu tuki da duk wadanda
suke samun biyan bukatun rayuwarsu daga ruwa,
suka tsaya can nesa. 18 Suka yi kuka sa'anda suka
ga hayakin kunarta. Suka ce, “Wanne birni ne ya
yi kama da babban birnin?” 19 Suka watsa kura a
kawunansu, suka yi kuka da karfi, da kururuwa da
bakin ciki, “Kaito, kaiton babban birnin nan inda duk
masu jiragen ruwa suka azurta daga dukiyarta. Domin
a sa'a guda an hallakar da ita.” 20 “Ku yi murna a
kanta, sama, ku masu ba da gaskiya, manzanni, da
annabawa, domin Allah ya kawo hukuncinku a kanta!”
21 Wani kakkarfan mala'ika ya dauki wani dutse mai
kama da dutsen nika, ya jefa shi cikin teku yana cewa,
“Ta wannan hanya, Babila, babban birnin, za a jefar
da ita kasa da karfi, ba za a kara ganinsa ba. 22 Muryar
masu kidar molaye, mawaka, masu busa sarewa, da na
masu busa algaita, ba za a kara ji a cikinta ba. Babu
wani mai kowanne irin sana'a da za a samu a cikinta.
Ba za a kara jin karar nika a cikinta ba. 23 Hasken
fitila ba za ya kara haskakawa a cikin ki ba. Ba za a
kara jin muryoyin ango da na amarya a cikinki ba,
domin attajiranki sune 'ya'yan masu mulki a duniya,
kuma ta wurin sihirinki kika yaudari al'ummai. 24 A
cikinta aka sami jinin annabawa da na masu ba da
gaskiya, da jinin duk wadanda aka kashe a duniya.”


**19** Bayan wadannan abubuwa na ji wata karar da ta
yi kamar muryar mutane masu yawa a sama suna
cewa, “Halleluya. Ceto, daukaka da iko sun tabbata ga
Allahnmu. 2 Hukunce - hukuncensa gaskiya ne da
adalci, domin ya hukunta babbar karuwan nan wadda
ta kazamtar da duniya da fasikancinta. Ya dauki fansar
jinin bayinsa, wadda ita da kanta ta zubar.” 3 Suka yi
magana a karo na biyu: “Halleluya! Hayaki na tasowa
daga wurinta har abada abadin.” (aiōn g165) 4 Dattawan
nan ashirin da hudu da rayayyun halittun nan hudu,
suka fadi suka yi wa Allah sujada shi da yake zaune
a kan kursiyin. Suna cewa, “Amin. Halleluya!” 5 Sai
wata murya ta fito daga kursiyin tana cewa, “Ku yabi
Allahnmu, dukanku bayinsa, ku da kuke tsoronsa, da
duk marasa iko da masu iko.” 6 Sai na ji murya kamar
na kasaitaccen taron mutane, kamar rurin kogi na
ruwaye masu yawa, kuma kamar tsawar aradu, cewa,
“Halleluya! Gama Ubangiji yana mulki, Allah mai iko
duka. 7 Bari mu yi murna, mu yi farinciki matuka mu
kuma ba shi daukaka domin bikin auren Dan Ragon
ya zo, amaryarsa kuma ta shirya kanta. 8 An yardar
mata ta sa kaya masu haske da tsabta na lilin mai
laushi” (domin lilin mai laushi shine ayyukan adalci
na tsarkaka). 9 Mala'ika ya ce mani, “Rubuta wannan:
Masu albarka ne wadanda aka gayyace su zuwa bikin
auren Dan Ragon.” Ya kuma ce mani, “Wadannan
kalmomin Allah na gaskiya ne.” 10 Na fadi a gaban
kafafunsa domin in yi masa sujada, amma ya ce mani,
“Kada ka yi haka! Ni ma abokin bauta ne tare da kai
da 'yan'uwanka wadanda ke rike da shaida game da
Yesu. Yi wa Allah sujada, domin shaida game da Yesu
shine ruhun annabci.” 11 Sai na ga sama a bude, na
kuma duba sai ga wani farin doki. Mahayinsa ana
kiransa amintacce da gaskiya. Yana shari'a da adalci
yana yaki. 12 Idanunsa kamar harshen wuta suke, a
kansa akwai kambuna da yawa. Yana da suna a rubuce
a jikinsa wanda ba wani da ya sani sai dai shi da
kansa. 13 Yana sanye da riga da aka tsoma a cikin jini,
kuma ana kiran sunansa Kalmar Allah. 14 Rundunonin
sama suna biye da shi a kan fararen dawakai, suna
sanye da lilin mai laushi, fari mai tsabta. 15 Daga cikin
bakinsa takobi mai kaifi na fitowa, da ita yake sarar
al'ummai, zai kuma mulke su da sandar karfe. Yana
tattake wurin matsar ruwan inabi da matsananciyar
fushin Allah Mai iko duka. 16 Yana da suna a rubuce a
rigarsa da cinyarsa: “Sarkin sarakuna da Ubangijin
iyayengiji.” 17 Na ga mala'ika tsaye a rana. Yayi
kira da murya mai karfi ga dukan tsuntsaye da ke
firiya a sama. 18 “Ku zo, ku tattaru saboda babban
bukin Allah. Ku zo ku ci naman sarakuna, da naman
sarakunan yaki, da naman manyan mutane, da naman
dawakai, da na mahayansu, da naman dukan mutane,
yantattu da bayi, marasa iko da masu iko.” 19 Na ga
dabban da sarakunan duniya da rundunoninsu. Suna
tattaruwa domin su yi yaki da wanda ke bisa doki da
rundunarsa. 20 Aka kama dabban tare da makaryatan
annabawa da suka yi ayyukan al'ajibai a gabansa.
Da wadannan alamu ya yaudari wadanda suka karbi
alamar dabbar da wadanda suka yi wa siffarta sujada.
Aka jefa dukansu biyu da rai cikin tafkin farar wuta
mai ci. (Limnē Pyr g3041 g4442) 21 Sauran aka karkashe su
da takobin da ke fitowa daga bakin mahayin dokin.
Dukan tsuntsaye suka ci gawarwakinsu.

**20** Sai na ga mala'ika na saukowa daga sama. Yana
da makullin rami marar iyaka, yana kuma da
babar sarka a hannunsa. (Abyssos g12) 2 Sai ya dauki
tsohon macijin, wanda shine iblis, ko shaidan, ya
daure shi shekaru dubu. 3 Ya jefa shi cikin rami marar
iyaka, ya rufe shi ya kuma sa hatimi a bisansa. Hakan
ya faru ne domin kada ya kara yaudarar al'ummai
har sai bayan shekaru dubu. Bayan wannan, dole a
sake shi na dan lokaci. (Abyssos g12) 4 Sa'annan na ga
kursiyoyi. Wadanda ke zaune a bisansu sune wadanda
aka ba ikon hukunci. Na kuma ga rayukan wadanda
aka fille wa kai saboda shaidar Yesu da maganar
Allah. Ba su yi wa dabban sujada ba ko siffarsa, suka
ki su karbi alamar a goshinsu ko a hannu. Sun sake
rayuwa, suka yi mulki tare da Kristi shekaru dubu.
5 Sauran matattun basu sake dawowa da rai ba har
sai da shekaru dubu din suka cika. Wannan shine
tashin matattu na fari. 6 Mai albarka ne mai tsarki ne
kuma wanda yake da rabo cikin tashin matattu na
fari! Mutuwa ta biyu ba ta da iko akan wadannan.
Za su zama firistocin Allah da na Almasihu za su
kuma yi mulki tare da shi shekaru dubu. 7 Sa'adda
shekaru dubu suka zo ga karshe, za a saki shaidan daga
kurkukunsa. 8 Za ya fito domin ya yaudari al'ummai
da ke kursuyoyi hudu na duniya, Gog da Magog ya
tattara su domin yaki. Yawan su zai zama kamar
yashin teku. 9 Suka bazu a fuskar duniya suka kuma
kewaye sansanin masu ba da gaskiya, kaunataccen
birni. Amma wuta ta sauko daga sama ta lankwame
su. 10 Shaidan, wanda ya yaudare su, aka jefa shi cikin
korama ta farin wuta mai ci, inda aka jefa dabban da
makaryacin annabin. Za su sha azaba dare da rana har
abada abadin. (aiōn g165, Limnē Pyr g3041 g4442) 11 Sai na ga
babban kursiyi da wanda ke zaune a kansa. Duniya da
sama suka guje wa fuskarsa, amma babu wurin da za
su tafi. 12 Na ga matattu manya da kanana- suna tsaye
gaban kursiyin, aka bude litattafai. Sai aka bude wani
littafi - Littafin rai. Aka yi wa matattu shari'a bisa
ga abinda aka rubuta cikin litattafan, gwargwadon
ayyukansu. 13 Teku ta ba da matattun dake cikinta.
Mutuwa da hades suka ba da matattun da ke cikinsu,
aka yi masu shari'a gwargwadon abin da suka yi. (Hadēs
g86) 14 Aka jefa mutuwa da hades cikin tafkin wuta.
Wannan shine mutuwa ta biyu - tafkin wuta. (Hadēs g86,
Limnē Pyr g3041 g4442) 15 Duk wanda ba a sami sunansa
a rubuce cikin littafin rai ba, aka jefar da shi cikin
tafkin wuta. (Limnē Pyr g3041 g4442)

**21** Sai na ga sabuwar sama da sabuwar duniya,
domin sama ta fari da duniya ta fari sun shude,
ba kuma teku. 2 Na ga birni mai tsarki, sabuwar
Urushalima, wadda ta sauko kasa daga sama wurin
Allah, shiryayya kamar amaryar da aka yi wa ado
domin mijinta. 3 Na ji babbar murya daga kursiyinta
na cewa, “Duba! Mazaunin Allah yana tare da 'yan
adam, zai zauna tare da su. Za su zama mutanensa,
Allah kuma da kansa zai kasance tare da su ya kuma
zama Allahnsu. 4 Zai share dukan hawaye daga
idanunsu, kuma babu sauran mutuwa, ko bakinciki,
ko kuka, ko azaba. Abubuwan da sun shude. 5 Shi
wanda yake zaune a kan kursiyin ya ce, “Duba! Na
maida kome ya zama sabo.” Ya ce, “Ka rubuta wannan
domin wadannan kalmomi amintattu ne da gaskiya”.
6 Ya ce mani, “Wadannan abubuwan an gama! Ni ne
Alpha da Omega, farko da karshe. Ga mai jin kishi, zan
bashi kyauta daga mabulbular ruwan rai. 7 Wanda ya
ci nasara, zai gaji wadannan abubuwa, ni kuma zan
zama Allahnsa, shi kuma ya zama da na. 8 Amma ga
matsorata, da marasa bangaskiya, da masu kazanta,
da masu kisan kai, da fasikai, da masu sihiri, da masu
bautar gumaka, da dukan makaryata, mazaunin su zai
kasance cikin tafki mai ci da farar wuta. Mutuwa ta
biyu kenan.” (Limnē Pyr g3041 g4442) 9 Daya daga cikin
mala'ikun bakwai ya zo wurina, wanda yake dauke
da tasoshi bakwai cike da annobai bakwai na karshe,
yace, “Zo nan. Zan nuna maka amarya, matar Dan
Rago”. 10 Sai ya dauke ni cikin Ruhu zuwa wani
babban dutse mai tsawo ya nuna mani birni mai-
tsarki, Urushalima, tana saukowa daga cikin sama
daga wurin Allah. 11 Urushalima tana da daukakar
Allah, shekinta yana kama da dutse mai tamani, sai
kace dutsen yasfa, garau kamar karau. 12 Tana da
babban garu mai tsawo, da kofofi goma sha biyu, da
mala'iku goma sha biyu a kofofin. Akan kofofin an
rubuta sunayen kabilu sha biyu na 'ya'yan Isra'ila.
13 A gabas akwai kofofi uku, a arewa kofofi uku, a
kudu kofofi uku, da kuma yamma kofofi uku. 14 Garun
birnin yana da harsashin gini goma sha biyu, a bisansu
akwai sunaye goma sha biyu na manzanni goma sha
biyu na Dan Rago. 15 Shi wanda yayi magana dani
yana da sandan awo na zinariya domin ya auna birnin,
da kofofinsa, da garunsa. 16 Birnin; da tsawonsa da
fadinsa iri daya ne. Ya gwada birnin da sandar awo,
mil dubu sha biyu a tsaye (fadinsa, da tsawonsa, da
tsayinsa duka daya ne) 17 Ya kuma gwada garunsa,

kamu 144, bisa ga gwajin 'yan adam (wanda shine
ma'aunin mala'ika). 18 An gina garun da Yasfa birnin
kuma da sahihiyar zinariya, mai kama da madubi mai
kyalli. 19 An kawata harsashin garun da kowanne irin
dutse mai tamani. Na fari yasfa, na biyu saffir, na uku
agat, na hudu emerald, 20 na biyar Onis, na shida
sardiyus, na bakwai kirisolat, na takwas beril, na tara
tofaz, na goma kirisofaras, na sha daya yakinta, na sha
biyu kuma ametis. 21 Kofofi goma sha biyu lu'u-lu'ai
ne goma sha biyu; kowacce daya a cikin kofofin daga
lu'u-lu'u daya aka yi shi. Titunan birnin kuwa zinariya
ce sahihiya, sai kace madubi garau. 22 Ban ga haikali a
cikin birnin ba, gama Ubangiji Allah Mai iko duka da
Dan Ragon su ne haikalinsa. 23 Birnin ba ya bukatar
rana ko wata su haskaka shi gama daukakar Allah ta
haskaka shi, kuma fitilarsa Dan Rago ne. 24 Al'ummai
za su yi tafiya cikin hasken birnin. Sarakunan duniya
kuma za su kawo daukakarsu cikinsa. 25 Kofofinsu
kuma ba za a rufe su da rana ba, babu dare kuma a
can. 26 Za su kawo daukaka da darajar al'ummai a
cikinsa, 27 babu wani abu mai kazanta da zai taba shiga
cikinsa. Ko wanda yake aikata abin kunya da karya,
sai wadanda an rubuta sunayensu a cikin littafin rai
na Dan Rago kadai.

22 Sai mala'ika ya nuna mani kogin ruwan rai, ruwa
mai tsabta. Yana fitowa daga cikin kursiyin Allah
da na Dan-Rago 2 ta tsakiyar titin birnin. A kowanne
gefen kogin akwai itacen rai, mai ba da 'ya'ya iri
goma sha biyu, kowanne wata. Ganyayen itacen kuma
domin warkar da al'ummai ne. 3 Babu sauran la'ana
nan gaba. Kursiyin Allah da na Dan Rago za su kasance
a cikin birnin, bayinsa kuma za su yi masa bauta. 4 Za
su ga fuskarsa, sunansa kuma zai kasance a goshinsu.
5 Babu sauran dare; ba za su bukaci hasken fitila ko
hasken rana ba gama Ubangiji Allah zai haskaka su.
Za su yi mulki har abada abadin. (aiōn g165) 6 Mala'ika
ya ce mani, "Wadannan kalmomi amintattu ne da
gaskiya. Ubangiji, Allah na ruhohin annabawa, ya
aiki mala'ikansa ya nuna wa bayinsa abin da lallai
zai faru ba da dadewa ba". 7 "Duba! Ina zuwa ba da
dadewa ba! Mai albarka ne wanda ya yi biyayya da
kalmomin littafin nan." 8 Ni, Yahaya, nine na ji na
kuma ga wadannan abubuwa. Sa'adda na ji na gan su,
sai na fadi gaban kafaffun mala'ikan da ya nuna mani
wadannan abubuwa domin in yi masa sujada. 9 Ya ce
mani, "Kada ka yi haka! Ni abokin bauta ne tare da
kai, tare da 'yan'uwanka annabawa, da wadanda ke
biyayya da kalmomin littafin nan. Yi sujada ga Allah!"
10 Ya ce mani, "Kada ka rufe kalmomin anabcin littafin
nan, gama lokaci ya kusa. 11 Wanda yake mara adalci,
bari ya cigaba da yin rashin adalci. Wanda yake mai
kazanta bari ya cigaba da kazantar da kansa. Wanda
yake mai adalci bari ya cigaba da yin adalci. Wanda
yake mai-tsarki, bari yaci gaba da tsarki." 12 "Duba!
Ina zuwa ba da dadewa ba. Sakamakona na tare da ni,
zan saka wa kowa gwargwadon aikin da ya yi. 13 Nine
Alpha da Omega, farko da karshe, mafarin abu da
karshensa. 14 Masu albarka ne wadanda suka wanke
rigunansu domin su sami izini su ci daga itacen rai
su kuma shiga birnin ta kofofinsa. 15 A waje akwai
karnuka, masu sihiri, masu bautar gumaka, fasikai,
masu kisan kai, da duk wanda yake kaunar aikata
rashin gaskiya. 16 Ni, Yesu na aiko mala'ikana ya
shaida maku wadannan abubuwa saboda ikilisiyoyi.
Nine tushe da zuriyar Dauda, tauraron asubahi mai-
haske." 17 Ruhu da Amarya suka ce, "Zo!" Bari wanda
ya ji ya ce, "Zo!" Kowanne mai jin kishi, da kowanne
mai bukatar ta, bari ya sami ruwan rai kyauta. 18 Ina
shaida wa duk mai jin kalmomin anabcin wannan
littafi: Idan wani ya kara a kansu, Allah zai kara masa
annoban da ke rubuce a cikin littafin. 19 Idan wani ya
rage daga kalmomin wannan littafin anabci, Allah zai
rage rabonsa daga cikin itacen rai daga cikin birni
mai-tsarki, wadanda aka rubuta cikin wannan littafi.
20 Shi wanda ya shaida wadannan abubuwa ya ce, "I!
Ina zuwa ba da dadewa ba." Amin! Zo, Ubangiji Yesu!
21 Alherin Ubangiji Yesu ya kasance tare da kowanne
dayanku. Amin.




*Na ga birni mai tsarki, sabuwar Urushalima, wadda ta sauko kasa daga sama wurin Allah, shiryayya kamar amaryar da aka yi wa ado domin mijinta. Na ji babbar murya daga kursiyinta na cewa, "Duba! Mazaunin Allah yana tare da 'yan adam, zai zauna tare da su. Za su zama mutanensa, Allah kuma da kansa zai kasance tare da su ya kuma zama Allahnsu.*
Ru'uya ta Yohanna 21:2-3

# Reader's Guide

Hausa at AionianBible.org/Readers-Guide

The Aionian Bible republishes public domain and Creative Common Bible texts that are 100% free to copy and print. The original translation is unaltered and notes are added to help your study. The notes show the location of eleven special Greek and Hebrew Aionian Glossary words to help us better understand God's love for individuals and for all mankind, and the nature of afterlife destinies.

Who has the authority to interpret the Bible and examine the underlying Hebrew and Greek words? That is a good question! We read in 1 John 2:27, *"As for you, the anointing which you received from him remains in you, and you do not need for anyone to teach you. But as his anointing teaches you concerning all things, and is true, and is no lie, and even as it taught you, you remain in him."* Every Christian is qualified to interpret the Bible! Now that does not mean we will all agree. Each of us is still growing in our understanding of the truth. However, it does mean that there is no infallible human or tradition to answer all our questions. Instead the Holy Spirit helps each of us to know the truth and grow closer to God and each other.

The Bible is a library with 66 books in the Protestant Canon. The best way to learn God's word is to read entire books. Read the book of Genesis. Read the book of John. Read the entire Bible library. Topical studies and cross-referencing can be good. However, the safest way to understand context and meaning is to read whole Bible books. Chapter and verse numbers were added for convenience in the 16th century, but unfortunately they can cause the Bible to seem like an encyclopedia. The Aionian Bible is formatted with simple verse numbering, minimal notes, and no cross-referencing in order to encourage the reading of Bible books.

Bible reading must also begin with prayer. Any Christian is qualified to interpret the Bible with God's help. However, this freedom is also a responsibility because without the Holy Spirit we cannot interpret accurately. We read in 1 Corinthians 2:13-14, *"And we speak of these things, not with words taught by human wisdom, but with those taught by the Spirit, comparing spiritual things with spiritual things. Now the natural person does not receive the things of the Spirit of God, for they are foolishness to him, and he cannot understand them, because they are spiritually discerned."* So we cannot understand in our natural self, but we can with God's help through prayer.

The Holy Spirit is the best writer and he uses literary devices such as introductions, conclusions, paragraphs, and metaphors. He also writes various genres including historical narrative, prose, and poetry. So Bible study must spiritually discern and understand literature. Pray, read, observe, interpret, and apply. Finally, *"Do your best to present yourself approved by God, a worker who does not need to be ashamed, properly handling the word of truth."* 2 Timothy 2:15. *"God has granted to us his precious and exceedingly great promises; that through these you may become partakers of the divine nature, having escaped from the corruption that is in the world by lust. Yes, and for this very cause adding on your part all diligence, in your faith supply moral excellence; and in moral excellence, knowledge; and in knowledge, self-control; and in self-control patience; and in patience godliness; and in godliness brotherly affection; and in brotherly affection, love. For if these things are yours and abound, they make you to be not idle nor unfruitful to the knowledge of our Lord Jesus Christ,"* 2 Peter 1:4-8.

# Glossary

Hausa at AionianBible.org/Glossary

The Aionian Bible un-translates and instead transliterates eleven special words to help us better understand the extent of God's love for individuals and all mankind, and the nature of afterlife destinies. The original translation is unaltered and a note is added to 64 Old Testament and 200 New Testament verses. Compare the meanings below to the Strong's Concordance and Glossary definitions.

### ***Abyssos*** g12

*Greek:* proper noun, place
*Usage:* 9 times in 3 books, 6 chapters, and 9 verses
*Meaning:*
Temporary prison for special fallen angels such as Apollyon, the Beast, and Satan.

### ***aïdios*** g126

*Greek:* adjective
*Usage:* 2 times in Romans 1:20 and Jude 6
*Meaning:*
Lasting, enduring forever, eternal.

### ***aiōn*** g165

*Greek:* noun
*Usage:* 127 times in 22 books, 75 chapters, and 102 verses
*Meaning:*
A lifetime or time period with a beginning and end, an era, an age, the completion of which is beyond human perception, but known only to God the creator of the aiōns, Hebrews 1:2. Never meaning simple endless or infinite chronological time in Greek usage. Read Dr. Heleen Keizer and Ramelli and Konstan for proofs.

### ***aiōnios*** g166

*Greek:* adjective
*Usage:* 71 times in 19 books, 44 chapters, and 69 verses
*Meaning:*
From start to finish, pertaining to the age, lifetime, entirety, complete, or even consummate. Never meaning simple endless or infinite chronological time in Koine Greek usage. Read Dr. Heleen Keizer and Ramelli and Konstan for proofs.

### ***eleēsē*** g1653

*Greek:* verb, aorist tense, active voice, subjunctive mood, 3rd person singular
*Usage:* 1 time in this conjugation, Romans 11:32
*Meaning:*
To have pity on, to show mercy. Typically, the subjunctive mood indicates possiblity, not certainty. However, a subjunctive in a purpose clause is a resulting action as certain as the causal action. The subjunctive in a purpose clause functions as an indicative, not an optative. Thus, the grand conclusion of grace theology in Romans 11:32 must be clarified. God's mercy on all is not a possibility, but a certainty. See ntgreek.org.

***Geenna*** g1067
*Greek:* proper noun, place
*Usage:* 12 times in 4 books, 7 chapters, and 12 verses
*Meaning:*
Valley of Hinnom, Jerusalem's trash dump, a place of ruin, destruction, and judgment in this life, or the next, though not eternal to Jesus' audience.

***Hadēs*** g86
*Greek:* proper noun, place
*Usage:* 11 times in 5 books, 9 chapters, and 11 verses
*Meaning:*
Synonomous with Sheol, though in New Testament usage Hades is the temporal place of punishment for deceased unbelieving mankind, distinct from Paradise for deceased believers.

***Limnē Pyr*** g3041 g4442
*Greek:* proper noun, place
*Usage:* Phrase 5 times in the New Testament
*Meaning:*
Lake of Fire, final punishment for those not named in the Book of Life, prepared for the Devil and his angels, Matthew 25:41.

***Sheol*** h7585
*Hebrew:* proper noun, place
*Usage:* 66 times in 17 books, 50 chapters, and 64 verses
*Meaning:*
The grave or temporal afterlife world of both the righteous and unrighteous, believing and unbelieving, until the general resurrection.

***Tartaroō*** g5020
*Greek:* proper noun, place
*Usage:* 1 time in 2 Peter 2:4
*Meaning:*
Temporary prison for particular fallen angels awaiting final judgment.

# Glossary +

AionianBible.org/Bibles/Hausa---Hausa-Bible/Noted

Glossary references are below. Strong's Hebrew and Greek number notes are added to 64 Old Testament and 200 New Testament verses. Questioned verse translations do not contain Aionian Glossary words and may wrongly imply *eternal* or *Hell*. * The note placement is skipped or adjusted for verses with non-standard numbering.

## *Abyssos*

Luka 8:31
Romawa 10:7
Ru'uya ta Yohanna 9:1
Ru'uya ta Yohanna 9:2
Ru'uya ta Yohanna 9:11
Ru'uya ta Yohanna 11:7
Ru'uya ta Yohanna 17:8
Ru'uya ta Yohanna 20:1
Ru'uya ta Yohanna 20:3

## *aïdios*

Romawa 1:20
Yahuda 1:6

## *aiōn*

Mattiyu 12:32
Mattiyu 13:22
Mattiyu 13:39
Mattiyu 13:40
Mattiyu 13:49
Mattiyu 21:19
Mattiyu 24:3
Mattiyu 28:20
Markus 3:29
Markus 4:19
Markus 10:30
Markus 11:14
Luka 1:33
Luka 1:55
Luka 1:70
Luka 16:8
Luka 18:30
Luka 20:34
Luka 20:35
Yohanna 4:14
Yohanna 6:51
Yohanna 6:58
Yohanna 8:35
Yohanna 8:51
Yohanna 8:52
Yohanna 9:32
Yohanna 10:28
Yohanna 11:26
Yohanna 12:34
Yohanna 13:8
Yohanna 14:16
Ayyukan Manzanni 3:21
Ayyukan Manzanni 15:18
Romawa 1:25
Romawa 9:5
Romawa 11:36
Romawa 12:2
Romawa 16:27
1 Korintiyawa 1:20
1 Korintiyawa 2:6
1 Korintiyawa 2:7
1 Korintiyawa 2:8
1 Korintiyawa 3:18
1 Korintiyawa 8:13
1 Korintiyawa 10:11
2 Korintiyawa 4:4
2 Korintiyawa 9:9
2 Korintiyawa 11:31
Galatiyawa 1:4
Galatiyawa 1:5
Afisawa 1:21
Afisawa 2:2
Afisawa 2:7
Afisawa 3:9
Afisawa 3:11
Afisawa 3:21
Afisawa 6:12
Filibbiyawa 4:20
Kolossiyawa 1:26
1 Timoti 1:17
1 Timoti 6:17
2 Timoti 4:10
2 Timoti 4:18
Titus 2:12
Ibraniyawa 1:2
Ibraniyawa 1:8
Ibraniyawa 5:6
Ibraniyawa 6:5
Ibraniyawa 6:20
Ibraniyawa 7:17
Ibraniyawa 7:21
Ibraniyawa 7:24
Ibraniyawa 7:28
Ibraniyawa 9:26
Ibraniyawa 11:3
Ibraniyawa 13:8
Ibraniyawa 13:21
1 Bitrus 1:23
1 Bitrus 1:25
1 Bitrus 4:11
1 Bitrus 5:11
2 Bitrus 3:18
1 Yohanna 2:17
2 Yohanna 1:2
Yahuda 1:13
Yahuda 1:25
Ru'uya ta Yohanna 1:6
Ru'uya ta Yohanna 1:18
Ru'uya ta Yohanna 4:9
Ru'uya ta Yohanna 4:10
Ru'uya ta Yohanna 5:13
Ru'uya ta Yohanna 7:12
Ru'uya ta Yohanna 10:6
Ru'uya ta Yohanna 11:15
Ru'uya ta Yohanna 14:11
Ru'uya ta Yohanna 15:7
Ru'uya ta Yohanna 19:3
Ru'uya ta Yohanna 20:10
Ru'uya ta Yohanna 22:5

## *aiōnios*

Mattiyu 18:8
Mattiyu 19:16
Mattiyu 19:29
Mattiyu 25:41
Mattiyu 25:46
Markus 3:29
Markus 10:17
Markus 10:30
Luka 10:25
Luka 16:9
Luka 18:18
Luka 18:30
Yohanna 3:15
Yohanna 3:16
Yohanna 3:36
Yohanna 4:14
Yohanna 4:36
Yohanna 5:24
Yohanna 5:39
Yohanna 6:27
Yohanna 6:40
Yohanna 6:47
Yohanna 6:54
Yohanna 6:68

Yohanna 10:28
Yohanna 12:25
Yohanna 12:50
Yohanna 17:2
Yohanna 17:3
Ayyukan Manzanni 13:46
Ayyukan Manzanni 13:48
Romawa 2:7
Romawa 5:21
Romawa 6:22
Romawa 6:23
Romawa 16:25
Romawa 16:26
2 Korintiyawa 4:17
2 Korintiyawa 4:18
2 Korintiyawa 5:1
Galatiyawa 6:8
2 Tessalonikawa 1:9
2 Tessalonikawa 2:16
1 Timoti 1:16
1 Timoti 6:12
1 Timoti 6:16
2 Timoti 1:9
2 Timoti 2:10
Titus 1:2
Titus 3:7
Filemon 1:15
Ibraniyawa 5:9
Ibraniyawa 6:2
Ibraniyawa 9:12
Ibraniyawa 9:14
Ibraniyawa 9:15
Ibraniyawa 13:20
1 Bitrus 5:10
2 Bitrus 1:11
1 Yohanna 1:2
1 Yohanna 2:25
1 Yohanna 3:15
1 Yohanna 5:11
1 Yohanna 5:13
1 Yohanna 5:20
Yahuda 1:7
Yahuda 1:21
Ru’uya ta Yohanna 14:6

## eleēsē

Romawa 11:32

## Geenna

Mattiyu 5:22
Mattiyu 5:29
Mattiyu 5:30
Mattiyu 10:28
Mattiyu 18:9
Mattiyu 23:15
Mattiyu 23:33
Markus 9:43
Markus 9:45
Markus 9:47
Luka 12:5
Yaƙub 3:6

## Hadēs

Mattiyu 11:23
Mattiyu 16:18
Luka 10:15
Luka 16:23
Ayyukan Manzanni 2:27
Ayyukan Manzanni 2:31
1 Korintiyawa 15:55
Ru’uya ta Yohanna 1:18
Ru’uya ta Yohanna 6:8
Ru’uya ta Yohanna 20:13
Ru’uya ta Yohanna 20:14

## Limnē Pyr

Ru’uya ta Yohanna 19:20
Ru’uya ta Yohanna 20:10
Ru’uya ta Yohanna 20:14
Ru’uya ta Yohanna 20:15
Ru’uya ta Yohanna 21:8

## Sheol


Farawa 37:35
Farawa 42:38
Farawa 44:29
Farawa 44:31
Ƙidaya 16:30
Ƙidaya 16:33
Maimaitawar Shari’a 32:22
1 Sama’ila 2:6
2 Sama’ila 22:6
1 Sarakuna 2:6
1 Sarakuna 2:9
Ayuba 7:9
Ayuba 11:8
Ayuba 14:13
Ayuba 17:13
Ayuba 17:16
Ayuba 21:13
Ayuba 24:19
Ayuba 26:6
Zabura 6:5
Zabura 9:17
Zabura 16:10
Zabura 18:5
Zabura 30:3
Zabura 31:17
Zabura 49:14
Zabura 49:15
Zabura 55:15
Zabura 86:13
Zabura 88:3
Zabura 89:48
Zabura 116:3
Zabura 139:8
Zabura 141:7
Karin Magana 1:12
Karin Magana 5:5
Karin Magana 7:27
Karin Magana 9:18
Karin Magana 15:11
Karin Magana 15:24
Karin Magana 23:14
Karin Magana 27:20
Karin Magana 30:16
Mai Hadishi 9:10
Waƙar Waƙoƙi 8:6
Ishaya 5:14
Ishaya 7:11
Ishaya 14:9
Ishaya 14:11
Ishaya 14:15
Ishaya 28:15
Ishaya 28:18
Ishaya 38:10
Ishaya 38:18
Ishaya 57:9
Ezekiyel 31:15
Ezekiyel 31:16
Ezekiyel 31:17
Ezekiyel 32:21
Ezekiyel 32:27
Hosiya 13:14
Amos 9:2
Yunana 2:2
Habakkuk 2:5

## Tartaroō


2 Bitrus 2:4

## Questioned


None yet noted




*Ta dalilin bangaskiya ne Ibrahim, sa'an da aka kira shi, ya yi biyayya sai ya tafi wurin da zai karba a matsayin gado.*
*Ya kwa fita bai ma san inda za shi ba.* - Ibraniyawa 11:8




*"When Pharaoh had let the people go, God didn't lead them by the way of the land of the Philistines, although that was near; for God said, 'Lest perhaps the people change their minds when they see war, and they return to Egypt'"* Exodus 13:17




*Saboda haka ne Dan mutum ya zo ba domin a bauta masa ba, sai dai domin shi yayi bautar, ya kuma ba da ransa fansa saboda da mutane da yawa.* - Markus 10:45




*Bulus, bawan Yesu Almasihu, kirayayye ya zama manzo, kuma kebabbe domin bisharar Allah.* - Romawa 1:1

## Creation 4004 B.C.

| | |
|---|---|
| Adam and Eve created | 4004 |
| Tubal-cain forges metal | 3300 |
| Enoch walks with God | 3017 |
| Methuselah dies at age 969 | 2349 |
| God floods the Earth | 2349 |
| Tower of Babel thwarted | 2247 |
| Abraham sojourns to Canaan | 1922 |
| Jacob moves to Egypt | 1706 |
| Moses leads Exodus from Egypt | 1491 |
| Gideon judges Israel | 1245 |
| Ruth embraces the God of Israel | 1168 |
| David installed as King | 1055 |
| King Solomon builds the Temple | 1018 |
| Elijah defeats Baal’s prophets | 896 |
| Jonah preaches to Nineveh | 800 |
| Assyrians conquer Israelites | 721 |
| King Josiah reforms Judah | 630 |
| Babylonians capture Judah | 605 |
| Persians conquer Babylonians | 539 |
| Cyrus frees Jews, rebuilds Temple | 537 |
| Nehemiah rebuilds the wall | 454 |
| Malachi prophecies the Messiah | 416 |
| Greeks conquer Persians | 331 |
| Seleucids conquer Greeks | 312 |
| Hebrew Bible translated to Greek | 250 |
| Maccabees defeat Seleucids | 165 |
| Romans subject Judea | 63 |
| Herod the Great rules Judea | 37 |

(The Annals of the World, James Uusher)

## Jesus Christ born 4 B.C.

## New Heavens and Earth

| | |
|---|---|
| | Christ returns for his people |
| 1956 | Jim Elliot martyrd in Ecuador |
| 1830 | John Williams reaches Polynesia |
| 1731 | Zinzendorf leads Moravian mission |
| 1614 | Japanese kill 40,000 Christians |
| 1572 | Jesuits reach Mexico |
| 1517 | Martin Luther leads Reformation |
| 1455 | Gutenberg prints first Bible |
| 1323 | Franciscans reach Sumatra |
| 1276 | Ramon Llull trains missionaries |
| 1100 | Crusades tarnish the church |
| 1054 | The Great Schism |
| 997 | Adalbert marytyrd in Prussia |
| 864 | Bulgarian Prince Boris converts |
| 716 | Boniface reaches Germany |
| 635 | Alopen reaches China |
| 569 | Longinus reaches Alodia / Sudan |
| 432 | Saint Patrick reaches Ireland |
| 397 | Carthage ratifies Bible Canon |
| 341 | Ulfilas reaches Goth / Romania |
| 325 | Niceae proclaims God is Trinity |
| 250 | Denis reaches Paris, France |
| 197 | Tertullian writes Christian literature |
| 70 | Titus destroys the Jewish Temple |
| 61 | Paul imprisoned in Rome, Italy |
| 52 | Thomas reaches Malabar, India |
| 39 | Peter reaches Gentile Cornelius |
| 33 | Holy Spirit empowers the Church |

(Wikipedia, Timeline of Christian missions)

## Resurrected 33 A.D.

| Where? Who? | | When? | | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| | | **Innocence** | | **Fallen** | | | | **Glory** | |
| | | **Eternity Past** | **4000 BC Creation** | **Fall to Sin No Law** | **1500 BC Moses' Law** | **Advent of Christ 0-33 AD** | **Church Age Kingdom Age** | **Great White Throne** | **New Heaven and Earth** |
| **God** | **Father** | God's Perfect Fellowship<br><br>John 10:30 | God's Perfect Fellowship with Adam in the Garden of Eden<br><br>No Fall<br>No Death<br><br>Gen 1:31 | Living in Unapproachable Light, 1 Timothy 6:16 | | | | God's Perfectly Restored Fellowship with All Mankind in the Holy City<br><br>No Hades<br>No Dead<br><br>Rev 20:3 | All Restored<br><br>Acts 3:21 |
| | **Son** | | | Pre-Incarnate, John 8:58 | | Incarnate, John 1:14 | Paradise, Luke 23:43 | | |
| | **Holy Spirit** | | | Everywhere, Psalm 139:7 | | Indwelling Believers, John 14:17 | | | |
| **Mankind** | **Living Mankind** | No Creation<br><br>No people<br><br>Gen 1:1 | | Serving the Savior or Satan on Earth, Ephesians 2:1-5 | | | | | |
| | **Deceased Believing Mankind** | | | Blessed in Paradise, Luke 16:22 | | | | | |
| | **Deceased Unbelieving Mankind** | | | Punished in Hades until the final judgment, Luke 16:23 and Rev 20:13 | | | | | |
| **Angels** | **Holy Angels** | | | Serving Mankind at God's Command, Hebrews 1:14 | | | | | |
| | **Imprisoned Angels** | | No Fall<br><br>No Unholy Angels<br><br>Gen 1:31 | Imprisoned in Tartarus, 2 Peter 2:4 and Jude 6 | | | | Lake of Fire Prepared for the Devil and his Angels<br><br>Mat 25:41<br>Rev 20:10 | Fallen Angels Forgiven?<br><br>Col 1:20<br>Yes?<br><br>Heb 2:16<br>No? |
| | **Fugitive Angels** | | | Rebelling Against Christ<br><br>Accusing Mankind<br><br>1 Peter 5:8 and Revelation 12:10 | | | Thalaasa, Rev 20:13 | | |
| | **First Beast Demon** | | | | | | Lake of Fire<br>Revelation 19:20 | | |
| | **False Prophet Demon** | | | | | | | | |
| | **Satan** | | | | | | Abyss<br>Revelation 20:2 | | |

# Destiny

Hausa at AionianBible.org/Destiny

The Aionian Bible shows the location of eleven special Greek and Hebrew Aionian Glossary words to help us better understand God's love for individuals and for all mankind, and the nature of after-life destinies. The underlying Hebrew and Greek words typically translated as *Hell* show us that there are not just two after-life destinies, Heaven or Hell. Instead, there are a number of different locations, each with different purposes, different durations, and different inhabitants. Locations include 1) Old Testament *Sheol* and New Testament *Hadēs*, 2) *Geenna*, 3) *Tartaroō*, 4) *Abyssos*, 5) *Limnē Pyr*, 6) *Paradise*, 7) *The New Heaven*, and 8) *The New Earth*. So there is reason to review our conclusions about the destinies of redeemed mankind and fallen angels.

The key observation is that fallen angels will be present at the final judgment, 2 Peter 2:4 and Jude 6. Traditionally, we understand the separation of the Sheep and the Goats at the final judgment to divide believing from unbelieving mankind, Matthew 25:31-46 and Revelation 20:11-15. However, the presence of fallen angels alternatively suggests that Jesus is separating redeemed mankind from the fallen angels. We do know that Jesus is the helper of mankind and not the helper of the Devil, Hebrews 2. We also know that Jesus has atoned for the sins of all mankind, both believer and unbeliever alike, 1 John 2:1-2. Deceased believers are rewarded in Paradise, Luke 23:43, while unbelievers are punished in Hades as the story of Lazarus makes plain, Luke 16:19-31. Yet less commonly known, the punishment of this selfish man and all unbelievers is before the final judgment, is temporal, and is punctuated when Hades is evacuated, Revelation 20:13. So is there hope beyond Hades for unbelieving mankind? Jesus promised, *"the gates of Hades will not prevail,"* Matthew 16:18. Paul asks, *"Hades where is your victory?"* 1 Corinthians 15:55. John wrote, *"Hades gives up,"* Revelation 20:13.

Jesus comforts us saying, *"Do not be afraid,"* because he holds the keys to *unlock* death and Hades, Revelation 1:18. Yet too often our *Good News* sounds like a warning to *"be afraid"* because Jesus holds the keys to *lock* Hades! Wow, we have it backwards! Hades will be evacuated! And to guarrantee hope, once emptied, Hades is thrown into the Lake of Fire, never needed again, Revelation 20:14.

Finally, we read that anyone whose name is not written in the Book of Life is thrown into the Lake of Fire, the second death, with no exit ever mentioned or promised, Revelation 21:1-8. So are those evacuated from Hades then, *"out of the frying pan, into the fire?"* Certainly, the Lake of Fire is the destiny of the Goats. But, do not be afraid. Instead, read the Bible's explicit mention of the purpose of the Lake of Fire and the identity of the Goats, *"Then he will say also to those on the left hand, 'Depart from me, you cursed, into the consummate fire which is prepared for... the devil and his angels,'"* Matthew 25:41. Bad news for the Devil. Good news for all mankind!

Faith is not a pen to write your own name in the Book of Life. Instead, faith is the glasses to see that the love of Christ for all mankind has already written our names in Heaven. *"If the first fruit is holy, so is the lump,"* Romans 11:16. Though unbelievers will suffer regrettable punishment in Hades, redeemed mankind will never enter the Lake of Fire, prepared for the devil and his angels. And as God promised, all mankind will worship Christ together forever, Philippians 2:9-11.




*Sai kuje ku almajirantar da dukan al'ummai. Kuna yi masu baftisma cikin sunan Uba da na Da da na Ruhu Mai Tsarki.* - Mattiyu 28:19